[1/7, 9:31 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

Page 1

Nimcyluv

Bright pens.... second batch

Marubuciyar....❤

Mijin malama

Munafukin miji

Moon

Idan ba ke

..... E.t.c and now *MUTALLAB*

for some reasons.... Akwai copywrite kar a haɗa mini ducoment, banda YouTube a bar mini kayana haƙƙina ne

Jami'an tsaro ne ta ko'ina cikin kayan kaki ma bambanta, duk da cewa yammacin ranar lahadi ne a watan Fabrairu bai hana ta gane fuskarsa ba. Cikin tashin hankali jikinta na rawa da kyarma ta nufe shi tare da ƙoƙarin cakomo wuyan babbar rigarsa tana furta cewa "Shi ne, wallahi shi ne, daman na ce zan gano shi" a gigice

mutumin dake ƙoƙarin shiga motarsa da aka buɗe masa ya yi baya yana mai ƙarewa matar kallo sosai sai dai ya kasa gano ko wace ita? Daga ina me kuma take buƙata.

"Wace ita?" Ya furta yana tambayar zuciyarsa tare da kallon gefe. "Wallahi shi ne, mugu azzalumi sai ka yi kuka, ka wulaƙanta " Jin furucinta ya saka yan'jarida dawowa kan ta, suka fara tambayar "Kin san shine? Mene haɗinki da shi?" Kafin ta yi magana wani ya ce "Arrest her, ku kamata"

A hankali ya jingina da jikin motar can ya numfasa yana kallon yaronsa ya ce "Wace ce? Na santa ne? To me ya sa take abu kamar ta sanni?"

"Sir da gaske ta sanka bana jin ko mutuwa ta yi ta dawo zata manta fuskarka, kuma zamanta a raye yana nufin abubuwan da yawa dole a yi wa tufkar hanci, kar a bari yan'jarida su samu ganawa da ita, even your securites, wannan matsalar kai da kai ce kuma zata shafi kimarka" cike da mamaki ya yi ta kallon yaron nasa na tsayin sacanni da ƙyar ya cije leɓe ya ce "To ina na santa? Me ya sa zata zama damuwata?"

"Sir ita ce wacce ka saka aka kawo maka ita, wacce ka yi wa fyaɗe a lokacin....."

"Ya isa!" Ya ce yana jin jiri na neman ɗauke shi, ya dubi tarin jama'ar da suke wajan can ya yi murmushi yana ɗauke fuska sai kuma ya ƙurawa yaron idanu ya juya ya kalli matar ya gyatsine fuska ya ce "kuma ta kasance a raye ya haka? To a yi hanzarin toshe wannan ɓarnar ya zama kamar ba a yi ba"

"Amma me ya kamata a yi mata?"

"A yi mata allurar hauka, wacce ake yi duk shekara da wata wata kana a kaita gidan yari, life in prison har ta mutu. Bayan haukan zata mance komai, su yanyan talakawa wama ya damu da su mutu ko su yi rai bata da wani mai tsaya mata kai mutuwa ma za ta yi" yana faɗin hakan ya shige mota. Tana takure a jikin ƙofar ɗakin da aka ajjiyeta idanunta ƙur a kan photonsa zuciyarta sai zafi take mata wani abu ya tsaya mata. Da sauri ta juya jin an buɗe ƙofa wani mutum ne sanye da farar

riga ya rufe fuskarsa hannunsa riƙe da ƙaton sirinji iya ruwan allurar da ya yi ja abin tsoro ne, ta fara ja da baya amma a haka ya fincikota tare da yin cilli da ita,ta faɗi saman carpet bai tsaya jiran komai ba ya caka mata allurar a ƙashin bayanta wajan spinal cord ihu ta fara da birgima idanunta ya shiga ƙaƙƙafewa jikinta na sandarewa ta dinga buga kanta da jikin bango tana buge-buge a hankali jini ya fara fitowa ta cikin hanci da bakinta tabbacin allurar ta amshe ta za kuma ta yi aikin da ake buƙata a jiki da ƙwaƙwalwarta.

******

Cikin sauri suke tafiya a wani ɗan dogon lungu mai duhun gaske tsarin wajan gabaɗaya a ƙuntacce yake kamar zunubin gidan yari. Magana suke ƙasa-ƙasa ɗaya daga cikin su kuma yana duba agogon dake hannunsa tare da duba cikar lokacin fuskarsa a haɗe take sosai. Sai da suka kawo ƙarshen ginin suka tsaya ya ɗaga kai a hankali ya dubi saman da kansa ke taɓowa ya ɗan rusuna sai kuma ya dubi jami'in tsaron dake wajan ya yi masa nuni daya buɗe ƙofar. "Yes sir!"

Bayan ya sara ya ƙame ya buɗe ƙaton kwaɗon yana toshe hanci saboda wari da zarnin wajan. SP Gali ya kalli team ɗin nasa cikin bada umarni ya ce

"Ku jira nan, idan akwai damuwa zan muku alama na san dai he can't do anything, ba zai iya komai ba" gabaɗaya suka jinjina masa kai tare da zagaye ƙofar fuskar kowannen su manne da baƙin gilas. A hankali Sp Gali ya tura ƙofar ya shiga yana durƙosawa saboda rashin girman wajan. Tunda kafin su ƙarasu wajan ya san da zuwan nasu har aka buɗe ƙofar tare da shigowa, yana durƙushe inda yake ya kifa kansa a ƙasa hannunsa dunƙule ya damƙe abu wanda tun kafin a kawo shi gidan abu yake a hannunsa, yin duniya yaƙi buɗe abun balle a san menene shi.

"Hey you!" Sp Gali ya ce yana saka ƙafa tare da buge ƙafarsa ganin yaƙi motsawa, tamkar gunki haka yaƙi motsi ya kuma ƙi ɗago kansa Sp Gali ya shiga kallon wajan ya rasa wanne irin hali ne da wannan yaron mai baƙar zuciya da taurin kai ya sauke numfashi cikin kwantar da murya ya ce "Ni idan na ce maka ina da tausayi na yi maka ƙarya, amma ka saka zuciyata karaya kana bawa kanka wahala kana bawa jami'anmu wahala. Me zai hana ka sauƙaƙa mana wahalar nan ka faɗa mana gaskiyar abin da ya faru a wannan rana kuma a wannan daren? Me ya sa ka aika abin da ka aikata? Ka kashe matarka, ka kashe ta har lahira kuma kaƙi magana shekara uku kenan kana wajanmu ka rainawa hukuma hankali da kotu, kai baka da zuciya ne dame kake taƙama saboda kana da tsari a jikinka ƙarfe ba zai ratsa naman jikinka ba, muna da kalolin azaba nau'i-nau'i amma gaskiya muke buƙata, ka

amsa cewa ka kashe matarka a zaman kotu na yau shikenan sai a yanke maka hukunci daidai da zaluncin da ka aikata"

Har Sp Gali ya kammala maganarsa bai motsa ba, babu alamun zai ɗago kai balle ya tanka. Sp ya miƙa hannu zuwa hannun mutumin dake dunƙule da abu zai amsa a firgice ya ɗago kansa yana buɗe dara-daran idanuwansa akan Sp Gali sai da zuciyarsa Sp ta motsa saboda wani mugun jaa da idanunsa ya yi. Fuska ɗaure ya yi wa Sp kallon warning har lokacin bai yi magana ba dukkan naman jikinsa rawa yake kamar zai kaiwa Sp damƙa fuskarsa baibaye da gashi kansa ma cunkus yake ba'a gane kamanninsa sosai saboda cikar gashi.

Sp ya duba lokaci sai kuma ya shafa kai ya ce "SCORPIO" nan ma ya sake ɗago kai da sauri ya zubawa Sp idanu "Idan ka bari na gano cewa kai ne Scorpio...."

Ya cije baki yana miƙewa tsaye ya furta "Zan addabi rayuwarka, gwara ka zauna a iya wanda ya kashe matarsa da dai ka kasance kai ne Scorpio. Mene asalin sunan naka?" Ya tambaya yana juyawa kamar zai fita saukar gurnanin da ya ji ya saka ya yi saurin juyawa idanunsa ya sauka wanda ake zargi da kashe matar tasa yaga ya dafe kai da hannu bibbiyu yana jujjuyawa ya dinga haɗa kansa da bango cikin sauri Sp Gali ya ce

"Team" a guje suka shigo hakan ya saka ɗan ƙaramin ɗakin cika fuskar Sp ba wasa ya ce "Ku danne shi a karɓo abin hannunsa dole mu san mene babu mamaki zamu samu hujja a ciki" yana cewa haka ya fita yana amsa kira. Ganin sunyo kansa ya yunƙura gabaɗaya ya fisu faɗin ƙirji da damtse amma suka rufar masa sanin cewa sarkin yawa ya fi sarkin ƙarfi ya saka shi damƙe hannunsa da kyau yana ɓoye abun da suka karɓa, kokawa suke da shi ya dinga haɗa su da bango ya kama hannun ɗayan ya karya bisa dole suka fice a wahale. Sp ya saka wasu manyan mutane fito da shi suka ɗaure shi da ankwa tare da sarƙa tun daga ƙafa har zuwa kansa.

A harabar Criminal Investigation department CID aka tsaya dashi domin tafiya zuwa kuto a rana ta ƙarshe wanda ke nuna ko a sake shi, ko a kashe shi ko kuma ya tafi gidan ɗan'kande. Team guda ne masu matuƙar basira da ƙwarewa akan aikinsu team ɗin ya haɗa da wanda yake ɓangaren Legal section, Anti-human trafficking, Medical Staff, Legal services, NDLEA, FID Federal investigation department. Gabaɗaya idanunsu yana kansa kowanne yana karantar yanayinsa amma shi ko a jikinsa banda faratansa na hannu dana ƙafa da aka ciccire wajan gana masa azaba

babu wani rauni a tattare da shi sai matsanancin baƙi da ya yi ya zama kamar mahaukaci saboda shekarun daya ɗauka a kulle daga kuto zuwa state cid zuwa Fid amma har tsayin shekarun bai buɗe baki ya yi magana da kowa ba, babu kuma wanda ya damu daya tsaya masa. Suna ta surutai ƙasa-ƙasa duk yana jinsu har sanda wani yake cewa "Babu hanyar da za a tilasta shi ya yi magana ne? Muna buƙatar muryarsa"

Sp Gali ya ce "Ina zargin wani abu game da matarsa daya kashe"

"Wanne abu? A binciken da mukai a wajan iyayen yarinyar tun farko ita ta nuna tana son shi, shi da ita class mate ne kuma age mate, tun suna shekaru 15 a secondary school suke soyayya. Me ya sa ya zaɓi ya kashe ta? Sun ɗauki shekaru tare bai taɓa yunƙurin rabata da duniya ba sai ranar da aka ɗaura musu aure? This is complicated" C.i.d Research ya jinjina kai ya ce

"Duk binciken da aka yi shine a ruwa, gwajin hannu, yatsun hannu da sahun tafin ƙafa da CCTV camera na kan titin unguwar da aka kai amaryar tasa duk bincika shine"

Shiru sukai suna tunanin gabaɗaya kansu ya ɗauki zafi. Yana da can inda yake ya ja idanunsa ya lumshe yana fesar da iska daga cikin hancin wacce hucinta ya sauka har saman fuskarsa “BESTIE” haka ya ji saukar muryarta a kunnensa kamar yanzu ne suke tare da ita. Ya sake lumshe idanunsa yana jin saukar dariyarta sosai ya tuna lokacin yana zaune shi kaɗai a cikin class ranar aka dawo hutun makaranta shi kaɗai ne zaune ciki yana sanye da farar riga sai wando blue black ya ɗora ƙafarsa ɗaya saman benci tare da yin baya.

A hankali ta shigo cikin class ɗin hannunta riƙe da lunchbox da textbook sai school bag data goya, hijab ɗinta daidai da ƙirjinta ita ce ta fara shigowa da mamaki take kallonsa zuciyarta na bugawa ta je ga zauna inda yake ta zuba masa idanu sai kuma ta ce "Ka yi holiday assignment?"

Ya buɗe manyan idanunsa bai ce komai ba ta sake ƙasa da murya ta ce "Na san bama ka yi ba ka daina haɗe mini fuska, ka naso a yi ta faɗa da kai da teachers" nan ma bai kula ta ba a hankali taci sautin da cikinsa yake yi sai ta jawo lunchbox ɗinta ta buɗe tare da tura masa gabansa ta ce "Your breakfast, ka ci kafin a shigo

na san baka karya ba" sai a lokacin ya buɗe idanu ya juya gabaɗaya yana kallonta sosai ta yi ƙasa da murya kamar zai yi faɗa sai kuma a hankali ya ce

"Kuma ga mayunwaci ko?" Ta yi murmushi ta ce "Da ƙyar na jure ban biyoka gida ba, na yi kewar ka sosai bestie" ya yi mata shiru sai kuma ya haɗe fuska sosai yana janyo abincin yaga dankali ne aka soya da ƙwai ya yi ɗan tsaki ya ajjiye spoon ɗin ya damƙa ya kai bakinsa ta yi saurin kama hannunsa ta ce

"Kai baka iya komai bane? Sai a yi maka dariya cin abinci da hannu" ya ware idanu sai kuma ya murtuke fuska ya ture hannunta a hankali duk da muryarsa a kumbure take ya ce "Ki daina kusanta kan ki dani, ni fa ba ɗan iska bane"

"Laaa Allah Ya baka haƙuri kai duk abin soyayya baka iya ba" a taƙaice ya ce "Ke kika santa" ta ja baya tana ɗaga hannu ta ce "Lalala to shikenan ni dai ƙaddararka ce, na faɗa a gida a yi mini aure, ka san me na ce?" Ya girgiza mata kai kawai yana sake damƙo dankalin yana dannawa cikin bakinsa saboda yunwa ko gani baya yi sosai ta buɗe gorar ruwa ta miƙa masa a hankali ta ce

"Na ce su yi mini aure wallahi bana son karatun nan, na ji aure nake so kuma na faɗa musu kai nake so, amma wai ban isa ba karatu ya zama dole kuma shekaruna sun yi kaɗan amma ai ma girma shekararmu 15 years fa, ko kai baka isa aure bane?" Ya yi mata shiru sai ta fashe da kuka sosai ta ce "I love you so much Bestie, don Allah ka aure ni zan zauna dakai a duk yadda kake ka taimakawa rayuwata" ya zame hannunsa tas ta miƙa masa tissue ya goge ya ja baya yana lumshe idanunsa har yanzu students basu fara shigowa ba, ta ɗan yi gaba kamar za ta shige masa ya cikin tsawa ya ce "Zan kwaɗe ki kuwa"

"But what if i told you i love bestie? You mean the world to me, wallahi aure nake so ba karatu ba" ta faɗa tana shasshekar kuka sai a lokacin ya kalleta fuska babu walwala ya dubi yadda take kukan sosai ya ce

"Ke, babanki ne ya mutu? Ko uwarki ce?" Ta girgiza masa kai ya sake haɗe fuska yana rarraba idanu a cikin ajin kamar mai neman wani abu can ya ce "To kece za ki mutu kenan?" Ta girgiza kai sai kuma ta ce "A'a"

"Kukan fa?"

"Na soyayyarka ne bestie taɓa ƙirjina ka ji wallahi ni ce ƙaddararka ba zaka gane hakan a yanzu ba, da ina da ikon cire abin da nake ji a ƙirjina da na yi hakan ina jin dama na mutu na huta kuma idan ban aure ka ba zuciyata zata iya bugawa"

"To gwara ta buga na huta da na ci, shekaruna 15 za ki lalata ni da batun aure, ke tashi ki ware daga nan ɗauki kwananki kar ki ƙara kawo mini abinci" ta miƙe jiki a sanyaye zata bar wajan ya nuna mata lunchbox ɗin daya cinye komai "Ko daɗi bai yi ba abincin"

Sai a lokacin ta kyalkyale da dariya kamar ba ita ta yi kukan ba, dimples ɗinta na lomawa ta ajjiye masa 500 ta yi waje tana cewa "You're my darling jarumina, i love you Mai dawa da jeji" ta faɗa tana sake yin dariya tare da yin waje.....

Ya yi saurin dafe kansa jikinsa na rawa yana jin dariyar nata na yi masa amasa kuwwa a kunne kamar yanzu ne take yi jikinsa ya ɗauki rawa sosai daidai lokacin aka tura shi cikin motar shiga babu biya, aka nufi kuto. Tun kafin a shigar da shi suka ci karo da wani saƙo daya basu mamaki ainun suka tsaya suna kallon juna sosai cike da tsoro da shakku musamman Sp Gali ya juya ya kalli wanda ake zargin a karo na farko yaga ya yi wani irin murmushin kefen baki wanda ya bada sauti kamat na tsaki yana murza kai gefe.

Cikin sauri Sp Gali ya ce "Amma wane ya yi hakan? Bayan ba a gama bincike an tabbatar da hakan ba, mene matsayin ran yarinyar daya kashe ina matsayin iyayenta" "Sp Ghali ka yi abin da aka ce, kuto ta wanke shi daga zargin da ake yi masa ku sake shi ya tafi gida baku da ikon riƙe shi"

Sp Gali ya girgiza kai cike da damuwa ya ce "Sir kana nufin bashi ya kashe ta ba" cikin tsawa ya ce "Ko shine ya zaka yi? Ka yi abin da ya dace a matsayinka na jami'i Sp Ghali karka matsa" jiki a matuƙar sanyaye Sp Ghali ya kunce shi tas ya ce "Congratulations. Ka sani shari'a saɓanin hankali ce" shi dai bai ce komai ba ya ciri biron gaban rigar Sp Gali ya fara yi masa rubutu a tafin hannunsa dam zuciyar Sp ta buga ganin ya rubuta kalmar SCORPIO kafin ya yi magana tuni ya juya ya fara tafiya cikin sauri duk da rashin kuzarin da yake dashi yana jin inda iskar yanci ke ratsa jikinsa yana shaƙa tare da kaiwa hunhunsa.

Kano/Birget

Dambe suke yi a tsakiyar tsakar gidan mata wajan uku ne kowacce da ɗaurin ƙirji ga tukunyar abincin dake saman murhu. Banda sautin hayaniyarsu babu abin da ake ji hatta Malam dake waje da Almajirai yana jin yadda suke aibata juna da zagin juna hakan ya saka ya miƙe riƙe da bulala yana ajjiye allon hannunsu da yake rubutu ya yi cikin gidan.

"Ke har kin isa ki ce za ki hana Mufeederh abinci a gidan nan? Wace ke?" Cikin ɗagawa Inna Binta ta ce "Ni Binta matar malam ki faɗa mini nawa Mufee ta bayar aka haɗa wajan yin abincin nan? Ke uban yaran nan bai bada kuɗin abinci ba, ba zai yiwuwa yara su haɗa kuɗi kuɗi a siyo dusar awara a yi dambun nan ki ce wai na zubawa Mufee ba yɔar banzar yarinyar da bata da kunya, kina kallo sauran yɔan'uwanta suka fita nemo kuɗi ita ta yi kwanciyarta tunda yɔar mai ce ai yanzu sai ta ci hantar ubanta Malam gashi can yana zaman banza ba fuss"

Mama dake ƙoƙarin ganin ta wafcin dambun a kwano ta ce "Daɗin abin dai ba yaranki kawai suka haɗa kuɗin ba, hadda Saudat ko Zaituna?"

"A'a ba ruwan Zaituna tun jiya nake ganin hazo-hazo a idanuna cikina banda salati ba abin da yake, Saudat da ciwon ciki ta kwana Olser ta buge ta saboda yunwa ki yi ta kan ki kawai wannan rayuwa Allah dai ya fisshe mu, amma yunwa za ta yi ajalin rabin jama'a a wannan zamanin" Mama Zaituna ta faɗa tana turo kwanan Saudat da nufin a zuba mata ta ɗan tsakura a ciki ta yafa a nata cikin. Inna Binta ta shammafe ce ta yi sama da tukunyar kasancewar ta sharifiya ta ce "Wallahi sai Mufee ta ci abincin nan" Mama Zaituna ta ce "To Allah Ya isa daman kun saba cin kayan Allah Ya isa in sha Allah sai ta yi aman shi" Inna Binta ta ji an cauɗa mata bulala a ɗuwawu ta yi saurin dire tukunyar ta ce

"Kan uba wanne mai tsautsayin ne haka?...," shiru ta yi ganin Malam ya ce "Kina sake magana ina ƙara cauɗa muku shasha kawai mara kan gado"

Ya juya wajansu ya ce "Mayu marasa godiyar Ubangiji kawai akan abinci duk maƙota da unguwa sai anjiku" Inna Binta ta ce "Yaushe rabon da muga sisi taka banda masifar tsiya kana bamu za mu yi haka ne?" Kan ta ya yi da bulala ta yi

saurin waftar dambun a hannu ta yi ɗaki tana "Ohho dai na ɗiba na mai da mugun miyau"

Haushin karnuka suka ji wanda rabon da su ji shekaru uku kenan gabaɗaya suka juya wani ihu Mama Zaituna ta yi tare da fatali da dambun da ake ta yin masifa akan shi har zaninta na kuncewa zuwa ƙasa ta yi saurin juyawa zata ɗakko ta zame da ɓawan albasa ta faɗi dif a ƙasa Kasancewar ƙatuwa ce sosai ta fasa ƙara da jan ɗuwawu ta shige ɗakinta hankali tashe. Shi kansa Malam sai da zuciyarsa ta motsa saboda tsoro ya dinga kallon karnukan da idanu yadda suke ɗaga jela tare da zaro harshe waje jibga-jibga dasu sai zagaye wanda ya shigo suke yi. Da ƙyar Malam ya ja numfashi ya ce

"Muɗallabi Ɗanmalam nake gani haka? Ya suka sake ka basu kashe ka ba, ni na ɗauka ma tuni ka mutu wallahi, ikon Allah" sosai kansa ke masa ciwo kamar zai rabe ga wani ciwo da jikinsa yake yana jin fatarsa na rawa, ya yi baƙi sosai amma manyan idanunsa na nan kayan jikinsa duk a yage ya zubawa Malam idanu.

"Kai Muɗallabi ba da kai nake magana ba? Yanzu da suka sake ka me suke nufi ka kashe yɞar mutane a banza kenan? Ba zan goyi bayan gaskiya ba dole na je wajan jami'an tsaron yanzu na bi ba'asi"

Cikin sauri Ammo ta fito daga ɗakinta jin sunan wanda aka kira zuciyarta har rawa take tana fitowa suka haɗa idanu dashi ya kafe jikin bango a hankali yaran gidan suka fara fitowa ya dinga bin guntattakin yaran da kallo wasu duk bai san su ba. Ya nufi Ammo ta yi saurin ɗaga masa hannu ta ce. "Ina jin tsoron kiran ka a matsayin ɗana na ji na yi dana sanin haihuwarka wallahi"

Ya buɗe manyan idanunsa sai kawai ya ja ya lumshe yana ƙara yunƙurin zuwa wajanta kenan ya ji ihu a waje kafin ya motsa Goje ya shigo da sauri yana cewa

"Mai dawa yɞan unguwa ne ɗauke da makamai wai za su ɗauki fansar....." Da sauri MOH ya ɗagawa Goje hannu baya son ma a kira sunanta a kusa da shi zuciyarsa buɗewa take sosai. Goje ya sake cewa "Ba yɞan unguwa kaɗai ba har da gajoji da cinnakun layi" kafin Goje ya ƙarasa sun ji ana cewa

"Ba iya Mai dawa ba har Malam da babarsa yau sai sun mutu da duka mutanen gidan sai mun ɗauki fansar yarinyar daka kashe tunda jami'ai sun sake shi a banza" Mutallab ya kalli karnukansa ya musu inkiya Tiger ne ya fara zuwa ƙofar ɗakin Ammo ya tsaya Rainbow ya je ƙofar gidan ya tsaya, Spider kuma ya tsaya yana kewaye Malam. Goje ya ce "Kai ƙarfe baya cinka tsine baya ratsa jikinka su Malam sune matsalar" bai magana ba kai tsaye ya nufi waje gaban Ammo ya faɗi ganin ba makami a hannun Mutallab. Inna Binta ta fito tana zunduma ihu tana jama'a su kawo musu ɗauki tana leƙa ɣar ƙaramar katangar gidan ganin tarin matasan da suke waje ɗauke da makamai ya saka Inna Binta kurma ihu tana faɗin "Ya gafilan zanbi waya kashifal gammi...." Bata gama ba aka raɗa mata gora aka ta faɗo ɗaga saman katangar ta baje wanwar a ƙasa Mufee ta fasa ihu tana yin wajan Inna Binta ganin haka sauran mutanen gidan suka shige ɗaki banda Ammo da Malam.

Moh na fita suka yi masa ƙawanya kasancewar akwai shafi a hannunsa duk wanda ya daka sai ya baje a wajan, suna da yawa sosai cike da rashin sanin cewa tsarin jikinsa ya karye ya shiga tsakiyar su ɗaya ya ɗauki dutse ya buga masa aka nan take ya fashe, wani ya ɗaga wuƙa ya soka masa a ciki nan take wuƙar ta shige Goje ya zaro idanu ganin sun yi nasara ya saka suka zagaye Moh suna kai masa sarawa, baya faɗa da makami bai san kuma ya ake yi ba, kafin wani lokaci sun kai shi kasa ko'ina na jikinsa jini ke fitarwa daidai lokacin tawagar mafarauta suka ƙarasu wajan tare da zugar karnuka faɗan ya koma tsakanin ɣan unguwa da mafarauta cikin mawuyacin hali Moh ya ja jikinsa a hankali jin wani yana waya da ɣan'sanda ji ya yi dama layya zana na wajansa a yanzu haka? Ya dinga tafiya yana jan jiki har ya bar unguwar ya shiga cikin wani waje mai kama da gonaki kuma jeji-jeji. Tana zaune cikin bukkar hannunta riƙe da ƙwaryar nono ta ji an faɗo cikin bukkar a gigice ta miƙe tsaye...

To ga dai shi nan ban san ya zaku amshe shi ba, amma tabbas zai zama daidai da ra'ayinku musamman iyayenmu mata da maza 😭da suke wasa akan yaransu. MUTALLAB zai zo da sabon salo in sha Allah za a yi kuka sosai kuma za a yi dariya fatana kar ku yi mini zagin da kukai a MIJIN MALAMA 😭ku amshi labarin da hannu bibbiyu ku tayani isar da saƙon zuwa ga manya ta hanyar yin sharing saboda Allah

08164069385

WhatsApp only

[1/7, 9:31 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

Page 2

Nimcyluv

Bright pens..... Second batch

⚠ Warning... For criminal issues

Cikin bukkar ya faɗa jikinsa jina-jina da jini sara ta ko'ina da ƙyar yake iya fidda numfashi, ya zube a gabanta idanuwansa a lumshe har yanzu yana jiyu sautin ihu da kukanta, ya kasa ceton ta, ta sake mutuwa, yaushe zata ci-gaba da rayuwa tana sake macewa akan idanuwansa? Ya cije jajayen laɓɓansa wanda jini ya ɓata sam bai damu da yadda yake shanye jinin yana koma masa ciki ba, a matuƙar fisge ya yi maganar mai sautin gurnani ya ce "Na amince, da gaske na amince Abbasa, zan zama mata maza, ki mayar dani jinsin mace ina tunanin zama macen ya yi daidai da tafiyar ƙaddarata! Zan zama mata maza, bana iya kwanaki ba, bana iya wa'adin sa'a ba, ba kuma iya na tafiyar sakwanni ba, ba kuma iya na gilmawar kwanaki ko shuɗewar watanni da nisan shekaru ba, a'a Abbasa, a'a Abbasa ina son zama mata maza ne na daidai da tafiyar agogo da adadin shekarun da zan yi a duniya"

Yadda furucin ke fitar da kan su, da yadda yake magana idanuwansa na fiddowa waje duka jikinsa rawa yake da ɓari yana wani irin tsuma bakinsa har wani hayaƙi yake yi jijiyoyin kansa tamkar zasu ratsa fata bakwai su keto, ganin halin daya shiga ya saka Abbasa cewa. "Iya zubin tunanin naka kenan? Iya jarumtar kenan? Mayar

da suffarka zuwa abi mafi nakasu a rayuwarka? Ka zama mace shin ko ka mace da....."

"Abbasa!"

Ya kira sunanta a karo na farko a tsawa ce, domin baya son tuna abinda take ƙoƙarin cewa "Shikenan shikenan, zaka zama jinsi biyu, mai halitti biyu" ya girgiza mata kai yana jin amo da sautin muryarta cikin wutar da suka babbaka ta ciki "Kawai ki nakasta ni" "Tabbas zaka nakasa, zaka zama kamar jaririn da aka haifa yau, zaka zama riƙaƙƙe zaka gagara, ubanka zai alfaharin haihuwarka duk da tsinuwarsa na tattare da kai, zaka sake yi rashi, rashi irin wanda baka taɓa yin irinsa ba, zaka samu dukkan wata shahara da ɗaukaka da kake buƙata, amma zaka dauwama a matsayin mata maza"

Ihu ya fasa yana ƙoƙarin miƙewa tsaye da ya yunƙura gefen cikinsa yake sake buɗewa saboda shafcecen saran da aka yi masa, jikinsa bashi da wani gurbin da babu sara.Abbasa ta miƙe ta ɗakko wani farin abu a hannunta tana zuwa kan shi ta danne shi da duka ƙarfin daya zo mata, ta ɗauki garin abun ta fara shaƙa masa a hanci yana shaƙa da ƙyar da sauri ya damƙi hannunta ya kifa fuskarsa da hancinsa gabaɗaya, yana ihu da gurnani jikinsa na rawa ya fara sambatu, Abbasa ta ce "A me ka zo waje na?"

"Taya" ya bata amsa a raunace idanunsa na lumshewa. "Wasu sun biyo ka ne?" Ya girgiza kai can ya ce "Cinnaku, Cinnaku na fi ƙarfin su" ya dinga juyya kansa can ya ce "Akwai Kimini a tattare dani, ya faɗawa ƙashi wani abu, sun nemi asawa da Tsohuwa....!" Ya kasa cewa komai idanuwansa har yanzu na hango yadda gangar jikinta take ci a wuta.

Ita dai Abbasa ta kasa cewa komai ta zuba masa idanu, ta dinga kallon yadda jikinsa je rawa a hankali kuma ya fara saki idanunsa ƙur a saman bukkar cikin fitar hayyaci da yanayi irin na maye yake sambatu tare da kiran sunayen da ita kanta mata sani ba. A hankali ta ce "Mutallab" bai amsa ba sai zuciyarsa kawai dake rawa ta hango hakan ne a yanayin yadda ƙirjinsa ke ɗagawa. Ganin ya zama kamar matacce tsoro ya kama Abbasa ta tuna ashe bai taɓa shaƙar abin da ta bashi ba a yanzu, maganin ƙarfe dana tauri kawai yake sha gashi kuma zaman da ya yi na shekara uku a hannun jami'an tsaro ya sa tsarin ya karye.

Kwarya ta ɗakko ta jiƙon wani magani tare da ruwa mai zafi ta fara danna goge masa jinin jikinsa sai a lokacin ta lura da gabaɗaya farcen yatsun ƙafafuwansa dana hannu babu ga jikinsa duk alamar an jona masa shokin akan tilasta masa amsa laifin da babu wanda yake da masaniyar komai akai, sun yi masa haka ne da nufin ya amsa laifin kashe matarsa da ya yi. Ta sauke numfashi tare da kallon bakinsa a hankali ta kara kunnenta a tausashe yake cewa.

"Ina son ta, ina son ta zuciyata zata fito ita ce wajan ta uku me ya sa.... Ina jinta a ƙasan zuciyata" Tunda suke bai taɓa yi mata zance ɗiya mace ba, haka bai taɓa magana mai tsayin da ya yi a yanzu ba, duk abin da ya saka Mutallab magantuwa ba ƙaramin abu bane ba. Miƙewa ta yi ganin kamar ya samu yin bacci ta fita waje zuciyarta cike da saƙe-saƙe.

Unguwar ta yi shiru saboda zuwan yan'sanda wanda da ƙyar suka raba tsakanin mafarauta da jama'ar da suka zo ɗaukar fansan wacce aka kashe zai ya zama kamar an saka kafiyo ne kasancewar babu wanda bai san labarin kisan rashin mutuncin da aka yi wa yarinyar ba. Tiger, spider, rainbow sune suke ta kai kawo a ƙofar gidan Malam saboda basu tsaro kamar yadda Moh ya saba musu ya raine su tamkar mutane hatta mara gaskiya suna ganewa. Da sauri suke tafiya hankali tashe gabaɗaya basa cikin nutsuwa ɗaya sai ɗaga hannu sama take ba'a jin maganarta sai sautin murya. "Ki yi haƙuri"

Sa'adah ta ce tana shafa hannunta a ƙirji alamar ban haƙuri da yaran kuramen da zata gane ta girgiza kai tare da sunkuyawa tana buga ƙasa ta ɗaga yatsa sama alamar rantsuwa. "Allah Ya kyauta, da kin bari mun ƙarasa gani ai ya kori ji Bafullatana" daidai nan suka ƙarasu ƙofar gidan ba kowa a rumfar Almajiran sai allonansu da rubar tadawa da yan rubobi na bara. Tiger ya ƙare musu kallo yana shinshina su sai kuma ya ja da baya yana ɗaga ƙafa ya basu hanya suka shige cikin gidan.

Da Inna Binta dake yashe a ƙasa suka fara cin karo jini na zuba a gefen goshinta ɗan tofinta a bankaɗe Allah Ya sa ba yara a wajan cikin hanzari Sa'adah ta nufeta tana girgizata ta juya ta yi wa Bafullatana alama data bata ruwa bata fahimci komai sai kawai ta kinkimo ruwa bokici guda ta kwarawa Inna Binta ajjiyar zuwa ta sauke a firgice ta miƙe zaune tana furta "Dambun Mufee, a kawo ɗauki jama'a dambun Mufee yan ta'adda za su kashe ni" ta ƙanƙame hannunta jikinta ya jiƙe jagab amma har yanzu dambun na hannunta ta miƙe ganin Sa'adah da Bafullatana sai kuma ta

ja tsaki "Irin bala'i wallahi Ammo ta haifawa unguwar Birget masifa ɗai-ɗai da ɗai-ɗai zai dinga kashe mu yana zuƙe jininmu ku duba wannan yarinyar ma ya kashe ta kari na uku"

Idanun Sa'adah ya cika da hawaye amma ta ɗauke kai ba tare data tanka Inna Binta ba. Inna Binta ta watsawa Bafullatana harara wacce ke ta ihu tana taɓo Sa'adah ta ja tsaki "Kurman banza da wofi gayya masifar, daga haihuwar kurma sai ta ɗan jagaliya" tana kaiwa nan ta shige daƙinta ta samu Mufee tana bacci ta yi maza ta tashe ta, tura mata ɗan guntun dambun ta yi a baki bayan ta cinye ta ce "to sha ruwa kiji abin da kika samu sai kuma gobe, ki yi addu'a ki goge Allah ki gode Muhammadur Rasulullah. Banda ina buɗe ido a gidan nan kema mutuwa za ki yi saboda yunwa kamar taki yar'uwar" sai kuma saka dariya sosai "Inna mene?"

"Tukunyar dambu ta kife dan ubanki da tuni ba ki lasa ba kema" Mufee dai ta buɗe manyan idanunta irin na Mutallab tana kallon Inna Binta.

Ammo ta dinga bin Sa'adah da idanu ganin yadda take kuka kamar ranta zai fita, Bafullatana kuma ta haɗe rai sai girgiza kai take "Ammo don Allah ina Mutallab yake? Da gaske ya dawo an sake shi? Sun wanke shi daga zargin da ake masa, yana ina?" Ammo ta ɗauke idanunta zuwa can gefe tana kallon wani waje daban a ɗakin nata can ta ce "Ki daina kira mini sunansa sallamamman yaron nan a kunnena Sa'adah, ki yi hankali watarana zai iya kashe ki"

"Ba zai taɓa kashe ni ba, duk lalacewar shi jinina ne ɗan'uwana ne a wannan halin da yake ciki na ɗauka za ki yi murna Ammo? Za ki ja yaronki jikinki ki nuna masa kulawa gudun kar ya sake lalacewa, kar ki ce za ki yi abin da kikai a baya duk lalacewar Mutallab kece wacce kika haife shi, tun yana ƙaramin kin san zuciyarsa yadda yake da zafin nama taurin kai. Kin san yadda yake da ƙulafucin uwa kodayaushe yana manne dake, me ya sa za ki yi haka?" Miƙewa Ammo ta yi ta nunawa Sa'adah hanya ta ce "Tashi ki tafi gidan mijinki, banga dalilin zuwanku ba ni bani da wani ɗa Mutallab kuma na sani kuskurena ya saka na haifeshi. Wallahi kika sake yi mini maganar tsinannen yaron nan sai na daina amsa gaisuwar ki har abada" tana kaiwa nan ta fice ta bar musu ɗakin, fuuu Bafullatana ta fice daga ɗakin zuciyarta na yi mata zafi Sa'adah ta yi shiru ita dai tana mugun son ƙannin nata ai da ba haka yake ba, ya kamata su amshi hakan matsayin ƙaddara!

Washegari Malam na zaune a rumfa yana sauraren karatun wani sabon almajirin shi. Ɗanyaro ne zauna gefe kusa da Malam yana lissafa sabbin kuɗin hannunsa yana dubu-dubu sai sheƙi yake ya duba yaga dubu biyar cif ya mayar aljihu ya zaro baƙar leda mai cike da gurasa da nama ya ya fara ci yana ajjiye lemo fanta a gefe. Ajjiye bulalar Malam ya yi ya ce "Ɗanyaro ina ka samu kuɗi da nama haka?"

"Bani aka yi Malam" kafin Malam ya sake magana Ɗanyaro ya miƙawa Malam baƙar leda guda mai ɗauke da gurasa a ciki da nama ya haɗa masa da dubu biyu ya ce "A yiwa su Mufee girki Malam"

Jiki na rawa ya amsa yana buɗe bakinsa "Da kyau yaron arziƙi, ina ka samu kuɗi fal haka sana'ar me ka fara?" Ɗanyaro ya girgiza kai kawai can kuma ya kalli Malam ya ce "Bana yin sana'a, kyauta ake bani kullum, bani kaɗai ba har Muhajeed da Iro" Malam ya yi sak tunani fal ransa ya sake kallon Ɗanyaro shekarunsa goma rak a duniya a hankali ya miƙe ya yi cikin gida.

****

A kusan tare manyan motoci biyun suka tunkaro babban gate ɗin ganin ya rigata kai hancin motarsa ya saka ta rage ta fiya, hannunta ɗaya a saman sitiyarin motar ɗayan kuma ta ɗan riƙe fuskarta a hankali ta lumshe idanunta gajiya ce a jikinta sosai da ƙyar take buɗe tuƙa motar don dai bata san wahalar driver ne.

"Fiyya" Ya kira sunanta a hankali cikin muryarsa mai cike da nutsuwa ta buɗe idanunta da sukai mata nauyi ta kalli wayarta ta manta video call suke yi ma suna haɗa idanu da shi ta ɗauke kan ta gefe tana ya motsa fuska "Fiyya na miki wani laifi ne? Kin sauya"

"I am sorry ina driving we'll make a call later" ya zuba mata idanu cike da so da ƙauna yana jin ina ma a janyo ranar aurensu da Fiyya a ce gobe ne? Ya sauke numfashi zuciyarsa na buɗe a hankali ya ce “I adore you Fiyya" ta buɗe idanu ta kalli cikin idanunsa sai kuma ta murguɗa masa baki ya buɗe idanu sosai sai ya girgiza kai yana dariya ya matso da fuskarsa dab da camerar "Na ji kamar ina shaƙar numfashinki...."

Ya yi shiru jin ana knocking ƙofar motar da take ciki, itama ta juya ganin wanda yake tsaye ya saka ta ɗan yi murmushi baya ganinta saboda duhun gilas ɗin motar amma murmushi mai kyau ne a fuskarsa. Ta cikin wayar ya ce "Waye?" Tana ɗaukar jakarta a taƙaice ta ce "Yaya Junaid ne"

"Ok" ya yi sai kuma ya ce "Fiyya" ta ɗago idanunta da sukai laushi ta kalle shi dasu can ƙasan maƙoshi ya ce “I love you Fiyya" da sauri ta kashe call ɗin tana haɗe fuska ta ɗauki wayar ta fita daga motar.

"Yaya J" yana murmushi ya ce "Manager" ta ɗan yi murmushi kawai ya amshi jakar hannunta "Me kika zo da shi"

"Ba kyau bincike J" ya jinjina kai suka nufi shiga gate J ya kalli driver ya ce "Ka shigo mata da motar, she left the key inside the car" Fiyya ta marairai ce fuska tana mannewa jikin J ta ce "Yaya J na gaji sosai"

"Sannu Manager, ko goyaki zan yi?" Ta buɗe idanu sannu yake ta yi mata har suka shiga babban parlon gidan yɑn samari wajan biyar a zaune a parlon duk dawowar su daga aiki kenan. Wajan tare suka dinga cewa "Sannu Manager" ta shige tsakiyar su tana kwanciya a cinyar Marafa ta ce "Thank you brothers, ku yi mini tausa akwai labari"

"Gulma dai ba labari ba, daka dawowa ko wanka ba ki yi ba kin zaunawa mutane a jiki ƙazamar banza" Shiru ta yi masa don basu fiye shiri ba sosai ta juya idanunta rufe, tana jin yadda Marafa ke ta danna mata farar ƙafarta. Yaya J kallonta kawai yake with different thinking running on his mind. Gabaɗaya suka juya jin tafiya cikin sauri ana sakkowa daga saman bene shiru duk sukai suna binsa da idanu domin basu san ya dawo gidan ba, hannunsa ɗaya zube cikin aljihu farar riga ce a jikinsa ta kakin sojoji a gaban rigar wajan gefe an rubuta A.A MARAFA.

"Kee!" Ya faɗa a tsawace da sauri Fiyya ta buɗe idanunta lokaci ɗaya kanta ta sara sosai tsawar ta ratsa kanta, ta miƙe zaune fuskarsa babu walwala kamar yadda itama ta yi kicin kicin da rai "Tashi a nan, stupid kawai" ta miƙe tsaye tana murguɗa baki ko inda yake bata kalla ba ta nufi saman bene kai tsaye daƙinta ta nufa idanunta cike da bacci ta faɗa saman gado cikin ƙaramin lokaci bacci ya ɗauke ta. Firgigit ta farka jin sautin labaran ɗ da ake faɗa a gidan rediyo wacce take cikin

ɗakin nata, ta miƙe tsaye ta ɗauki rediyon ta ƙanƙame a jikinta tare da lumshe idanunta wasu hawaye masu zafi suna shiga bin idanunta. Ta cikin idanunta take hango fuskarsa a lokacin da rigima ta haɗa su da ita sai take ganin kamar yanzu ne komai yake faruwa.

Students ne an cika sosai saboda class partyn da ake yi na kammala exam maza da mata babu teacher ko ɗaya tunda ta shigo hall ɗin makarantar tasu take duban inda zata ganshi. Cikin sa'a ta ganshi yana zaune saman window sanye da gajeren wando fari tas sai armless ɗin riga wacce duk aka yanke hannunta gashin kansa rabi a aske ya zubawa wani tafkeken gidan masu kuɗi idanu ta waje baya ko ƙiftawa kamar an ce ya juya ya ganta tsaye ta zuba masa idanu yaja tsaki kafin ta yi magana an shigo an ce "Mutallab, principal yana nemanka an kai ƙarar ka wai kana son Fiyya"

Ya ware idanu abin da bai taɓa zuwa tunaninsa ba kenan sai kuma ya cije baki "Shi principal ɗin ubana ne Malam Abdullahi kenan?" Ya juya ya kalleta sosai ya ce "Sai godiya, ni? Kuma ke hauka kenan"

"Kai ne mahaukaci" furucin ya fita daga bakin Fiyya "Kuma na yi maka nisa, kasan yadda nake da masoya a makarantar nan amma ni ubana ba soyayya ya kawo ni ba, karatu zan yi ina da buri mai faɗi da zan cimma" Ya miƙe tsaye yana kallonta daga sama har ƙasa a ransa yana ƙissima abu "Shi uban naki can ta matse masa, karatun banza kawai ka zama mai iko shine"

"Ba dai ubana sai dai....." Ya buɗe idanu sai kuma ya fasa abin da ya yi niyya ganin hawaye a idanunta abin da bai taɓa gani ba. Da sauri ta fice daga hall ɗin ta zaga baya ta durƙushe a wajan tana fashewa da wani irin kuka kamar zata haɗiye zuciya "Daddy na shiga uku ina son Mutallab"

Ƙanƙame redion ta yi tana sake fashewa da kuka jikinta har jijiiga yake ta ce "Na shiga uku Daddy, ba zan iya ba I can't do it ina son shi.

Kamar daga sama haka ya faɗo cikin gidan, jikinsa duk liƙe da bandeji jini na ɗiga kaɗan-kaɗan kwana biyu yana jinyar raunin bai san waye ya yi masa ɗinki ba. Idanunsa jajur har lokacin saboda bai gama dawowa daidai ba sai muzurai yake yi ya ja ya tsaya yana kallon murhun da aka sauke abinci akai ya juya ya kalli ɗanwaken dawar da Inna Binta ta yi ta shiga daƙi ɗakko magi ta barbaɗa ko arziƙin

yaji bai samu ba, yaja kwanon da hurɗu-hurɗu yake tura ɗanwaken kafin wani lokaci ya kammala cinyewa tas ya zube a wajan ya kwanta ya rufe idanu, wata nutsuwa yake jin daya kwanta a tsakar gidan mahaifin nasa. Ya yi kamar bacci yake yana jin Inna Binta ta lailayo ashar ta ƙunduma ta ce "Wanne ɗan abu takazar ne ya cinye mini abinci Mufee wanne mayunwacin ne mara godiyar Ubangiji" tsit ta yi ganin Moh kwance hannunsa duk manja taja baki ta tsuke ta ɗauke kwanan tana suɗewa a zuciyarta tana jan Allah Ya isa. Har ya shiga ɗakin Ammo ta bankaɗa labule ta ce "Wallahi abincin da ɗan ta'addar ɗanki ya cinye mini Allah Ya isa, kawai kin haifa mana jaraba ko ɗanɗana ɗanwaken ban yi bafa ya cinye" ta dinga zagin Ammo ta uwa ta uba ta shige ɗaki tana sake suɗe kwanon da ƙyar ta samu rancen ɗari biyu ta yi cefane da ledoji ta dafa.

Tana shiga ɗaki ba jimawa ta ji an bankaɗo labule sai ta zuciyarta ta buga ganin shi tsaye hannunsa riƙe da gora ya suke askara a gefen ƙugunsa ga gori a hannunsa, ya juya ya kalli Mufee da hannu ya yi mata alama data fita cikin sauri ta fice tana fita muryarsa a daƙushe kamar dole ya ce "Tiger spider a yi mata aiki" manyan karnukan suka faɗa cikin ɗakin Inna Binta ta fara ihu tana maƙale jikin sif "Nafsi nafsi jama'a na shiga uku ya Allahu Ya Rahmanu, don Allah ka yi haƙuri Muɗallabi zan bawa Ammo haƙuri ka rufa mini asiri kar Mufee ta zama marainiyya" Haushi kawai karnukan suke Tiger na kai mata cafka Inna Binta ta fashe da kuka fitsari na bin ƙafarta ta ce "Hal'àtaka hadisul gashiya ni Binta na shiga uku"

Moh ya ce "Sai godiya" gabaɗaya karnukan suka tsaya cak Inna Binta na haki ta jiƙe gabaɗaya da fitsari har lokacin tana maƙale jikin sif kamar ba zai magana ba ya ce "Bani ƙudin nan" jiki na rawa ta miƙa masa ɗari biyar ɗin hannunta ya amshe ya yi waje ta sake sif ɗin ta fashe da kuka tana faɗin "Tsinannen yaro manta ganin yaron dake son uwarsa kamar mutuwa ba irin shi" Moh na fita ya leƙa ɗakin Ammo ta ɗaga kai tana ganinsa ta ɗauke fuska ya yi ta kallonta ya jima tsage kafin ya sauke labulan ya juya. Yana fita wani babur na tsayawa a gabansa aka cillo masa takarda da gudu aka ja babur ɗin tare da barin wajan. Ya ɗauki takardar ya buɗe rubutu ne bai fi layi biyu ba a hankali ya fara karantawa.

Mai dawa baka gajiya? Sau dubu zaka kula mace sau dubu zamu kashe ta. Karo na uku kenan ga misali akan matarka nan da jan biro akai rubutun ya juya da sauri amma tuni babur ɗin ya ɓace ɓat waye wannan? Su duka shi ne silar mutuwar su kenan? Waya ya amsa hannun wani Almajiri ya kira wata number ana ɗaga aka ce "Sai godiya" Ya numfasha

"Duk inda yɑn daba suke ka haɗa mini su" ta cikin wayar aka ce "Mene haɗinka da daba ko dai ka fara shaye-shaye a state cid ɗin?" Moh ya cije baki ya ce "Zan fitini mutane, na ji daɗin zama can"

"To me za su yi maka?" Wannan yaran da suka sare ni iyayensu za su ɗauki sabbin ciki yau, yɑn cikin gari ne a yi mini kan me uwa jawabi" yana faɗin hakan ya kashe kiran ya goge number tas ya lumshe idanunsa ya buɗe sai kuma ya cije leɓe zuciyarsa zafi take sosai ji yake dama ya yi kuka, amma ba a haife shi don ya zubar da hawaye ba ya ɗaga idanu sama ya ce "Da gaske ni na kashe ta amma ba zaku taɓa sani ba" daidai lokacin mafarauta suka kawo kai suna busa ƙaho da buga gangaga suka zagaye Moh ana "Sai Mai dawa ina uban wasu ga namu wuya a ina wuya a daji, kai ne mai Tiger kai ne mai gadon tawada" Jikinsa ya hau ɓari da karkarwa tsumin shi ya motsa idanunsa na ƙaƙƙafewa ya yi kururuwa tare da ɗaga gora sama ya ja ya ƙame sai jikinsa dake rawa ya fara "La'ilahaillahu, sai ni ɗan babana Malam Abdullahi ɗan malam ɗan gatan Ammo ƙanin Sa'adah ƙanin Bafullatana waye ce bani ba Muɗallabi sarki Mai dawa da jeji" gabaɗaya suka zagaye shi suna sake zuga shi daidai lokacin kuma suka ganta kamar daga sama.....

In sha Allah za ku ji abin da baku taɓa ji ba 😘

08164069385

WhatsApp only

[1/7, 9:32 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

Nimcyluv

Bright pens....Second batch

Da sauri ya nufe ta kamar zai kai mata cafka, ta yi saurin ja baya idanunta cikin nasa. Yana tangaɗi ya ja ya tsaya a gabanta tare da ƙura mata idanunsa da suke lumshewa, har yanzu jikinsa ɓari yake domin basu daina buga ganga da ƙahon da suke busawa ba kamar masu yin gangi.

Hannunsa ya ɗaga musu cikin sauri suka daina abin da suke, cikin izza da gadara ya basu umarnin tafiya har lokacin idanunsa yana kanta ganin yadda take kallon shi kamar ya ta saba ganin halittarsa. "Ban yi zaton a haka zan ganka ba, autan Ammo me ya sa?" Ya ɗauke kansa yana haɗe fuska sosai ba wargi banda cewa ita ce ba zai taɓa tsayawa ba. Cikin raunin murya kamar za ta yi kuka ta ce "Me za ka yi da wuƙa haka?" Ya buɗe ido sosai sai bai magana ba, a hankali ma ya bi gefen ta zai huce ta yi saurin riƙe masa hannunsa tana faɗin "Ni ɗin ma? Yau za a ji kan mu da kai, kar ka faɗa mini sauyin da ka yi ya zagayo har kai na?"

Ya ɗago kai ya kalle ta ya kalli hannun data riƙe shi da shi, hannunta fari tas saɓanin nasa da yake mai kauri kuma baƙi irin na majiya ƙarfin nan wanda suke tashe akan shekarunsu. "Don Allah ka tsaya mu yi magana, ni ko gidan ba zan shiga ba wajanka na zo" ya cije bakinsa ya mai da kai gefe cikin muryar mai kauri ya ce "Kin ci darajar Ɗan Amina, mene sakin?" Ta girgiza kai kawai tana duban gefe dakalin dake wajan ta gani ta je ta zauna akai, ta yi masa alama ya zauna amma ko motsi bai yi ba, ta san cewa yana jinta amma hankalinsa na kan hanya sai waige-waige "Mutallab ka kalle ni bafa wani zai kawo maka farmaki ba" ta nisa idanunta cike da ƙwalla ta ce "Don Allah kai ne ka kashe ta? Ba zargin ka nake ba Autan Ammo ni me iya rufa maka asiri ce idan ya zama kana da laifi ka faɗa mini gaskiya na maka alƙawarin ko Ammo ba zan faɗawa ba, ka kashe matarka ko ba kai bane?"

Ya juya da wani irin sauri yana kallon fuskarta da take kallon shi cike da damuwa, idanunsa ya yi jajur naman jikinsa na motsawa ya kasa furta komai. Miƙewa Anty Hameeda ta yi tana girgiza kai kuka na cin ƙarfinta "Ko minti ashirin ba mu yi da kai maka matarka ba, sai labarin mutuwar ta muka ji da kisan wulaƙancin da aka yi mata. Mutallab kai ne fa muka gani tsaye akan gawarta, kai ne fa riƙe da wuƙar da aka kashe ta da ita jikinka duk jinin matarka innalillahi wa'inna ilaihirraji'un na kasa yadda ka kashe ta, daman soyayyar da ka nuna mata na iya fatar baki ne?" Wani irin ihu Anty Hameeda ta yi tana kaiwa jikin bango ganin ya ɗaga hannunsa ya yo kanta sai kuma ya tsaya cak, a hankali da baya da baya ya dinga ja yana ƙare mata kallo sai kuma ya taune bakinsa idanunsa kamar zasu zazzago don girma kallo ɗaya

idan ya yi dasu sai an razana da ƙyar ya iya ware laɓɓansa biyu da sukai masa nauyi sosai ƙasan zuciyarsa na ta fasa banda cewa Anty Hameeda ce tabbas da sai ya karya ta gida huɗu.

"Ni na kashe ta, ta cancanci haka ne" ya juya da sauri Tiger da spider da rainbow suka bi bayansa kamar zai tashi sama haka ya sha kwana. Zubewa Anty Hameeda ta yi a wajan tana rushewa da kukan baƙin ciki, su waye suke da saka hannu wajan lalacewar Mutallab? Ba komai ta sani ba ita ba ma'abociyar zaman garin bace ita da mijinta ta dinga kuka da ƙyar ta rarrashi kan ta, ta miƙe tsaye kamar zata shiga gidan nasu sai kuma ta fasa tana ƙoƙarin barin wajan ta ji Malam ya ce "Hameedatu me kike anan ina mijin da yaran naki?" Kanta a ƙasa ta ce "Suna gida, ina yini Malam?" Ya jujjuya yana kallon hannunta ganin babu komai ya ce "Ba za ki shiga bane?" Ta girgiza masa "Zan juya wajan Mutallab na zo" ya jinjina kai domin ba wannan ne a gabansa ba.

"Ba wata mutalla da zan iya samu a wajanki na siyo wainar rogo?" Ta buɗe jakarta ta zaro kuɗi tana irgawa ya yi maza ya fisge ya ce "Mene na lissafi? Maza jeki wajan yaranki kuma na ja kunnenki babu ke babu yaron nan idan ba su kike watarana ya ja miki masifar da za ki ƙare rayuwarki a gidan ɗan kande ba" bata ce komai ba sai data juya zata tafi ta ce "Duk lalacewar Mutallab kai ne ka haife shi, jininka na wanzuwa a nasa" tana kaiwa nan ta yi gaba abinta saboda ɓacin rai da damuwa ko gabanta bata gani sosai.

Moh na kwance a saman wani dutse idanunsa a rufe tun bayan barin shi wajan Anty Hameeda ya zo wajan ya kwanta, zuciyarsa a cunkushe take babu gurbin samun sauƙi a cikinta duk yadda ya ke son tuna waye shi me ya sa ya zama haka sai ƙwaƙwalwarsa ta yi hooking, ya ɗauki zafi sosai ta yi ta processing ya ji Ammo ɗinsa kawai yake son kasancewa da ita yanzu. Ya motsa kaɗan zazzaɓi ne sosai a jikinsa saboda saran da aka yi masa bai gama warkewa ba, baya kuma shan magani wacce zata iya kula da shi baya jin zai iya zuwa wajanta. Ya ƙanƙame jikinsa sosai abubuwa da yawa baya son tunawa sai ya cimma muradin zuciyarsa sai ya ɗauki fansa na abin da aka aika, sai ya bayyana abubuwa da dama tunda har suka bari ya shiga cikin gidan yari ya kuma yi shekaru uku a Cid ya rayuwa cikin masu aikata manyan laifuka. A sama ya ji an kira sunansa

"Mai dawa, sarki mai jeji" bai buɗe idanunsa ba, bai kuma ɗauki murya ba haka baya buƙatar sanin waye don hakan babu abin da zai ƙare shi da shi. Ya nemi waje ya zauna yana furta "Ka saɓe Mai dawa ka basar, fansa kake buƙata ba raunin

zuciya ba, ka ajjiye tunanin baya ka fuskanci burinka ka zama abin da kake muradi kafin aga bayanka" har lokacin bai buƌe idanu ba, ko inuwarsa bata motsa ba. Mangal ya ƌaga kai yana busawa samaniya hayaƙin sigari "Idan kana son yin bacci cikin nutsuwa ka manta komai ya kamata ka sha wannan" ya zaro abu a aljihu yana kalle-kalle sai a lokacin Mai dawa ya buƌe rinannun idanunsa ya juya ya kalli mai maganar irin kallon waye kai? Mangal ya ce "Ka dake musulmi akul musulmu, zuwa na yi na taimaka maka"

"Riƙe wannan tiramol ce, ko doki ya sha sai ya gane barno gabas take kana afawa za ka ji zam-zam komai ya zama labari" Mai dawa zubawa ƙwayar idanu shi bai taɓa shan ta ba, bai taɓa shaye-shaye ba ya juya ya kalli Mangal "Da gaske zan yi bacci?" "Darr ne ai aikin wannan kamar yankan wuƙa ne, mai ƙirin ce da ƙyar aka bani ita ina karɓa na doƙu nan" jikin Mai dawa na rawa ya amshi ƙwayar guda ƌaya ya cilla cikin bakinsa, yana runtse idanu ya yi shiru. Mangal ya zubawa Moh idanu a ransa yana jin wani daƌi da kuma farinciki bai taɓa yin aikin da za a bashi kuƌi masu yawan da aka ce ba irin na yau, gashi ya yi nasara Moh ya sha ƙwayar. Jikin Moh ya ƌauki rawar zafin zazzaɓi duk da irin dariyar da yake da ita, gashi duk inda ya motsa ciwon shi jini yake babu wani wanda zai iya duba lamarinsa sannu a hankali ya fara dafe kan shi da wani irin gurnani yaga sama na jujjuya masa ya ƌaga hannu da niyyar ya tare sama ya faƌo daga saman dutsen sai saka hannu yake yana tare sama a hankali kuma jikinsa ya fara saki yana jin wani shuu a tsakiyar kansa yana game jikinsa gabaƌaya zuciyarsa da tunaninsa suka dinga kissima masa kawai ya kashe kansa ko ya cinnawa gidansu huta gabaƌaya kowa ya mutu har shi.

Ganin laɓɓansa na motsawa alamar yana magana ba'a ji sosai ya saka Mangal matsawa tare da kafa kunnensa a bakin Mai dawa cikin mawuyacin hali yake furta "Safiyyerh... Safiyyerh...Safiyyerh" Mangal ya maimaita sunan a fili “Safiyya?” wace haka? Ko ita ce wacce ta mutun wacce aka kashe? Ya miƙe tsaye ya ƌauki wayarsa wata number daya haddace ya saka ya kira ana ƌagawa Mangal ya ce

"Sakin nan ya kammalu, yanzu zan zo a taya na amshi fararen" shiru ya yi yana sauraren mai maganar kafin ya ce "Jira jira jira nifa cikin uwata aka haifan ba ƌan zina ba, na maka al'ƙawarin dole zan bawa Mai dawa ƙwayar kuma da sannu zai zama namu. Sai dai na ji yana kiran sunan wata ƌawa wai Safinu ko Safiya?" Ya ƙara yin shiru ya numfasa ya kalli Moh dake kwance a wajan ya ce "A'a Oga ni bana sabga da masu ƌan kwalin nan. Da ƙirin ka oga kanka baya kullewa a fice kake sai na doƙu yanzu" Kashe wayar Mangal ya yi kuma ya goge kiran cikin sauri kuma ya bar wajan.

Baya tantance halin da yake ciki, sai dai yanayin na yi masa daɗi sosai shi ba'a sama ba shi ba'a ƙasa yana fatan ya dauwama har ƙarshen rayuwarsa. Duk da a cikin giyar maye yake bai hana shi gano fararen kyawawan idanunta masu matuƙar ɗaukan hankali ba, a lokacin da take masa wannan duban ji yake kamar ba zai taɓa aikata abu makamancin haka ba amma ƙuruciya da wawta ya saka komai ya wakana a lokacin da duk su biyun basu ankara ba. Gani ranar yake kamar yanzu a cikin idanunsa ya juya da ƙyar yana buɗe idanu zuwa gefe guda sai fara hango kansu su biyun a shekarun da suka huce suna tsaye tana jifansa da wani irin kallo.

Suna tsaye za su shiga practical a lokacin, ya jingina da jikin bango ƙafarsa ɗaya a jikin bangon ɗaya a ƙasa ya harɗe hannayensa duka biyun a ƙirji students ɗin yake kallo yana mamakin abin da ya saka ƴan mata ke burge wasu mazan, as a man kuma good man kawai ka nemi kuɗi ka yi arziƙi ka shahara a duniya shi ya fi, ka zama mai iƙo da faɗa a ji, ka zama wanda zai iya samun abincin da zai ci da safe kuma ya ci da rana ya ci kuma da dare ya bawa ƴan'uwasa da duk mai jin yunwa ya zamana kuma ka kasance mutumin da ake shakka duniya ta san da zamansa bawai kana namiji ka ƙare a wajan wata yarinya ba. Yana cikin wannan tunanin ya ji an ja mugun tsaki ya buɗe idanu ya ganta sosai ya buɗe idanunsa da suke a rufe kodayaushe cike da gashin idanu masu tsayi.

"Kai ai babu macen da zata soka a school ɗin nan, sai dai kaga ana soyayya" bai taɓa tsayawa ya tanka ta ba sai lokacin har zai mata shiru sai ya ce "Ok" ta haɗe fuska "Saboda macen abinci ce ko iskar shaƙa daya zama dole Mutallab ya amfana dasu?" Ta yi masa sheƙeƙe tana nuna masa ɗaliban makarantar da kana ganinsu zaka san iyayensu nada arziƙi sosai kowanne a students ƙuruciya da tashen balaga na ɗawainiyya da su. Ta ce "Mata ai sune jin daɗin maza, kai fa mace ko kiss bata taɓa yi maka ba a school ɗin nan" Mutallab ya yi ta kallonta daga sama har ƙasa "Matar Moh zata zama mai irin halin MOH" har ya juya sai yaga bata ci bulus ba ya tako har inda take ya zuba idanunsa cikin nata kamar yadda take kallon tsakiyar nasa idanun yana sake matso da fuskarta "About the kiss, ƙilan Moh ya ji ƙan ki ya yi miki don naga shi kike buƙata"

Tsoro ya kamata amma ta dake ta fara ja baya ya yi saurin saka ƙata ya falleta kamar zata kita ya saka hannu ya cafko gaban wandon uniform ɗinta ya dawo da ita dab dashi yana sauke mata numfashi a hankali kuma ya ɗora fuskarsa..... "Mai dawa" kiran da aka yi masa ya saka bidiyon abin da ya faru a baya saurin gogewa a idanunsa har lokacin idanunsa na kafe waje guda sosai yake son sake tuna abin da ya faru a lokacin ya gagara. Goje ya ce "Nan ka auno kenan, na samo sha ɗayan gayen nan. Ya naga kamar a buge kake?" Goje ya faɗa yana tattaɓa jikin Moh ya ji zafi sosai idanunsa kuma ya kaɗa ya yi ja ya san babu abin da zai fahimta koda ya

yi masa bayani "Mene haɗin mafarauci da shaye-shaye?" Shi dai ya yi shiru kawai zumbur kuma ya miƙe tsaye kamar wanda ya tuna wani abu ya juya idanu wuƙar da ya gani a jikin Goge ya fusga duk yadda Goje ya yi da shi amma ya kasa amsar wuƙar cikin sauri kuma ya mara masa domin ganin me zai aikata?

Tafiya suka dinga yi har suka kawo titi ya tsayar da mai napep ya faɗa shima Goje ya faɗa ciki. Shi kansa bai san ina za a kaisa ba. Tafiya suka sosai har suka ƙarasu daidai wajan wani ƙaton kamfani wanda kaf Kano babu wanda bai san zaman wannan kamfanin ba. Iya haɗuwa ya haɗu ginin kamfanin ma abin sha'awa ne ga masu tsaro ta ko'ina. Ya tsayar da mai napep ɗin ya sauka "Kuɗi na?" Ya buɗe ido sai ya share "Malam haƙƙina na daƙƙoka daka waje mai nisa ina da wajan zuwa" Goje ya ce "An cinye"

"Kut, ni da haƙƙina daman tunda na daƙƙo ku na ji kuna warin wiwi na san cewa ɓarayi ne ku, cikakken ɗan zamani ne nima ku bani kuɗina yanzu ku na daki kuɗin" Goje ya ce "dan babarka zo ka daka idan ka haifu" mai napep ɗin ya share shi, ganin Mai dawa ya yi shiru yana kallo kamfanin ya nufi inda yake ya damƙi wuyansa ya ce "Kai ka tsare ni ai...," kafin ya ƙarasa maganar Mai dawa ya damƙi hannunsa ya matse ya bada sauti ƙass har lokacin ya kafe kamfanin da idanu. Mai napep ɗin na ihu yana neman ɗauki Goje ya zaro wuƙa yana bubbuɗe jajayen idanu hakan ya saka ba wanda ya zo wajan kowa saurin barin hanyar yake gudun kar tsautsayi ya faɗa masa. Mai dawa ya saki karyayyen hannun mai napep ɗin ya ƙara damƙar ɗayan zuciyarsa na tafasa har yanzu ba komai yake ganewa ba, ya sake karya hannun daman ba tare daya sake shi ba ya ce

"Goje"

"Mai dawa sarki mai jeji, sai godiya"

"Kamfanin meye wannan? Na waye kuma?" Goje ya kalli tafkeken kamfanin da manyan motoci ke ya shiga da fita kafin ya ce "Sai godiya, ciki ne a kan sabgar nan bani da ilimi akan wannan massarafar"

Mai dawa ya saki mai napep ɗin da ya karya masa duka hannunsa biyu yana ja da baya a hankali ya ce "Ina son shi, ina son ya zama mallakina" cikin sauri Goje ya ce "Me kake so?"

"Kamfanin"

Tana zaune akan kujerar dake haɗɗan office ɗin, cikin nutsuwa dake danna system ɗin gabanta files da yawa cike saman table ɗin hankalinta na kan aiki sosai kana kallon fuskarta zaka san serious ce ita akan aikinta bata da wasa ko kaɗan. Brown suit ce a jikinta mai riga da wando ta yi rolling kanta da mayafi zagayayyiyar fuskar ta fito sosai ta saka wani shade a idanunta baƙi. Wayarta ta fara ƙara alamar kiran ta san tunda ya fara ba zai daina ba, cikin nutsuwa ta murja kujerar ta yi ba, suu kuma ta kujerar zuwa inda wayar take ta ɗaga kiran tana sawa a hands free

"My manager" ta ɗan buɗe idanu ta cikin glasses ɗin ta yi shiru tana ta danna system a hankali ya ce "Maamah" ya kira ta kamar yadda suka ce mata ta sake yin shiru domin bama ta jinsa sosai "Fiyya ina miki magana?"

"Yaya J yaushe zaka fara ɗaukan aikinka very serious, ina kan aiki fa" ya yi murmushi mai kyau tana jin sautin shi a kunnenta "Sanda kika so na zama Mamaa"

"Uhm kiran fa?"

"Kin ci abinci, nina manta Captain ya saka na kira na tambaye ki" cak Fiyya ta tsaya da abin da take ko dai bata ji daidai ba "what?" Ya ce "Kin ji ai" a taƙaice ta ce "Na ci" ya ce "Good, ƙarfe nawa za ki tashi?"

"Ina da meeting Yaya J ka biyo ka ɗauke ni i can't drive cikina ciwo" cikin sauri ya ce "Subuhanallahi! Bari na zo na duba ki ko kawai mu tafi gida" kashe wayar ta yi domin ba wani ciwon ciki da take so take ta saka kanta busy sosai ko zata manta da wasu abubuwan. Knocking aka fara tana ji ta yi shiru can ta ce "In" ya buɗe ya shigo idanunsa ya sauka a jikin sunanta dake manne a table ɗin “SAFIYYERH A. MARAFA” ya ɗauke idanunsa yana rusunawa ya ce "Good day Maa"

Da hannu ta yi masa nuni ya zauna bayan ya zauna, still idanunta akan system tana danna keyboard ta miƙo masa file ya ɗauka ya ce "Wannan fa?" A nutse ta ce "I have to ask, daga ina file ɗin nan? Wanne kaya aka fitar aka samu ruɓanyar kuɗi kashi wajan goma cikin awa guda Accounter?" Ya ɗan shafa kai ya ce "Maa ni ma haka na gani, kawai aka ce na kawo ki saka hannu"

"To ba zan ba" ta ce a taƙaice. "Maa ya zama dole fa"

A hankali ta ɗago idanunta sai kuma ta cire glasses ɗin idanunta manyan fararen idanunta tas a kan shi ya yi saurin ɗauke nasa idanun saboda kwarjin da ta yi masa "Ni ce Manager, ka faɗawa duk wanda ya turo ka cewa ba zan ba, ina buƙatar explanation me aka siyar a kamfanina nan har aka samu shigowar kuɗi kimanin 5.1B cikin awa guda, ba details na abin da aka siya sai file na zuwan kuɗin kuma yanzu ana buƙatar fitar dasu daka account ɗin kamfani? This is complicated" zai yi magana cikin tsawa ta ce "Out of my office accouter" cikin saurin ya miƙe tsaye yana ficewa daga officer ɗin. Numfashi Fiyya ta sauke ta rufe idanunta da sauri kuma ta buɗe jin an shigo ba tare data bada umarnin a shigo mata officer ba. Cikin sauri ta miƙe tsaye tana ɗan ja baya ta shiga ƙare masa kallo daga sama har ƙasa ta yi mamaki to babu security a ƙofar office ɗin nata ne? Da ƙyar ta ja numfashi tana saukewa ta ce.

"Who are you? Waye kai.

For more information

08164069385

WhatsApp only.

[1/7, 9:32 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

Nimcyluv

Bright pens....Second batch

Ƙarewa office ɗin kallo ya yi yana buɗe idanunsa akan Fiyya wacce ta ɗan ja da baya tana ɗauke kanta gefe. "Ya Allah i really missed her, Safiyya A. Marafa" ya furta yana kallon makaken photon Fiyya dake cikin office ɗin kafin ya ƙarasa ciki murya a hankali ya ce

"Wa kike tunanin zai zo banda mijinki Fiyya? You're enjoying teasing me" sai a lokacin ta sauke ajjiyar zuciya a ɓoye tare da ɗan yin murmushi mai kyau wanda ya saka shi lumshe idanunsa ya buɗe "Like this.... I missed you completely Fiyya ba shiri na dawo gida fa"

"Ina yini ya hanya?" Ashraf na kallon files ɗin gabanta ya ce "Allahamdulilah. Ya naki aikin Manager?" Ta ce "Lafiya, me ka zo yi a kamfanin ko kana da business damu ne?"

"Eh, babban business ma" tana kallon system ba yabo babu fallasa ta ce "Ohh" kallon ta ya dinga yi yadda take operating system ɗin cike da nutsuwa fuskarta a kame ba wargi hakan bai hana kyan fuskarta bayyana ba ya ja numfashi ya sauke yana jin wani abu sosai na fuskarsa a kan Fiyya ya kalli agogon hannunsa ya ce "Ko gida ban je ba, ina son na samu nutsuwa da kallon fuskarki dear" kamar baza ta ce komai ba sai kuma ta ce "Ok" mamakin halinta na ko ina kula yana damunsa cikin damuwa yana sassauta murya ya ce "Fiyya" ta ɗago ta kalle shi sai kuma ta zame idanunta.

"Na kasa fahimtar me kike nufi dani Fiyya anya kina so na kamar yadda nima nake son ki? I told you na dawo saboda ke amma ki ce mini wani ok? To hell with the ok ɗin na tsani irin wannan ɗabi'un naki, da na yi miki uzurin rashin sabo ne amma for good 5years muna abu ɗaya dake? Idan customers ne kya musu fara'a ki yi welcoming nasu, amma ni da zan zama mijinki kwana kwana nan kike ma haka, ko wanne gardi ya zo office naki kin zama wata kamar jerry abar kallon kowa" ya

girgiza kai cikin damuwa da ƙunci yana zare gilas ɗin idanunsa tare da buga table ɗin gabanta ya ce

"A cikin abu biyu dole ne a yi guda"

Kallon Ashraf kawai take ta tabbatar yana da anger issues tama rasa me za ta ce masa don takaici ya zo har office ɗin ta kuma yana yi mata hayaniya, yana ƙoƙarin tara mata jama'a. Ko motsi ba ta yi ba, tana juya kujerar da take kai a hankali idanunta zube a kansa. "Ina ji Ashraf" bata taɓa kiran sunansa ba sai yau hakan ya saka ya kalleta da sauri ransa ya ƙara ɓaci.

"Aure ko aiki, ya zama dole ki zaɓi guda ɗaya a ciki"

"Ok" ta sake cewa tana miƙewa tsaye tare da ɗaukar jakarta da wayarta da makullin mota ta zaga a hankali zata shige shi ya yi saurin saka hannu ya riƙo nata hannun cikin sauri ta kalle shi tare da jefa masa wata iriyar harara sakinta ya yi ya matsa dab da ita yana sauke mata hucin numfashin ɓacin ransa dake fitowa tun daga ƙasan zuciyarsa.

"Ki bani amsar abin da na buƙata kafin ki fita, aikin ki ko aure"

Ta taune leɓenta tana ware masa manyan idanunta sai kuma ta kalli wayarta tare da buɗewa ta shiga wajan photos pictures ɗinsa ta nemo wanda ya yi kyau sosai ya saka ƙananun kaya lokacin bashi da lafiya ta je duba shi ya fito harabar gidan tana murmushi ta ce "My patient, bari na ɗauki photo as evidence karka mutu bani photon nunawa yarana masoyin da ya tafi ya bar Fiyya" a lokacin juyawa ya yi ya kalleta daga kwancan da yake ya wurga mata harara sai kuma ya miƙe tsaye yana nufar inda take ta yi saurin yin baya tana masa wani irin murmushi ya tsaya yana kallon ta sai kuma ya ce

"To make you clear, ba ki da wasu yara sai na Ashraf, ba ki da wani miji sai Ashraf ba wanda za ki yi wa takaba sai Ashraf.... Ashraf na Fiyya ne Fiyya kuma ta Ashraf ce in sha Allah" murmushi kawai ta yi bata ce komai ba ta ɗauke shi photon yana langwaɓe kai gefe.

Fiyya ta shafa screen ɗin wayarta tana kallon photon kamar yanzu ta ɗauka cikin muryar mara hayaniya idan tasu ta ce "Ya ce wai na zaɓa aiki ko shi, kar ya buƙaci jin amsar daga bakin Fiyya" fisge wayar ya yi "Dole ki bani amsa yanzu ba sai anjima ba" ta gyara tsaiwa tana fuskantar shi da kyau a hankali ta matsa dab da shi ta ce "Allah Ya baka wacce ta fi Fiyya" Ashraf ya yi sak can ya ce "Me kike nufi?"

"Ina nufin na haƙura da auren, na zaɓi aikin" tana kaiwa nan ta fisge wayarta cikin sauri ta yi waje ya bita da kallo zuciyarsa na ta fasa. Tana fita ta kalli security ta ce "Idan ya fito a rufe mini office" waje ta yi ko Elevator bata tsaya shiga ba ta sakko ta bene dake a wajan 5 floor office ɗin nata yake. Sai gaisheta ake yi amma ba wanda ta saurara idanunta har dishi-dishi yake saboda ɓacin rai.

Misalin 1:43 dare ya nutsa ana samawa zuciya nutsuwa ya yinda kowa yake bacci a lokacin ne safiyarsa ta waye. Ya tsaya a ƙofar gidan yana kallon gate sosai ya jima a wajan kafin ya juya ya kalli Goge da Darma cikin hanzari Goje ya shiga buga gate ɗin gidan kamar zai cire shi, sun jima kafin daga bakin ƙofar suji an ce "Waye?" "Buɗe" Goje ya ce yana zare wuƙa tare da matsawa jikin ƙofar mai gadin a ruɗe yake sosai ya ce "Kamarya na buɗe a wannan zamanin da muke cikin insecurity na sani ma ko yʻan fashi ne?"

"Sune" Darma ya ce yana yin muzurai shi kaɗai ne a cikin su yake a buge shi Moh abin da Mangal ya bashi har yanzu bai gama sakin shi ba, shi ya sa ba komai yake ganewa ba. "Wallahi ba zan buɗe ba, babu mamaki kun ji Alhaji Wada ya dawo gari shine za ku yi masa fashi"

"Ko ka buɗe gidan nan na rantse da Ɗan Amina na shigo sai na yi maka ɓalli-ɓalli" ai kowa mai gadin ya ce "Ka yi mini ɗari-ɗari ma amma babu abin da zai saka na buɗe daman ƙasa babu lafiya ga yaron can daya dawo abin tsoro ana ta surutu a unguwa ya kashe matarsa kuma ya shigo cikin al'umma zai lalata jama'a..." Kafin ya ƙarasa faɗa Moh ya saka ƙafa ya daki ƙaramar ƙofar nan take ta ɓalle ya faɗa cikin gidan, da sauri mai gadi ya ja baya ba wani sanin Moh ya yi ba kawai zancen ya dawo kunnensa da labarin kisan daya game ko'ina a shekaru uku da suka shige. Goje ya daƙo mai gadin ya falle shi ya faɗi "Kai har ana cewa ka buɗe ƙofa kana ƙi?"

"Goje"

"Sai godiya" Moh ya numfasa yana durƙosawa daidai fuskar mai gadin "Me ya ce a yi masa?" "Sai godiya ɗari-ɗari ya ce yana buƙatar tsini" ihu mai gadin ya saka ya ce "Wallahi tallahi ƙarya nake"

"Zaɓi ɗaya" cewar Moh yana fito da askira ya ajjiye gefe ya sake fito da wata wuƙar ya ajjiye ya jima a duƙe kamar mai tunani sai ya ce "Ko ɓalli-ɓalli ko yan uku ko na jaki"

"Ɓalli-ɓalli" mai gadin ya ce da sauri ya ɗauka wani abun za a ɓalle da idanu ya kalli Goje da Darma suka riƙe mai gadin tare da juya shi yana ihu da komai Moh ya ɗauki ankarar ya dinga tsaga masa a baya jini na fitowa shi kansa zuciyarsa ce kawai ke ingiza shi ya yi hakan kuma daidai gani yake yanzu daidai yake da tsarar kowanne mutum haka ƙwaƙwalwarsa ke karantar da zuciyarsa. Tun mai gadin na kuka har ya yi laƙwas sai nishi yake fitarwa, suka yar da shi a wajan cike da tafiyar taƙama yana taku ɗaiɗai jikinsa na buɗewa cikakken namiji a tsaye matashi dake kan lokacinsa. Cikin sa'a ya samu ƙofar shiga babban parlon gidan a buɗe ya kutsa kai yana kallon tangamemen parlon ya dinga kallon komai, iya haɗuwa ya haɗu sai ƙarar a.c ya lumshe idanunsa ya buɗe ya jima kafin ya ƙara shiga cikin ɗaya parlon su Goje na biye dashi.

Alhaji Wada na zaune shi da iyalansa basu da jima da sauka daga ƙasar ba. Yana saman kujera matarsa na gefe sai yaransa guda biyu mace da namiji kayan ciye-ciye fal a gabansu bama su damu da cin abincin ba sai ice-cream dake hannunsu suna sha. Da sauri Alhaji Wada ya miƙe tsaye yana kallon matasan da suka shigo ya juya ya kalli matarsa da yaran ya ce "Su waye ku? Me kuka zo yi mini a gidana a irin wannan lokacin?"

Moh bai ce komai ya zaga ya zauna saman kujera ya jingina ya ɗora ƙafarsa a saman table ɗin yana kallon abincin Goje da Darma na tsaye sai muzurai suke yi cikin sauri Alhaji Wada ya ɗauki wayarsa zai kira yan'sanda "Ba wani abu da zai bani tsoro, yadda aka fara dakai dole a ƙare da kai Alhaji Wada"

"Waye kai? Me aka fara dani" fuskar Moh a rufe ya saka hannu ya zame abin da ya rufe fuskar da shi "Idan maye ya ci ya manta ai uwa ba zata manta ba, idan kare na

yawo zabo na yawo za a haƈe ya ranar" ƙirjin Alhaji Wada ya buga ya yi baya da sauri ya ce "Kai ne? Me na yi maka"

"Ba labari na zo baka ba, ba fansa na zo ɗauka ba na zo ka ganni kasan ina raye ina numfashi ka san cewa na cika ɗan babata Ammo Mai dawa nake sarki mai jeji, na gode Ɗan Amina da ka zama kai ne silar da ya saka na gano wasu abubuwan" Alhaji Wada jikinsa rawa kawai yake ya ce "Don Allah kar ka yi mini komai kar ka taɓa yarana basu san abin da ya faru ba" "Idan zan yi mana jira, idan na yi sai ta ɓaci. Ina je store ɗin gidan nan?" Da hannu Alhaji Wada ya nuna masa hanya ita kam matar ta kasa motsi saboda tashin hankali bata taɓa ganin fuska mai ban tsoro irin wannan ba, yaran sai takurewa waje guda suke yi ko haƈa idanu da Moh basa son yi" ganin har lokacin Moh bai tashi ba ya saka Alhaji Wada cewa "kar ka ce zaka mini komai" shi dai Moh kallon Alhaji Wada kawai yake zuciyarsa na tuna masa irin zaluncin da ya yi masa da hannu ya nuna masa yaran cikin kakkausar murya ya ce "Ko dan waƈan nan, ba zan so su zama abin da na zama ba" ya juya ya kalli Goje ya yi masa fito da inkiya suka nufi store ɗin kayan abinci kamar hauka haka suka dinga fito da buhun shinkafa katon na taliya da maroni su magi da galan na mai suka jide waje guda.

Yana bada faƈi ya miƙe tsaye ya nuna kayan abincin "Ka raba a masallaci ka haƈawa mutane da haushin kare guda goma-goma, ka kai har gidanmu" Ya juya zai fita sai ya tsaya ya saka hannu a aljihu ya zaro kunama ƙatuwa baƙa ƙirin da ita ta ɗaga ƙari sama ya damƙi hannun Alhaji Wada ba tare da yaran sun gani ba, ya cilla kunamar ciki ya damƙe hannun. Azaɓa ta saka Alhaji Wada zubar da hawaye zufa na yanko masa sosai da sosai a hankali cikin ƙasa da murya ya ce "Ka kira cinnaku yɑn'sanda kenan ka faƈa musu an yi maka fashi, idan sun tambayi waye karka yadda ka ce Mai dawa, ka ce SCORPIO" yana kaiwa nan ya kashe kunamar ya soke jikin bango da sauri ya fice kamar walƙiya, su Goje suka mara masa baya.

Fiyya na durƙushe a gabansa kanta a ƙasa ji take dama tana da ƙarfin yin kuka a yanzu, ta kasa fahimtar sai yaushe ne komai zai daidaita ya tafi daidai? Tana haƈiye abubuwa da dama ba tare da kowa ya sani ba bata bari a san rauninta amma yau ita aka saka gaba akan abin da sam bai kai ya kawo ba? Ita zaiwa haka?.

"Safiyyerh A. Marafa"

Ya kira sunanta a karo na uku sai a lokacin ta ɗago kai ta kalli Daddy dake zaune saman kujera hannunsa riƙe da carɓi fuska ba wasa ya lura sai ya dage sosai akan Safiyyerh.

"Ya kuka yi da Ashraf me neman auren ki?" A hankali ta ce "Ba komai Daddy"

"Ba komai Daddy, na gaji da jin wannan daga bakin ki Safiyyerh ke kina nuna mini ke mai wayo ce kuma kin girma kin isa ki yi handling dukkan wasu matsalolinki ko? Ke jaruma mai experience akan aikinta Managern FS WORLD INVESTMENT COMPANY? na yarda kina da wayo tunda na kasa sanin damuwarki tsayin shekaru na yarda kina da experience hakan ya sa cikin ƙaramin lokaci kika zama Manager but amma.." ya yi shiru yana kallon ta sai kuma ya ce

"Safiyyerh kina buƙatar aure shine cika da ƙimar kowacce mace, me kike buƙata a rayuwa da ba a yi miki ba, wanne gata ban yi miki ba da kika ce kin fasa auren Ashraf?"

"Daddy ya ce na zaɓi aiki ko aure"

"Sai kika zaɓi me?"

"Aiki" Daddy ya dinga kallon yʏar tasa shi ya rasa gane wani mataki zai ɗauka a kanta.

"Ba za ki yi auren ba kenan, baƙin cikin jikoki kike mimi Maama? Sai na faɗi na mutu za ki yi auren me ya sa kika kasance stubborn ne, ko don kinga ina biye miki?" Fashewa ta yi da kuka sosai ita kanta bata san kukan ya ƙwace ba, kalmar mutuwar da Daddy ya faɗa ya firgitar da ita sosai idan Daddy ya mutu ta shiga uku.

"Daddy gasu Yaya J, su Marafa, su Captain Daddy me ya sa sai ni za a yi aure ne? Ni ce ƙarama fa nawa nake gabaɗaya ko aure za ka mini ka ƙara mini lokaci Ashraf zafin zuciya ne dashi baya fahimta ta a kodayaushe"

"Maama kuma taurin kai, ji da kai while zafin zuciya, Safiyyerh dole za ki yi aure" runtse idanunta sosai kenan duk abin da take ya tashi a banza? Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un me ya sa Ashraf zai yi mata haka me ya sa zai haɗata da mahaifinta? Ta kasa cigaba da kukan abu ya tsaya mata a wuya sosai. Har Daddy ya je bakin ƙofar shiga sashinsa ya tsaya ba tare daya juya ba ya ce

"Cikin satin nan zan ɗaura miki aure da Ashraf in sha Allah"

Dum! Haka ta ji zuciyarta ta buga da ƙarfi har tsakiyar kanta kuma ta ji hakan, ta runtse idanunta sosai take ƙoƙarin jan numfashi ta kasa ta yi saurin riƙe wuyanta da take jin kamar an soka mata abu a ciki saboda zafin da yake. Cikin sauri J ya ƙarasu parlon daman ya shigo da nufin yiwa Daddy sai da safe ya nufeta yana riƙo hannunta ya ce "Manager lafiya? Mene?" Kafin ta bashi amsa Marafa shima ya shigo ya nufe ta, haka Dr Hash gabaɗaya suka zagaye ta suna tambayarta lafiya kasancewar suna mugun son ƙanwar tasu kamar rai. Hannun J ta riƙe gam tana nishi hawaye na zubu mata sosai ta kasa magana hakan ya saka Dr Hash miƙewa ya ɗakko ruwa mai sanyi ya yiwa J alamar ya ɗago ta, a hankali ya dinga bata ruwan tana sha ya zame rubar ruwan.

"Junaid kwantar da ita saman kujera ko ka kai ta ɗaki"

"Bari ta ƙara jin dama dama a dai ƙaro gudun acn ta fi shaƙar iska da kyau" cikin sauri Marafa ya nufi wajan ƙaro a.c a hankali suka ji an ce

"Kar ka ƙaro" ya juya ya kalli Captain dake zaune kan kujera abin shi yana dannawa, yana zaune Daddy ya kira Fiyya duk maganganun da sukai yana zaune har halin data shiga. "Captain daman kana ciki kana kallo Maama ba lafiya?"

"Ni na ɗora mata?"

"Amma baka ce mata sannu ba, she's our little sis our favourite" kallon da Captain ya yi wa Marafa ya saka dole ya yi shiru dukkan su ba wanda ya iya cewa Captain komai domin sun san hali basa shiri da Fiyya bai shiga sabgarta ba, duk abin da ya

shafe ta babu ruwansa da shi. Ko magana bai fiya yi ba ana ganinsa kowa ke nutsuwa domin shine babba a cikin su Fiyya kuma Auta. Fiyya ta yi lamo jikin J tana sauke numfashi Dr Hash na riƙe da hannunta jin jikinta ya fara ɗaukan zafi sosai. Da ƙyar ta lallaɓa J na riƙe da ita suka haura sama duka sauran mazan suka bi bayansu banda Captain da yake harkar gabansa.

Wajejen 2:30 Daddy ya sauke numfashi yana kallon yadda take sauke numfashi a hankali ko a baccin bata da walwala ya juya ya kalli Captain dake tsaye hannunsa zube cikin aljihu "Aliyu me na ragi Maama da shi a duniya dana kasa fahimtar meke damunta? Ita ɗaya ce mace yaɗata laifi ne don na so ta yi aure?"

Captain dai ya yi shiru idanunsa a saman fuskar Fiyya Daddy ya miƙa hannu ya taɓa goshinta ya ji har lokacin da zafi daman ya fi ƙarfin awa guda zaune a wajan, yana cikin Captain ya buɗe ƙofa ya shigo da tunanin babu kowa cikin ganin Daddy ya saka dole ya tsaya. "Maama ki yi mini alfama ki yi auren nan, shi ne abin da za ki yi ki faranta rai na" ya gyara mata hannunta daya lanƙwashe kana ya miƙe tsaye zai fita

"Aliyu mu je"

"After you daddy"

Daddy ya jinjina kai ya fita yana janyo ƙofar. A hankali Captain ya nemi waje ya zauna a gefen gadon ya zuba mata idanu sosai, a nutse a kamo hannunta ya riƙe cikin nasa jin jikinta zafi sosai ya saka ya saki hannun ya ɗakko towel da ruwa ya dinga goga mata a goshi har lokacin yana riƙe da hannunta har sai da zafin ya ragu, bai tashi ba yana zaune aka fara kiran sallar farko cikin sauri saki hannunta ya miƙe tsaye yana haɗe fuska J ne ya shigo a hankali ya bi Captain da idanu har ya fice daga cikin bedroom ɗin na Fiyya.

*****

Cikin gidan ya faɗo babu ko sallama Inna Binta na zaune har za ta yi magana ganinsa tsaye ya saka ta yi shiru da bakinta. Yau ranta fari tas an yi musu rabon abinci Malam ya basu ya ɓoye sauran. Ɗakin Ammo ya nufa yana ɗaga labulan

ɗakin ya ganta zaune tana ɗaura kuɓewa tun kan ya shigo jikinta ya bata yana hanya saboda gabanta daya tsananta faɗuwa.

Ya shiga ɗakin ya zauna ita dai bata kalle shi ba, sai kallon ta ya ke yi can ƙasa da murya kamar ba shi ba ya ce "Ina yini Ammo?"

Miƙewa ta yi maimakon ta amsa masa, ya cije bakinsa yana rufe idanu kwanon abinci ya jenyo ya buɗe yaga taliya ce jallof ta ji albasa nan da nan yawunsa ya tsinke ya tuna rabon shi da abinci har ya manta.

"Alhaji Wada ya bawa Malam, idan da zuciya ai ba za ka ci abincin daya bamu ba" cak ya tsaya yana kallon abincin kamar zai tashi sai kuma ya nutsa hannunsa ciki ya ɗebo lauma zai kai bakinsa cikin sauri aka ce "Allah Ya isa ban baka ba ida ka ci abincin nan" Malam ya kalli Ammo ya ce

"Bana ce kar ki yarda ya shigo gidan nan ba? Wato har abinci kika bashi ko?" Ta girgiza kai ta ce "Ɗauka ya yi"

Jiki a sanyaye Moh ya miƙe ya fice daga cikin ɗakin yana saka ƙafa ya banko ƙofar da ƙarfin gaske yana zuwa daidai inda Inna Binta ke gyara shinkafa ya saka ƙafa ya yi fatali da farantin shinkafar ta tarwatse ya yi waje kamar zai tashi sama. Ta dafe ƙirji tana rafka salati "Ƴar gwamnati ce fa Allah ya isa wallahi".

Goje ya dubu Mangal ya ce "Me ka bashi wai? Yake wannan sambatu da mimmiƙar haka?"

"Sha fara kaga aljan ce, ita za ta yi aiki a jikinsa, daga sama aka bani ita" Goje ya juya ya kalli Mai dawa ya sauke numfashi cikin damuwa ya ce "Dole sai ka koya masa shan waɗannan abubuwan ne?"

"A'a ina zaune ya zo mini kamar an koro shi yana huci ya ce na bashi irin abin da na bashi kwanaki saboda damuwar zuciyarsa ta kau ya manta da komai ni kuma na bashi sha fara kaga aljan"

"To gashi nan yana ganin aljanin ai" da ƙyar ya samu ya yi bacci a wajan. Bayan ya farka Mangal ya bashi abinci ya girgiza kai "Mai dawa idan kuɗi kake so ina da hanyar da zan yi maka ka dinga samun kuɗi sosai cikin sauƙi har ma ka taimaki wasu" tunda ya farka sai lokacin ya ɗaga kai ya kalli Mangal alamar ina ne? "Bangar siyasa kasan yanzu muna gab da fara shiga sabgogin siyasa uban gidana cikakken ɗan siyasa ne, shima yana da uban gida kuɗi zaka samu sosai a sabgar nan ina faɗa maka"

"Kai ni" kawai ya iya cewa yana miƙewa tsaye.

Suna zaune a wani haɗaɗɗan parlo inda suke karɓe wa su yi meeting na sirri. Gabaɗaya suka kalli MUTALLAB TAHHB SCORPIO ɗaya daga cikin su ne ya ce.

"Mene sunanka"

"Mai dawa"

"Kai mafarauci ne?" Ba tare daya kalli mutumin ba ya ce "Darr" babban mutumin ya jinjina kai sosai ya zaro wani photo a aljihu ya ce "Kafin mu yi maka bayanin su waye mu, me muke buƙata da kai, fara ganin wannan ka saka dai a ranka mu yɗan siyasa ne"

Shi dai Mai dawa bai ce komai ba, aka ajjiye masa photon a gabansa "Ɗauki ka buɗe ka gani mana"

Wani daga cikin mutanen ya ce "Manager ce a FS WORLD INVESTMENT COMPANY aiki za ka yi mana a kanta kafin mu faɗa maka aikin mene ka fara ɗaukan photon kaga wacece" a sanyaye ya ɗauki photon kafin ya kai idanunsa kai....

08164069385

For more information

WhatsApp only

[1/7, 9:32 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

"Safiyyerh Abdu Marafa Manager ce a Kamfanin FS WORLD INVESTMENT COMPANY kuma yɑ a wajan tsohon leccara, muna buƙatar ka yi mana kidnaping ɗin ta" Moh Kallo ɗaya ya yi wa photon da suka bashi ya ɗauke kai

"Ka santa?" Shi dai bai ce komai ba.

Eng Ali wali ya dinga kallon Moh yana tunanin abubuwa da yawa a ransa kafin ya ce "baka gama ganin photon bane, ko da yake yana da kyau da ƙare mata kallo maybe ka zama silar mutuwar ta ko ka kashe ta da hannunka, ka ya zama dole ka gane kamamminta"

Goje ne ya ɗago kai da sauri yana kallon Eng Ali wali kafin "Sai da kai mai gida wannan aikin ai ko ni zan iya yin shi ba sai Mai dawa ba, ka huta ka sarara mai gida"

Eng Ali wali ya yi murmushi yana jingina da kujera ya ɗauki ƙafarsa ya ɗora akan ɗaya ya kalli Mai dawa wanda ko motsi bai yi ba sai jujjuya photon da aka bashi yake. "Ko Mangal ba zai iya aikin nan ba da ya fika wayo a sabgar balle kai da na sani yanzu, shi wannan Mai dawan idanunsa na kalla na san zuciyarsa za ta iya aikata komai"

Ya yi shiru sai kuma ya ce "Ni ɗan siyasa ne babu mamaki ka taɓa ganin poster na ko bana, shekaruna takwas ina riƙe muƙamin Ɗan majalisa na tarayya a jam'iyyar da nake ta kara, bani da ra'ayin haƙura da kujerata kamar yadda ake yi mini kirarin idan na yi na gama na karya kujerar. Siyasa jinina ce Mai dawa, bana jin akwai wani dalili da zai zo ya saka na haƙura da kujerar na amma wannan karon na yi karo da

muruci wanda yake shirin yi mini wahalar dafawa ko ta halin yaya ne dole na sake hawa kujerar nan a karo na huɗu. Hon Maɗatai yana tare da manya wanda suka san kan siyasa ciki da bai dole mu fito da salo na musamman wanda zai kai su ƙasa. Hon Maɗatai shine ɗan takarar jam'iyyar hamayya kuma yana da ƙarfi har yanzu ba'a san mene rauni ko aibun shi ba amma akwai jita-jitar data zo kunne na domin tabbatar da gaskiyar al'amari ya saka na kawowa cikin jama'ata"

Sai a lokacin Mai dawa ya ɗago kansa ya ɗan kalli Eng Ali wali kamar ba zai ce komai ba sai ya cije baki yana karkatar da kai gefe ya haɗa hannayensa biyu suka bada sauti mai ƙara cikin wata murya ta izza ya ce

"Mene haɗin ta da maganar yawar ku?"

Eng Ali wali ya ce "Wa kake magana"

"Ita ɗawar mai ɗan kwalin?"

Cikin rashin fahimta Eng Ali wali ya ce "Meye ɗawa da ɗan kwali kuma?" Mangal ya yi murmushi yana "Ka fice Mai gida, ɗawa da mai ɗan kwali mace kenan ake kwafa maka zancen" Ya ce "Yaran naku sai ku"

Miƙewa Mai dawa ya yi tsaye yana ɗora ƙafarsa a saman farar kujerar dake parlon kallonsa kawai Eng Ali wali ya yi bai ce komai ba. Sai wani ya ce "Mai dawa farar kujera ce fa?" "Ko takaddar jikinka zan ɗora ƙafa akai" wanda ya yi maganar ya yi saurin kallon farar shaddar dake jikinsa fara tas da ita sai ya ja bakinsa ya yi shiru. Moh ya kalli gefe yana furzar da iska daga bakinsa ya ce

"Me ya sa ka neman, bayan kana da gajojinka?"

"Saboda kai ne baƙuwar fuska a cikin wannan sabgar tamu, ba wanda zai gano cewa a tsagina kake za ka yi aiki mai kyau hankalina ya kwanta da kai Mutallab" wani irin kallo Mutallab ya jefa masa idanunsa sun sauya kala ya yi murmushi ya ce

"Oh Mai dawa da jeji, ya batun yarinyar ka santa ne ko ka taɓa ganin fuskarta?"

"Na santa ko ban santa ba ina jin bashi kake buƙata ba. Yaushe kake so a kawo maka ita?" Girgiza kai Eng Ali wali ya yi ya ɗauki ruwa ya kurɓa ya ajjiye kana ya miƙe tsaye yana zagaye parlon hannunsa a baya "Ka jira umarni na, kawai ka zama cikin shiri a koyaushe zaka iya jin kira. Akwai gidan dana samu a bayan gari zan baka makullin ko ka ɗakko ta can zaka ajjiyeta kai ne zaka dinga kula da ita har yanzu lokacin da muka shirya abin da mukai niya, a cikin gidan akwai kayan aiki irin naku wanda za su sama muku nutsuwa"

Goje ya jinjina kai cike da jin daɗi kafin ya ce "Mai gida za a siya mana mota mai iska kamar yadda muke yaƴan iska?"

"Za a yi muku komai, ku riƙe amana. Sai dai kawai sharaɗi ko da wasa kar ku nuna kun sanni idan ina buƙatar ganin ku a wannan gidan zamu dinga haɗuwa, ku buɗewa kowa idanu kar ku ji tsoro da shakkar komai ni zan tsaya muku har zuwa ci zaɓe" Moh ya ce "Bayan cin zaɓan fa?"

"Kamarya?"

Ya buɗe manyan idanunsa sosai a kan Eng Ali wali a karo na farko ya ƙare masa kallo "Mene farashin aikina?" "Nawa kake so?" Ya yi shiru yana tunani can ya ce "Zan sanar"

Eng Ali wali ya ɗakko ƙatuwar bana da fastoci ya bawa Goje da yawa ya ce "Kuje ku fara da aikin liƙawa wannan a unguwanni da saƙo da lungu ya zamana babu wanda ake ganin sai Eng Ali wali, bayan wannan akwai wani dattijo da yake zuwa gidan rediyo yana yi sojan baka kuma duk ni yake kushewa yana son jiƙa mini aiki a tabbatar an saka shi yin shiru da baki da kowacce hanya" kuɗi ya ciro daga cikin Aljihu ya miƙawa Goje ya ce "Aje a yi caji a huta" har Moh zai juya sai kuma ya tsaya ya cake waje guda kamar saƙago ya ce "Me ya sa kuke son a kamata?"

"Aiki ne kawai naka wani abu ba sai ka sani ba, mune shuwagabanni ku dai a baku kuɗi da kayan sararawa shine" kai tsaye Moh ya ce "To nemi wani" Eng Ali wali ya ce "Me ya sa? Bayan kai ka cancanta?"

"Ba zan ba"

"Shikenan na gane, Safiyya Abdu Marafa na faɗa maka yɑ ce wajan tsohon leccara, yana kawo mini barazana a sabgar siyasa tare da nuna rashin cancanta a fili. Matasa na jin maganarsa abin da ya zaɓa kuma da shi suke yin aiki a yau ɗin da muke ciki matasa sune siyasa ina so a sa shi yin mubaya'a dole. Kasan da yawan lokaci Malamai suna kawo mana cikas" Mai dawa ya jinjina kansa alamar ya ji sai dai bai yi magana ba a hankali ya duƙa yana buɗe hannu ya ce "Sai godiya"

"Sai godiya" Mangal da Goje suka faɗa suna zagaye shi. Cikin sauri kuma ya fice daga cikin parlon suna mara mishi baya.

Eng Ali wali ya dubi wanda ke zaune sai kuma ya yi dariya sosai ya ce "Amfanin su kenan fa babu wani aiki da ɗan daba zai iya yi maka banda bangar siyasa kashe kashe da sare-sare mu kuma sai mu jefe su da abin da sukewa"

Fiyya na tsaye gaban madubu tana gyara rolling mayafin kanta yau ma suit ce a jikinta ta mata riga da wando blue black ta amshe ta sosai ta kalli kanta a madubin she missed the old Safiyyerh komai nata sabo take jin shi, ta ji kamar ta rasa wani abu mai amfani a tattare da ita amma mene? Shi ne abin da sam ta gaza fahimta ko a cikin bacci. Ta sauke numfashi tare da ɗaukan wayarta da jakarta tana ƙoƙarin buɗe ƙofa ta fita Ummi na shigowa cikin ɗakin Fiyya ta yi baya tana bata hanya kafin ta ce "Good morning Ummi" daga sama har ƙasa Ummi ta kalle ta sai kuma ta je can bakin gado ta zauna tana sake kallon Fiyya "Ina za ki?" "Ummi Company"

"Junaid told me ba ki da lafiya, na yi bacci da wuri" a hankali ta ce "Lafiya lou nake Ummi ga alama kin gani zani aiki"

"Fiyya bana son irin wannan shigar taki, kuma ki haƙura da aikin nan yau za a kawo kayan auren ki" da sauri ta ce "Aure kuma Ummi? Ba sai nan da watanni ba?"

"To Daddynku ya ce cikin satin nan"

"Shikenan zan je aiki"

"A'a ki haƙura yau" marairai ce fuska ta yi sosai kamar za ta yi kuka ta ce "Ummi akwai buƙatar na je, ina da meeting da ma'aikata ba zan jima ba" Ummi bata san damuwar Fiyya dole a hankali ta ce "Allah Ya tsare ki dinga kula ke dai macace ba namiji ba, kina lura da abubuwa da kike yi" Fiyya ta yi dariya tana yin waje ta ce "Kuma ki saka tsoron Allah a ran ki Fiyya ban da wulaƙanta jama'a, al'umma ta Annabi ce" Ummi ta girgiza kai kawai ta ce "Wato kin haddace kenan"

"Dole na Ummi"

Cak ta tsaya tana riƙe kan ta Ummi ta ce "Subuhanallahi Fiyya kina lafiya? Ba za ki haƙura da zuwa aikin nan ba?" Ta ɗan ya tsuna fuska da nuna alamar ba komai ta ce "Kawai na ji kaina kamar an saka mini shocking" gaban Ummi ya faɗi sosai sai bata nuna ba ta kama hannun Fiyya suka sakko ƙasa.

Dr Hash ne ya fito shima sanye da farar riga ta likitoci Fiyya na kallonta ta ce "Likita bokan ture, kuma fiɗe ku ɗinke"

"Kamar wasu mahauta" ta yi murmushinta mai kyau tana lumshe idanu "Barka da safiya Dr" ya yi mata murmushi "The whole Manager in the world" Ta buɗe ido shima ya buɗe kafin su ce komai J ya fito shima yana cewa "In the world mana, wannan kamfanin nan ku ina ne basu da reshe ni dai watarana zan zauna ki bani labarin kamfanin sosai na ji ai na yin wanda yake da shi" "Kai Yaya J nima ban san ko na waye" ya buɗe ido ya ce "Ban gane ba?"

"Da gaske nake Yaya ban san asalin me shi ba, kawai dai na san ni Manager ce"

"Ji nake Ashraf's father is the owner of the company"

Ta tura baki gama tana harar shi "Kuma ka sani kake tambayata" ya ɗaga mata gira ya ce "Zan zo ki nema mini alfarma wajan surukin naki nima ya bani ko messenger ne" bata kula shi ba. Ɗago kai ta yi suka haɗa idanu da shi yana zaune ya watsa mata harara yana ɗauke kan shi gefe "Aliyu ba yau zaka tafi bane" ya yi shiru a hankali kuma ba tare daya ɗago kai ba ya ce "A'a"

"Ok na ɗauka yau ne, ni wallahi duk firgitar dani kake mutum ba walwala kamar a filin yaƙi nan fa gida ne, amma kodayaushe kamar an yi maka dariya ko yaya ne ka dinga murmushi"

"Ban iya ba Ummi"

"Murmushin ne baka iya ba Aliyu? Ka gwada zaka iya" ya miƙe tsaye yana yin waje "Ban san yadda zan ba" "Ina kwana Captain?" Fiyya ta faɗa tana haɗe fuska ko inda take bai kalla ba ya yi waje abin shi. Shi dai J murmushi kawai yake yi halin Captain na bashi malam sosai suka jera shi da Fiyya suka fita. Mota ta shiga yana ɗaga mata hannu shima ya shiga tasa motar kowa ya kama hanyar wajan aikin shi. Fiyya na driving a nutse ta hangi wata mota na bin duk inda ta yi sai ta taɓe fuska ko a jikinta a fili ta ce "Ɗan wahala ko waye"

Daddy dake zaune bayan shigowar Ummi cikin parlon sama ya kalleta ya ce "Me kike cewa Ummi?" Ta damuwa ta ce "Kwana biyu ba a amshi maganin Fiyya ba, kuma kamar ciwon zai tashi" ya ajjiye littafin hannunsu yana saka glasses ya ce "Wani abin ya faru?" Ta numfasa yana faɗin "Irin abin da ya faru kwana ki tana jin kamar ana mata shocking a kanta, ni wallahi bana son ma ta dawo daidai bana fatan ubangiji ya ƙara gwada mini tashin hankali dana gani shekarun baya" Daddy ya jinjina kai "Nima addu'ar da nake a raina shi ya sa ma na matsu kawai a yi ai maganar auren nan, wallahi bana son Maama ta dawo old Safiyyerh"

"In sha Allah hakan ba zai kasance ba"

Meeting hall ɗin ya yi shiru sai muryarta dake tashi cikin faɗa tana ɗan buɗe hannayenta tare da yin baya ta ce "Wanne irin rainin wayo da hankali ne, file ɗin dana ajjiye shi a office ɗina ina jiran a kawo mini proof hujjar abin da aka fitar aka

samu shigowar kuɗi zuwa asusun kamfani kamar yadda Accounter ya faɗa mini shine za a ce wai na yi signature a file aljana ce ni da zan taso da gida na zo kamfani na saka hannu, idan zan saka me ya sa ban yi ba tun da file ɗin ya zo table ɗina?" Ta miƙe tsaye tana kallon su gabaɗaya duka maza ne ita kaɗai ce mace ta koma ta zauna tana juyi a kan kujerar "I need to find out the truth, meke faruwa a wannan kanfanin. Md da kai da secretary za ku kai ni na duba ko'ina a wannan kamfanin yau ɗin nan, kai kuma Director ka kawo mini record ɗin komai daga watan daya shige zuwa yau ɗin nan, ina buƙatar statement yanzu a office nawa" ta sauke numfashi fuska a haɗe sosai "An gama" secretary ne ya kalleta kamar a tsora ce yake ya ce "Manager akwai baƙi da suke jiran ki"

File ta ɗauka ta miƙe tare da ficewa daga cikin meeting hall ɗin. Bata nufi office ɗin ta ba inda suke ganawa da baƙi ta nufa ta tura office ɗin a hankali a hankali ta yi sallama ta shiga. Manyan mutane ta gani su biyu zaune a kan kujera kana ganin su ba sai an yi magana ba ta zauna kan kujera mai cin mutum biyu a ladabce ta ce "Ina kwanan ku? Welcome to FS WORLD INVESTMENT COMPANY i am Safiyya A. Marafa how can i help you?" Wani rushehen mutum ne daya Hakim ce a kan kujera ya dinga kallon ta kamar zai haɗiye ta idanunta dai na kan system tana ta dannawa da aikin tura saƙo can ta ɗago kai suka haɗa idanu ta sake kame fuska ta ce "How can I you? Ta ya ya zan iya taimaka muku"

"Ba ki gane ni ba"

Sarai ta gane ko waye ta ce "Yau na taɓa ganinka"

"To ma sha Allah. Sunana Hon Maɗatai zan saka hannun jari ne a cikin wannan Company"

"Ok, me kake buƙata?"

Ya gyara zama sosai ya ce "Za a dinga bani shinkafa, suger, wake a kan farashin yadda Company yake siyarwa ni kuma zan ɗora kaso 50 domin cin riba amma daga lokacin Company ba zai sake siyarwa da kowa kaya ba sai ni" Fiyya ta dinga kallon shi sosai a ranta tana mamakin son zuciyar wasu ya suke so talakawa su yi da ran su ne? Burin shuwagabanni talaka ya faɗi ya mutu saboda yunwa? Ta yi jim sai kuma ta ce

"Da wata ce matsayin Manager ba Safiyya A. Marafa ba do wataƙila ka samu wannan damar a yanzu ina maka murna da cewar we're not interesting anymore, da wannan zai fi kyau ka buɗe naka masana'antar ka nemi matasa marasa aikin yi wanda suke lalacewa ka basu abin yi" ya dinga kallon ta can ya ce "Kin san waye ni? Yʼan'mata ki bi a hankali fa"

"Ai ba a yi wa Fiyya maimaici Hon Maɗatai ba zamu baka hannun jari ba You can leave" ya miƙe tsaye yana jin ba'a taɓa yi masa wulaƙancin da yarinyar ta yi masa ba "Safiyyerh ko? Ki bi a hankali haɗuwar farko ce wannan, zan tafi amma zan dawo"

Ficewa ya yi rai ɓace zuciyarsa na zafi. Fiyya ta ɗauki kayanta ta nufi office. A hankali take bin bayan Md da Secretary ɓangaren kayan abinci aka kaita kana da mai daga can baya wajan shara inda ake ajjiye bukar kamfanin ta dinga jiyo wari da sauri ta nufi wajan Md ya ce "Manager sharar kamfani ce nan" bata kula shi ta nufi wajan sharar tana rufe hanci da f facemask kamar an ce ta juya idanunta ya sauka akan yatsun hannu guda huɗu da suke a leda ƙuda na bin su.

Tunda ya nufu layin su tiger na biye masa baya hannunsa riƙe da gora yara suke watsewa sai waje ake bashi hatta almajirin Malam sai da wasu suka bar wajan banda Ɗanyaro dake zaune yana danna sabuwar wayar daya siya sosai Malam yake ji da shi yanzu lokaci zuwa lokaci yake yi malam alheri na kuɗi ga nama da yake kawo masa, sai dai cikin dare Ɗanyaro zai lallaɓa ya gudu ba zai dawo ba sai safiya. Moh na ƙoƙarin shiga gidan Malam ya tare ƙofar ya ce "Na haifi yaro sunan shi Muɗallabi amma yanzu bani da wannan yaron na bar wa yʼan iska shi da yʼayʼan banza tunda ya zama shaiɗani ba zaka ja mini masifar da zan mutu a gidan ɗan kande ba" Moh zuciyarsa ta fara tafasa har wani hayaƙi ke fita ta cikin bakinsa ya dinga kallon asawan nasa ya kasa cewa komai ya leƙa surar gidan ko zai ga Ammo amma sai Inna Binta dake suɗe tukunya tana faɗin "Matsalata ɗaya a duniyar nan abinci idan na ci na ƙoshi Mufee ta ci ni fa ko a jikina" Juyawa Moh ya yi kamar zai yafi sai kuma ya nufi saman katanga ya kama ya dire ta cikin gidan Inna Binta ta zabura tana faɗin "ƙulna naru ƙulni bar dan wasalamun Allah Ibrahim, auzubillahi" jikinta sai rawa yake masifar tsoron Mai dawa take kamar ran ta sauran jama'ar gidan duk suka shige ɗaki banda Mufee da ta yi tsaye tana kallon shi sosai idanunsu yake iri shi bai san wace ita a gidan ba, bai damu daya sani ba yara ne kamar yaƙi wasu iyayensu basa cikin gidan.

Labulan ɗakin Ammo ya ɗaga ya ganta zaune tana ninke kaya ya fi minti goma tsaye kamar zai juya sai kuma ya shiga cikin ɗakin idanunsa akan kwanon abinci sosai yake jin yunwa idanunsa na rufewa ya miƙa hannu zai ɗauki abincin Malam ya ce "Kana ci zan maka Allah Ya isa ka tashi ka bar mini gida tsinannen yaro" da sauri Ammo ta kalli Malam sai kuma ta ɗauke kai.

Jikin Moh ya fara rawa jijiyoyin kansa na mimmiƙewa jin uban daya kawo shi duniya na yi masa Allah Ya isa ya yi ƙasa da kansa idanunsa kamar za su fito waje ya ji babu abin da yake buƙata sai ƙwayar da Mangal ya bashi ya sha, ita kawai zata sauke masa abin da yake ji ya manta da komai, yaushe ne zai zama daidai kamar kowanne mai rai an ci zalin shi an lalata masa rayuwa. Ya miƙe da sauri yana banko ƙofar ya yi waje "Sallamammen yaro Allah dai ya rabani da ƙaddara na huta"

Kai tsaye Moh dabarsu ya nufa yana zuwa suka mimmiƙe Darma na faɗin "sai godiya Mai dawa sarki mai jeji, wani ya ce ba kai ba yanzu mu fito mu yi farfesun hanjinsa"

Yanayin fuskar Mai dawa a bar tsoro ce ya takure waje guda yana jin kamar zuciyata zata fito waje don baƙin ciki. "A sama yake ku bashi sha fara kaga aljan" cewar Darma Mangal ya girgiza kai ya ce "Ba za ta yi masa ba, kawai a yi masa allurar fenta"

"A'a ta yi masa girma yaushe ya faɗo sabgar kar ka luda masa ya yi mana na jakuna yanzu" zaro sirinjin ya yi Moh ya ƙurawa siririn idanu ganin yadda Mangal ke zuƙo ruwan ciki ya fara girgiza kai da ƙyar ya ce "Kar ka yi mini Ka bar ni da tunanin bana son mantawa" kokawa suka fara yi da shi ya ɗauki Darma ya buga da ƙasa Mangal ya faki idanunsa ya caka masa allurar a gadon baya. Jinjiga ya fara sosai cikin ƙaramin lokaci ya yi shiru yana jin shi kamar a samaniya yana yawo yanayin ya yi masa daɗi sosai ya ji zuciyarsa wasai a wannan yanayin bacci ya ɗauke shi. Can cikin dare ya farka kam shi ya yi masa nauyi har yanzu bai dawo daidai ba, babu komai a cikinsa ya miƙe tsaye yana layi kamar zai faɗi Mangal ya ce "Mai dawa"

Ya yi masa shiru yana ɗaukar wuƙa ya soke ya ɗauki fitila ya riƙe "Dare ya yi ba, kana fita waɗancan ɗankokin za su iya kama ka gashi babu da goge a hannu ka zauna, kasan kuma yɑn cikin gari sun shigo sun samu labarin mun yage musu poster bama wannan ba ɗazo an ga gawar wani to ana tunanin mu ne kuma yaron ɗan cikin garin ne fansa suka zo ɗauka,na bibiyi abun shi yaron ƙwacan abar magana ya yi jama'a kuma sun fara ɗaukan doka a hannunsu suka rufe yaron da

duka har ya mutu. Su Cokali kuma ba za su haƙura ba kar muna zaune su ci mu da yaƙi"

"Sai godiya"

Ya furta da ƙyar daga nan sake yin shiru yana shirin barin wajan kamar zai kifa "Ina zaka ne? Ka dawo ka kwanta"

"Kai fa ba Malam zan haɗaka da Rainbow"

"Shikenan ina zaka yanzu" ya cije leɓe zuciyarsa na ayyana masa abin da zai yi shi ne daidai allurar sai gaibu take faɗa masa a hankali ya ce "Zan kashe Malam ya baza lahira"

For more information

08164069385

WhatsApp only

[1/7, 9:32 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

Page 6

Bright pens... 2nd batch

□for the adults and criminal side please □ just take it as a lessons

Goje daya farka daga bacci ya yi saurin miƙewa yana furta "Malam ɗin zaka kashe mahaifin naka?" Ya yi shiru bai yi magana ba, yana sake riƙe wuƙar a hannunsa da kyau duk jikinsa rawa yake, ga wani irin ciwo da kansa yake yi masa sosai, idan ya tuna abubuwan da aka aikata masa sai ya ji zuciyarsa ta bushe ta kuma ƙeƙashewa. Ya saka ƙafa ya banga je Mangal dake tsaye zai shige Goje ya yi saurin shan gabansa yana ɗaure fuska sosai ya ce "Saboda kana jin kanka a sama ta bakwai kake jin komai za ka iya yi? Me ya sa ba zaka yarda sarki sammai ke yin komai ba, mu fa ba haihuwar ta zubar bane ko yaya ne mun san abin da ya dace kashe mahaifinka ba shi ne mafita ba Mai dawa" ya ɗaga jajayen idanunsa kamar zai ci babu yadda ƙwaƙwalwarsa take faɗa masa ba daidai haka komai na duniyar yake yi masa babu daɗi maƙoshinsa na yi masa zafi da raɗaɗi wani abu ya tsaya masa da ƙyar ya iya buɗe bakinsa ya ce

"Ya zan yi?"

Kai tsaye Goje ya ce "haƙuri, ka bi komai a sannu mai dawa ita gaggawa aikin yɑn annaru ce. Kashe Malam a yanzu ba zai rage maka kashi goma a cikin ɗari na damuwar da kake ciki ba, iya wuya iyaye ne su"

"Ba iyaye na bane, ka bari ko ɓalli-ɓalli na yi masa" ganin da gaske shirin tafiya ya ke yi ya ce "Idan kaga ka bar wajan nan sai dai ni za ka fara kashewa" Ya ƙuri da idanu yana kallon Goje har wani hayaƙi ke fita ta cikin bakinsa ya wani cije gefen baki yana karkatar da kai gefe. Kamar wasa Goje ya ga Moh ya nufe shi da wuƙar shima yaƙi matsawa yana ganin kamar wasa ne yana ƙoƙarin kawai Goje sara su kaga mutane kamar daga sama sun zagaye su. Moh yaƙi motsawa sai Goje da ya yi baya ya cake yana zazzaro idanu tare da ɗaga gora sama. A kallon farko Mai dawa ya gane cinnaku ne yɑn'sanda sai ya ɗauke kai shi Goje bai faɗa da labarin ba saboda shigar fararen kaya suka yi.

"Eng Ali wali ya aiko mu wajan ku kawo muku kaya" sai a lokacin Mangal ya ƙarasu yana tale ƙafa ya ce "Kaya sun sauka da zafin su kenan yallaɓai, amma eh kun razana mu shigowa ba notice sai mu ɗauka dire aka yi mana" ɗan'sandan ya yi murmushi kawai ya ce "Kuna da kamar Ali wali za ku ji tsoro? Kune matasan da yake ji daku a yanzu musamman wannan da naga ko kallo bamu ishe shi ba" Goje ya juya ya kalli Mai dawa da yake kallon wani sashi daban alamar baya ma jin me suke cewa "Mai dawa sarki me jeji wajanka aka aiko mu domin aikin bana yara bane"

"Faɗi"

Moh ya ce yana bada faɗi ba tare daya kalli da ɗan'sandan ba. Abu ya fito da shi a jaka ya miƙawa Mangal ya amsa ya ce "Ka a dana kada a je a yi ta sha ana ɓarna, Eng Ali wali ya ce akwai fita ta musamman kuma ƙauyen da za shi basu da kirki dole tafiyar sai daku a ranar zaku cake ku bawa samaniya yazo ta yi hadari" Mangal ya buɗa ya ce "Dar hakan ya yi mana, sai Eng Ali wali ko ana su ko ba'a su ya zama dole don uwatar" Police ɗin ya juya kan Mai dawa a hankali cikin magana mai muƙamin ya ce

"Ka taɓa jin mai suna Scorpio?"

"Wa?" Goje ya ce da sauri yana kallon Mai dawa da sai a lokacin ya juyo ya kalli Jafar shima Jafar ya kalle shi da kyau ya ce

"Akwai matsala ne babba, Scorpio yana yi wa Eng Ali wali barazana, yana da babbar hujjar da zai iya kawo masa matsala a mulkinsa kuma babu shakka ko waye Scorpio akwai alamar ya shirya fito na fito da Eng Ali wali, to muna jami'ai ba zamu bari ba tunda a jikin shugabannin da yʼan dabarun mu muke samun namu rabon. Ali wali yana buƙatar ka taya shi gano waye wannan Scorpio da sunan shi kawai ake ji ba kamanni"

"Kamarya kenan?"

Mai dawa ya tambaya a taƙaice yana jin ƙirjinsa na buɗewa saƙo ya fara isa kenan a fili kuma ya sha kunu sosai. Jafar ya dafa kafaɗar Mai dawa ya ce "Kamar kai yanzu kowa ya san sunanka Mutallab inkiya Mai dawa saɓanin shi da sunan Scorpio kawai muka sani, babu wanda Eng Ali wali ya yarda da shi sai jami'an Dss ka baza jama'arka su tayaka binciko asalin waye Scorpio akwai kyauta mai yawa idan hakan ya tabbata, kuma ya ce ka faɗi kome kake so zai baka"

Wani irin kallo Moh ya dinga yi wa Jafar na kan kaga biri, biri ya ganka kifi na ganinka mai jar koma sai kuma ya ɗaga kai sama yana kallo sama cikin kumburarriyar murya ya ce "Bayan Dss da shi uban gidan naku waye ka ji yana neman SCORPIO?" Jafar ya ce "Me ya sa kake tambaya?"

"To kuje ku yi aikin da kan ku" ya faɗa yana juyawa cikin sauri Jafar ya riƙo shi ya ce "ka dinga sassautawa zuciyarka da fushi. Bayan Dss akwai jami'ai mafi hatsari da suke neman shi idanu rufe FID Federal investigation department, basu da imani wannan mutanen jami'ai ne da ba zaka taɓa tunanin ta ina zasu cimmaka ba, suna iya zuwa a suffar mahaukata ma ko mai neman taimako, su kakkarya mutum ko su kashe shi ko haukata shi ba wani abu bane a wajan su"

"Suka kasa kama Scorpio?" Jafar ya watsa hannu ya ce "Sannu sannu da zarar sun gane kamanmin su, babu mamaki su ɓullo ta wata hanyar kafin hakan ta fara ka ruga su kai hari,mun gama magana da kai Mai jeji" ya yi shiru bai ƙara cewa komai ba "Ka yi shiru?"

"Ka bada sha ɗayanka, zamu jauwalo ka idan akwai sagi" cewar Goje Jafar ya girgiza kai "Ka bar shi ya yi magana" Moh ya sake kame fuska babu wasa kuma yaƙi cewa komai sai ma fito daya fara yi yana kallon bindigar dake hannun ɗaya ɗan'sandan. Bisa dole suka juya suka tafi ba tare daya tanka su ba,daman Goje ya san ba maganar zai yi ba. Goje ya juya ya kalli Mangal da yake zuƙar wiwi a hankali ya ce "Ka raina musu hankali waye Mai dawa waye Scorpio"

"Ni ne, MUTALLAB TAHHB SCORPIO"

Mai dawa ya ce yana zare idanu waje manya gwanin tsoro da razani har sai da Goje ya ja da baya don bai taɓa ganin halittar idanu kamar ta Moh ba ƙwayar ta juye kamar bata mutane ba kuma sai ƙara ware manyan idanun yake yi.

"Akwai matsala Moh idan suka gano cewa kai ne Scorpio, za su yi maka illa gwara ka ɓace kawai daga yankin kafin komai ya sarara" "Gawata za su iya gani su haƙura da nema na" Ya furzar da iska daga cikin bakinsa kansa ya yi masa nauyi

"Goje an yi sake tunda aka bari na je state cid,ba san komai ba amma a fitar dani. Zan iya haƙura da komai banda abin da yake damuna a zuciya ni da kai na zan bayyana cewa nine Mutallab Tahhb Scorpio da zarar na cika muradina na abin da na yi niyya"

"Mai dawa"

"Sai godiya"

"Ina tunanin ka haƙura ka bar wa Allah komai duk zamu baza mu je gare shi ya yi mana eh hisabi" Moh ya taune harshe yana kaɗa leɓe tare da saka harshe ya kashe wuƙar dake hannunsa "Zafin nake ji a zuciyata zan yi ɓarna, zan sha jini"

"Kamar wani maye? Shi Ali wali ɗin me ka yi masa ne?"

Mai dawa ya ja idanunsa ya lumshe ko yaya idan ya yi shiru sautin kuka biyu yaje ji a kunnen shi, tare da jiyo ƙarar wutar dake cinye jikin nata hakan ya saka baya iya runtsawa idan ba wani abu ya afa ba haukwata shi ake son yi. "Na yarda da kai Goje, ka ci amanata askira zan saka maka a maƙoshi" "Ni ɗan halak ne. Yanzu ya batun Manager ɗin? Ka santa ne na ji baka bashi amsa ba" jin ya yi shiru ya saka shi cewa

"Ko dai ka san Managern kamfanin?"

"Karka ka daman"

*****

Fiyya na zaune a saman gadonta tunda ta dawo take kwace tunani ne fal a cikin zuriyarta ga wani irin tsoro da bata taɓa jin shi ba, a karo na farko ta ji tana son sanin komai da komai na Kamfanin FS WORLD INVESTMENT COMPANY, da duk mutanen da suka saka hannun jari a ciki data rufe idanunta yatsun hannun take ganin da aka yanka aka zuba cikin leda sosai taga rubutu jikin ledar amma ta manta bata duba ba. Ta juya a hankali tana kallon wayarta kamar mai tunanin wani abu kuma sai ta ɗauki wayar tana dannawa numbersa ta kira aka danna line busy. Har zata ajjiye wayar sai ta ji an kira ta zubawa sunan idanun kafin ta ce.

"Ashraf..."

Kiran ta ɗaga ta kara a kunne ta yi shiru ta cikin wayar ya sauke numfashi da ƙyar muryarsa a hankali.

"Na ji tsoro Fiyya" ta ɗan tura bakinta gaba kamar yana kallonta muryarta mai daɗi ta ce "He said he was scared" ya ƙara fidda numfashi kamar tana gabansa "Maama kina wahalar dani da kika zaɓi aikin nan na kusa mutuwa, na ji ba zan iya barin ki ba kuma ke ce dai wacce nake so Fiyyar nan tawa"

"Ba na ce ka daina ce mini Maama, why not Fiyya kawai?" Kamar mai raɗa a hankali Ashraf ya ce "I am sorry bestie me"

Dum! Haka ta ji kan ta ya yi masifar sarawa da sauri ta dafe kan nata tana jin kamar wani abu na janta a gigice cikin faɗa ta ce "Karka sake kira na da wannan sunan" ta cikin wayar ya ce "Ba zan sake ba amma lafiya kike? Yanzu kike mini magana cikin soyayya Fiyya me ya sa sometimes kike abu kamar bake ba? Are You okay?"

"Kai na ke ciwo"

Tana cewa haka ta kashe kiran ta cillar da wayar nata zuwa gefe guda. Da sauri ta miƙe babu ko hula a kan gashinta yana tashi sama tana dafe da kanta bata ganin ko gabanta duhu ne a cikin idanunta haka ta dinga sauka akan matattakalar benen. Karo ta yi da mutum cikin sauri ta kama hannunsa tana ɗorawa a kanta "Yaya J kai na zai cire wani abu nake ji, ciwo yake mini kamar ana jana" gabaɗaya ta rikice ta ƙanƙame shi har zufa ke tsattsafo mata.

Kama hannunta ya yi ya jata saman kujera taƙi sakin shi ya zauna a hankali tare da zaunar da ita ta yi saurin ɗora kanta a cinyarsa ya riƙe mata kan yana murza goshinta nata very careful kar ta ji zafi. Sun jima kana ta shiga sauke ajjiyar zuciya numfashinta na sauka ya ɗan leƙa fuskantarta yaga bacci take ya saka hannu ya juyo da fuskarsa yana zuba mata idanu ya riƙe hannunta har lokacin bai ce komai ba.

"Aliyu"

Da sauri ya saki hannun nata yana zame ta ya miƙe tsaye Ummi ta kalli Fiyya ta kalle shi ta ce "Ita kuma lafiya take bacci a nan? Yaushe ta shigo gidan ai lokacin tashi bai ba?" Captain dai ya yi shiru ta juya ta kalle shi sosai ta ce

"Lafiya take?"

"Ban sani ba"

"To ya naga kana haɗe rai duka zaka kawo mini me kai komai naka babu walwala Aliyu ka dubi girman Allah ka dinga murmushi shifa yin murmushi sunna ne ta ma'aiki" ya shafa kan shi yana zuba hannu a aljihu cikin gaskiyarsa ya ce "Ban iya ba wallahi Ummi ki koyan"

"Shi murmushin? Allah ya rufa asiri to wannan matarka ta shiga uku" yana dai tsaye bai ce komai ba. "Maama?"

"Ummi"

"Maama ta shi yammaci za ki yi ƙunci ko ciwon kai idan kikai bacci" ta buɗe fararen idanunta suka haɗa idanu ta sha kunu sosai tana tura baki ya zabga mata uwar harara ta yi baya zata koma baccin.

"Kee" ya kira sunanta ta buɗe idanu "Tashi kafin na yi balle da wannan silar ƙafafuwan" miƙewa tsaye ta yi ta murguɗa masa baki bata ce komai ba shi kuma ya yi kamar zai juya ya damƙo hannunta ta ƙwalla ihu daidai nan Daddy ya shigo parlon cikin sauri ya sake ta.

"Da kyau Soja gwara ka nuna ƙarfinka akan ɗiyata, yanzu zaka tattara ka koma inda ka fito"

Captain ya juya ya bar parlon gabaɗaya yarinyar haushi take bashi har zuciyarsa. Daddy ya kalli Fiyya ya ce "Maama, yaushe za ki girma ina ganin wawtar wanda ya ɗauki muƙa min Manager ya ba ki wallahi"

"Daddy kune kuke raina ni wallahi, na girma am matured enough" ya girgiza kai kawai kasancewar t.v. na kunne aka fara karato taƙaitattun labarai. Sunan Scorpio aka fara ambata matsayin wanda jami'an tsaro na hukumar FID Federal investigation department suke nema idanu rufe. Dake t.v a hankali ta juya ta kalli mai karanto labaran matashin ɗan jarida dake aiki a gidan t.v na VOA juyawa ta yi ta ce "Daddy ɗan bani aron wayarka"

"Ki yi me da ita?"

"Wayata zan kira, ina son fita ne wajan Kinal" ya miƙa mata wayar ta ɗan jim tana ɗaga hannunta tare da copy na wasu numbersa sai kuma ta miƙa masa bayan ta yi deleting tana murmushi "La la la na tuna inda na sata"

Ya kalli t.v ya kalleta ya kuma kalli wayarsa, ya dai amsa a ransa yana mai jin tsoro da mamakin kaifin tunanin Maama. Ummi kuma ta ce "Ayi ta neman mutum kamar kiyashi shi kuma ya rasa sunan da zai sawa kan shi sai kunama?" Daddy bai yi magana ba Ummi da abin ke ta cinta ta kalli Fiyya dake shirin haurawa sama ta ce "Maama ta shi me ya yi ne?"

"Ummi ina zan sani, idan kika ɗauke yadda ake juya biyar ta zama goma ba abin da Fiyya ta sani" tana cewa haka ta haura cikin sauri tana nanata numbersa dake kanta cikin sauri ta yi wanka ta shirya cikin abaya ta yi rolling tare da fesa turare sauri-sauri take a haka ta sakko hannunta riƙe da waya ko jaka bata ɗauka ba. Daddy ya dube ta ya kalli lokaci "Wai zuwa wajan Kinal baya tashi sai yamma? Ita Kinal ɗin nan ta dinga zuwa mana zai fi"

"Daddy ba jimawa zan yi ba, na jima ban je ba mun gaisa ba"

"Maama bani da nutsuwa haka kawai idan kika fita gari ya hargitse bani number Kinal ɗin nan na kira ta" kafin ta yi magana J ya yi saurin ƙwace wayar Fiyya ya ce "Bari na kira maka ita Daddy" babu sunan Kinal a jerin wanda ta yi waya dasu yau cikin sauri ta amsa ta ce "Number Kinal a kashe yaje fa J wai ni yarinya ce na san yadda zan kare kai na no body can come and hit me" Ta kalli Daddy da Ummi ta juya ta kalli J ta ce "To tsoran na mene ni Safiyya A Marafa?"

"Allah Ya tsare Maama jeki" amsawa ta yi da amin ta raɗawa J kunne "J akwai gulma yau bari na je na dawo" tana fita harabar gidan mota ta shiga ta yi mata key cikin nutsuwa dake driving har ta fita ganin ta hau kan titi ta dubi bayan motarta ta cikin gilas wata ajjiyar ta sauke mau nauyi ta rufe idanunta ta buɗe sai kuma ta ɗauke hanyar ta nufi wani titin daban a zuciyarta addu'a take yi sosai.

*****

Eng Ali wali na zaune a parlo cikin wani gidansa da yake ganawa da yan siyasa masu mara masa baya a kujerar shi. Ya dubi CSP chief Superintendent of Police ya ce "Ina son ku ɗauke idanunku akan yarana, ko me kuke buƙata zan baku idan ɓarna sukai zan ji da komai" Csp ya ce "Hon yaushe za mu cigaba da zuba idanu yan dabarka suna yin yadda su kaga dama a garin nan musamman a unguwar Birget gashi lamarin na shirin haddasa faɗa tsakanin yan cikin gari da su yan Birget, mu jami'ai ne mun san gaskiya muke take ta"

"Ku cigaba da takewar su wannan yaran suna da wa'adi dana samu na ci zaɓe ko inuwata babu mai gani a cikin su. Don haka ku rufe idanunku a toshe kunnuwa, zuwa gaba har matsayi zan saka a ƙara maka mu yi yan dabaru" CSP ya jinjina kai Eng Ali wali ya ɗakko kuɗi mai yawa ya miƙa masa yana cewa "Idan kun kama masu dilar ƙwayoyi da kayan maye na san ana miƙa su hannun NDLEA ko? Ka tabbatar ƙwayoyin na zuwa wajan Jafar shi kuma zai bawa yarana, kar ka sake sunana ya fito daman ai yayan asara ne ko an kama su ba za su taɓa furta ni suke yi wa aiki ba, lastly magana akan Scorpio ɗin nan yana neman bani ciwon kai bana son ya zama damuwata, idan F.i.d suka riga ku kama shi akwai matsala"

"Karka damu hon mun zuba yaran mu ta ko'ina"

Eng Ali wali ya ce "Lallai Scorpio ya zo hannu kafin zaɓe"

Cikin sauri Fiyya ta fito daga cikin motarta tana shiga cikin wajan data zo a reception ta tsaya na wasu mintina tana zaune ta fito tana murmushi ta ce "Ikon Allah kamar tare kuke?" Fiyya ta buɗe idanunta sosai ta ce

"Wa?"

"Captain yayanki"

Gabanta ya faɗi ta kasa cewa komai Kinal ta zauna ta ce "Wallahi zuwan shi biyu fa, nima dai na yi mamaki amma ya ce aiki yake dubawa shi ne ya leƙo mu gaisa har ma na tambaye shi ke sai bai bani amsa. Amarya ya kike ya sabgogi"

"Good. Yanzu lokacin ku ne Kinal siyasa ta matso ana ta fama da habaice-habaice"

"Kamarya habaici?"

Fiyya ta cire gilas ɗin idanunta ta ce "babu abin da mawaƙa suka iya sai habaici wallahi ku zagi wanda kuke so kuma ku yabi wanda ku kaga dama" Kinal ta yi murmushi ta ce "A'a ni ba ruwana idan an kira ni dai waƙa ina yi amma ai ni ta soyayya nake yi tunda a nan na fi kauri, ina nan ina shirya miki ke da Ashraf" Fiyya ta sauke numfashi ta ce

"Ina cikin matsala Kinal ban so faɗawa kowa ba wallahi"

"Subuhanallahi matsala wacce kuma? A kamfanin ko gida ko wani wajan?"

"Kema kin san a gida ba wanda zai mini komai sai mai baƙin halin nan, tunda ya dawo ya uzzura mini ko parlo bana fitowa mutum sai baƙar zuciya ɗan wahala kawai aikin kawai" Kinal dai ta zuba mata idanu kafin ta ce "Mene damuwar?"

"Kwana biyu da suka shige ana bibiyata kullum idan na fita, harta nan wajan da na zo sai da aka biyo ni, ni ba damuwata kai na ina tsoron su Daddy su sani kin san abu idan ya same ni tashin hankali suke shiga. Kinal ban san su waye ba me kuma suke buƙata saboda bani da issues akan kowa wallahi na ji kawai ina son sanin wanda ke following nawa duk inda na je gwara mu yi fito na fito da shi, da na ce ko na yi hayar ƴan daba nima suna take mini baya?" Kinal ta buɗe idanunta sosai ta ce "Daman na fara zargin kina da taɓin hankali Fiyya, ke yanzu ina kika san inda ƴan daba suke bare ki je? Bakya tsoro ko shakka ai matsalarki police ne wannan ina ganin a gayawa Captain kawai" tsaki Fiyya ta yi tana miƙewa tsaye "gwara duk abin da zai same ni ya zaman da dai na faɗawa Captain ni ina da abin yi" "Ƴan daban za ki yi haya yanzu kenan?"

"E" sai kuma ta koma ta zauna cikin nutsuwa ta kalli Kinal ta ce "Akwai abubuwan da bana ganewa kwana biyu kamfaninmu ina son na yi bincike duk abin da na samu ba daidai ba wallahi sai na kaiwa hukuma Kinal yatsun hannun mutum na gani a cikin kamfanin fa?" Kinal ta zare idanu waje ta ce "A'a ki fara samun mai kamfanin ku yi magana dashi tunda ke ce Manager" "Sai yanzu na fara tunani, i wonder aka bani Manager a kamfanina bayan akwai maza da yawa sosai da na yi tunanin ko experience ɗina ne yanzu kawai na ji ina zargi"

"Zargin me?"

Ta ɗaga kafaɗa ta ce "I don't know, na fara bincike dole zan gano gaskiya" Kinal ta ce "To ki bi a hankali Please Fiyya we care about you ni ma zani anniversary na makarantarmu FGC dana shigo Kamfanin gobe, har waƙa na yi mana yanzu haka wani Eng Ali wali na yi wa waƙar da aka saka ni" shiru Fiyya ta yi tana nanata sunan FGC a ranta "Na ji kamar na san makarantar nan fa"

"Ke da ba ita kika yi ba ina za ki sami, ni a can na yi secondary school kinga"

"Haka ne bari na je"

"To ki kula Please kar ki saka kan ki cikin matsala don Allah Fiyya" murmushi kawai Fiyya ta yi tana ficewa daga cikin studio ɗin.

*****

Kamar an cillo shi haka yaga Mai dawa ya faɗo masa cikin office ɗin nasa da yake tare da manyan mutane sosai tun kafin ya yi magana ya ce "Kowa zai iya tafiya" duk suka fice ya ɗaga kai ya kalli Mai dawa ya ce

"Ka daina zuwa ina nake ni zan dinga neman ka"

"Ka yi ƙarya"

"Ni nake maka ƙarya Mai dawa?" Ya wani haɗe fuska tamau fuskarsa ɗauke da sabon yankan da aka yi masa jiya har yanzu ba'a gyara ba. "Kai ai ba Malam Abdullahi bane da ba zan ce kana ƙarya ba"

Eng Ali wali ya jinjina kai ya ce "Me ya kawo ka yanzu? Har cikin office nawa"

"Ka saka ni aiki har biyu, da kamo maka ɗawar can da nemo Scorpio" ya shagiɗar da baki gefe ya yi fito wanda ya cika office ɗin sosai "Na je gidan asawanta jiya"

"Kana nufin gidan Abdu Marafa?" Ali wali ya ce yana miƙewa tsaye cike da tsoro Mai dawa ya ɗaga ƙafa ya ɗora a saman table ɗin gaban Ali wali "sharaɗin kawo maka ita barewar shi ne mallaka mini kamfanin FS WORLD INVESTMENT COMPANY, aikin Scorpio kuma ka saka cinnakunka cire hannu daga sabgar ka bar mini ni zan nemo maka shi, bana haɗa aiki da wasu"

Ali wali ya ce "Mene haɗina da kamfanin nan? Karka saka ni rigimar da tafi ƙarfina da ka san ma'anar abin da FS WORLD INVESTMENT COMPANY yake nufi ba zaka haɗa kan da shi ba, wannan Kamfanin ciwon idanu ne" Mai dawa ya ce "Ni Mutallab Tahhb ɗan babana Abdullahi da inkiya Mai dawa bana harin abu na haƙura, wannan kamfanin shi ne burina" Ali wali ya goge zufa ya ce "baka san kamfanin ba shi ya sa a ba ki yake maka wahalar faɗa ni Ali wali sabgar siyasa na sani na saka gaba, ka bar ni a haka ba zaka saka ni a masifa ba"

"Waye mai kamfanin?"

"Sannin hakan daidai yake da tunuwar asirin manyan mutane da dama, ka bar komai yadda ka sani" jinjina kai Mai dawa ya yi ya ce "Zan maka jahilanci ne, ka riƙe amana ka bi sharuɗan da na ce zan maka komai ni ɗan daba ne kai mai neman iko da muƙa mi ni na sare na kashe mu bauta maka shi ne. Batun kamfanin zan yi bincike da kai na, kar ka zama butu don wallahi sai na yi maka daƙiƙanci"

"In sha Allah, daga nan har bayan zan yi maka komai"

"Dar zan doƙa yanzu sai godiya"

Yana fita Eng Ali wali ya ɗauki waya ya kira Csp ya ce "Waye Mutallab yaron da ya fito daga wajan state cid kwanan nan bayan ya yi shekaru uku a wajan su" ta cikin wayar Csp ya ce "Sunan shi dai Mutallab ya kashe matarsa aka aka kama shi, daga baya kotu ta sake shi a zama na ƙarshe ba wanda ya san dalili" Ali wali ya kashe wayar yana sauke numfashi a fili ya ce "waye MUTALLAB?"

For more information

08164069385

WhatsApp only.

[1/7, 9:32 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

Page 7

Bright pens... 2nd batch

The door is open... Ga masu buƙatar ayi musu tallah. Na hango wasu ƙwailaye a conversation group da Mikiya writers 😛Maman Sayed ta ce a faɗa muku akwai maganin gargajiya cikin sati guda komai zai kankama haɗaɗɗan maganin da Fiyyar Ashraf ke amfani da su ta ce a baku numberta ba... 08063114606

Washegari da safe Fiyya na ƙoƙarin buɗe ƙofa ta fito da nufin zuwa office ya rigata buɗe ƙofar, kallo ɗaya ta yi masa ta ɗauke kan ta zuwa gefe a hankali kuma can ta ce "Ina kwana?" bai amsa ba sai cewa da ya yi "You told Abba za ki wajan wata, amma kin yi ƙarya ina kika je?" Manyan idanunta ta ɗago ta kalle shi ta ce "Ƙarya kuma?" Ya rufe ƙofar ya tsaya "Idan kina yi mini kamar ba ki gane ba, kwaɗa miki

mari zan yi maybe it will help you to understand it very well" ita mamakin shi take yi "Ni fa Manager ce business zai iya fitar dani ko'ina" ya buƈe mata manyan idanunsa sosai sai kuma ya ce "ina kika je" ta tura baki gaba sosai ta yi gefensa za ta shige ya saka hannu ya fisgota kafin ta yi motsi ya ƈago fuskarta ya wanka mata mari ƙwayar idanunsa tamkar zata fito waje yana ihu a saman kan ta ya ce "Idan na sake maimaita miki tambayar sai na tabbatar yatsun hannuna sun kwanta fuskarki"

"Sai dai ka kashe ni" ta yi maganar ko gezau gefen fuskarta ya yi jajur dakakkiyar zuciyarta kuma ya saka ta nuna ko a jikin ta, ƙasan zuciyarta kuma wani zafi da raƌaƌi take ji "ni kike cewa na kashe ki?" Hannu ta saka zata ƙwace nata hannu idanunta cikin nasa ba tsoro ta ce "Me kake so na yi maka? Ka shigo kana tambayata abin da ban sani ba, ka saka hannu ka mari fuskar da kullum nake shafa mata mayuka masu tsada, ni ka mara ban maka komai ba, tunda ka tsane ni ka kashe ni kawai" da ƙyar ta iya ƙare maganar saboda muryarta dake rawa Captain ya saka hannu ya sake ƈauke fuskar Fiyya da mari yana huci ya ƙara ƈaga hannu zai mare ta cikin sauri ya tsayar da hannun nasa ganin hancinta na fitar da jini sosai kuma yaƙi tsayawa.

Ta yi masa ƙuri da idanunta da ruwa ya kwanta a ciki, jinin kuma bai fasa zuba ba daidai nan aka buƈe ƙofar tare da shigowa ciki da sauri Fiyya ta nufi wajan Daddy ta riƙe shi tana fashewa da kukan dake cin ran ta jikinta har wani irin rawa yake yi da ɓari jinin dake fita a hancinta kuma ya shiga ɓata masa farar rigar jikinsa. Daddy ya juya ya kalli Captain daya haƈe fuskarsa "Aliyu me ka yi mata?"

"Ni kuma?" Ya tambayi daddy irin bai ma san me ya faru ba "To ita da waye haka ji bi yadda take kuka hancinta na jini kuma kai na gani a ƈakin, dole kasan mene ya faru" cikin damuwa daddy ya yi maganar wacce sai da ta bayyana saman fuskarsa ya ƈago Fiyya yana duban ta sosai ya ƙara kallon Captain

"Maama wannan jinin fa? Daman kina yin haɓo ne wani abun Aliyu ya yi miki?" Ita dai Fiyya taƙi cewa komai sai shasshеƙar kuka take yi numfashinta na yin sama, Daddy duk ya rikice baya wasa da al'amarin daya shafi Maama ko kaƌan a ƙasan zuciyarsa yake jin soyayyarta ya kuma tabbatar ita ce rauninsa Fiyya kawai za a taɓa a iya nakasta rayuwarsa. "Ya isa daina kukan haka nan, Allah Ya nuna mini sati mai kamawa ki tafi gidan mijinki ni ma zan fi samun nutsuwa da hakan zan fi samu nutsuwa idan kikai auren nan Safiyyerh"

"I love you daddy" Fiyya ta ce a hankali tana rungume daddy ya shafa kan ta cike da soyayya "daddy love Safiyyerh" tuni Captain ya fice daga cikin parlon. Anty Turai da zuwan ta gidan kenan ta ce "Ikon Allah. Yaya kai ne kake ɗaurewar yarinyar nan gindi wallahi ka lalata da soyayya take yin abin data ga dama, ko Aliyu baka tambaya abin da ta yi masa ba ta wannan figaggiyar yarinyar kake"

"Fita daga ɗakin nan Turai" rai ɓace Anty Turai ta fice tana zabgawa Fiyya harara ranta duk a ɓace. Daddy ya kalli Fiyya sosai kamar zai yi magana sai kuma ya ce "jeki wanke fuskarki I'll drop you"

"Daddy daman i missed your drive wallahi" murmushi ya yi mata a duk santa zai kalli Fiyya sai gabansa ya faɗi ya juya a hankali ya dubi picture ɗinta dake gaban madubi sanye da kayan graduation ta yi wani kyakkyawan murmushi ta rungume hannunta tana kallon gefe guda. Ya ƙarasa ya ɗauki photon ya shafa a hankali "Maama na ni kamar na yi ba daidai ba, bani da wani zaɓi ne i am sorry Safiyyerh Abdu Marafa" ya lumshe idanu ya buɗe a kan photon "kina tunanin kin yi girman da za ki iya kula da kan ki, ki kuma yankewa kan ki hukunci? Maama ba kin san komai ba a rayuwa you're nothing but a stubborn girl"

Ya ajjiya photon ya ɗauki wayarta babu wani password a kai dudduba abu ya fara a nutse yana yi yana kallon ƙofar bandaki can ya sauke ajjiyar zuciya ya ajjiyar wayar daidai nan ta fito. Ya yi waje yana "Ki same ni a ƙasa"

Suna tafe a hanya daddy na driving a nutse ta ce "Daddy" bai kalleta ba yana dai sauraren ta domin program ɗin da ake yi da Eng Ali wali a redio shi ne ya ɗauke masa hankali. "Zan raka Kinal FGC"

Wani burki ya ja a kusan tsakiyar titin Fiyya ta dafe kai tana "Subuhanallahi"

"Mene haɗin ki da FGC Maama?"

"Daddy Kinal zan raka suna yin taro na makarantar zan bita idan na tashi aiki" zufa har fitowa daddy take a saman goshi sunan FGC ba ƙaramin gigita masa lissafi ya yi ba. "ba za ki ba" shagwaɓe fuska ta yi "don Allah daddy wallahi na ji ina son zuwa"

"Wallahi mistakenly kika je shegiyar makarantar nan sai ranki ya ɓaci kuma sai kin daina fita hatta aikin sai kin ajjiye. Wallahi Safiyyerh Abdu Marafa idan kika je za ki san waye Abdu sai na zane miki jiki da carbi ko bulala" ta yi ƙasa da kanta zuciyarta duk babu daɗi idanunta na cika da hawaye tun tana ƙarama take yin biyaya a komai akan abin da ya yi crossing da buƙatar daddy.

Hannunta riƙe da jakarta ɗaya hannun wayarta data kara a kunne suna magana da Kinal, duguwa ce hakan yasa bata fiya saka takalmi mai tsayi ba suit ce jikinta as always fara tas mai riga da wando ta yi rolling da black ɗin mayafi idanunta sanye cikin wani shade glasses mai kyau a hankali take tafiya tana ɗan jinjinawa mutanen kamfanin kai with so much respect tana da girmama mutane kawai rainin hankali ne bata ɗauka "Kinal ki je kawai idan na koma gida za mu yi magana, daddy ya hana" yadda ta yi furucin ya bayyana ainihin abin da take jin a zuciyarta.

"To shikenan nima na zo studio ne zan yi waƙa idan na koma gida zan shirya za mu yi video call na nuna miki cikin FGC ɗin" Fiyya ta ɗan taɓe baki daidai lokacin da take isa bakin ƙofar office nata security ya matsa ta buɗe ta shiga ta buɗe idanu ganin Ashraf zaune a office ɗin "Kinal mu yi magana anjima" ta cire wayar tana kallon Ashraf daya miƙe tsaye yana mata murmushi

"Kuma da permission ɗin wa ka shigo?"

"Wake neman permission idan ana batun ganin mata, na zo ganin matata ne" ta ajjiye jakar hannunta tana zama saman duguwar kujera "Sannu mai mata" ya miƙe ya dawo kan kujerar yana leƙa fuskarta

"Miji ɗaya gare ki a duniya kuma nine" cikin wasa ta ce "Ai kowa ba zan aure ka don ka ji"

"Funny Fiyya" a yanayinta na rashin damuwa da soyayyar ta ce "How are you?" Yana kallonta yana ji wani abu sosai game da ita "Fiyya na yi kuskure wallahi bana sanin ina shige limit ɗina sai na yi wani abu. Ni na san ba wani sona kike ba amma idan kika yi haƙuri watarana za ki ji son nan ko yaya ne kullum kina ƙara nesanta kan ki dani yayinta zuciyata ke ƙara kusanto kanta gare ki. Komai da lokacin shi idan mukai aure muka rayuwa inuwa guda I'll definitely be honest to you, ina jin

kishin ki a ƙirjina ne a nan nake ji kina mini motsi Fiyya" ya nuna ƙirjinsa saitin zuciyarsa sai ya ɗan juya gwanin tausayi

"Amma bakya so na"

"Who told you that?"

Ashraf ya buɗe idanunsa "When are you gonna tell me you love me?" Tana kallon shi tana murmushi ita tana son shi sosai kawai bata san ya zata nuna bane sometimes rigimarsa ke sawa ta bijire itama ta miƙe tsaye tana danna kiran number messenger bayan ya ɗaga ta ce "Call Md for me, ka kira mini Md da Secretary hadda accouter" ta ajjiye ta ce ta haɗa shayi a cup guda biyu ta saka cokali tana miƙawa Ashraf ɗaya idanunta cikin nasa ta ce "San da aka kai ni gidanka matsayin mata" ya lumshe idanu ya buɗe

"I'll wait as far as you're with me. Abin da kawai nake buƙata shine ki so ni. Ki so ni ko da kaɗan cikin yadda nake sonki ne"

*****

Anty Hameeda na sunkuye a madaidaicin parlon gidanta tana duba jarkokin lemon ginger ɗin da take siyarwa ta ji hucin mutum da sauri ta miƙe sai kuma ta yi baya a razane ganinsa tsaye a gabanta yana waige-waige kamar wanda aka biyo ga wani irin yanka a ƙarƙashin wuyansa da alama yanzu akai masa jini ja zuba, ya yi zuru-zuru sai huci yake yi naman jikinsa musamman na ƙirjinsa na motsawa "Ɗan autan Ammo wannan hucin fa kamar an biyoka wani abun ka yi? Wane ya yanke ka haka me ka yi masa?" Bai kula ta ba ya juya ta bi bayan shi kitchen taga ya nufa ba jimawa ya fito da kwanon abinci daidai nan wata mata ta fito tana ganin Mai dawa ta yi saurin sakin butar hannunta ta ce

"Wannan tantirin ƙanin naki uban ne ya zo yi mana a gida? Yaushe ma aka sake shi innalillahi wa'inna ilaihirraji'un mugun ji da mugun gani Ubangiji ya kare Allah wadaran yɜan daba ya tsine musu albarka ya saka su fita a cikin ajalin su" matar ta faɗa hawaye ya cika idanun Anty Hameeda ta ce "Baba ina laifin ki ce Allah ya shirya ɗa fa na kowa ne bawa kuma sai me shi, ciki ne mai haife-haife baka san me

Ubangiji ya ɓoye ba suma fa ƙaddara ce ba wanda ya zaɓi yadda rayuwarsa zata kasance"

"Ai duk wani ɗan daba ƙarshe wulaƙantacciyar mutuwa ce ko idan sun sha ta faɗa musu babu daɗi su kashe kan su, ko kuma su haukace garin shaye-shaye ko garin faɗan daban su a kashe su. Allah wadai" Moh dai bai yi magana ba abinci kawai yake ci hannunsa ko wankewa bai ba duk jini Anty Hameeda ta shige ɗaki bayan ta share hawayen idanunta lemo ta ɗakko masa da ruwa ta ajjiye tana kallon yadda kusan rabin fuskarsa ya yi tabo da yanka yaro ba ya kalle shi ihu zai yi ba annuri a fuskar nan. Duk yawan abincin ya cinye ta sha ruwa ya shanye lemon tas "Na Ammo yanzu kana jin abin da ka zaɓawa rayuwarka shine daidai ka ji tausayin mu don girman Allah. Wallahi daka kasance cikin wannan rayuwar gwara ka dinga aikata abubuwan da kake a baya, jibi yadda ka yi muni ka zama ƙazami sai warin dauɗa kake yi. Na je gida sun ce sun fi sati uku ko gilmawar ka basa gani wai malam aure zai ƙara kuma da ƙyar idan ba Ammo zai saka ba, na rasa wake bashi kuɗi ya fi son ya yi ta auri saki ana haifa masa yara yana kasa kulawa da tarbiyyar su"

Tamkar bada shi take ba haka ya yi ko gezau can ya miƙe tsaye ta ciro kuɗi dubu ɗaya ta bashi ya kalle ta ya kalli kuɗin idanun nasa a rine kamar gauta yaƙi amsar kuɗi ganin inda ya nufa hannunsa riƙe da wuƙa ya saka Anty Hameeda ihu ta ce

"Me za ka yi ka rufa mini asiri kar ka kashe mini aure na shiga uku" ko kallon ta bai yi ba, ya ɗaga labulan ɗakin Baba tana sujjada ya same ta. Tsartuwa ya yi ya fito da kunama ya cilla mata a cikin hijabi kafin ta ankare ta ɗago jin abu na bin bayanta kamar kunamar tsafi ta shige mata riga ya zaro askira ya daidaici ɗuwawunta ya lafta mana wani uban yanka, baba ta saki ihu tana ta shiga uku ya yi saurin fita askirar na zubar da jini da.

Yana fita su spider suka rufa masa baya. A cikin wani kango ya kwanta ya yi shiru cikinsa zafi saboda faɗan da sukai da ɣan cikin gari akan fita wajan kamfel da sukai kilashin. Ya rufe idanu zuciyarsa na buɗewa wani irin ɗaci yake ji a cikin maƙoshinsa wani a ya tokare masa kamar yanzu komai ke faruwa haka yaga magic ɗin idanunsa ke hasko masa bidiyon komai ta ciki inda take tsaye.

Yana zaune a gida a lokacin yana jin yadda karatun Almajirai ya cika masa kunne ya yi kicin-kicin da fuska. Ammo ta kalle shi ta ce "Yau kuma waya taɓa jarumin

Ammo?" Ya yi mata shiru don bai fiya cewa komai ba idan ran shi ya ɓaci kafin ta sake magana wani yaro ya yi sallama ya ce "Wai bestie ya zo in ji bestie"

"Waye bestie? Injiwa jeka tambayo"

Mutallab a lokacin bai motsa ba ya hakimce kamar sarki kansa a ƙasa yaron ya dawo ya ce "Wai in ji Safiyyerh matar Mutallab bestie"

Baki buɗe Ammo ke kallon Mutallab ta ce "Na Ammo yaushe ka yi aure bani da labari yau naga abin da ya fi ƙarfina, yara ƙananu daku wacece Safiyya" ya miƙe tsaye daga shi sai gajeren wando ta wata riga ƙarama "ban san ta ba"

"Ikon Allah"

Fita ya yi yana shan kunu ganinta tsaye suna haɗa idanu ta yi ƙasa da kan ta. Ya dinga kallon ta yana jiran ya ji mene "meye ne?" Ya tambaya.

Hawaye ya gani a idanunta fal "Ni a gidanku zan kwana" tar ya gama buɗe shanyayyun idanunsa a kanta "wanne gidan?" Ta nuna masa gidan "sai ki ce ke wa?" Tana masa shagwaɓa wacce daman ya san hali

"Matar Mutallab, baka zo makaranta ba yau ba kyau fashi" da wani irin ƙarfi ya ce "Safiyyerh!" Gani an yi kanta.

*** “Safiyyerh” ya ƙwalla kiran sunanta yana zabura kamar yanzu ne abin ke faruwa jikinsa duk rawa yake ganinsa shi kaɗai a kangon ya saka ya kifa kansa zuciyarsa na wani irin tsalle tana huci jijiyin kansa sun fito sun yi kwance saman kan shi. Ƙwayar Rohypnol ya ɓalle ya haɗiye har huɗu ya yi shiru jikinsa ya yi weak yana ganin kangon na jujjuya masa lokacin gudu yadda idanunsa suka gane masa cikin jini kwance saman gado ya sake faɗo masa, ya dinga jujjuya kansa ƙwaƙwalwarsa ta tsaya cak kamar wacce ta yi hooking da sauri ya zaro takardar daga cikin aljihu tsoron ƙara kalla yake ya yi saurin damƙe ta cikin hannunsa sai kuma Ammo ta faɗo

masa a rai bai damu da jinin dake fita a wuyansa ba ya yi kwance a ƙasa shi kaɗai kamar maraya.

Yammaci liƙis yana zaune gaban ta, ya kalleta a karo na farko ya ce "Me ya sa kika buƙaci na ce ina son company?" Abbasa ta ajjiye abin hannunta ta kalli cikin bukkar ta ce "Sanda ka faɗa mini waye Mutallab, ka bani labarinka zan faɗa maka hujjata tare da dalilin cewa ka cewa Ali wali kana son kamfanin FS WORLD INVESTMENT COMPANY"

"Bakya tsoro na kashe ki?" Ta dube shi ta saka hannu tana goge masa wajan ciwon "ba zaka iya kashe ni ba babu abin da zaka iya yi wa Abbasa. Ya batun zama mata mazan? Mene dalilin daya saka kake so ka zama?"

"Bana son haɗa danganta da kowacce kurciyya, ba idan aka yi baru aure kenan ana wani abu ba, to bana so ba wacce za ta yi sha'awar zama dani mata uku kenan babu su saboda ni ki mayar dani mata mazan" "baka watarana zaka iya buƙatar lafiya ko kasancewa da mace"

"Sai godiya kafin lokacin na cika muradaina na baza ƙiyama ki mayar dani" ta dinga kallon shi ta ce "Ka tabbata ka yi tunani"

"Ki aikata kawai"

"An gama, riƙe wannan" abu ta bashi ya amsa ya sha ba jimawa bacci ya ɗauke shi. Bai san lokacin daya shafe ba sai farkawa ya yi ya gan shi an wanke masa ciwon an saka audiga ya yi shiru yana jin he just missed something very important.

Message ɗin Eng Ali wali ya gani kan yana son ganinsa da gaggawa ya tura masa address ɗin wajan. Mai dawa na tsaye yana kallon Eng Ali wali da ya yi badda kama ya zame facemask ɗin fuskarsa yana kallon Mai dawa ya ce "Mai dawa" bai magana ba sai fito yake yi.

"Abdu Marafa ya shiga gidan rediyo yau da safe ya sake jaddada ra'ayinsa akan ƙin takara ta yana kuma janyo hankalin matasa da su farka a daina amfani da su, domin yanzu matasa sunw siyasar wannan mazanin. Gwara youth su haɗa ƙungiya suna fitar da wanda suke ganin ya cancanta ya zana shugaba ba irina ni Eng Ali wali ba. Mutallab a fara shirin ɗakko yarinyar nan yadda zamu saka harshen Abdu Marafa ya yi laushi dole zai kawo kasa ya yi mubaya'a a gare ni Eng Ali wali" Mutallab dai ya yi shiru abin shi.

"Mutallab ina magana ka yi shiru?"

"Yau kake so a kawo ta ko gobe? Kai yanzu tukun mene ra'ayin naka akan matasa?"

"Bangane ba"

"Ka gane mana, ka zama ɗan halak cikin gyatuma idan ka ƙi cika mini alƙawari bayan cin zaɓe zan maka jahilci. Jinin malam Abdullahi ke guna a jikina idan na so dole na janyo maka farinjini amma na daina wannan sabgar yanzu. Na rantse da ɗan Amina ka yi mini ba daidai ba za kaga ba daidai ba ɗan malam nake ka daina ganina haka" Ali wali yace

"Ai kai ƙanina ne, amma waye kai? Zan so jin tarihinka ka faɗa mini waye kai Mutallab?" Nan da nan Mutallab ya sake haɗe fuska tamau ya yi shiru. "Shikenan zan maka komai ka tabbatar ka sato mini yarinyar nan babu lokaci ban san me Hon Maɗatai yake shiryawar ba amma shirun da ya yi yana nufin komai. Sai batun nemo Scorpion"

"Zan tafi zan aiko Mangal anjima" yana faɗin hakan ya fice kamar walƙiya.

Kwana biyu da faruwar abin da Captain ya yi bata ta ɗauke walwala daga gidan kodayaushe tana sama, tun lokacin bata sake jin motsin shi ba. Abubuwa da yawa ke damunta yadda ciwon kai ke damunta tana jin kamar ana jona mata wani abu, bata iya bacci. Ga matsalar kamfani da kullum manyan kuɗaɗe ke shigowa cikin asoson kamfanin an rasa daga ina? Ta yi duk binciken daya kamata ta kasa gano bakin zare masu gadi sun tabbatar mata da cikin dare manyan motoci na zarya a kamfanin hakan ya saka ta ɗauki niyyar dole yau zata saci hanya ko wajan ƙarfe ɗaya na dare ta fita tana jin hakƙin kula da kamfanin yana kanta ne. Ta ƙara adding

number cikin jerin numbersa ɗin abubuwan da take buƙatar sanin abu kai ma'ana hadda hujjar daddy na hanata yin wasu abubuwan. Miƙewa ta yi tare da yin wanka ta tare da alwala ta gabatar da sallar issha ta yi addu'a sosai da azkar wanda ke sanya mata nutsuwa tare da kusantata ga Ubangiji. Fiyya ta dinga kallon kanta cikin madubi sometimes tana jin kamar ba ita ba, she missed the old Safiyyerh. Buɗe ƙofar akai tare da shigowa

"Zaman ɗaki manager ta fara kenan?" Murmushi kawai ta yi tana juyawa ta saka hijabi

"Yaya J, how are you?" Ya yi murmushi

"Nothing without manager, ki fito daddy na kira an kawo invitation card" ta haɗe fuska ya yi baya yana ɗaga hannu ya ce "cut me out Fiyya da kan shi ya saka akai yi komai" "wai dole sai an yi mini aure ko me daddy ke tsoro?"

Shiru J ya yi sukai waje ta samu Dr Hash zaune ta ce "Dr good day, ina gefen kan mutum na ciwo yana ganin reflection na wasu abubuwa what was the problem?"

Dr Hash ya ɗago kai haka J da kuma Marafa Ummi ma kallo Safiyyerh take daddy na zaune yana ji bai ɗago ba. Ta buɗe musu manyan idanunta Dr Hash ya ce "Me kike gani?" Kawai ta haɗe fuska ta ce "babu" wajan daddy ta ƙarasa ta durƙusa har ƙasa ta kashe shi ya miƙo mata waya Ummi ta ce "Ki zaɓi furnitures ɗin da kike so" ta yi sak tana kallon su dai daddy ya Aman wayar ya ce "Babu buƙata, zuciyata ta kasa nutsuwa zan yi requesting da an ɗaura auren kawai Ashraf ya bar ƙasar dake" da sauri ta kalli daddy "Daddy aikina fa?" "Za ki bar aikin" ta girgiza kai ta ce "ba zan maka musu ba daddy kai mahaifina ne ina yin biyayya a komai, amma don girman Allah ka bar ni daddy akwai binciken da nake yi a kamfani da zarar na kammala zan je duk ƙasar da kake so idan ma ƙare rayuwata ne a can zan yi" daddy bai kulata ba ya miƙe ya bar wajan J yana jin babu daɗi Ummi ma ta yi shiru babu yadda za ta yi da daddy idan abu akan Maama ne sai dai a kalle shi ta jawo Fiyya jikinta ta dinga bata haƙuri tana kwantar mata da hankali, Fiyya ta rungume Ummi tana kuka. Kamar kullum J Kalla ne yake sanar da an samu gawar wani babban mutum mai suna Alhaji Haladu da aka shiga aka kashe har gidan shi ana kuma zargin Scorpion ne saboda shaidar daya bari na sunan Scorpion a jikin bango. Ta dinga kallon screen ɗin t.v sai kuma ta miƙe "kin ci abinci?" Ta girgiza kai "na ƙoshi an yi mini formatted folder a wayata Yaya J"

"Formatted kuma ko dai kin shiga wani wajan ne" ta ɗaga masa kafaɗa ranta duk a ɓaci. Kwanciya ta yi sukai waya da Ashraf yana ta mata maganganun masu daɗi har ta yi bacci.

**** Idanunta ya kalla muryarsa a hankali ya ce "There's something about you that make me feel like you actually use magic about me, many things I do because you, many things I don't even know or remembered when I started doing them. The love I have for you is so real baby. Yet, ban san me ya sa zuciyata take yawan bijiromin da kokwanton yiwuwar samunki a rayuwata ba. I love you Safiyyerh"

“I love you Safiyyerh”

A gigice ta farka daga baccin tana ihu da ƙanƙame pillow jikinta na rawa sosai da ɓari da sauri Daddy ya buɗe ƙofa ya shigo haka Ummi da Yaya J wajan karfe biyu na dare "Fiyya mene? Maama mene?" Ta sakko daga kan gadon a gigice ta nufi wajan daddy bakinta na rawa ta kama hannun daddy ta ce

"Mutallab daddy, Mutallab who is Mutallab?"

For more information akan littafin MUTALLAB. Via 08164069385

WhatsApp only

Na'ima Sulaiman Sarauta

Assalama alaikum

Hajiya muna da ingantaccen maganin gyaran nono wadda ya amsa sunansa magani

Maganinmu ingantaccen maganine da yake tada jijiyon nonon da suka saki y'ar uwa breast dinki ko yakai silifas saboda kwanciya kikai amfani dashi in sha Allah zakiga amfaninshi acikin 1week maganinmu powder ne yana ciko da breast y gyarasu

bashi da illa ajikin mutum munyi amfani da saiwoyi da magunguna gargajiya domin gyaran breast 08063114606 ina garin kano karki sanya y'ar uwa nono yana karawa mace martaba a gurin mai gida maganinmu kowa zai iya sha wadda zatai yaye ko gyara budurwa duk zasu iya sha breast dinki ya ciko yayi bull -bull

[1/7, 9:32 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

Page 8

Bright pens... 2nd batch

"Daddy na ji kamar gangar jikina ta wanzu da wannan mai sunan, na ji ƙirjina ya mini nauyi numfashina ya taɓa gauraya da nashi daddy ina jina kamar bani ba, daddy who is Safiyyerh? Daddy tell me something about me, don Allah wallahi zuciyata bugawa take i missed something very important... Daddy!"

Ganin duk sun yi mata shiru ya saka ta girgiza daddy da hannunta biyu "waye Mutallab daddy?" Duk suka sake yi mata shiru kamar basu fahimci me take nufi ba Dr Hash da bai jima da shigowa gidan ba saboda aikin kwana ya yi a asibiti ya nufi inda Fiyya take tsaye yana leƙa fuskarta ya ce "Mutallab kuma?" Ta kasa magana sai bin su take da idanu daddy ya yi namijin ƙoƙarin wajan kama kafaɗun Fiyya ya ce "Maama waye haka? Kinga irin abin da nake faɗa miki akan muhimmanci da ƙarfin addu'a kina sake da gaske kina wasa da azkar"

Sakin daddy ta yi ta nufi wajan Ummi ta ce "daddy na san ke za ki faɗa mini" nan ma Ummi ta kama hannun Fiyya ta ce "Mamaa ban san me kike nufi kowa kike magana akai ba, kamar mai iskokai ki farka kina surutai mene haka kike safiyyerh?" Da sauri ta saki Ummi ta nufi wajan Yaya J ganin ta nufu shi ya yi saurin juyawa ya fita da sauri yana dafe kan shi. Fiyya ta sake juyawa wajan daddy jikinta duka rawa yake da ɓari kamar mazari ta kama hannun daddy ta ɗora a saitin ƙirjinta idanunta na cika da hawaye bakinta na rawa da ƙyar ta ce

"Ni ban buƙaci sanin wani abu bayan hakan ba, ban ce dole na san wani abu ba ka yi mini alfarma ka faɗa mini waye shi waye Mutallab? Daddy please...!"

Kasa magana ta yi jin an tsira mata sirijin allura ta runtse idanunta ta saki daddy ta juya a hankali ta kalli Dr Hash ta sake nutsa ganinta cikin idanunsa ta kalli allurar hannunsa sai kuma ta yi murmushi ta sake juyawa ta kalli photon daddy dake gefen

gadonta "why? Me ya sa ake mini allura daddy i love you" sai kuma ta lumshe idanunta jikinta ya saki ta ji kanta ya mata nauyi tunaninta na ruɓanya gudun zuciyarta na ƙaruwa, kamar wacce ake yi wa updating haka take jin ƙwaƙwalwarta ganinta zata faɗi ya saka daddy ya riƙota ya jima bai ji tausayin abu ko wata halitta a duniya irin Fiyyarsa ya dinga kallon fuskarsa cike da so da ƙauna a hankali ya kwantar da ita saman gado ya ɗora kan ta a saman cinyarsa ya dubi Dr Hash ya ce

"Hashim ya zan yi da Fiyya ta fahimta me zan yi Hashim, Awais ya ya zan yi da Maama?" Ya faɗa yana kallon Marafa duk suka kasa magana Ummi idanunta ya yi jajur baccin da basu koma ba kenan sukai spending sauran lokacin wajan Fiyya sai addu'a yake yi mata. Dab da asuba ya miƙe ya fice daman shi ya yi saura ya kulle ƙofar.

Duk da nauyin da kanta ke mata bai hana ta motsa ba saboda kiran sallah wanda hakan alama ce ta cewa kai musulmi ne da zarar lokacin asuba ya yi dukkan wani rai a duniya daya kasance musulmi sai ya motsa, bakinta ɗauke da addu'a ta ce

"الحَمْدُ لله الذِي أحْيَانا بَعْدَ مَا أمَاتَنَا وإلَيْهِ النَشُور "

muryarta da ƙyar take fita a hankali ta ji an ɗan matsa hannunta, ta motsa yatsun hannun ta ji shi sarƙe dana wani ta rufe ido ta san cewa Yaya J "ni ka cika mini hannu"

Ya buɗe ido ganin yadda ta murguɗa masa baki bai motsa ba a hankali ya zare yatsun shi ganin tana ƙoƙarin juyo da fuska zuwa ina yake ya miƙa hannu da sauri ya kashe hasken ɗaki the same time ya miƙe ya fice yana rufe ƙofa ta bi door way ɗin da kallo.

****

Ammo na zaune a cikin ɗaki kamar yadda ta saba kodayaushe Malam ya ɗaga labule yana daga tsaye ya kalli Ammo ya ce "Ba dai tunanin wancan gantalallan kike ba? Kamar wacce aka ce na mutu kike takama ki yi ni ɗaki kwana ɗaki, to idan ma shine ki sawa zuciyarki ruwan sanyi da salama ki sallama shi, yanzu ke ba kifi samun nutsuwa ba da bakya ganin gilmawarsa yana saka miki faɗuwar gaba" ita dai bata tanka shi ba ta cigaba da aikin da take yi. Ya sake duban ta da kyau yana furta

"Aure zan ƙara na hango wata yar duma-dumar bazawara fara tas sakin wawa ku yanke shawara a cikin ku wa zan saka" a sanyaye ta ce "Allah ya sanya alheri, duk wacce ka saka babu komai ko ni ɗin ce"

Malam ya juya zai fita Anty Hameeda ta shigo idanunta zuru-zuru alamar ta yi kuka gaban malam ya faɗi ya ce "mene kuma Hameeda?"

"Malam wajanka na zo da Ammo don Allah ku saurare ni" ya yi jim sai kuma ya yi ɗakin Ammo ta bi bayansa gaishe su ta yi kafin cikin sanyin murya ta ce "Ammo ke uwa ce kin ɗauki cikin Mutallab watanni wajan 11 ɗaya yake zaune kafin ki haishe shi, kin ji zafi da raɗaɗin naƙida wajan haihuwarsa, kin shayar da shi kin goya shi a bayanki, kin bashi abinci, kin ƙaunaci Mutallab sai dai ƙaunar da yake miki kamar har ta ninka wacce kike masa, idan bashi da lafiya baya yadda kowa ya taɓa shi sai ke ban san yaushe ne ko yaya ne ya zama haka ba, labarin da nake da shi akan Mutallab ba cikakke bane, zamana a Lagos ya saka ban san wasu abubuwan ba, kin ƙi faɗa mini yadda ya zama haka kin hana a faɗa mini, shin bakya jin rauni irin na uwa? Ƙauna irin ta uwa da ɗanta, duka bakya jin hakan kike barranta kan ki da autanki Ammo, hannunka baya taɓa ruɓewa ka yanke ka yar kar ki manta kalmar da ake cewa idan ka ƙi naka duniya ta so shi, idan ka so naka duniya ta ƙi shi, Ammo ga duniya da bakin jama'a na rige-rige kai Mutallab kabari idan kyautata zaton watarana za a kashe shi ko ya je inda ba zai taɓa fitowa ba..,"

"Allahamdulilah da zai mutum ai da ya sawwaƙa mini da yɗan'sanda Mutallab masifa ya zame mini ni na gode Allah da bana ganinsa cikin idanuna" kallo malam kawai Anty Hameeda ke yi da ƙyar tana haɗiye abu mai ɗaci a maƙoshi ta ce

"Dukkan iyaye suna saka hannu cikin abin da ya fi gaban sanin mutane.Kowannen su yana ba da kaɗan daga jikinsa. Ta haka, abin da ya yi girma a cikin uwa ya zama mutum. Saboda haka, ba abin mamaki ba ne, sa’adda da aka haifi jariri, mutane sukan ce _mu’ujizar haihuwa_ , haƙiƙa, haihuwar yara ita ce hakƙin iyaye na farko. Da farko, jarirai suna dogara ƙwarai ga iyayensu, amma sa’adda da suke girma, suna buƙatar fiye da a mai da hankali ga abincinsu kawai. Suna bukatar taimako domin su yi girma a tunaninsu, a motsin rai, a ɗabi’a, da kuma a ruhaniya.

Domin su yi girma da kyau, yara musamman suna bukatar iyayensu su yi ƙaunarsu. Ko da yake yana da muhimmanci a furta kalami na ƙauna, ya kamata ayyuka su tokara hakan. Haƙiƙa, yara suna bukatar misali mai kyau daga iyayensu. Suna bukatar ja-gora a ɗabi’a, mizanai da za su bi a rayuwa. Kuma suna bukatar wannan tun suna ƙanƙanana zuwa gaba. Abubuwa masu ɓata rai suna iya faruwa kuma suna faruwa sa’adda da ba a taimaki yara ba har sai da ya makara" kukan da take dannewa ya ci ƙarfinta

"Ammo idan Malam bai fuskanta ba ki daure ki gane don girman Allah, shi kaɗai autanki ɗanki tilo ɗaya namiji da Allah Ya ba ki idan babu ranku shi ne zamu kira da sunan uba, zai mana walicci a ko'ina bai kyautu don ƙaddarar Ubangiji ta kitta a rayuwarsa ku ce za ku juya masa baya ko wofitar da rayuwarsa har haka ba, akwai hakƙin iyaye akan yara haka akwai hakƙin yara akan iyaye shin kina buƙatar Ubangiji ya tuhume ki da hakƙin Mutallab? Allah da kan shi cikin hadisi mai girma ya ce; yʻayʻanku amana ce kuma kiwo ne a gare ku, lallai za mu tambaye ku wannan amanar da kiwon idan an ce ki faɗi inda yake a yanzu ba za ki faɗa ba wannan abun da kuke kun bashi dama da lasisin ƙara lalacewa ne idan yaro ya ɗaƙko hanyar kangara jawo shi aje jiki a nuna masa ƙauna da soyayya"

Miƙewa ta yi tsaye tana share idanunta "ya zo mini jikinsa duk sara kamar korarre mara iyaye a duniyar nan har na yi na gama magana bai tanka wani kuskuren iyaye ke haddasa shi"

Tana kaiwa nan ta fice abin ta inda ta shige Inna Binta da Mama Zaituna na kokawa akan wani ƙanzon tuwon da aka baza ya bushe sai ya yi gwanin sha'awa tana ɓantara da kaiwa baki ta ce "eh, kya yi kya gama wannan ƙanzon sai na bawa Mufee ke ni fa akan abinci ba wani kirki gare ni ba, ba zan zauna yunwa ta yi ajalina a gidan nan ba, tunda mai gidan zuciyarsa a mace take bai san fus na hakƙin iyali ba sai auri saki da tare yara kamar yʻayʻan ɓeraye kowanne kana kallonsa yunwa zata fara maka sallama a jikinsa haba me ake da hali na..." Da sauri ta yi shiru ganin malam tsaye ta yi mamaki da bai tanka mata ba ya shige.

Safiyyerh ta sakko daga saman bene tana yi tana duba wayarta ganin saƙon da Ashraf ya tura mata cewa ya ɗan yi tafiya ba ta yi reply ba ta riƙe wayar. Yaya J ta gani zaune ta juya masa manyan idanunta da suka sake fitowa farare tas ta ce

"Office ɗin kenan?"

"Ina ni ina zuwa office banga yadda little sis ta farka daddy's favourite" ta girgiza kai tana ɗan murmushi iya leɓe ta ce "Yaya J kenan, good morning"

"Kin tashi lafiya sai ina?"

"Office, ina da meeting kuma Yaya J ka yi mini addu'a Please da wannan kyakkyawan harshen naka, zan baka labari mai daɗi" ya ware hannunsa ya ce

"To ina jira ko na kai ki office ɗin?" Ta girgiza kai ta juya tana nufar sashin daddy dake ƙasa. Fiyya tuni ta manta abin da ya faru ta manta wani Mutallab fresh take jin kan ta, tana yar waƙarta ta turanci tama manta ta shigo parlon daddy dake zaune ya zuba mata idanu ta yi saurin rufe ba ki ta ce

"Ka yi haƙuri daddy i enjoying when i sing a song, don Allah ka yafe wa Maama"

"Sai an yi magana idan kin yi laifi kina buɗe manyan idanunki kinawa jama'a turancin yaran zamani ke ba kowa naki da yake bature"

"To babana babban laccara ne wanda ake alfahari da shi dukkan matasa ke son shi saboda ƙoƙari da iyawar shi" Fiyya ta ce tana zaman ƙasan ƙafafun daddy "Tiger" sak ta yi jin sunan da ya kira ta da shi, lallai an taɓa donganta ta sa wannan sunan na Tiger ta share kana ta gai da daddy.

Ya amsa cikin kulawa duk motsin da take akan idanunsa Fiyya na da mugun wayo dana da wani experience da Qualities bata yin abun da za a iya following footsteps ɗin ta, she is a clever girl faɗanta har tsoro yake bashi ga taurin kai da miskilanci har addu'a yake Allah ya sassauta mata sai gashi Ubangiji ya gyara komai a lokacin da bai zato ba. Ya ɗauke kai yana kallon wani gefen

"Aliyu yaushe ka dawo?" Idanunsa a kan waya yana dannawa, wandon uniform na sojoji ne jikinsa sai fara t.shirt tas wacce ta kama damtsen hannunsa ya saka p.cap ta sojoji fuskarsa kamar ya ce ya shiga uku can ya ce

"Da daddare"

"Dare da yaushe? Aliyu kai kana son shigowar dare kamar mara gaskiya?" Captain ya ɗan kalli daddy ya ce "Tun 12"

"Kuma baka shigo ba me ya sa?"

"Kawai daddy" ficewa ya yi yana cilla wayar a aljihu yana jin Fiyya na gaishe shi ko inda take bai kalla ba. "daddy ni ba zan iya ɗaukan wannan halin ba wallahi bai ishe ni kallo ba zan daina ko gaishe shi ina dalili, Safiyyerh Abdu Marafa na da class babu mai ɗaga mini shoulder, duk wannan abun da ya yi aure a waje ne yake soja" Ranta duk a ɓace ta miƙe tana cewa daddy ta tafi ya ce "Allah Ya tsare Manager ya shirya safiyyerh Abdu Marafa". Kasancewar sauri take yi ta saka ta yi driving kamar zata tashi saman bata wasa idan tana kan titi, tana isa ta buɗe office ta shiga fahimtar da sabuwar envelope a table ɗin ya saka ta sa hannu ta ɗauka tare da buɗewa taƙaitaccen rubutu ne mai ɗauke da jan biro wanda ke nuna rayuwarta na cikin matsala. A hankali ta fara duba consent ɗin da takardar ke ɗauke da shi tana ajjiye waya.

“Jarumtarki bai kai ki tsaya bincike akan FS WORLD INVESTMENT COMPANY ba, kina iya ɗaukan rubutun matsayin wasa amma gargaɗi ne da jan kunne ga yara masu rawar kai irin ki. Ki tsaya da binciken da kike you're nothing but a manager”

Ta dinga juya takardar a hannu tana jin confidence nata na ƙara hakan kamar wata dama ce aka haska mata na nuna cewa lallai akwai ƙullalliyya a wannan kamfanin, kuma ta shirya buɗe faifai ko da za su yi zubaibai ƙwarya ne, ko da gaskiyar da take ƙoƙarin bayyanawa zai yi silar barin ta numfashinta daga ƙirjinta. Ta yi Addison na cikin abubuwan da take ƙarawa a binciken za ta yi komai ko hakan na nufin fito na fito da surukinta ne. Zama ta yi ta fara duba files na sabbin kayan da aka kawo can ta saka aka kira mata accouter bayan ya shigo ba tare data kalle shi ba ta ce

"Accouter kana buƙatar wani abu ne?"

"Allah Ya taimaki manager kamarya fa?" Still bata kalle shi ba ta yi baya tana duba maganar da aka turo mata yanzu a waya ta ce "kawai kuɗi idan kana so na buƙatun rayuwa"

"Ina jiran lokacin albashi ya yi ai nasan za a sallame mu da wuri" ta ɗago idanunta masu sanyi ta zuba a kan shi sai ta cillo masa ƙaramin file ta ce "na saka hannu ka yi signature as a accouter ka cire 1m a asusun kamfani na baka" da mamaki ya ce

"Ni kika bawa kuɗin?"

"E, ko baka so?"

"To na ga ban yi wani aikin da na cancanci 1m ba kin sa na fara jin tsoro ba zan iya cin abin da ba haƙƙina ba" ta ɗan yi murmushi ta janyo files ɗin ta yaga ta ce "meye cikakken sunanka ma?" Rainin hankalin Manager mamaki yake bashi sai kawai ya ce Wazeer" da hannu ta ce ya je yana fita ta saka aka kira mata MD abin da ta yi wa Accouter shi ta yi wa Md cikin sauri ya ce

"Yanzu kika ɗakko hanya manager da za ki haƙa ramin da za ki iya binne kan ki ciki ai duk sai na raina wayonki wallahi da ajin nan naki ko mene a ƙasa ba ruwanki mind your own business rayuwar nan kana kallon wasu abubuwan kake yi kamar baka sani ba, to a haka cibiya ta rai ne mu kuma yanzu hankalin jama'a da yawa na kan siyasa, matasa na neman hanyar karatu, wasu na can suna bautawa ƴan siyasa, wasu sojan baka wasu rayuwar social media wasu bangar siyasa wasu kasuwanci. Safiyyerh da yawa ana yin abin da ya samu ne ko yazo hannu ba wanda kake ganin cancnatar shi ba, ba a duba capacity na abu ko a siyasa kana ji kana ganin wanda ya dace amma kake rufe idanu ka ɗauki baragurbi saboda yana watsa maka hatsi mu ɗin kamar ka ji suka ɗauke mu, think big Fiyya ke macace babu mai ce miki don me, akwai kuɗin da shi kan shi Alhaji Baihaƙi bai sani"

"Kana son siyasa"

Md ya yi murmushi ya ce "Safiyyerh siyasa yanzu ai kusan a jinin kowanne matashi take, kinga muna da jam'iyyu uku ɗaya ce mai ƙarfi saboda ita ke riƙe da muƙami ma'ana ƙasar a nan Hon Maɗatai yake neman takarar kujera, sai jam'iyyar su Eng Ali wali sai last jam'iyya wacce mutumin cikin ta ya fi kowanne nagarta kuɗi masu dame shi ba, da ƙyar aka taushi zuciyarsa yake muƙamin kusan matashi ne matasa na son shi amma kasancewar yana cikin jam'iyya ƙarama kusan sabuwa ya sa ba a yin maganar shi ma kuma da ba musulmi bane" Safiyyerh ta jinjina masa kai ta ce

"Ka bawa accouter ya yi signature a baka 2m, enjoy yourself MD, but sunan wanda kake bani bayani yanzu?"

Ya washe bakinsa ba ƙaramin jin daɗi ya yi ba ya ce "Abraham Denial David, shine ɗan takarar"

"Yana da hannun jari a nan ne?"

"A'a, i don't think zai saka hannun jari a nan gaskiya" a hankali ta ce "Me ya sa?"

"Kar ki zurfafa a bar maganar, za mu yi aiki tare" sallamar shi ta yi tana jin zata yi amfani da Md da accouter Md zai taimaka wajan sanyawa ta san sirrin kamfanin cikin sauƙi accouter zai taimaka wajan bayyana komai. A gefe guda tana jin kamar ta shiga batun siyasar Abraham ɗin kawai ta ji ya yi mata she just want to help him.

****

Su da kan su sun kwana biyu basu saka shi a idanunsu ba, ba kuma su samu labarin inda yake ba sai yanzu da suka ganshi kamar walƙiya kwance a ƙasa idanunsa buɗe yana kallon sama Darma ya ce "Sai godiya wanda ya ce zai bi sawunka ya wahala, ɗan malam yaƙi halin malam dafinka ƙarinka masifa ne idan ka taɓa mutum da shi"

"Darma"

"Ka dake Mai dawa ka jima ka yi lastin irin na dabino, wa kake so a taka a kashe ko a yi masa fiɗa" Darma ya ce yana buɗe hannu sama tare da karkatar da baki hannunsa riƙe da ledar pure water ya nannaɗe a hannu yana kaiwa baki tare da zuƙa. Mutallab ya sake buɗe idanu a sama ya kasa cewa komai tunaninsa ya tafi wani wajan. Goje ya ce "Sai godiya matsalar goge ce ko wato ka kayan lantarki"

"Zaman gidan yari ba daɗi,amma na ji daɗi"

"Ka ce ka tuna na jakuna nan cinnaku tsakaninmu da su sai ƙarfe ba ma'ana ka tuna na jakin da suka haɗa maka kenan"

"Ina jin zafi a ƙirjina farcuna na da suka cire mini sun ƙi fitowa, zan ɗauki fansa Goje"

Kafin su yi magana an yi sallama an ƙarasu cikin sauri Mutallab ya rufe idanunsa jin muryar zabuwa. Goje ya dinga kallon wacce take tsaye "Bayin Allah sallama nake muku fa" Mangal ne ya kalleta sosai ya ce "Yi batu" ta ɗan rausayar da kai gefe ta ce "Amma dai ku musulmai ne amsa sallama wajibi ce"

"To alaiki, mene sagin aiki kike so a yi miki?"

Kinal ta fito da littafi da biro ta ce "Sunana Kinal ni mawaƙiya ce, har zan shige na hango ku na ji ina son tambayarku na ji ina son na yi waƙa akan ku kasan mu da mu da marubuta kusan aikin mu ɗaya muna da son bin ƙwaƙƙwafi" Goje ya ce "To ina ruwan mu? Fece kafin na yi miki lahani"

"Ku ba yan shaye-shaye bane? To akan shaye-shayen zan muku tambaya ina yin waƙar zan kawo muku ku ji, idan kun yi shaye-shayen me kuke ji mene dalilin daya saka kuka fara shaye-shaye kuma kuke harkar daba"

Moh na jin su ya juya musu baya zaka ɗauka bacci yake, ransa duk a ɓace saboda jin muryar mace da ya ji ya san daya juyo zai iya kashe ta tsaf don bashi da wani business da mata. Darma ya ce

"Yanzu yadda muke ji za mu faɗa miki kenan?" Kinal ta yi saurin cewa "E, wallahi na iya waƙa ina da murya sosai babu mamaki idan na yi waƙar na saka a YouTube ta je viral na saka a tiktok ta yi trending" Darma ya ce "To ni dai tun daga sanda a gida na yi...,"Da sauri Goje ya tsayar da shi yana cewa "Kai amma ɗan tsinanniya ne kai, ba haka ake bayani ba"

Miƙewa ya yi ya ce "bari na faɗa miki" wuƙa ya zaro a ƙugunsa Kinal ta zare idanu tana yin baya cikin sauri Mangal ya tare bayan jikinta na rawa ta fasa ihu jin yadda Goje ya yanke ta da wuƙa a fuska,ya danna mata ledan wiwin a baki ta fara zare ido tana ihu. Sai a lokacin Moh ya juyo yana kallon yarinyar ya cije bakinsa tare da juyawa exactly irin ihun da Safiyya ta yi lokacin zata mutu.

"Gani ya kore ji, idan kin rero waƙar muna dakon ki a nan sata ɣar munafuka"

Darma ya dinga tuntsira dariya sosai yana riƙe ciki "Amma Goje baka da imani kamar fa fitsari ta yi a wando gaskiyar kurciyar nan akwai jan ido ga bayani nan kin gani ganin idanunki ai" ya juya ya kalli Moh ya leƙa ga wata cukurkuɗaɗdiyya takarda yake karantawa shi ba wani karatu ya yi ba "Wai wannan takardar mece kamar ta asiri kodayaushe tana wajanka, kamar numfashin shaƙa ka faɗa mana ta mece" cikin sauri ya ɓoye yana damƙe ta a hannu Goje ya ce

"Nima sai fakon farar nake na mata karatun makarantar allo, na rasa wacce tsiyar ce a ciki"

"Goje"

"Sai godiya"

"Zan saka maka tsini idan ka taɓa takardar nan ko na saka su tiger cinye ka ɗanye, wallahi zan iya kashe ka akan takardar nan"

Kafin su yi magana an zo da babur an cillo wata takarda da sauri mai babur ɗin ya juya, Mangal ya miƙe tsaye ya ɗakko ya buɗe cikin sauri ya kalli Mai dawa dai kuma ya miƙa masa amsa ya yi ya duba, photo na gudu biyu ne ɗaya zanen fuskar wata kamar dai mahaukaciya sai kuma photo jira-jirai, photo me mai magana ga wanda yake da cikakken lissafi a gefe an rubuta FS WORLD INVESTMENT COMPANY.

****

Kwana biyu Safiyyerh ta yi busy duk wani family sun zo saboda gobe ne ake ɗaura auren, kamar auren munafurci ba wata gayya ko shagali ɗaurin aure ne kawai ana yi kuma Ashraf zai ɗauki matarsa su tafi. A daren ranar Safiyyerh ta riga data gama accepting auren Ashraf ta yarda bata da wani miji sai shi zata sawa zuciyarta yadda zata zauna da shi tunda tana son shi ko ba can ba. Waya suka yi da Ashraf ya dinga tsokanarta "Har na hango idanun Maama a ɗakin miji, mijin na kuma Ashraf ta yi nasarar samun kyakkyawan saurayi" ta murguɗa masa baki ta ce "Zan fasa" ya yi saurin cewa "Idan ki kaga ba ki auri Ashraf to mutuwa na yi ko ke kika mutu, da gaske Fiyya ina son ki Allah shine shaida duk da ina dalilin auren ki ko saka ni akai na yi hakan amma na yi you're my life partner har janna in sha Allah"

"Kamarya? Mene dalilin auren?"

"Ke ba ki da wani favourite words ne sai kamarya, zan faɗa miki komai a daren ranar da kika zama halaliyyar Ashraf zan faɗa miki, zan sauƙaƙa miki binciken da kike akan Company" a ruɗe ta ce "Ta ya ya kasan ina bincike akan Company"

"Safiyyerh kenan, that's is the difference between man and woman, ina da baƙi sai goben idan na zo ganin matata a wannan lokacin dole na rungume ki halal runguma zan miki Safiyyerh" hankalinta duk a tashe waye Ashraf ne me ya sa daddy ya amince da auren shi? Ta kasa magana har ya kashe kiran sai ya ƙara kiranta video call ƙura mata idanu ya yi taga yana shiri cikin sauri ta ce "Kuma sai ina?" "Inda kika aike ni" ta buɗe idanu

"Kamarya?"

"I miss you Fiyya shine abin da na manta na ce miki, a nan nake jin motsin ki" ya nuna mata saitin ƙirjinsa, daga nan ya kashe wayar. Daga ƙarshe ta yi zamanta cikin bedroom Awais har bedroom ya shigo ya dinga mata shira "Yaya Aiwas ka ɗan yanke mini farce" "to ban taɓa ganin amarya irin ba tunda nake a duniya" ya jawo ƙafar ya fara yanke mata farce ta rufe idanu.

Washegari da sassafe Fiyya na bacci daddy da kan shi ya tashe ta, ta farka da ƙyar saboda kan ta dake ciwo mamaki ta yi ganin kusan family a ɗakin ya kalleta ya ce "Kin dai yi sallah ko?" Ta ɗaga masa kai "Daddy lafiya?" Ya yi shiru ya ce "Junaid je ku fara yin gaba, Captain an kira shi yanzu daga can headquarter, Ummi ɗakko mini

hijabin Maama" Hijab ya karɓa ya saka mata ya riƙe hannunta Anty Turai ta yi gaba tana zabgawa Fiyya harara har harabar gidan suka je, abin mamaki gidan shiru ta rasa meke faruwa a motar daddy suka shiga yana baya riƙe da ita Awais na jan motar da Ummi. Motar Fiyya kuma da ita Captain ya yi using wajan fita saboda shi bai Fiyya ɗaukan tashi ba. Fiyya ta yi shiru kan ta a ƙasa,har suka ƙarasu cikin babban gidan mai tarin jama'a daidai lokacin aka fito da shi daddy na riƙe da hannunta ya ce "Mamana je ki masa addu'a"

"Addu'a? Daddy waye?" Ta furta muryarta na rawa ta juya ta kalli makarar da aka ajjiye gabanta ɗauke da gawa, ya sake riƙe hannunta da kyau ya jata zuwa gaban makarar ya duƙa tare da yin namijin ƙoƙarin buɗewa. Fiyya numfashinta ta ji ya ɗauke lokacin da idanunta ya yi arba da gawar Ashraf dake kwance cikin makara, jira ya fara ɗaukar gangar jikinta da gaske Ashraf ne kwance ba yau aka ce za a ɗaura musu aure ba shine zai mutu anya gawar Ashraf ce numfashinta ya tsaya cak tana daga tsayen suka ji ta yi wani irin ajjiyar zuciya tare da yin baya cikin sauri a tare daddy da J suka tare ta, ta ƙarasa suma a jikinsu.

Bayan sallatar gawar Ashraf da binne shi duk ana zaune ana addu'a daddy ya ce yana neman alfarma don Allah suka ce tame "Kar a tambayan hujja ko dalili a yanzu ina son a ɗaura auren Safiyyerh da Aliyu".

for now na san a ranku za ku yi ta wasu wasu, wasu ma su ce ba su gane inda labarin ya nufa ba😉ku dai nutsu tafiyar kura ce mai tsarƙaƙƙiyya har nishaɗi kuke bani idan ana comment tafiyar da hasashe ku lissafi ba zai taɓa kawowa tunanin mutum ba, kar ku ji kun karaya domin na san dole a gaba zaku buƙaci labarin, har yanzu shimfiɗa muke yi iya shafi 8 mukai

Littafin MUTALLAB na kuɗi ne kuma za a ke yin posting kullum. An fara biya yau domin shiga paid group na MUTALLAB.

MUTALLAB.

Book 1, 2 &3

500 Naira

0116886423 Union Bank Na'ima Sulaiman S.... A tura shaidar biya ta nan 08164069385 ku yi ku biya a sati uku mu kammala

Domin gyaran nono ❤

Assalama alaikum

Hajiya muna da ingantaccen maganin gyaran nono wadda ya amsa sunansa magani

Maganinmu ingantaccen maganine da yake tada jijiyon nonon da suka saki y'ar uwa breast dinki ko yakai silifas saboda kwanciya kikai amfani dashi in sha Allah zakiga amfaninshi acikin 1week maganinmu powder ne yana ciko da breast y gyarasu bashi da illa ajikin mutum munyi amfani da saiwoyi da magunguna gargajiya domin gyaran breast 08063114606 ina garin kano karki sanya y'ar uwa nono yana karawa mace martaba a gurin mai gida maganinmu kowa zai iya sha wadda zatai yaye ko gyara budurwa duk zasu iya sha breast dinki ya ciko yayi bull -bull

[1/7, 9:33 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

Page 9

Bright pens..2nd batch

"Bani da wani zaɓi sai na hakan, haɗa auren Aliyu da Safiyyerh kar ku tambayan dalili kar a tambayan cikin Safiyyerh da Aliyu waye ba ƙwayar halittata bace ta yi sanadin zuwan shi duniya, hankalina zai fi kwanciya kafin Ashraf ya kwana cikin kabari ya zamana Safiyyerh nada igiyar aure a kan ta" ajjiyar zuciya Sharfaɗi ya yi idanunsa a kan Prof Abdu Marafa ya ce "Me kake jin tsoro da kake so dole ka aurar da ita, Allah Ya gani amintar mu ya saka muka yanke hukuncin haɗa yaran nan aure saboda ƙarfafa zumunci, to kana taka Ubangijin talikai na tashi nasa kuma shine gaskiya, Ashraf ya rasu baya duniya ina tunanin ka bar yarinyar nan ta samu nutsuwa ta duba wanda take so yake son ta sai a yi mata aure, kar a ƙuntata rayuwar yarinya"

"Sharfaɗi ba zaka fahimta ba, ka yi mini wannan alfarma ka wakilci Aliyu ni zan wakilci Safiyyerh ga jama'a su shaida Please sai a haɗa a yi addu'a har ta Ashraf" J zufa har yanko masa take yi na tsananin mamaki mene haɗin Captain da Safiyyerh da za a yi musu aure? Baya son zuciyarsa ta gasgata abin da yake jin tsoro ko wassafo shi cikin kan shi, Safiyyerh fa and Aliyu? Ya Allah! Shi dai Awais kan shi a ƙasa Dr Hash daman baya wajan yana can duba Fiyya tunda ta faɗi wajan ya yi shiru can daddy ya ce

"Kawai alfarma nake nema zan ji daɗin hakan idan ka yi mini"

"To shikenan, waye maɗaurin auren?"

Daddy ya nuna wani abokinsa, Sharfaɗi ya ciro kuɗi mai yawa a cikin aljihu ya dire ya ce "Ni Sharfaɗi ina nemawa ɗana Aliyu Abdu Marafa auren Safiyyerh Abdu Marafa a wajan waliyi na wannan yarinya" daddy ya saka hannu ya ɗauki kuɗin ya ce "Ni Abdu Marafa uba a wajan Safiyyerh Abdu Marafa na bawa Aliyu Abdu Marafa auren yarinyar wajena Allah Ya sanya musu albarka" addu'a aka yi nan take kuma aka ɗaura auren a gaban shaidu ma ɗaurin ya ce

"Aure ya ɗauro a kan sadakin da Sharfaɗi ya bawa dubu ɗari biyu, Allah Ya sanya albarka tsakanin Aliyu da Safiyyerh ya kuma kaɗe fitinar da kan iya wanzuwa a tsakaninsu" duk aka amsa da amin. Daddy ya lumshe idanunsa yana sauke ɓoyayyiyar ajiyar zuciya nutsuwar ta saukar masa, bashi da sauran fargaba a yanzu Safiyyerh ta zama matar wani.

Kasancewar rasuwar ɗan babban mutum ce kamar Sharfaɗi ya saka manyan mutane zuwa gaisuwa, yan kasuwa da yan siyasa da wanda dai suke jin kansu wasu ne a garin. Kallo kallo aka shiga yi tsakanin Hon Maɗatai da Eng Ali wali dukkan su cikin shiga ta alfarma, ga mutane da take musu baya kowanne da tarin yan jagaliya da yan daba gudun kota kwana. Hon Maɗatai ya yi murmushi yana miƙawa Ali wali hannu ya ce

"Kwana da yawa Ali wali?" Ali wali ya ɗauke hannu sai kuma ya juya ya ce

"Ba yanzu ba ka jira na wani lokaci komai zai haska, za a yi tsawa walƙiya ta bayyana munafukan da suke ɓoye cikin duhun ciyayi" murmushi Hon Maɗatai ya yi kawai yana furta "Allah Ya nuna mana" gaisuwa duk sukai sai dai daddy tsakaninsu kawai addu'a ya miƙewa daga wajan. Bayan yin ta'aziyya Hon Maɗatai ya ce "Allah Ya yi wa Ashraf Rahama, ya taƙaita iya kan shi" Sharfaɗi ya juya ya kalli Hon Maɗatai kana ya kalli Eng Ali wali sai kuma ya ce "Amin, yanzu ba gashi ba gwanin sha'awa a dinga siyasa bada gaba ba sai an fi samun nutsuwar zuciya data ƙwaƙwalwa duk wanda zai samu wannan kujerar Ubangiji ya gama rubutawa kawai dai lalube ake yi cikin duhu ku haɗa kai da hannu kowa ya yi kamfel nasa babban jin daɗin ba jam'iyyarku ɗaya ba"

Cikin jinjina kai Hon Maɗatai ya yi murmushi daman shi bashi da wata matsala da Eng Ali wali shi yake haukan shi hankalinsa na kan wanda ya yi shiru, shirun nasa kuma yana nufin babbar barazana a gare shi "Siyasa ai ba zata haɗa musulmi irina faɗa da wani ba, munga jiya mun ga yau muna da tabbacin za muga gobe mai kyau, ni fatana na samu gurbin saka hannun jari a kamfaninka idan aka bani dama an yi mini komai Sharfaɗi" daddy na jin su can aka kira shi waya da sauri ya miƙe tsaye yana neman uzurin tafiya Eng Ali wali ya bisa da idanu.

Cikin dare Fiyya ta farka da wani irin ciwon kai na ɓari guda, ta kasa buɗe idanunta a hankali ta saka hannu ta dafe kan ta duk da halin cewa bai hanata yin addu'a ya yi tashi a baccin ba domin tabbatarwa da kanta ba a cikin kabari ta farka ba. "Sannu Maama" shine abin da Ummi ta iya cewa tana hamdala a ranta domin shirun ya yi yawa ta damƙe hannunta sosai

"Ummi kai na ciwo, ciwo nake ji a gefen kaina" jikinta har rawa yake na tsananin ciwo Ummi ta ce "Maama zai daina in sha Allah, bari a kira likita"

"Ummi daddy fa?"

"Yanzu ya fita, ki yi ta addu'a komai ya yi farko yana da ƙarshe, wannan ciwon kan zai daina miki watarana buɗe idon ki kalle ni" a hankali ta buɗe idanun ganin yadda idanun ya yi jajir ya saka Ummi cewa "Subuhanallahi wannan jan kuma na magani da mene?"

"Ummi jimawar da ta yi a kwance da ciwon kan shine ya saka idanun ja yanzu daddy zai shigo Fiyya zata ji sauƙi ki kwantar da hankali" daidai nan daddy ya buɗe ƙofa ya shigo J na bin shi a baya da Dr Hash, ganinsu kuma ya saka komai ya dawo tunanin Fiyya ta runtse idanunta tana jin fargaba na saukar mata. "Da gaske Ashraf ya mutu daddy? Da gaske an binne Ashraf babu Ashraf ya mutu yanzu haka yana kwance cikin kabari mijin da zan aura ranar ɗaurin aurena ya mutu daddy na shiga uku" daddy ya kama hannun Fiyya cikin nutsuwa ya ce

"Laa, sam ba ki shiga uku ba tana iya yiyuwa ya shige iyakar shi ne, kuma mutuwa a hannun Ubangiji take idan lokacin ya yi kota wacce siga ce dole wannan rai ya koma wajan wanda ya samar dashi, Maama da gaske mijin da za ki aura mutu ki sawa ranki haƙuri ki yi masa addu'a ki saka salama ki ɗauka bashi ne zaɓinki ko alheri gare ki ba, Ubangiji na yin komai a lokacin ya yi niyya babu mai tuhumarsa hujjar hakan domin shi ishasshe ne ki yi addu'a Safiyyerh Ashraf is no longer alive pray for him" juyawa Fiyya ta yi ta zubawa daddy manyan idanunta wanda yake cike da hawaye da ƙyar ta ce "Ashraf ya mutu ya bar ni cikin zullumi daddy, inama tuntuni aka ɗaura mini aure da shi, innalillahi wa'inna ilaihirraji'un wayyo ni Safiyyerh"

"Zullumi na me kuma Safiyyerh kin ga abubuwa da yawa a rayuwa sai mutuwar Ashraf zai tsaya miki? Ba za ki yi addu'a ki sawa zuciyarki sallama, kuma wani hanin ga Allah baiwa ne kamar yadda aka sanar yau ɗaurin auren ki da Ashraf Allah bai yi ba, haka kuma alƙawarin Allah gaskiya ne igiyar auren wani ta hau kan ki Maama" ta yi shiru don ta tabbatar daddy ba zai fahimce ta ba, ba zai gane me take nufi ba, ta yi missed Ashraf tun ba'a je ko'ina ba ta ji inama ita Ubangiji ya ɗauki rayuwarta ya bar Ashraf ko da bai aure ta ba, babu mamaki ta dalilinsa wani ya san abin da yake ɓoye gashi ta mutu ya barta da wani irin damuwa ba tare daya bar mata ƙofa ko ɗaya da zata gane ba komai ba.

"Daddy me ya sa ka haɗa aure na da Ashraf tun fari?" Daddy ya kalli Fiyya cikin kwantar da hankali "Saboda ya cancanta kuma ya dace Maama ki yi shiru da wannan maganganun duk zafin ciwo ne yake sawa kike furta su kamar saukar ruwan sama ki yi addu'a" ta jinjina masa kai a hankali ta zare hannunta daga cikin nasa idanunta rufe sai sauke numfashi take yi ba tare da ta ce komai ba ta juya ta kwanta maganganun Ashraf na dawo ba, a ranta ta dinga masa addu'a ita bata taɓa sanin bashi da lafiya ba, he never told her he was sick innalillahi.

Dr ne ya shigo zai yi magana daddy ya yi saurin girgiza masa kai alamar kada ya ce wani abu serious Dr ɗin ya zubawa Safiyyerh idanu ya ce "za'a sallame ta yau kamar yadda ka buƙaci baka son kwana zan mata allura amma before"

"Thank you Dr"

Dr Hash ya miƙe ya ce "daddy zan je asibiti ina da aikin dare Awais zai yi dropping nawa bana jin daɗi" Ummi ta ce "Kuma baka jin daɗin zaka tafi kamar dole ka yi kwanan tsaye ba'a ɗaukan uzuri ne" ya ɗan yi murmushi kawai ya ce "Ummi ai ba zai yiwu na amshi kuɗi na ƙi aiki ba, sai Ubangiji ya kama ni da wannan hakƙin ki yi addu'a zan iya" ta ce "To Allah ya sauwaƙe ya bada sa'a ya kuma kare"

"Amin Ummi"

Dr ɗin ya yi wa Fiyya allura ta samu bacci mai nauyi, Ummi dai kallon daddy take jin ya kira Aliyu ya zo ya ɗauki Fiyya nan da 20 minutes shi zai tafi tare da Ummi har lokacin Aliyu bai san da batun auren ba kamar yadda Fiyya bata ɗauki maganar daddy serious ba. Ya gyara mata kwanciya ya miƙe Ummi ta miƙe tana shafa kan Safiyyerh a haka suka fita. Har wajan ƙarfe 1:30 Fiyya na kwance tana bacci lokaci zuwa lokaci wata nurse ke shigowa duba ta. Yana tsaye hannunsa biyu zube cikin aljihu ba zai ce ga abin da yake tunani ba, amma fuskarta kawai yake kallo ganin yadda a bacci ma take ɓata rai ta sauke ajjiyar zuciya, ƙofa aka buɗe ya yi saurin yin baya yana kame fuska sosai.

Dr ya kalli Captain ya ce "Sai yanzu na ɗauka ma ko a nan zata kwana" Aliyu dai ya yi shiru ya zaro waya ya fara dannawa "ga maganganun nata wannan za a yi amfani da shi lokacin...," "Ka kira su, sai ka musu bayani" shi daya tsaya tunanin yadda zai tashe ta yake ga daddy sai kiran shi yake banda haka da ba zai zo bama, ya saka ƙafa ya fara zungurun gadon dr ya ce "Allurar da aka yi mata nada ƙarfi sai dai ka ɗauke ta" siririn tsaki ya yi "to ɗauke ta kai" ganin fuskar Aliyu cikin serious ya sa dr ya nufi Fiyya zai ɗauke ta zuwa waje kafin ya ƙarasa kawai yaga Captain ya saka hannu da drip ɗin da mayafin nata ya ɗaga sama ta zabura ta yi saurin riƙe shi Idan ba kuskuren ji ya yi ba ya ji kamar ta ce "TAHHB" ya sata gaban mota ya kwantar da kujera kamar wanda ake bi haka yake jan motar.

****

Yana durƙushe ya tsattsare mutumin da jajayen idanunsa wanda suka shige ciki alamar a buge hannunsa riƙe da askira gefe kuma jibgegen karan shi Tiger ne da

duk a cikin karnukan ya fi son shi. Ya saka askira ɗin a cinyar mutumin ya nutsa jini ya fara fita sosai yana ihu da kururuwa cikin tsakiyar daren ga duhu ko'ina ya ce

"Wai me ya sa baka da imani ne, zaka raba mini cinya biyu"

Duk da cewa a buge yake amma tar ya buɗe idanunsa, cikin muryarsa da kana ji ka san shi ba ma'abocin magana bane da wani kalar sautin mai kama da gurnanin zaki ya ce

"Ka gane ni yanzu?" Ya jinjina kai yana wani irin nishi da kakari kamar na mutuwa ya ce "Na gane na gane, wallahi na gane ka"

"Good" ya sake nutsa askirar ya yi feshi kunama ta faɗo ta shige cikin wandon birnin ya ce "Sanda aka yi mini baru ma'ana aure, da nazo kai na ganin bakin ƙofar gidana, haka ne?" Ya sake faɗa yana ƙara cilla masa wata kunamar baƙa ƙirin ta sake shigewa cikin wandon mutumin, Darma da Goje sun tale shi kowanne ya take hannu ɗaya mutumin ya yi shiru hakan kuma ya sake fusata Moh ainun

"Idan aka bani ciwon kai hauka nake yi ba zaka ka ji daɗi ba, a yunwa ce nake, yi batu" kamar zai mutu cikin kakarin mutuwa ya ce "Zan yi, zan yi magana" suka sake shi suna kallon shi.

"Mutane kala biyu ne suka shigo a wannan daren da aka kawo ta, na farko sun bani kuɗi fuskar su a rufe take na biyun ma sun sake bani kuɗi suma fuskar su a rufe take amma sun bani saƙo na baka tun a wannan lokacin, bayan an kama ka na rasa wa zan bawa na dinga bulayi kawai na haƙura, daga baya kuma aka zo aka sake cewa na bada wannan saƙon na ce a'a sai sukai mini tagoma shi da kuɗi har miliyan ɗaya kawai na basu ai kan ƙasar nan yadda muke fama da babu da yunwa ga iyalai ina dasu kawai na amsa na bashi"

Darma ya ce "ka ji kimini yɗan yankin nan ba za ku gama da duniya lafiya ba, da ƙyar kusha ruwan alkausara" Moh ya zubawa mutumin jajayen idanunsa sai kuma ya miƙe tsaye magana yake son yi amma ta maƙale a harshen shi da ƙyar ya ce "Ku yi masa ɓalli-ɓalli" yana cewa haka ya juya.

"Baka ji ba, ai na haddace abin da aka rubuta harafi uku ne a jiki. A.M.A, sai wani suna nada ban kamar sunan asibiti kamar sunan unguwa idan na tuna zan zo na faɗa maka amma don Allah kar ku yi mini komai a tausaya mini sabuwar amarya ce dani"

"Ni tawa matar ko kwana ban yi ɗakinta ba, duk irin gwagwarmayar dana sha, uhmmm" ya yi shiru a lokacin sautin muryarta yake ji na kakarin mutuwa a kunnensa can ya miƙe kawai ya yi gaba. Goje ya ce "Zan dinga zuwa lokaci lokaci domin kana cikin taskar Moh"

Da sauri suka bi bayansa ganin har ya yi nisa sosai "Mai dawa daman ka iya yaran nasara na ji ka ce Good"

"Na yi kala da wanda iya turanci ko mota ko amfani da waya ne?" Kallon tsaf sukai masa Darma ya ce "Ciki ne kai yasin sai fama kake da kan ka ba wannan maganar a basar kawai ya maganar ɗawan nan?" Kamar zai yi shiru sai ya ce "Bana son sabga da mace zan iya kashe ta kamar yadda itama ɗayar na kashe ta"

Darma ya fashe da dariya sosai yana kaɗa kan shi ya ce "ba wannan ba wallahi wata figigiya da ita, suma dai basu da man kai wai ita ce manja" Goje ya ce "matsalar kai daƙiƙi ne ajawo sam ciki ne kai, manager ake cewa dake mayen garau garau ne kai wai manja ai uwar manja gaja kawai" Darma dai bai kuma Goje ba ya ce "Maganar gaskiya wannan za a iya karya mata ƙugu a wajan ɗakko ta ma sille kenan, Mai dawa ko kai baka ganta bane" Ya yi musu shiru yana jinsu dai "Sai godiya, ina magana baka ganta ba wata yar shila da ita?"

"Ita wa?"

"Manja ɗin"

"Idan ka ƙara ce mana manja a wajan nan za kaga manja ganin idanunka, ɗan wahalar yaro kawai" Mutallab dai idanunsa a lumshe tunanin da yake yi daban, kalmomin da mutumin ya faɗa masa nata yawo a cikin kan shi. A.M.A Ya kasa

fahimtar kowanne harafi me yake nufi sai kawai ya taune bakinsa ƙirjinsa na buɗewa duk jikinsa tsami yake masa ya buɗe idanunsa ya kalli sama yana ganin yadda gajimare ke gudu yana haɗewa tare da warewa muryarsa bata wani fito sosai can ƙasa ya furta kalmar.

"her eyes look alike, tiger".

Washegari misalin 12 na rana Safiyyerh na saman bene cikin ɗakinta ta dinga kallon Kinal bata da nutsuwa sosai da babu abin da zai hanata yin dariya. Kinal ta share hawayenta tana ɓata fuska cikin sanyin murya ta ce "Kalli yadda sukai mini da fuska daga tambaya na ɗauka za su faɗa mini ashe yan wahala, ni bada wata munufar na je wajan su ba wallahi kawai su bani amsa na ƙara gaba"

"To ga amsar nan ai"

"Maama fuska ita ce kyan mace fa, yanzu idan tawa ta lalace waye zai aure ni haka? Sun kusa tsaga mini baki gashi yanzu ina da aiki a ƙasa sosai har Hon Maɗatai zan yi wa waƙa" Safiyyerh ta yi shiru tana tunani so take ta fice daga cikin gidan secretly amma no way "wai ina magana kina ji ba zan shariyar nan naki damuna yake, na zo ɗebe miki damuwa da kewa na rashin Ashraf kamar yadda Ummi ta buƙata duk da ciwon da bakina yake mini ina da zuba ke kina ignoring nawa for God sake"

"Idan ba ƙi auro ba sai ki auri ɗan daban kawai" Kinal ta yi tsaki ta ce "Kuma zan iya, mene a ciki"

"Shi auren ɗan daban?" Fiyya ta buƙaci amsa tana kallon Kinal. Kinal ta ce "Deal, nama yi miki alƙawarin in dai ina da numfashi wallahi wallahi sai na auri ɗaya daga cikin yan daban nan, kamar ni mawaƙiya za su yi wa haka? Uhm" Fiyya ta lumshe idanu ta buɗe deep down ƙirjinta na bugawa sai ta ce

"You most like them ma, yan daban ai sun iya soyayya"

"Ke ta ya kika san sun iya?" Shoulders kawai Fiyya ta ɗaga ba tare da ta ce komai can ta sauke numfashi tana kallon Kinal ta ce

"Kinal Ashraf ya rasu, mijin da zan aura ya bar ni Kinal ina cikin damuwa ina jin da old Safiyyerh ce ba zan ce ina cikin damuwa ba, gwara ta kashe ni haka nake ji" Kinal ta jinjina kai "Fiyya something is over doesn't mean your life is over, ki yi haƙuri mu ɗauki ƙaddara ki yi wa Ashraf addu'a Please kar ki saka damuwa wani abun ya zo yana damun ki daman ke idan kika birki ce kamar mai yar mero a ka, ƙaddararmu zata zama mai kyau muna tare da addu'ar iyaye ai" sun jima tare da Kinal har yamma kana ta tafi gida tana jin dole ta sake komawa wajan yan kodin ɗin nan.

Da ƙyar da daddare Fiyya ta sakko ƙasa bayan tayi sallar issha tana sanye da hijabi har ƙasa, fuskarsa looking ok ba yabo ba fallasa sai dai ta faɗa idanunta ya fito akwai damuwa a tattare da ita. Inda ta yangi su J ta nufa ta shiga tsakiyar yan mazan ta zauna a nutse ta ce "Sannun ku" Awais ya ɗago ya kalleta ya ce "Yawwa Manager ya ƙarin haƙuri?" Idanunta ya juya ta cije baki ta ce

"Allahamdulilah,thank you" daddy dake kallon ta cike da tausayi ya ce "tashi a nan wajan Safiyyerh"

"Daddy me ya sa?"

"Ki dai tashi na ce ko?"

A sanyaye ta miƙe sai kawai ta yi sama ya bita da idanu a hankali ta ce "Sai yaushe zaka faɗa mata batun auren?" Daddy ya ce "Da sai an kammala Visa ɗin ta, na san wacce take da ita a baya ta yi expired, to Safiyyerh stubborn girl ce da na yi maganar visa zata kalli cikin idanuna ta fara mini turanci wayonta tsoro yake bani, kuma yanzu i feel very comfortable da Aliyu matsayin mijinta duk da basa shiri amma ba zai ɗaga mata ƙafa bana son dai ta yi rayuwa a wajan shi kamar Prisoner, za ta yi shakkar yi masa abu"

"Kana ganin zata amince da auren?" Ya miƙe tsaye yana haurawa sama ya ce "In sha Allah" daman daga sallah ya dawo shine ya zauna. J dai baya uhm baya uhm'uhm abubuwa da yawa ke yawo a ƙasa wanda baya rasa nasaba da tunanin wace Safiyyerh waye Aliyu?

Ummi ta kalli yadda ya shigo ba wanda ya kula kamar bai ga kowa ba ta ce "Aliyu tun safe ina ka je ne?" Ya buɗe ido ya yi shiru ta ce "Kuma ka ci abinci ne? Kodayake ba'a tambayar soja ko ya ci abu da za'a buɗe cikin ka duk ganye ne" kallon Ummi kawai yake kuma ya yi shiru

"Yaushe zaka tafi goben?"

"A'a, night Ummi" ya ce yana shigewa cikin ɗakin shi dake part ɗin mazan.

Fiyya ta ci kuka a ɗaki kamar rai da sauri ta buɗe system ɗinta taga saƙo a e-mail nata tun sanda sukai last called da Ashraf bayan hakan ta minti ashirin da wajan biyar. Maganar daya tura mata ya saka ta buɗe idanu sosai.

Safiyyerh daddy ya zo ya fita yanzu, ko ma dai menene ki tabbatar ba ki bawa wani damar mallakar FS WORLD INVESTMENT COMPANY ba Fiyya mutane biyar sune mamallakan wannan kamfanin mutane masu haɗari ko ni ban san su ba, da ina da yadda zan yi a yanzu zan faɗa miki komai domin sauƙaƙa miki, ki fara nemo ma'anar FS shine key ɗin binciken, don't cry when you miss me i love you"

Safiyyerh was shocked, thinking me ya saka Ashraf ya yi mentioned sunan daddy a lokacin, meke shirin faruwa ne gabaɗaya kan ta ya ɗauki zafi da gaske ta yi rashin Ashraf sai yanzu ne take jin gudun zuciyarta na ruɓanya aikinta a kan Ashraf ɗin. Ta kwanta tana rufe idanunta ƙarar notification na wayarta ta saka ta buɗe idanu tana janyo wayar a hankali, rubutu a taƙaice mai ɗauke da azanci da ɓoye manufar abin da ake so a bayyana.

“laifi akan laifi again? Kodayake shi laifi tudu ne Safiyyerh ke inuwar wani ce ki yi ƙoƙari kar a saka ki shiga wuta”

A gigice ta ce "Na shiga uku ni Safiyyerh"

****

Cikin dare ne wajan biyu da arba'in motarsa na gefen titi cikin duhun daren ya saka facemask ya rufe fuskarsa tsoro da fargaba ya gaba gitta masa zuciya a hankali ya zuge glasses ɗin motar babu mai cewa shine a ciki, yana buɗewa ya faɗo cikin motar ya ce "Kira cikin dare? Ban fiya son ina tsaka da wani aikin kuma ana kira na wani ba, ya akai?"

Photo ya fito masa da shi na wani kyakkyawan yaro fari tas da shi idanunsa buɗe ya shagwaɓe fuska tare da miƙa hannu alamar a bashi wani abu, yana sanye cikin wasu ƙananun kaya baƙaƙe. "Na gani photon waye? Wannan yaron fa?"

"Ɗan gidan Safiyyerh ne" ya furta yana lumshe idanu tare da yin baya ya jingina da kujerar zuciyarsa na buɗewa sosai tsoro da fargaba na cika shi "What! Safiyyerh yaronta kuma?"

"E, idan kaga Safiyyerh ka gan shi kamar an yi kaki ban san ko ta san da yaron ba a tabbatar an gano mini inda sa Safiyyerh take"

Kwanakin wajan biyar da rasuwar Ashraf daddy bai faɗawa Fiyya batun auren ba, haka ma Aliyu Fiyya kullum sai ta fita wajan aiki ba kuma ta dawowa da wuri. Yamma wajan magariba take driving a gajiye take sosai fahimtar ana bin bayanta ya saka ta ƙarawa motar giyar da sauri ta ɗakko waya number J ta fara kira amma bai ɗauka ba, ta shiga kiran ta daddy amma a kashe duk wanda take tunanin kiran number shi a gidan ta kira bata samu ba,

ta kalli madubin taga har yanzu motar na biye da ita, tare da wasu babura biyu bata iya hango fuskar mutanen amma kallo guda ta yi musu ta san yan daba ne, ko dai masu satar mota ne ko satar waya ta shiga uku. Baburan guda biyu suka cimma ta ɗaya ya saka hannu ya daki glasses motar nata, ta yi gefe tare da ƙarawa motar gudu suma suka take mata baya a lokacin tsoron da ya yi mata yawa ya saka ta

fara gani dishi dishi kan motar na neman kwace mata, cikin sauri tana ƙanƙame steering ta shiga lalubar numbersa bata da tabbacin ko tana da ita cikin sa'a ta gani ta danna kiran sai da ta yi kiran biyar bai ɗauka ba, gashi hanya babu mutane a kira na shida ya ɗaga cikin ɗaga murya da fitar hayyaci ta ce

"Yaya na shiga uku Captain wasu ne"

Ya yi mata shiru can ya ce "Who are you?"

"Yaya Safiyyerh ce wasu ƴan daba suka biyo ni gashi titi babu kowa, Captain suna da yawa wasu a babur wasu a mota na kira number kowa a gida basu ɗauka ba gashi ciwon kaina kamar zai tashi bana ganin hanya sosai kan motar ƙwace mini yake" ta cikin wayar Captain ya yin siririn tsaki can ya ce

"Ina ruwana?"

"Captain kashe ni fa za su yi innalillahi wa'inna ilaihirraji'un!"

"Allah Ya ji ƙan ki"

littafin MUTALLAB

Na kuɗi ne we're still on free pages. Ka biya a yi adding naka a paid book before mu yi cutting free pages ɗin. MUTALLAB.

Book 1, 2 &3

500 Naira

0116886423 Union Bank Na'ima Sulaiman S. A tura shaidar biya ta nan 08164069385

[1/7, 9:33 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

Bright pens..2nd batch

"Kamarya Allah Ya ji ƙai na, Captain ina faɗa maka biyo ni ake yi za'a kashe ni, kana cewa Allah Ya ji ƙai na, i called you saboda na rasa wanda zan kira Please help me" ta cikin wayar Captain ya yi tsaki ya ce

"Kee, ina ruwana idan sun kashe ki who cares about your life, zan kira daddy a ɗauki gawarki ok" kashe wayar ya yi. Safiyyerh wani irin zafi ta ji a zuciyarta da raɗaɗi bata san ma wanne gurbi zata saka Aliyu ciki ba idanunta ya kawo hawaye baƙin cikin kiran da ta yi masa tana zargin kanta da laifinta ne. Ta cikin madubin motar take sake kallon motar dake bib bayanta da kuma sauran baburan ta runtse idanunta a fili ta ce "Ya Allahu Ya Rahmanu ka dubi Safiyyerh ka kawo mata ɗauki..Daddy!"

Ta kira sunan daddy a gigice tana sakin steering motar bata sake sanin abin da ya faru bayan nan ba.

Yana tsaye fitowar shi daga motar kenan ya dubi yadda ta yi flat kwance a ƙasa gefen kanta da jini ya kalli sauran jami'an tsaron da suke wajan "Is she ok? Tana numfashi?"

"She is, buguwa ne kuma Allah Ya rufa asiri motar ta tsaya da kanta, ba'a yi nasarar kama ko mutum ɗaya ba, yarinyar ce dai bamu san wace ita ba za mu duba id card nata sai a kira iyayenta a shaida musu ko asibiti ne a tafi da ita" ya yi maganar cikin girmama kan shi a ƙasa, wanda ke tambayar ko Fiyya na raye ya yi baya rungume da hannunsa can ya duba a gogo sai bai ce komai ba "Sir meeting ɗin naka? Ina tunanin ka je kawai za mu kula da komai tunda shugaban jam'iyya da secretary na jam'iyya na jiran zuwan naka" kafin ya yi magana cikin sauri wata mota ta ƙarasu wajan kamar zata tashi sama ko gama daidaita tsaiwar motar bai yi ba ya fito idanunsa a kan Safiyyerh, mutumin ya dubi fuskarta shima a hankali kuma ya ce.

"Easy Captain, ka kira ni sanda muke kan titin da take ta kuɓuta Allahamdulilah" jinjina kai Aliyu ya yi cikin girmamawa ya ce "thank you"

"Anything for you Aliyu, amma ku kula tana da harshe zuciyar nan tata irin take ce, Allah Ya bata lafiya" Aliyu dai na tsaye idanunsa akan fuskarta ya kasa magana har mutumin ya shiga motarsa driver ya ja, jami'an tsaron suma suka shiga motar suka marasa masa baya cikin tafiyar sirri. Ya jima yana kallon ta hannunsa riƙe da wayarsa tunanin yadda zai yi da ita, yʻar mitsitsiyar yarinya ta fito da shi, banda darajar daddy da babu abin da ya yi masa zafi sanin cewa idan Fiyya ta mutu hakan na nufin tsayawar numfashi daddy ya saka ya lallashi zuciyarsa. Cak ya ɗauke ta ya saka ta a gaban mota yana yin baya da kujerar a ransa ya ji ba zai zama driverna ba, ya ɗauki wayarta ya rufe motar yana shiga ya tare da zama ya sake juyawa ya kalle ta da kyau sosai jinin ke fita a goshin nata ya taɓe bakinsa kawai a hankali kuma yana ɗora mata tissue ya furta

“Fitinanniyya... Safiii”

Farar safiya ce gari ya yi shiru amma shi idanunsa biyu, yadda ya ga dare haka ya ga rana idanunsa tarwai a sararin subuhana yana kallon sama da abubuwan da Ubangiji ya wanzar a cikinta, a hankali ya juya ya kalli Darma da Goje sai kuma Mangal dake can gefe guda ya sha ta gaya masa babu daɗi sai lilo yake da ƙafarsa a sama. Mangal ne ya buɗe idanunsa da sauri ya miƙe zaune yana murza idanunsa alamar bai gama wastsakewa ba.

"Jeji naka dawa taka ka huta mai dawa, ba dai gaba da gaba ko ta baya ƙaryar mutum dan uwatar ya aka yi ba ka yi kasa bane ka raya daren da gadin mu?" Moh ya yi shiru ƙirjinsa sai ɗagawa yake. "Ina tsoron shirun nan naka don ba zai haifar da ɗa mai ido ba, ka tara dafi a cikinka jira kake ka samu inda zaka sauke ƙarin dake damun jikinka ka sarara a kaiwa mai duka lillahi kukan kawai" sai a lokacin ya juyo da gajiyayyun idanunsa da suka shige ciki duk girman da suke da shi, sun yi wani bala'in ja ya zubawa Mangal ido

"Talk da turanci kenan da hausa na goga maka yi magana sarkin jeji"

"Mangal"

"Yes inji masu jajayen kunnuwa bi ma'ana na'am" muryar Moh bata fita sosai a lokacin duk wanda ya nutsu zai hango wani irin sanyin murya da yake da shi da sauti maraya hayaniya. "Wacce cuta aka taɓa yi maka a rayuwa wacce ba zaka iya yafewa ba?"

"Kan uban nan, ni ai ka sani a kusurwa kaina ya kulle wanda sukai mini kuma tuni sun girbe abin da suka shuka bana yafiya bana cuta bana bari a cutan" cije baki kawai Moh ya yi yana lumshe idanunsa da sauri ya buɗe su tar saboda yadda yake jin kakari da numfashin fitar ranta yana yi masa amo a kunne, ya mirgina kaɗan ya ɗauki ƙafarsa ɗaya ya ɗora akan ɗaya yana girgiza wa ya zubawa zara-zaran yatsun ƙafarsa idanu tare da rungume hannayensa a ƙirji.

"Wai what happened Mai dawa?"

"Ka dai na yi mini turanci don uwarka"

"Dan tsinanniya ba, ba uban da ya iya kuma ya san ai duk bama ji shima a Legas ya koya" cewar Goje yana farkawa tare da zama dukkan su babu wanda yake da niyyar miƙewa domin yin sallah. Goje ya kalli Mutallab ya ce "Yaushe za a kwalo berewar nan ne? Ka yi shiru karfa ka jiƙa masa aiki"

Da sauri Mutallab ya kalli Goje jin sunan daya kira na barewa ya lumshe idanu ya buɗe zuciyarsa na bugawa sosai sai bai ce komai ba can dai ya miƙe zaune a hankali kuma ya tashi tsaye ya zaga bayan katanga ya daɗe kafin ya dawo wajan Darma ya kalli hannun Mai dawa ya buɗe idanu ya ce "Bura... Wannan ƙwayar ka shanye to kwarankwasa ka shirya zama mahaukaci, ƙwayar doki ce fa? Wai kashe kanka za ka yi akan wasu yanyan jakuna ka fito musu gaba da gaba mana, a yi komai duk abin da zai faru ya jima bai faru ba, ƙarshe dai gidan ɗan kande ne kuma mu ba wai baƙin ta bane"

Mutallab ya tsaya cak a tsakiyar wajan naman jikinsa na motsawa musamman kakkauran ƙirjinsa mai faɗi sai kawai ya shagiɗe bakinsa gefe kamar zai yi murmushi da sauri ya tsuke fuska zuciyarsa na tuna masa shekarun da suka shige a fusge ya furta "Sai godiya" gabaɗaya suka miƙe tsaye suna maimaita

"Sai godiya"

Basu fargaba sai ganin tarin wasu yɗan daba suka gani suna fitowa daga wasu lunguna a ƙalla sun fi su ashirin ɗauke da gorori wasu wuƙaƙe. "Dara ta ci gida lallai an raina mu, mu wasu daƙiƙai zasu kawowa farmaki har lukanmu?" Cewar Darma Mangal ya kalle su ya ce "Kuma suwaye ku yara?"

Wani daga cikin su ya fito ya tsaya a gaba ya ce "Sanin sunana ko waye ni bashi da wata fa'ida a gare ka, da zaka tambayi wanne kalar kisa zan maka zai fi maka, amma saboda gudun tilawa ko tafiya ƙiyama da tunanin wanda ya kashe ka lallai zan goga maka sunan nawa". Ya zaro wuƙa daga cikin ƙugunsa idanunsa akan Moh da bai ma kalle su ba sama kawai yake kallo yana jin yanayin na yi masa daɗi ya ɗora da "Uban yɗan daba nake maganin ƙananun yara masu ɓoyewa a saƙo, to cut you short sunana Lauje, ban duƙo dan na saka muku makami ba, na zo na tafi da uban gidan naku salin alin akasin hakan wajan bijire mini zai saka an samu kwacewar lissafi dar kenan" wanda ke kusa da Lauje mai suna Modara ya ce

"Ka saɓo shi a wuya mana sai ka tsaya ɓata yawun da Ubangiji ya halitta a bakinka Oga?"

"Ban zo don rigima ba, bisa umarnin Hon na zo wannan shine"

Darma ya matsa gefe yana nuna musu Mai dawa Moh kenan ya ce "Bisimillah gashi nan kuje da shi kuna da hannu na san" Moh ya sake juya musu baya maganganunsu da gaske ciwon kai da zafin zuciya suke ƙara masa hannunsa kawai yake dunƙulewa yana hura iska sama ko yaushe ya zama sa'annin yara irin su Lauje?

"Ji mana"

Mutallab ya juyo yana gyara tsaiwa idanunsa a birkice Lauje ya dinga kallon Mai dawa, shi bai ya yi tunanin haka yake ba yaji ana Mai dawa da Mutallab sai ya ji sunan Mutallab kamar na ƙananun yaran ganin Mutallab cikakken namiji a tsaye

mai kakkauran hannu da buɗaɗɗan ƙirji gabaɗaya jikinsa a murɗe yake musamman damtsen hannun ya basar ya ce "Shige muje"

Da hannu Mutallab ya yi masa alama da ya zo ya tafi dashi, Lauje ya nufi wajan Mutallab ba tare da sanin cewa akwai shafin hannu a jikinsa ba ganin ba wani makamani hannunsa ya saka ya nufe shi. Yana miƙa hannu da sunan kama shi Mutallab ya yi masa wani naushi a gefen ƙirji, nan take Lauje ya fara fari da idanu ƙashin gefen ƙirjinsa ya yi ƙara ya sulale a wajan ba numfashi. Ganin hakan ya saka su Modara ja baya a tsora ce ya ce

"Kut ya bazar dashi ba, wannan mahaukaci ne"

"Bai mutu ba tafiyar zango ƙalilan ya yi kawai ya samu karaya a ƙirji, kar dai ku manta da Mai dawa kuke magana masu jeji da namomin jejin da kansu matsalar gajanci kenan kun tari mutumin dake da shafi a hannunsa duka ɗaya ka sume gwara ya saka maka kaifi daya saka hannu, ya zame muku hadda. Yi batu waye ya aiko ku?"

"Hon Maɗatai"

"Wani abu ne haka? Me za a yi masa?"

Modara ya ce "Bamu sani ba, ya ce yana buƙatar ganinsa shi kaɗai kuma a sirrince"

"To ba zan zo ba"

Cewar Moh yana cije bakinsa hannunsa har yanzu rawa yake baya son yin kisa, idan ya riƙe wuƙa bai san me zai iya yi ba kuma sam. Da mamaki Modara ya ce "Kasan waye hon Maɗatai kowa? Wallahi taimako zai baka shine kawai yake jin tausayin yɼan daba irin mu"

"Ɗan daba irin ka dai, shi Malam Abdullahi ne balle ya yi mini baki, ko Malam Abdullahi can ta matse masa" Modara ya buɗe baki da nufin sake magana "Kana

kira mini sunansa sai na yi maka sabuwar kaciya" ba shiri ya tsuke bakinsa suka ja Lauje tare da barin wajan cike da takaici.

Safiyyerh na kwance tana bacci tun bayan sallar asuba da ta yi, Dr Hash ya sake ɗaura mata ruwa a hankali kuma ya ji tana surutai ƙasa-ƙasa ya kasa kunne da kyau ko zai ji mene take cewa "Ashraf ka taimaka ka dawo ka faɗa mini ma'anar FS, ka faɗa mini suwaye mutane biyar ɗin da kake magana akai, Ashraf the company is belong to your father,ko a mafarki ne ka faɗa mini ko a fatalwa ne ka zo mini bazan ji tsoro ba, Ashraf i really really need your help, don ka dawo" Dr Hash ya juya ya kalli daddy da ya yi ƙasa da kan shi

"Daddy akwai damuwa fa, meke faruwa da Fiyya ne? Me take buƙata wajan matacce ne Ashraf zai fito daga kabarinsa kuma ya yi mata, daddy Ashraf ya rasu fa ranar da za a ɗaura musu aure da Fiyya me ya sa ba za ta yi tawakakkali ba, me ya sa wai?"

"She loves him so much, tana son Ashraf ne shi ne dalili" cewar daddy yana sake matsawa tare da zama a bakin gadon ya kama hannun Fiyya ya riƙe cikin nasa da kyau "wannan zafin hannun fa? Her temperature is too high, bana son zazzaɓi a jikin Maama ka yi wani abu Dr Hashim" Dr Hash ya ce "Ciwon kanta da bugawar ne ya saka mata zazzaɓi, na yi mata allura zuwa anjima zai sauka ai"

Maimakon Fiyya ta yi shiru sai ta cigaba da surutan sosai tana furta "Ni ba Tiger ba ce Tahhb, why are you decided to call me Tiger?" Kamar a gaske kamar kuma yanzu ne ta ji saukar muryarsa a tsakiyar kanta, sautin ya sauka a ƙirjinta "Saboda ke matar Moh ce Tiger, zama matar Moh is not easy we most fight together halinki irin na tiger ne, matar Moh" tar da buɗe idanunta a gigice a kuma sauti na ruɗani ta ce "Motar Moh"

Daddy da Dr Hash suka kalli juna jin abin da ta furta kafin su yi magana Safiyyerh ta juyo ta kalli daddy sai ta yi murmushi mai kyau wanda suka jima basu gani a saman fuskarta ba, ainahin murmushi da kyawun Safiyyerh daya shuɗe ya dawo fil ta riƙe hannun daddy a nutse ta ce "His voice daddy, muryarsa ce"

"Shi wa?"

"Tahhb" daddy ya yi murmushi yana shafa sumar kanta ya ce "ai kuwa na ji nima, ki yi bacci Maama za ki samu sauƙi in sha Allah" ta jinjina masa kai tana riƙe da hannunsa har lokacin ta ce "In sha Allah daddy, in sha Allah daddy" jikinta ya saki ta koma bacci daddy ya sauke numfashi ko samun sukunin karyawa bai yi ba, ya dubi Dr Hash ya sake duban Fiyya ya ce "Ka yi mata allura kafin ta farka"

"Daddy ka duba Maama tana cikin damuwa ba, baka jin allurar zai saka ta dawo da ɗabi'unta na baya daddy yin allurar ba mafita ba musamman ga lafiyarta, tsayin shekaru na daddy har yaushe ne ka duba Safiyyerh don Allah" miƙewa tsaye daddy ya yi ya ce "Ka yi hakan Dr Hashim Abdu Marafa, completely tsayin rayuwa haka nake son ganin Safiyyerh" jinjina kai Dr Hash ya yi sai ya haɗa allurar har guda biyu ya juya bayanta ya caka mata cikin sauri ta ƙanƙame jikinta wani irin azaba da raɗaɗi take ji a duk sanda aka yi mata allurar. Yana yi mata ya fice ba tare daya sake kallon daddy ba. Ya zubawa photonta idanu yana juya mata baya a hankali ya ce

"Ki yafe mini Safiyyerh ki fahimce ni ki fahimci mahaifinki, i am sorry Safiyyerh" fita ya yi ya rufo ƙofar ya nufi parlonsa a zaune ya tarar da Ummi tana kallon shi ta ce

"Ya jikin nata? Ta farka ne?" Ya zauna yana numfasawa "Ta sake yin bacci, ina Aliyu?" "Kasan sai ya yi niyya yake shigowa" daddy ya ɗauki wayarsa ya kira number Aliyu yana ɗagawa ya ce Aliyu zo mana ya ajjiye ya kalli Ummi cikin kulawa ya ce

"Ina jin kamar haɗa auren Aliyu da Safiyyerh na yi kuskure ina jin kuma hakan shine mafita, ina jin tsoron tambayar da dukkan su za su yi mini wacce bani da amsar su, da gaske bani da wannan amsar tasu Ummi, ba komai Safiyyerh take ganewa tana jin ta isa ta yankewa kanta hukunci ita ba kowa face yarinya mai wayon gaske da tunani Safiyyerh bata san komai ba ita kawai yarinya ce"

"Ka san dole zaka jira amsar wannan tambayar da kake tsoro, amma sanar dasu auren shine zai fi maka a raina ina jin Maama ba zata yi maka gardama ba" kafin ya ce wani abu Aliyu ya buɗe ƙofar ya shigo da izinin daddy kamar kodayaushe wandon sojoji ne a jijinsa da farar riga tas ya ɗora hula p.cap a kan shi ya zauna kansa a ƙasa yana furta "barkan ku da safiya"

"Aliyu ya aiki, baka san Maama ba lafiya bane naga baka shigo ba?"

"Na sani" ya ce kawai a taƙaice yana danna wayarsa "Ka sani kuma? Shine ba ka yi mata sannu ba me ya sa kake haka ne Gadanga, me ya sa kai zuciyarka bata motsawa sai akan Maama meke damun tunaninka baka ɗaukan responsibility ɗinka as a brother"

"Idan bai ɗauki responsibility nasa matsayin yaya ba, yanzu zan ɗauki responsibility Safiyyerh a matsayin mijinta" da wani irin yanayi Aliyu ya juya ya kalli daddy yana son sake tabbatar da abin da ya faɗa masa a zuciyarsa wani irin fargaba ne ya wanzu ciki a fili kuma ko gezau ya dai zubawa daddy idanu can ya ce "kamarya?"

"Da kai da Safiyyerh baku da wata kalma da za ku replying mutum ko responding maganarsa sai kamarya? To kamarya dai yadda ka ji ai aikin da ka yi na soja bai saka ka daina jin Hausa ba, har gwara Safiyyerh ma" daddy ya gyara zama Aliyu dai kallon mahaifin nasa kawai yake da wani irin yanayi mai ɗauke da zallar mamaki.

"Aliyu ni ban isa na saka dole ba, ban kuma isa na tilasta rayuwarka yin abin da ka yi niyya ko baka so ba, Aliyu ni dai mahaifinka ne ka saka hakan a zuciyarka. Bani da wanda zai mini wannan rufin asirin kaf family, ka manta da batun Junaid da Awais da kuma Dr, kar ka tambayi mai ya saka na zaɓe ka na ji a raina zaka kula da Safiyyerh ko bayan bana numfashi ko bayan ƙasa ta rufe mini idanu na zaɓi aura maka ita saboda dalili mai ƙarfi, na yarda da ingancinka" Ya yi shiru Ummi kuma Aliyun take kallo shi kuma yana kallon daddy da duk nutsuwarsa. "Ranar da Ashraf ya rasu a ranar aka ɗaura maka aure da Safiyyerh, don Allah don girman Allah karka tambayan tsakaninka da Safiyyerh waye ba jinina ba, wannan tambayar shine abu mafi girman laifi a gare ni, ka taimaka ka yi mini alfarma ka riƙe Maama ka amshe ta matsayin matarka"

Captain ya kasa motsi balle magana bai ma san mene zai ce ba. Daddy ya matsa hannunsa "Don Allah Aliyu"

"Ita ta sani?"

"A'a, kai na fara sanarwa Safiyyerh bata da wata matsala ga umarni na" Aliyu ya sake yin shiru idanunsa a ƙasa har ya juya baya ya sake juyawa ya kalli daddy a hankali ya ce "tell her first, ko bana son ta zan yi ƙoƙarin ganin na fara son Safii in sha Allah"

"Ba zan tambaye ka ni ne ba ɗanka ba ko ita, zan bar tambayar a raina har sanda ka shirya faɗa mana gaskiya ni da ita, zan rayuwa da fargabar sanin amsa, da gaske daddy zan so Safii iya tsayin numfashi tunda kai ka zaɓa mini ita"

Daga Ummi har daddy kallon Aliyu suke musamman daddy bai yi tunanin jin wannan amsar ba ya dinga kallon Aliyu ba ko ƙiftawa "da gaske zaka so Safiyyerh? Ka san Safiyyan da nake nufi Aliyu?" Aliyu ya buɗe idanunsa wanda hula ta ɗan rufe masa su

"Safiyyerh Abdu Marafa ko ba ita ba?"

"Ita, zaka so ta ka ce?" Daddy ya sake faɗa da mamaki

"Bata da Qualities ɗin da za a sota ne?"

"Haka ne tana da shi, na shirya tafiyar ku za ku bar ƙasar nan nan da kwana biyu bana buƙatar ku gabaɗaya a yanzu domin nutsuwar zuciya" Aliyu ya sake duban daddy ya ce

"Kuma? Ka bar tafiyar nan daddy" sai kuma ya juya gabaɗaya ya kalli Ummi da daddy

"Aliyu soja ne, so i will be with her always"

Yana cewa haka ya fita da ƙyar ya yi jarumtar kai kansa ɗaki ya cire p.cap ɗin kansa ya shiru ba auran ke damun shi ba, tunani ya fara wa daddy ya haifa tsakanin shi da Safii?

Da yamma Safiyyerh ta ɗakko ƙasa bayan tafiyar Kinal daga ita sai duguwar rigar bacci kanta ba hula sosai ƙuruciyar nan tata ya bayyana, ta zauna saman kujera ta lumshe idanunta ta zama wata ira tun bayan tashin ta daga bacci jikinta ba ƙwari. I dake kallonta ya ce "Sannu Manager, ya jikin yanzu?"

"Bayana ke mini ciwo Yaya J, ina jin Dr Hash ya mini allura, bana son allurar nan Yaya J bana jin daɗin ta watarana zata kashe ni don Allah ka cewa daddy ya daina sawa Dr ya yi mini" idanunta ya shiga kawo ruwa ta yi lamo da kanta saman hannun kujera. Daman yana bakin ƙofa jin abin da take cewa sai kawai ya juya shi kuma Yaya J ya ce "Ki yi haƙuri Maama za a daina miki in sha Allah" ta yi shiru kawai.

Dr Hash na zaune a lambun gidan yana waya kasancewar baya da wani aiki a asibiti hutawa yake kashe wayar ya yi ganin Captain tsaye a kan shi. "Babban yaya barka da fitowa" kamar ba zai zauna ba sai kuma ya nemi waje ya zauna fuskarsa kamar kodayaushe babu walwala ya jima a haka kana ya ɗaga kai ya kalli Dr Hash "Akwai wani abu da kake son faɗa ne Captain?"

"Ka daina yi mata allurar da kake mata"

"Me ya sa?"

"Haka dai na ce, idan kuma ka yi zaka sha mamaki" Dr Hash ya ce "Wannan kam ai daddy zaka faɗawa shine ke bada umarni"

"Wa kake da suna, ka da ka sake ka kuma yi mata idan ba haka ba kuma wallahi zaka kwana ɗakin duhu" yana cewa haka ya miƙe tare da barin wajan.

*****

Hon Maɗatai na zaune gabansa zube da fastocinsa yana magana da wani yaronsa wajan keɓantacce ne kamar lambu haka yake bai san da zuwan mutum ba sai huci da ya ji ta bayansa ya juya da sauri sau kuma ya buɗe idanu waje kafin ya ce

"Ya zaka faɗo mini kamar ɓarawo?"

"Da ɗan siyasa da ɓarawo uwa ɗaya ta haife su, waye kai?"

"Baka san waye ni ba a garin kake nufi?"

"Ba'a haife ni da na sanka ba, ka aika akawo ni ina fatan saƙona ya iske ka?"

Hon Maɗatai ya kalli mutumin gabansa da wani ya ce "Waƙa ta yi, da ita za'a fara fita yawon kamfel a biya a dinga sawa a gidajen rediyo" ya ciro kuɗi miliyan biyu ya bawa mawaƙin ya ce "Ga sadakin ka, ina fatan waƙar gaba tafi wannan akwai wata zabiya wai ita Kinal A Awaya" cikin jin daɗi mawaƙin ya amshi kuɗin ya ce "Na san Kinal ai ta iya waƙa, ba dai ta shahara sosai bane"

"To sai mu saka ta shahara na ji ta yi Ali wali waƙa, ta yi sosai ta zuba kalamai na fikira harshen nata akwai zaƙi dani kuma kawai ya dace a nemo mini ita" "zan kawo ta in sha Allah hon, ka yi ka gama ka karya kujerar dambu mai hawa uku Allah Ya kare ka ɗan Majilisa kai ne da nasara Hon" "zaka iya tafiya sai na jika"

"Akwai taliya da atamfa da su Omo suger, a tabbata duk local government ɗin da aka je kamfel an basu, a kuma ɗauki photo da bidiyo za a bawa yan social media su baza shi ko'ina. Sai sauran magana na siyan ƙuri'u za ku yi da p.a you can leave Musbah" Musbah ya miƙe tsaye ya fice sai a lokacin ya juya ya kalli Moh dake tsaye fuskarsa duk rauni

"Nan ai ba jeji bane, ni kuma ba naman jeji bane ba have a seat"

"Bana zama"

"Saboda me?"

"Tsaro, yi magana"

"Shi wanda kakewa aikin baya kula da lafiyarka ne dubi fuskarka Mutallab"

"Ka kira ni da Moh ko Mai dawa sai mu yi magana" Hon Maɗatai ya jinjina kai ya ce "Ina son sanar maka na haɗa hannu da Dr Abraham, ta yiyuwa ya janye muƙamin da yake nema ƙarƙashin jam'iyyarsa idan haka ta gaske zamu kai Ali wali ƙasa ne, ka haɗa hannu dani lallai za ka ji daɗi"

"Me ka shirya yi wa matasa idan kaci zaɓen?" Hon Maɗatai ya ɗaga kai ya kalli Moh sai kuma ya yi murmushi ya ce

"Inganta ilimin su, rage musu kuɗin makaranta samar musu da ayyukan yi cusa musu ra'ayin noma da muhimmanci yinta"

"Su kuma yan daba fa? Wanda kuke anfani da su wajan cimma burikan ku, bayan yaran ku na keɓe kuna tattalin tarbiyar su ba ruwansu da sabgar siyasa sai mu yayan talakawa yan wahala kuma yan daba mashaya mune yan bangar siyasar ku a yau, a gobe a manta damu jibi kuma a neme mu shine ko?" Hon Maɗatai ya yi murmushi ya ce "Mutallab kenan, duk wata nasara da muka samu ai daku zamu rabata ni mulki da siyasa tamkar don su ne aka haifan, ina da kyakkyawan tanadi akan ku ba za a bar rayuwarku haka ba"

"Me kake buƙata"

"An saka ka kamo Manager ta kamfanin FS WORLD INVESTMENT COMPANY ko?"

"Wanne kiminin ya faɗa maka?" Hon Maɗatai ya miƙe tsaye yana zagayawa ya ɗauki fasta ɗinsa ya dinga kallon kansa ta ciki can ya ce "kai yin aikin ne a gabanka, mu yan siyasa da idanu ɗaya muke bacci mun raba kunnuwanmu ko'ina, ka dai sani a siyasa babu masoyi na dindin haka ma maƙiyi, iya ruwa je fidda kai kowa ya iya allonsa ya ce wanke kuma ni da Ali wali ai sahun qiwa ne ya take na raƙumi kowa da abin da yake buƙata, idan ka yi kidnaping yarinyar ka tilasata maka ta saka mini hannu domin na saka hannun jari a wannan kamfanin shine abin da nake buƙata" Jin Mutallab ya yi shiru ya saka ya ce "Ko baka ji ba?"

"Na ji"

"Mene alaƙar ka da makarantar FGC?"

"Ban sani ba, maganar kuɗin aikinka sai na yi aikin zai sanar. Sai godiya" yana cewa haka ya bar wajan.

Kasancewar Monday ce Safiyyerh ta shirya da wuri zuwa office har yanzu jikinta bai warware ba dole amma ya zama sai taje. Ba jimawa Md ya shigo bayan sun gaisa fuskarta dai a kame ya shafa kai ya ce "Manager gari ya ci wuta fa" idanunta akan wani ducoment tana juya kujera a hankali kamar ba za ta yi magana ba sai kuma ta ce "Nawa kake buƙata Md?"

"Ko dubu ɗari biyar ne zan yi maleji"

"Zan saka accouter ya baka miliyan ɗaya" ya dinga mata godiya sosai ta yi murmushi kawai ta ce "Mene ma'anar FS ni kam Md?" Tsam ya yi da ransa sai kuma ya ce "Ba zan iya ba ki wannan amsar ba Safiyyerh, zan dai faɗa miki abin da ba ki sani ba" ta sake juya kujerar hannunta a haɓarta tana murmushi mai kyau "Ina ji Md"

"Yatsun da kika gani kwanaki gaskiya ne, ana siyar da ƙodar mutane a wannan kanfanin tare da jarirai, ana kuma dillacin ƙwayoyi, sauran abun ki yi bincike da kan ki za ki iya dacewa" yana cewa haka ya fita. Kasa motsi Safiyyerh ta yi numfashinta ya tsaya cak da ƙyar ta miƙe ta ɗauki ruwa ta sha ta dawo saman duguwar kujera ta zauna zufa ta dinga yanko mata a hankali ta ware rolling na kanta ta rufe idanu tana kiran sunan Allah. Knocking aka yi da ƙyar ta ce "In"

Ta buɗe idanu da mamakin ganin wanda ya shigo, ya ƙarasu cikin office ɗin "Ba dole ki buɗe idanu ba Safiyyerh, idanunki kenan?" Ta yi murmushi tana gyara zamanta

"I. Qasim kai ne"

"Ni ne Safiyyerh"

Ya nemi waje ya gaisa ta ce "Yaushe gari kuma?" Ya yi murmushi ya ce "Zama likita a garin nan is not easy Fiyya, ya batun ciwon kan ki kowa?" Ta ce

"Yana nan"

"Ayya sorry, akwai maganganu da zan ba ki in sha Allah da allura, gudun kar ki dinga sha ba daidai ba zan dinga zuwa dasu kina sha a gabana na yi miki allurar, za ki samu sauƙi in sha Allah"

"Thank you I. Qasim na gode sosai" wayarsa aka kira ya kalleta sai kuma ya miƙe tsaye tare da yi mata alama da yana zuwa. Ta bishi da idanu har ya fita.

*****

Safiyyerh ta dinga kallon daddy kamar mahaukaciya saboda rashin fahimta ta ce "Daddy, aure da Yaya Aliyu ka ce dani kuma Safiyyerh, mu duka yaya anka ne fa" hawaye ya fara suntiri a saman fuskarta ta saka hannunta ta toshe kunnuwata tana girgiza kanta gabaɗaya ta jiƙa hijabin da ta yi sallah da shi da hawaye "ruɗanin da kake sani a kullum yana shirin haukatar dani daddy, ba auren ne ban yi na'am da shi ba na kasa fahimta ne dani da Captain waye wanda ka haifa waye ba ɗanka ba"

"Ku duka yarana ne Maama, idan har kin yarda ni uba ne a gare ki kuma kina so na da ƙaunar farincikina ki amince da auren Maama, ba zan taɓa cutar dake ba ni ubana ne, uban ƙwarai kuma yana zaɓawa yaransa abun ƙwarai ne ki yi mini biyayya Safiyyerh, kin ji ko?"

"Na amince daddy zan amince da abin da ya fi wannan ma, Allah Ya sa shine mafi alheri a gare ni" ta faɗa tana rushewa da kuka da sauri kuma ta yi waje ta nufi ɗakinta ta faɗa saman gado ta dinga wani irin kunjin kukan kamar ranta zai fita wai

wanne irin abu ne haka? Ta shiga uku meke faruwa aure fa, auren ma da Captain innalillahi wa'inna ilaihirraji'un addu'a take Allah ya yafe mata komai ta fahimta da ƙyar bacci ya ɗauke ta ko abinci bata ci ba. Cikin dare ta farka ganinta ta yi rufe da bargo ta yi saurin buɗe ido don bata san kwanciya a duhu gashi an kashe mata hasken ɗakin babu mamaki Yaya J ne. Gani ta yi wajan ɗaya da rabi ta miƙe ta ɗauki ɗan makullin mota da wayarta ta saka hijabi har ƙasa, ƙofa ta buɗe ta sauka downstairs ba kowa ta buɗe ƙofa ta fita mota ta shiga mai gadi ya buɗe mata cikin sauri ta nufi kamfani gari shiru sai hasken fitilo na titi ta dinga duban hanya ba wanda ke biye da ita a haka ta isa kamfanin ta ajjiye motar a waje, ciki ta shiga wajan mai gadi sun jima suna magana ya ce "Ana shigo da mata cikin dare ana kuma fita da su, na yi bincike abin da ya saka ke iya ɓangaren abinci kika sani to akwai asibiti a cikin wannan kamfanin" ta ce "Ka ɗauki number motar ko haddacewa?"

"A'a ranki ya daɗe"

"To shikenan na gode Baba, ga wannan" ta ɗauki kuɗi ta bashi a cikin aljihun rigarta. Tana ƙoƙarin buɗe gate ɗin kamfanin ta fita kawai ta ji ƙarar dingowar mutane, ta juya da sauri suka haɗa idanu da Darma da kuma Goje da Mangal wani irin mummunan faduwar gaba ne ya sameta lokacin da idanunta ya shige cikin nasa shi bai kai ga dingowar ba yana zaune saman katangar shima ɗin ita yake kallo babu ƙiftawa...

MUTALLAB PAID BOOK ne a jerin littafan bright pens. We're still on free pages kar ki bari a yi bake.

MUTALLAB.

Book 1, 2 &3

500 Naira

0116886423 Union Bank Na'ima Sulaiman S a tura shaidar biya ta nan 08164069385 via WhatsApp only.

DOMIN INGANTA NONO

Assalama alaikum

Hajiya muna da ingantaccen maganin gyaran nono wadda ya amsa sunansa magani

Maganinmu ingantaccen maganine da yake tada jijiyon nonon da suka saki y'ar uwa breast dinki ko yakai silifas saboda kwanciya kikai amfani dashi in sha Allah zakiga amfaninshi acikin 1week maganinmu powder ne yana ciko da breast y gyarasu bashi da illa ajikin mutum munyi amfani da saiwoyi da magunguna gargajiya domin gyaran breast 08063114606 ina garin kano karki sanya y'ar uwa nono yana karawa mace martaba a gurin mai gida maganinmu kowa zai iya sha wadda zatai yaye ko gyara budurwa duk zasu iya sha breast dinki ya ciko yayi bull -bull

[1/7, 9:33 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

Page 11

Bright pens.. 2nd batch

Ya ƙura mata idanu yana daga zaune saman katangar a hankali yake girgiza ƙafarsa, fuskarsa rufe da baƙin ƙyalle a lokacin duniyar ya ji tana masa daɗi yana jinsa kamar a cikin jirgi ana juyawa dashi, shi ya sa yaƙi sakkowa ƙasa daga katangar, shi kansa bai san wacce irin ƙwaya Mangal ya kawo masa ba. Fiyya ma shi take kallo ganin shi kaɗai ne ya rufe fuskarsa Goje da Darma da Mangal suka zagaye ta, ta juya ta kalli securityn da yake on duty ranar ta nuna masa Goje

"Su kuma waɗannan fa security?" Kai tsaye ya bata amsa da "Ban san su ba, amma Hajiya akwai hatsari bamu san me suka zo nema ba" Goje ya matsa kusa da ita yana kallon ta

"Mai dawa wannan ce ƙuruciyar? A hotun kamar bata kai haka girma ba, yar firit da ita kamar benu, nan kuma an ci kuɗin jama'a an sha madara da milo an yi ɓulɓul" sai ƙarewa Fiyya kallo yake ita kuma ta yi tsaye tana jin yadda warin wiwi ke dukan hancinta kamar za ta yi amai amma taƙi matasa saboda taurin kai irin na Safiyyerh Abdu Marafa da rashin tsoro. Tsaki ta yi kawai ƙasan zuciyarta kuma tsoro ne fal ga ƙirjinta dake bugawa kamar zai fito waje sai buɗe manyan idanu waje take yi.

"And what is my business with you? Me kuke nema a wannan kamfanin kun zo sai warin ganye kuke mini" Mutallab ya sake buɗe manyan idanunsa jin sautin muryarta zaƙwai a cikin kansa ya kalli bakinta dake motsawa cike da masifa duhun dare ne amma kamfanin haske tar tar ko'ina. Mangal ya lailayo ashar ya dannawa Safiyyerh "ke dan ƙaniyarki mune muke warin ganyen, su waye sila idan baku ba, yʼar wahalar yarinya idan ban bawa tiger namanki ɗanye ya cinye ba"

Safiyyerh ta juya ta kalli tiger daya hauro ya zauna kusa da Moh, yana zaro harshe waje ta nuna karan da hannu ta ce "abin da ya fi namana ɗanye, banda rainin hankali jikin nawa zaka ɗauka ka bawa shegen karan naku, idan kuɗi kuke buƙata na baku don nasa na yin caji kuke nema, stupid" Goje ya juya ya kalli Mai dawa ya ce "ba zamu rage wa yarinyar nan tsayin harshe ba kuwa? Kauɗinta ya yi over, ka je ka zauna matsalar idan ka sha wannan ƙwayar baka gane komai yanzu babu mamaki jinka kake a saudia"

Moh ya lumshe idanunsa ya sake buɗe su a kan Fiyya duk motsin da take yi a kan idanunsa sai dai ba wani fahimta yake ba muryarsa a cunkushe mai ban tsoro ya shafa kan tiger ya ce "shiit"

Tiger ya diro shima ya diro ya tsaya a kan ƙafafuwansa hannunsa ɗaya yana murza gashin kansa wanda ya zama wani iri ba kyan gani na shegun shahararrun yʼan daba ɗin nan.

"Mai jeji ƙirit ka ankare ba lokaci ka ɗaƙkota a kafaɗa mu fece kafin kwalawa su kawo kai dan akwai kimini a nan wancan mai fararen kayan" ya nuna securityn wajan wanda shi kaɗai ne kawai ya rage. Safiyyerh ta ja baya tana juya idanunta ta ce "ban gane ya saɓo ni kafaɗa ba kamar wata yʼar iska ko mara gata, kai naga alamar kai ne shugabansu ko? To wallahi ba wuƙa ba ko bindiga ce bana tsoro kana taɓa ni sai na raba ai an ce ba wani ƙwari ne daku ba" ta ƙare maganar tana kallon cikin idanun Mutallab wanda tun ɗazo shi take kallo shi kuma yaƙi furta komai.

"Ki iya harshenki yʼar kanzagi ko na fitar miki da jini yanzu na shata miki bille a wannan fuskar kamar gwada" juyawa ta yi ta ce "Baba wai where are the securities? Where are the rest ka kira su yanzu" kafin baban ya motsa Mangal ya saka ƙafa ya kwarfe shi zuwa ƙasa, ya sake saka ƙafa ya danne masa baki. Darma ya zaro wuƙa ya ce "Ke fitsararriya ce ko? Ba wata uwar muke nema ba ke muka zo ɗauka, don ke muka cikin wannan kamfanin ke za mu yi kidnaping yanzu kin fahimta kin gane ko, ki shige salin alin ko na ɗauke ki yanzu na haura dake wallahi"

Fiyya ta buɗe idanu tana kallon wuƙar dashi kansa Darma ɗin ta yi murmushi zuciyarta kuma bugawa tsoro ya shige ta, ƙoƙarin danna recoding take a wayarta hannunta ya shiga rawa ta dake a ƙasan zuciyarta tana kiran sunan Allah da ƙyar ta furta "kidnaping kuma ni, ni Safiyyerh Abdu Marafa za ku sace, ni Safiyyerh matar soja guda kuna hauka ne ko kuna tunanin mijina zai bari hakan ta kasance?"

Jin furucin Safiyyerh ya saka Moh sake kallonta da sauri yana hana zuciyarsa abin da yake ji, haka kawai ya dinga jin tafasar zuciya ya nufi wajan Safiyyerh jikinsa na rawa idanunsa suka fito waje kamar zasu faɗo da muryar mai ban tsoro mafi muni ba muryar ba ita kanta fuskarsa abar tsoro ce tsaf mutum zai dinga mafarkin ta. Hannunsa riƙe da wuƙa yana kallon cikin idanunta da kyau dab da ita ya ce "Ba mijinki ba ko ubanki Abdu Marafa aka bani umarnin daƙƙowa ko kashewa sai na yi balle ke" ya cije bakinsa ya feshi ya cilla mata ƙatuwar baƙar kunama ta shige ƙirjinta kai tsaye, zufa ta dinga yanko mata saboda tsananin azaba ta kasa ihu ko kuka ga warin da yake yi yana neman kashe ta, idanunta ya juye ya yi ja ta zuba masa idanu tana kallon fuskarsa data yaye,ta miƙa hannu da nufin shafo fuskarsa ta ji ya caka mata wuƙar a gefen cikinta ta yi wata ƙara tana buɗe idanu duk yadda jikinta ke rawa ga jini na zuba mai hanata sake kai hannunta ta shafo fuskarsa ba, daidai nan ya yunƙura zai saɓata a kafaɗa suka ji shigowar motoci na jami'an tsaro, bai niyyar barinta ba yadda Goje ke jan shi da ƙarfi ya saka kawai ya sake ta a wajan yana furta “Mutallab”

Ɗaya bayan ɗaya suka kama katangar suka haure daman kuma kaf kamfanin ita ce ƙaramar katanga wacce babu kwalabe jikinta.

Securities kala biyu ne dana fararen kaya da masu uniform sai shi da yake sanye da wando three qauter da farin takalmi da riga baƙa ko p.cap ɗin kansa babu, ya nufe ta sauran suka nufi wajan baba suka fara ɗaukan statement "Baba kwantar da hankalinka babu abin da zai sameka in sha Allah, bayan waɗannan yan daban da suka zo, an bamu tabbacin a daidai yanzu Scorpion ma yana wajan nan ko kuma ya zo" a hankali Aliyu ya juya ya kalli baban jin tambayar da ake masa, sai kuma ya ɗauke kai ya saka hannu ya ɗauki Fiyya zuwa cikin mota bayan ya kwantar da ita ya tsaya yana kallon wanda ke ɗaya motar a tsaye da yake ce masa "Ya akai kuka barta ta fito cikin dare haka? Macace ita fa"

"Sir ƙuruciya, thanks for the call"

"Anything for you Captain Aliyu" suka shiga mota duk suka bar wajan ya rage sai jami'an F.i.d kawai da suke tambayar baba.

Su Goje cikin kwalabati suka shige suka ɓoye suna zare idanu da muzurai a hankali ya ce "Akwai matsala jami'an tsaro ne fal yasin, baka dai bar sheda ba kuma me ya saka ka caka mata wuƙa idan ta mutu fa?" Moh ya yi shiru can ya ce

"Ba zata mutu ba"

"A ciki ka soka mata wuƙar fa? Baka kalli yadda jini ke zuba bane da zaka ce wai ba zata mutu ba?" Kai tsaye Moh ya ce "ba zata mutu ba"

"A buge kake shi ya sa, askira ka caka mata fa na ɗauka tsoratar da ita kawai za ta yi"

A firgice ya kalli Goje idanunsa kamar za su faɗo "Goje, idan ka sake maimaita mini cewa na saka mata wuƙa zan maka jahilci yanzu wallahi zan iya kashe ka"

"Kashe ni mana daman ai daba babu wata amana a ciki dole na faɗa, ɗaƙkota aka ce kawai ka yi ba kashe ta ba" Mutallab ya wani juya cikin zafin nama ya damƙo wuyan Goje cikin sauri Darma ya shiga tsakiya ya ce "Sai godiya kar a yi haka akwai amana, kai Goje ka iya bakinka idan ba farkawa kake so ka yi ka ganka a ƙiyama ba" Moh ya cije bakinsa kansa na wani irin sara masa yana girgiza kansa ya kalli sama "duk sanda na sake ganinta sai na kashe ta don uwarka" duk sukai masa shiru sun daɗe a wajan kafin jami'an tsaron su bar wajan suka fito tare da barin wajan suma kallo ɗaya za ka yi wa Moh ka ɗauke kai saboda yadda yake huci ya fiddo da ƙarin jikinsa neman inda zai sauke kawai yake.

The following days.

I. Qasim ya ce "Tunda ta bar I.c.u ai Allahamdulilah, she will soon recovering"

"Dr Qasim ba dai abin ku kuke mana na likitoci ba, ya jikin Maama don Allah ita ce kawai last hope ɗina" Dr Qasim ya yi murmushi ya ce "Safiyyerh zata ji sauƙi in sha Allah, ba'a caka mata wuƙar inda za ta yi mata illa ba ta zubar da jini sosai ne sai kuma zuriyarta data ninka gudun da take yi, ka yi mata addu'a"

"Shikenan Allah Ya bawa Maama lafiya,zan iya shiga ai kwana biyu ba'a barin mu shiga sai na ji kamar har yanzu bata dawo hayyacinta ba" I. Qasim ya girgiza kai ya ce "Daddy kana son Safiyyerh da yawa, shiga ka ganta" har bakin room ɗin da take ciki ya shiga ya shiga sanye da kayan daya dace a shiga aga mara lafiya. I. Qasim ya juya ya fita daddy ya zubawa Safiyyerh idanu tana ƙwace ta sake yin fari a barka da farar mace ta ɗan faɗa an ja mata rigar marasa lafiya zuwa saman ƙirjinta duk da baya kaya a jikin sai iya rigar an buɗe wajan ciwon da akai mata aiki a wajan ya zuba mata idanu ya matsa a hankali yana kama hannunta addu'a ya shiga yi mata sosai ta samu sauƙi zuciyarsa duk babu daɗi idan ya rasa Maama bai san yaya zai yi ba kuma.

"Allah Ya baki lafiya Maama, don Allah ki rage wa kan ki fitina da zaƙewa cikin wasu al'amuran kalli yadda za ki saka rayuwarki ta lalace, Safiyyerh ban shirya ba ban shirya ba Safiyyerh" ya damƙe hannunta yaga bakinta na motsawa amma sam baya jin me take cewa. Ta shi ya yi ya fita yana sake yi mata addu'a a ransa na samun sauƙi da rangwame.

Bayan ya fito waya ya saka ya kira Aliyu yana ɗagawa ya ce "Aliyu kana ina ne, an fito ita daga i.c.u amma babu kai a wajan bana son haka fa, da baya da yanzu ba ɗaya bane matsayin Safiyyerh ya jima da sauyawa"

"Allah Ya sauwaƙe"

Kawai Aliyu ya furta ta cikin wayar daga nan ya yi shiru ran daddy ya sake ɓaci yana jin kamar ya yi kuskure na aurawa Aliyu Safiyyerh na damƙa masa dukkan ragamar rayuwarta da tunanin zai kula da lamarin Safiyyerh amma ba lallai hakan ta kasance ba, sosai abubuwa da yawa ke damun zuciyarsa yana hana shi sukuni tare da rashin isasshen bacci, idan Safiyyerh ta tare a gidan mijinta dole ne ya amshi responsibility da Ubangiji ya ɗora masa na mijinta.

Ummi na kallon daddy da jajayen idanunta ta ce "Ina ta zuba idanu rayuwar yarinyarta na neman lalacewa, ka yi abubuwa da yawa Professor na ja baki na yi shiru da tunanin duk abin da ka yi daidai ne, zuciyata ba zata ɗauka ba Safiyyerh gabaɗaya nawa take ni kawai ta haƙura da aikin wannan Companyn da bana gane masa ai shekarunta bai kai ya kawo ba, ban shirya rasata ba" daddy ya yi shiru yana kallon yadda Ummi ke kuka.

"Ki tashi muje dare na yi" da sauri ta kalle shi tana share hawaye ta ce

"Kuma ban gane muje ba zuwa ina?"

"Ai kin san majinyata basa kwana a wannan hospital ɗin, patient ne kawai yake da alhakin kwana" tun kafin ya kammala magana take girgiza masa kai "i don't think zan iya barin wannan asibitin da Safiyyerh ita kaɗai, ni bana ma ganewa irin haka ka yi musu magana ko a nan zan iya kwana I'll manage" Daddy ya yi gaba yana furta "Kar na sake maimaita miki" dole ta miƙe bayan ta sake leƙa Fiyya ta yi waje.

Kafin a rufe shigowar masu ziyara Yaya J ya daɗe zaune gaban Fiyya yana kallon fuskarta, da kwanakin baya ne zai riƙe hannunta cikin nasa yana ta mata sannu da addu'a yanzu kallon ta kawai ya kasa koda yin addu'ar ma, can ya miƙe ya fice haka Awais da Dr Hash duk suka shigo basu da tabbacin bacci take ko farkowa ne ba ta yi ba. Wajajen 2 na dare ya buɗe ƙofar ya shigo bayan I. Qasim ya bashi damar hakan daman aikin kwana zai yi idanunsa a kanta har ya shigo ya rufe ƙofar a hankali ya tsaya gabanta hannunsa biyun zube cikin aljihu ya ɗauki minti a ƙalla ashirin kafin ya ƙarasa ya zauna bakin gadon har yanzu bacci take ya dubi hannun da ruwa yake shiga ya dubi ɗaya hannun da jini ke shiga a hankali ya kama hannun drip ɗin da yake ɗan mitsi-mitsi ya riƙe cikin nasa a hankali yake murza yatsunta can ya ji ta riƙe hannunsa ya ɗaga kai yaga tana jujjuya kanta sai a lokacin ya lura da sauyin ƙarar da na'urar ke yi.

Safiyyerh tana buɗe idanu ta rufe saboda wani fau ɗin haske daya shige mata ciki sai kuma hawaye ya fara bin idanunta ya ɗan sunkuya yana kallon fuskarta. Ta sake buɗe ido ta kalle shi ta dudduba taga ba kowa ta rufe idon still ta buɗe har lokacin jujjuya kanta take yi "Yaya" ya yi mata shiru ya sake cewa

"Me na yi musu?" Still shiru ya yi mata ta buɗe idanu ta kalle sai ta fashe da kuka sosai ƙirjinta na ɗagawa ya damƙe hannunta

"Yaya"

"Safii..." Ya kira sunanta a hankali ta ce "Kai na zai cire ƙirjina ciwo cikina ciwo yaya mutuwa zan yi"

"Allah Ya yi miki Rahma" sai kuma ya matsa dab da kan nata ta saka hannu ta riƙe nashi ta yi shiru a hankali ta sake cewa "Captain"

"Manager"

"Na ce musu mijina soja ne, wai ko sojan zasu kashe balle ni" ta yi shiru ta sake cewa "Ka riƙe mini kai na ciwo yake mini sosai na shiga uku daddy wayyo" maimakon ya riƙe kan nata sai ya ɗora goshinsa saman nata, ta buɗe idanu ta kalli fuskar Captain kamar zau haɗe da data a nutse ya ce "sun kashe kin?" Ta girgiza kai

"Me ya sa?"

"Ban sani ba" ya ɗan murza mata goshinsa yana kallon cikin idanunta ya ce

"Saboda ke matar soja ce" ta yi shiru kawai tana kallon shi can ya matsa yana sauka ya zauna saman kujera.

Washegari da sassafe yan sanda suka shigo room ɗin lokacin tana zaune ta ɗan jingina da jikin gado, statement na abin da ya faru suke tambaya. Sp Ghali ya kalli Safiyyerh data sunkuyar da kanta ƙasa ya ce "Da suka zo sun faɗa miki abin da suke buƙata?" Ta girgiza musu kai.

"Za ki iya gane wani daga cikin su? Suna ko kammani?" Ta ɗago ta kalli Sp Ghali dake tsaye ta ce "Idan na gane kamannin sai me za'a yi to?" "Zamu kira a zana mana fuskar wanda kika gane ne"

"To ban gane ba"

Duk suka tsora mata idanu musamman daddy ta buɗe idanunta itama ta ce "Kamarya? To na gane ne?" Daddy ya ce "Maama wa kija ji ya ce wani abu?"

Sp Ghali ya dinga kallon Safiyyerh yana jin wani irin abu a ransa na motsa masa sai ya yi murmushi ya ce "dear kin ce basu nemi komai ba, ba wanda kika gane ba suna amma haka kawai sai su caka miki wuƙa think Safiyyerh" sarai Safiyyerh ta tuna sunan da ta ji ya ambata na Mutallab sai ta yi shiru a hankali kuma ta ce

"Sp kasan matsalar da ƙasar nan take ciki musamman Jiharmu akan ƙwacan waya, wayata zasu ƙwace ni kuma na hana saboda ina da abubuwa a ciki shine sukai mini haka" ya jinjina kai ya ce "Haka ne dear za mu yi bincike zan gano kowaye za mu hukunta shi ƙarƙashin hukuma bisa kundin da aka wanzar, get well soon dear" ya sake faɗa yana murmushi kan ta dai a ƙasa yake. Sallama sukai dasu daddy suka tafi. Captain na zaune ko tari bai yi ba wayarsa kawai yake dannawa can ya miƙe ya fita daddy ya bisa da kallo haka Yaya J ganin ko sannu bai yi Fiyya ba daman bai jima da zuwa ba.

Eng Ali wali ya dinga kaiwa yana kawowa ransa duka a ɓace ya kalli Mai dawa ya ce

"Yanzu daka kashe ta fa? Wai me kake nufi da wannan abin da ka yi ne Mutallab?"

"Ka dai na yi mini ihu kamar Malam Abdullahi" Ali wali ya jinjina kai kawai ya ce "Kasan ka raina ya ɓaci kake cewa haka? Ya zan aike ka ka yi sato yarinya kuma ka caka mata wuƙa salon ka ɓata mini aiki da sanyin safe ake kama fara ba mai dawa"

"To na fasa"

Ali wali ya buɗe idanu ya ce "Meka fasa ɗin? Ba dai ɗakko yarinyar ba kake nufi?" A taƙaice ya ce "Shi"

"Haba uban mafarauta, kai baka san wasa ba kai kamar ɗa kake a wajena fa" sai a lokacin Moh ya buɗe idanu ya kalli Ali wali yanzu dai normal yake ba'a buge ba "baka haifan ba, san da aka haifan baka da labari" ya yi fito yana miƙar da ƙafa ya ce "To ka kira ɗan naka ya yi maka aikin, mu fa kuke sawa a wahala har a yi zaɓe aci a cinye ka hau kujerar ba lallai yaranka suna ƙasar ba, ba'a rainawa Moh hankali ka bar mu matsayin yʻan daban kawai" Ali wali ya ce

"Ya batun yarinyar?"

"Na ji" ya ce yana miƙewa tsaye har zai shige ya dawo ya ɗauki bandir ɗin kuɗi yʻan dubu-dubu ya watsa cikin aljihu. Sautin daya ji kamar gurnani kamar kuka kuma ya sa ya nufi ƙofar da yaje jin hakan ya murɗa handle zai buɗe cikin sauri Eng Ali wali ya riga shi ya ce "Haba Mutallab idan iyalina ne a ciki fa?" Moh ya zubawa Ali wali ido ya kalli ƙofar sai kawai ya fice yabar wajan. "Ɗan wahalar yaro ɗan jaraba Allah Ya nufa na lashe kujerar ganina sai ya yi maka wahala"

Hon Maɗatai yana zaune ya kalli Sp Ghali ya ce "Ka lemo record ɗin nasa?"

"Na samu Hon amma cin dai amana ne irin namu na jami'an tsaro amma fidda record ɗin wani criminal ya saɓawa kudin tsarin ƙasa" Hon Maɗatai ya ce "Waye Mutallab?" Sp Ghali ya ce "Nothing serious about him hon, shekaru uku da suka shige an kama shi da laifin kashe matarsa ranar da aka kai masa ita matsayin amarya, kafin nan yana da record na zama gidan yari na watanni sai kuma taɓa guduwa Legas, a baya kuma kafin hakan shi mafarauci ne ma'abocin shiga jeji ya yi farauta"

"Hon akwai matsala ne? Na ga ka yi shiru?"

"Batun Scorpion ba, case ɗin yarinyar nan Manager a ranar ance shima Scorpion ya je wajan" Sp Ghali ya ce "Hon Scorpion da yʻan siyasa irin ku yake da matsala fa, ko mutumin daya kashe last yana da za hujjar kisan mune dai bamu sani ba, waye

Scorpion ba wanda ya sani jami'an mu na neman shi haka F.i.d Federal investigation department wallahi suna kama shi wannan kisa ne nan take ko su yi masa allurar hauka" "Al'amarin Scorpion ya yi kama da ɗaukan fansa fa, za mu zuba ido ya kashe mu ne? Ku hanzarta nemo ko waye Sp Ghali"

"In sha Allah Hon"

Aliyu na zaune saman kujera daddy ya ce "Kaji ai ko?" Ya jinjina kai kawai "Zuwa dare sai ka ɗauke ta ku tafi can part ɗin dake gidan daman tuni an zuba komai empty dai yake to ɗazo an kaiwa Safiyyerh kayanta, Aliyu Safiyyerh amana ce idan ka ci amana ba zan yafe maka ba, na yi haƙuri na rabu da kai amma na so kun bar ƙasar gabaɗaya" addu'a daddy ya yi musu sosai duk da Fiyya bata wajan. Aliyu ya tashi ya fita. A daren ranar yan jarida suka shigo saboda hirar da za su da daddy. Sosai aka yi hirar inda yake cewa. "har kullum ni Professor Abdu Marafa bana goyan mutumin da bashi da wata nagarta wanda baya duba rayuwar yaranmu matsa wanda kuma zuwa gaba sune zasu gaje mu, duk wanda ya buƙaci ku zaɓe shi ku fara duba nagartar shi waye shi, bane background na rayuwarsa waye shi tun farko? kar a yi amfani da talauci da rashin iliminku a saka ku yi zaɓan tumun dare a wannan lokacin matasa yana da kyau ku yi gangami ku magana da murya ku saka iyaye na gida ƙanne da yan'uwa su zaɓi cancanta, wannan masu gamu taliya gishiri ko masu siyan ƙuri'ar mu basu ne wanda suka dace ba, ƙuri'armu ita ce ya'cinmu kana siyarwa baka da damar yin zaɓe ku kalli yadda ake mayar da ƙananan yaran yan daba masu bangar siyasa ana basu ƙwaya suna aikata zunubi suna kai kansu inda za'a kashe su, ku faɗa mini ko sau kun taɓa ganin ɗan wani daga cikin yan takarkarun nan? no! Sai yaran talakawa wanda basu da ilimi ko basu da sana'a sai a yi amfani da wannan damar a janyo su a kurɓata musu rayuwa a ƙarshe kuma ko gidan yari yaro ya tafi wallahi sai dai iyayensa su yi fafutuka duk da cewa har da laifin wasu iyayen a lalacewar yaran, matasa ku haɗa ƙungiya da za ku dinga taimakon juna kar ku yadda da mulkin kama karya kuna kallon shekaru huɗu da suka shige yadda zaɓe ya kasance"

"Professor Abdu Marafa kenan a yayin da yake bawa matasa shawara akan su miƙe tsaye domin ƙwatuwa jiha yan'cinta. Professor mai ya sa duk maganar da zaka yi akan matasa ne? Da batun shaye-shaye ko daba?" Daddy ya rantse idanunsa yana jin zuciyarsa na yi masa zafi can ya ce

"Dan jarida kenan baki abin magana, saboda matasa sune yau, sune gobe haka jibi matasa sune cigaban ƙasan idan har aka tsaya musu aka fitar da iri mai kyau,

shaye-shaye kuma....," sai kawai ya yi shiru. Yakasai ya ce "Gabaɗaya abin da zamu iya naɗa kenan a wannan satin, zamu cigaba da bibiyar professor Abdu Marafa domin ganin haƙar tasa zata cimma ruwa ko yaya ne? Ni Khalid A Yakasai nake cewa a huta lafiya"

****

Numfashi Mutallab ke fitarwa a hankali jikinsa duk yanka saboda faɗan da suka yi da yan cikin gari bai san adadin mutanen daya sara ya fitarwa da jini ba, bashi da tabbacin ko bai yi kisa bama rabin fuskarsa duk yanka ne wani wajan har ya zame masa tabo. Goje shima cikinsa rauni ne da ƙyar yake fidda numfashi a hankali ya ce "Sun kashe Darma fa, ni ban ɗauka haka zuwa kamfel ɗin yake ba, wallahi sun kashe Darma na yi ƙoƙarin kai masa ɗauki amma ta kai nake"

"Goje"

"Na'am, Sarki"

"Nemi maɓoya" ya ce "Idan na ɓoye kai fa? Naga ba zaka iya tashi ba gwara ni ma kai ma da tuni sun kai ka kushewa, gashi wannan ɗan jakar Mangal ban san inda yake ba, balle a jira Ali wali a faɗa masa koda taimakon da zai mana"

"Wai baka jina idan ba ƙiyama kake shirin zuwa ba ka tashi ka face Goje" da sauri Goje ya miƙe ya yi kwana saboda ƙarar motar kwalawa da ya ji, Moh ya saka hannunsa a aljihu ya danna laya tuni ya ɓace a wajan.

Abbasa ta dinga kallon Mutallab kamar baya numfashi ta girgiza kawai ta kalli mai yi masa treatment ɗin bayan ya gama ya miƙe ta ce "Sannu da ƙoƙari" ya jinjina mata kai ya fice kawai. Ta yi shiru tana sake kallon Ɗan'malam.

Kamar yadda daddy ya buƙata Safiyyerh ta tare cikin part guda da yake gidan daga can baya, ita dai da to kawai take binsa sai kuma idanu ta yarda ba zai zaɓa mata abin da bai dace da rayuwarta ba, ta amince zata zauna da Captain Aliyu zata koyi son shi. Cikin sauri yake gudanar da komai kamar mai tsoran wani abu. A harabar

gidan Aliyu na tsaye yana kallon Awais da yake cewa "Yaya ban gane tambayar da kake mini ba"

"Ya sunanka ma?"

Da mamaki Awais ya ce "Ikon Allah Yaya ni fa ƙaninka ne tsayin shekaru baka san sunana ba?" Aliyu ya haɗe fuska ba wasa ya ce "Kuma dole akai na haddace, seriously bana iya tunawa"

"To kai ne Baba captain Aliyu sai Junaid sai Dr Hash sai ni Awais sai Maama" "Ok, shi likitan wanne allura ya ke yi mata ban damu na san ba a baya yanzu ina so"

"Wai Dr Hash da ya kewa Fiyya? Ban sani ba gaskiya Yaya why not ka tambaye shi?" Wata tsawa ya dakawa Awais yana cewa "Get lost mumu" fita ya yi daga cikin gidan gabaɗaya.

Har ɗaya saura Safiyyerh na kwance a bedroom ta yi shiru tana jin ciwon na yi mata zafi ta yi kuka sosai na rashin sanin dalili har bacci ya ɗauke ta. Cikin bacci ta ji an buɗe ƙofar an shigo ta yi saurin rufe idanu yana sanye da kayan bacci farare ya ƙarasu ya duba magungunan yaga ko ɗaya bata sha ba, ya ƙarasa bakin gadon ya zauna shi gabadaya ya manta cikakken sunanta na gaskiya rashin sanin ne zai ce kawai ya saka hannu ya janyo ƙafafuwanta zuwa ƙasa ta matso dab da shi da sauri ta buɗe idanu, suna haɗa idanu ta tura baki tana juya fuska

"Zan saka bindiga na harbe ki a iska kina juyawa" ta kalle shi ta ce "To yaya ciwona ka fama mini" kallon da yake mata ya saka ta miƙe zaune "kin accepting auren?" Ta jinjina kai ta ce "Na yi kamar yadda ka yi na san daddy yana da nasa dalilin damuwata ɗaya na rashin sanin gaskiyar ni ce yar daddy ko kai, amma aure tun kafin na zo duniya Allah Ya rubuta wanda zai zamo miji gare ni ina da sani daidai gwargwado zan zauna ƙarƙashinka duk da baka so na, ko kana so na?" Ya girgiza mata kai alamar

"A'a"

"Ni ma,sai mu koyi son juna" ya kalleta kawai sai ya ce "Muga ciwon" "Yaya a wajan ƙirjina ciwon yake fa" da rashin fahimta ya kalli ƙirjin ya kalleta kuma ya nisa ya ce "Kuma mene a ƙirjin?" Ya faɗa yana yaye rigar.

WE'LL SOON END OF THE FREE PAGES. Ku hanzarta biyan 500 domin karanta Mutallab posting za mu babu ɓata lokacin ba lallai ku fahimta a yanzu wanda suka shiga paid group sune da batu ko rabin book 1 babu shiga ba. Tsakiyar labarin akwai muke, mene ya faru a farko me zai faru tsakiya ba zaku taɓa sani ba ko a sashe.

MUTALLAB.

Book 1, 2 &3

500 Naira

0116886423 Union Bank Na'ima Sulaiman S a tura shaidar biya ta nan 08164069385

[1/7, 9:33 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

Page 12

Bright pens..2nd batch

Hannunsa ta cire da sauri ta ce "ciwon fa a wajan ƙirjin yake yaya" da mamaki Captain ya kalleta ya kalli ƙirjin, da gaske bai san mene matsalarta da hakan ba. Ya ɗauki lokaci kafin ya ce "kuma mene special a ƙirjin?"

"Baka sani ba?" Fiyya ta buƙaci jin amsa ganin har lokacin kallon ta yake da alama processing ƙwaƙwalwarsa take yi shi dai ya san wajan da aka caka mata wuƙar kawai zai gani. Bai sake cewa komai ya miƙe tsaye ya nufi fita, Fiyya ta bisa da idanu tana jinjina rainin wayon Captain yana abu kamar baya fahimta. Ta yi shiru bayan fitar tasa, ta ɗan jingina da jikin gadon thinking me ya sa abubuwa suke juyawa tare da faruwa ne? Ba wani tsanar Captain ne a zuciyarta sosai ba, kawai

yadda yake abubuwansa ke ƙular da ita amma kaf yayyanta tana matuƙar so da ƙaunar su. Damuwar bai shige dalilin daddy na aura mata Captain ba, bayan shi blood brother ɗinta ne. Yanzu ita ce ba jinin daddy ba ko Aliyu? Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un!

Da sauri ta riƙe ƙirjinta jin zuciyarta na harbawa, duk yadda take ƙoƙarin ko a cikin bacci ta sake ganin gilmar reflection ɗin shi ta gagara, ko sautin muryar tasa ma ta mata sai kuma tunanin mahaukacin daya caka mata wuƙa ya faɗo cikin ranta wai shi Mutallab? Who is he?

"Who is he?"

Muryarta ta sauka a tsakar kanta tana nanata mata tambayar da zuciyarta ta yi mata a fili. "To ya ɗauke ni ya yi mini me? Safiyyerh Abdu Marafa ai ba sa'ar yara bace, bata zama teddy ba, the whole manager anya ya san me yake ce mini? Ba sai ya sake ganin ko inuwar fiyya ba balle ya aiwatar da abin da ya yi niyya a kaina, aikin banza aikin wofi don ma dai ban san ya zaro wuƙar bane zuwa gaba Captain zan lallaɓa ya ara mini bindigarsa problem solved"

Ita kaɗai take ta yin mita ta zubawa madubi idanu bayan ta miƙe tsaye. Wanka ta yi tare da alwala bayan ta idar da sallah ta ɗauki skin products mai kyau dake sa fatarta laushi ta yi ta ƙyalli, tana son amfani da kayan Aisha s bayero skin care nd herbal medice, ta ɗauki riga mara nauyi saboda ciwon jikin nata. Kasa bacci ta yi ta ɗauki system ɗinta ta fara dannawa hannunta riƙe da ruwan zafi ta jima suna tattaunawa da Md da Secretary ta email kafin ta rufe system ta yi addu'ar bacci ta kwanta sai dai ciwon ya dameta da zafi har zazzaɓi ya saka ta.

Washegari da ƙyar ta yi sallar asuba don bata yarda ta shige ta, ta rufe jikinta da duvet ta girgiza kai da ƙyar baccin ya sake ɗauke ta. Har 12 bata fito ba, sanin abin da ya faru da ita ya saka ba'a nemi ba'asin rashin zuwan nata kamfani ba.

Wajejen ƙarfe biyu ta buɗe idanunta dalilin ƙamshin da ta ji da kuma goshinta da ake murzawa a hankali, ta juya ta kalle shi taga waya ya ke yi muryarsa ƙasa tana jin yadda yake magana one by one jin ana kallon shi cikin sauri ya ce "i will call you later"

Ya juya suka haɗa ido a hankali ta ce "Ina yini?" Ya yi mata shiru yana kallon kanta da sauri itama ta kalla sai yanzu ta lura kan nata yana cinyarsa ne shi kuma hannunsa na gefen fuskarta "ɗaga ni"

"Yaya bani lafiya fa" ya harareta kawai ya yi shiru shima ya ji zazzaɓin ta juya masa baya tana sauke kanta idanunta rufe zafin zazzaɓin na ƙaruwa ji tayi ya ɗago ta zaune kamar wacce zai zaunar a cinyarsa ya faki idanunta ya damƙe gefen cikinta ta yi ƙara tana riƙe shi "Ki dai na yi mini sauti haka, za ki je zaman barrack lazy" ta haɗe fuska tana ji yana taɓa cikinta yaga wajan ciwon na jini ya saka hannu ya shafi ciwon ya taɓo jinin da hannu can ya miƙe yana juyawa.

"Captain jini wajan yake yi ka fama mini na shiga uku" idan ba kuskuren ji ta yi ba, muryarsa ta ji ya furta "Allah Ya ƙara"

Cikin dare ne yana tsaye ya fito daga cikin motarsa sanye da manyan kaya na alfarma da fuskarsa rufe da facemask ya dubi yaran da suke gabansa ya ce "Ina buƙatar aiki cikin gaggawa bana son wani mistake idan aka samu akasi ina cikin taraddi, kuna kallo abu ya taho lokacin na neman cimmana" Ya buɗe idanu yana sake dudduba inda yake tsaye gani yake kamar ana ganinsa za kuma a iya gane wanene shi.

"Mai gida wanne kalar aiki ne ya fito da kai cikin duhuwar nan, faɗa taka cikawa tamu sai da kai iya wuya ba wani shege a baya wallahi" ya ɗan yi murmushin jin daɗi yana kallon mai maganar da kana ganin shi zaka san a buge yake cikin maye kamar kullum

"Idanun mutane nake so, maza uku mata uku" ya ce yana kallon wanda yake faɗawa maganar ganin yadda ya yi shiru kamar dai ban fahimta ba. "Aiki ja idanun bama na mutum ɗaya ba? Akwai kuskure fa"

"Yanzu akwai wani aiki da zan iya sakawa ka yi mini da zai fi ƙarfinka? Kai ɗin amintacce nane na kuma yarda da ƙwarewarka ina jin daɗin business da kai wallahi" ya zaro kuɗi masu yawan gaske ya miƙa masa, ya sake zaro wata ƙwaya kala daban-daban masu kyan gaske da tsada kana gani kasan manya ne ke shan irin ta. "Ka fara riƙe wannan kuɗin nasan kana buƙatar caji a kanka kafi yin aiki yadda ya kamata, idan ka kammala ka sanar mini zan faɗa maka inda zaka ajjiye

ko?". "Ka yi ƙarko irin na dabino sai da kai wallahi yau zam dani, ko kan mutum ka ce na kawo maka a yadda ƙwayar nan ke buɗe mini tunani kawowa zan, ba ƙaramin ilimi ne dani ba da tuni fa ni zan yi ministan kuɗi nace na fasa, kaf ƙasar waye bai sanni ba don uwar mutum" sambatu kawai yake na maye ya bugu ƙarshen buguwa, shi mutumin dariya kawai yake basa hakan kuma na yi masa daɗi ainun. Mota ya shiga ya bar wajan shi kuma ya gangara ya shiga lungun titin da suke. Tunda ya tafi ya zauna cikin yan'uwansa mashaya yake tunanin ta ina zai fara? Ina zai samu mutane har ya ƙwaƙwule idanunsu hankali kwance? Ya yi shiru yana kallon sama yana ta furzar da iska mai ɗauke da warin sholi dana bakin gabaɗaya.

*****

Mutallab ya tanƙwashe ƙafafuwansa kamar wani sarki ya kuma ɗora hannunsa saman cinyarsa cikin kowacce ƙafa, kallon Abbasa yake tun ɗazo take magana yaƙi cewa komai ko tari kuma bai yi ba, raunukan jikinsa ya kame sai saura, ido biyu za ka yi da shi ba zaka ƙara marmarin kallon nasa ba, babu rahama a fuskarsa nan zaka ɗauka tunda Ammo ta kawo shi duniya bai taɓa yin murmushi ba, ko haɗa hanya da inda fara'a take.

"Kalli nan"

Ya dubi abin da take nuna masa, zanen kamfanin ne da photon jariran sai kuma kalmar A.M.A "Da fari mu fara gano ma'anar kalmar A.M.A, photon jariran kuma mai sauƙi ne ana nuna maka har jarirai da aka haifa yau ana siyar da shi a kamfanin FS WORLD INVESTMENT COMPANY, abu biyu ne wanda dole za ka yi ko kusan ukun, da fari sato ita wannan yarinyar ta yiwu a samu wani haske tattare da ita, na biyu kasan yadda duk ka yi ka mallake wannan kamfanin cikin sauƙi, na uku...," sai kuma ta yi shiru ta dinga kallon Moh ciki da bai

"Waye Mutallab, waye kai, dole ka faɗa mini asalin waye kai kana ji na?"

"To na haƙura"

Ya miƙe tsaye a hankali a lokacin ras yake sai abubuwan da sukai masa tsaye a zuciya da maƙoshi "Dole na san waye kai, ko ka faɗa mini ko ba ka faɗa ba, abu na uku sai ranar da asalin naka ya zo kunnuwana zan furta maka shi" bai dai yi

magana ba, hannunsa zube cikin alijun kayan da Abbasa ta basa ya sauya da ƙyar yafi ƙarfin minti ashirin a tsayen yana harhaɗa kalmomin abin da zai ce mata ransa duk a jagole. "Lalacewar Moh bai kai ya sato yarinya ba"

"Kuma dole a yi hakan fa"

Ya yi waje abinsa yana yana ƙoƙarin ficewa daga cikin bukkar ta ce "Baka da lokaci fa Mutallab, kuma baka da ikon taɓa ta a waje idan ba kana shirin komawa gidan yari bane, kasan yadda za ka yi dai wish you all the Mutallab"

Bai ƙara bi ta kanta ba, ya dinga ɗora ƙafafuwansa a ƙasa kamar mai tsoron taka ƙasa sai haɗe fuska yake yana kwaɓewa duniyar ya ji ta yi maza zafi ta ko'ina, ya rasa ina zai je me kuma zai yi sai ɗaga yatsun ƙafarsa yake wanda suke zara-zara matar nan Abbasa ta fara takura masa ko waye ya ce ta yi masa gyaran farce? Yama a ka yi ta samu mai yin aski ya wani kwashe masa suma? Bakin bishiya ya samu ya zauna ya sunkuyar da kansa ƙasa, zufa ta shiga tsattsafo masa ta tsakiyar goshi ya sa yatsa ɗaya yana gogewa ya shafa jikinsa ba kayan garawa ko ɗaya yana buƙatar fita daga yanayin da yake ciki, baya son tunawa ko da wasa.

“One day i will leave you, duk son nan da nake maka”

Ya ji saukar muryarta a kansa ta sauka har ƙasan zuciyarsa a ɗan lumshe idanunsa da ya yi, ya juya zuwa gefe sai yake ganin bidiyon abin da ya faru bayan kammala assembly, at that time yana can baya zaune ya yi shiru yana kallon students bai san da zuwanta ba sai ganinta ya yi ta baya kamar zata shige jikinsa ya fiddo manyan idanunsa waje yana miƙewa tsaye hannunsa ɗaya zube a aljihu ya dinga kallon ta da ƙyar ya furta "And what is this Safiyyerh?"

"Bestie shi ake cewa love mana" ta langwaɓar da kai gefe yana sake kallon yaluwar fuskarta kamar zabiya. "To iskanci za ki mini?"

"Iskanci kuma bestie? Me ya sa kake haka ne, son ka kawai nake yi fa why are you doing this to me? Kai ba'a gane maka sam? Ko murmushin masoya ne ka dinga yi mini mana, bafa ni na ɗorawa kai na son ka ba" idanunta ya cika da waye tana jin zuciyarta na yi mata zafi bata ganin komai a idanunta sai fuskar Mutallab.

"A love? Shine za a yi wa mutum fyaɗe a soyayyar??" Ta buɗe idanu tana rufe baki jikinta har rawa yake tana jin kamar ta idda abin da zuriyarta ke umartar ta "To ka yi haƙuri idan dai na mutu ka huta, kuma idan baka zo gidanmu yau ba Allah a wajan Ammo zan kwana" fuskar nan a ɗaure ya ja sirirn tsaki ya shige cikin class kafin ya ƙarasa ya ƙara jiyo ta a bayansa tana sake yunƙurin riƙe shi da sauri ta juya sai kuma ta ɗauki school bag ɗinta ta fice daga makarantar tana kuka.

*** "i missed the hug" ya furta ƙasan zuciyarsa lokacin da bidiyon abin ya ɗauke daga kusa da shi, ya yi shiru yana tunani har yamma ta yi lis bashi da niyyar tashi daga wajan baya son shiga cikin jama'a yana jin nan ɗin shine daidai da ina ya kamata ya ɓoyewa kwalawa. He feels uncomfortable a cikin jama'a haka nan.

Safiyyerh na zaune bayan ta dawo daga kamfani ko ɗaki bata shiga ba idan ta tuna yadda Hon Maɗatai ya sake matsa mata akan hannun jarin da yake son sawa a FS WORLD INVESTMENT COMPANY sai ranta ya sake ɓaci, duk dukiyar da Ubangiji Ya bashi bai gode Allah ba, mutane nawa ne a wannan duniyar da basa ci, idan anci na safe ana fargabar na rana, idan na rana ya samu dare kuma sai dai a yi salatin Annabi a sha ruwa a kwanta, masifar rayuwa ta yi wa talaka dirar mikiya, yunwa na neman illata su ga lalura ga rashin aikin yi? Amma hon Maɗatai shi dukiya yake nema idanu rufe yɗan siyasa da yawa kansu kawai suka sani suke ginawa, mene amfanin talaka ya je ya yi zaɓen? Gabaɗaya sabgogin dimokuraɗiyya ya lalace son zuciya kowa yake bi. Ta yi tsaki tana jin ko zata rasa kujerar Manager ɗin ba zata taɓa bari Hon Maɗatai ya saka hannu a kamfanin ba.

Miƙewa ta yi ta nufi bedroom bata ɗauki wani lokaci ba ta fito sanye da wando da riga,wandon iya cinya kanta ko ɗan kwali babu da mamaki take kallon Captain ganin ya ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya yana danna mata system ga wayarta a hannunsa kafin ta ƙarasu ya kashe system ɗin ya ajjiye har wayar. "Yaya me kake nema a system ɗita kuma?" Ya yi mata shiru ta zauna kawai tana buɗewa bata sake kallon shi ba, ta shiga duba dukkan ayyukan da aka fitar yau da sauri ta kira accouter da number da take amfani da shi na kamfanin tana girgiza ƙafa a hankali cikin faɗa ta ce

"Accouter me nake gani a haka? Kuɗi fa kimanin miliyan 500m yanzu sun shigo account na kamfani dana gani a bayanai, bayan tafiyata me aka fitar ne shinkafa ko me?" Faɗa take sosai domin ta iya faɗa ajin ƙarshe ce a fannin.

"Manager nifa kina tunawa accouter ne kawai, bani ke da alhakin saka hannu a fitar kaya ko shigowar su ba, kawai ni ke saka hannu a duk wani kuɗi da zai shigo ya fita, i am nothing but a Accounter"

Miƙewa tsaye ta yi tana riƙe ƙugu ta ce "Rubbish; ka tura mini ducoment na PDF via email na abin da aka siya har miliyan 500m yanzu yanzu accouter"

"Ki yi magana da Md ni kawai kuɗin naga shigowar su babu wani file daya zo officer nawa, trust me manager ba zan ɓoye miki, na san dai bayan tafiyarki Professor Abdu Marafa ya shigo kamfanin" "daddy!"

Ta furta da ƙarfi "E, mahaifinki shi"

"Kamarya to?"

"Shine ban sani ba" sai kawai ta kashe wayar ta ajjiye waje guda, ta sauke numfashi da ƙyar ta shiga uku meke shirin faruwa ya ake ƙoƙarin amfani da ita ba tare data sani ba?"

"Yaya" bai amsa ba idanunsa a ƙafarta ta ce "Yaya bacci nake ji" "to ina ruwana"

Sai kawai yaga ta ɗora kanta a cinyarsa maimakon ta juya masa baya sai ta juyo wajan cikinsa ta yi shiru tana kallon ƙirjinsa dake buɗe. Ta yi shiru tana sauke numfashi shi dai bai yi magana ba, bai ɗauka haka take da masifa ba yana jin ƙirjinta na ɗagawa a hankali kuma bacci ya ɗauke ta. Cikin baccin ta ji hucin numfashi ta buɗe idanu kallonsa ta dinga yi yadda ya kifa fuskarsa a tata hannunsa ɗaya tamƙe cikin nata "Captain" da sauri ya buɗe idanun ya ƙurawa cikin idanunta ido sai kuma ya ɗauke fuska yana haɗe rai. Fiyya bata ce komai ba ta miƙe zaune shi kuma ya shige cikin part ɗinsa yana taku da sauri sai shafa kai yake yi.

Notification ta gani kamar wancan lokacin saƙo ne ta dm nata. Ta buɗe ba wani magana mai tsayi bane sai dai maganar dab take da rusa tunaninta ta bi saƙon da kallo inda ake cewa.

“bai ci a ce kin yi mantuwa mai nisan haka ba, ki tuna akwai hakƙin wani kan ki Allah Yana kallon ki TIGER“ ta dafe kan ta to hakƙin waye a kanta waye mai wannan saƙon kuma? Tsaki ta yi ta miƙe ta bar parlon. Bata sake ganin Captain ba har dare ta yi kwanciyarta.

****

Cikin sauri take tafiya tana yi tana juyawa sauri take ta isa chemist amsar maganin ga dare ya raba mijin nata ya fita. Kamar daga sama taga mutane sun tsaya gabanta fuska rufe "Su waye ku? Don Allah ku rufa mini asiri magani zan siyo" muryarta na rawa ta yi maganar. Haɗa idanu sukai sai suka ɗaga ta sama tare da danna ta cikin napep ɗin basu tsaya ko'ina ba sai wani kango a nan taga wasu mutanen kwance kamar basu da rai, kuka take tana duk addu'ar data zo bakinta "Don Allah kar ku cutar dani don Allah ku rufa mini asiri da yarana da rayuwarsu"

Tana ji tana gani suka danneta tun tana ihu har ta kasa jini kamar an yanka rago babu imani suka cire ƙwayar idanunta duk biyun tare da watsa su cikin aliju da gudu suka fice daga kangon.

Bayan ta dawo daga wajan aiki ta shige gidan Anty Turai saboda kiran da ta yi mata, a parlo ta samu Anty Turai da yaranta da kuma wasu yan mata zaune. "Ina yini Anty?"

"Sannu matar Captain Aliyu Marafa?" Cewar Anty Turai ita dai Safiyyerh idanunta akan waya bata ce komai ba Waheeda ta ce "Mama wai shi Uncle captain ɗin son ta yake yi ne? Ni banga abin so a jikin wannan zabiyar ba sam sam wallahi" Zahiderh ta yi saurin cewa "Ina fa? Captain ne zai ce yana son Fiyya never wallahi, kawai dai auren dole aka yi masa, wannan fari ko na lalura"

Safiyyerh dai jinsu take Anty Turai ta ce "Sannu Safiyyerh, ya kamfanin yanzu ai Aliyun ya bar nan wajan Zahiderh ya zo ki dinga haƙuri da shi ya jaddada mini baya buƙatar ki cikin rayuwarsa bai san me zai yi da zabiya ba" miƙewa Safiyyerh ta yi ta ce "To Anty a ɗaura masa aure da Zahiderh ni bani da wata matsala, zabiya kuma ina jira ku halitto irin kalar idan da sauƙi, so kuma ba abin da ya yi mini zafi da shi zan zauna da mijina haka tunda zaɓin daddy ne, wallahi babu wanda ya kai level ɗin ɗagawa Fiyya hankali" Anty Turai ta miƙe tana nuna Fiyya idanunta ya rufe sam bata kula da shigowar shi ba, balle ankarar da ita da su Waheeda suke ta ɗaga hannu zata mari Fiyya dake tsaye tana juya idanunta ta ji an riƙe hannun.

Tun zuwan shi ta ji ƙamshin turaren nasa, ya tsaya a bayanta Anty Turai ta kalli Aliyu ta kasa cewa komai ya saki hannunta yana matsawa bayan Fiyya ya zagaye hannunsa a ƙugunta ya jata jikinsa daga baya yana sake kallon Anty Turai "Shekararki nawa Anty yaushe na zo gidan naki kuma? And who told you bana son ta?" Duk a dagule yake maganar yana sake haɗe Fiyya da ƙirjinsa kasancewarta duguwa sosai so ma sha Allah. "Aliyu ni zaka shigo gida ka faɗawa haka?"

Bai kalleta ba sai Fiyya daya kalla wacce take shirin juyawa idanunta cike da hawaye ya yi saurin riƙo hannunta yana "Wait" sai kawai ta kifa kanta a ƙirjinsa tana shasshekar kukan da bata shirya saboda ganin idanunsa "Anty karki sake mini haka"

"Idan na sake me za ka yi Aliyu na ce me za ka yi?" Ya girgiza kai ya rungume Fiyya tsam a jikinsa ya ce "Ban san me zan iya yi ba, kawai dai na faɗa miki, kuma i love my wife" Fiyya ta yi saurin ɗago kai ta kalle shi ya ɗage mata gira "Yes, I love You Safii" yana cewa haka ya kama hannunta suka fice.

***

Suna zaune a dabarsu ya yi sauri ya miƙe tsaye Goje ya ce

"Sai godiya, ina aka nufa don shirwa kake baka jewar banza, ɓauna mai tafiyar ɗaukan rai jeji naka dabbobi naka, a lafiya mai dawa" jikinsa ya ji ya fara kakkarwa tsohon tsuminsa na neman tashi ya yi ƙasa da kansa yana ƙoƙarin hana kansa yin kirari da amsar saƙon Goje, ya bar wannan layin tuni. Da ƙyar yana girgiza kai ya ce

"Goje"

"Sai godiya, wuya a ina wuya a daji kai ne mai dawa da jeji na Malam Abdu shalelen Ammo, ƙanin Sa'adah da Bafullatana a lafiya aminin Hamida, ɓauna taka mesa taka ba wani bayanka jan biro maganin daƙiƙin yaro Allah Ya ja da ran mai dawa" gabaɗaya jikin Mai dawa ɓari yake yana damƙe hannunsa wajan ganin mai ɗaga su sama ba har can cikin kansa yake jin kirarin. Kawai ya juya ya bar wajan "Wai ina zaka ne kasan yanayin da ake ciki fa akwai cinnaku"

"Baka haifan ba balle ka tambayan karka biyo ni" yana cewa haka ya bar wajan ya jima yana tafiya kafin ya ƙarasu gidan sai ya saka maƙulli ya buɗe ya shiga.

A ɓangaren su Safiyyerh tunda suka bar gidan Anty Turai suka shiga mota basu ce komai ba ya kuma haɗe fuska itama bata ce komai ba, daidai wani gida a bakin titi taga ya tsaya ya kalle ta "Kar ki fito jira ni nan" ta jinjina masa kai. Fita ya yi ta jingina tana ɗaukan waya, abin da ta fara cin karo da shi a X picture ɗin wani kyakkyawan yaro yana murmushi ya rufe idanunsa saboda hasken da ya yi masa yawa kamar ka taɓa shi jini ya fito, ta dinga kallon picture ɗin sai kawai ta yi skipping zuwa next tweet.

A hankali ya buɗe ƙofar ya shiga idanunsa zube a saman tafkeken screen ɗin computer dake jikin bango, gabaɗaya wajan nau'in kayan computer ne kala-kala. Ya ɗan dafa kafaɗar wanda yake zaune akan kujera yana juyawa a hankali, kallo ɗaya zaka yi masa kasan mayen computer ne masanin hakin da duk wani surƙulle. Captain ya ce "Where are you hiding?" Ya ɗaga idanunsa a hankali ya kalli Captain bai ce komai ba kuma ya cigaba da danna wayar, Captain ya saka hannu ya dungure masa kai ya nemi waje ya zauna yana taɓa computer shima. Da sauri ya miƙe kuma jin sautin muryarta da yadda take ƙoƙarin buɗe ƙofar ya yi saurin miƙewa ya nufi ƙofar daidai nan Fiyya ta shigo "Yaya gaskiya yunwa nake ji akwai hadari sosai a gari ina tsoron ruwa"

"Muje"

Ya yi saurin faɗa yana kama hannunta tare da rufe ta da jikinsa leƙawa take son yi ya saka hannu ya juyar da fuskarta ya jata waje, shima ɗin dake zaune ya juyo a nutse ganin sun fita ya saka ya cigaba da abin da yake yi.

Cikin dare Fiyya na bacci ta ji ana buga ƙofar parlon kamar za a cire ta, ta miƙe da sauri riga da wando ne jikinta na bacci wandon iya cinya ta saka slipper ta fito, tana mamakin mai ya sa Captain ya kai dare har haka? Ta buɗe ƙofar "Yaya ka tashe ni daga musulmin bacci da nake..." Shiru ta yi tana yin baya ganin shi tsaye a bakin ƙofa su Goje da Mangal a bayansa "Kai ne me ka zo yi mini har gidan mijina, matar aure ce ni fa" banko ƙofar Moh ya yi ya shiga yana ƙarewa parlon kallo

"Mai dawa ɗauke ta mu shige kar a yi ta kwanaki" ta gudu Fiyya ta juya zuwa part ɗin Captain tana kirin sunansa a tsora ce kafin ta ƙarasa Moh ya saka ƙafa ya falleta ta faɗi ƙasan tayal idanunsa ya yi jajur domin ba haka ya zo da su ba, jin ana shirin buɗe ƙofar ɗakin Captain Moh ya kalli Goje da sauri Goje ya laɓe a baya kafin Captain ya fito, cikin sauri ya rufe fuskarsa da ƙyalle.

"Safii are you ok? Peanut ihun nan fa wife?" Yana fitowa Goje ya saka gora ya maka masa a ka kasancewar Captain bai shirya ba ya faɗi a wajan da sauri kuma Moh ya ce Goje ya ɗauki Fiyya ko me ya tuna sai ya saka hannu ɗaya ya sunkuceta a kafaɗa yana ɗaga wuƙa sama suka fice daga gidan...

MUTALLAB.

Book 1, 2 &3

500 Naira

0116886423 Union Bank Na'ima Sulaiman S a tura shaidar biya ta nan 08164069385

Zan yi cutting free a shafi na 15 in sha Allah. Wannan shafin □□□□□□ku hanzarta yin payment kafin wannan lokacin yanzu kuma na labarin a rufe yake zuwa gaba za ku ce kun shiga uku ashe haka abin yake😂😂ina ƙara tuna muku ba fa farkon labarin muke a tsakiya muke waya san mene ya faru a farkon? Me kuma zai faru a gaba? Just pay 500 naira only.

[1/7, 9:33 PM] Sis Fauzy: *❤ MUTALLAB ❤*

Page 13

Bright pens..2nd batch

Safiyyerh na durƙushe a ɗan ƙaramin ɗakin da suka ajjiye ta ciki, warin sigari ya cika ɗakin sai yunƙurin amai take yi ta kasa, ta shiga tashin hankali da tunanin suwaye waɗannan da suka je har gidan mijinta suka dake shi tare da yin kidnapped ɗinta? Me suke buƙata a wajanta waya saka su yin hakan? Da alama ba kuɗi suke nema ba wani muradi ne a ran su da suke son cikawa manufar da bata san ta mece

ce ba. Ta ɗago kanta da ƙyar tana buɗe kumburarrun idanunta saboda kukan da ta yi da hanzari ta fara buga ƙofar da hannunta tana girgizawa tare da faɗin.

"Wai baku da imani ne me na yi muku idan kuɗi kuke buƙata ku bani waya na kira daddyna zai biya duk abin da kuka buƙata na fansa ta, macace ni fa a gidan mijina kuka je har gabansa kuka sato ni, don Allah ku buɗe mini wallahi wari zai kashe ni babu iska a ɗakin ku tausaya mini" abin da take faɗa tana dukan ƙofar da hannu, amma ko tari ba ta ji sun yi ba, kuma tana da tabbacin suna jinta ta sake ɗaga murya ta ce

"For the sake of Allah, da girman iyayenku ku mayar dani gida gaban iyayena me na yi da za a yi garkuwa dani,ku barni da raina kar ku kashe ni zan muku kwatancen gidanmu ku je wajan daddyna a baku dukkan kuɗin da kuke buƙata, idan ba ku yarda ba ku a cikin kuɗina zan baku wallahi mahaifina ya ji abin da ya same ni mutuwa zai yi, innalillahi wa'inna ilaihirraji'un me na yi muku ne kukai garkuwa dani na shiga uku ni Safiyyerh Allah ka kawo mini ɗauki" ta sake durƙushewa a bakin ƙofar ta tura kanta cikin cinyoyinta saboda warin sholi daya gama hautsina mata ciki kamar kayan cikinta zai fito haka Safiyyerh ke ji, duk girman idanunta sai da ya yi mitsi-mitsi abin ka da zabiya da ƙyar take buɗe idanun nan, ba sunan wanda bata kira ba hadda Anty Turai akan su kawo mata ɗauki Yaya J ya sha kira. Ta sauke ajjiyar zuciya tana karanta addu'ar neman tsari da kuɓuta daga magauta ta yi zumbur ta miƙe saboda fitsarin dake mintsinin mararta.

A can wajan ɗakin a cikin gidan da su Goje basu san da shi ba, duk suna zaune suna busa kayan shaye-shayensu hayaƙi ya cika wajan, wani na shan sigari wani na shan sholi wani wiwi sun hautsina sai surutai suke yi. Moh na gefe ɗaya ƙwance ƙafarsa ya ɗora akan ɗaya idan yana acting ka ɗauka jinin sarauta ne ko wanda yake da aljanu sarakai a kansa, duk ihun da Fiyya take yi da surutai yana jinta. Goje ya kalle shi ya ce "Wannan yarinyar tafa dame mu wallahi, ka kira ka faɗa masa tunjiya mun ɗakko ta ya san abin yi"

Shiru ya yi yana sake kaɗa ƙafarsa a hankali har lokacin idanunsa a rufe yake. Goje ya kalli ƙofar ɗakin da Fiyya ke ciki ya sake kallon Moh kafin ya miƙe tsaye ya ce "Ina da matsala da jin kuka gaskiya, ko dai a rufe mata bakin ko a ɓara bakin biyu yanzu da askira"

"Mangal"

Da sauri Mangal ya kalli Moh jin ya kira shi domin tunjiya da suka ɗakko Fiyya ko tari bai sake yi ba, bai runtsa ba har gari ya hawaye ba wanda kuma ya kula a cikin su. "Ankar sarki, faɗa taka cikawa tamu akwai wani sagi a ƙasa ne?"

"Bana son hayaƙin nan" lokaci guda suka kalle shi a take suka cillar da sigarin tare da saka ƙafa suka murje "Angama sai mene na gaba?" Bai magana ba ya juya musu baya a hankali ya buɗe idanunsa ya zaro takardar da yake faman ajjiya kamar rai, kusan kullum yana karantawa sama da sau wajan biyar a rana abu ɗaya ne amma sai ya ji baya fahimta,baya kuma ganewa, ya zubawa rubutun idanu Goje shima ya leƙo kai yana kallo ganin ya ninke ya ɓoye ya saka ya yi siririn tsaki "Na ji takaicin rashin makarantar da ban, shi ilimi ko yaya yana da rana"

"Ina zargin wannan takardar bata tsafi bace, kamar ita ce ransa ko iskar dake shaƙa ya manta da komai amma banda ita, watarana sai na sace ta yasin" dariya Goje kawai ya yi ya san Mangal faɗa kawai yake yi. "Mai dawa kasan a yankinmu an sace mutane har biyu, yau da sakaliya anga gawar ɗaya ba idanu" ya juyo a hankali ya zubawa Goje idanu kamar mai tunani sai kawai ya miƙe yana taku ɗaiɗai ya fice daga cikin gidan, suka bisa da idanu ganin yau ya zama wani so silence kamar ba Moh ba.

Safiyyerh ta ji an turo ƙofar da sauri ta miƙe tsaye tare da ja baya, mutum biyu take gani Goje da Mangal shi kuwa tunda ya cillar da ita a ɗakin bata ƙara ganin shi ba. Abincin hannunsa ya cilla mata da ledar ruwa pure water ta kalli takeaway ɗin da ruwan, ta ɗauke kai a hankali tana sake ja baya "Saura ki ƙi ci kamar na ɗazo, idan kuma kika sake yi mana amai a nan sai kin lashe abin ki tas" ta ƙurawa wajan ido ta ce "Ba zan iya cin abinci a nan ba, ni bana shan ruwan leda abincin ma ba irin wannan nake so ba, ko nama babu akai"

"Kuma a ina kike tunanin ganin nama? Don ma kin samu an kawo miki dar yarinya saboda kina Manager kun saba cin mai kyau a sha mai kyau, a saka suttura a shiga mota a kwana cikin a.c ga naru a gida 24/7, a ci shinkafa basmati da ruwan gora dole ki ce haka, ɗiyar ƙaruna"

Girgiza masa kai ta yi muryarta na rawa ta ce "Da gaske nake maka, ni kawai a bani ruwan jakar da lemo ko snacks" Goje ya dinga kallon ta ganin she is serious juyawa ya yi zai bar wajan ta yi saurin cewa "Don Allah ku bani waya na kira daddy na

maka alƙawarin yanzu za a kawo kuɗin da kuke buƙata wajan nan akwai sauro headache da fever zai kamani" ta langwaɓar da kai gefe alamar neman alfama.

"Ki jira Mai dawa ya zo, sai ki tambaya bani da ikon haka. Da kike maganar kuɗi kin ji mun ce muna buƙata ne? Ba kidnapped ɗin ki mukai domin a bamu kuɗin fansa ba, mun sato ki saboda a koyawa asawa hankali a rage masa tsayin harshensa da yake da kauɗi kin gane? Daga yanzu ki cire rai da samun yanci"

"Daddy?"

Safiyyerh ta faɗa a gigice tana dafe kan ta idanunta ya cika da hawaye, tausayin kanta dana daddy ya cika mata zuciya babu wani wanda take so a duniya sama da daddy da Ummi me za su yi masa rayuwarta suke son kassarawa tabbas idan suka taɓa kimar mahaifinta. "Me daddy ya yi muki, mene alaƙae sato ni da kukai da mahaifina me kuke nema a wajansa na roƙe ka da girman Allah kar ku cutar da mahaifinsa kar ku illata rayuwarsa, shi ne jin daɗi da farincikin zuciyata, ku duka kuna da iyaye na tabbata ba za ku so rasa su a rayuwarku ba ka ji tausayina Please brother"

"Ni ba brother naki bane ni ɗan daba ne sunana Goje kin gane, idan kina buƙatar wani abu kina iya bubbuga ƙofar" kafin Safiyyerh ta yi magana ya yi sauri rufo ƙofar ya fita. Ya je ya samu Moh a wajen gidan zaune ya sake tanƙwashe ƙafafuwansa ya kalle shi sosai kana ya ce

"Scorpion"

"Kana son faɗar sunan, zan manna maka hauka Goje zan ja maka ruwa". "Me ya sa baka son na dinga faɗa ne? Ai dafinka ma ya fi na kunama ni ina son sunan" Moh ya yi shiru yana sake harɗe hannayensa duka biyun ya zubawa samaniyya idanu. "Idan zan nuna maka asalin kalata a Scorpion ba zaka ɗauka ba, za ka daina haɗa idanuwa dani sauƙin sunan na wajan faɗa ne, ka kalle ni a Moh ko Mai dawa ok"

"Yadda ka ce haka za a yi, ya zamu yi da yarinyar nan yanzu? Kwananta ɗaya da wuni fa, kuma bata cin abinci"

Cikin rashin fahimta Moh ke kallon Goje su yake ya tambaye shi wacce yarinyar bakinsa kuma ya yi masa nauyi ya dinga juya idanunsa akan fuskar Goje, fahimtar hakan ya saka shima Goje cewa

"Manager wacce Ali wali ya saka mu ɗakko yarinyar da muka je gidansu jiya" haɗe fuska sosai Mai dawa ya yi idanunsa ya shige ciki haka kawai ɓacin ransa ya sake ninkuwa ya yi shiru ya datse laɓɓansa kamar zai raba su gida biyu ya yunƙura zai tashi Goje ya ce "Wannan sauyin na yanzu na mene? Na fara jin daɗi a raina kwana biyu baka sha ƙwaya ba, lafiya dai?"

"Mutallab" still ya yi shiru Goje ya sake kiran sunansa yana leƙa fuskarsa ganin babu alamar zai kula shi kawai ya miƙe ya fice ya bar wajan.

***Gabaɗaya suna zaune a cikin parlon banda shi dake tsaye, zuwan nasan ake jira amma tunda ya shigo bai kalli kowa ba balle ya yi magana, fuskar nan a murtuke kamar kodayaushe. Yaya J, Awais Dr Hash, Anty Turai Waheeda sai Ummi dake zan gefe bata cewa komai sai goge hawayen da yaƙi tsaya mata take yi. Daddy baya uhm baya uhm'uhm kansa a ƙasa zuciyarsa ta bugawa da ƙarfi yama kasa yarda da abin da ake faɗa har lokacin gani yake wasa ake yi masa da hankali da kuma wahalar da zuciyarsa da ake saboda anga yana ƙaunar Safiyyerh ƙauna mai tarin yawa an fahimci ita ce rauninsa.

"Captain Aliyu Abdu Marafa shiru ba naka bane, ba muzo nan da a shiru ba a matsalar kidnapping ba a yi mana wasa" cewar Sp Ghali daya ƙara amsar case ɗin Safiyyerh a karo na biyu ya ɗaga kai ya kalli masu gadin asalin gidan da kuma na part ɗin su Captain sai kuma ya ce "Heyy you man, mene sunanka da aikin da kake yi?" Cikin rawar murya ya ce "Sunana Isma'il ni mai gadi ne Yallaɓai"

"Isma'il sanda abin ya faru ƙarfe nawa ne? A daidai lokacin kana ina kuma?" "Ban san ƙarfe nawa bane a lokacin don ban duba a gogo ba, sanda abin ya faru kuma ina bakin gate ne amma kafin nan na miƙe na shiga banɗaki kama ruwa wallahi gaskiya nake faɗa maka Yallaɓai"

"To na ƙaryata ka ne? Kenan Isma'il bashi da sani akan waɗanda suka shigo gidan ko? Da ɗauke Safiyyerh?". "Duk abin da na ce maka na yi ƙarya abu ɗaya na sani fitowar su ɗauke da ita, hannunsu riƙe da makamai ɗaya ya ce na buɗe ko ya ɓola

mini ciki na ji tsoro haƙiƙa sai na buɗe ashe sun yi parking mota wata ɓaka mai kyau daga can gefe"

Murmushi kawai Sp Ghali ya yi yana duban ɗaya ma'aikacin ya ce "Kai kuma fa? Mene information?" Shi wannan jikinsa har ɓari yake don tsoro ya ce "Yadda na gansu Allah Ya sa naga Annabin Rahama, misalin biyu da arba'in ne ina zaune na ji ana dirowa ta katanga kafin na yi magana ɗaya ya make ni yana nuna yatsarsa a baki alamun na yi shiru, ni kuwa na yi shirun don wallahi a lokacin na ɗauka mai gida shi sojan kenan daman shi ke kai wa dare a waje saboda yanayin aikin nasa, suka ɗaure ni ina hango sanda suka nufi part ɗin tunda can babu masu gadi daga nan ban san mene ya faru ciki ba sai gani mukai sun fito da ita a kafaɗa kamar ma a sume take yadda ta langwaɓar da kai"

Daddy da Captain suka runtse idanunsu lokaci ɗaya, kowanne tunanin da yake daban a ransa, is he a loser? Captain ke tambayar kansa or he is falled as a husband maybe da yana kwana ɗaki ɗaya da Safii da hakan bai faru ba, idanunsa ya ƙara sauya kala. Daddy ma nasa tunanin dabanne, ko dai ya yi gaggawa ne ba yanzu ya dace ba? Ko mistake ya yi daya aurawa Aliyu Safiyyernsa ne? Is he a loser? Daya kasa tsare rayuwar yarinyarsa mace ɗaya tilo a duniya ko dai da gaske he is falled as a father?

Kafin kowa ya yi magana ta shigo cikin gidan a gigice duk da nutsuwar da take da ita, da sauri kuma Daddy ya miƙe tsaye cike da tsoro da mamaki hatta Captain sai da ya ji wani abu mai kama da faɗuwar gaba, who told her? Tun kafin ta yi magana daddy ya yi saurin matsawa kusa da ita ganin yadda take ta zare idanu fararen idanunta fuskar nan nata ya ɗakko rana kamar ta yage don fari "Zahiyerh"

Girgizawa daddy kai ta yi a daburce ta ce "Ina Maama?" Ya yi shiru yana ƙoƙarin riƙe hannunta ta ƙwace ta yi baya da ƙarfi kuma ta ce

"Ina Maama? Ka bani ita na tafi da ita where is Safiyyerh"

"Safiyyerh has been kidnapped"

"Kidnapped?" Ta maimaita tana juyawa ta kalli Sp Ghali anya ya san wacece ita da yake furta mata maganar anyi garkuwa da Safiyyerh kai tsaye bai tauna harshe ko ya lissafa maganar ba, Safiyyerh fa? Sp Ghali zai yi magana daddy ya girgiza masa kai yana sake kallon Zahiyerh wacce zuciyarsa ke buɗewa a duk sanda ya kalle ta. "Ummimi please ki kwantar da hankali ki samu nutsuwa tafiyar nesa kikai jirgi kika hau"

"To na ji, ka faɗa mini meke faruwa da Safiyyerh?" Daddy ya sauke numfashi a hankali kuma ya nuna Sp Ghali ya ce "As he said, he told you already Safiyyerh has been kidnapped"

"Uhm"

"Komai zai daidaita Ummimi" ita dai bata sake magana ba can ta ɗaga kai ta kalli Aliyu da sauri ya zame idanunsa ƙasa ta harɗe hannayenta a ƙirji ta tsaya jikin hawa steps ɗin bene. "Afuwa Sp muje ko?"

"Next question ɗin mu akan Captain ne"

"Ok ka yi mana" in ji Anty Turai.

"Aliyu kafa yi haƙuri kalar aikin ku na sojoji daban, namu daban kowa da nasa iyawa da ƙwarewar a nasa ɓangaren ok. Aliyu kai ne zaka faɗa mana abin da ya faru a cikin gidan su waye suka sace maka mata har cikin gidanka a matsayinka na soja wanda kodayaushe zaka iya samun ƙarin matsayi na aiki, ya akai haka ta faru? Su waye?"

"Ban sani ba"

Kai tsaye Captain ya bada amsa "Baka sani ba? Har kuma suka ji maka ciwo kada ka saka na fara zarginka na yi tunanin sace Safiyyerh set up ne kuma ne ka yi plans ɗin hakan, ka sace matarka?"

Aliyu ya dinga kallon Sp Ghali a hankali kuma ya ce "E". "kana nufin ka sace matarka Safiyyerh?"

"E" ya sake cewa

"Aliyu!!" Daddy ya kira Aliyu da ƙarfi ya miƙe ya ce "Da gaske ka sace Safiyyerh?" Kamar idanun Captain za su faɗo ƙasa saboda yadda suka fito waje sai kawai ya lumshe ido ya buɗe ya ce "E, na sace ta daddy" yana cewa ya fita daga parlon yana banko ƙofar da ƙarfi kamar ya cire ta. "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un!" Muryar Ummi ta karaɗe parlon ɣan mazan dai sukai shiru.

"Karya yake yi" Ummimi ta ce har yanzu taƙi zama lokaci zuwa lokaci kuma tana duba wayarta kawai sai tabi bayan Aliyu. Daddy har jiri yake gani baya so a fitar da maganar ya fiso a yi komai secretly har Safiyyerh ta dawo gare su amma sai yaushe ne?. Only God knows.

****Ammo na zaune ta yi shiru a ɗakinta kamar kodayaushe ta yi nisa a tunaninta bata ma san Malam ya shigo ba sai muryar Inna Binta da ta ji a sama wajan ƙofar ɗakin tana faɗin "Yanzu don Allah Ammo da rana ma ba za ki daina kwantar miji kina satar kwana ba, wacce irin jaraba da masifa ce haka ni Bintalo jaraba kala-kala Malam ɗin duk da basir ya cinye shi da rana ma ba za a bar mana miji mu dinga ganinsa duk da ba wata tsiyar yake yi mana ba" Ammo ta cira kai ta kalli Inna Binta ta juya ta kalli gefe har yanzu ba taga Malam ba cikin rashin fahimta ta ce

"Kamarya?"

"Ohho shafa ki ji mace an girma amma sai shegen munafurci da kissa wato kafin ki gama sallama ɗan naki wa duniya kafin ya gama zama ɗan ta'adda ya miki aikin mallake malam ko? Shi ya sa kaf gidan nan kin fi kowa yawan yara" Ammo ta kasa cewa komai da ƙyar ta buɗe baki ta ce

"To ina Malam ɗin yake yaushe ya shigo mini?" Ta banka mata harara ta nuna mata malam dake zaune ya yi shiru a hankali ta furta "Ikon Allah ki yi haƙuri ban san ya shigo ba" Malam ya yi gyaran murya ko kallon Inna Binta bai yi ba cikin damuwa ya

ce "Ammo ki nutsu ki ji me zan ce miki babu tabbacin abin dai har yanzu, ki yi haƙuri idan har hakan ya kasance gaskiya"

Jin haka ya saka Inna Binta neman waje ta zauna a bakin dakalin ɗakin Ammo ita dai wacce ake maganar domin ta shiru ta yi tana bin Malam da kallo gabanta na faɗuwa ba wai yanzu ta saba da faɗuwar gaba ba, ta ji wannan ta musamman ce. "Gawa aka tsinta....," "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un! Na Ammo?" Malam ya ƙura mata idanu bai taɓa zaton tunanin wancan gantalallan yaron mara amfani a duniya zai zo ranta bq, ya girgiza kai kana ya yi shiru caraf Inna Binta ta ce "Idan shine ai gwara ka faɗa ko kuwa? Kai aka cire masa ko wuƙa ce harsashi ne ko rayata ko babbake shi aka yi kasan haka ake yi wa ɣan daba, wallahi wani da aka rutsa shi ɣan unguwar jahilin duka sukai masa, ashe shima dai irin tsinannen yaron naka ne wuƙa bata huda shi, suka dinga rutsa masa dutse aka ina sai da kan ya ya yi dugu-dugu a nan cikin gari akai abin, da iyayen nasa suka je wajan ɣan sanda cewa sukai su yi haƙuri gawar ba zata ɗakko ba ta yi muni yaron nan dai da yake bashi da rabon rahama ko sallah ba a yi masa ba, yana can za a yi gwaje-gwaje da gawar ɣan makaranta daman ƙarshen duk wani ɗan daba kenan"

Malam ya yi shiru bai yi zaton haka Inna Binta take ba, Ammo rasa kalmar da za ta yi amfani da ita ta yi wajan yi wa Inna Binta, ta yi shiru tana sunkuyar da kai.

"Malam ka faɗa mata kawai sai ta ɗauki don gana"

"Wallahi tallahi ko"

Mama ta yi caraf ta faɗa ashe itama tana laɓe a jikin taga daga waje. Ya girgiza kai kawai cike da takaici kana ya ce "Gawa aka tsinta ta mace an cire mata idanu biyu kuma an cillar da ita bakin hanya, aka kira ana tunanin kamar gawar" haka kawai ya ji yana jin tsoron kalmar da abin da zai biyo baya Ammo ta ƙura masa idanu a sanyaye ta ce "Sa'adah ce ko Bafullatana ko Hameeda?"

"Hameeda"

"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un! Astagafirulla Allah mun tuba jama'a an cire idanun Hameeda gatan na ammo ta shige jama'ar gida Hameeda ta mutu a kawo mana ɗauki" a gigice Inna Binta ta zari mayafi tana ficewa zuwa maƙota. Mama kuma ta

yi shiru idan haka ne ba ƙaramin gigita mutuwar Hameeda ya saka ta ba. Ammo bata ce komai ba a ranta tana nanata kalmar Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un! Ita kawai ta yi mata saura a cikin baki "Ba a tabbatar bata, saboda haka ki taso muje a gani ƙila ki fini ganewa sosai" kafin Ammo ta yi magana Baba uwar mijin Anty Hameeda ta shigo tare da mijin idanunta ya yi ja cikin sauri Mama ta ce

"Yaya lafiya dai Baba?"

"Ina lafiya, Hameeda ce daga fita siyo magani da daddare mun neme ta mun rasa kwana biyu kenan wallahi". "Shikenan ta tabbata an kashe Hameeda" kafin ka ce me cikin gidan ya cika Inna Binta sai rusa ihu take yi tana sun shiga uku an kashe musu yarinya. Koda aka kawo gawar Hameeda ba kowa ya iya gani ba kamar dodo har ta fara wari an cire kyakkyawan idanun nan nata. Ammo ta dinga tuna nasihar Hameeda ta ƙarshe da ta yi musu,daga nan bata sake dawowa gidan ba wani abu ya tokare wuyan Ammo ta kasa magana balle kuka sai kallon gawar take cike da sarewa.

****Kamar kullum yau na Goje ya buɗe ƙofar tana durƙushe duk ta fita daga cikin hayyacinta idanunta ya faɗa ba zaka taɓa cewa Safiyyerh bace. Ya dire mata abincin yau dai pure water ɗin hadda sanyin shi "Kar ki sake buga mana ƙofa domin ba wanda zai buɗe miki"

"Ka ɗauke bana ci"

"Dar kin yi kyan kai yar kurciya" ya juya baya ta faki idanunsa ta zare ƙaramar wayar data gani a jikin aljihunsa ta yi saurin ɓoyewa. Goje kuma ya dawo cikin harabar gidan Moh ya gani zaune yana sake karanta takardar sai ya yi murmushi yana dafa kafaɗar Moh ya ce

"Ni dai na fara gajiya da siyo abinci gaskiya" banza Moh ya yi yana ninke takardar tun daren da aka kawo Safiyyerh bai sake ganin kamarta ba sai sautin kukanta da yake ji kullum yanzu ma kukan take tana buga musu ƙofa da ƙarfi a fusace ya miƙe tsaye ya nufi ƙofar ɗakin Goje ya bisa da kallo can ya miƙe ya bi bayansa. Da ƙafa ya daki ƙofar ta buɗe da sauri Safiyyerh ta miƙe cak kukan nata ya tsaya a maƙoshi ta tattare ta haɗiye ta mayar zuwa cikinta, fitsarin dake mintsinin mararta ya saki kansa ya fara zuba a gefen ƙafarta, dukkan wata gaɓa ta jikinta ɓari take yi. Ashe

da bata san waye ba, bata san waye ya yi kidnapping nata ba sai yanzu cikakkiyar siffarsa ta bayyana zubi da tsarin da halittar da Ubangiji ya yi masa mai firgitarwa bata san waye mafi muni a cikin yan daba amma ta san wannan tantirin ne ko daga tsaiwar da ya yi, cikakken namiji a tsaye majiyin ƙarfi matashi kuma mai jini a jika da cikakkiyar lafiya shine matsayin ɗan daba tsaye a gabanta gefen fuskarsa wani zabcecen yanka wanda akai masa ɗinki har ya zama tabo. Salati take ƙoƙarin yi ta kasa ta gama jiƙa wajan da fitsari ƙiris ne babu numfashinta ya yi ƙaura daga ƙirjinta ta yi saurin ƙasa da idanunta.

"Ka yi haƙuri kar ka mini komai, don Allah ko nan waje ne ku bar ni na fito kalli skin ɗina zai lalace akwai ants a nan waje" ta tattare hannun rigarta tana nuna masa farar fatarta da ta yi wani irin tabo ritsi-ritsi kamar kwanciyar ji fuskarsa ta kumbura ta yi jaa sai susa take yi saboda ƙaiƙayi. Ta langwaɓar da kai ta ce "Ka gani ko na sake nuna maka har bayana" ta juya bayan tana ƙoƙarin ɗaga rigar ta ji ya daki ƙofar da mahaukacin ƙarfi kafin ta juyo ya bar wajan. Ta sauke ajjiyar zuciya feeling reliver ganin ƙofar a buɗe.

Tana fitowa suka haɗa idanu da shi da sauri ta juya kanta na bugewa da jikin bango, anya tana da hankali da lissafi kuwa? Fitsari fa a wando sai ya tsuke fuska. Suna zaune Mangal ya shigo yana hakki da sauri Goje ya zare wuƙa sama tiger ya yi zumbur ya miƙe tsaye yana gurnani Moh kuma kallon Mangal yake yana jiran ya ji suwaye suka biyo shi don yana da yaƙinin ba wanda ya san gidan da suke.

"Kai ɗan wahala mene su waye suka biyo ka?"

"Daga layin su Mai jeji naje an yi rasuwa kuma a gidansu Moh aka anyata lahira wallahi" duk suka juya suka kalli Moh shima ɗin kallon nasu yake fuskarsa ba wani sauyi kawai ƙarashen maganar yake jiran ji. "Sai aka ce waye ya baza? Iyayen Moh dai akwai sauran rai wannan dar in sha Allah"

"Wai ko Hamida ko Hamda, idanu aka ƙwaƙule mata ashe tana cikin mutanen da aka sace ta" Moh tunani yake yi ina ma ya san mai sunan Hameeda tasa Hameedan ba zata taɓa mutuwa a irin wannan halin ba, sam ba zata mutu ba duk da yanzu ba ruwansa da ita. Bayan wasu shuɗewar daƙiƙo zumbur ya miƙe tsaye kansa na sarawa a dagule ya furta "Amini?"

Da sauri kuma ya yi wani ɗaki suna shiga suka same shi yana cakawa kasan wata sabuwar allura da Ali wali ya basu da maye, bayan ya zuƙe ruwan a jikinsa ya ƙara ɗakko wata ya sake cakawa kansa sirinjin ana ukun Goje ya yi saurin matsawa ya ce "Easy Mutallab,zaka haukata kanka a banza kasan wacce irin allura ce ko dan baka jin turanci muma bama ji, haukatar da mutane take yi fa?"

Sakar masa allurar ya yi ya sake ɗakko wata Goje ya sake riƙe wa ya ce "Wallahi in dai ina nan ba zaka sake yi ba" ya ƙara sakar masa ya ɗakko fenta zai yi Goje ya ƙara riƙe, Moh ya shammaci Goje ya ɗauke shi ya damfara shi da ƙasa ya saka ƙafa ya take hannunsa hannun ya yi ƙara, ganin yana shirin kashe shi ya sa Mangal ya ɗakko abu ya makawa Moh aka, ya ɗauke ƙafarsa ya juya yana kallon Mangal da sauri Mangal ya zare Goje ya fito da shi daga ɗakin da gudu suka fice daga cikin gidan.

**The following days.

Buɗe ƙofa Captain ya yi ya shiga ɗakin a hankali wanda ya yi wa Aliyu mugun sani shi zai lura da ramewar da ya yi. Idanunsa akan Ummimi dake zaune gefen gado hannunta tsakanin cinyoyinta ta sunkuyar da kanta ƙasa ya ƙarasa ya duƙa gabanta ya ɗora hannunsa a cinyarta a hankali kuma ya leƙa kansa ta ƙasa ya kalli fuskarta suka haɗa idanu ta zabga masa harara lallausan murmushi ya yi mata a hankali ya ce "Love"

"Aliyu fita"

Ya girgiza mata kai ya yi shiru sai lokacin ta yi shiru tana ƙare masa kallo "Ciwo ka yi ne Gadanga?"

"A'a love"

"Kuma yaushe ka damu da Maama har haka ka dame?"

"Love, Safii is my wife" ta wani buɗe idanunta na rashin fahimta "Waye Safii?"

"Safiyyerh, your Maama" da sauri ta miƙe tsaye tana girgiza kai "Yaushe aka yi haka? Tunanin waye hakan decision ɗin waye wannan professor ko?" Gani take sauri take yi amma sai ta cire ƙafa ɗaya take mayar da ɗaya ta fice daga ɗakin a parlo taga duka mutanen gidan hadda police da team na musamman da suka fara bincike akan sace Safiyyerh Abdu Marafa. "Ashe daman baka yarda ba professor za ka iya mini haka? Bana baƙin ciki da auren da ka yi musu amma ina da hakƙi na sanin ka haɗa Safiyyerh da Aliyu aure, Professor burinka ya cika ƙudirinka ya tabbata ka aurawa Safiyyerh Aliyu" masifa Zahiyerh take yi tai Hausa tai turanci ta koma larabci ba wanda ya tanka ta, kan Abba a ƙasa. Da ƙyar Aliyu ya janye ta a ransa ya gode Allah da bata ce a raba auren ba tsaf zata iya. Ta nemi kujira ta zauna sai nishi take yi na rashin lafiya.

"Zo Aliyu" ya ƙarasa wajanta ta nuna masa kusa da ita ya zauna, sai kawai ta rufe idanu ta kwanta ta yi shiru a hankali ya fara danna mata kanta Dr Hash shima ya ɗauki ƙafarta data kumbura ya fara danna mata sai a lokacin Daddy ya buɗe idanu ya kalleta ya girgiza kai fatansa kafin ta farka Safiyyerh ta dawo gida.

"Sp har yanzu ba wani kira da muka samu akan batun sace Safiyyerh, ina zargin anya issues na kidnapping ne?". "Za su kira ai sun sauya salo ina mai tabbatar maka cewa za a kira Safiyyerh zata dawo gida" daddy ya jinjina kai ya yi shiru.

Wayar Aliyu ce ta fara ƙara yana dubawa yaga kamar private number har sai share sai ya yi tunanin ko masu sace Safiyyerh ne? Da sauri ya amsa kiran was the first abin da ya ji daya nemi buɗe masa zuciya sautin kukan Safiyyerh ƙasa ƙasa ya runtse idanu can ya ji ya ce "Yaya Please help ants za su cinye mini fata Yaya za su kashe ni"

"Safiyyerh listen"

Karo na farko daya kira sunanta "Take a heart peanut, ke matar soja zama jaruma". "Yaya am scared wuƙaƙe" ya buɗe idanu ya ga duk kallonsa suke yi hadda daddy Sp Ghali ya yi masa alama ya saka speaker. "Kina ji na?" Kamar tana gabansa ta ɗaga kai "Be strong Maama, daddy is here for you, Ummi kowa ma hadda ni am here for you yʻan mata, hadda Ummimi" da wani irin sauri ta ce "Ummimi? Ummimita Yaya?"

"Sure, ki nutsu wanne waje suka kai ki, za ki iya tuna suna ko wanne abu da zai bamu haske?"

"Yaya sun rufe mini idanu ban san komai ba, don Allah ka taimaka mini daddy help me please" idanun daddy ya yi jajur already anyi connecting na wayar an fara bincke da ƙoƙarin tracking daga ina wayar ke zuwa. Shima kuma daga can haɗaɗɗan ɗakinsa da suke zube da kayan na'ura kamar hauka ya saka abu a kunne ya ɗora ƙafa yana girgiza kai a hankali yana jin conversation ɗin Safiyyerh da Aliyu yana yi yana duba time da cije leɓe.

Abin da Aliyu bai taɓa yi ba kenan ƙoƙarin jan Safiyyerh da hira da ya ji Ummimi zata motsa zai yi saurin girgiza ƙafarsa "In sha Allah i will save you Safii, ki yi ƙoƙarin gane wani abu ki yi addu'a" tana ƙoƙarin sake magana suka ji ihunta da ƙarar buga wayar da ƙasa "Safiyyerh kina nan kina kan kayi baby?" Aliyu ya jere tambayar. Kafin sun an kare daddy ya sulale a wajan babu numfashi.

****Tunda su Goje suka fita yake abu ɗaya kamar wanda za'a zarewa rai, sai buge buge yake yana fasa komai na gidan kumfa na fita a bakinsa ihun da ya yi da gurnani shi ya saka Safiyyerh sakin ihu tana yin cilli da wayar a gigice ta miƙe har lokacin kayan bacci ne a jikinta, tana fita ta ganshi a tsakar gidan ya yi tumu-tumu wani irin mahaukacin tausayinsa ya ratsa zuciyarta ta duba babu kowa a gidan sai ta yi tunanin wannan opportunity ne da zata bar gidan hankali kwance, bata damu da kayan jikinta ba sai kawai ta nufi ƙofa da gudu tana ƙoƙarin fita ta ji muryarsa cikin mawuyacin hali kamar ana fisgar ransa abin da ta ji ya saka ta tsaya ta yi jim itama kanta na sarawa tana gani bibbiyu ta sake yunƙurin buɗe ƙofar ta ji ya ce "Safiyyerh....!" Ya faɗa da ƙarfi a gigice ta juya taga ita yake kallo yana ƙoƙarin tashi ya kasa yana miƙo mata hannu...

MUTALLAB IS NOT FREE

We'll soon end the free pages. ka yi payment a yi naka a paid group.

MUTALLAB.

Book 1, 2 &3

500 Naira

0116886423 Union Bank Na'ima Sulaiman S a tura shaidar biya ta nan 08164069385

Yʻan Niger kuma ya gadda tsarin yake.

'Yan Nijar ku turo carte airtel ta 300fcfa saman wannan layin 84506476

[1/7, 9:33 PM] Sis Fauzy: *This is not a love story,but a love that builds a story, and a love that destroys the story.*

❤ MUTALLAB ❤

Page 14

Bright pens...2nd batch

Author's books

Munafukin miji

Moon

Mijin malama

Tsintacciya

Idan ba ke

Sirrinmu

E.t.c

Follow on Arewabooks

Follow on telegram

Remain 1 free page

Jikinta rawa yake ganin ya kafe ta da idanunsa har lokacin kuma kakkarwa nasa jikin yake yana fesar da numfashi. Ina ya san sunanta? Take tambayar kanta. A hankali Moh ya lumshe idanunsa bayan ya janye su daga gare ta yana ɗan ciccije bakinsa.

Safiyyerh ta kasa fita, idan ta bar shi ya mutu alhalin zata iya taimaka masa Ubangiji zai kamata da laifin rashin tausayi da imani, ta salwantar da rai ta hanyar ganganci da son zuciyarta.

"Safiyyerh taki rayuwar fa? Kashe ki za su suma fa, ya kamata ki bar wajan nan tunda kin samu dama, shi kinga kamar mahaukaci ne maybe" zuciyarta ta bata shawara cike da gamsuwa ta jinjina kai tare da kama handle ɗin zata fice.

Haɗa idanu suka sake sanda ta juyo ya dinga kallon ta rinannun idanunsa sai ta saki hannun ƙofar tana ɗaga ƙafa zata nufe shi.

"Run Safiyyerh, run away run Safiyyerh"

Ta sautin muryar zuciyarta a cikin kunnenta ta sauka har tsakiyar kanta ƙirjinta ya dinga ɗagawa tana son tafiya bata kuma san meke janta zuwa gare shi ba. Ta girgiza kai

"Save him frist" ta furta a iya harshenta. Yana ganin ta nufo inda yake ya rufe idanu kafin ta ƙaraso ya juya baya yadda ba zata ga fuskarsa ba. Jikinta a sanyaye ta durƙusa cike da tsoro ta kasa magana can ta yi ƙarfin halin furta

"Ina ke maka ciwo?"

Ya mata shiru ba bacci yake ba, domin tana hango yadda ƙirjinsa ke ɗagawa sosai yana ƙoƙarin ganin ya hana kansa yin abin da ƙwaƙwalwarsa ke umarta shi. "To faɗa mini inda maganin yake na ɗakko maka"

Jin shirun ya yi yawa ta matsa tana leƙa fuskarsa suka haɗa ido ya zaro mata manyan jajeyen ƙwayar idanun ta yi saurin ɗauke nata idon "Tab kalli idanunka fa, ko asibiti zaka je?" Ta yi maganar tana ƙoƙarin kai hannu zata taɓa shi ya mirgina gefe yana haɗe fuska kamar ya ce ya shiga uku, da zata gane to tabbas ita ɗin ce baya son gani ko jin muryarta ta kura masa hakan

yake yi sosai ya tsuke fuska yana rufe idanu Safiyyerh ta miƙe gabaɗaya hopefully ya buɗe ido ko ya bata amsa ba sarewa ta sake miƙa hannu dukan da ta ji ya kaiwa jikin bango ne ya saka ta yi baya tana zaman yʻan bori,shima ya tashi zaune yana zazzaro idanu daidai lokacin su Goje suka shigo ya kalli Safiyyerh da take yarfe hannu saboda bugewar da ta yi ya dubi Moh daya miƙe tsaye yana tangaɗi ya shige ɗaki yana rufo kansa a ciki. "Ke me kikai masa?"

"Kʻato da shi me zan masa?"

"Abu a duhu na san matan yanzu ba kunya ce da su ba, idanu rufe suke afkawa maza" da mamaki Safiyyerh take kallon Goje zuciyarta babu daɗi ga takaicin rashin guduwa gana wancan da ko inda take bai kalla ba duk maganar da ta yi masa, ta matsa tana takure jikinta waje guda sai yanzu ma take jin kunyar shigar jikinta sosai, ita Safiyyerh yau ita ce take rayuwa a wajan yʻan daba mashaya kuma yʻan ta'adda hawaye ya cika idanunta sosai mutanen da sam basu suwaye su ba, basu san kansu ba basu da wani amfani a wajan al'umma.

"Ke kina ji ko?"

"Safiyyerh sunana"

"Mene ya daman kuma warning zan miki kar ki kuskure ki sake zuwa wajan shi idan kina son tsira da ranki ba, ba kema ko Abdu Marafa bane a nan wallahi zai iya ganin bayansa, ki yi abin da ya shafe ki kawai ki tsaya iya matsayin ki na wacce akai garkuwa da ita kuma ɓarayin gwamnati". "Shi wa?"

Ya nuna mata ƙofa "kin gane ai"

"A'a" wuƙa ya zaro yana gwalo idanu waje ya ce "Idan na cire miki yatsa ɗaya za ki gane ai"

"Ni mu yi magana ta fahimta daku, me kuke buƙata zan baku koma mene amma ku rabu dani don Allah ina kyakkyawan fata da muradan da nake son cimma a rayuwa

naga ku babu inda kuka saka gaba rayukan ku ma sam baku damu dasu, wallahi ina buƙatar rayuwa mai tsayi da zan bar baya mai kyau ba zaku ɓata mini rayuwata ba, kuma warin sigarin nan juya mini kai yake da ƙyar nake shaƙar numfashi, ni macace mai hankali da ilimi wacce iyayena suka bawa tarbiyya daidai gwargwado in da ilimin addini saɓanin ku da ba lallai ko ummul kitahhb kun iya ba, yʻan daba ne ko masu laifi rayuwarku a gurɓace take ba a yi muku tarbiyya ba" hatta Moh dake cikin ɗaki idanunsa a sama yana kallon rufin kwano sai da ya waro ido yana sauraren maganganun da take cewa, Mangal ya yi mata ƙuri da nasa idanun haka Goje

"Wuyanki ya isa yanka ba laifinki bane za mu yi maganinki"

"To me na ce na ba daidai ba, don Allah ku ba yʻan daba bane yʻan ta'adda kuma ga tantirin can shine shugaban naku da alama asalin daƙiƙi ne ajin ƙarshe sai wari dauɗa dana rana ga na shaye-shaye wallahi...," saurin haɗiye maganar ta yi ganin shi tsaye a kanta yana huci ta miƙe tsaye hannu ya ɗaga kamar zai kwaɗa mata mari ta kurma ihu tana ƙanƙame jikinta "Don Allah ka yi haƙuri ƙarya nake yi wayyo daddy wayyo captain" sai idanunsa suka sake jirkicewa ta buɗe idanu taga ya zuba mata nasa idanun fuskarsa dab da nata sai juya ƙwayar idonsa yake a saman fuskarta kamar mai son tantancewa wani abu.

Ta tura baki cike da tsiwa ta ce "Kana kwaɗa mini mari zan rama tunaninka rabuwa zan yi dakai ka ci bulus? Bayan an ce duk wani ɗan shaye-shaye bashi da wani ƙarfi hayaƙi ya cinye shi" Goje ya ce

"Wannan yarinyar yʻar wasa ce bayan kuɗi data iya sarrafawa har rashin kunya ta iya Allah kar ka rabu da ita" Shi dai Moh na tsaye yana kallon ta ita kuma ta kasa jure ganin ƙwayar idanunsa ta yi ƙasa da kanta tana murguɗa masa baki, bata ankara ba ta ji ya cilla mata baƙar kunawa cikin riga ta zumduma ihu a gigice ta yi kansa zata riƙe shi ya yi saurin baya yana ficewa daga gidan Goje yana ta dariya da buga ƙafa

"Kinga aikin Mai jeji gana Scorpion nan"

****Eng Ali wali yana zaune a gidan wutawarsa yana zantawa da wasu manyan mutane masu taimaka masa a harkar kamfel ya dubi P.a ya ce "P.A ina tunanin iya

abin da ake buƙata kenan kuma na bada, ka sani ba kuɗi yanzu a ƙasa kamfen ya cinye komai, you can manage ko?"

"Ba damuwa amma muna da raguwar list na local government wajan biyar da bamu je ba yanzu haka, ga ɣan media sun matsa kasan mutane babu amana gwara a fara watsa musu hatsi tun yanzu fa a yi maganin yunwar data addaba musu" Ali wali ya yi murmushi yana juya kai kafin ya ce "Ku je za mu yi magana zuwa dare ina da hira da ɣan zuwa dare we'll talk" P.A ya kalli mutanen ya ce

"Don't make any mistakes idan kun shiga gidan rediyon ku tabbatar kun yi abin da ya dace, kar kuma ku nuna wata alaƙa tsakaninmu da ku yadda na faɗa muku haka zaku faɗa" "In sha Allah, ai harma da abin da baku buƙata ba mu indai za a biya mu ai buƙatar maje hajji sallah zamu farfaɗi ayyukan bogi da ya yi kuma ya yi mana"

"Nice to hear this, you can leave ku je"

Tafiya suka yi suna murnar ɣar dubu biyar biyar ɗin da za a basu akan faɗar abin da ba haka bane. Ali wali na shirin miƙewa ya ji numfashi a bayansa ya juya da sauri, tsaye ya ga Moh fuskarsa rufe sai ƙwayar idanunsa da take a fili ya cake yana muzurai. "ka bani tsoro amma"

"Mara gaskiya ko a ruwa zufa yake"

"Me na yi na rashin gaskiya?" Ya yi masa shiru yana wani irin fito ya ɗauki ƙafarsa ɗaya ya ɗora saman kujera yana zaro kunama ya ajjiye saman kujerar wajan ta fara yawo tana ɗaga ƙari sama ta kumbura sosai. "Yaushe ka shigo? Na ce ni zan dinga nemanka bawai ka dinga biyo ni duk inda nake ba, bana so a san ina mu'amala da kai"

"Saboda annoba ne ni? Tunda ka jawo ni haka zaka shanye duk abin da na dama, na kwalo yarinyar mene next?" Murmushi Ali wali ya yi ya ce "Ai na san kun ɗakko ta, tunda CSP ya yi mini magana akan case ɗin kidnaping sannu namijin duniya"

"Zan kawo ta nan"

"Ina? A'a ka bar ta nan wajanku zan baka key ɗin wani gida sai ku tafi can kwafi sararawa ni bani da gaske koda zaka dinga huta gajiyarka a wajanta kana rage zafi" Moh ya ɗaga kai ya kalli Ali wali da kyau.

"Wacce gajiyar, sanyi ne a jikinta?"

"Kana abu kamar ba wayayye ba, mu bar maganar ka yi mini aiki na farko and i appreciate it. Sai batun Scorpion" daidai nan kunamar dake yawo a wajan ta shige hannun Moh ya matse ta ya yar waje guda Ali wali ya cigaba da cewa "Scorpion ba zai bar mu ba, Hon Maɗatai yake hari a yanzu nasan kuma bayan nan ni ne a list, yana neman zame mana masifa yana kawo mana barazana a akan siyasarmu gwara Hon Maɗatai ya samu dukkan abin da yake nema a mulki ya samu nasa rabon ni yaushe na fara? I will never let that happen ba zan bari ya yi galaba akai na ba"

"Me za ka yi?"

"Zan tabbatar an nemo shi an ɓatar da shi, don ba haka kawai yake yin abin da yake ba akwai abin da ya taka yake taƙama da gadara dashi, ka yi ƙoƙarin nemo mini shi kafin hukumar FID su kama shi zan ruɓanya maka abin da duk na yi niyya"

"To kuna da case da shi?" Ali wali yace "Pardon? Kamarya kenan"

"Basar"

Key ɗin gidan ya basa, hadda na mota Moh yaƙi amsa wai he don't know how to drive ya basa kuɗin abincin Fiyya mai kyau da duk abin da take so.

"Kaƙi faɗa mini waye kai dai ban san komai dangane da kai ba Moh, sunanka kawai na sani Mutallab without surname and middle name, whatever shikenan dai" Moh ya ƙara ɗaga ƙafa zai fita Eng Ali wali yace

"One more think Mutallab"

"Ali wali ka kira ni da ɗan daba ko ɗan ta'adda sai mu yi magana" Ali wali ya yi murmushi ya ce "Sai godiya" ya tsuke fuska Moh.

"Professor Abdu Marafa ya mini mummunan tabo a zuciyar matasan jihar nan,ya ɓata mini suna na ji ina son ɗanɗana masa kwatankwacin abin da ya yi mini ta hanyar ramuwar gayya wacce ake cewa tafi ta gayya daɗi, kamar yadda ya ɓata ni shima haka nake so a ɓata tarihin tarbiyyar gidansa da sunan da yake taƙama da shi, a dinga masa kallo a matsayin wanda ya gaza" Ya yi shiru yana sauke numfashi yana duba wayarsa ganin shugaban jam'iyya na kiran shi ya miƙe tsaye.

"Bayan sato budurwar yarsa da kuka yi har gida, ina son ka yi Safiyyerh Abdu Marafa fyaɗe, ina son ka yi wa Safiyyerh Abdu Marafa ciki kaga tana da auren wani, wani kuma daban ya yi mata ciki wanin ma ɗan daba, ɗan daban da basu san waye shi ba, kaga Safiyyerh zata haifi ɗan zina ko"

"Ɗan zina?"

Moh ya maimaita a fili Ali wali ya ce "To ɗan mene? Yayinda da wani wanda ba mijin yarinyar ba ya keɓe da yarinya har ta samu ciki wannan cikin ya sunan shi? Cikin shege ba haka lissafin yake, idan na ce wani zan bawa wani aikin lissafin Eng Ali wali bai gama cika ɗari over ɗari ba, dole kai zaka aikata haka Mutallab dole kai zaka yi wa Safiyyerh ciki domin dauɗar gora ciki kan shata"

"Wanne zunubi ita yarinyar ta aikata, gyatuminta ne kamar batun nan ba zan ba, shi kuma daman cikin yinsa ake yi? Ba kawai girma yake ba?" "Au baka san yin ciki ake ba? Shekarar nawa?"

"Koma mene ba za a yi ba" Ali wali ya yi murmushi ya ce "Dole zaka yi, ka rubuta kuma ka ajjiye sanda za ka yi baka sani ba jeka" bai wani ɗauki maganar Eng Ali wali da muhimmanci ba ya fice daga gidan.

***Safiyyerh ta rufo ƙofar bayan ta gama dubawa ta kalli Goje ta ce "Kawai ku siyo mini kayan abincin na dinga dafawa sai ina san muku?"

"Kin iya wato ne?"

"Mene wato?" Ya ce "Shi girkin nake batu" ta jinjina masa kai ya miƙe tsaye ya ce "Da kin yi dabara daman ba ki da wani amfani. Ita mamaki ta yi ganin kitchen hadda tukunya plates da spoons ga risho da sauran tarkace. Babu jimawa Goje ya dawo hannunsa riƙe da Indomie guda biyar da ƙwai guda goma hadda kayan miya da magi ya bata ya ce

"Ta yi musulmin daɗi kin ji Manager"

Ta samu kanta da yin murmushi a ranta kuwa dabara take yi ta samu hanyar guduwa. Suna tsaye ya faɗo cikin gidan sai ya yi turus yana kallon Goje yaƙi yadda ya kalle ta, ta ƙasan idanu ita kuma take binsa da idanu mamakin yadda jikinsa yake a murɗe take har ƙasan zuciyarta ta ji tana shakkarsa. "Barka da antayowa mai jeji ya ƙarin haƙuri" banza ya yi masa ya shige ciki Safiyyerh ta ce

"Au rashi ma aka yi masa?"

"Yayarsa aka sace sai jiya aka kanta an ƙwaƙwale mata idanu" Safiyyerh ta zare idanu tana dafe ƙirji sai tausayinsa ya kamata a raunace ta ce "Kuma bai je gida ba? Anya yana son yayar tasa kuma kun tabbatar wannan ba mahaukaci bane?" Shi dai tuni Goje ya bar wajan. Ta gama dafa Indomie wacce ta ji azabar Attahiru rabon da ta shiga kitchen a rayuwa ta manta fuskarta ta yi jajir da wani irin roɗi-roɗi idanun sukai micin-micin ta dinga mata ƙaiƙayi fuskar saboda zafin wuta ta nemi kaɗan ta juye musu a faranti.

Moh yana kallon yadda ruga lauma kamar mayunwata sai jan yaji suke yi ya kalli Indomien ya kalle su can ya miƙe ta ce "Kai baza ka ci ba? Ni ina son yin sallah fa" duk suka share ta, suna gama ci suka fice tare da rufo ƙofar ya rage sai ita kaɗai ta haɗe kai da qwwia ta dinga kuka kamar ranta zai fita har bacci ya ɗauke ta a wajan.

Cikin bacci ta ji an cillo mata abu ta miƙe da buɗe idanu tsaye ta ganshi ya juya baya leda ce ya cillo ta buɗe taga duguwar riga guda biyu da hijabi da takalmi ta yi ta mamakin yadda ya san size ɗinta ta miƙe tsaye yana jin zata zo wajansa ya nufi hanyar fita ta sha gabansa ya yi turus ta dinga kallonsa shima yana kallonta

"Wai kai baka yin magana ne, ko yar dariya babu kafin na tafi mu ƙulla mu zama abokai" ta miƙo masa hannu ya kalli hannunta mai ɗauke da siririn zobe sai yatsunta zara zara da su "Am Safiyyerh Abdu Marafa You?" Ya sake yin shiru ta langwaɓar da kanta gefe guda ta ce "Ina son zama ƙawarka fa, zan maka labarin daddyna da yadda yake so na, da labarin kamfanin da nake aiki hadda labarin Ashraf wanda zan aura ya mutu aka aura mini captain labarin Ummimi da Kinal ƙawata i will tell you everything, abota Frist?" Ta sake miƙa masa hannun a karo na uku. Gefenta ya bi ya shige yana rufe ƙofar gidan ya bar ta tsaye da hannu a ƙaƙe takaici ya ishe ta shi wannan yana ɗan ta'adda yana jin kansa kamar ɗan gidan ƙaruna saboda faɗin rai ga miskilancin masifa the manager ita Safiyyerh take magana ake sharewa bai san cewa akan dole take yin maganar ba? Ta lumshe idanunta hawaye na cika cikinsu da ƙyar ta yi alwala ta fara jero salloli. Goje ne ya shigo da sauri ya ce

"Ke kina ina fito maza taso" ta miƙe za ta yi masa gaddama kawar Moh ya shigo ya damƙi hannunta ta kalli baƙin hannunsa da ɗan mitsitsin nata farin hannun ya jata sukai waje mota ta gani bai tsaya jiran komai ba ya dannata a gaba Goje ya shiga baya Mangal dake tsaye ya ce

"Waye zai ja motar yanzu? Ni ban iya ba kuma haka?"

Moh dake shirin shiga mazaunin driver ko me ya tuna ya kalli Safiyyerh a karo na farko ta ji muryarsa a sake ya ce "Dawo nan" tsoran shi take ji ta fito ta koma wajan driver ya dawo ita ta tashi, ya cilla mata key ɗin motar "Muje" bisimillah ta yi ta fara driving ta juya ta kalle shi ta ce "Ina?" Ya bata wayar hannunsa wacce yanzu ya shigo da ita ta duba location da ya fara driving cikin sauri har suka bar wajan.

Mintuna kaɗan da barin su motoci suka tsaya a ƙofar gidan Captain ya fito jikinsa danye da uniform na sojoji da suka amshe shi sosai ga ƙatuwar bindiga sauran yaransa suka fito a hankali ya dinga bin wajan da kallo har ya shiga cikin gidan abin da ya fara cin karo da shi ya sanya zuciyarsa bugawa ganin rigar baccin Fiyya yashe a ƙasa ya ɗuka ya ɗauki rigar idanunsa ya sauka akan wani busasshen jini ya dinga kallon gidan a nan ya kalli ƙwayoyi kala-kala da wuƙaƙe da gorori ya lumshe idanunsa "Where are you Wife? Ina suka kai mini mata?"

"Captain kuma ka tabbatar tracking ɗin nan ya nuna?" Ya jinjina kai don baya jin zai iya magana. "Sun gudu, amma ya akai sukai san an yi tracking location nasu har suka gudu da wuri haka?"

Captain ya girgiza kai irin bai sani ba "Ka kwantar da hankalinka matarka zata kuɓuta ko kana tunanin sun yi mata wani abu ne?" Captain ya nuna masa rigar baccin Safiyyerh da jinin dake wajan mutumin ya dafe kai ya ce

"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, in sha Allah ba abin da muke zato bane muje" fita sukai Captain ya ji a ransa ba zai bar abin haka nan ba.

Mutallab wani gida ya kai su madaidaici mai kyau da tsari da yake can bayan gari duk suna zaune Safiyyerh kanta na ƙasa tana mamakin yawan shiriun bawan Allan nan, idan ya yi shiru shi kaɗai sai ya saki ajjiyar zuciya ko ya ƙurawa waje guda ido.

***Wajan sati guda babu labari akan batun sace Safiyyerh ba kiran waya babu komai Daddy ya hana a faɗi maganar ko a social media ko a gidan rediyo ya ce a bar ta tsakaninsu. Yana ƙwace hannunsa maƙale da ruwa muryarsa a hankali ya ce "Aliyu waye ya saka?"

"She is my wife daddy"

"And? Ɗan sanda ne kai ko soja?"

"Zan iya amfani da uniform ɗina ko babu haka ai she is my responsibilities yanzu na kula da haƙƙina zan ji na zama lusari idan ban nemo Safii ba, kar ka dakatar dani daddy police su yi nasu aikin ni na yi nawa"

"Ka cire hannunka a ciki Aliyu"

"Ok zan jire akan wanne dalili?"

"Aliyu yanzu baka tunanin dalilin hakan su yi mata wani abu ne? Baka san su waye mutanen nan ba, duk abin da zaka ji a bayan nawa dana Zahiyerh yake kar ka yi kuskuren da za su salwantar da rayuwar Maama na roƙe ka, mutanen ba mutunci ne da su ba kamar komai hannun Sp Ghali" Aliyu ya miƙe ya nufi ƙofa "I am sorry daddy idan kaga na tsaya to na mutu ne, idan da numfashi a ƙirjina ba zan gusa ba sai na dawo da Safiyyerh cikin rayuwata i am sorry" yana cewa haka ya bar ɗakin.

Daddy ya rufe idanunsa daya cika da ƙwalla ya wani irin ramewa ko abinci baya ci Ummi ta ce "Ka san halin Aliyu da baka fito masa ta haka ba, gwara ka saka Ummimi yi masa magana" daddy yaƙi cewa komai. Wayarsa ta fara ƙara number ya gani sai ya yi sauri ya ɗaga yana kaiwa kunne aka ce.

"Barka, ina magana da Professor Abdu Marafa na sani ko baka amsa, zan fara da yi maka ya jiki don ina da yaƙinin kana nan zuciyarka na ciwo bari na ɗora maka da wata maganar ban sani ba ko zaka iya jure jin abin da zan faɗa. Yarinyar da kake ji da ita ni na saka a sato mini ita Safiyyerh kenan ina son ka lashe aman da ka yi da kanka. Professor ni ɗan siyasa ne lissafin ɗan siyasa daban yake dana Malami, bana barin kota kwana daman mun saba saka jama'a a uku, wallahi ka shiga komata yanzu nine da wasan ka fara lissafa ranakun mutuwar yarinyarka daga yanzu" da sauri Daddy ya ce

"Waye kai?"

"Sarai ka ɗauki ne muryarta professor, kana magana da Eng Ali wali mai neman takarar ɗan majalisa, ka hanani bacci yanzu lokaci ne da zaka ji abin da nake ji". "Ali wali me kake buƙata me Safiyyerh ta yi maka karka cutar mini da yarinyar don girman Allah kar ka taɓa ta"

"E, ba zan taɓa ta ba muddin ka yi abin da nake so"

"Me kake so?"

"Ka dawo jam'iyyata kuma tsagina ka lashe aman da ka yi ka kuma gyara ɓarnar da ka mini na rusa mini dukkan shirina, yadda ka ɓata sunana a wajan matasa da al'umma a gidan rediyo da kai da ɗan jaridar da yake mara maka baya ku sake sabon lale wajan wanke ni inma kana buƙatar kuɗi zan bayar hakan ba laifi bane ba"

"Uhm Ali wali kenan tun yanzu har ya yi sauri haka? Ni kake cewa idan ina buƙatar kuɗi kaga na yi maka kala da mabuƙaci? Kamar dai ka manta waye Professor kana buƙatar tuni na, laaa la la dama sauran lokaci ai. And da kake batun Safiyyerh tunaninka ita ce raunina ko?" Daddy ya tsige ruwan hannunsa da ake ƙara masa ya sakko daga saman gadonsa daman tuni ya nunawa Ummi ƙofar fita tun kafin ma ya ɗaga kiran.

"Ka yi kuskure sosai, Safiyyerh is nothing to me kuma she never be my headache idan ka so ka saka wuƙa ka yankata a yanzu is doesn't matter for me, idan akan Safiyyerh ka kira ka mini warning ka makara Ali wali tunda Safiyyerh ta bar gidan nan ko da dai da rana ban taɓa tunaninta ba siyasa ce kai kuma yaro ne mu zuba mu gani"

A ɓangaren Ali wali dariya shima ya yi ya ce "Lallai prof ka cika ɗan siyasa, to wallahi ka shirya ganin gawar Safiyyerh a wannan daren ku tara yan jana'izarta". "Idan ka haifo kuma kai cikakken ɗan iska ne idan har ba zina akai ka haifeka ba na roƙeƙa Ali wali don Allah ka kashe Safiyyerh nima fa wani aikin ka rage mini..," ƙit Ali wali ya kashe wayar daddy ya saki dariya yana wani irin murmushi wata number ya kira ana ɗagawa ya shige toilet yana saka key, ya jima ciki kafin ya fito ya zauna saman gado Dr Hash ya shigo da Yaya J ganin daddy zaune ya saka dr cewa "Daddy ya jikin naka?" Hawaye ya cika idanun daddy ya ce "ba abin da zai tafi daidai babu

Safiyyerh zuciyata zafi take my innocent Fiyya, Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un ina tsoran halin da Ummimi zata shiga" ganin hawaye a idon mahaifin nasu ya saka Junaid ficewa dr ya zauna ya dinga lallaɓa daddy da bashi bakin za a ga Safiyyerh in sha Allah.

Aliyu yana zaune a ɗakinsa aka buɗe ƙofa tare da shigowa ya ɗaga kai ya kalleta ya miƙe da sauri duk da babu fara'a a fuskarsa amma sai da ya saki ajjiyar zuciya. Ta juya idanunta "Nan ka ɓoye?" Ya girgiza mata kai

"Ka cigaba da binciken inda Safiyyerh take Aliyu kar ka saurari mahaifinka ka ji ko?" "in sha Allah Ummimi" ta zuba masa ido sai ta juya ya ce "Tafiya za ki yi?"

"Me zan maka?"

"Love, ganin ki nake son yi" ta haɗe rai tana cewa "To ɗakko zani na goyaka" ya buɗe idanunsa ya yi wajanta yana rungume ta ya saki ajjiyar zuciya "I love you Ummimi, and I love Safii too"

Kan shi ta shafa ta ce "Kawai ka zaɓa ni ko ita" ya lumshe idanunsa ya yi mata shiru, rungume shi ta yi a jikinta ta yi shiru tunani daban daban a ranta sai kuma ta sake shi ta ce "Fito waje" saƙo Aliyu ya samu cikin gaggawa sunansa ya fito a jerin sojojin da za a yi posting nasu wajan aiki ya dinga kallon saƙon yaushe ma ya dawo da za a sake tura shi wani wajan bayan babu shi a sojojin da aka yi list? Sai kawai ya fita da nufin zuwa kiran da ya samu domin bata uzurin yana da wani muhimmin aiki akan nasa iyalin ya manta da batun a tsarin aikin sojoji babu sauyi idan har a zaɓe ka.

****Mafarki ta yi mai ban tsoro ta farka a gigice tana kiran sunan TAHHB sai haki take yi fitila taga an kunna an hasko ta ya zuba mata idanu a ransa yana ƙara mamakin wannan hasken nata gefensa zabtareriyar addace saboda tsaro ya miƙe a hankali ya kunna hasken parlon sai a lokacin Fiyya ta lura da Goje dake cikin kwance cikin jini haka Mangal ga wuƙaƙe a gefen su sai numfarfashi suke yi. Ya taka ya je gabanta ya tsaya can ya duƙa dab da ita baki ta buɗe za ta yi ihu ya saka yatsarsa a bakinsa "Shhhh" ta yi tsit ya cake addar

"Mene?"

"Ban kira ka ba wallahi" ya zuba mata idanunsa masu kaifi ta janye nata "sunan wa kika kira to?"

"Tahhb"

"Sunanki ne? Ko na Abdu Marafa?" Ta girgiza kai "Mafarki na yi a mafarkin na ji sunan, amma ban sani ba ni na manta komai na mafarkin ma kai na ciwo yake i have a headache"

Ya ɗaga addar ya cake ta tsakanin ƙafafuwanta sai sheƙi take yi ya ce "Ko dai ki faɗa mini waye Tahhb ɗin da kika dame ni da kiran sunansa yanzu ki na ɓula miki cinya"

"Don Allah ka yi haƙuri wallahi ban san shi ba"

"Ke wace?" Moh ya tambaya "Safiyyerh sunana" ya cije bakinsa sosai ya ce "Matar soja ko?" Ta jinjina masa kai

"To ni waye? Kuma ya nake a wajanki?"

"Wallahi ban san ka ba, kai ba kuwa bane a wajane" idanunsa har ruwa yake ya daka mata tsawa a gigice ya ce "Waye ni? Waye ni waye tell me....

❤1 page remain ba zan taɓa buɗe komai ba shafi 15 is nothing nothing ku biya you'll never regret sai mun yi nutsu za ku fahimci labarin MUTALLAB bai haɗa hanya da kowanne kalar labari ba, idan za ka yi kuka ka fara tun yanzu 😭😂ba kuma zan taɓa sauya labarina a yadda nake ba, you better shut up...

MUTALLAB.

Book 1, 2 &3

500 Naira

0116886423 Union Bank Na'ima Sulaiman S a tura shaidar biya ta nan 08164069385

'Yan Nijar ku turo carte airtel ta 300fcfa saman wannan layin 84506476

[1/7, 9:33 PM] Sis Fauzy: *The story of a thug husband MUTALLAB, as a good parents za ku bada auren yarinyarki ga ɗan daba ɗan ta'adda? Ban ce ku fara kuka tun yanzu ba,ban ce ku ji soyayyar ciki kamar a ƙirjinku ake wanzar da ita ba.* *The story of TIGER and MOH The destiny of CAPTAIN and FIYYA. Finally the eternal love* *between..The love that separate them and back them together❤😭*

❤ MUTALLAB ❤

Page 15 last free episode

Bright pens.. 2nd batch

For more updates follow Mutallab on Arewabooks in sha Allah ❤

Page 15 shine last free pages na labarin, kar ka yi tunanin ganin wani page ɗin a waje ka yi payment a yi naka into paid group akan 500 kacal, love ɗin da kuke showing yanzu ne zai yi aiki□MUTALLAB.

Book 1, 2 &3

500 Naira

0116886423 Union Bank Na'ima Sulaiman S a tura shaidar biya ta nan 08164069385 'Yan Nijar tsarin biyan zai kasance ta *Stock na airtel*. Ku yi wa wannan layin 84506476 magana sai ta ba ku lambar da za ku turo mata stock ɗin. Kafin ɗorawa da inda muka tsaya zamu ɗauki hutun zango na sati ɗaya tal😂 maybe har a yi albashi ko masu mining ta fashe musu.

Godiya ga Hajja Aisha Abubakar Khadhfsum data biyawa mutane 8 □ ga masu business zaku iya badawa a tallata muku idan kun ɗauki nauyin page in sha Allah.

Ba zan manta da BESTIE ba□I so much love her wish you all the best Aunty Nazeefah Sabo Nashe ta ce HADARIN GABAS yana hanya. Ina son ta sosai😮😮

Gaisuwa ga haƙarƙarina😂□uwar gidan Viper tunda mun amince Nabila ce amarya Ayushercool masoyiya. My beb Zee kumurya sai tallafe ƙirji muke muna sata a addu'a gashi zata fara yi mana ZAYTOON a watan Nuwamba i love them sosai□

Conversation bana ce kuci kanku ba, saboda ina ƙaunarku Sarautar's library Mutallab fans, Nimcy paid group my ArewaBooks people. Mikiya writers Association Mikiya fans AUTAR MANYA❤ Ubangiji Ya bar ƙauna.

Last free pages

What if I tell you, I love you?

"kar ki ce ba ki sanni ba, kar ki ce haka dole ma tarihin rayuwarki ba zai taɓa cika ba sai da sunana, dole a same ni a cikin rayuwarki sai dai idan za ki cire wani sashi na cikin tarihin" ya furta yana huci da gwame numfashi Safiyyerh was shocked and speechless at the same time ta kasa kallon shi wani irin tsoro shi take ji mai girma ya ratsa zuciyarta. A hankali ta ɗago kanta zuwa gare shi hawaye na taruwa cikinsu yana sauka akan fuskarta

Ta ƙura masa ido da sauri kuma ta girgiza kai ta ce "Wallahi da gaske ban san ka ba, ban taɓa ganin ka ba sai kwanakin nan, i don't even know your name balle kai,me ya sa zan sanka to?" za ta sakar masa kuka ya ɗora yatsarsa a baki ya ce

"Shhhh" ba shiri ta yi shiru tana sauke ajjiyar zuciya shi dai har lokacin fuskarta yake kallo yana murza tsinin wuƙar a ƙasa. "To kai ka sanni ne? Ni ka cire mini wuƙar nan ka ji ɗan baƙi" ta furta tana juya idanu ta langwaɓar da kanta gefe guda.

"Ki daina kiran sunana daga yau"

"Sai na dinga ce maka me to? Ka faɗa mini ban ma san sunan ba ai" ƙoƙarin biye mata yake wajan ganin ya samu abin da yake buƙata amma a duk kalma ɗaya daya furta ko kafin ya furta sai ya fama hautsina kan shi kafin ya san me zai furta mata. Wuƙar ya ɗauke ya cilar gefe guda ya juya ya kalli Goje jira ya ke yi safiya ta yi ya fara tunanin yadda zai samu likita ya ji ta ce

"Kai ne ka yanke su ko? Ba kyau wallahi ka mutu a haka wuta zaka tafi babu fashi kana kallo za mu shige aljanna muna jiyo ihunka a cikin lazza ko saƙara tunda baka da wani aiki a rayuwarka sai daba da bushe-bushe cikinka ba komai sai ƙwaya da hayaƙi, gabaɗaya gudanawa kake daka zaɓi wannan rayuwar ne ɗan baƙi? Bayan rayuwa akwai mutuwa fa karka bari ka mutu cikin wannan halin ba zaka ji da kyau wajan Mala'iku ba"

"Kina da ɗan'uwa mala'ika ne?"

"Subuhanallahi, kai ko wa'azin baka so kamar jinin fir'auna ni tausayinka kawai nake ji tunda baka gani shikenan" ta haɗe fuska irin ta ji haushin nan har ƙasan zuciyarta ita ƙyamar shi take yi rayuwarsa a gurɓace take babu wani abu na birgewa ko ban sha'awa a ciki deep down kuma tausayin rayuwar tasu take ji tana jin da tana da iko tabbas ba zata taɓa gazawa ba wajan ganin ta taimaka musu. Ya rufe idanunsa yana daga zaunen saman kujera ya ɗauki ƙafa ɗaya ya ɗora akan ɗaya ya fara yin fito wanda ya cika ɗakin a hankali kuma ya zaro sigari zai kunna ta yi saurin cewa.

"Matsalar daƙiƙi kenan a rayuwa, shi da kansa bature ya ce tana lalata lafiya dake babu arabi ba boko ba'a gane komai ai shikenan, goodness Safiyyerh what exactly wrong with you, that's not your business" ta faɗa lokaci guda kuma tana miƙewa tsaye sai dai bata kai ga zuwa inda ta yi niyya ba ta gan shi tsaye a gabanta hannunsa riƙe da sigarin yana zuƙa da fesarwa, ta saka zata rufe hancinta ya sa hannu ya tukare jikin bango ya sata a tsakiya sigarin a bakinsa yana binta da

jajayen idanu bakinta na rawa ta girgiza kai ta ce "Mene haka wai?" Ya yi shiru yana duƙawa fuskarsa dab da nata har lokacin ita ɗin da yake kallo

"Iskanci ne wannan matar aure ce ni fa, saboda ƙwaƙwalwarka bata faɗa maka daidai ko? Idan ka sato ni a gidan mijina shine yake nufin me? Zan barka ka yi yadda ka so ko ƙazamin jikinka ya taɓa fatar Safiyyerh ba zan taɓa yafewa kai na ba, da babbar murya ina faɗa maka ni Safiyyerh matar aure ce ka ji ko? Kana jin Hausa ai?"

Ya zare sigari hayaƙin daya zuƙa ta cikin bakinsa ya dinga fesa mata a fuska ta fara tari tana ɗauke kai, ya ƙara zuƙar sigarin a baki ya matsa dab da fuskar tata ya sake fesa mata lokacin ta buɗe baki za ta yi magana gabaɗaya ta haɗiye hayaƙin, a gigice ta fara tari tare da kakarin amai ganin da gaske aman za ta yi,ya matsa a wajan tare da shigewa wani ɗakin. Safiyyerh ta durƙusa tana riƙe ciki saboda wani irin ciwo da yake yi mata ga amai dake ƙara hautsina mata kayan ciki ta rasa yadda za ta yi ta kwanta tana riƙe cikin da dinga rusa kuka. Duk abin da ya fara Goje na jinsu kawai yana cikin wani hali ne tsautsayi ya saka su fita a daren sukai karo da yan daban cikin gari sun shigo ɗaukar fansar wani faɗa da aka yi can kwanaki shine suka rufar musu, a cikin yan daban cikin garin wanda yake jagorantar su me suna Bakin wuta shine ya sare su shi kuma Moh sai da ya sari wajan mutum goma a yaran Bakin wuta wanda kuma shine faɗan su na farko a rayuwa ba wanda ya san wani, a cikin yaran ba sai da aka buɗewa wani ciki kuma duka aikin Moh ne yana da tabbacin kuma Bakin wuta ba zai bari haka nan a ci bulus akan shi ba.

Goje ya juya kaɗan ya kalli Safiyyerh dake kuka sosai kamar ranta zai fita itama yarinyar naci gare ta ga bakin tsiwa da Moh na taɓa mace da tuni Safiyyerh bata duniya ya san ba zai iya kashe ta ba amma zuwa gaba zata gane bata da wayo idan ta cigaba da kai shi bango. Tana kukan a haka bacci ya ɗauke ta bata ji kiran sallah ba amma tunda ta motsa bakinta ɗauke da addu'a ta san asuba ta yi ta miƙe da ƙyar ta nufi banɗaki ta yi alwala ta jima tana azkar kafin ta yi raka'atul fijr kana ta yi sallar asuba. A hankali ta dinga leƙa shi abin da ya bata mamaki bai shige ganinsa durƙushe a kan qwiwinsa ba yana kallon gabas ba kuma sallah ya yi ba, kan shi a ƙasa ya yi shiru kamar zata shiga sai kuma ta fasa ta tsaya cak ta samu kanta da yi masa addu'a samun sauƙi da mafita a rayuwarsa da shiriya idan yana da rabo.

"Allah Ya shiryarka idan kana da rabo"

Ya ɗago kan shi ya juya kaɗan suka haɗa ido, ba ƙaramin gigita ta yi da ganin idanunsa a haka ba, ya ƙura mata ido a ransa girman nacinta yake ƙara jinjinawa duk da bai yi mamaki bai kuma zama sabon abu ba, bai fiya son takura ba wani lokacin. Safiyyerh ta harɗe hannayenta a ƙirji ta ce "Ko yunwa kake ji na daba maka abinci? Ko shayi?"

"To na zo na yi maka shira? Ko waƙa?"

"Get out..."

Ya ce a hankali muryarsa ƙasa ta buɗe ido jin ya yi turanci ta ce "Wow ashe a ɗan san wani abu, nifa ba zan fita ba bakina ciwo yake na rashin magana gaskiya" kafin ya yi magana ta shiga cikin ɗakin ya yi saurin tashi da ƙyar ya nufi kujera ya kwanta ƙafarsa ɗaya a armchair ɗaya a can saman kujera hannayensa ya harɗe a ƙirji idanunsa rufe. Safiyyerh ta zauna a ƙasa ita kanta bata san me ya sa take son yin magana da shi ba, ta ji kuma tana barin wajansu zata haɗa Kinal da shi ita take son auren ɗan daba a hankali muryarta a nutse ta ce "Sunana Safiyyerh Abdu Marafa, ni ce auta a gidanmu..." Ta ɗan yi shiru bata ga alamar yana ma jinta ba kamar bacci yake yi haka yanayinsa ya nuna bata karaya ba ta sake matsawa ta ɗora da faɗin.

"Mahaifina professor ne ya koyar a jami'o'i da yawa a wannan ƙasar cikakken lakcara ne matasa na son shi sosai saboda yana taimaka musu da shawarwari. Ina da yayyi huɗu babban yayenmu sunansa Aliyu muna ce masa Captain shi soja ne, bashi da kirki gabaɗaya baya dariya kamar kai ɗin nan amma shi ba baƙi bane fari tas, yana da ilimi he is educated, sai mai bi masa Dr Hash likita shi a ɓangaren kwakwalwa Neurologist, shi rayuwarsa ba sawa ba hanawa sai my favourite Yaya J sunansa Junaid shi aiki biyu yake yi aikin banki da business, ina son shi sosai kamar yadda yake so na, rayuwarsa abar sha'awa ce wallahi. The last one Awais Shi kuma ɓangaren siyasa yake so amma daddy baya so yanzu dai ya ce yana son zama shahararren ɗan kasuwa ne, sai kuma ni Safiyyerh nima na yi karatu ina aiki yanzu matsayin Manager a FS WORLD INVESTMENT COMPANY, ina da saurayina da nake so kuma yake so na Ashraf sunansa ɗan mai kamfanin da nake aiki ne, akwai wasu abubuwa da bana ganewa a kamfanin..." Shiru ta yi da sauri kuma ta kalle shi taga har yanzu idanunsa rufe yake bai motsa ba

"Kodayake shikenan, saura kwana ɗaya auren mu da Ashraf ya rasu, Ashraf died ya mutu ya bar ni cikin tsoro da fargaba, a ranar daya rasu a ranar ne aka aura mini

yayana Aliyu, da dai bana jituwa da shi sam amma ƙaddara ta haɗa kuma Ubangiji kaɗai ya san dalilin hakan, wannan shine labarin Safiyyerh Abdu Marafa"

Ta leƙa fuskarsa taga idonsa still a rufe ta tura bakinta gaba "Nima sai ka bani labarinka ai muna zaune waje guda bai kamata bamu san juna ba" miƙewa taga ya yi ya nufi ƙofa kafin ta bi bayansa har ya fice daga cikin gidan.

****Eng Ali wali ya dinga kallon Moh da yake tsaye kafin ya ce "Ina wayar daka amsa wajena? Mene amfaninta ina kira baka ɗauka wai?"

"Ba gani gabanka ba?" Moh ya ce yana kame fuskarsa kamar kodayaushe.

"Yarinyar nan tana wajanka ko Mutallab?" Moh ya yi tsaki a fili da ƙarfi kuma ya ce "Ni a tarihina sau ɗaya ake faɗa mini magana na haddace ka yi batu kawai" ya ƙarasa maganar yana jawo flask ɗin shayi ya tsiyayi ruwan zafi ya saka madara da su milo ya nemi waje ya zauna ya janyo biredi da plate ɗin ƙwai ya fara ci duk zafinsa da taurin kan shi a nutse yake cin abinci sai dai baya laumar wasa

"Daman kai aka kawowa abincin karin Mutallab? Ai shikenan magana nake so mu yi very important akan yarinyar nan daka ɗakko" ya yi shiru can ya ce "magana nake maka fa ka yi shiru"

"Kunne ke ji"

"Professor ya raina mini hankali wai ko kashe yarinyar nan zan yi ko a jikinsa yana nufin bai damu da ita bane ko mene? To wallahi ni Ali wali zan bashi mamaki, yarinyar nan kafin ya ganta sai ikon Allah don haka ka yi yadda na ce a kanta, ka yi mata fyaɗe ka yi yadda ka so da ita har ta samu ciki yadda zamu watsa labaran yarinyar professor Abdu Marafa ta yi cikin shege ya kore ta daga gida ni kuma na ɗauke ta na kula da ita har zuwa haihuwa,kaga daga nan hankalin jama'a zai yi kan Professor Abdu a bar batuna ni kuma na yi amfani da wannan opportunity wajan cin nasara a zaɓen da yake gabatuwa, don this time ba zan taɓa barin Hon Maɗatai ya yi nasara a zaɓe ba zan yi duk abin da zai tabbatar dani ne na ci zaɓe ko a can hukumar zaɓan inec na shirya tsaf ba gudu ba jada baya siyasa sai ɗan siyasa, harkar siyasa da zama wani a harkar ƙasar nan sai ka nuna ba wani shege ka cire

tausayi da imani, ba ri ka ji Mutallab duk wani ɗan siyasa kan shi kawai ya sani" ya numfasa yana ɗaukar ruwa ya sha.

Moh dai har lokacin shayin yake sha hankali kwance abin shi. Ali wali ya duƙa ya ce "Dole ka yi wa Safiyyerh fyaɗe dole ne ka yi wa yarinyar nan ciki, samun cikinta shine plan ɗina na farko da zai kai ni matakin hawa kujerar ɗan majalisa"

"To ya ake cikin?"

"Baka san yadda ake yin ciki ba, ciki na haihu fa?"

"E, ban sani ba"

"Mutallab, da ake cewa ka yi aure a ranar an kashe maka matarka da me za ka yi da auren da ka yi"

"Bayan a yi wa mutum girki ya ci ya yi bacci akwai wani abu ne? To ni ban iya yin ciki ba, sara da soka kawai na sani a rayuwa da shiga jeji, ka bar batun hakan bani ba ko waye ba za a yi mata wani abu ba"

"Moh"

"Ali wali" Mutallab ya ce yana yin kyatsa yana miƙewa tsaye kuma. "Mutallab yadda aka fara aikin nan da kai, to da kai za a ɗora kuma a ƙarashe dole zaka yi wa Safiyyerh fyaɗe i am telling you this, za ka ce na faɗa maka"

"To ka fara bani matarka na yi mata ai kana da ita, sai kace Professor ɗinne ya yi mata" Ali wali ya dinga kallon Moh ganin how serious he is da maganar kuma da gaske yake. "Ni zan shige zan na ji kira idan ka shirya bani matar taka tunda yarinyarka Noor bata ƙasar"

"Ina kasan ina da yarinyar Noor?"

"Ali wali kenan"

Hanyar fita ya yi kamar wancan karan ya ƙara jin sauti mai kama da ihu ya dinga kallon ƙofar kafin Ali wali ya ƙarasu har Moh ya buɗe ƙofar ya shiga cak ya tsaya ganin wata mahaukaciya zaune sai ihu take ita kaɗai gashinta ya rufe mata fuska ya juya ya kalli Ali wali ya ƙara kallon matar bai yi magana ba ya saki ƙofar zai fita Ali wali ya ce "Ka manta kaga wannan, sirrina ne"

Ko magana Mutallab bai yi ba ya kwashi kuɗi ya yi waje abinsa yana rufe fuskarsa. Bayan ya fita Ali wali ya ɗauki waya ya yi kira ana ɗauka ya ce "an samu matsala P.A yau wani yaga ajjiyata, fitar maganar nan daidai yake da zuwana gidan yari" ta cikin wayar P.A ya ce

"Kafin ka je gidan yarin ka fara tura wanda yaga ajjiyar taka can"

"Mutallab ne"

"Tab, matsala kenan ina ruwan ciwon idanu wannan yana matsala kuna samun akasi za kaga ba daidai ba" Ali wali ya yi murmushi ya ce "Ina da tsari P.A idan na tabbatar na ci wannan kujerar zan yi tuggun da za a yi wa Mai dawa ɗaurin rai da rai a gidan yari, ka zo mu yi magana wai kasan har batun yɑ ta Noor ya sani, uhm sai ka zo dai"

Yana gama wayar ya duba interview ɗin da za a yi da dukkan wani ɗan takarar ɗan majalisa daka mabanbanta jamꞌiyyu wanda BBC ke shiryawa hakan yana nufin za su haɗu waje guda da Hon Maɗatai da Dr Abraham Denial David yana da buƙatar ya zauna ya rubuta dukkan abin da zai faɗa a wajan.

***Yana zaune ya zubawa yaron idanu gabaɗaya ba zai shige shekaru biyu da watanni ba a duniya ya yi wayo gwanin shaꞌawa duk wanda yaga yaron sai ya burge shi akwai shiga rai da ƙyar yake buɗe idanu saboda farin da yake da shi ya sauke

ajjiyar zuciya yaushe zai rabu da damuwar ran shi sai yaushe zai ga Safiyyerh ya nuna mata abin da Ubangiji ya bata, daga samun cikin har haihuwar ba wanda ta sani. A fili ya ce "Come back please Safiyyerh, where are you ina kika shiga haka me ya sa hakan? Jininki fa Safiyyerh haba my innocent Mahmah"

"Ka dinga yin addu'a komai zai daidaita ya zama tarihi Ubangiji yana gani kuma yana kallo ba zai bar addu'ar ta tashi a banza ba, zata dawo ta damu ɗan ta, zata dawo a faɗa mata gaskiya, mu ma muna da namu laifin"

"I missed Safiyyerh dear, ki bar ni na koka" ya ƙarasa ya ɗauki babyn ya rungume a jikinsa hatta farinsa irin na uwarsa ne sak yaushe zai ga Safiyyerh ne? Wayarsa ya ɗauka ya yi kira ana ɗauka ya ce "Har yanzu ba wani information akai ko?" Ya yi shiru can ya ƙara cewa "Ka san komai ba, ka san yadda na samu na tsira da raina bana sha'awar komawa kuma ni da aikin lauya har abada, komai namu a can muka baro bani da picture ɗin Safiyyerh ko guda wallahi zan yi ƙoƙarin neman ƙwararren mai zane na gani ko za a dace thank you"

Kashe kiran ya yi ya ajjiye wayar yana sake rungume yaron da ko ɗomin jikin uwa bai sani ba, balle ya sha nono kamar yadda kowacce uwa ke shayar da nata ɗan.

***Safiyyerh na zaune bayan ta gama musu girki Goje yana ci da sauri yana ƙona harshe ta ce "Kaci a hankali mana akwai zafi" ya yi murmushi ya ce "Allah dai ya ba ki kada Manager"

"Amin"

Suka yi shiru can ta ce "Wai ba ka ce yayar wannan babban naku ce ta mutu ba? Me ya sa yake zaune a nan wai, ina yayenku suke" Goje ya ce "Babata ta mutu ni haka baba, shi kuma iyayensa suna nan cikin Birget Scorpion ai baya son zuwa gida ko unguwarsu baya son zuwa, tun bayan daya dawo daga gidan yari wajan state cid"

"Kai me ya yi haka to? Kwanansa nawa a wajansu"

"Shekara uku"

Safiyyerh ta jinjina kai har ranta ta ji tana son cin labarinsa waye shi a hankali ta ce "Ai daman naga baya ji shikenan da wuƙa a hannu ya sari wani wacce kalar rayuwa ce haka?"

Goje ya ce "Manager kenan, ai yanayi ne ke sanyawa a zama haka babu wanda ke son zama mutumin banza fa, ki gane hakan". "Son zuciya dai, Ubangiji daya halicci bayinsa an ce baya ɗora musu abin da ba za su iya ba, a tsaftace halicci kowa tun daga cikin uwa mahaifiya, a nan son zuciya ne da rashin wadataccen imani a zuciya da kuma yana da ilimi ai ba zai yi hakan ba" Goje ya ce

"Ko? Kin san shi ne kin san waye shi? To ki maye masa gurbin abin da ya rasa sai kiga ya dawo daidai idan an yi sa'a"

"Me ya rasa shi ɗin?"

"Soyayya, ta uwa, ta mahaifi, ta mata"

"Ok nan wai a haka yana da mata?"

"Ta rasu" Goje ya ce a taƙaice ta yi shiru "Ki gwada cewa kina son kiga ki ce za ki aure shi" da sauri Safiyyerh ta kalli Goje ta ce "Kasan me kake cewa ne? Ina da aure fa ai zunubi ne haka"

"Zance kenan, ba ki da wani aure yarinya haka kalar masu auren take kenan?" Safiyyerh ta yi shiru ita dai ko bata aure shi ba kawai za ta yi using opportunityn ɗin nan ya bata labarinsa, ko a lissafin ƙaddarorinta babu batun zama da ɗan daba balle soyayya har ace aure amma idan har zai bata labarinsa lallai za ta yi wani abu. Ta yi murmushi ta ce

"Kana da gaskiya ka gano ni, ai kaf ƙawayena ni ce bani da aure to bana son gori shine fa nake cewa ina da aure shi Captain ɗin ai yayana ne don ka ji, amma kana ganin zai so ni? He is such a arrogant, boring person yana da matsala"

"Ki gwada mana"

"Zan ƙoƙarta, ya sunan shi ok ka ce Scorpion ko?"

"Mutallab sunan shi, mantawa na yi"

"Wow a nice name, sunan shi ya fi shi kyau shine kuje ce masa mai jeji? Kai ya sunanka?" Ya yi mata shiru kawai sai ta miƙe ta shige ɗaki.

***A karo na biyu Aliyu ya kalli Commander ya ce "Sir ka yi replacing nawa da wani mana"

"Aliyu me ya sa kake yin haka, na lura kamar aikin soja ya fara fita daga ranka ko? Ka je ka yi tunanin tun farko wahalar daka sha kafin zama abin da ka zama, ƙiriƙiri an ƙara maka muƙami amma ka nuna baka son ana kiranka da sunan muƙamin sai Captain? Why?"

"Sir to a ɗan bani sati guda ok?"

"Ba zai yiwu ba, ka je ka fara shiri cikin daren nan da kwana biyu za a poster ku" rai ɓace Aliyu ya miƙe ya fita bai taɓa Jin takaici da kuma dana sanin zama soja ba a rayuwarsa sai wannan lokacin, shekarunsa nawa a duniya sai yaushe zai cigaba da jurewa yaushe zai ta yin haƙuri baya son shiga cikin ko barrack ne balle a nisanta shi da garin, ya samu sauƙi daga matsalar mata ga kuma wannan matsalar he need his wife, seriously he need his Safii yana buƙatar Safiyyerh a gefensa.

Daddy ya dinga kallon Aliyu kafin ya ce "Aliyu mene plan ɗinka akan case ɗin nan wai? Sp Ghali yana neman information ka ja baki ka yi shiru na ce ka cire hannunka a wannan matsalar ko, ka san me hakan yake nufi?"

"Daddy Safiyyerh fa matata ce hakƙin kare ta yana wajena so allow me to do daddy ka rabu dani"

"Allow me to do daddy" daddy ya maimaita ya juya ya kalli Ummimi dake zaune tana kallon Aliyu ya ce "Kin gani ko Zahiyerh idan Aliyu ya saka na rasa Maama zai yi mamakina" murmushi kawai ta yi ta ce "Matarsa ce fa, ta ya ya zai yi wasa da ranta bayan yana buƙatar ta cikin tasa rayuwar, bana son wani magana mai tsayi da bayane babu mai yi wa Safiyyerh kutse a rayuwarta ka sani, su yi nasu binciken shima ya yi"

"Aliyu bar wajan nan"

Fita ya yi rama rasa wanne kalar tunani zai yi, daddy ya lumshe idanunsa a fili ake ganin bugawar zuciyarsa bai shirya ba sam, baya jin kuma akwai abin da zai iya kawo masa cikas bai yi maganinsa ba.

Daddy ya gargaɗi kowa akan kar a fitar da maganar sace Safiyyerh kwatsam zance ya fita a shafin daddyn wanda shi kansa bai san yaya aka yi ba, wayarsa kullum na hannunsa balle ya ce wani ya ɗauka ya yi posting cikin yaran, ya tabbatar kuma ba hacking wayar aka yi ba, aka fara kiran wayarsa domin tabbatar da gaskiyar al'amarin ya rasa ya ya zai yi kawai ya ɗauki wayar ya kashe.

***Mutallab na zaune yana sauraren Goje Safiyyerh ta fito ta saka hijabi har ƙasa bai kalle ta sai haɗe fuska da ya yi ta ce

"Abokina Goje barka ya jiki naga an yi maka treatment, ku siyo ka yayyenki na dinga yi muku tunda dai dabar ya zama dole na iya ai" murmushi ya yi

"Na ɗauka lissafin kuɗi kawai kike ai? Ashe likita ce"

Ta yi murmushi ta ce "Ina yini?" Ta faɗa tana kallon Moh ya yi kicin-kicin da fuska bai amsa ba.

"Wallahi kyau kake mini idan kana haɗa fuskar nan, na ji ina son ka kuma zan iya aurenka wallahi" ya juya ya kalleta da sauri ta kashe masa idanu ɗaya ta ce

"What if I tell you, I love you?" Ta sake cewa

"Idan fa ka amince zan so ka har numfashina na ƙarshe a duniya, kawai dai kar ka wulaƙanta ni"

"Ke bar nan"

Ya furta a kausashe kamar ya ce ya shiga uku "Na san saboda na ce maka ina da aure ne, wasa nake yi don kar ku yi mini wani abun ne na faɗa fa, trust me i love you kuma na ji zan iya aurenka a yadda kake, zan baka farinciki walwala da jin daɗi ka amince mini ka ji dear" Moh ya dinga kallon ta wani irin kallo wanda bai ma san yana yi ba,sai dai ba'a tantance kallon na mene yanayin fuskarsa bai bada damar hakan ba, kaifin idanunsa ya saka Safiyyerh ƙasa da nata idanun, duk da shaye-shayen da ya ke yi da ɗaukar wuƙa matsayin abokiyar rayuwa da tarin raunukan da suke fuskar bai hana wani irin tsoro da shakkarsa ta gitta a zuciyar Safiyyerh Abdu Marafa ba, wani kwarjinin take hango wa na musamman a fuskar Mutallab Tahhb haibarsa da kwarjininsa mai ban tsoro ga namiji balle ɗiya mace sai yanzu take ji ta yi tsaurin idanu wajan tunkarar shi da wannan maganar mai kama da tatsuniya a gare shi, gare shi kallon kin raina mini wayo ya kewa Safiyyerh da tunanin ko ta samu matsala da nata tunanin tunanin ne? Idan ba matsala ta samu na gushewar tunani ba abu mamaki ne gare shi da jin furucinta ya yunƙura zai tashi ta riga shi miƙewa kanta a ƙasa hawaye na zuba a idanunta.

"Don darajar da Allah Ya yiwa Manzon Sallallahu alaihi Wasallama ka saurare ni, ba zan taɓa juya maka baya ko da nasani b a kasancewa ta da kai, kai musulmi ne nima musulma ce babu haramci idan mace ta ƙaunaci namijin daya kwanta a ƙasan zuciyarta, a kullum na ganka sai na ji zuciyata na kiran Safiyyerh wannan shine ƙaddararki zaɓin da kike jira irin namijin da kike fata, idan zuciyata ta kusanci zuciyarka sai na ji tawa zuciyar ta sake buɗewa da tarin tausayinka, kullum mutuwa nake da farfaɗuwa da soyayyarka ta yan kwanakin nan data rutsa da zuciyar Safiyyerh Abdu Marafa, kullum mutuwa nake da son ka, wallahi...," kasa cigaba ta yi saboda kukan daya ƙwace mata da gaske, da ace ita yɑr wasan kwaikwayo ce irin fina finai da ake haskawa sai ta ce a yanzu acting take, duk abin da take faɗa she doesn't mean it, iya laɓɓanta ne kawai ta yi hakanne saboda ta yi kutse cikin

rayuwarsa ta san waye shi me ya sa ya zama abin da ya zama, tana son jin labarai mai kama da hikaya ko almara ko na soyayya.

"Will you love me?" Ta ce tana marairace masa fuska tare da ɗan turo masa jajayen cute lips ɗinta, ya bi lips ɗin da kallo ta haɗe hannaye waje guda ta langwaɓar da kai

"Please, Safiyyerh loves you a nan a cikin nan ɗina"

Ta nuna masa saitin ƙirjinta wajan zuciya da yatsarta manuniyya sai ƙifta idanu take. Har lokacin bai ce mata komai ba kamar yadda ta lura yawan magana ba ɗabi'arsa bane yana wanzuwa da shiru da tunanin ya fi masa. A duk maganarta ɗaya ƙare haɗe fuska yake yi ya zaro sigari ya kunna ya saka a baki da ƙarfi ya zuƙi hayaƙin yana jin saukar hayaƙin ƙasan ƙirjinsa ya hura kumatu ya matsa dab ya fesa mata a fuska ya yi gaba abin shi yana taku ɗaiɗai irin he don't care. Safiyyerh ta bisa da idanu ta yi shiru ta ji ta damu sosai a ranta tana Astagafirulla data tuna da gaske ita matar aure ce matar Aliyu Abdu Marafa ce ita halaliyyarsa ta jingina da jikin bango tana lumshe idanunta.

Moh bai ƙara dawowa cikin gidan ba, har dare ya nutsa bama shi ɗaya ba kusan dukkan su basa nan ta dinga sallah tana addu'a har girki ta yi musu ta ajjiye amma ya yi sanyi. Tana haka ta ji an buɗe gidan da sauri an shigo ta buɗe ƙofa ba tsoro ta fito Mangal sai nishi yake yana kallon ta, da gudu Goje shima ya shigo yana shigowa kuma ya rufe ƙofar ya zube a ƙasa ta kalle su cikin sigar damuwa ta ce "Ka rufe ƙofar shi kuma fa?"

"Bai shigo ba?" Ta jinjina masa kai ya miƙe tsaye ya ce "Jagwal kenan, ai kuwa bama tare"

"Innalillahi kamarya like how bakwa tare?"

"Ke bafa wani abu saɓe kawai ki je ki yi kasa ko". "A'a don Allah ka je ka nemo shi ka ji ɗan'uwanka ne fa idan wani abu ya same shi ai ba za ka ji daɗi ba, shi ma ba zai bari komai ya same ku ba" ya yi murmushi ta lura yana da fara'a ba kamar

sauran ba "Ubangiji nada kyakkyawan tanadi a rayuwar Mai dawa, ba yanzu zai mutu ba kin ji ko?"

"Na kawo muku abinci?"

"Dar daidai kenan kin taimaki yan hanjina jagwalo shi nan a ɓatar da shi a rufawa ciki asiri" abincin ta ɗakko ta kawo musu duk yadda taso su wanke hannu ƙi sukai Kodayake haka ogan nasu shima yake. Har bacci ya ɗauke ta bata saka shi a idanunta ba. Sai da asuba ta fito dafa ruwan wanka kamar jiya haka ta ganshi ya yi shiru yana kallon sama, tunanin maganganun da Abbasa ta yi masa yake da abin da Ali wali ya dinga nanata masa akan Safiyyerh.

"Bai kamata gwarzona ya wanzu yana tunanin da zai iya illata masa rayuwarsa da zuciyarsa ba, haba mafaraucina" ya juya ya kalle ta, ta kashe masa idanu ta ce "Yes, ba farautar dabbobi kawai ka iya ba ka yi dacen farautar zuciyar yar Professor Abdu Marafa" kamar a buge yake haka ta lura da shi musamman yanayin zaman da ya yi, sai a lokacin ta lura da yankan dake damtsen hannunsa ta ƙarasa ta duƙa ta ce "Subuhanallahi faɗa ka je ka yi haba mai sunan manya, Muhammad Mutallab fa masu sunanku salihan banyi ne"

Ya duƙar da kan shi ƙasa ta je ta ɗakko kayan da Goje ya kawo ta zauna dab da shi, ta kamo hannun nasa sarai ya jita amma bai kula ta ba, tunani ne ya addaba masa. Ya shiga hura masa iskar bakinsa ganin yankan na kumfa data saka magani ta gama yi masa treatment ta kalle shi taga ya rufe idanu miƙewa ta yi zata fita kamar daga sama ta ji ya ce

"Cikakken sunanki"

"Safiyyerh Abdu Marafa"

"Cikakke" ya sake maimaitawa "Haka sunan yake fa Jarumi"

"Shi Abdu?"

"E, sunan daddy kenan Abdu" ya buɗe jajayen idanunsa ya watsa mata su ta yi saurin yin ƙasa da nata idanun ta fidda ran zai yi magana har zata juya ya ce "Ƙarya, idan na tuna miki na kwaɗa miki mari ko?". "Allah ni dai haka na sani babana ne fa"

"Uhmm" ganin kamar da magana a bakinsa kuma a buge yake ta matsa ta zauna ta ce "Jarumi, do you want to say something? Say it. Ka ce wani abu Jarumi"

"Faɗi mana Jarumi"

"Tiger" ya ce a hankali ta ce "Me ka ce? Ban ji ba"

"Ammm, hmm kika ce ba ki da aure?" Ta ce "E, bani da shi like a told you" ya buɗe ido ya zura mata idanu yana ta kallon ta da ƙyar ya iya cewa "za ki so ni?"

"Zan aure ka na rayu da kai idan ka faɗa mini labarinka waye kai?" Ya sake yi mata shiru "Ina ji"

"Zana ba ki labarina idan za ki aure ni"

"Ni Safiyyerh na yi maka wannan alƙawarin zan rayu da kai a duk yadda rayuwa ta yi da kai Jarumi" ya miƙa mata tafin hannunsa a hankali kamar mai jin tsoro ta kalli hannun cike da rashin fahimta, jiran ba'asi take shi kuma ya yi shiru sun ɗauki minti biyar da wasu daƙiƙo a hankali ya sake furta "Promise" ta dinga kallon hannun kafin ta yi Astagafirulla da tunanin Ubangiji ya yafe mata saboda igiyar auren wani ce a kanta ta ɗora ɗan ƙaramin hannunta cikin nasa, tana sawa ya damƙe kamar abin da yake jira kenan ya yi shiru ya lumshe idanunsa muryarta na rawa ta ce "I Promise you Jarumi" yana riƙe da hannun bai cika ba bai kuma yi magana ba can ya sake ta, ta fara masa magana sai dai ko tari bai kuma yi ba tunaninta bacci yake yi ta dinga kallon shi tana son hango kyau ko ko muninsa.

A daren ranar su Goje basa nan sai shi ɗaya yana busa hayaƙi a sama yake jinsa sosai ya ji an buɗe ƙofa an shigo, maza ne har su huɗu sun rufe fuskokinsu ya damƙi wuƙarsa kafin ya miƙe ɗaya ya cafki wajan yankan da Safiyyerh ta gyara masa ya janyo hadda naman wajan suka fara kokawa yana buga su da ƙasa, cikin sauri Safiyyerh dake bacci ta farka zata fito daga cikin ɗakin ya yi baya da ƙarfi ya tura ta ciki ya rufe ƙofar ta taga ta leƙo tana kiran shi, taga ya ɗaga wuƙa ya sokawa ɗaya a gefen wuya ya ƙara soka masa a ciki ya watsar da shi can gefe yana kakari, Safiyyerh ta zaro idanu tana rufe baki saboda ihu za ta yi ganin yadda aka yi kisan kai akan idanunta, bata san mene ya faru ba taga ɗaya ya zaro sirinjin allura ya zirarawa Moh a damtsen shi, ya sake zaro wani ya yi masa da azama Moh ya ɗaga wuƙar hannunsa ya sari wanda ya yi masa hakan ya goce ganin sun yi masa allurar suka ja wanda yake kwance kamar gawa suka bar gidan, a hankali ya yi baya ya zube saman kujera jini na ɗiga jikinsa

Ilahirin jikin Safiyyerh rawa yake cikinta ya ƙulle ta shiga uku, kisan kai aka yi akan idanunta haka dabar take dama? Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un. Moh kuma minti goma ya yi yawa ya ji zufa na yanko masa jikinsa ya yi sanyi wani irin baƙon al'amarin ya fara ziyartar gangar jikinsa yana sauka a mararsa, abin da bai taɓa tunani ba idanunsa ya shige ciki ya ɗauki ƙwaya ya zura a ƙasan harshen shi da tunanin zai daina ji, amma ina kan shi ya hau ciwo ya miƙe da ƙyar ya nufi ɗaki jin tsigar jikinsa na miƙewa da zubewa sanyi na ratsa shi komai na jikinsa ya bubbuɗe al'amarin buƙatuwar wani abu. Ya kwanta ya yi shiru can ya mirgina ya yi rufda ciki ya lumshe idanunsa ya jiƙe shimfiɗar lokacin ɗaya da zufa da jinin da yake zufa a jikinsa, ya rasa ciwon ciki yake ko mara ko zazzaɓi? Jijiyoyin kan shi sun miƙe raɗau lallai ya ji akwai abin da yake buƙata ya dinga juyi ya shanye sigari kwali wajan biyu amma ba abin da ya sauya ba zai ce tsautsayi ne ya kai shi ɗakin Safiyyerh ba saboda kawai tsintar kan shi ya yi a ciki.

Safiyyerh na bacci ta ji hucin numfashin mutum a fuskarta ta buɗe idanu da sauri ihu za ta yi ganin fuskarsa kamar zai haɗe da tata ta yunƙura zata tashi ya saka hannu ya mayar da ita kwancan "Dan Allah karka mini komai ka yi haƙuri ba zan sake kula ka ba, innalillahi na shiga uku daddy ka yi na tuba don Allah" bai kulata ba yana daga durƙushen da yake dab da ita ya miƙa hannu ya kashe wutar ɗakin gabaɗaya.

LAST FREE PAGES

Waye Mutallab?

Waye Scorpion?

Wace Safiyyerh?

Waye Daddy?

Mene FS WORLD INVESTMENT COMPANY?

Labarin Mutallab da tarihinsa ya fi wannan da muke ciki yanzu ai za ku zo jin wannan soyayyar ta ƙuruciya ba?

Mene yake saka a fara daba da shaye-shaye?

Wanne ganganci iyaye suke yi akan yara?

Mece siyasa da cikakken tarihin dimokuraɗiyya?

Za ku su sanin ya ake mulki a ƙasar nan?

Har ku yi supporting yaran ku?

Soyayya na saka shaye-shaye ne ko daba? Me ya sa Mata har uku suka mutu ta sadanadin MOH me ya sa ya kashe matarsa SAFIYYERH?

YAUSHE SAFIYYERH TA HAIFI YARO?

maza hanzarta yin payment chat with me on WhatsApp 08164069385

BRIGHT PENS... 2ND BATCH □□

[1/7, 9:33 PM] Sis Fauzy: Chapter 16: You're my destiny

“Don't touch me” Safiyyerh ta ji saukar husky voice ɗinsa cikin kanta, sautin ya ratsa jiyiyon ƙwaƙwalwarta ya sauka har tsakiyar ƙahon zuciyarta da take bugawa, ban da ta san bai iya turanci ba tabbas za ta ce the voice is belong to him kai tsaye, tuna cewa shi ɗan daba tantiri ne kuma ɗan ta'adda uwa uba kidnapper ya saka ta tattara shakkunta a kan shi zuwa gebe, hasken ɗakin ta kunna har lokacin jikinta rawa yake ta juya a hankali ta dube shi, duba na tsanaki ya kifa kansa tsakanin ƙafafuwansa tare da tura hannunsa ya matse ƙafafun da kyau, jikinsa na wani irin ɓari domin har naman jikinsa rawa yake ya haɗa uwar zufa dukkan wata jijiya ta jikin nasa sai da ta bayyana tana amsar yanayin da ya shiga. Wani abu mai kama da tsoro ya ruski zuciyar Safiyyerh muryarta na rawa ta dube shi

"Baka da lafiya ne Jarumi? Meke damun ka?" Ta jera masa tambayar amma ko motsi bai yi ba, balle ta saka ran amsawa ta matsa kusa da shi tana leƙa fuskarsa amma ko idanunsa bata hango ba sai jijiyar kansa dake harbawa, wani abu ya gilma a ƙirjinta ta ji kamar zuciyarta ta motsa, motsin da bata san na mene ba a raunace ta ce

"Talk, ka faɗa mini meke damunka abinci za ka ci? Ko tea zan haɗa maka?" Duk ta rikice musamman jinin dake zuba a jikin nasa wanda ana ɗaukan wani lokaci komai zai iya faruwa ta miƙe cikin sauri ta bar ɗakin ba jimawa ta dawo hannunta riƙe da Frist acid box da Goje ya kawo ta shiga fito da kayan ta matsa dab da shi duk da zuriyarta cike take da tsoro ta saka hannu zata ɗaga rigar jikinsa ta ji ya ce

"Shhhh, kar ki taɓa ni"

"Kamarya kar na taɓa ka, salon ka mutu Allah ya kamani da laifin salwantar da rai, i am Safiyyerh the whole manager mai sarrafa biliyoyin kuɗi, amma hakan baya nufin bani da imanin da tausayin da har zan zuba maka idanu jininka ya tafi a banza ba, kuma wa zai so rasa jarumi? Kai Jarumi na ne, don haka ka tsaya now i am a doctor don't move" ta yi maganar in a serious tone.

"Kar ki taɓa ni" Moh ya sake tattara dukkan ƙarfinsa wajan sake maimaita furucin da ya yi har lokacin kuma bai ɗago kai ba. Safiyyerh mamakin yadda ta ji muryarsa na fita a hankali ta yi, ba rauni a cikin sautin sai zallar buƙatuwa na wani abu sai sake curewa waje guda yake. "Nifa bana gane ma'anar na rabu da kai, mene a jikin naka banda sara da suka? Haba jarumi ba'a san irin ku da rigima ba, ko kuna rigima ai bakwa yi wa mace" ya yi shiru bai tanka ta ba, ta san kuma ba lallai ya sake cewa komai ba sun fi minti goma a haka can ta ji ya ce

"Naaa, switch off the lights" ta juya ta kalli hasken ɗakin ta kalle shi da garjejen jikinsa

"A'a haske ai rahama ne haka kawai na kashe ban san me zai faru ba,daga ni sai kai? Ka bari na dinga ganin komai ina yi maka dressing ina kallon rigimammiyar fuskarka". "Kee, kika taɓa ni duk mai ne yi miki ko ya biyo baya shikenan" ya ce yana ɗago kansa, wani irin fitsari ta ji ya ɗaure mata mara yana mintsininta ba ƙaramin tsoro idanunsa suka bata ba, ta karanci psychologist ko ta nutsu lallai zata iya hango hutar feelings ɗin da yake yawo cikin idanunsa ya kaɗa ya yi jawur. Safiyyerh ta yi saurin ja baya tana ɗaga hannunta sama tare da girgiza masa kai "Laaa la la, nama fasa yi maka treatment ɗin yi bacci abin ka"

A hankali komai na idanunsa yake warware wa daga maye zuwa wani abu nada daban, wanda yake da tabbacin ko mene abin da yake ji, lallai yana wajan Safiyyerh, a wajan Fiyya zai samu he just look at into her eyes, ya dinga kallon jikinta daga sama har ƙasa, ba wai relief yake samu ba, wani irin processing ƙwaƙwalwarsa ke yi masa a hankali ta fara masa tunanin wani long term memories daya shuɗe wanda yake zane daram a idanun zuciyarsa yadda take tsaye a gabansa haka wancan lokacin, kamar kuma yanzu ne take tsayen idanunta cike da hawaye.....

**** “Idan mutum na zama ƙaddarar mutum, lallai kai ne tawa ƙaddarar, you're nothing but my destiny, a ƙirji nake jin duk zafin abun, a nan nake jin ciwon" ta nuna masa tsakiyar ƙirjinta inda zuciyarta ke harbawa, hawaye na cigaba da zuba daga cikin idanunta. Yana zaune saman kujera saboda lokacin break ne, gudun haka ya saka ya keɓance kan shi yana avoiding ɗinta. Yana jin kukan nata ya kasa ce mata komai sai ƙafarsa da yake kaɗawa a hankali yana gyara zaman goron dake damtsen hannunsa.

"Zan iya mutuwa, ko sai na mutu ne zaka ji kana so na? Don't let that happen, ka daina wasa da feelings ɗina kana wahalar dani har ciwo na yi satin daya shige" ta ɗan langwaɓar da kai gefe alamar tausaya wa tana tura masa bakinsa gaba. "Ba kaga na rame ba?"

"Da kin mutu, zan fi jin daɗi" ta bubbuɗe idanu waje ta juya ganin ba wasu students da sai ta ji kunya domin ya gama yarfata. Kafin ta yi magana ya juyo gabaɗaya ido cikin ido yake yake kallon ta muryarsa ba wasa ya ce "Yama sunanki? Ina ji zan haƙura da cikar burina na bar makarantar nan saboda ke, kin takura rayuwata kin ƙuntata ni kin hanani sukuni, wai so hauka ne? Da za ki gane yadda nake jin zafi a tawa zuciyar a duk sanda kika kalli cikin idanuna kika furta mini wai kina so na, are you crazy? Are you mad? Wai iyayenki daman soyayya suka kawo ki ne ki yi a school ɗin nan ko karatu, babban takaicina kamar ni yar ke ki addabe ni da so? Har nawa kike yaushe aka haife ki? Shekararki nawa a duniya? Irin ku ne guntattakin yaran nan masu rawar kai, mace har mace ba aji, what a stupidity? Are you not Ashamed? Oh irin ku ne wanda last subject teacher ya yi bayani akan yara masu tashen balaga?..."

Maganar yake yana runtse idanu, har zuciyarsa yake furucin cike da takaici kuma yake zuba mata narkakkun idanunsa, ita kuma kan ta a ƙasa hawayen ma ya kasa

fita daga cikin idanunta, sai yanzu ta san cewa kuka rahama ne kuma yana cikin abu mafi sauƙi da yake samar da sukuni a zuciya bata farfaɗo daga maganganun da yake gasa mata ba ya ɗora da. "Laa, ba za ki lalata mini ƙuruciya ban cimma komai a rayuwa ba, ni dai ina roƙan ki saboda iyayenki ki dai na bibiyata kina manne mini kamar kaska, kai ni ba zan taɓa manta tarihin makarantar nan ba, zanen ƙaddarata baya cika daidai sai an saka sunan wannan makarantar oh, bawan Allah Na Ammo" ya yi maganar very serious, da tunanin ya yi ending tare da solved na problem ɗin shi da ita, ai da sauri ya buɗe manyan idanunsa jin gabaɗaya ta shige jikinsa ta rungume shi numfashinta na wani irin fisga, afa secondary school suke? Ya ilahil alamin, wannan ta zame mishi jarrabwa ya dinga ƙoƙarin rabata da jikinsa, ta yi masa wani irin riƙo a tight hug wanda ya fito daga can ƙasan zuciyarta hakan ya sa ta fara jin sassauci saboda ɗan ƙaramin connection ɗin da suka samu "Shikenan, zan barka zan haƙura da soyayyarka kafin nan ai na ji an ce kana aiki kai Ɗan'malam ne, na roƙe ƙa da girman Allah ka yi mini aikin da zan manta da kai a rayuwata, zan manta da kamanminka a ko a cikin baccina, ka yi mini wannan alfarmar" fisgeta ya yi daga jikinsa, saboda ya fara jin developing feelings towards opposite sex yana attacking nasa wannan da akai musu magana a matakin Adolescence, bai jira komai ba ya watsa mata yatsu biyar a fuska yana poiting hannunsa zuwa gare ta "Haka kika ce? Za kiga aikin Ɗan'malam za ki manta da ko sunana ne completely a rayuwarki" a lokacin har students sun fara bayyana a wajan ta tsuguna a wajan muryarta bata fita sosai ta ce

“I love you beyond words, I love Mutallab”

***Kau! Kau! Safiyyerh ta ji saukar maruka a fuskarta, bata san yaushe ya miƙe har ya matse ta a jikin bango haka ba, sai numfashinsa ta ji mai sauka da warin sholin daya sha, wani abu na bugarta ta kasa magana. Kamar yanzu ne haka yake jin abin abin saboda abubuwa da suka masa yawo a zuciya ya dinga kallon cikin ƙwayar idanunta ƙirjina na buɗewa da ƙyar ya iya gwame numfashi ya furta

“Good, kin mata ɗin completely?"

"Me ɗin? Ya zaka matse ni a jikin bango kana na manta, amai nake ji zan iya yi maka a jiki" da ƙyar take iya maganar, ta zame idanunta daga nasa ba zata jure kalla ba ko kaɗan "Wai wanne irin abu ne haka? A karan farko ka caka mini wuƙa, again kazo har gida ka sace ni, yanzu ka mare ni ban yi maka komai ba, ka mayar dani gaban iyayena ka rabu dani duk abin da kake so zan baka, ina da kuɗi a lot of

money, na gaji da zama da yɾan ta'adda mashaya, soyayyar ma na fasa allow me to go don girman Allah"

"You builds and destroys everything"

Kamarya? Ta tambaya a ranta ita sam bata ganewa "Who are you,waye kai? Me kake nufi"

"Fita" ya ce da ƙyar da ƙyar yake motsa ko yatsarsa ne, banda cewa shi ne abin ya faɗa masa yana da yaƙinin da ita ɗin ce da tuni ta jima da ya yi masa fyaɗe, wani irin zafi yake ji yana keto ruɓu bakwai na farar jikinsa ya buɗe bakinsa kamar zai magana sai kuma ya hura mata warin abin da take gudu da gayya, gabaɗaya kayan cikinta suka hautsi ne, ya kasa motsi balle ya bata hanya idan har ya ɗaga hannunsa lissafin ne zai sauya, Fiyya ta dinga kakarin amai ta saka dukkan ƙarfinta wajan ture shi amma ina, ko motsi baya yi baya ya zai matsa cikin rashin sa'a kuma jiri ya kwashe shi da shi da ita sukai ƙasa, ita ta fara faɗuwa ta fasa ihu shi kuma ya faɗa jikinta azaba ta saka kawai ta saki kuka wani irin ɗaci take ji a ranta ta dinga ture shi, ya yi shiru sai sauke numfashi yake ya fi ƙarfin minti ashirin kafin ya janye jikinsa cikinsa ya miƙe tsaye ya nufi waje idanunsa rufe, Safiyyerh ta dinga kuka ta cure waje guda tana ja masa Allah Ya isa kafin kuma ta fara sheƙa amai kamar ta mutu.

Yana fita ya ja kwalin sigari ya dinga zuƙa yana fesarwa, komai yake baya jin daɗi bashi da nutsuwa sama da shekaru uku kenan. Yana ji aka fara kiraye kiraye amma ya kasa motsi zuciyarsa sai magana take yi masa ita kaɗai.

****M. General ya dinga kallon Aliyu da mamaki fuska kuma a haɗe cike da gargadi da takaici da kuma nuna dole sai ya yi abin da ake so ya ce "MAJ, domin ba zan iya ce Captain ba gwara na faɗa maka asalin muƙamin da kake da shi a yanzu, da farko ka faɗa mini hujjarka na ɓoye matsayinka a aikika wa danginka da mutanen jiha da ƙasa? A.A MARAFA ko ka manta wahalhalu da ɓata lokacin da ka yi akan uniform ɗinka da aikinka? Gashi yanzu dama ta sameka na ƙarin wani Matsayin kake wasa da wannan opportunity ɗin are you okay?"

"Yes, i am"

"Your not serious MAJ, dole ka je fa kama fara shiri tun yanzu ina ɗaga maka ƙafa ne saboda dalilai da yawa banda haka uhm" M.General ya yi shiru yana kallon MAJ Aliyu wanda yake amsa sunan Captain saboda wani dalili.

"Sir, ba lallai ku fahimta ba akwai nauyin daya hau kai ne ina buƙatar sauke shi, ka yi mini afuwa a sauya sunana"

"Saboda matarka?" Kai tsaye Aliyu ya ce "Idan ka ce hakan ba laifi" Ya jinjina kai can ya ce "This is serious, mace ta shigo rayuwar MAJ, idan ka manta bari na tuna maka ka yi karatu a NDA Nigerian Defense Academy, wa'adin shekara biyar ka yi a makarantar lokacin yaye ɗalibai ka fita da igiyar farko zuwa SND LT second Lieutenant matsayi mai tambarin star ɗaya kenan, daga nan ka je course zuwa Taraba state for 6month bayan ka dawo ka samu matsayin Lieutenant LT tambarin star biyu, bayan nan ka yi shekara huɗu ka samu matsayin Captain CPT tambarin star 3, daga nan ka ji shekara huɗu ka yi course da exam ka tsalleke wannan matakin, ka samu matsayin Major MAJ, tambarin tsuntsu ɗaya" M.General ya yi shiru yana juya kujera

"Matsayin da mahaifinka bai san da shi ba, ka nemi alfarmar ɓoye sunanka shekaru kenan kana a matsayin MAJ, yanzu dama ta sameka an yi posting naka zaka je Jaji Military cantonment Kaduna za ka yi course na shekara ɗaya, da zarar kaci ka haye ka samu igiya ta gaba idan baka samu ba ka maimaita, Aliyu matsayin LT COL kake shirin rasawa fa? Ka san matsayin LIEUTENANT COLONEL kowa?"

"Na sani"

Aliyu ya ce fuskarsa ba walwala kamar ya ce ya shiga uku M.General ya buga table ɗin gabansa ya ce "Stupid dole ka je ko ka fuskanci hukunci, wannan sunayen daga wajan Lieutenant General ya fito sun karɓa ta hannun Chief of Army staff ne kuma, wallahi MAJ ka kiyaye kan ka daga sharrin sojoji malam get lost mumu" Miƙewa Aliyu ya yi rai ɓace ya fice zuciyarsa a cunkushe. Yana fita MG ya kira waya ba jimawa aka ɗauka cikin girmamawa ya ce "Done Sir" haka kawai ya ce ya kashe wayar ya ajiye.

MAJ Aliyu na isa gida a main parlo yaga jama'ar gidan da jami'an tsaro ya ɗan tsaya ya kalli Ummimi ya kalli daddy da Ummi sai kawai ya nufi part ɗinsa "Aliyu" ya ji

kiran Daddy hakan ya sa ya tsaya ba tare daya juyo ba cikin takaici Daddy ya ce "Me kake shiryawa? Aliyu idan ka yi making any mistakes ka saka aka kashe mini yarinya wallahi zan baka mamaki, na ce ka cire hannunka daga wannan maganar kaƙi ko?". "Daddy me kake so na yi?" Kai tsaye ya ce "Ka cire binciken da kake akan wanda suka sace mini Maama, ka bar hukuma su yi aikin su ga Sp Ghali nan zai yi abin da ya kamata, ka ji ko"

"Shittt, ka san ciwon da ka saka mana a zuciya a yan kwanakin nan ni da Safii Daddy? Ka san me muke ji a cikin ran mu? Kasan fargaba da zullumin daka saka zuciyoyinmu, ka san halin da ɗayan mu zai shiga iya ya kasance ba kai ne wanda ka haife wani daga cikinmu tsakanin ni da Safii, idan mu duka ranka ne na san na yi ilimi daidai gwargwado babu aure tsakanin sister and brother, idan ba haka bane ni ne ba ɗanka ba ko Safiyyerh? Tell me daddy, ban san komai na ka aura mini Safii without my knowledge na yi accepted auren itama ta yi, bamu soyayya a zuƙatanmu muna ƙoƙarin fara ginawa, an zo an ɗauke mini mata har gida sai na naɗe bakin hannu na yi shiru? bayan inda da damar kuɓutar da ita? Safii daddy my wife, ashe ma Aliyu bai amsa sunan soja ba, su yi aikin su na yi nawa" tunda ya dawo gidan da ƙasar, bai yi magana mai tsayin haka ba sai huci yake, idanun Ummi cike da hawaye ta ci kuka ta gode Allah wasa wasa sace Fiyya na neman zama babban abu gashi shiru ba amo ba labari. "Aliyu ka san ba zan cutar da kai ba ko? To ka yi abin da na ce ka basu information na yadda aka sace ta"

"Uhmm"

"Ina magana kana uhm? Aliyu ni, ni ko Aliyu mahaifinka?"

"Daddy zan basu information ɗin kafin nan ka fara amsa mini tambayoyina, Daddy waye ni Aliyu? Wace kuma Safiyyerh? Ya akai batun sace Safiyyerh ya fita a wayarka? Mene ya saka aka ga motarka a ranar da aka caka mata wuƙa? Daddy me ya sa kukewa Safiyyerh allura? Wacce kuma allura ce? Daddy ya akai ka aura mini Safiyyerh a ranar da saurayinta wanda zata aura Ashraf ya rasu? kuma me ya saka yanzu kake son na janye hannuna daga binciken sace matata, matar soja ni MAJ A.A MARAFA?" Daddy ya dinga kallon Aliyu da tarin mamaki musamman jin muƙamin MAJ ya fi komai gigita shi da bashi mamaki. "Aliyu ina son ka saki Safiyyerh yanzu ba sai anjima ko gobe ba, ina son ka sake ta tunda idda bata hau kan ta ba"

"Divorce? Safii zan saka daddy me ya sa?" Daddy ya ce "Daman ni na aura maka ita baka sani ba, yanzu kuma na sace ka sake ta bisa umarmina ka sakar mini yarinya yanzu now". "Over my died body, idan akwai rabuwa to mutuwa ce zata raba ni da matata Safii, idan kuma kana son na sake ta ka bani amsar duk tambayoyin da na yi maka" yana cewa haka ya juya kamar zai tashi sama, Ummimi ta bisa da idanu tana girgiza kai. A wannan karan Daddy ji ya yi ciwon gaske na neman kama masa zuciya ya yi baya cikin sauri Dr Hash ya riƙe shi yana zaunar da shi. Sp Ghali ya ce

"In sha Allah Safiyyerh zata dawo gida na maka wannan alƙawari, kuma duk wanda muka samu da saka hannu wajan sace ta zai girbi hukunci daidai abin da ya aikata, zamu tafi zuwa anjima ko gobe zamu dawo duka ma'aikatan ɓangaren gidan Captain suna hannunmu, babban abin damuwar bincike ya sake nuna mana bayan wanda suka sace Safiyyerh akwai tabbacin zuwan Scorpion wajan lallai ya kasance a wajan"

Kasa magana Daddy hakan ya saka Sp Ghali da shi da team ɗinsa barin gidan. Daddy ya juya ya kalli Ummi dake kuka kamar ranta zai fita kafin ya yi magana ta miƙe ta bar wajan, J ma ya fice daga parlon Ummimi ta kalli daddy ta ce "Professor mene haka? ka tabbatar Safiyyerh ta dawo cikin ƙoshin lafiya" ta miƙe da ƙyar tana haki ta nufi part ɗin Aliyu ta same shi yana haɗa kaya ta nemi waje ta zauna ta san komai zata ce ba zai yi magana ba yana gama haɗa kayan ya ɗauki jakarsa ya kalle ta ya ce "I will leave"

"Where?"

"Zan dai tafi"

"To ka sakar masa yarinya ka ji ko Gadanga" ya dinga kallon Ummimi can ya ce "Ok ni ne ba ɗan shi ba kenan?"

"Yaushe na ce haka?" Bai magana ba kawai ya ɗauki jakarsa ya yi waje tana ta kiran shi ya yi mata banza ya yi gaba. A harabar gidan ya ci karo da Dr Hash, dr ya yi murmushi ya ce "Babban yaya ba dai tafiya ba?". "Ka faɗa mini wacce allura kakewa Safiyyerh,kuma akan wanne dalili?" Dr Hash ya ce "Na faɗa maka Daddy zaka...." Wani irin wawan mari Aliyu ya saukewa Dr Hash yana nuna shi ya ce "Idan

na ƙara tambayarka ka ce mini haka sai na tabbatar na karya wata gaɓa ta jikinka kafin na sake maimaita maka tambaya, wacce allura kakewa Safiyyerh?" Dr Hash ya dafe kunci sai ya yi murmushi ya ce "Akan Safiyyerh kake wannan? Kar kasu sanin dalili domin ina da yaƙinin ka ji hujjar yi mata allura zaka tsane ta ne, tsana mafi muni kuma kafin ka bar gidan nan sai ka tsinke igiyar aurenka da yake kanta, ka bar hakan tunda baka san komai ba daman ita dauɗar gora ciki kan shata, kamar Safiyyerh matsayin new Safiyyerh da take rayuwa a yanzu kar ka buƙaci sanin wacece old Safiyyerh, wallahi ka ji ko wacce sai ka tsinewa kan ka na amincewa da aurenta...

MUTALLAB ❤

Paid book

Book 1&3 #500

0116886423 Union Bank Na'ima Sulaiman S 08164069385 for more updates follow on Arewabooks

[1/7, 9:33 PM] Sis Fauzy: Chapter 17: Who is Safiyyerh?

Paid book chat this number via WhatsApp to subscribe urs 08164069385

Dr Hash ya sake dafa kafaɗar MAJ Aliyu ya ce "One more thing, kar ka nemi jin tarihin Safiyyerh domin zai iya tarwatsa maka zuciya, ina faɗa maka hake ne a matsayina na ɗan'uwanka kuma ƙaninka, idan Ubangiji ya rufewa bawa wani abu, yana nufin sanin abun ba alheri bane ga rayuwarsa ina farinciki kuma daya kasance kai ne mijin Safiyyerh ina murna sosai amma kamar komai a yadda yake babban yaya, bana nufin abu ne mara kyau ya shuɗewa komai na rayuwar Ubangiji yana da nufin samuwarsa a kan shi. Ka zauna da Safiyyerh matsayin new Safiyyerh kuma matarka don Allah" MAJ ALIYU ya dinga kallon ganin nasa cike da shakku da rashin fahimta wani abu kuma ya tukare masa a wuya, kasancewar rauninsa baya bayyana ya sa za kaga serious face a tattare da shi.

"Who is Safiyyerh? Mene ya faru da ita? Kenan an yi using nawa ne wajan aura mata ni? Exactly?" Ya yi furucin da yake nuna how sad he is, idanunsa ya shige ciki Dr Hash ya girgiza kai ya ce "MAJ ni fa kamar masinja ne a wannan motar, ka nemi driver sai ya yi maka bayani amma komai yana da dalili da kuma hujja, karka manta soyayyar dake tsakanin zuƙata biyu ma'ana iyaye da yaransu, zamani ya sauya MAJ kowa mafitsara yake nema a rayuwa idan zaka iya ka tsaya Safiyyerh domin ba lallai ka sake ganinta a cikin rayuwarka ba, idan ba zaka iya ba ka barwa zakaru fagen ka ɗauki hakan matsayin wata fitila dana baka" a hankali Dr Hash ya girgiza kai yana yin baya tare da ɗaga hannunsa sama sai kuma ya yi murmushi sosai ya ce "Naaa, bana nufin za a kashe maka Safiyyerh ka saka idanu a kanta kawai" yana cewa haka ya juya ya bar wajan.

MAJ Aliyu ya jima tsaye a wajan, ya jima abu bai bashi mamaki ba bai kuma tsaya masa a rai ba. Mota ya shiga bayan ya saka kayansa cikin sauri ya fita daga motar daidai sanda daddy yake fitowa daga cikin gidan shima hannunsa riƙe da maƙulin nasa motar. Tuƙi yake amma ya rarraba tunaninsa har ya isa ɗan ƙaramin gidan ya fita da sauri yana rufe motar, ya jujjuya yaga babu kowa sai ya shiga ya rufe gidan kamar kullum a zaune ya samu matashin saurayin wannan karan ya kifa kansa saman table ɗin gabansa, hannunsa ɗaya ya ɗora a saman keyboard na computer da yake operating nata a hankali Aliyu ya ƙarasa ya zauna ya ɗan juya ya kalle shi a nutse ya ce "Muhammad" da ƙyar ya buɗe idanunsa da suke a lumshe looking so sexcy, kana kallonsa za kaga nutsuwar dake tattare da shi a handsome and gentle man Indeed kallo ɗaya ya yi wa Aliyu ya zame idanunsa yana daidaita zaman nasa, Aliyu ya dubi baƙar fuskar Muhammad sake ɗan sheƙi da manyan idanunsa nutsuwarsa har tsoro take basa.

"Muhammad, cikin ne?" Ya girgiza masa kai ya dubi MAJ Aliyu a hankali kuma ya ce "Are you stay with me?" Kai tsaye ya ce masa "No,zan tafi ne"

"Shiiiit got it wrong"

Muhammad ya furta yana dunƙule hannunsa tare ja baya ya cigaba da danna computer can ya nisa ya ce "Last time da kazo da wata mace" Aliyu ya tsaya da abin da yake alamar yana jin Muhammad "Na ji muryarta, na taɓa ganinta"

"Safiyyerh ka gani? Yaushe ma ka zama free har ka fita cikin jama'a, fita kake bana nan ashe?" Sosai Muhammad ya yi mamaki kamar ba zai magana ba sai ya ce

"Fita? Why should i? Laaa, na ganta da ciki i saw her with a pregnant" Aliyu ya miƙe tsaye jikinsa duka rawa yake da ɓari idanunsa ya yi jajur ya taune harshe

"Safiyyerh with pregnant? Ina ka ganta yaushe kuma?"

"Shekaru biyu da watanni, ba zan manta muryarta ba, na juya na ganta naga kun tafi" Ya faɗa cikin ƙasa da murya mara hayaniya har zai magana sai kuma ya yi shiru. "Are you drunk? Muhammad ka sha wani abu ne yau, ka cigaba da shaye-shaye ne? Wannan maganar ba ta yi kama data wanda suke cikin hayyacinsu ba, ba Safiyyerh ka gani ba, Safiyyerh ba zata taɓa samun ciki ba idan ma zata samu to dani ne ƙwayayen haihuwarta na Aliyu ne" Muhammad dai bai ce komai ba ya miƙe yana zagayawa ya ɗauki wani remote da pencil ya fara showing wani abu zuwa ga Aliyu, MAJ kuma tunda ya ga Muhammad ya miƙe tsaye ya san ya bar maganar kenan ba zai ƙara cewa komai akai ba. Aliyu baya fahimtar komai ya miƙe ya zaga wajan Muhammad ya ce "Za mu yi magana, stay safe ok?"

"Akwai wani mai kama dani ne? Kake tsoron na fita, ba zan taɓa fita ba kar ka damu" Aliyu ya kalle shi sai kuma kawai ya juya ya fita. Muhammad ya bi bayan Aliyu da kallo a hankali ya lumshe idanunsa can ƙasa zuciyarsa ya furta "SOPHIE"

***"Aliyu idan wannan ne damuwarka ka ɗauka ta zo ƙarshe, zan bibiyi case ɗin da ƙasa na maka al'ƙawarin matarka zata kuɓuta muddin ba hannun Scorpion ta faɗa ba" Maj Aliyu ya kalli MG da sauri jin sunan Scorpion daya ambata a hankali ya miƙe tsaye ya ce "Zan je, ba zan dawo sai na yi nasara" MG ya miƙe da sauri Aliyu ya yi salute nasa cike da girmamawa yana fita kuma ya nufi mota zuwa ya nufi airport zuwan nasa airport ya yi daidai da cikar lokaci ya shiga ya zauna a kujera ya daɗe a haka kafin ya buɗe idanu jin ana jan hannunsa ya juya idanunsa ya sauka akan wani kyakkyawan yaro fari tas da ƙyar yake buɗe ido don fari, yaron asalin kyakkyawa ne ga shiga rai, a tsora ce Maj ya dinga kallon baby boy ɗin, daya lumshe idanunsa ya buɗe, kamannin Fiyya yake hangowa a fuskar yaron, har yanayin ƙiriniyarta domin yaron ya kasa zama sai ƙoƙarin hawa cinyar Maj yake, shi kam ya kasa motsi don mamaki ya dinga kallon yaron da wani irin yanayi na shakku da tantama. "Sorry ya damake Amsh baya ji, ka yi haƙuri" Wata mata ta furta tana ɗauke Amsh daga jikin Maj, har yanzu idanun Aliyu na kan yaron da ƙyar ya ja numfashi ya sauke a haka jirgin ya ɗaga zuwa sararin samaniya zuciyar Maj Aliyu na Kano tare da tunanin halin da Fiyya ke ciki gangar jikinsa kawai yake tare da shi a cikin jirgin.

****Da yammacin ranar lahadi Moh na zaune gaban Abbasa ya tanƙwashe ƙafarsa idanunsa kafe a kanta a hankali ta furta "Kamar zan iya amince mata" Abbasa ta ɗago kai ta kalle shi ta yi murmushi ta ce "Ka santa ne?" Ya girgiza mata kai alamar bai santa ba "Yaushe ka fara yadda da mata?"

"Sanda na fara yadda dake" ya bata amsa ta sake jinjina masa kai ta ce "Mace za ta yi tasiri a zuciyarka kenan? Ka fasa cimma muradin naka? Ka ajjiye dukkan wata manufarka da ɗaukar fansar matarka? Idan gabaɗaya ka haƙura da wannan dole ne ka mallaki kamfanin FS WORLD INVESTMENT. Mutallab ƙaddararka na tattare da wannan kamfanin, har yanzu ne za a dinga amfani daku matasa yan siyasa na cimma burukan su a kan ku? Rayuwarku nada amfani, ina buƙatarka ina buƙatar ganin ka cimma burinka"

"Ke ɗin wacece da lokacin ɗaya kika kutso kai cikin rayuwarta? Me kike nufi dani? Iyayen da suka haife ni yanzu nine a idanunsu wanda suka tsana, jama'ar unguwa sun tsane ni, duk inda na zaga guduna ake yi, maimakon a yi mini addu'a sai a fara tsinewa mini, ɗa na kowa ne, ni ban zaɓi zama ɗan daba ko mashayi ba, sune suka zaban a tarihin rayuwa kowa yana da ɓangare mai kyau, da mara kyau ni wannan ɓangaren nawa aka sani MUTALLAB TAHHB ɗan daba ne ɗan shaye-shaye ɗan ta'adda ba kuma zan daina ba, sai idan ƙaddara ce ta yi galaba akai ne, tunda ana tsangwarmu za a gani" a maganganunsa zaka fuskanci ƙuncin da zuciyarsa take ciki bai taɓa yi mata magana mai tsayin hakan ba a nutse ta ce "To wanne ɓangare ne naka mai kyau? Tunda mara kyau aka sani? Ko sau ɗaya ka bani labarinka ka bani tarihin rayuwarka, wacce ƙaddara ce ta rusa rayuwarka daga dama zuwa hagu? Waye MUTALLAB?"

"Uhm" ya ce ya miƙe tsaye domin a hankalina yake bai sha komai ba ta dinga kallonsa a tsaya cikakken namiji matashi mai jini a jika. "An kashe mata uku wanda suka shigo rayuwarka,kar ka bari a kashe ta huɗu, kar ka amshi Safiyyerh kar ka bari zuciyarka ta rinjaye ka har ka bata matsayi, na yi bincike kuma ya tabbatar kai ka kashe matarka da hannunka ba zaka taɓa musa mini ba, ka kashe matarka ka nunawa jama'a kamar anci zalinka"

"E, da gaske nina kashe ta shine hukuncin ta, ta cancanci ta mutu"

"Na sani bana saɓa lissafi Mutallab, hujjarka na kashe ta da laifin data aikata maka ne ban sani ba. Abu ɗaya zan faɗa maka karka yadda ka amshi Safiyyerh domin ita ɗin matar aure ce, zai fi kyau ka yi amfani da damar da kake da ita a hannu wajan sanin sirrin FS WORLD INVESTMENT COMPANY, Ka rabu da Safiyyerh matar aure

ce". "Na ji zan rayu domin ta" da sauri Abbasa ta ce "Kana cikin hankalinka? Matar auren zaka rayu da ita? Matar aure fa"

"Ba zata taɓa zama matar aure ba, idan ya kasance haka zan kashe auren nata,ko na kashe mijin, ita ɗin Matar Moh ce" yana faɗin haka ya fice daga bukkar kamar walƙiya. Bai san mene ya faru ba a hanya yana tafe ana nuna shi duk da rufe fuskarsa da ya yi, hakan ya saka ya zaro wuƙa yana tafe yana buɗawa tare da zazzaro idanunsa ya dinga bin lungu har ya bar cikin duhuwar ciyayin.

Safiyyerh na zaune ta ji ya shigo babu ko sallama ta miƙe da sauri haka kawai take jin tsoron shi ya ƙarasa ya zauna saman kujera yana huci ta tattara nutsuwarta ta ce "yin sallama wajibi ne Jarumi, kai fa babban suna gare ka ba'a san irin ku da haka ba, idan ka yi sallama ka nemawa mutum aminci ne, idan ya amsa ya nemaka aminci ne, yin sallama wajibi ce haka amsa ta kuma ko ka yi sai an baka damar shigowa" bai kulata ba ya zaro sigari ya bata hayaƙi kwana biyu dai bai yi faɗa ba. Safiyyerh ta shagwaɓe fuska ta ce "Kuma daka shigo ina saka kaya fa? Sai ka ganni haka?"

Sai a lokacin ya juya ya kalle ta, to tunaninta mene? Ina ruwansa da ita da kuma jikinta? Mahaukaciyar yarinya kawai "Sai na ji kamar ina rayuwa tare da mijina ne, idan na ji numfashinka a gidan nan har nutsuwa nake samu, ka sato ni ina nufin ka yi kidnapped ɗina maimakon na damu amma a kullum buƙatar kasancewa da kai nake a duk halin da kake ni ban damu ba, ba ruwana da kai ɗan daba ne na ji zan yi fighting akan soyayyarka, i will fight for your love, i will fight idan zan zama wacce zata sama maka farinki, i don't care with your habits, i don't care with my family ka yarda dani ko sau ɗaya ne, ka bani dama irin damar da kowanne namiji yake bawa mace a rayuwa, ina son wannan damar ko sau ɗaya ne zan yi amfani da ita wajan dasa maka soyayyata a ƙirjinka, zan kai ka zuwa wajan Professor"

"You can't" ta ji ya ce can ƙasan maƙoshinsa yana rufe idanu dif dif dif haka zuciyarsa ke harbawa baya son ko jin muryarta ta kuma kasa ganewa, ya juya mata baya a hankali ya ji sautin shasshekar kukanta na sauka cikin kunnensa bai kulata ba ta ce "Ka tausaya mini wallahi ina son ka" ta furta fat fat fat haka ta ji tsokar tsakiyar ƙirjinta na motsawa tare da buguwa, ta ji kalmar son a tsakiyar kanta ya sauka a ƙirjin da sauri cikin ranta bayan zuciyarta ta tuna mata da cewa “Safiyyerh what are you doing? Kina matar aure kina son wani?” ta girgiza kai ta ce "Astagafirulla"

Moh ya miƙe tsaye zaune yana kallon ta a mamakance sai kuma ya taune harshe da laɓɓansa ya jima a haka kafin ya ce "Kina so na? Ni ko?" Ya yi poiting hannunsa zuwa ƙirji yana nuna kan shi.

"E, haka ne"

"Mijinki wanda kike aure fa?" Ya cilla mata tambayar yana tsare ta da manyan idanunsa sai cin magani yake kamar kuma an tilasta masa yin tambayar yadda yake magana da ƙyar. Tunani ta fara da zuciyarta

“Safiyyerh think, idan na ce masa ni matar aure ce ina da aure ba zai saki jiki dani ya bani soyayyar da nake buƙata har naji waye shi ba, my husband is no longer with me, wannan da yake gabana ya yi kidnapped nawa is the one who i pray for, zan faɗa masa ina son shi, i will tell him ina son shi, da na ji waye shi zan bar shi na koma wajan my poor husband Aliyu, the one who i love" gama tunaninta kenan ya saka Safiyyerh girgiza kai ta ce "Na yi kama da matar aure ne? Bani da aure ko saurayi bani da shi.." tana faɗin haka ta yi Astagafirulla a ranta. Shiru ya yi mata ita a dole ya amince ta, ta marairace fuska sosai tace...

"Na rantse da Allah, na rantse da Allah, na rantse da Allah bani da aure ni Safiyyerh bani da miji"

Cak taga ya miƙe ya bar wajan ya shige ɗaki bata ƙara ganinsa har dare ya nutsa su Goje suka shigo. Ta kalli Goje ta ce "Aboki ba zaka bani labarin jarumi ba?" Ya ƙura mata na mujiya sai kuma ya ce "Maganar kisan matarsa ya tashi, iyayen yarinyar sun ƙara ɗaukaka ƙara da nufin basu yarda ba anci zarafinsu ba a ɗauki ran yarinyarsu a banza ba, maganar da ake yanzu sun kama Malam shi mahaifin Mai dawa, wai ya san inda yake ba za su sake shi ba sai ya zo hannu"

"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, to shi kuma me ya yi musu wai? Ba mai laifi ake kamawa ba?"

"Yʼa yʻan daƙiƙai ne, namansu ha halatta aci tsaf aka bani zanci mutanen nan jahilai ne" Moh suka ga ya fito da sauri Goje ya miƙe tsaye ya ce "Ina zaka?" A hankali ya ce "Zan miƙa kai na, a saki mahaifina" Goje ya ce "Ba za a yi haka ba, ita shari'a saɓanin hankali ce mu bi komai a sannu" da rinannu idanunsa ya dinga kallon Goje

ya kasa cewa komai sai huci yake fitarwa yana juya idanun nasa ƙirjin nan da harabawa nan da nan ya fara birkicewa "Ka yi magana da wanda ya saka aka kama Manager, ta fara barin wajanmu sai mun yadda za a yi, akwai Jagwal zamanta wajan namu"

Juyawa ya ya shige ɗakin daya fito, ya ɗauki wata ƙwaya ya tura a bakinsa ya danne a ƙasan harshe ta fara narkewa. Suna jiyo yadda yake buge buge hakan ya saka Safiyyerh ƙarasawa bakin ƙofar ta ce "Ashe da gaske baka da imani? Kai ba cikakken mumini bane? Maimakon ka kira sunan Ubangiji ka yi masa kirari sai ka fara shan abun maye? Ba'a maganin damuwa da damuwa, idan tunani ya gushe hankali ke nemo shi, haba Jarumina, kira sunan mahaliccinka ko sauya ne repeat after me, Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, ka yi ta maimaita hakan a ranka" shiru ta ji hakan ya saka ta zame a hankali ta jingina da jikin ƙofar hawaye na sauka daga cikin idanunta zuwa fuska wani tausayinsa take ji sosai tun bata san waye shi ba, haka kawai ta ji bata fargabar zama kusa da shi “Ya Allah" sai kuma ta kalli ƙofar ta shafa ta ce "You are not alone, you have Fiyya kana da Maama"

***Eng Ali wali ne ke kaiwa da komowa a office ɗinsa ya ja tsaki ya ce "Zai jiƙa mini aiki yaron nan, ina son ya kawo mini yɗar gidan Professor Abdu ko bai yi mata fyaɗen ba na saka wani, ni fa akan biyan buƙatata bana tsoro bata shayi kuma a wannan karon sai na hauka kujerar ɗan Majilisa, na tabbatar na sauke Hon Maɗatai akan kujerar da yake iko da ita, har matsayinsa a cikin zauren Majalissa na chief whip sai ya dawo hannuna"

"Distinguish, ina ganin ba matsalar yarinyar nan ce a gabanmu ba, baka da labarin Dr Abraham Denial David sun haɗa hannu da Hon Maɗatai?" A gigice Ali wali ya ce "Ban gane haɗa hannu ba, ina cewa basa ga maciji da juna"

"Uhm, shi maƙiyi ko yaya yake ba'a raina shi a siyasa, Dr Abraham dumped all progressive congras NNY for the New people life NPL da shi da mutanensa kaf" sosai tashin hankali ya bayyana a fuskar Ali wali ya share zufa ya ce "Kuma ba plan bane ko shirin yin Anti party?" Secretary ya ce "Bana jin haka, ka san shi Abraham tsayayyen mutum ne mai magana ɗaya siyasar ma ba damunsa ta yi ba, sun haɗa hannu ne domin su kai ka ƙasa" "Hakan na nufin jawo Professor Abdu Marafa jikina ne ta ƙarfin dole, kuma burina ba zai cika ba sai da wannan yarinyar gashi ɗan iskan yaron nan ina kiransa yana neman lalata mini aiki"

"Akwai matsala dai gaskiya" Ali wali ya ce "Kar ka damu tun a primary elections sun ga irin ƙarfin da nake da shi, jeka kawai secretary" miƙewa Secretary ya yi ya ce "Distinguish, ka san siyasa kuwa? Siyasa hanya ce ta ɗarewa ko samun hawa madafun iko domin mulkar jama'a a takaice za'a iya cewa ana yin siyasa domin bayyana manufofi tsakanin masu neman kujerar mulki kuma ana yin siyasa ne tsakanin ɓangarori guda biyu ko sama da haka ba'a kowanne nau,in mulki ake gudanar da siyasa ba sai mulkin dimokoraɗiya mulkin farar hula da jama'a suke zaɓar shugaba bisa kundin tsarin mulkin ƙasa. Ana siyasa domin hamayya da juna tsakanin jam'iyyu, dole ka sauya taku kasan su waye a tare da kai shawara ce" yana kaiwa nan ya fita karo suka ci da Professor Abdu ya dinga kallonsa irin kallon sanin nan na wani abu daban.

Ali wali ya dinga kallon Prof, Daddy ya yi murmushi ya ce "Eng Ali wali ɗan takarar Majalissar jiha ne ko na tarayya? Ga kifi daga sama gasasshe" Daddy ya ce yana zama kan kujera ya dinga juya kujerar a hankali ya nisa ya ce "Ka yi mamaki ko, ganin likita na je ba wanda ya sani na biyo ta nan wajanka, naga kamar baka yarda da abin da na ce ba ko? Da gaske ko sassara gangar jikin Safiyyerh za ka yi bai damu Professor Abdu Marafa ba, matsalar dake ta damuna ka yi mini magani babban albashir na yi magana da mai kamfanin FS WORLD INVESTMENT COMPANY an bawa Hon Maɗatai damar saka hannun jari,na buƙaci kuma a bani duka hannun jarin da Safiyyerh ta saka da kason ta dake cikin kamfanin, zan tattara dukkan ducoments da dukiyarta na yi signature su zama halaliyyata, zan kuma rufe bakin matata da yarana da Zahiyerh akan labarin. To Safiyyerh ba ciwon kai na ba ce ba kuma raunina ba ce, sam ƙwaƙwalwarka bata aiki ka tura Safiyyerh ne idan ya dace ka haɗata da abin da ya dace,kuma su biyun zasu same maka ciwon idanu, nama yi mamakin yadda aka baka damar hawa takara baka da tunani sam Eng Ali wali" ya miƙe ya fice daga officer ɗin. A hanya ya yi wa J waya yana nishi da ƙyar cewa ya kasa driving mutuwa zai yi idan ba a nemo masa Maama ba.

****Bacci Safiyyerh take ba tare da sanin tana mafarki ba sai fisge fisge take tana zabura "Kar ka mini haka daddy me ya yi maka? kar ka cutar da shi kar ka cutar da shi, shi ɗin wanda zan aura ne bai san komai ba, iyayensa ma basu sani ba, zan bar shi idan ka so bari na har abada, wallahi ni na kai masa kai ne soyayyar da nake masa ce, ina son shi i love Tahhb daddy ina son Tahhb..." Da sauri ta buɗe idanu a gigice tana maimaita "Ina son Tahhb daddy" jikinta duka rawa yake yana tsugune gabanta ganin ta kasa nutsuwa kamar mai shirin taɓa wuta ya damƙi kafaɗunta ya girgiza da ƙarfi ya ce "Parrot, your Tahhb is here your husband is here" hannunsa ta damƙa tana rusa kuka "Kar ka bar ni, kar ka sake barina daddy zai raba mu ina son ka Tahhb....

You can now read page 16 to 20 on ArewaBooks search the book

Na'ima Sulaiman Sarauta

Nimcyluv

[1/7, 9:33 PM] Sis Fauzy: Chapter 18: Selfishness

Mutallab a paid book chat this number via WhatsApp to subscribe urs 08164069685... For more updates follow on Arewabooks.

Ya zuba mata idanu yana jin tana sake cewa "Daddy wallahi idan kukai masa wani abu zan gudu daga gidan nan, zan bar gidan nan Daddy me ya sa kuka kasa fahimtar cewa zuciyar Safiyyerh zaku tarwatsa? Daddy da hannunka zaka kashe yaɗarka me na yi da na cancanci ka kashe ni? Saboda na ce ina son shi, ina son ruwa da dacewa Daddy? So bai san nasaba, cancanta, arziƙi, ko launin fata ba, balle ya yi zuciya hisabi da abin da ya dace, i love him the way he is, idan zaka raba ni da shi,ka fara kashe ni kamar yadda ka yi niyya, ba wani abu bane don uba ya kashe yaɗar cikinsa yaɗar daya haifa akan buƙatarsa" Safiyyerh ta cigaba da ihu da fisge-fisge idanunta rufe gani take data buɗe idanunta zata daina mafarkin, zata fita daga yanayin da take ciki wanda bata fatan ya gushe daga cikin idanunta.

A hankali kamar mai tsoron taɓa jikinta ya saka hannu ya matse ƙafafunta yana jinjigata ya kasa yi mata magana "Open your eyes Tiger, buɗe idanun" ta girgiza masa kai idanunta sharkaf da hawaye ta riƙe hannunsa "Ba zan buɗe ba, ina buɗewa zan ga babu kai a gabana Tahhb, kana kallon su daddy zasu raba ni da kai, za su rabani da mijina me ya sa Daddy baya son ka, don Allah kar ka tafi daga wajena kar ka sake guduwa ka bar ni"

"Ina nan, ni dai mijinki i am here just because of you Safiyyerh, buɗe idanu kiga mijinki Mutallab, ke matar Moh ce Tiger, ko ƙaddara ba zata sauya hakan ba"

"Da gaske ba zaka sake guduwa ba? You'll love me back? Na dinga jiranka a ranar baka zo ba, ni ko Jarumi,ni Safiyyerh ka bari?" Moh ya kasa magana idanunsa ya yi wani irin jaa ruwa ya taru a cikinsu, da ace yana yin kuka tabbas da a yanzu duk wanda ya kalli ƙwayar idanun Moh zai san hawaye yake, sai dai shi baya jin yana da wani abu daya rage masa a rayuwa balle ya saka shi kuka, ya yi ƙasa da kansa har yanzu yana riƙe da kafaɗunta. Riƙe shi ta yi cikin shasshеƙar kuka while she's smiling at the same time ta taɓa cikinta "Har yanzu wajan da aka cakan wuƙa yana nan, numfashina bai ƙare a duniya ba shi ya sa ban mutu ba, ashe rabon ganin mijina ne"

Rinannun idanunsa ya buɗe yana kallon fuskarta, har yanzu idanun nata a rufe suke still ya kasa furta komai, sai kallon ta yake zuciyarsa na wani irin zafi da tafarfasa. A hankali Safiyyerh ta miƙa hannunta ta shafi fuskarsa sai ta yi murmushi tana girgiza kai ta ce "Ka barni da soyayya, ka sanni da alkunya ka barni cikin jinya ka tafi, haba jarumi" Ya sake yi mata shiru a hankali kamar mai tsoron ganin abu, slowly slowly ta fara buɗe idanunta daya gama kumbura ganinta ya sauka a saman ɓakar fuskarsa ta zuba masa idanu ta ƙura cikin idanunsa ido, shima ɗin ita yake kallo da sauri kuma ta yi baya daidai lokacin da wani shocking ya gilma ta cikin kanta ta yi saurin saka hannu ta riƙe kan, tana runtse idanunta jikinta duka rawa yake ga wani irin azaba da tsakiyar kanta ke mata, ta dinga kallon Moh kamar mai shirin tuna wani abu, wani irin zillo zuciyarta ke yi mata tana buɗewa ƙirjinta na bugawa tsit, tsit,tsit haka ta ji jijiyoyin cikin ƙwaƙwalwarta zuba harbawa harbin da take jinsa daidai da bugun ƙirjinta.

"Me kake yi a nan?"

Safiyyerh ta ce tana kallon Moh dake durƙushe ya zuba mata idanu ta ɗan dafe kai tana kwaɓe fuska "Bacci na yi, i had a bad dream, na kasa tuna komai ko ka ji me na ce?"

"I got it wrong, baka ji komai ba ai shikenan" ta sulale a wajan ta zauna ta haɗe kai da qwwia can ta ɗago ta kalle shi ta ce

"Ina jin kamar ina da matsala da brain ɗina, anya ba haukacewa zan yi ba? Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, i wish a gida nake dama a gida nake Dr ya yi mini allurar da yake mini"

Miƙewa ya yi da baya da baya ya fara tafiya cikin sauri kuma ya juya zuwa ɗakin da yake ciki, wanda daman daga nan ya fito sanda ya ji tana surutan yana shiga ya rufe ƙofar. Safiyyerh ta jima a wajan da ƙyar ta miƙe tsaye saboda kukan da ta yi da ciwon da kanta ke yi mata, sai ta zama so silence bata da wani kuzari duk iya ƙoƙarin da ta yi wajan ganin ta tuna mafarkin ta kasa, sosai kan ya yi mata nauyi deep down na zuciyarta tana jin kamar akwai abun dake going a tunaninta wanda ba nata ba. Har zata shige sai kuma ta leƙa ta tagar ɗakin ta hango shi ya yi rufda ciki ga tarin kwalayen sigarin daya shanye ga wata ƙwaya da ya yi wurgi da ita sosai ta ji babu daɗi sai ta juya ta shige cikin nata ɗakin.

***Ammo ta ɗaga kan ta bayan ta amsa sallama da gaisuwar da Sa'adah ke yi mata tana jin Sa'adah ta ce "Yanzu ina aka kai Malam Ammo, daman case ɗin Mutallab ba'a gama shi ba?"

"Sa'adah kenan, bakwa son gaskiya cikin lamuranku kin taɓa ganin ƙarya ta kore gaskiya kin san zunubin da ɗan'uwanku ya yi? Sa'adah kun san zafi da raɗaɗin da zuciyata ke yi mini kisan kai fa, ina tsananin takaici daya kasance ni ce wacce na yi cikin Mutallab, na raini cikin na yi naƙidarsa na haifar, na shayar da shi ruwan nonona Sa'adah anya ba sauya mini yaro a ka yi, anya shine Mutallab ɗin da na ji zafin naƙudarsa...,"

"Subuhanallahi, me kike cewa haka Ammo kar ki ƙarasa lalata shi da munanan kalamanki, Ammo ko sau ɗaya ba ki taɓa bawa Mutallab dama kin ji ta bakinsa ba kar ki yi masa mummunan alkaba'i wallahi har gobe shi jininki ne ba zaki hana jama'a furta Mutallab ɗan Ammo bane, da kin ja shi a jiki a lokacin da abubuwan suka lalace, da kin nuna masa kuskuren abubuwan da yake, da kin yi masa addu'a, da ba ki nuna masa tsangwama ba. Amma kin juya masa baya sanda yara suke lalacewa mu iyaye sai muce a lokacin za mu tsane su don Allah ki yi wa Mutallab addu'a idan yana da rabo zai shiryu" murmushin takaici Ammo ta yi tana girgiza kai

"Sa'adah kenan, bayan abubuwan baya ki duba a sanadinsa Hameeda ta rasa ranta yaranta sun zama marayu, a sanadinsa yanzu mahaifinsa yana wajan hukuma wacce baƙar kadara na haifa a cikina? Ciki mai haife haife sai ya bani yaron da yafi ƙarfina ya fi ƙarfin ubansa ya fi ƙarfin al'umma ya fi ƙarfin jami'an tsaro ina jin kamar na yi masa Allah Ya isa....," a gigice Sa'adah ta rufe bakin Ammo tana rushewa da kuka ta ce "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un. Hasbunallahu wani'imal wakil"

Ta kasa magana sai ta sunkuyar da kanta tana rushewa da wani irin kuka mai ban tausayi da cin zuciya, Ammo ajjiyar zuciya kawai take saukewa dole akwai zunubinta na faruwar komai. Da ƙyar Sa'adah ta miƙe ta saka hijabi ta fita Inna Binta na wanke rama zata kwaɗantawa Mufee ta ce "Iska na wahalar da mai kayan kara, ai tunda kuka haifi ɗan daba abubuwan da za su dinga faruwa kenan ni dai banci nanin ba, nanin ba zata taɓa cina ba na ji da yunwar cikina ma data Mufee, ita kanta Zaituna data fita bulayi mamaki take bani yasin"

Sa'adah bata kula Inna Binta ba ta yi waje hankali tashe duk inda take tunanin za'a kai Malam ta je police stations har babu adadi Inna Binta ta kalli yaran dake tsakar gidan bakunansu a bushe duk yunwa suke ji ta fashe da dariya har tana tuntsirawa ta ce "Wallahi ubanku ya janyo muku"

Sa'adah ta kalli Ɗanyaro ta ce "Kai kuma saboda Malam baya nan wayar ka karɓo haka?"

"Tawa ce ai" ta buɗe ido "taka kuma? Ka san kuɗin wayar nan kuwa?" Ya yi mata murmushi yana jujjuya wayar ya ce "Na sani, ai bani kaɗai nake da ita a wannan makarantar ba, Iro yana da ita haka Muhajeed haka ma Salmanu"

"Sana'ar me kuke yi? Ko dako kuka fara Ɗanyaro"

"A'a kifi daga sama ne ya sauka, idan rabonka ya rantse dole sai ka samu muma haka ne" ta dinga kallon fuskar Ɗanyaro da mamaki

"Wanne kifin ka samu daga samu kenan Ɗanyaro?"

"Sirri ne" yana faɗin haka ya miƙe ya bar wajan ta bishi da idanu.

***MAJ Aliyu ya dinga kallon commander cike da mamaki kafin ya ce "Sir ban fahimce ka ba, pardon please?". Commander ya yi murmushi ya ce "MAJ Aliyu kenan, na sanka farin sani sarai ka fahimta na san kuma ka gane na ce ka ciro mini Id card ɗinka, Ka cire uniform ɗinka kuma ka bani bindigarka ai ka ji yanzu tunda Hausa na yi"

"Yes sir, ma'anar cire uniform ɗina ne ban fahimta ba, bafa Captain nake ba, A.A MARAFA mai matsayin MAJOR MAJ nake kaki mai tambarin tsuntsu, a gaban yarana kake maganar na cire Uniform nawa kuma na baka bindiga laifin mai na yi?" Aliyu ya furta yana zazzaro idanu waje zuciyarsa ta motsa, daga zuwan shi cikin Barrack ɗin zata tare shi da maganar iska wacce ba zai taɓa lamunta aci zarafin shi ba, ba zai taɓa yarda a wulaƙanta shi a gaban yaransa ba. Yadda zuciyarsa ke rawa haka sauran gaɓɓan jikinsa.

Brigadier General ya sake yin murmushi ya ce "Kuma sai mene da rank ɗin Maj? C'mo my friend remove the uniform, ka ajjiye bindigar wajanka ok"

"I am sorry sir BG i can't" Aliyu ya ce yana ƙoƙarin kiran number waya da sauri ya ji an fisge wayarsa kafin Aliyu ya juyo Brigadier General ya wanke Aliyu da mari ya sake zabga masa wani marin, idanun Aliyu kamar su faɗo ƙasa saboda ja yaƙi motsawa shi mamaki yake yi wanne laifi ya aikata har haka? Ance an yi posting nasa zuwa wani dajin duk da matsayinsa ya shige haka, daga nan kuma zai yi exam amma daga zuwa sai reshe ya juye da mujiya?

"I said drop the gun Maj Aliyu"

"I can't, a faɗa mini laifina idan na yi na amsa idan ban yi ba na faɗa, haka ake daman daga zuwa a fara tarata da wasu abubuwa da ban sani ba" hannu Brigadier General ta tafa sojoji su kaiwa Aliyu ƙawanya "Ku ƙwace mini bindigar hannunsa a cire mini rigar jikinsa" Aliyu ya ja ya ƙame yana jiran yaga waye zai zo idan yake su kansu sojojin tsoron zuwa wajan Maj Aliyu suke domin sun jima da sanin waye shi, kokawa aka fara dashi suka kasa ƙwatar bindigar ta baya aka zo tare da shammatar shi aka danna masa wata Jijiya a wuyansa ya juya da ƙyar idanunsa ya buɗe bai gama ganin kowaye ba, dishi dishi a hankali ya ce "Daddy" sai kuma ya sulale a wajan a haka suka ja shi a ƙasa a cikin Barrack ɗin suka nufi wani gadirom da shi.

***I. Qasim ya gama gwada Daddy kafin ya ce "Daddy kana hutawa, jikinsa baya motsi jininka ya hau gashi ya nuna ka yi tafiya mai ɗan nisa yau ɗin nan, muna buƙatar lafiyarka". Girgiza kai Daddy ya yi da ƙyar yake iya magana ya ce "Qasim ta ya zan samu nutsuwa a zuciyata? Ka tuna Safiyyerh bata tare dani, ka dubi lokacin daya shuɗe ba Maama a gidan nan, sannan ka ce na samu nutsuwa?" I. Qasim ya

ce "Haka ne, amma idan Safiyyerh ta dawo ta sameka a haka ba zata ji daɗi ba ka san yadda take son ka ai, Please be patient mu cigaba da addu'a duk inda take Ubangiji ya kuɓutar da ita ya kuma kare ta"

"In sha Allah, na saka ana ta addu'a ana sauke alƙawari da sadaƙa"

Ummimi ta shigo tana daddana waya Daddy ya kalleta ya kasa magana ta ɗan dube shi ta ce "Ina ta kiran Gadanga wayar a kashe, Aliyu baya kashe waya" Daddy ya yi jim sai kuma ya ce

"Junaid ɗakko mini wayata muga" miƙewa Junaid ya yi ya ɗakko wayar Daddy ya amsa ya shiga kiran number Aliyu amma a kashe, Junaid ya kira, haka Ummi Qasim ma haka hankalinsu duk a tashe. Sai kawai Ummimi ta fashe da kuka ta ce "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un Aliyu me ya samu Aliyu kuma, miji da mata lokaci guda" Daddy ya ce "Ki daina kuka kin san yanayin aikin nasu, bari na kira MG mu ji" cikin sauri Daddy ya fara kiran Major General yana ɗagawa Daddy ya yi gyaran murya ya ce "Ka yi haƙuri na kiran ka kwatsam, mun kira wayar Aliyu mun ji shiru"

MG ya yi shiru Daddy ya ce "Ina tare da iyayen yaran a free kake"

"Matsalar network ne, babu mamaki sun ƙarasa cikin jejin ne amma mun yi waya da commander dake jan ragamar tawagar lafiya lou suke, idan ya samu sukuni zai kira"

"Thank you, na gode sosai "

"Babu damuwa amma kamar bai kamata ku damu ba, Aliyu soja ne kuna iya yin fiye da shekara ba ku ji daga gare shi ba" sallama suka yi gabaɗaya. Ummimi ta sauke ajjiyar zuciya sai yanzu ta samu nutsuwa haka Ummi. Daddy ya kira wayar Sp Ghali yana ɗagawa ya ce "Ya ake ciki ne?"

"Muna nan muna ta ƙoƙari bincike na tafiya, amma na rasa ta ina muke samun matsala ana ta yi mana kutse cikin na'ura da mun samu mun fara tracking location

sai a lalata mana komai, kuma duk wanda yake yin hakan ba ƙaramin gwani bane mun kasa ta ina yake" miƙewa Daddy ya yi a hankali ya nufi Upstarts yana cewa "Ya akai to Aliyu ai yanzu ba zai zame muku matsala ba" magana ya cigaba da yi a hankali ba'a jin me yake cewa. Ummimi ta lumshe idanunta ta furta "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un"

Eng Ali wali yana ta masifa idanunsa akan Csp ya ce "Lamarin yaron nan babu mutunci, ane mu mini shi duk inda yake da kuma yarinyar da take wajansa dole na kawo ƙarshen komai ba zan yi sagegeduwa ba a yi mini sakiyar da ba ruwa, takarar ɗan majalissar tarayya ba wasa ba ce wallahi, zan yi duk iya ƙokarina"

Jafar ya ce "Distinguish kana wasa da kujerar ne kamar, A matakin gwamnatin tarayya dama matsayin uku garemu Shugaban ƙasa, Sanata, Ɗan majalisar tarayya, kuma idan Scorpion yana raye a duniya dukkan ku ba zaku taɓa samun wannan kujerar ba, lokaci baya jira, ni a tunanina ku nemi sulhu da Scorpion ɗin nan ku ji matsalarsa daku, ku hanzarta yin hakan kafin jami'an FID su kama shi, ina tunanin Safiyyerh kuma ita Manager ɗin why not kawai a kashe ta"

"Jafar idan na ce ga abin da mu kaiwa Scorpion ɗin nan na yi ƙarya, ni ban ma san shi ba ban san me yake buƙata ba. Safiyyerh kuma ba za a kashe ta ba, ina da wani picture nata za a yi editing a fitar tsirara na san dawa za a haɗata a picture ɗin karka damu, ni yanzu matsalata biyu ce zuwa uku, waye Mutallab waye Scorpion sai batun Professor Abdu Marafa shi na gane kamar dukiyar yarinyar ya kewa"

"Idan haka ne ku zauna ku daidaita tsakaninku da Hon Maɗatai da Dr Abraham kuna cikin matsala, matsala kuma ba'a raina ta a siyasa"

Ali wali ya ce "Ok shikenan, zan tura maka photon yarinyar zan maka bayanin abin da nake buƙata, a ƙirƙiri fake account a handles na social media a yaɗa komai na fara gajiya ƙwan ya fashe warin ya damu kowa"

***Safiyyerh na dafa Indomie the only abin da ta iya kenan sai tsirarin abubuwa a hankali ya leƙo ta juyo ta kalle shi ta ce "Masoyi abin ba sallama?" Ya jingina da jikin bangon wajan ta kammala ta juye Indomie a faranti ta saka cokali, ta yi waje bayan ya bata hanya ya sake binta har inda take ta ce "Za ka ci ne? Kana ta biyo ni bafa guduwa zan yi ba, ina nan tare da kai har sanda ka yi niyyar mayar dani gida" hannu ya saka ya janye farantin ya ajjiye cokalin ya saka hannunsa ya kai lauma ta

ce "Say Bisimillah saboda zaranar da shaiɗan da kuma neman albarka a abincin" bai kalleta ba, ita dai kamar lauma uku ya yi wa Indomien ya cinye tas ta zare ido ta ce "kafa cinye? Ni kuma fa?"

"Ki cinye ni"

Ta yi murmushi sosai "kusan halinku ɗaya da Yaya Aliyu, Allah sarki Captain" ta yi maganar a hankali sai kuma ta ce "Yaushe zaka mayar dani gida, tunda ba zaka so ni ba?"

"Wacce allura ake miki?"

"Nima ban sani ba, kawai dai ana yi mini ita ko na tambaya ba'a faɗa mini ta mece"

"Kin sanni?" Fuska ba walwala ya yi tambayar ta girgiza kai ta ce "Ban san ka ba, ina dai fata wannan sanin ya zama sanadiyar faruwar abubuwa da yawa"

"Koda hakan zai saka ki sanni mijinki ne?" Wani rainin hankali da wayo ta ji sai ta yi dariya ta ce "Kana nufin ko hakan zai saka ka aure ni? E, na yarda" ya yi mata shiru a hankali kuma ya ce "Zan bar garin nan, kafin nan zan ba ki labarin da ba kowa ya sani ba daga nan ya rage naki wajan tuna baya ko akasin hakan yanzu ba sai anjima ba za ki ji kowaye Mutallab, kuma kema ya zama dole ki bani information akan Kamfanin nan naki ƙila na taimaka miki, kuma ki sani daga yanzu rayuwarki ta zama ba iya taki ba, wannan tsiwar taki ya saka na ji zan faɗa miki sirrina ban ce ki yi mini kuka ko tauysawa mini ba, bana buƙatar tambaya"

A hankali ta jinjina kai ta ce "Yadda ka ce haka zan yi my love" ya zamo ƙasa kusa da ita ya jima yana kallon ta ya fi ƙarfin minti ashirin a tausashe ya ce asalina ya fara da....

Read chapter 19 and 20 on ArewaBooks

[1/7, 9:34 PM] Sis Fauzy: Chapter 19: Where is my son

Shiru ya yi mata, Safiyyerh ta langwaɓar da kai ta ce "A haka za ka bani labarin kana ja mini rai da aji? Ba shiru ake ba da ka ce asalina sai ka ɗora kawai muje ba jira, ka saka duk na zaƙu wallahi, ni na jima ban ji abin da nake son ji irin labarinka ba Jarumi" ya zuba mata idanu baya ko ƙiftawa a karan farko ta ji tsigar jikinta ya fara tashi ƙirjinta ya motsa wani abu mai kama da feelings and emotions na kama zuciyar da kyau, ta ja baya daga kusa da shi ta yi shiru kanta a ƙasa.

"Ke ma za ki iya bada labarin nawa ga wani" ya ce yana furzar da iska daga cikin bakinsa har lokacin kuma ya kafe ta manyan idanunsa wanda yake lumshe su lokaci zuwa lokaci. "Ni na sanka ne balle na bawa wani labarinka?" Ta tura masa baki tana murguɗa masa shi kuma ya girgiza kai kawai ya yi mata shiru a hankali ya zaro wayar dake aljihunsa ya fara dannawa da sauri ya ɗago kai ya kalli Safiyyerh ta ganta ke ƙasa, ya sake kallon screen ɗin wayar hannunsa, ba'a tantancewa damuwarsa ko shiga tashin hankalinsa, ya saka hannu ya shafi fuskar wayar ya sake kallon Safiyyerh a hankali ya ce

"Kee.... You"

Ta juyo ta kalle shi, ta buɗe masa idanu saboda kallon tuhumar da yake mata, kallo ne irin na why are you doing this to me? Kallo ne na what are hiding? Kallo ne da yake nufin you are not alone Safiyyerh! "Wannan kallon fa? Bashi ko tara ko wani abu na cinye maka ban sani ba"

Bai kulata ba sai kawai ya miƙe yana hana jikinsa rawar da yake yi, cikin sauri itama ta miƙe ta ce "Wai me ka gani a wayar haka, dama ka ara mini ko game na dinga yi" gabaɗaya ya juya zuwa gare ta, ta yi saurin jingina da jikin bango banda idanu baya hayaƙi da ta ce hayaƙi idanunsa ke fitarwa, bakinta ya shiga rawa ta kasa furta masa komai, saboda yadda ya takure ta a jikin bangon tare da sata a tsakiya naman ƙirjinsa ya dinga rawa sai zazzaro manyan idanunsa yake waje kafin ta yi magana ya daka mata tsawa ya ce "Ina ɗana? Where is my son?"

"A baby? Ɗanka kuma?"

"Zan kwaɗa miki mari kika sake mini question akan question"

"Ina zan ga ɗanka kuma ni Safiyyerh, kai ɗin ma yaushe na sanka balle na san kana da ɗana, kuma idan kana da yaro what is my business a wannan issue ɗin da zan ɗaukar maka yaro"

"Shhhh a liar, ashe kin haihu" a wannan point ɗin, Safiyyerh ji ta yi kan ta zai buga ya tarwatse, tuni hawayen da yanzu baya neman shekararta wajan fita ya shiga sauka akan farar fuskarta, ta dinga girgiza masa kai amma ta kasa magana sai kawai ta fashe da kuka tana yin ƙasa da kan nata, da zai gane daya matsa, da zai gane daya daina kusanta kan shi zuwa gare ta, a duk wata musayar magana da suke yi zunubi ne a gare ta, tana auren wani, tana rayuwa da wani daban a keɓantacce waje a ƙasan zuciyarta ta ce "Allah ka gani, bada nufi na yi ba, Allah kar ka tuhume ni da cin zarafin igiyar auren Aliyu, na bar mijina na zo wajan ɗan daba. Astagafirulla Ya Allah"

"Ban yi tsammanin dani dake duk mun isa samun ciki ba, ina nufin ban yi zaton na isa bawa mace ciki ba a wancan lokacin, kema ban yi zaton kin isa ɗaukan ciki ba, har na biye miki muka aikata zunubin dake bibiyar rayuwarmu, daman an ce mace shaiɗaniyya ce kin yi tasiri a rayuwata, lallai kin yi galaba, kin ganni kina nuna kamar ma ba ki taɓa ganin mai kama dani ba a dukiyarki, balle ki tuna ke ce shaiɗaniyyar da kika shigo rayuwata kika rusa komai nawa kika lalata tarbiyyata, kika ƙwace mini ƙuruciyata, me na yi miki? Why why why?"

"Why??"

Ta ji why ɗin ya sauka a ƙirjinta, Safiyyerh couldn't speak tana shasshekar kuka ta ce "Ni ce shaiɗaniya? Me na yi maka ni Safiyyerh? Na rantse da Allah da Annabi ban taɓa ganinka ba ko dai ka sake yin shaye-shaye ne? Wacce ƙwaya ka sake sha take faɗa maka ba daidai ba?" Duk ta ruɗe jikinta nata rawa, shi kuma ya kafe ta da rinannun idanunta har mamakin yadda baya gajiya da ƙura mata ido da yake maimakon ya yi faɗa ko ihu wannan karan muryarsa a raunace yana sake matsar da fuskarsa zuwa gare ta ya ce "You leave me if you want, saboda ke ba kowa bace face muguwa last tambaya da zan miki ina yaron da kika haifa yake?"

"Jarumi!"

Safiyyerh ta kira sunansa a tsora ce gani take kamar ya haukace ya ɗage mata duka girarsa biyun tana kuka ta dube shi "Ni Safiyyerh ban taɓa tarayya da wani ɗa

namiji ba, ta ya zan samu cikin haihuwa tunda ba'a ruwa ake samu ba, how? Na ce how?"

"How? ta yadda dai kika lalata ni a baya haka to"

"Ka samu matsala" fuskarsa ba walwala sam kuma yana nufin abin da yake magana akai, ta zata iya tuna waye shi zata san shi ba ma'abociyar wasa bane, zai iya irga murmushin da ya yi a duniya, gabaɗaya bai ga abin da zai saka shi murmushi a duniyana balle dariya. Ya ɗaga hannu kamar zai ɗauke ta da mari ta saka ɗaga nata hannun, ya yi tsaye yana kallon ta ta ce

"Tunaninka me? Zan zauna ka mare ni wallahi kwaɗa maka mari zan yi nima na dawo da kai cikin hayyacinka" sai gabanta ya hau faɗuwa ganin ya sake matseta a bangon ya ce "Remember??"

"Me"

"I missed the hug, da kike ta bibiyata"

"Ni ɗin? Over my dead body"

Ya yi kamar zai riƙe ta, ta runtse idanunta tana sakin ƙara a hankali kuma ta ji ya damƙi hannunta ya ɗora a ƙirjinsa da yake bugawa "Labarina ba zai taɓa kammala ba harafin sunanki ba, ko a baya ban taɓa cewa ina son ki ba, balle yanzu kawai kim cutar dani Allah zai saka mini" yana cewa haka ya sake ta, ta faɗi a wajan yana harhaɗa hanya ya fice daga gidan bayan ya rufe ƙofar Safiyyerh ta sauke ajjiyar zuciya wannan mutumin ya fara samun matsala da tunaninsa zuwa gaba zai iya haukacewa.

Ta yi shiru thinking wanne hali Daddy yake ciki na rashin ta? Allah ya sa dai bai shiga damuwa ba kar wani abu ya same shi ta shiga uku, he mean the world to her shine inuwarta. Ta lumshe idanunta tunanin Aliyu ya sauka a ƙirjinta mamakin yadda ta yi accepted yayan nata ba wani tashin hankali, kodayake duk abin da Daddy ya zaɓa mata a rayuwa dole zata amsa, ko wuta ya ce ta shiga babu musu zata shiga saɓon Ubangiji ne kawai ba zata yi ba, shima ba zai taɓa cewa ta yi ba,

Ummiminta Yaya J, Awais, Dr tuna waɗannan mutanen ya saka ta fashe da kuka zaman gidan ya yi mata ba daɗi wajan Daddy kawai take son komawa taga a wanne hali yake ciki? Ta haƙura da jin labarin nasa gabaɗaya.

Moh na fita ya nemi wani dakali a gefen gidan ya zauna ya yi, bawai tunani yake ba shi kan shi bai san dalilin shirun nasa ba. Zuciyarsa yake son bawa dama na tunanin Aby da Ammo amma ya gagara ya ji ya zare su daga cikin zuciyarsa da rayuwarsa kamar yadda suka kyamatar shi.

"Mai dawa"

Ya juya ya kalli Goje sai bai ce komai ba Goje ya ce "zaman mu a nan wajan akwai hatsari Mai dawa, yarinyar a san yadda za a yi da ita mu kama gabanmu"

"Wai ina ta magana ka yi shiru, wannan halin naka na tsana kai ba'a abin arziƙi da kai". A hankali ya furta "dake ni ba ɗan arziƙi bane shine"

"Kai na ƙasa, tuba nake waye mutum ai ko aljani sai ya shirya. Mai dawa akwai zance a ƙasa, kafin nan kunna abar maganarka ka kai gidan sauti ka ji wani yare"

"No" a ɗan hassale Goje ya ce "Wai mene matsalarka da gidan rediyo ne? Kai komai baka so kafi gane ka yi ta zama cikin kunci kana bankawa cikinka hayaƙi kana yi wa kan ka allura da shan mugawayen ƙwayoyi? Ka dinga sassautawa kan ka"

Moh ya ɗauke ƙafarsa ɗaya ya ɗora saman ɗaya yanayin zamansa kamar na sarakai a hankali ya dinga girgiza kan shi "Na tsani redio, da masu gidan redion"

"Saboda suna baza cigiyar kama Scorpion da tukuici ga wanda ya kawo ko information nasa ne?"

"Oh, jeka faɗa if you want" Goje ya girgiza kai ya ce "Ba haka nake nufi ba, lalace ta bata haka ba cin amanarka ka tuna dani da kai duk abu ɗaya ne, halayya ɗaya muke ɗabi'a ce kawai ta bambanta mu" ya cije bakinsa, hopping ko zai ji sassauci

daga cikin zuciyarsa wanda yake fata ya ɗago rinannun idanunsa masu kaifi da ban tsoro cikin sauri Goje ya yi ƙasa da kansa wani irin shakkar Moh ya ɗar su a zuciyarsa ga wani irin kwarjini da ya yi masa a idanu "Akwai bambanci, duk ta'addancinka baka taɓa kisa ba"

"Kai ma ɗin baka taɓa ba, sai ɗaukan hanya ka daina jawa kanka jarfa ana zaune lafiya yanzu ma ya muka kaya"

"Goje"

"Mai dawa, uban mafarauta"

"Kabar mutum idan ka gan shi, ko kai baka san waye ni ba, kabar ni a yadda nake showing kai na gare ku, idan na yi shiru ka basar ina ɗage maka ne, Moh baya magana, Moh baya son takurawa, Moh baya son surutu redion ce kuma bana ra'ayi Scorpion kuma da ake magana ba zan taɓa bayyana ba sai na gama yi musu illa, ta'adin da na yi bani da tabbacin zan wanye da Ubangiji lafiya" Goje da ƙyar ya iya ɗago kai ya kalli Moh, ya ga tuni har ya tashi ya bar wajan kamar walƙiya ya kan rasa inda yake zuwa da yawan lokaci ba'a taɓa gane abin da shirunsa yake nufi, ba'a gane sawun tafiyarsa idan ya taka ƙasa sai ya tabbatar bai bar shaidar yatsun ƙafarsa ba kafin ya ɗora da tafiya.

***Sharfaɗi na zaune a office ɗinsa na FS WORLD INVESTMENT COMPANY matsayin chairman of the company. Ya ɗan kalli Professor Abdu ya ce "Kamar baka da ikon amsar dukiyar Safiyyerh daga wannan Companyn Professor Abdu Marafa, saboda dukiya tata ce kuma saka hannunta, idan ya zama dole mutum ya cire hannun jarinsa muna da tsare-tsaren da muke bi, ba kara zube kamfanin yake ba to ina mai baka haƙuri akan hakan"

"Sorry for yourself Sharfaɗi" Sharfaɗi ya ji saukar muryar Professor bawai mamaki ya bashi ba, yana dai tunanin yadda ya rufe idanunsa ta doke kuma yake son ƙwace dukiyar Safiyyerh, tunda Safiyyerh take sisi na salary ɗinta matsayin Manager bata taɓa amsa ba, sai ma kawo wani kuɗin da take ta saka tana daga cikin top 5 richers na masu hannun jari a kamfanin, kuma ita ce ma'aikaciya wacce tafi kowanne ma'aikaci zaƙaƙuranci.

"Safiyyerh dai yɑta ce ina da iko da abin da yake mallakinta, kafin a kammala rubuta sunanta dole a samu sunan Abdu Marafa a maƙale da nata, ka faɗa mini tsare-tsaren ku zan bi presidua ɗin komai idan hakan yana nufin bani dukiyar Safiyyerh dake wannan kamfanin"

"I am sorry Abdu Marafa, amma ba mai yiyuwa bane hakan"

"Mene zai hana hakan yiyuwa?" Daddy ya ce yana buga table ɗin gaban Sharfaɗi tare da miƙewa tsaye "Please a mutunce leave my office, dukiya umarnin mai ita kawai take ji dole sai mun samu saka hannu Safiyyerh a wannan file ɗin" ya miƙewa Daddy file ɗin yana zagayawa. Daddy ya ɗauki file ɗin ya yi murmushi sai kuma ya kalli Sharfaɗi ya ce "Idan Safiyyerh ta mutu waye zai gaji duk abin da ta mallaka"

"Wanda suka dace mana, ko a kamfanin nan sai wanda ta saka sunansa a matsayin wakilinta"

"You say it all, ni ne wakilin Maama" murmushi kawai Sharfaɗi ya yi yana ɗaukan key ɗin motarsa ya ce "Zaka gani"

Professor ya yi waje, shima Sharfaɗi haka daddy ya nufi motarsa thinking ta ina zai fara neman signature na Safiyyerh? A haka ya isa gida ya yi parking motar daidai nan Dr Hash shima ya dawo daga asibiti ya kalli Mahaifin nasa "Daddy fita ka sake yi jininka ya hau sosai fa, kada wani abu ya sameka". Daddy ya girgiza kai a hankali ya fara tari yana dafe kan shi nan da nan idanunsa sukai jajur da sauri Dr Hash ya kama Daddy zuwa cikin gidan lokacin Ummimi na zaune fuskarta ba walwala ta cire idanunta zuwa kan su sai bata ce komai ba Ummi kuma ta ce "Subuhanallahi ba dai jikin bane? Yaushe ya fita na ɗauka yana cikin part ɗinsa"

"Na je Companyn da Maama ke aiki, ko zan samu wani bayani amma shiru" idanunsa kamar za su zubar da hawaye ya juya ya kalli frame ɗin picture ɗinta, ta yi murmushi fararen idanun nan nata sai sheƙi suke, ta tsuke laɓbanta kana ganin bakinta kasan na tsiwa ne lokacin basu jima da dawowa daga Saudia ba, har Yaya J na tsokanarta Hajiya guda babu haƙorin makka ta murguɗa masa baki ta ce "Ai don Allah na yi, ba sai an san na je ba"

"Ina kike Maama? Ina kike safiyyerh Allah Ya sa ba su cutar mini da yarinyar ba, Safiyyerh kina lafiya dai ko? Na kasa taimakon ki, arziƙina bai yi mini rana ba" Ya girgiza kai yana dafe saitin zuciyarsa Ummi ta share hawayen da yaƙi tsaya mata ta ce "Shi ya sa ban amince da dawowar mu ƙasar nan ba, amma kun kasa fahimtata kalli yanzu babu Safiyyerh. Allah ka kare mini yarinyata ka sanya tana hannu na gari, ka dubi wawta da rashin lissafinta ka kiyaye mana ita" sai kuma ta fashe da wani irin kuka duk duniya yarinyata ɗaya a duniya mace Safiyyerh, da ita take shawara amma yanzu ba Safiyyerh a tare dasu. "Junaid ka samu Gadanga a waya?" J ya girgiza mata kai alamar a'a shi tun sanda aka yi auren Safiyyerh da Aliyu ya rasa bakin magana baya fahimtar abubuwa da dama. Da J da Dr Hash suka kama Daddy zuwa part ɗinsa dake upstarts bayan sun kwantar da shi J ya juya Dr Hash ya ce "Daddy"

"Ya aka yi Hisham?"

"About Maama's sick, condition nata ta kusa cinye lokaci ba'a yi mata allura ba, rashin yin allurar ka san me yake nufi, mu duka ba zamu iya ba idan hakan ya kasance ka san taurin kan Safiyyerh da kafiya da naci, ga ta da ƙulafuci da saka abu a rai, ita bata yadda da gazawa ko kasawa. Ban san me ya saka haka ba daddy komai da zai faru Ubangiji ya riga daya rubuta, baka tunanin zuwa gaba halin da za a iya saka Aliyu idan gaskiya ta fito, kamar anza zalunce shi ne ka ɗauka ni ne Captain wallahi ko da gida da mota da biliyoyin kuɗi ba zan iya accepting Safiyyerh as my wife ba, ka saka na fara tunanin ko Aliyu ne ba ɗanka ba shi ya sa ka zaɓi laƙaba masa ita? Tunda bai san mene ya faru ba. Laifi tudu ne daddy daga ɗakin asibiti dana bar Safiyyerh kafin na fito ka ɗauke ta kun dawo gida, ko aikin da akai mata bai kammala daidai ba, ka rabata da...."

"Hisham, out of my room"

"Daddy" a tsawace ya ce "na ce ka fita daga ɗakin nan ko?" Dr Hash ya dinga kallon daddy sai kawai ya juya ya fita zuciyarsa na zafi da tafarfasa. Bayan fitar Dr Hash daddy ya ɗakko file ɗin da Sharfaɗi ya bashi ya fara dubawa wata iriyar zabura ya yi yana buɗe idanunsa ganin sunan ALIYU ABDU MARAFA da Safiyyerh ta saka matsayin shine next of kin.

***Sa'adah ta dinga kallon Sp Ghali ta ce "Shifa wanda kuke nema rabon da mu ganshi mun manta, kuma kun san zaku sake kama shi kuka sake shi tun farko?

Wane ya hana a yanke masa hukunci, ita gaskiya fure take bata yʻayʻa kuje ko kama Mutallab bawai mahaifinsa ba" Sp Ghali ya ce "Ki iya bakinki a gaban hukuma kike, hukuma sai da rarrashi haka tsarin aikin yake idan ba yaro akwai uban yaro, kun je kun haifi kangararre mara amfani cikin al'umma wanda gwara mutuwarsa da haihuwarsa, gwara ɓarinsa da cikinsa shine kika kwaso ƙafa kina faɗa mana shirme, ki buɗe kunne da kyau kiji kaf jihar Kano da Nigeria baku da wanda ya isa ya kare Scorpion Tahhb daga tuhumar da ake masa, idan kuma akwai Bisimillah"

"Gaskiya ne ba ka yi ƙara ba, bamu da gata sai na Allah wanda ya halicce mu, ya samar mata da numfashi tun a ciki muna gode masa a yadda ya bar rayuwarmu, mun amshi jarrabwar daya samar a zuri'ar mu, amma ka sani ba wanda yake so ya kasance ɗan iska ko ɗan daba, Ubangiji baya shawara da mutum wajan zamuwarsa talaka ko mai arzƙi, wata shari'ar sai a lahira a gaban Rabbil samawati. Kai ma daka kasance ɗan sanda ba iliminka bane ko dabararka ba wayonka bane ko sahalewarka, kunfa yakun ce ta Ubangiji ta sauka akan ka, shi mahaifinmu da kuka riƙe kuka haɗa shi da mugawayen mutane shaiɗanu iyayen yarinyar ne suka ce ku kama shi?" Sp Ghali ya yi mata banza don bata ita yake yi ba, ya saka wasu police su fitar da ita idan kuma taƙi a haɗa da ita a ɗaure. Haka Sa'adah ta juya da abincin data zo da shi, wannan dalilin ya saka bata zo da Bafullatana ba domin sai ta musu hauka a cikin state cid ɗin.

***Da yamma bayan ya kammala sallar la'asar ya ci abinci jikinsa sanye da Dag Flight running short red ɗin riga da black wando iya cinya bai ƙarasa sauka ba, jikinsa duk a murmurɗe sai Bionic hand gloves a da sauri da sauri yake running akan machine ɗin ya haɗa zufa sosai lokaci lokaci yake share zufar data gama jiƙa masa six pack ɗinsa slowly slowly kuma ya fara rage gudun har ya kashe gabaɗaya, a sauka a hankali tare da barin training room ɗin ya tafi wajan hutawa bayan ya ɗakko coke a hannunsa mai sanyi, baƙar fatarsa sai sheƙi take da ƙyalli ya tsaya jikin window yana shaƙar iskar dake kaɗawa ya lumshe idanunsa ya buɗe ya kurɓi coke ɗin shi kaɗai sai haɗe rai yake yana ɗan kwaɓe fuska sai kuma ya ɗauki wayarsa ya duba number har yanzu dai bata shiga

“Muhmmad”

Saukar muryar da baya taɓa manta sautin ta a kunnensa haka yanzu ma ta sake saukar masa idan komai nata ya bar shi to banda wannan muryar sai kuma ya haɗe fuska a fili ya ce "When i catch you…. Sophie" sai ya ɗauke tunanin ya ji kamar ya fita waje ya ji ya yanayin garin yake a yanzu gabaɗaya a takure yake. Ƙarar

computer ya dawo da shi daga tunanin cikin sauri ya saka wayara a aljihu yana furta "Oh no"

Da yatsunsa biyu ya dinga shafa screen ɗin dake jikin bango, yana shige abubuwa ɗaya hannunsa da remote control a nutse komai ya fara backup zuwa cikin computer bakinsa ya mayar gefe kamar zai yi murmushi ganin yadda lokaci ɗaya ya yi musu kutse ya rusa komai da suke yana gamawa ya saita zuwa Voa muryar J kallah ya sauka kunnensa.

***Ture farantin abincin Safiyyerh ta yi tana yarfa hannunta saboda wani irin ciwo da mararta take yi mata da ƙyar ta miƙe ta fito zuwa parlo ta durƙushe ƙasan ƙafafuwanta. Mangal ya dube ta ya ce "Yar wahala ashe attajirai ma suna kuka, ɓarayin gwamnati"

"Kana da matsalar tsinannen yaron nan, shegen surutu kamar haihuwar aku"

Mangal ya yi shiru yana jan sigarin da yake sha Goje ya kalli Moh ya ce "Kamar bata da lafiya fa" ya yi masa banza ya lumshe idanunsa. Safiyyerh ta kasa daurewa ta fara kuka sosai ta ce "Wallahi mutuwa zan yi wayyo cikina wayyo daddy wayyo Yaya J,na shiga uku zan mutu Captain"

"Kut dumadu wai ciwo ta kewa kuka nan dai babu Professor balle ki ji motar ambulance"

"Mai dawa" ya juya a hankali ya dubi Goje "Bata da lafiya fa"

"Wai kai akan kuwa baka da imani ne?" Nan ma ya yi shiru kawai Safiyyerh kuka kawai take ta haɗa zufa, tun tana yi har ta fara sakin ajjiyar zuciya amma Moh ko yatsarsa bai motsa ba, Goje ya gama masifarsa da bala'in sai ya miƙe ya fita daman tuni Mangal ya fice. Ya miƙe zaune yana motsa damtsen hannunsa da baƙar rigar jikinsa ta kama shi, da ƙyar ya yi wanka ya saka shima saboda surutun tsiya data dame shi. Ya buɗe idanu ganin jini a jikinta can ya saka ƙafa ya zungure ta, ta yi masa banza domin bacci ya fara ɗaukan ta ya zamo zuwa gabanta ya duƙa yana kallon ta taƙi ɗago ya leƙa fuskarta suna haɗa idanu ta murguɗa masa baki, sai kuma ta fashe da kuka sosai ta ce

"Ba ruwanka dani, ka bar ni na mutu na fasa son ka ba, bana son ka get lost"

Gefen Safiyyerh damuwarta ta ninku bata da walwala da farinciki idan ba muryar Daddy ta ji ba, ko fuskarsa ta gani sai ta ji ta samu nutsuwa a ranta ta dinga cewa daddyna mijina, tattara sabgar karatu ta zubar a gefe makarantar ma ta dame ta ta ji dama kawai a cire ta. Baya iya bacci sai ta rungume filo a ƙirjinta, kullum sai ta kwashi kayan Ummeyh na S Bayero ta sha, lokaci ɗaya jikinta ya fara buɗewa ƙirjinta ya cicciko fatar jikinta ta sake sheƙi hips ɗinta ya buɗe, sai ta fara saka hijabi hakan ya saka Ummeyh ba ta yi noticing komai ba, ba kuma ta taɓa tambayar Safiyyerh dalilin saka hijabin ba, bata tsaya da lura da kayan matan nata ba. Bata ɗauki zancen Safiyyerh na aure da take yawan yi mata ba.

***Mai dawa na ƙofar gidan tsaye da Kimiyya da zuwansa kenan Malam Ayuba ya ƙarasu wajan da sauri yana kuka tare da cewa "Me muka yi maka, daga maganar aure shi ne zaka kashe mini yata kazo kaga halin da take ciki"

Mutallab ya dinga kallon Malam Ayuba, kuma ya yi burus Kimiyya ne ya ja hannun Mutallab suka rufawa Malam Ayuba baya, tun kafin su isa suka tarar an cika ƙofar gidan ga wani hayaƙi na tashi kamar gobara, da sauri ya faɗa ciki yana shiga ya jiyo muryar Diyna na cewa

"Zai kashe ni, Mutallab ne wallahi shine ina son shi ina son shi" sosai wuta ke ci a ɗakin da take ciki, gashi ƙofar ta manne taƙi buɗewa, duk wani ƙokari da Mutallab zai yi but he couldn't save Diyna's life, yana jiyo ihunta ta cikin wutar tana babbakewa ya kasa ceton rayuwar Diyna, tun tana ihu har ta daina ta mutu a cikin wutar gobara tana ambaton sunansa wanda duk wanda ya zo sai ya gasgta cewa shine ya kashe Diyna.

Back to story.

Ya ja numfashi mai tsayi ta cikin bakinsa ya fesar, kansa na juyawa kamar yanzu ne yake jiyo ihun Diyna a kunnensa. Ya buɗe jajayen idanunsa ya kalli Safiyyerh dasu, ta yi saurin ɗauke kai wani irin tsoran shi da shakkarsa take ji, magana yake son yi mata amma ya kasa.

Safiyyerh ta yi ƙarfin halin cewa "shikenan Diyna ta rasu?" Ya ɗage mata girarsa biyun, almar e;.

"Allah sarki. Allah Ya ji ƙan ta" sai kuma ta fara kuka ƙasa ƙasa, tuna cewa yanzu fa shi mahaukaci ne yana da taɓin ƙwaƙwalwa? Ta dinga rusa masa kuka wanda shi kuma ya yi ko gezau kamar ma kukan nishaɗi yake saka shi, sai dai duk wani motsin Fiyya akan idanunsa yake ya dinga jin kan shi na sara masa, ya saka ƙata ya zungure ta, taƙi daina kukan ya sake zungurinta nan ma ta yi masa banza, ya saki wuƙar hannunsa wacce jinin jiki ya fara bushewa amma sarar da aka yi masa shi har yanzu yana nan, ya matsa dab da iya ya duƙa tare da saka hannu ya tallafo haɓarta ta runtse idanunta tana faɗin Astagafirulla a zuciyarta, duk abin nan bai saka ta manta ita matar aure ce ba.

"Shhhh, Quiet"

Ta kasa daina kukan ta cigaba da kallonsa kuma ya yi ƙasa da murya yana sake duƙar da fuskarsa dab da tata, yafi minti uku yana kallon fuskarta kamar mai son tantance abu, sautin muryarsa daga ƙirjinta take fitowa ya ce "Shiru, ko na yi miki abin da nake ta riƙe da shi tsayin shekaru" ta dinga shasshekar kuka a hankali ya saka yatsarsa, manuniyya ya fara kewaye lips ɗinta da ita, cikin wata murya ya ce "Duk macen da tace tana so na, sai a wayi gari ta mutu, Diyna ita ce first, mata uku suna mutuwa saboda ni, ana cewa ni na kashe su, daga cikin har matata wacce na aura, gawar data zama gawa ta ƙarshe ita ce gawarki Safiyyerh" ya yi shiru yana cigaba da zagaye lips ɗinta da yatsarsa.

[1/7, 9:34 PM] Sis Fauzy: Chapter 24: If he is your husband, who am i?"

Safiyyerh ta zame fuskarta, cikin kuka ta ce "da gaske kana da taɓin ƙwaƙwalwa? Mahaukaci ne kai, don Allah ka ƙaryata zuciyata, ka ce mini lafiya ƙalau tunaninka da ƙwaƙwalwarka suke" kuka take sosai kamar wacce aka cewa Professor Abdu Marafa ya mutu, da ƙyar take jan numfashi ta kalle shi taga yana nan durƙushe gabanta ita kuma yake kallo.

"Jarumi" ya ɗage mata girarsa biyun, ta ce "Karka raunata zuciyata da jinkimarka, kar ka saka mini soyayyarka ta dole, domin hakan ba ƙaramar jarrabawa bace a wajena, ka yi mini komai amma kar ka bari na kamu da tsananin son ka, wannan zuciyar dake cikin ƙirjina...," ta yi shiru tana nuna masa ƙirjinta da yatsa, ya kalli ƙirjin sau ɗaya ya mayar da idanunsa zuwa kan fuskarta musamman idanunta.

"Ba zata jure ba, ka faɗa mini wanda ya saka ka sato ni, kuma ka ƙarasa bani labarinka, ba zan jure zaman a nan ba"

"Hmm"

"Na ji tausayin Muneeberh na jima ban ji mutuwar data tsaya mini irin wannan ba, ban ɗauka akwai wanda suke cikin halin na yunwa da rashi har haka ba sai a cikin labarinka. Sannan Aby bai..,"

Ta yi shiru tana sunkuyar da kanta zuwa ƙasa, domin ba zata jure kallon cikin idanunsa ba; for a while. "Mugu ne" Moh ya yi furucin numfashinsa na sauka a fuskarta, ta girgiza kai a hankali ta ce "A'a ni ban ce"

"Ce" ya ce, yana miƙar da hannunsa saboda jinin dake zuba inda aka yanke shi. Safiyyerh ta girgiza kai tare da yin shiru, har ƙasan zuciyarta take tsananin jin tausayin talaka,idan baka da kuɗi a rayuwa shikenan kai ba mutum bane. "Don Allah ka matsa daga kusa dani, wallahi tsoro kake bani kuma mun yi kusa da juna sosai" shi dai bai ce mata komai ba, sai idanunsa masu kaifi daya kafeta da su kamar mai son fahimtar wani abu, yana kallon ta yana motsa bakinsa.

"Jarumi" Moh ya dube ta, cikin raunin murya da sabon tashin hankalin daya mamaye fuskarta ta ce "Bayan daba da shaye-shaye da kuma bangar siyasa da ka yi amma baka taɓa yin..." Ta yi shiru, ya buɗe mata ido.

"Kee" ya kira ta cikin dakakkiyar muryarsa ya yi kiran, ta ji mararta ta kumbura kamar za ta yi fitsari, ta fara inda-inda sai kuma ta ce "Uhm amm ba komai"

"Ƙarya kina, talk" domin da yawan lokaci a furucinsa zaka fahimci yana da alaƙa da jinin yarabawa. Ya fara juya wuƙar hannunsa ta ce "Me za ka yi da wuƙa yanzu? Ba dai faɗa ba?"

"Ke zan yanka, ba'a rainawa Moh hankali, zan fara nuna miki da gaske ina da taɓin hankali" kamar ta saki fitsari haka Safiyyerh ta ji ta ce "Haba Jarumi, me ya kawo maganar nan kuma? Wai ba'a wasa da kai ne?" Bai kulata ba, ya cigaba da juya wuƙar ya ɗaga tare da nufar gefen cikinta, ta yi zumbur zata tashi ya miƙa hannunsa ya damƙi gefen cikin nata ya miƙe tsaye da ita a hannunsa, ta haɗiye

wani irin yawu da ƙyar sai ƙifta masa idanu take, banda kiran sunayen Allah guda ɗari babu ɗaya da take babu abin da take a ranta.

"Allah Ya baka haƙuri Jarumi"

"Ce...!" Ta ce "Amma baka taɓa aikata zina ba, bayan abubuwan da ka yi ko?" Ita kan ta bata san ta yi maganar ba, kawai abinne ke ci mata zuciya ba tare da sanin dalili ba. Mai dawa, ya kafe ta da idanu musamman ɗan siririn zanen S ɗin dake wuyanta wanda aka yi da baƙin abu, ya haska fatar wuyan sosai a barka da zabiya.

"Baka taɓa aikata zina ba ko? Ka faɗa mini baka taɓa aikata zina ba don Allah Jarumi, don Allah ka taimaki Safiyyerh da zuciyarta"

"Mece zina?" Ya tambaye ta. Ta ce "Baka sani ba?" Ya mata shiru, ta ce "A yi abin auratayya ba aure" ya shagiɗar da bakinsa zuwa gefe ya ɗaga idanunsa ya kalli sama ya jima a haka fuskarsa nan ba walwala kamar kodayaushe, ya sakko da idanunsa ya sake zubawa wuyanta ido.

"Yi yadda zan gane"

"To a yi iskanci ba tare da aure ba"

"Shhhh, idan wanne ne na taɓa, da kuma ke na yi iskancin har mun samu sakamakon hakan, ɗa kenan ko?"

Dum! Haka Safiyyerh ta ji a tsakiyar kan ta, wasu abu kamar jonin wutar lantarki suka fara yi mata tarnatsi a cikin kan nata, ta yi saurin dafe kai jikinta na rawa ta yi baya kamar zata faɗi, amma bawan Allan ko motsi bai yi ba, balle ya tare ta. Cikin rashin fahimta ta ce "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un! Ka taɓa zina? Na shiga uku ni Safiyyerh wai me ya sa baka da ɓoye abu ko da ka aikata? Ka san tabon da ka ajjiye mini a zuciyata kuwa? Har na mutu ba zan manta wannan kalmar ba, saboda kaga ina son ka na damu da kai? Shine bari ka nemo hanyar ƙuntatawa zuciyata?" Ta fashe da wani irin raunataccen kuka, a lokacin mantawa ta yi da igiyar auren Maj Aliyu uku da yake kan ta, wani irin tiriri da zafi take ji, zuciyarta a matse take a takure cikin ƙuntataccen ƙirjinta, ta ji iskar wajan ta yi mata kaɗan.

Miƙewa Safiyyerh ta yi cikin sauri ta nufi hanyar fita cikin daren idanunta rufe ko ganin gabanta ba ta yi, bayan ta buɗe ƙofar tana ƙoƙarin fita ta ji ya saka hannunsa ya damƙo ƙugunta ya haɗo da wanda dake jikinta a jerin kayan daya kawo mata, a gigice ta juyo saboda wani irin miƙewa da gargasar jikinta ta yi cikin faɗa ta ce "Wanne irin iskanci wannan zaka riƙe mini ƙugu, ko sha fara kaga aljan ɗin ka watsa eh?"

"Iskanci?" Ya buƙata? Don shi bai ga abin iskanci ba. Ba ki Safiyyerh ta buɗe da nufin cewa "Ka sake ni, ina da aure ina miji so, Maj Aliyu ina da auren wani a kai na haramun ne ko jin muryarta balle taɓa wani sashi daga jikina" sai ta yi shiru, tuna cewa ai bai san tana aure ba taga duk wani bayani da za ta yi masa ba zai fahimta ba ta kwantar da murya ta ce "Abin da kake ba kyau, ka cika ni" a hankali ya sake ta, yana ta kallon ta da zai iya kuma ya jure zai tambaye ta akan mene iskanci yake nufi, a tsakanin lokacin nan ya furta masa kalmar iskanci sai wajan uku. "Ka yi haƙuri don Allah" ya sake mata shiru kawai.

"Bai kamata a ce ina zaƙewa tare da kutsa kai cikin rayuwarka har haka ba, na ni kawai zan rayuwa da kai don Allah ka bani wannan damar"

"Ki dinga ce mini ɗan iska?"

"Baka haka nake nufi ba, kalmar zina ta mini tsauri da yawa wallahi i can't take it from you"

"Uhm" ya ce ya juya yana tangaɗi sosai ya fita daga cikin gidan tare da rufe ƙofar da ƙarfi.

"Ka yafe mini Captain, Ka yafe mini Aliyu naci amanar aurenka da yake kaina, na wulaƙanta igiyar aure, na rusa yadda da amincin da Daddy ya yi mini, na saka ƙafa na rushe wannan ni'imar na yi tarayya da waninka, wanin da bai dace ba, wanin da bashi da cancanta ko rabin nagartar da kake da shi. Ni shaiɗaniyya ce kamar yadda yake faɗa, na sake ribatarsa, da wanne ido zan kalli mahaliccina wajan yi masa bayanin da aurena na kula wani namajin daban?" Safiyyerh kuka take sosai, jikinta na wani irin ɓari ta takure waje guda ta cusa kan ta tsakiyar ƙafafuwanta. "I am sorry Aliyu, ka yafe mini.... Ka yafe mini na wulaƙanta aurenka" shiru ta yi saboda ganinsa da ta yi tsaye a kanta, sai muzurai yake yi mata da ƙyar ta ce "Don Allah

Mutallab" sai ta yi shiru jin sunan nasa ya yi mata wani irin kwarjini "Ka mayar dani gidanmu, da ka yi garkuwa dani idan wani abu kake buƙata ka kira iyayena za su baka koma mene, saɓon Ubangiji ba kyau"

"Idan shi mijinki ne, ni waye?"

Rawar jikinta ya tsananta ta girgiza kai laɓɓanta na rawa "Kamarya?" Safiyyerh ta kasa fahimtar tun kafin faruwar komai da fitar Mutallab, taɓin hankalinsa ya motsa musamman yanzu da yake tsaye yana zazzaro manyan idanunsa waje, jikinsa na rawa ya ɗuka gabanta kai ya ɗago za ta yi magana, ta ji ya shaƙe mata wuya ya fara kifa mata mari a fuska idanunsa sun tara ruwa, wata azaba yake ji a cikin kan nasa, Safiyyerh ta fara kakari shatin yatsunsa suka zauna a fuskarta, gashi da iya ƙarfinsa ya shaƙe ta idanunta suka ƙaƙƙafe numfashinta ya fara tsayawa a ƙirji ta saka hannu ta damƙe ƙirjinsa tana shura ƙafa.

Goje na shigo cikin tashin hankali, ganin Moh ya shaƙe Safiyyerh zai kashe ta ya sana ya nufi wajan su da sauri ya ce "Mai dawa"

"Ya dai? Me ta yi maka ka sake musu yɑ wallahi" sai a lokacin ya lura tamkar Moh baya cikin hayyacinsa, ya fara ƙoƙarin ture shi amma ya kasa, daya matsa sai yaga ya fara kawo masa damƙa da ƙarfi yake cewa "kar ka zo nan"

Goje ya rasa yadda zai yi Safiyyerh har fitsari ta yi saboda wahala, ta ƙanƙame ƙirjinsa da hannunta biyu har tana taɓo kwantattun gashin da suke wajan, cikin sauri Goje ya faki idanun Moh ya danna masa wata jijiya dake bayan wuyansa, nan take ya saki Safiyyerh ya dafe wuyansa a hankali ya sulale a wajan ba numfashi, Safiyyerh ba ta faɗo jikinsa a sume. Mangal daya shigo yanzu yana haƙi ya buɗe ido ya ce "Yaƙi suka yi ne? Wai ragas kenan yarinyar nan tana raye kuwa?"

"Kai baka faɗar alheri ne?"

Mangal ya ce "Daga tambaya? Faɗa suka yi ne ko mene?". "India ne da Pakistan ɗan wahala ɓace daga nan" ko a jikinsa ya nemi waje ya zauna, shima Goje ya

zauna. Goje bai damu da duk wasu kayan maye ba hakan ya saka zaka ganshi a ɗan nutse.

Da safe Mutallab ne ya fara buɗe idanunsa da ƙyar yana dafe kan shi da yake sarawa tare da juyawa, ya dinga mamakin abin da ya saka shi kwanciya a nan wajan, ya dafe kai a hankali yana ɗan haɗe fuska. Nauyin da ya ji a ƙirjinsa da numfashi da ya ji yana ɗauka ya saka ya ɗan yunƙura zaune ya zubewa fuskarta idanu, ganin yadda ta yi jawur ga yatsun ƙwance a fuskar, ya kalli wuyanta shatin farata ya gani duk an ƙwarzane mata wuya, ya rufe ido ya buɗe tas komai ya dawo kansa ya dinga kallon ta, ya miƙa hannu kamar zai taɓa ta sai ya fasa saboda zafin zazzaɓin da ya ji, ya ture kan ta miƙe tsaye ya nufi ɗaya ɗakin tare da rufo ƙofa.

Yadda ta sume da kanta, haka ma yanzu ta farfaɗo tana jan numfashin wahala ta ja jiki ta miƙe, ta dinga kallon ita ke ƙwance a ƙasa, ita Manager guda? Safiyyerh, Fiyyar daddy a wajan ɣan daba kuma a ƙwance a nan ta dinga kuka sai da ta yi mai isarta ta yi shiru. Goje ya dube ta ya ce "Zan buɗe miki ƙofa ki gudu, domin za ki iya rasa rayuwarki a nan wajan a hannunsa, ni fatana da burina bai huce rayuwarsa ta gyaru kamar kowanne mutum ba, mun san cewa akwai ƙaddarorin da babu yadda muka iya da su, dole mu yi haƙuri mu zuba idanu har lokacin da Ubangiji ya so, ki tashi ki je zan faɗa masa ban san yadda aka yi kika fita ba"

Safiyyerh ta yi shiru sai ta ce "Zan gane hanya?" Ya ce "E, ta shi"

Ta miƙe jikinta na yi mata tsami ta saka abayar dake wajan, ta zura takalmi kan ta ko ɗan kwali babu ta nufi ƙofar fita, Goje ya bita da kallo. Tsayawa ta yi ya ce "Fece mana" Safiyyerh ta girgiza kai ta ce "Ba komai idan na tafi?"

"Ban gane ba komai ba?"

"Wallahi ba zan iya barinsa ba, ba zan iya tafiya ba ka yi mini afuwa" da mamaki Goje ya ce "Ubanki ne shi da ba za ki iya barinsa ba? Shi babu abin da sai same shi sai ikon Allah, ke kuma a banza zai kashe ki wallahi" sulalewa ta yi a wajan ta zauna, tana fashewa da kuka sosai ta ce "Wallahi zan zauna da shi, ba zan iya tafiya ba ka yi mini uzuri" wani siririn tsaki Goje ya ja ya miƙe tare da barin gidan, tana nan zaune ita kaɗai kamar mayya ta ji ya buɗe ƙofa ya fito, ta takure ya kalle ta ya

share, ya zaro sigari ya kunna ya farawa busawa yana sha yana lumshe idanunsa da kaɗa ƙafa kamar yana enjoying moment ɗin.

Yana yi yana kallon ta, amma ba za a taɓa cewa kallon nata ya ke yi ba, sai daya shanye kara goma ya miƙe zuwa ɗaki bai jima ba, ya fito ya dawo gabanta ya durƙusa. Ta fara ja baya tana takurewa tare da girgiza kan ta, so yake ya ce mata sorry amma the last abin da zai iya kenan a rayuwarsa bada haƙuri, Safiyyerh ta miƙe zata tashi a kumbure yana cika da batsewa ya ce "Koma"

"Ka yi haƙuri, ba zan iya zama inda kake ba" ya miƙa hannu zai taɓa wajan yatsun dake fuskarta ta ta zana ta fasa ihu tana ganin kamar sake shaƙeta zai yi, shi kuma ya riƙe ta gama suka fara dambe duk ta fita hayyacinta ya matse ta a ƙirjinta ya rufe ta da hannunsa cikin muryar gargaɗi a raunace ya ce.

"Finally i accept that, I'm always the wrong person in everyone's story, everyone's life" ya yi maganar a hankali kamar mai raɗa, can ya cika ta, ta matsa gefe guda tana jin wani iri lallai akwai wani abu a tattare da shi wanda yake jan ta zuwa gare shi.

"Bana bada haƙuri, zahirina kika gani just take it" ya jingina da jikin kujera ya zuba mata idanu a hankali kuma ya ɗora da bata labarin domin haka tafi fahimtar hakan sosai.

***After Diyna's death

Duk inda aka zaga sai a ce Mutallab ɗan gidan Malam Abdullahi mai allo ya kashe Diyna, saboda tun kafin wutar ta kama take kuka tana kiran sunan Mutallab, al'amarin da ya yi wa Malam zafi a cikin ransa, ganin yadda ake laƙaba sunansa a jikin na Mutallab ransa ya ɓaci ainun, yana jin haka kawai yaro ba zai ɓata masa suna a gari ba, aure kuma dole sai ya yi masa naganin kangara da lalacewa kenan.

Yana cikin tarin almajiran ya shigo cikin gidan yana sabaɓi ya tarar da Mama Zaituna ta yi zauna saboda ki karyawa ba ta yi ba, Ammo hankalinta na kan kuka da take ɗaurawa saboda ta mayar da hankalinta a kan sana'a sosai kodan bikin Sa'adah da za a yi. "ina wannan gangararren yaron yake ina ya shiga?" Ta yi masa shiru ya ɗaga hannu ya zarara mata bulala, ya ce "Ina magana domin iskanci kina mini shiru? Ina makashin yake mai ɗakkowa jama'a magana ba gaira ba dalili, yanzu ya tabbata ya kashe musu yarinya a banza? Sai ya maɗiɗi ake dani a gari shi

ya sa na ji ba fara zuƙewa? Shegen yaro ya ɗakko jinin masifa da shegiyar zuciya kafiya da naci kamar na kafuran farko, anya ba lalatacce bane ba?" Ammo ta yi ƙasa da kai tana shafa inda Malam ya zabga mata bulalar Mama Zaituna ban da dariya babu abin da take yi kafin ta ankara itama ya cauɗa mata bulalar. Zumbur ta miƙe ta yi ɗaki. Malam ya hau faɗa yana kumfar baki.

Mutallab da shigowarsa kenan ya tsaya cak a bakin ƙofar Malam ya ce "Yawwa yawwa ɗan asara haihuwar asara, da gaske ka kashe Diyna ka kashe musu yarin"

"E, na kashe ta"

"Innalillahi ka kashe ta fa kace?" Ya yi shiru, Malam ya dinga aibata Mutallab alkaba'i kala-kala ya ce "Kuma aure ba fashi, idan kaga dama itama yarinyar ka kashe ta" ya jinjina kai bai ce komai ba. "Ka je wajan abokina Malam Umaru, akwai yarinya tana nan wajansa marainiyya ce ka je ku gana cikin satin nan za a ɗaura muku aure"

Gabaɗaya naman jikinsa rawa yake yi da wani irin ɓari zuciyarsa na tafasa. Tun bayan faɗan da ake yi masa bai ɗago ba, balle ya tofa tasa "Ina jin kamar na haifawa kaina matsala" cewar Ammo.

Ya ɗago rinannun idanunsa wani irin ruwa ne kwance a cikinsu, jijiyoyin kansa sun yi ɗoɗar tare da jerewa suna harba masa.

"Mutallab" ya ji zuciyarsa ta kirayen shi, kiran da sai daya ja numfashi ya haɗiye abinsa zuwa ciki ba tare daya fesar ba, yana jin hucin zuciyarsa na keto ruɓin fata bakwai da Ubangiji ya halitta a jikinsa, me ya sa suke son yi wa rayuwarsa iyaka da jin daɗi ne? shahara tare da daular da yake mafarki suke son yi masa farraƙo da ita? Da gaske arziƙi yake so, iko yake buƙata, lalle suna son tauye rayuwarsa.

A hargitse ya furta "Kar ka yi mini baki, Aby da kun sani da ba ku yi cikina ba, da kun sani da baku yarda kun haifan ba, karku ƙuntata rayuwata ba zan ɗauka ba" Kuka Ammo take sosai ya saka ƙafa ya buga jikan ƙyauren nan take ya faɗo, ya

dinga dunƙule hannunsa jini na zuba rezar dake cikin tafin hannun nasa na shigewa ciki hannun.

"Idan na lalace ku na lalacewa domin zama zan yi mu raba hisabin tare" Ya faɗa yana zaro ƙatuwar mesa daga cikin aljihunsa ya rataya a wuyansa.

"Me kake so?"

Kai tsaye ya ce "KUƊI, IKO!"

"To kai da kuɗi sai dai idan ana yi a lahira, tagayyararran yaro kawai, ɗan banza mai irin zuciyar abu lahab" wani irin abu ne ya kama zuciyar Mutallab mai kama da rauni, zuciyarsa ta dinga rawa tana masa motsi a ƙirji ya matsa kusa da Malam ya durƙusa akan ƙafafuwansa kan shi a ƙasa ya dafa ƙafafuwan Malam ya ce "Aby Abu Lahab ɗin da aka ambata a cikin Alqur'ani, cikin suratul Masad kake haɗawa jininka da shi, wanda ya yi Annabi Muhammad Sallallahu alaihi Wasallama tawaye shi kake dongana shi dani? Me na yi da zafi haka? Ni Aby ni ni ko? Na roƙe ka daka daina kar abin ya wa Mutallab yawa, ba zan jure ba ka yi mini aikin gafara Aby, ka mini addu'a ka nema mini shiriya idan kuskure nake" Aby ya saka ƙafa ya hankaɗe Mutallab ya nuna shi da yatsa ya ce

"To me haihuwarka ta tsinana mini? Dame ka ƙare ni da shi banda tashin hankali, nikam da nasan cewa abin da aka haifa kenan gwara a zubar da kai tun kana ciki ma ya istigigari, ban hango ta inda zaka iya taimaka mini ba a rayuwa" ya yi ƙwafa ya fice daga cikin gidan, har ya yi nisa ya dawo ya ce "Saura na samu labarin ka je kaga yarinyar can ba, wama take da suna? Jaanah" Mutallab ya yi ta zama a wajan ya miƙe ya isa inda Ammo take ya ce "Barka da yamma" ta yi masa shiru ya yi ta tsaiwa can ya ce "Zan ɗaura miki" sai kawai yaga ta miƙe ta bar wajan shima ta fita zuciyarsa a raunace.

***Kimiyya ya shigo parlo yana murmushi ya kalli Jeddah dake zauna tana duba abubuwa, shigar alfama ce a jikinta kana ganinta ka san ba sai an yi magana ba irin manyan hajiyoyi ne wanda suka gama ganin dukiya da arziƙi kala-kala. Ya ce "Can ki Jeddah "

"No idea, ba zai shige maganar abokinka ba" Kimiyya ya zauna yana shafa kai ya ce "So, he is finally here" ya yi maganar yana nuna mata Mutallab da ya yi ƙiƙam a bakin ƙofar shigowa parlon. Jeddah ta ɗaga kai ta kalle shi, taga ai ya kerewa kimiyya a tsayi da jiki da komai, ta dubi shigar mafarautar dake jikinsa ya cake fuska ba yabo ba fallasa.

"Kai ba so ka ba, mene ya haɗaka da tsaiwa kuma? Come in; shigo ciki"

Kimiyya ya yi murmushi wanda baya barin fuskarsa ya ce "Bashi da yadda ne Jeddah" "Ok" kawai ta ce tana sake kallon Mutallab ɗin, a hankali ya shigo yana tafiya ɗaiɗai shi idan aka ce ya zauna tamkar an haɗa shi da aiki ne ya durƙusa ya ce "kina lafiya?"

"Allahamdulilah, shekararka nawa ne? Ni naga jikinka bai nuna mini shekarun da Kimiyya ke faɗa ba, kalle ka kamar ka goya shi?"

"Sai dai na tambayo"

"Baka sani ba? Where is your birth certificate?" Ya buɗe ido, Kimiyya ya ce "Takaddar haihuwa wai take nufi" Ya girgiza kai alamar babu, Jeddah ta ce "Ok, irin takaddar allurar da akewa yara suna jarirai?" Nan ma ya yi ta ce "Allah Alhakkamu, Kimiyya zai baka uniform, mun kammala komai, a makarantar za a ƙarasa abin da ba mu yi ba, the fee payable per annum is N300,000 per student, so har ka gama makarantar ba wani damuwa, ina fatan kuma ba za a yi asarar kuɗin tara ba ko?" Shi dai bai ce komai ba, yana kallon ƙasa banda yanayinsa ya fara sauyawa masifar girmamawa ta Mutallab ko haɗa ido ba zai da ita ba. "Jeddah shi fa kamar robot eh ne, yana da basira da gane abu"

"To ya batun exchange ɗin da za ku yi?" Ya ce "Na faɗa masa, Allah Jeddah idan ki kaga abubuwan da ya sani akan computer yanzu you'll be surprise za ki yi mamaki sosai" Ta jinjina kai ta ce "I like surprises, ina son abin mamaki"

Mutallab ya yi da ƙyar wajan faɗin "Na gode, Allah Ya amfana zuri'a"

"Yi wa kai ne ai"

Yin duniya ta ce ya tsaya bless ta Kammala abinci amma yaƙi, suka nufi part ɗin Kimiyya a tare suka dinga abubuwa Mutallab ya ɗauki abu ya saka a kunne ya yi shiru kamar daga sama cikin mamaki ya ji ya kutsa kai cikin wayar wasu da suke yi, ya janyo kujerar ya ɗauki abu ya sakawa Kimiyya, mamaki ya cika Kimiyya ya dinga kallon Mutallab sukai shiru kuma suna jin conversation ɗin mutanen wanda kamar haɗaka suka yi, da tsantsar mamaki Kimiyya ya ce "Mu faɗawa Jeddah"

"No, ka yi saving recording"

Kimiyya ya fara saving kamar yadda Mutallab ya ce, sukai shiru shi Mutallab ko a jikinsa, Kimiyya kuma gabaɗaya hankalinsa a tashe yake.

Da daddare Mutallab ya shirya cikin kayan da suka zame masa kamar suttura a yanzu, daman tuni iyaye sun fara jawa yaransu kunne a kan su fita sabgar Ɗan'malam, dama shi ba abokai ne da shi ba rayuwarsa kawai yake, abokinsa ɗaya TARIQ. Bayan ya isa ya yi tsaye a ƙofar gidansu Jaanah, ta fito ta tsaya bai kalleta ba, a yanayinta kawai ya san cewa bata cancanta da zama matar Moh ba, ba za a taɓa ganin Matar Moh haka ba. "Ina yini?" Ya yi mata shiru ta ce "Bawan Allah na fito an ce mini zance kazo wajena, na yi sallama shiru, na gaisheta shima shiru" idan gini ya motsa Mutallab ya yi magana.

Ta yi murmushi ta ce "Mazan fama kenan, su TAHHB manya"

"Tahhb?" Ya maimaita sunan a ran shi, ta ce "Ka mini kyau da suna Tahhb, na ji kuma na amince zan yi rayuwa da kai" bai sai mene ya ja ra'ayinsa da Jaanah ba ya juya kamar zai kalleta ya fasa. "Ta ce Sunana Fatymerh, amma ana kira na da Jaanah.....," ta fashi rayuwarta gabaɗaya abin ta manta ne kawai bata faɗa ba, Jaanah akwai shiga rai tana da surutu kamar taci naman aku ta kalle shi ta ce "Tahhb"

"Tahhab" ta sake kiran sunan shi a karo na biyu, bai amsa ta ce "An ce wai ka kashe Diyna, idan na amince da auren naka nima kashe ni za ka yi? Zan mutu?"

Ya juyo sosai, fara ce ita tas tana matsagaicin jiki kana ganinta ka san bata da kwanciyar hankali saboda kayan da suke jikinta. Ta yi murmushi sai kuma ta gyalgyale da dariya sosai har tana saka ta dafa shi, a lokacin hannunta zafi zau ta ɗauke hannunta ta ce "Afuwan, zazzaɓi nake yi ka ji hannuna zafi ko?"

"Tahhab, ni dai ko zan mutu ba komai, balle ba zaka kashe Jaanah ba, zan rayuwa tare da kai, kaima babanka ya mutu? Babarka ta mutu ne ko?" Bata tsammata ba, ta ga ya girgiza mata kai ta ce "Ayya na ɗauka baka da Mama da Papa, Tahhab zan aure ka" ya miƙe tsaye ya miƙa mata ledar hannunsa, ta amsa ta leƙa taga gurasa ce da nama ta saka hannu ta ɗauki naman za ta kai bakinta ya ce "Kamata" ta ɗago kai, taga wani waje yake kalla daban ta sake yin dariya ta saka naman a baki ta ji ya ce "Naman Gafiya ne...., ki shiga ciki Mutallab ya amince da auren ki"

[1/7, 9:35 PM] Sis Fauzy: Chapter 25: Jaanah

Jaanah ta ce "Da gaske ka amince zaka aure ni Tahhb? Kuma ba zan mutu kamar wacce zaka aura ta farko Diyna?" Ta yi furucin cikin roƙo da tausayawa, bai juya ya kalleta ba, sai ta ɗauka ko ya fasa ne? Cewa za'a yi mata aure, at her young age ya zama maɓudin tashin hankalinta, bayyana mata wanda zata aura, ma'ana Mutallab Ɗan'malam ya zama tambaya a cikin zuciyar Jaanah, ganin Mutallab tsaye gabanta matsayin wanda zai aure ta ya zame mata dukkan amsarta, ya share mata shakku da kokwanto."Idan ni zan wa kai na aure ba zan aure ki ba" ya yi shiru, ya kalleta da kyau kallo na daƙiƙo "Idan kuma yi mini za'a yi, Mutallab baya da wani zaɓi ok" "Na gane, na gode hakan ma" Jaanah ta ce tare da yin murmushi ta jingina da katangar dake gidansu, with different thinking running on her mind. Har ya shigewa ganinta bata bar wajan ba, kamar mai using magic haka ta ji zuciyarta tattara tare da tafiya wajan Mutallab, ta ji koma mene zata amince da shi. Bayan Jaanah ta shiga cikin gidan ta cigaba da aikin da take yi, Malam Umaru ya ce "Ya kuka yi dashi kuma?" Ta ce "Ya ce na faɗa maka ya amince da auren" Malam Umaru ya jinjina kai cikin jin daɗi ya ce "Madallah, gwara duka mu aurar daku ai ko hankalinmu zai yi ɗaya"

"Baba baka son ganina har haka ne? Ai aure bar Ubangiji ne haka malaminmu yake faɗa mana" Jaanah ta faɗa hankalinta kwance, shi kuma Baba ya ce "Ba shakka Jaanah ni kike faɗawa haka? Daman auren kike jira a yi miki kenan?" Ta ajjiye abin da take yi tare da yin jigum sai kuma ta ce

"Baba kai kace za ka yi mini auren nan, idan ban yi maka biyaya a duniya wa zan yi wa? Dole na yi maka idan ina son wanyewa da duniya lafiya, shine iya abin da zan yi na rabauta da lahira ta"

"Kenan murna kike za a yi miki aure? Daman abin da kike so kenan Fatymerh?"

"E, baba domin kai ma kana murna, ni na ji Tahhb ya yi mini" Jannah ta ce, tana lumshe idanunta ji ta yi kamar rana ɗaya ta zame mata shekara guda da sanin Mutallab, ta ji ta damuw da shi, ko idanunta ta rufe tsaiwar shi take gani cikin duhuwar idanunta, idan abin da ake kira shine so; tana matuƙar son Tahhb, soyayya mara adadi. "Anya Jaanah? Kina ta kuka bakya son auren har bulala na saka miki a jiki shine za ki ce haka?" Janaah ta fidda fararen idanunta waje sai kuma ta yi murmushi ta ce "Ya zan yi da ƙaddarar Jaanah? Labarin Jaanah ba zai cika ba sai da Mutallab Ɗan'malam" tana cewa haka ta miƙe ta shige ɗakin da take ƙwance zuciyarta ta fara haiƙo mata kanta a matsayin matar Mutallab.

Mutallab ne ya shigo cikin gidan bayan gari ya waye hantsi ya yi, Malam na kishingiɗe yana gyanyaɗi sai Ammo dake aikin sana'arta, Mama Zaituna ta yi jigum da hannu a haɓa. Sarai ta ji sallamar da ya yi amma ta share shi ya dire baƙar ledar hannunsa Malam ya buɗe idanunsa ganin baƙar leda ya saka ya miƙe zaune ya ce "Meye a cikin baƙar leda?"

"Ina kwana?" Mutallab ya ce yana durƙushewa a saman ƙafarsa, yana duban Malam ɗin, Malam ya ce "Ban kwana ba, mene a leda na ce maka wai? Kasan bana shiri da irin ledojin nan"

Ya dinga kallon Aby, yana jin inama ya ce Mutallab Allah Ya yi maka albarka,inama ya ce Mutallab meke damunka? Ko sau ɗaya ne ya bashi rana irin ranar da kowanne ke farinciki da iyayensa, ya yi hira da shi ƙila abin da yake danƙare a zuciyarsa ya wareware ya samu sukuni ko yaya ne, ya numfasa ya ce "Nama ne da kayan miyya". "Ko kai fa, idan kana haka ai lafiya lou zamu zauna da kai wallahi, ke ɗauki a sarrafa mana shi yanzu kin ji ko, sai ka basa kuɗi a siyo biredi" ya zame ya zura hannunsa cikin aljihu ya ɗakko dubu biyu ya bawa Malam. Yana washe bakinsa ya ce "Iyee farare har biyu?"

"Batun yarinyar Aby"

"Ka je ka ganta ko?" Sai ya jinjina masa kai, ya miƙe tsaye kafin ya ce "Ina da matsala, kar na dinga dukar musu yarinya"

Aby ya ce "Idan ka yi niya ka kashe ta kamar yadda ka kashe Diyna, ai na jima da sanin ɗan ta'adda na haifa, makami ne kawai baka fara ɗauka ba, ɗan'uwansa fir'auna yaro da zuciya a ƙeƙashe anya zaka wanye lafiya Muɗallabi?"

"Aby abin farinciki ne ka haifi ɗan'uwan fir'auna, ka yi mini duk bakin da za ka yi mini wallahi ko tsinewa Mutallab ka yi ba zan damu ba, duk masifar dana ɗakko tare zamu raba, idan ba ku yi cikina ba sai ku faɗa mini wanda suka, domin baku cancanta da zama iyayen Mutallab ba" Ammo ta juyo ta kalle shi, idanunta ya wani irin sauyawa, Mutallab ya kafe Aby da idanu yana jiran jin me zai ce, gwara ya faɗa musu sai su ɗanɗani irin ɗacin da yake ji a ƙasan zuciyarsa. Baki a sake Aby ya ce "Mu kake faɗawa wannan muna nan maganganun?"

"Nima ni kake faɗawa ɗan'uwan fir'auna ne ni, Aby kar ka fara sawa ina dana sanin zama a cikin Ammo, na ji daman tun ina ciki na sauya mahaifa zuwa na wata uwa daban...," kafin ya ƙarasa Ammo ta ɗauke shi da mari, ganin yaƙi matsawa ta ɗakko itace ta fara maka masa, ta mance da raunin kan shi, shi kuma ko motsi bai yi ba, ganin jini na zuba a kan nasa ya saka ta ajjiye itacen ta shige ɗaki tana goge hawayen idanunta, ganin yadda yake muzurai da manyan idanunsa ya saka Aby ya ƙi tankawa ya yi masa shiru ya ce "Ke Zaituna ɗauki ki dafa naman nan, yanzu zan fita nemo biredi" ta ce "To Malam" ya juya ya kalli yaran da suke zaune sun kafe shi da idanu ya ce "Zaku tashi daga nan ko sai na cicci gidanku?" jikinsu na rawa suka tarwatse daga taskar gidan, ya fice yana yin sababi kamar zai ari baki.

Mutallab yana zaune tsakar gidan, jinin kansa har ya gaji da ɗiga ya fara bushewa, aka gama dafa naman da komai aka rarraba yaran sai murna suke yaushe rabon da suci nama? Mama Zaituna kamar zata cire yatsun hannu haka ta dinga yi. Malam ya kammala ci ya yi gyatsa ya kalli MUTALLAB kan shi ke a ƙasa kamar wani basarake ya ce "Nama ya yi daɗi, ga zaƙi madalla ina ka samu nama haka da yawa?" Aby ya ce "Muɗallabi magana nake kana kunnen uwar shegu dani?"

"Point of correction Aby, Mai dawa sunana, nama kuma a dawa na samu shi" ya ce yana murza hular saƙin dake kan shi, hannunsa ɗaya riƙe da kokara. Aby was shocked, ya ce "Wacce dawar? Ba naman kasuwa bane?"

Mai dawa ya jinjina kai yana miƙewa tsaye tare da cakewa ya ɗaɗɗage girarsa biyun ya ce "Naman maciji, da Gafiya ne" yana faɗin hakan ya fice ya bar musu gidan, Aby ya juya ya kalli Mama Zaituna itama ta kalla shi, a kusan tare suka ruga da gudu zuwa bakin rariya, suka dinga sheƙa amai kamar zasu fitar da kayan cikinsu, tun suna yi da ƙarfinsu har jikinsu ya yi sanyi. Sa'adah data fito daga ɗaki domin yin wanka ta kalli yadda Malam da Mama Zaituna suna zube a ƙasa suna mayar da numfashi, Sa'adah ta juya ta kalli ƙanwarta Ikram ta ce "Ikram mene ya same su?"

"Na'am da Mutallab ya kawo ne ya ce musu na maciji ne da Gafiya"

"Auzubillahi...," sai kuma Sa'adah ta fashe da dariya, ta durƙusa tana riƙe ciki tare da yarfe hannunta tana faɗin "wayyo Allah cikina, daga cin naman sai amai kenan? Ke Ikram naman ba daɗi ne?"

"Akwai daɗi sosai, laaa kinga Malam yana gudawa" Ikram ta ce tana nuna Aby da yatsa, Sa'adah ta juya, exactly; kamar yadda Ikram ta ce gudawa ce ta kwacewa Aby ya numfasa da ƙyar ya ce "Zo zo nan Sa'adah taimake ni, zayo yana bina naman maciji azzalumin yaron nan ya bamu, ban yaf....," Sa'adah ta yi saurin cewa "A'a Malam, irin bakin da kake yi masa ne ya fara tasiri gashi nan ka fara gani, don Allah ka yi haƙuri kar ka furta wata magana bayan wannan" ta taimaka masa ya tashi,ya nufi bandaki yana shiga Sa'adah ta kwanta har da birgima saboda da dariya Ikram ma ta dinga dariya tana buga bokici Sa'adah data juya ta kalli Mama Zaituna a ƙasa tana numfashi sai ta sake fashewa da dariya ta ce "Naman maciji, gudawa wayyo ni Sa'adah".

Yammacin ranar Mutallab ya ji zuciyarsa na jan shi zuwa gare ta, kawai dai surutun yake son ji a cikin kunnuwansa. Ya juya ya kalli Kimiyya ya ɗan yi gyaran murya, Kimiyya ya ce "Maza suna ganin miskilancinsa a wajanka, ina ga mace Please?"

"Kamarya?" Mutallab ya ce yana sakkowa daga kan tudun da suke zaune, yana ɗan ya motsa fuska yana jin shi duk a takure kwana biyu ya ɗan saba da shiga dawa

cikin jeji. Kimiyya ma ya sakko ya ce "Kamar yadda ka ji, kana da ɗabi'ar shari'a da jijji da kai, a yi magana sai ka yi kamar baka ji ba" yana ɗan bubbuɗe idanu tare da ja da baya ya ce "Ni? Ni ɗin?"

"You, You ɗin. Ka sani ai idan ma haka ne ko akasin hakan"

"Lallai" Mutallab ya ce, yana jinjina kansa, da gaske bai ga wani shari'a ba bai san ya ake yin ta ba. Juyawa sukai suka fara tafiya kimiyyar ya ce"Akwai wata sister ta, Allah ya ɗora son wani bawan Allah to irin halinku ɗaya ne, yana da miskilanci,tana shan wahala sosai kasan ance miskilin mutum yafi mahaukaci ban haushi, itama kuma ta nace ka san halin soyayya ai" da rashin fahimta ya ce "A'a" Mutallab ya ce kimiyya ya yi dariya ya ce "Lokaci zaka santa ai" sun yi nisa a tafiya Mutallab nata tunanin abin da zai cewa Kimiyya, a hankali ya furzar da iska daga cikin bakinsa ta fidda hucin zafi a nutse ya ce "Aure take so su yi kenan?". "E mana, he loves him so much. Ba irin nacin da ba'a yi ma da faɗa amma ta nace daga nan fahimci soyayya ƙaddara ce, halitta ce a zuciya sai aka barta"

"Sunansa fa" Mutallab ya buƙata yana saka yatsa ɗaya a tsakiyar goshinsa a hankali yake murzawa ya zubawa gefe guda ido, suna cigaba da tafiya a haka. Kimiyya was so confuse, ya ce "Me za ka yi da sunan kuma Moh?"

"To bar shi"

Ya girgiza kai, ya zaro wayarsa a aljihu kiran farko ta ɗaga Kimiyya ya ce "My dear how are you, ya kike ne?" A can ɓangaren ta amsa shi, ya ɗora da cewa "Yama sunan wannan ɗan wahalar? Saurayin naki?" Ya tambaya tare da sauraren ta a fili ya ce "Haysam" sai kuma ya kashe wayar ya juya ya kalli Mutallab ya ce "Wai Haysam sunansa ta ce, akwai wani abu ne Moh?" Mutallab ya juya da rinannun idanunsa da lokaci ɗaya sukai ja, ya kalli Kimiyya dasu, sai bai ce masa komai ba. "Ina faɗa maka sunan nasa fa, wai Haysam kamar wani sunan tsuntsu" Mutallab ya sake juyawa ya kalli Kimiyya idanunsa a birkice ya ƙara yi masa shiru. Kimiyya ya cigaba da surutu, can yaga Moh ya dafe kansa yana furzar da iska "Friend lafiya kake ne? Ko akwai wani abu?"

"Ƙalau" Moh ya ce, sai kuma ya sanya hanyar inda za shi ya yi nisa da Kimiyya ya ce "Mu haɗu dare ko safe ok?"

Bai jira me Kimiyya zai ce ba ya yi tafiyarsa, Kimiyya ya girgiza kawai kawai yana jinjina miskilanci irin na Mutallab ɗin.

***Baba Umaru na zaune a tsakar gida shi da matarsa suna tattaunawa, Jaanah na ɗaki ta yi shiru,tana tunanin ko dai ya fasa auren nata ne? Shi ya sa bai ƙara zuwa inda take ba? A hankali ta miƙe zaune saboda kiran da aka yi mata, kanta ko ɗan kwali babu ta fito ta ce "Gani Baba?" Baba ya dube ta ya ce "Ya ake ciki ne?" A hankali ta ce "To bai sake zuciya ba" Baba ya numfasa ya ce "Ko ke za ki gidan nasu kin ji lafiya?" Ta yi saurin girgiza kai, Allah Ya yi wa Jaanah kunya ta kasa cewa komai. Baba na shirin magana yaga inuwar mutum tsaye a kan shi bata ko motsi, ya ɗan razana ya juyawa yana salati sai kuma ya hangame bakinsa ganin wanda yake tsaye.

Jaanah ta juya suka haɗa ido dashi ya yi tsaye a tsakar gidan hannunsa ɗaya riƙe da leda ɗayan kuma ba komai sai zura shi da ya yi a cikin aljihun rigar ya kafe Jaanah da ido, gashinta sai motsi yake kasancewar tana da yalwar suma har gaban goshi, sun jima suna kallon juna kafin ta yi ƙoƙarin zame idanunta ba dan zuciyarta ta gaji da ganin idanunsa ba, ta ji nutsuwa ta saukar mata sai kuma kunya ta lulluɓe ta. Baba Umaru ya ce "Ikon Allah, to haka ake zuwa gidan mutane ba ko sallama?" Ya ce yana miƙewa tsaye tare da kallon Jaanah ya ce "Shige ɗaki Jaanah"

"To" ta miƙe ta nufi hanyar ɗakin gani ta yi Mutallab ya biyo bayanta ta ɗan tsaya shima ya tsaya cikin faɗa Baba ya ce "Ya zaka bita ɗaki? Waje zaka koma"

Mutallab, ya juya gabaɗaya zuwa inda baba yake suka kalli juna sai ya zame idanunsa ya kalli Jaanah dake wasa da yatsun hannunta ya ce "Sai na yi me a waje? Wajanta na zo ai". "Daka zo wajanta sai ka bita ɗaki saboda hauka ake yi? Ko haukan naka ne ya motsa iyee? Ai na ji labarin dalilin haukan ake so a yi maka aure, kawai ka faɗo mini gida babu ko sallama, kuma ka bi yarinya cikin ɗaki bayan tsakanin mace da namiji na uku shaiɗan ne, idan ya zance kazo ka tsaya a waje yanzu zata fito" ya ƙare maganar cikin faɗa.

"Wani abu ne zai faru idan na bita ɗakin? To ta fito wajan haka"

"Baka san mene zai iya faruwa ba kenan idan ka bita ɗakin, Jaanah ai ba namiji bace haka kawai zuciya ta ribace ka a kan ɗiyata? Ka je wajan yanzu zata fito"

Mutallab ya ce "Sai na yi me idan ta ribacen? Muje" ya kalli Jaanah yana faɗin haka. "Bari na sako hijabi to" ya kafe ta da idanu, ta yi saurin juyar da kanta gefe ya koma gefe ya tsaya baba ya yi cikin ɗaki ganin Mutallab bai da niyyar fita daga cikin gidan nasa. Hijabin ta sako ta dawo tsakar gidan tana murmushi ta tsaya sai kuma ta durƙusa ta ce "Ina yini?" Ya yi shiru, ya dinga kallon ta bai ce komai ba. Ta ce "Ganina kazo yi? Nima da tunaninka na kwana a zuciyata Tahhb, ina fata ba sauya ra'ayinka ka yi a kan Jaanah ba ko?" Hannunsa mai ɗauke da ledar ya miƙa mata ta saka hannu biyu ta amsa ta buɗe ciki, kamar wancan karan nama ne da gurasa amma wannan ta fasa mene kamar tsuntsu ne haka aka gashe shi ga fika fikinsa nan.

"Jaanah yʻar gatan mijinta, duk ni ɗaya ne Tahhb?" Jin ya mata shiru ta sake cewa "Ka zauna muci ko?" Ta ce tana juyawa ta ɗakko faranti ta dawo tare da jan kujera ta zauna, ta juye gurasar a ciki da naman ta ce "Ka zauna mu yi hira mana, daman tun safe ina ɗaki" ya yi ƙiƙam sai kuma ya durƙusa daidai inda take, har yana jiyo numfashinsa ta tura masa farantin naman ta ce "Ci, ka rage mini" ba shiri ta ɗauka ta fara ci ta lumshe idanunta ta buɗe

"Naman mene yau aka samu a dawa? Wannan bana gafiya bane"

"Yʻar shila" ya ce yana duban yatsun ƙafarta duba na tsanaki, wanda data san me yake kallo data gudu ɗaki ko ɓoye ƙafarta. Ya miƙe ya juya ya nufi hanyar waje

"Tahhb, Tahhb....," Jaanah ta ce tana biyo shi da ɗan gudu ya tsaya ta ce "To baka ce komai ba" ya dube ta sai kawai ya fice daga cikin gidan ya nufi hanyar nasu gidan wanda yake jin kamar ana masa farraƙu da zaman gidan iyayen nasa.

A tsakar gida ya samu Sa'adah ya zaune shima bayan ya ɗan kaɗe wajan ta ce "Na Ammo daga ina haka?" Bai kalle ta ba ya ce "Kin aike ni ne Yaya?" Ta ce "Ah ah, na dai damu ne ban ganka ba, babu Bafullatana ba Anty Hameeda ba Muneeberh gidan ya yi mini faɗi, kai kuma ba'a hirar abin arziƙi da kai ko zaman gidan ba ka yi" ya mata shiru ta ce "Abin da ka yi baka kyauta ba, Na Ammo iyaye ba abin wasa bane kullum albarkar su muke nema, ba zamu taɓa biyansu abin da suka yi mana a gidan duniya ba, ko zaka goya Ammo ko Malam a baya tun daga nan garin Kano,

unguwar Birget ka kai shi Makka a ƙasa wallahi baka biya ladan haihuwar da suka yi maka ba, rayuwa na tattare da ƙalubale mu yi musu uzuri don Allah"

"To, wa'azi kike mini kenan Yaya?" Ya ce yana naɗe ƙafa tare da yin zaman da ya saba na tanƙwashe ƙafafuwansa waje guda ya ɗora hannunsa a saman cinyoyi. Sa'adah ta ce "Wace ni tinatarwa ce kawai na yi maka ita"

"Uhmm".

"Ka je ka basu haƙuri har Mama Zaituna, a dinga sanyaya ruwan sanyi ana shan ragowar ruwan alwalar sallar asar Tayo" ya yi kicin-kicin da fuska can ya miƙe ya nufi wajan Malam ya ɗaga balulen ya hango Aby ƙwance sai ya shiga ya durƙusa,ya jima a zaune kafin ya ce "Aby" malam ya ɗago kai ganin Mutallab ya saka ya yi shiru. "Na yi laifi ka yafe mini Aby, ka daina aibata ƙuruciyata baka san ya girmana zai kasance ba, ka yafe mini" Malam ya yunƙura ya ce "Ni wai? Na yafe maka na shiga banɗaki ba adadi, Allah Ya isa Allah Ya isa abin da ka yi mini zaka gani" Mutallab ya miƙe ya fita rai ɓace yana zuwa ƙofar gida yaga Kimiyya tsaye. Sai kuma ya juya zuwa ɗakin zaure.

Kimiyya ya dinga kallon ɗakin da Mutallab ke rayuwa ya miƙa hannu zai taɓa wani buzu ya ji ya ce "A'a, ba ruwana"

"Gani to, amma wannan ɗakin na lafiya ne haka Mutallab? Waɗannan abubuwan fa? Wancan ɓangaren dana kayan fulani kala-kala fa shi na mene?"

"Quiet, sunan ma?"

"Haysam"

"To yana da aure ai, har ma da raya wallahi".

Da mamaki Kimiyya ya kalli Mutallab kafin ya ce "Tab, bangane ma'anar yana da aure ba? Ya aka yi ka sani?" Banza Mutallab ya yi masa yana cigaba da abin da

yake yi. Kafin ya ce "Za ta yi auren nasa, ita yar uwar taka". "Ka ce yana da aure har da yara kuma ka ce zata iya auren nasa ban fahimta ba"

"E, akwai rabo a tsakani da kuma ƙalubale haka alƙalumma suka nuna" Kimiyya ya numfasa ya ji ya fara tsoron Mutallab a ran shi, amma soyayyarsa ƙara yawa take a zuciyarsa "Tsafi kake yi kenan Mutallab, ba kyau fa"

"Jini ka gani ko jarirai"

"Bokanci kenan? Kimiyya ya faɗa a raunace cike da damuwa don bai ji daɗin hakan ba. "Zan baka sirri daga cikin Alkur'ani ka bata ta yi da zuciya ɗaya, sirrin jefa soyayya a zuciyar wanda kake tsananin so, wallahi wallahi ko waye a duniya muddin ka yi masa sai ya ji babu wanda yake so a duniya sai kai, amma kar a yi domin cutar da wani, Mutallab bai lamunta ba, wannan sirrin ga wanda suke cikin jarrabawar soyayya ne ok" Kimiyya ya jinjina kai ya ce "To zan faɗa mata"

"Mene sirrin?" Kimiyya da ya buƙata, har lokacin kuma Mutallab bai haɗa idanu da Kimiyya ba tun shigowarsu ɗakin.

"cikin dare zata tashi ta yi lafila raka'a biyu, ta yi miftahul amàl, sai ta karanci ummul kitahhb, fatiha keman ƙafa 113, ana fara aikin ranar Lahadi, Litinin, Talata, kwana uku ake yi. Bayan ta yi sallah tana kallon alƙabila za ta yi karatun, sai kuma ta yi woridin Ya-ƙahharu ƙafa 113 shima sai salatin fatih 113 shima, shine abin da za ta yi washegari da safe ta yi sadaƙa ta wainar gero"

Kimiyya kallon Mutallab kawai yake yi kana ya ce "To mene sadaƙar?". "Ka jira ta yi"

"Amma ba kyau"

"Na sani, ai ba'a shiga dawa don ƙarya ka kalli komai ka yi shiru. Me ya sa kake wasa da sallah?"

"Ni kuma?"

"E, kai ɗin sallah bata dame ka ba, zan yi faɗa abubuwa da yawa game da kai sallar ce mai muhimmaci ka gyara ka ji" yana cewa haka ya miƙe ya fita daga cikin ɗakin, kunya ta kama Kimiyya da gaske bai damu da yin sallah a kan lokaci ba. Bayan sun fito sun waje ya ce "Monday ne zaka fara zuwa makaranta, are you ready?" Mutallab ya jinjina kai, suka koma can waje guda suka zaune Kimiyya kaɗai ke yi masa shiri shi dai jinjina kai kawai yake domin ji ya yi bakinsa na yi masa ciwo. Yana daga inda suke ya hango Sa'adah na zance ganin tana ta murmushi saurayin na dariya kamar ba namiji ba ya ji ransa ya ɓaci sosai, yana kuma nan ya hango wasu masa biyu da Malam Umaru da Aby ya taɓe bakinsa.

Jaanah.

Sanda ta biyo bayan Mutallab tana faɗin "Tahhb, Tahhb...." Ta faɗa ne a lokacin ba tare da tunanin zai tsaya ɗin ba, ita kuma zuriyarta ba zata jure ba, ta sauke ajjiyar zuciya tana dafe ƙirji ganin ya tsaya, ta ji kamar ta ƙarasa gabansa ta kama hannunsa ta ɗora a ƙirjinta ko hakan zai saka ya ji yadda zuciyarta ke bugawa, tana bugawa saboda shi, tana bugawa saboda soyayyarsa, tana bugawa ne saboda yadda ya yi tsaye a gabanta. Ta langwaɓar da kan ta ta ce "To baka ce komai ba?" Yadda ya juyo ya duba ta, sai ya ji zuciyarta na tarwatsewa ƙirjinta na buɗewa, ta yi waiting to hear from him sai kawai taga ya fice. Jaanah ta fi bayan Mutallab da kallo, ta sulale ƙasa a nan inda take, ta jima kafin ta shiga gida da tunanin Mutallab maƙale a zuriyarta.

Duk motsin da take yi shi take ji yana mata yawo a tsokar ƙirjinta. "Jaanah" Baba ya kira sunanta ta amsa tana miƙewa zaune ya ce "An saka ranar ɗaurin auren ku, gobe da maraice a kawo kuɗin sadaki yanzu mahaifin Muɗallabi"

"To Baba" ta ce a raunace hawaye na bin idanunta ya ce "kukan na mene kuma Zarah?"

"Baba me ya sa kake son aurar dani ne?"

Zama ya yi yana kwantar da muryarsa ya ce "Ba komai Jaanah, rayuwa ce ta yi tsada tun bayan rasuwar iyayenki nake ta fama yanzu ƙarfina ya ƙare idan na aurar dake wani nauyin zai sauka a kaina" tana kuka ta ce "Shekaruna 14 baba, aurar dani shine mafita? Shikenan na amince amma ina dukiyar da aka mutu aka bar

mini?" Jikin Baba na rawa ya ce "Wacce dukiya? Waya faɗa miki na sake jin wannan maganar sai ranki ya yi mugun ɓaci Jaanah" fashewa ta yi da kuka sosai, tabi Baba da kallo har ya fita waje. Ta yi kuka son ranta a lokacin an yi sallar magariba ta saka hijabi ta saka takalmi ta nufi inda zata samu Mutallab.

Yana zaune a waje kamar koyaushe shi kaɗai ya hango ta, ya yi ta kallon ta yana mamakin ina zata? Sai yaga ta nufo shi, tana zuwa ta durƙushewa a gefen ƙafafuwansa ta fashe da kuka mai raunata zuciya. Ya yi shiru don bai san me zai ce mata ba, ganin kukan ba mai ƙarewa bane ya saka ƙafa ya zungure ta, yana miƙewa tsaye ta miƙe tana kare fuskarta ya dinga kallon ko'ina yaga ba mutane ya yi ƙasa da murya ya ce "Mee?"

"Baba ya ce an kawo sadakin auren mu ɗazo" sai ta kuma fashe masa da kuka jikinta har rawa yake, ya bubbuɗe idanunsa yana dire kokarar hannunsa a ƙasa, bunjimar rigar farautar dake jikinsa na kaɗawa.

"To, shi ne na kuka?"

"Na tuna abin da malam ya ce ne, idan an yi musamman ƙanan yara masu ƙarancin shekaru wai ana samun yoyon fitsari idan akai tarayya tunda shekarun basu kai ba, kuma idan yarinya ta samu ciki zata iya mutuwa, kaga shekaruna 14 fa"

Ya bubbuɗe manyan idanunsa da tsoro shima ya ce "To! Mun shiga uku, kar mu yi yoyon fitsari to" ya faɗa cikin nutsuwa da alamun gaskiya cikin maganarsa.

"To ai kai namiji ne, ni ce zan samu cikin ai kuma ni ce ƙarama"

Ya ce "Ni kuma nine mai yin cikin ai, shekaruna 14 nima"

"Innalillahi yaya za mu yi, ashe da gaske malamin ƙawa'idi yake?" Ta sake fashewa da kuka tana girgiza kai, ya matsa dab da ita ganin kamar zata fita hayyacinta ga dare ya yi, ya duƙa fuskarsa daidai tata ya ce "Jaaa...."

Ya kira sunan nata, ta ce "Jaanah ne sunan ai" "Oh... Da gaske ban isa bawa mace ciki ba, ni tsoro nake ji kije gida ba abin da zai faru ko?"

"To ba za ka yi mini cikin ba? Ƙawayena sun ce idan aka biya sadaki wai amarya na biya"

Ya dinga kallon ta, da gaske suka su biyun shekarunsu sha huɗu, amma ƙuruciyar Jaanah ta girmama. Ya numfasha ya ce "To za ki biya ni sadakin kenan yanzu?" Taƙi magana ta dinga kuka tana diddire masa ƙafa ya sake matsawa kamar zai kama hannunta sai ya fasa, bai tsammata ba yaga ta ɗora kanta a gefen ƙirjinsa ta fashe da wani irin raunataccen kuka, bai ce mata uffan ba ta dinga kuka hawayenta na jiƙa masa riga, da gaske yana son ce mata wani abu amma ba zai iya ba. Ta janye kanta a hankali ta ce "Zan je gida"

"Hmmm" ya ce tana kallonsa sai ta juya tana share hawayen idanunta shima ya juya mata baya zai tafi gida, ƙarar sautin muryarta ya ji a kunnensa, tana kiran sunansa, ya ji kiran ya sauka har ƙasan zuciyarsa, da sauri ya juyo wani irin sandarewa Mutallab ya yi ganin yadda Jaanah ke salati tare da ihu wuta na cin jikinta, cin bana wasa ba, wuta ce wacce kamar gas ya kama haka take ci a jikin Jaanah.

[1/7, 9:35 PM] Sis Fauzy: Chapter 26: Who are you

Paid book #500

Pay before you read 08164069385

Follow on Arewabooks

Not edited

Jaanah was screaming, tana ihu da salati lokaci guda tare da kiran sunan Mutallab,wutar na ƙara cin naman jikinta. Mutallab ya yi cak idan akwai abin da ya tsayar da tunaninsa waje guda, ƙwaƙwalwata ta daina moving ƙirjinsa ta daina bugawa shine ganin Jaaanah na ci a cikin wutar, and he can't do anything to help her. Wani irin mazari jikinsa yake kamar ana kaɗa masa ƙahon gangi cikin azama ya ƙarasa wajanta daidai lokacin ya daina jin sautin fitar muryarta, yana ƙoƙarin cikin wutar ya bata kariya da gangar jikinsa ya ji an yi saurin janye shi. "Ina zaka? Cikin wutar zaka shiga? Kar a kwashi gawa biyu domin ita kam ta riga data rasu sai haƙuri" Mutallab ya juya ya zubawa Kimiyya idanunsa da suka koma launin rawa-rawa kamar bana mutum ba, yadda ƙirjinsa ke rawa haka haka gangara jikinsa ya kasa furta komai a lokacin mutane har sun fara taruwa, maganar ta isa kunnen Baba Umaru sai gashi da sauri yana kururuwa.

"Ya kashe mini yarinya, ya kashe ta jama'a a taimaka mini kaico, wayyo Zaraha'una wayyo Jaanah" kuka yake da ƙarfinsa mutane suna riƙe shi, lokacin wutar ta mutu dalilin ruwan da aka sheƙa mata, sai dai Jaanah rai ya yi halinsa, she died with smile on her. Baba ya ƙanƙame gawar Jaanah da jini ke zuba wajan wutar da ta ci "Allah Ya ɗaiɗaitaka in sha Allah a rayuwa ba zakaga daidai ba, ba zaka taɓa yin farinciki ba, ka kashe mini marainiyyar Allah" ya girgiza kai sai ya kuma rushewa da kuka ya ce "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, wanne irin zalunci ne wannan? Wanne irin rashin imani ne, lafiyar Allah yarinya ta fito ashe wajanka ta zo shine ka kashe ta kamar yadda ka kashe matar da za'a aura maka ta farko? Kenan yanzu duk yan'matan unguwar nan sai ka kashe su?"

"A'a baba bafa shi ya kashe ta ba, tsautsayi ne kuma lokacinta ne ya yi kamar kowanne mumuni" Kimiyya ya faɗa a raunace idanunsa kuma akan Mutallab ganin jikinsa har yanzu rawa yake yi, ya kafe gawar Jaanah da idanunsa.

One by one kuwa ya dinga gabatar da kansa, Kimiyya ya miƙe ya gabatar da kansa, ya kalli ta kusa da shi da take duba littafi sai harhaɗe rai take yi a hankali ya ce "Dear, ke ake jira" ba tare data ɗago ba ta ce "Jira, for?" Ya ce "Gabatar da kai" ta ɓata fuska har sai da Uncle John ya sake magana ta miƙe ta ce "Safiyyerh.... Sunana"

"Safiyyerh....?" Mutallab ya nana a zuciyarsa, sai kuma ya kalli Parrot ɗin kusa da shi yaga ta miƙe tsaye tana goge idanunta. Uncle John ya ce "Uhm sai ke"

Muryarta a hankali ta ce "My name is Safiyyerh Abdu." Da mamaki Uncle John ya kalleta, sai kuma ya sake kallon yarinyar dake bayanta ta kusa da Kimiyya

"You Safiyyerh, itama Safiyyerh, ke Safiyyerh Abdu ko? Ke kuma?" Ya faɗa yana nuna ta kusa da Kimiyya ya ce "Safiyyerh waye?" Kai tsaye ta ce "Safiyyerh Abdu....

Not edited □□□

Mutallab

Paid book

Pay before you read

08164069385

[1/7, 9:35 PM] Sis Fauzy: Chapter 28: A phone call

Kusan Mutallab ya riga ta zuwa da wuri, bayan ya shigo ya zauna ta shigo hannunta riƙe da bag, ta zauna a desk ɗin da yake bayansa, amma daga shi har ita babu wanda ya lura da wani. Da tsananin mamaki Uncle John ya ce "So we have two different Safiyyerhs in this class, wanda suke amfani da suna ɗaya, kuma suna amsa sunan mahaifi ɗaya, wonderful; abin mamaki" Uncle John ya furta yana jinjina kansa, duk da rashin kasancewarsa musulmi bai yi mamaki da hikimar Ubangiji ba. Ya dubi Safiyyerh ta kusa da Mutallab, ya sake duban Safiyyerh wacce take baya kusa da Kimiyya ya bubbuɗe idanunsa ya ce "Idan an samu first name, da surname dole iri ɗaya a middle name dole a samu bambanci, mene sunan kakanki first Safiyyerh?"

Ya nuna Safiyyerh da har yanzu take murza idanunta, ta ɗan ƙifta su sai kuma ta watsa hannayenta irin bata sani ba can ta ce

"Safiyyerh, just call me Safiyyerh Abdu....."

"Abdu wa?" Ta girgiza kai alamar bata sani ba, sai ya jinjina mata kai ya ce "Second Safiyyerh fa? Mene sunan grandfather ɗinki?" bayan ta ɗago kanta ta zubawa Uncle John idanu ta dinga kallonsa ta kasa magana, Kimiyya ya yi ƙasa da murya ya ce "Me ya sa kike yin haka ne?" Ta ware idanu bata kalli Kimiyya ba, tana dropping pen ɗin hannunta a desk chair ɗin ta ce "To ya yake kallona haka? Ban gane ba, me kuma zan ce?" Kimiyya ya ce "Ke da Safiyyerh kuna amfani da suna ɗaya hadda na mahaifi, to yadda za'a gane ku yake nufi ki faɗi sunan kakanki" ta sake juya masa idanu ta ce "Wanda ya haifi babana?"

"Shi, haka nake nufi"

"Oh, Safiyyerh Abdu nake amfani da shi, a gida ma Safiyyerh ake ce mini, friends and family duka Safiyyerh Abdu ne..... Amma zan ke amfani da wani sunan, Aafiyyah" John ya ce "Aafiyyah?" Ta jinjina masa kai ya ce "Ok, yanzu mun

bambance akwai Safiyyerh Abdu akwai Aafiyyah Abdu, next person please?" Ya faɗa yana nuna Mutallab da ya jingina baya ya harɗe hannayensa a ƙirji idanunsa buɗe ya zubawa yatsun Safiyyerh idanu a rashin abin da zai kalla, zuciyarsa sai ruɓanya aikinta take yi yana jin kansa daban a cikin sauran ɗaliban. Ta yi ƙasa da murya bayan ta leƙa fuskarsa ta ce "Bestie Uncle John yana magana"

Zame hannunta da ta yi, ya saka Mutallab lumshe idanunsa ya buɗe sai a lokacin ya yarda yatsun hannun nata yake kallo, bai kalleta ba kamar mai avoiding haɗa idanu da ita haka ya juya ya kalli Uncle John da yake cewa

"Mene sunanka"

"Mu....," Uncle John; ya dakatar da Mutallab wajan cewa "Ka miƙe tsaye kamar kowanne ɗalibi ka ji?" Mutallab baya son hayaniya da son a dinga nanata masa magana, gently ya miƙe tsaye yana zuba hannunsa cikin aljihu fuskarsa ba yabo babu fallasa ba kuma a gane yanayin da yake ciki, domin babu wani mood akan fuskarsa da zai iya fasallata halin da zuciyarsa take ciki ya ce "Muhammad Mutallab Abdullahi" slowly slowly ta ɗago idanunta ta kalle shi, tun daga ƙafafuwansa da suke ƙasan desk, har zuwa yanayin yadda zuba hannunsa a cikin aljihu, ta kai dubanta ga faffaɗan ƙirjinsa daya ɗan ɓalle gaban rigar, ta juya idanunta lokacin da ganinta ya sauka akan fuskarsa da take baƙa, she can't describe abubuwan da idanunta suka gane mata, nan da nan gudun da zuciyarta ke yi mata ya ƙaro cikin sauri ta ɗauke kanta tana taɓe fuskarta.

Kamar ya san cewa kallon shi ake yi ya cuccure girarsa waje guda, ya shigar da lips ɗinsa na ƙasa cikin baki wanda ya riga ya zame masa jiki a hankali ya koma ya zauna, sai kuma ya ɗago kansa jin ana cewa "Muhammad ko Mutallab wanne zamu dinga cewa?" Maganar ya fito daga cikin bakin wani ɗalibi, yaƙi magana sai Safiyyerh ce ta ce "Ku kira shi da Mutallab haka sunan yake" kasancewar subject ɗin maths ne ya saka aka fara yi musu rubutu, kuwa yana yi amma shi yana kallon rubutun Uncle John yana lissafa su a kan shi tas, ita kuma ta zubawa fuskarsa idanu musamman lips ɗinsa tana mamakin abin da yake jin idan ya yi hakan.

Bayan kammala karatu Uncle John ya rubuta class work kuma nan da five minutes zai amsa, Safiyyerh tattaro dukkan abubuwan da suke cikin kanta idan ta yi calculating sai taga ba daidai ba, lokaci guda duk ƙoƙarin da take da shi a maths ɗin ya gudu, tare da yin hijira daga cikin ƙwaƙwalwarta, ta ji ta zama empty head bata

fahimtar komai sai bugawar da zuciyarta take yi, tana doka mata da ƙarfi ta cikin ƙirjinta ta zama wata irin uncomfortable ta ji kamar bata taɓa sanin ma'anar 1 ba balle 2, littafin ma wani irin duhu yake yi mata a cikin idanunta, a hankali ta ajiye biron hannunta ta ɗora kanta a desk ɗin ta lumshe idanu, zafin da ta ji a saman fuskarta ta fahimci kuka take, irin kukan nan mara sauti kuma mai cin zuciya.

"2 minutes left"

Uncle John ya faɗa, wanda ya sanya Safiyyerh ɗago kai, a hankali kuma ta fara rubuta abin da take tunanin daidai ne daya zama amsar questions ɗin.

Da an gama class work ɗin sai fita breakfast, lokaci ɗaya suka fito a tare, bai ko kalli inda suke ba ya je ya yi dropping, Aafiyyah ta haɗe fuska sai kuma ta a ajjiye nata ta koma wajan zamanta, sai da kowa ya kammala kafin Safiyyerh ta miƙe ta isa wajansa ta bashi za ta juya ya ce "Safiyyerh Abdu....."

"Come back, zo nan Safiyyerh" ya faɗa cikin ɗaga murya. Yana cilla mata ya ce "Mene wannan ɗin?"

"Answers.... Na yi answering duka tambayoyin Uncle"

"Ok na gani, shige ki zauna"

Ta juya, haushi ne ya cika Uncle John ya kasa yi mata faɗa ma, sai kawai ya fice daga cikin class ɗin. A hankali kowa ya fara fita ya rage daga Safiyyerh sai Mutallab, sai kuma Aafiyyah data zaro wayarta hankali kwance tana dannawa. Kimiyya ya ce "My crush lafiya bakya zuwa makaranta kwana biyu, sai na ji kamar duniyar ce zata rikito mini zuwa kai na.... To Allahamdulilah yau dai kin zo zan samu sukuni acikin zuciyata amma da kamar mara lafiya haka nake jina" Ta harare shi bayan ta miƙe tsaye ta ɗauki lunchbox ɗinta, Kimiyya ma ya miƙe tsaye bai ko kalli Mutallab ya yi waje abinsa, har Aafiyyah za ta fita ta ce "Congratulations dear"

"For....?" Safiyyerh ta tambaya.

"Happy birthday" cewar Aafiyyah.

"Oh ba ki manta ba, thank you ya hanya kuma? Kin dai yi niyyar zuwa makaranta yau ko namesake?" Aafiyyah ta ɗan shagwaɓe fuska a hankali ta ce "Ya birthday partyn?"

"Daddy ya fasa, Wahee ta haɗa mini sharri" Aafiyyah ta lailayo wata ashar ta yi ta ce "Wannan na sha faɗa miki bata da hankali fa, kike zuba mata idanu watarana sai ta yi miki abin da ba ki taɓa tunani ba, kinga ni wallahi ko waye baka isa ka taka ni na rabu da kai ba, i skipped that level, idan kuma ba ka yi mini komai ba babu ruwan kallo da gajiya, ki rufe idanu ki ci ubanta sai ku zauna lafiya, yar abu ta kaza kaza, ƙazama irin ta ma" Safiyyerh tana buɗe ido, haɗe da dafe ƙirji ta ce "Daddy sai ya dake ni idan na yi haka". Siririn tsaki Aafiyyah ta yi ta ce "Sai ki ce aljanu ne suka buge ki, ba kisan kin yi ba ko?" Murmushi kawai Safiyyerh ta yi ta ce "Ke dai kawai masifa kike ji da ita yau, Aafiyyah meet my friend Mutallab, bestie na ne" ta faɗa tana nuna masa Aafiyyah dake tsaye a wajan.

"Bestie ga Safiyyerh my namesake, domin ka fi ganewa ka ce mata Aafiyyah "

Maimakon ya amsa, sai ya miƙe tare da zagayawa ya bar ajin daman basu yake kallo ba, takaici ya cika zuciyar Aafiyyah ta tsani jisgi ƙwarai, ta tsani wulaƙanci tabbas, ta tsani nuna mata bata isa ba zahiri, nan da nan ta ji idanunta ya cika da hawaye da sauri ta haɗiye su, ta kalli Safiyyerh dake cewa "Ki yi haƙuri ko bai ji ba" harara kawai Aafiyyah ta watsawa Safiyyerh sai ta koma wajan zamanta ta fasa fita gabaɗaya. Safiyyerh ta miƙe jikinta a sanyaye ta yi waje tana jujjuya da idanunta tana jin zuciyarta a dunƙule waje guda a ƙirjinta. A can ƙasan wata bishiya ta hango shi zaune saman kujera, ya ɗauki ƙafarsa ɗaya ya ɗora a saman kujerar ya miƙar, a hankali kuma ya buɗe gaban rigarsa domin duk a takure yake jin kansa, tun kafin ta ƙarasu ya san cewa ita ce ya kame fuska ta yi sallama a nutse ta zauna ta ce "Abin da kake yi ba kyau fa, ka share Aafiyyah" jin ya yi mata shiru ta rausayar da kanta zuwa gefe kafin ta ce "Rayuwa ba zata taɓa tafiya daidai kana tare da mutane ka ce ba zaka kula su ba, wannan ba halin musulmin ƙwarai bane ba, Allah da kansa ya karrama Ɗan'adam domin mutum ne mai daraja da kima, babu riba a wulaƙanta jinsin mutum wala mace wala namiji, ka yi abota za ka yi farinciki zuciyarka za ta yi fari, ka yawaita magana da nishaɗi zaka rabauta da samun nutsuwar zuciya, mu fa duka yan'uwa juna ne" ta washe masa fararen haƙoranta da suke a jere.

He just staring at her, her face, listening to her voice kamar mai jin maganar na sauka a kansa, sai ya yi shiru. Har lokacin kallon ta yake yi. "Thinking of me, me ya sa na fiye surutu ko?" Safiyyerh ta tambaye shi tana dariya, ta sake cewa "Zan iya cankar yaranka, muga, idanunka suna nuna wani abu, suna faɗar wani abu" ta sake yin murmushi ta ce "Got it, Yaruba boy bari na yi maka addition da Fulani, idanunka Yaruba and Fulani yake faɗa mini" ta gyara zama ta shiga fito da chocolates ɗin jakarta, ta fito da breakfast ɗinta ta ajjiye a gabansa.

Without looking at him ta ce "Mayya kake ce mini ko bestie? I know, na ji zuciyata ta faɗa mini"

E, da gaske mayya ya ce mata a daidai lokacin ya kuma ji mamakin yadda akai ta gane, ta ɗago kai ta ce "Ina da wayo fa sosai, daddy yana yawan faɗa mini hakan...," a daidai wannan lokaci a tsakanin da suka gitta abin da Safiyyerh ta manta ne kawai fata faɗa masa ba, labarin gidansu da jama'ar gidan komai da komai sai data faɗa masa. Ta ce "Ni dai ko za kana zazzaro mini sexcy eyes ɗinka na yarda, kai ne bestie na kuma kai ne" shiru ta yi lokacin data ɗago kanta idanunta ya sauka a cikin ƙirjinsa dake buɗe, da chocolates ɗin bakinta da yawon da ya cika bakin gabaɗaya suka shige cikin maƙoshinta ta fara tari sosai har lokacin kuma ƙirjin nasa take kallo, shima ya cake a gabanta baya ko ƙifta ido.

Suna zaune Kimiyya ya ƙarasu, ya kalli Safiyyerh ya ce "Budurwar Captain, ki je Uncle John na kira" gabanta ya faɗi ta sha jinin jikinta, sai kuma ta miƙe ba tare data ɗauki komai a wajan ba. Bayan ta bar wajan, Kimiyya ya nemi waje ya zauna ya ce "Ashe ka zo makarantar kenan"

"Na koma ne?" Mutallab ce a hankali yana zaro ɗan kuttun da yake kunna hayaƙin ƙarfe a ciki "Na ji mamaki ne duk da abin da na faɗa maka ba ka yi zuciya ba" yana busa hayaƙin kai tsaye idanunsa akan Kimiyya ya ce "Wani abu?". "A'a mu bar maganar ya shige, ya kamata ka daina kula Safiyyerh saboda zama lafiya" da mamaki Mutallab ya dinga juya sunan Safiyyerh kafin ya ce "Safiyyerh? Waye haka mace ko namiji?" Kimiyya ya ce "Bana son wulaƙanci, Safiyyerh wacce ta tashi daga nan wajan yanzu ita nake nufi ka daina kulata saboda zama lafiya shawara ce buddy"

"Shi ne na ce a jinsin mace take ko namiji?" Mutallab ya faɗa a kasashe. Ran kimiyya ya fara ɓaci don haka ya ce "Mata maza ce, ji rainin wayo kai Mutallab komai sai ka jisgahi kake jin daɗi?"

Ya girgiza kai ya ce "Da gaske kallon namiji nake mata, ka sanni ai, na shafe minti talatin ina kallon ta,na tabbatar cewa wai ba ɗan'uwana namiji nake kallo ba, amma na kasa hango suffar mata a idanunta, na kasa gano irin abin da na gani a tattare da Jaanah, ka ɗauka kamar kai haka naga ita wacce kake magana akai"

Kimiyya ya kalli Mutallab ya ce"Kasan wace Safiyyerh kuwa? Ita kakewa kallon namijin?" Mutallab ya ɗaɗɗage girarsa, yana sake zuƙar hayaƙin da yake cikin ɗan kuttun idanunsa ya rikiɗe ya juye kamar gaushi a daƙile ya ce "Nawa aka biya kuɗin makaranta ta? Uniform, books komai da komai" Kimiyya ya faɗa masa ya ɗakko waya ya ce "Wannan taka ce in ji Jeddah saboda karatu, system ta so siya maka ta ce ka fara da wannan, waya ce akwai sim a ciki da kuma numberta"

"Ita kuma nawa ce kuɗin ta?"

Kimiyya ya faɗa masa, ya jinjina kai ya ce "Zan biya, duka zan biya". "Ban gane zaka biya ba, me zaka biya?" Cewar Kimiyya yana gyara zaman shi da kyau. Murmushi Mutallab ya yi yana lumshe idanunsa ya buɗe ya ce "Ai ni ɗan Malam Abdullahi ne mai makarantar allo ta almajirai, ɗan talakawan nan, ni ne wanda bani da power, freedom, bani da ilimi, ni ne dai wanda ka kira da jahili, ni ne dai wanda ka cewa talauci ya zamewa abokin rayuwa, ni ne wanda ka aibata da ni da iyayena saboda talakawa ne, saboda naka iyayen jinin ƙaruna ke gudana a jikinsu" Mutallab ya ciccije bakinsa yana sake tsuke girarsa har lokacin wani irin murmushin yake yi ya ce "Ba ka yi ƙarya ba, Malam Abdullahi talaka ne bai ajjiye ba, bai kuma bawa Kowa ajjiya ba, sai dai Allah Ya bashi ɗa mai ƙaunarsa wanda zai iya sadaukar da komai domin shi, ka rubuta ka ajjiye ba zan taɓa wulaƙanta ba, kuma talauci ba zai taɓa zama abokin rayuwar Mutallab ba, zan biya ka In sha Allahu, ban yi lalacewar da za'a dinga mini gori ba, komai da ka yi mini da kai da Jeddah i appreciate it, na ɗauke shi matsayin bashi"

Ya miƙe tsaye har zai juya sai kuma ya ce "Shhh, ka ce mini boka, matsafi, zaka iya cewa na kashe Diyna da Jaanah idan ka so domin ina fargaba da cewa ba ni ɗin ne na kashe su ba, saboda taɓin hankali da nake da shi. Kayi ƙarya dai na faɗa tsafi nake ko bokanci, ko mene nake yi ka ganni da idanunka, ka huta lafiya abokina ɗan

mai arziƙi, ka yi haƙuri ba'a bin Moh bashin magana" ya tsallake ya bar Kimiyya a wajan, shima kimiyya ya bi Mutallab da idanu, bai taɓa jin takaici faɗawa wani ko gorantawa wani ba irin yau, maganganun Mutallab sun tsaye masa a zuciya, murmushin da yake fuskar Mutallab ƙirƙirar su ya yi, domin ya fi kowa sanin cewa Mutallab baya murmushi bare dariya jikinsa a sanyaye ya miƙe ya koma cikin class.

Bayan komawa, Uncle John ya shigo class ɗin ya rabawa kowa class work ɗin, yana murmushi ya bawa Aafiyyah ya ce "A karo na farko Aafiyyah score ɗin ki ya zo ɗaya dana wani, yama ɗara naki da kaɗan" nan da nan ta haɗe fuska ta ce "Uncle waye? Nawa score ɗin both" ya miƙa mata nata ya ce "8/10" ya ce "Mutallab ga naka, 9/10 keep it up my friend" amsa ya yi ya juya, Aafiyyah ta amshi nata Uncle John na fita ya yayyaga kamar za ta yi kuka ta ce "I hate him, na tsane shi".

***Mutallab yana zaune a ɗakin Ammo dab da magariba bayan ya gaisheta taƙi amsawa zama ya yi tare da cigaba da danna wayar hannunsa, juyawa kaɗan sai ya tuna maganganun da Kimiyya ya faɗa masa. "Waye ya saka a makaranta?" Ya ji saukar muryar Ammo a kunnuwansa ya ajjiye wayar a hankali kuma ya ce "Wa..." Ta katse shi da cewa "Kodayake bana buƙata, Allah Ya taimaka"

"Amin" ya ce

Sa'adah ta shigo hannunta riƙe da bokicin farar data soya, yana ganinta ya tsuke fuska ya fara shirin miƙewa zai fice, ta ɗakko farar ta miƙa masa ta ce "Auta ci ka ji" idanunsa ya yi luu numfashinsa ya nemi tsayawa, da ƙarfi ya ce "Yaya ban so kar ki sa mini, ban so" bata yi aune ba taga ya yi ball da farar gabaɗaya ta tarwatse a tsakar ɗakin, jikinsa na tsuma idanunsa ya yi jajur masifa za ta yi masa taga ya kafeta da idanu da ƙyar ya ce "Yaya..." Ta yi masa shiru tana ja baya kamar zai mata kuka ya rausayar da kai ya ce "Yaya na ce ban so" "Allah Ya baka haƙuri na ɗauka wasa kake yi mini" yana ƙanƙance idanunsa ya nanata "Wasa? Moh yana wasa ne yaro ne ni da zan yi wasa?" Sai ya yi ƙwafa yana banko musu ƙofar ɗakin ya fice abin shi. Ammo ta yi murmushi ta ce "Ikon Allah, Allah Ya rufa asiri"

Sa'adah ta ce "Ammo wai me ya ke yi haka ne? Naga har ƙadangare yana daƙƙowa idan fitinarsa ta tashi, ranar nan fa da ƙatuwar mahauniya na gan shi ya shige cikin ɗakin zaure, akan farar zai fara abu kamar zai mutu" tsoro duka ya kama Sa'adah, Ammo ita dai murmushi kawai take yi wanda bata saba yinsa ba "Kinga wallahi zuwa gaba kika ƙara bashi farar nan haɗuwarku ba za ta yi da kyau ba, kin san

halinsa ai da gaske baya wasa idan yace baya son abu da zuciya ɗaya yake faɗa, tun yana ƙarami baya son fara da ruwan sama wallahi"

Sa'adah ta yi shiru, Ammo ta ce "Na harhaɗa abin da zan iya haɗawa na kuɗi anjima ki kaiwa mai aikin kayan ɗakin naki Sa'adah "

"To Ammo, Allah Ya ƙara rufa mana asiri. Nima zai kai cikon kuɗin filas ɗin, shikenan Malam ba zai yi komai a bikin nawa ba? Haƙƙinsa ne fa?". "To jeki tambaye shi mu ji" Sa'adah ta yi shiru a ranta tana jin tausayin Ammo sosai.

Mutallab yana fita, ya nemi waje ya zauna har lokacin bai ci abinci ba ya kuma kasa faɗawa kowa yunwa yake ji. Haka kawai ya samu kansa da son duba karatun da aka yi, ya miƙe ya shige gida ya ɗakko jakar was the first abin da ya fara gani a cikin jakar shine farar takadda ƙarama, da short note a jiki ya nemi waje ya zauna ya warware takaddar a hankali ya fara duba abin data ƙunsa.

Blackman with beautiful eyes, I love your angry face, I love your i don't care attitudes, I LOVE YOU

He reads, yes he reads it, he read the sentences more than ten times, ya sake yin shiru tare da addition na numbers ɗin adadin daya ɗauka yana karanta rubutun, babu abin da ya bashi mamaki sai angry face ɗin da aka rubuta, shi akwai wanda zai ce yana son shi ne after Jaanah? who wrote it....? Who wrote this? Who says all this? Yake ta tambayar kansa ya kasa fahimta, bai san mene ya faru ba sai ya ji yana son adana wasiƙar, wanda ya bata title ɗin da _Forbidden message_ haramtaccen saƙo domin bai haɗa hanya da irin waɗannan abubuwan ba. Ya jingina da jikin bangon ɗakin nasa, ya rufe ido sai ya ji zuciyarsa na bubbuɗewa tare da tsuke masa a ƙirji, ya juya a hankali zuwa madubin da yake ɗakin ya zubawa kansa idanu, ai yama manta da wani abu da mutane suke halitta a duniya wanda zaka iya ganin biyuninka ta ciki wai shi madubi. Ya zubawa photocopyn nasa ido, yana son hasaso angry face ɗin, but he couldn't ta cikin ƙirjinsa zuwa maƙoshinsa ya ji maganar ta fito “liar” e, maƙaryaciya mana ya san ko waye macace ya sake lumshe idanunsa sai ya ji zuciyarsa na ƙara gutsistsirewa a ƙirjinsa into pieces, ba akan komai sai akan wannan forbidden message ɗin.

***Fitowar ta kenan daga parlon ciki zuwa main parlor, jikinta sanye da dakakkiyar atamfa ta ji sarƙa a wuya, hannunta sanye da zobe. Tunda ta shigo take kallon shi, har ta ƙarasu ta zauna tana ɗaukan remote tana ƙaro gudun ac, ba tare data kalle shi ba ta ce "ka bashi haƙurin?" Kimiyya ya juya ya kalli Jeddah ya ce "Eh" ta jinjina kai ta ce "Sai ya ce me?" Ya yi shiru ya kasa cewa komai kansa kuma a ƙasa, ta ajjiye remote ɗin da take sauya channel dashi ta ce "Bana maimaita magana ka sani kimiyya" a hankali muryarsa na rawa ya ce "Ya ce wai zai biya kuɗin daga baya" ta yi shiru, irin shirun nan na fahimtar abu kana ta ce "Kuɗin me zai biya?" A hankali ya ce "Wanda kika kashe na makaranta, da duka abubuwan da kikai masa har ma wayar da kika bayar ya ce zai biya" ta girgiza kai sai kawai ta yi masa banza ta ɗauki wayarta tana dannawa bayan ta harɗe ƙafafuwanta ɗaya kan ɗaya, ya san ba za ta yi magana ba ya ce "I am sorry Jeddah, ki yi haƙuri, i am so sorry don Allah" ta ce "haƙuri na mene kake bani shi har haka?" Tuni idanunsa ya cika da ƙwalla ya zame daga kan kujerar zuwa ƙasan ƙafafuwanta ya ce "Shine ya fara share ni, Jeddah kin sha faɗa mini babu kyau shariya ko wulaƙanta Ɗan'adam saboda kowa da kalar baiwa da ni'imar da Ubangiji ya yi masa. Wallahi Mutallab ne shine ya fara yi mini"

"Ya yi maka me?"

"Share ni, ya fara wulaƙanta ni"

Jeddah ta jinjina kai ta ce "You're not nice, you're not serious, you're not a good person, a good friend, and you never be.... Kai ba abokin ƙwarai bane, kai ba mai rufawa abokinsa asiri bane, ba irin abokin da ake fatan samu bane, ba kuma irin wanda ake cewa abokin a kashe a binne bane. Kana proud da kuɗin mahaifinka tunda shine ya bawa kansa ko? Ba Allan daya halicci Mutallab bane ya bawa babanka arziƙi, yana bacci ya farka yaga dukiya a kusa da shi ko? Ashe Islamiyyar asarar kuɗi muke yi, ka manta Ubangiji ke bawa wanda ya so, ya azurta wanda yaga dama, mutum baya taɓa zama hundred percent, shi uban naka ka tambaye shi hundred percent ne shi? Kuɗin shine komai nasa? Kowa daka gani a duniya Kimiyya Ubangiji tuni ya rubuta samu da rashinsa tun kafin zuwansa duniya, so ka yi farinciki ka yi wa abokinka gorin ilimi dana arziƙi, har Annabin Rahama ya bar duniya bai yi irin arziƙin da ake tunani ba, idan ya ci na yau yana fargabar na gobe ne, akwai sanda tsanani ya yi tsanani dutse ya ɗauka ya ɗora a saman cikinsa saboda ya yi masa nauyi ya daina jin yunwa. Batun ilimi, ka taɓa ganin wanda ana haihuwarsa a duniya ya ce A ko B? Annabi Muhammad Sallallahu alaihi Wasallama matse shi akai a cikin kogon hira aka ce masa, iƙƙira ya ce naá ana bi ɗarik. Kimiyya ba wanda ake haifa da iyawa, ba wanda ake haifa da dukiya kowa yana

zuwa duniya da al'ƙawarin Allah a tafin hannunsa, kowa yana rayuwa da ƙaddararsa ne wacce take bibiyarsa kamar inuwa ka gane"

Kuka yake yi sosai, Allah ya ɗora masa ƙaunar Mutallab a zuciyarsa ya ce "Ba zan sake ba, wallahi Jeddah sanda na faɗa ba har zuciya bane, i don't meant it, i regret it, Allah don ya ji haushi na faɗa ba zan kuma ba" ta girgiza ƙafa ta ce "Ƙarya kake, yadda ka daddage ka gasa masa wannan maganganu watarana ma zaka iya, ai wallahi gori sam bai yi ba, kuma za ka ci gidanku ne" ya dinga kuka yana bata haƙuri hadda rirriƙe ƙafafuwanta ta ce "Na ji, na haƙura je ka ɗauki abinci ka ci, Allah Ya tsare ya kiyaye gaba, ya kuma yi muku Albarka bakiɗaya" Ajjiyar zuciya kimiyya ya sauke yana rungume Jeddah ya ce "My favourite person as always..... I love you" ta shafa ƙasa sai kuma ta dungure shi ya hantsila ya tashi yana dariya. Wanka ya yi, ya sanya jersey da wando trouser black ya ɗan kama shi ya taje kansa. Daman ya riga da ya yi sallar issha sai ya bararraje akan ƙaton gadonsa yana buga game, wayarsa ce ta fara ringing ya ɗaga ya kai kunne ya ji ta yi shiru sai ya yi dariya ya ce "Safiyyerh....."

"Yes, how are you?" Ta faɗa a sanyaye cikin sanyin muryar nan nata ya ce "Allahamdulilah, ke fa?" Ta ɗan numfasa ta wayar can ƙasan maƙoshinta ta ce "I want to invite you my birthday party" Ya mirgina ya ce "Haba dai, yaushe ne kuma? Time, venue? Dress code" siririyar dariya ta yi mai sanyi ta ce "Kai fa sai a hankali, wani abu ne dress code?" Ya yi dariya shima ta ce "Za mu yi magana gobe, daddy ne ya shirya mini ai amma a gida, ya ce na yi invating duka friends ɗina, both maza da mata". Kimiyya ya ce "Amma dai daddy ya duba mana, ki ce mutumin zai zo ya siyi cake abu nasu captain maganin a kwaɓe su" ta ɓata fuska kamar yana ganinta ta ce "You are not nice Kimiyya" ya ce "I know....." Sukai shiru gabaɗaya can ya ce

"Yarinya ta girma kin fara amfani da waya iyeee, daman naga kwana biyu sai wani ma sha Allah kike abin ki, are you on WhatsApp?"

Ta ce "Naaa, ka faɗawa abokinka"

"Wanne abokin nawa?"

"Blackman"

Kimiyya ya tuntsire da dariya sosai shi dai muryarta na burge shi saboda sanyinta har ya yi yawa a hankali ya ce "Mutallab ko kike nufi? Ba zai zo ba" a taƙaice ta ce "Me ya sa?" Ya ce "Nasan halinsa" nan ma ta ce "Kamarya?" Ya ce "Kawai dai ba zai zo ba, kima sakawa ranki haka" ta yi shiru ya ce "hy dear" ta ce "send me his number, via dm ok"

"Safiyyerh jinin Prof ke yawo a jikinki ko? Magana kaɗan turanci, bashi da waya to ki siya masa"

"Bari mana, turan good night"

Kashe kiran ta yi, kimiyya ya tura mata number. Sai kuma ya kunna data ya shiga WhatsApp, group zai shiga sai kuma yaga kamar Aafiyyah na online ya fara typing ya tura mata "Hy Aafiyyah" ta buɗe ta gani sai ta share shi.

"Hy Aafiyyah"

"Hy Aafiyyah"

"Hy Aafiyyah....." Ya jera mata lokaci guda yana yin dariya don ya san halinta, emojin ta tura masa na naushi tare da guntun saƙo kamar haka. “Headache”

"Safiyyerh za ta yi birthday"

"Na sani"

"Za ki zo?"

Sai ta zare masa idanu, ta fara typing ta daina. Ya ce "Mene?"

"Mele"

"Za ki zo?"

"Maybe.... I will think"

**Safiyyerh ƙwance a ɗakinta saman gado, lokacin ta ci kuka ta ƙoshi tunda ta dawo daga makaranta Wahee ta sace score ɗin data samu a class work na math ta nunawa Ummeyh da daddy, ran daddy ya ɓaci sosai ya nemi bulala mai lafiya ya zane Safiyyerh cif numfashinta har ɗaukewa ya yi saboda azabar duka, data buɗe baki za ta faɗawa daddy cewa ita fa karatun ne kwana biyu bata ganewa sai ya daka mata tsawa. Ta dinga kuka kamar ranta zai fita, Ummeyh ma ta yi mata tas ba wanda ya bata listing ears, ta shige ɗaki taƙi fitowa cin abinci akai magariba akai issha shine abin ya damu daddy sosai yana son Safiyyerh kamar rai, ya shigo har ɗakin ya rarrahe ta ya mata alƙawarin birthday party a gobe da daddare ta yi invating duka friends ɗinta, hakan ya sauƙaƙawa Safiyyerh damuwar zuriyarta sosai.

Wahee ma ta yi farinciki, captain zai zo dake tafi Safiyyerh shekaru da kuma aji sai ta ji bari ta yi using opportunity ɗin itama.

Was the first person da Safiyyerh ta fara invited shine Kimiyya, ta kira shi suka fara magana har zuwa lokacin da yake ce mata;

"Safiyyerh jinin Prof ke yawo a jikinki ko? Magana kaɗan turanci, bashi da waya to ki siya masa" ta dinga jin abin da yake faɗa, wanda ita kuma bashi take son jin ba, da yawan lokaci kimiyya ya fiya wasa cikin lamuransa ta ɓata fuska kamar ba za ta yi magana ba sai kuma ta ce masa

"Bari mana, turan good night"

Tana zaune a wajan hannunta riƙe da wayarta ta ji notification tana dubawa taga number ce, ya yi saved nata da buddy. Ta dinga kallon number sai ta shiga ta yi rename ɗinta da sunan “Bestie” ta samu kanta da fargabar kiransa, domin bata san a yadda zai ɗauki kiran ba ta ji kamar ta haƙura, amma daga dawowarta gida zuwa yanzu da take zaune a kan gado ta azabtu, ita kanta bata san ainahin abin da yake damunta ba. A hankali ta janyo filo ta rungume a ƙirjinta tare da yin dialing numbersa, tana ta ringing ba'a ɗauka ba har ta katse, ta sake kira nan ma shiru a kira na uku aka ɗauka, bayan ɗaukan kiran Safiyyerh ta samu kanta cikin tsoro da fargaba, ta sake ƙanƙame filon a ƙirjinta a hankali ta ce.

"Hy"

Bai yi magana ba, ta yi shiru tana jin saukar numfashinsu lokaci guda a hankali ta sake cewa

"Hy" "Hy" "Hy"

Ta jera masa har uku, dib.. dib... dib... Kamar tafiyar agogo haka zuciyarta ke bugawa ta cikin ƙirjinta, tana cure mata waje guda. Ta tattaro duka nutsuwarta ta ce "Baka ji ba" bisa mamaki ta ji saukar muryarsa a daƙile ya ce "Na ji" motsin da ƙirjinta yi ya saka ta fahimci cewa akwai wata halitta a jikinta bayan ita wato zuciya, wacce take bugawa domin shi, only him. "Shi ne ka yi shiru?" Daƙiƙo suka shuɗe kafin ya ce

"Mene hy? Arne ni? By the way, who am i speaking with?" A hankali ta ce

"Oh! Assalamu Alaika"

Ya yi shiru ta ce "Safiyyerh ce"

"Shhh, Safiyyerh? A gender wacce, mace ko namiji?" Tambayar ta yi mata girma a zuciya da zafi sai ta ce "Bestienka ce fa, naga yau ka tafi gida da wuri daga

makaranta" ya yi shiru kawai tana ji yana jan numfashi ta cikin wayar ta ce "Ina gayyatarka bikin ƙarin shekaruna, my birthday party"

"Birthday party?" Ya nanata ba tare daya sani ba. Safiyyerh ta ce "E bestie, a gidanmu za a yi"

Kai tsaye ya ce mata "Ni ba ɗan iska bane to, kar ki sake kirana" zai kashe wayar ta ce "Mene ya kawo maganar iskanci kuma? Ko zan maka iskanci kuma a gidanmu?..... No..... No please" ta dinga masa magana ya yi shiru sai kawai ta fashe masa da kuka ta cikin wayar har da ɗan ihunta ta ce "Wallahi wallahi idan baka yi mini magana ba sai na zo gidanku a daren nan ba tare dasu daddy sun sani ba, ai na san gidan naku ka ji na rantse maka da Allah kuma ka san na isa kaffara, Allah ko wani abu zai same ni a hanya sai na zo yanzu a daren"

"Ok, sai kin zo".

MUTALLAB

08164069385

A yi weekend lafiya

[1/7, 9:35 PM] Sis Fauzy: Chapter 29: 2 fighters

Safiyyerh sai ta ji tunaninta ya tsaya cak, wayar maƙale a kunnenta. "Ok. Sai kin zo?" Ta maimaita a zuciyarta, maimaicin da ta ji ya kusan tarwatsa jaririyar zuriyar dake son girmama shekarunta. Ta yi shiru, she just want to make a sense na abubuwan da suka tattauna tsakaninta da Mutallab, but ta kasa believing abin da zuciyarta take raya mata, idan zuciyarta za ta yi wa adalci dole ne ta yi following umarninta, wato bin abin da zuciya ke so, hakan kuma kai tsaye ne da cewa ta je gare shi. Ta duba screen ɗin wayar taga ya jima da katse kiran, daman muryarsa ta nuna kamar ya fara bacci, kiran da ta yi masa ne ya tashe shi, domin a daƙile yake maganar kamar an tilasta masa yinta bisa dole. A hankali ta ajjiye wayar a saman filon data ɗora a cinyarta, ta daddafe kuncinta duka biyun da tafin hannunta.

"Na shiga uku ni Safiyyerh"

Ta furta a fili, ta rasa yadda za ta yi da tunanin zuciyarta, ko rufe idanunta ta yi shi take gani, he saw him, ganinsa take yi, he saw him with his face angry, and his sexcy eyes.

So take yi ta tabbatar da abin da take ji, duk da ta fahimta, sai sai abin da ta fahimta are different da yadda take ji a gangar jikinta. A hankali ta ɗauki wayar ta fara duba numbers ɗin da aka turo mata, ta ɗauki wata number ta kira har kiran ya katse ba'a ɗauka ba, ta sake kira cikin sa'a aka ɗauka a hankali ta ce "Afuwa na tashe ki daga bacci dear" ta ce a nutse, wacce ta kira ta ɗan yi shiru can ta cikin wayar ta ce "Forget about me, ke me kike yi ba ki yi bacci ba?" Safiyyerh ta ce "Na saka baccin ne Aafiyyah, will you help me please?" Aafiyyah dake jin Safiyyerh ta cikin wayar ta ce "Ina ji, ki haɗe tambayoyin a cure"

"Aafiyyah idan mutum zai gane yana son wani ya ake ji don Allah? Amma don't take my question serious kin ji". Ta ce tana marairacewa saboda fargaba. "Tun da ba serious ba ce, carry your question and leave" itama Aafiyyah ta bata amsa, da sauri Safiyyerh ta girgiza kai ta ce "Kin ji matsalarki ai, ba'a magana ta fahimta dake, ina cikin wani hali"

"Kamarya?" Aafiyyah said.

"I think i am in love, na ji kamar na faɗa cikin soyayya Aafiyyah" ya ɗauki Aafiyyah 30 seconds kafin ta ce "Uhm, ina ji". Safiyyerh ta ce "Ai ban tabbatar bane, so nake ki faɗa mini yadda zan gane kuma na yarda da cewa e, i am in love ɗin, sai na san yadda zan tari aradu da ka, shine kawai" Aafiyyah ta ce "Ina aiki yanzu dai kam, amma kin bani mamaki Safiyyerh gabaɗaya guda nawa muke da za ki ce wai kina ji kin faɗa soyayya, ita soyayyar kogi ce da ake faɗawa cikinta? Ina jin yanzu ne za ki yi cikar shekaru goma sha biyar da haihuwa a duniya, ko dan kinga kina da girman da za a iya tunanin kin zarta shekarunki? Ko don kinga kina da kyau eh? Ko dan kin tashi gidan masu kuɗi eh? And don Allah tell me something where is your dreams? Ina mafarkanki suke? Ina long and short term goals ɗin ki da kika yi wa kan ki tsari, ki ka yi wa kan ki planing to achieve? Where are they? Ina kika yi keeping nasu?"

"Aafiyyah, i don't know what come over me, koma dai mene na fahimci a yanzu karatu ba shine tsarina ba, idan abin da zuciyata ke raya mini zan yi to babu karatu Aafiyyah, bani da wani plans da zan yi achieving nasu..... Da gaske" sai kawai ta fashe da wani irin matsanancin kuka, Aafiyyah ta yi shiru tana sauraren kukan da Safiyyerh ke rera mata ta cikin wayar, tana shasshe ƙar kuka ta ce "Kamar na samu matsala haka na ke ji, ko idanuna na rufe bana ganin komai sai idanunsa wanda suke faɗa mini abubuwa da dama, Aafiyyah i know nothing about the love, but a name, sunan kawai. Ba za ki gane ba, farkon sunansa idan na ji zuciyata bugawa take, ina son hira da shi, ina son ganinsa kusa dani.... Ban san me hakan yake nufi ba, i really really don't know, i don't understand!"

"This is what we call love and romantic....Ga amsar ki nan"

"Amma wa kike so haka?" Aafiyyah ta ɗora da tambayar. Kamar Aafiyyah na gaban Safiyyerh ta girgiza mata kai ta ce "Secret crush, zan faɗa miki not today not tomorrow ƙila watarana" duka suka yi shiru, kowa kuma da tunanin da yake a cikin zuciyarsa, saboda hira suke a nutse they act as matured as other people, a maganganunsa ba zaka tsinci ƙuruciya ba. "Uhm Safiyyerh kenan, shikenan?" Safiyyerh ta yi murmushi ta ce "wanne kalar cake kike ganin zai fi kyau?". "Za mu yi magana gobe idan muna raye a makaranta, and i will tell you something" sai da safe suka yi wa juna kana suka kashe kiran gabaɗaya.

After a called, Safiyyerh ta yi shiru tana tunani ta rasa yadda za ta yi da zuciyarta. Ta miƙe a hankali tana ajjiye wayar daga ita sai kayan bacci ta buɗe ƙofa, ƙafarta sanye da bedroom slipper ta sauka zuwa downstairs, waje ta nema a parlon ƙasa ta zauna watching a movie, sai dai ta raba hankalinta gida uku, ɗaya a kallon, ɗaya a tunanin Mutallab, ɗaya a ɓangaren daddy.

"Safiyyerh"

Ta yi saurin juyawa taga Ummeyh ta caɓa uban ado, tana sanye da wasu kayan bacci masu masifar kyau sai ɗaukan ƙamshin kwalacca da humrar da ta yi order a wajan S Bayero take yi, hannunta riƙe da wata ƴar ƙaramar ruba ta zuma. Bayan Safiyyerh ta kalli Ummeyh sai ta ɗauke kai ta ji haka kawai ranta ya fara ɓaci, Ummeyh ta ce "Me kike yi a cikin daren Safiyyerh?" Da hannu Safiyyerh ta nunawa Ummeyh t.v lokacin an hasko wasu masoya rungume da juna, wanda a shekarun

Safiyyerh bai ci ace tana kallon irin waɗannan movies ɗin ba. "Idan kin gama ki kashe ki je ki kwanta, zan shiga wajan daddynki"

"Sai ki fito yaushe? Ko sai da safe?" Safiyyerh ta tambayi Ummeyh har lokacin kuma bata kalli Ummeyh ba. "Eh, sai da safe"

"Miji daɗi, Ummeyh kina son daddy da yawa, nima in sha Allah haka zan so nawa mijin fiye ma dake,ni idan na shiga ɗakinsa ma ba zanna fitowa ba"

"Sai ki haɗiye shi" Ummeyh ta bawa Safiyyerh amsa, ta ɗora da faɗin "Yʼar ƙaramar ki dake kin riƙe sunan miji ba tare da sanin ma'anar ta ba ko Safiyyerh?" Safiyyerh ta juyo a lokacin ta kalli Ummeyh da idanunta da suke lumshewa ta yi murmushi ta ce "Ummeyh kenan".

"Ban gane ba, kwalliyar tawa ce ba ta yi ba na sauya ko mene? Prof yana son jambaki da ƙamshi sosai, duba mini kiga" ta faɗa tana jujjuyawa a gaban yʻarta ta, Safiyyerh ta ce "Shi jambakin zai kai Safiya ne a bakinki? Kin yi kyau sosai Ummeyh, Allah Ya nuna miki nawa auren" Safiyyerh ta faɗa, tana jin wani abu na bin jikinta sosai. Ummeyh ta ce "Amin ɗiyar arziƙi, goodnight"

"Goodnight"

Safiyyerh na zaune tana kallon zuciyarta na sake jaddada mata cewa "Follow your heart Safiyyerh" ta ɗaga idanu ta kalli lokaci taga ai shabiyu na dare ya shige, ta fara tunanin idan ta nemi alfarma wajan Wizzy zai kai ai secretly ba tare da daddy ya sani ba, ta miƙe ta nufin hawa saman bene ta sako after dress sai taga Wahee ta sakko ƙas da alama ruwa ta sakko sha, cikin sauri ta fara murza idanu alamar bacci take yi, kallo ɗaya Wahee ta yi mata ta ɗauke kai ta nufi wakan deep freezer dake gefe guda. Al'amarin daya tilasta wa Safiyyerh haƙura da zuwa ganin Mutallab, takaicin hakan ya saka ta ji hawaye masu zafi sun cika idanunta, gishirin da ta ji a bakinta ne ya saka ta fahimci hawayen ya samu damar zuba da kansa ta miƙe ta nufi bedroom.

***Mutallab bayan ya gama duk abin da ya ke yi, ya je wajan Malam yi masa sai da safe ya yi masa banza, ya leƙa ɗakin Ammo ta tarar ta yi bacci suka haɗa idanu da Sa'adah ta yi saurin ɗauke nata idanunta, ya buɗe ido sai kuma ya ce "Sai da safe Yaya" ya juya ya nufi ɗakin zaure, ya barbaje tarkacan abubuwansa a gaba, hadda farin goro da wata wuƙa da ya yi rubutu a jikinta da tawada, wani kwalli yake son haɗawa daya binciko sirrinsa so yake ya tabbatar ko sirrin zai yi aiki. Bayan ya kammala haɗa kwallin ya zaro layoyin ya caccaka musu allurai a kai ya ajjiye gefe guda. Rigar jikinsa ya cire, har zai kwanta ya sake cire singlet ɗin ta ciki ya lumshe idanunsa jin iska ta ratsa shi wacce ta shigo ta tagar waje, ƙirjinsa a bubbuɗe ya sha ƙirjin ya buɗe ido, jin alamar kwantaccen gashi, ya tsuke fuska.

Ya dudduba littafansa na makaranta ya yi dukkan assignment, har zai kwanta sai ya tuna da wasiƙar nan, ya ɗakko ya sake karantawa shi dai rubutun jiki ya na saka masa nutsuwa haka kawai, ya mayar ya ajjiye ya raɓa gefen tabarmar ya kwanta ya lumshe idanunsa, maganganun Kimiyya suka fara rige-rigen dawowa cikin ƙwaƙwalwarsa a hankali bacci ya ɗauke shi. Sama-sama ya fara jin vibration a ɗan nesa da kunnuwansa, bai buɗe idanunsa ba sai ɓata fuska da ya yi baya son fara bacci ya tashi gashi yana da nauyin bacci shi ya sa yana jimawa bai kwanta ba, vibration ɗinne ya cigaba da yi yaga dai za'a addaba masa, ko idanu bai buɗe ba ya miƙa hannu ya janyo wayar ya ɗaga ya yi shiru, wanted to hearing from the person, haka kawai jikinsa ya basa ita ce, no one but her. He got it right domin muryata ce ta sauka a kunnensa inda ta ce.

"Hy"

Sarai ya jita sai ya yi shiru, ya kuma kasa kashe kiran, dalilin tashinsa ba gaira ba dalili yake son ji. Ta dinga magana har sanda ta ce yi maganar bikin ƙarin shekarunta, ya ji mamaki ƙwarai yar ita za a yi wa birthday? Iyayenta kuma su zuba idanu, kodayake ai ɗiyar Professor ce su masu kuɗi komai a wajansu lafiya lou ne. Amma mene haɗin namiji da sabgar mata? Iskanci ne kawai. Tsaki ya ja a ƙasan ransa jin yadda take kuka ba gaira babu dalili saboda sangarta da lalacewa irin ta yaran masu kuɗi. A hankali ya ce "Ok. Sai kin zo" yana faɗin hakan ya kashe kiran can ya kashe wayar bakiɗaya, tsaf zai mayar da wayar nan idan za'a addabi rayuwarsa don dai karatu kawai zai yi da ita, kuma ko ɗazo ta yi masa amfani.

Ajjiye wayar ya yi ya juya tare da rungume hannunsa a ƙirji kamar yadda ya saba a haka bacci ya ɗauke shi mai nauyin gaske.

Bai sai ya aka yi ya makara bayan ya yi sallah ba, bai kuma san lokaci ya ja ba sai tsinkayo muryar Sa'adah da ya yi a cikin kansa, tana tashinsa a bacci, ta dinga kiransa yaƙi ko motsawa sosai yake jinta ko idanunsa ya kasa buɗewa, ta hau jijiiga shi tana faɗin "Auta, Auta zaka makara a makarantar da kake zuwa fa, ka tashi takwas ta kusa" bai san me ya ce mata ba sai ji ya yi ta ce "Makarantar ce babu yau?" Ya mata shiru. Miƙewa ta yi ta koma cikin gida ta samu Ammo ta haɗa kunu tana juyawa bayan ta ƙara gasara ta ce "Ammo Muhammad fa yaƙi tashi, kuma zai makara a makarantar" Ammo ta kalli Sa'adah kafin ta ce "Ina ruwana kuma? Kika sani ko wani abu ya sha haka?"

"Wani kalar abu zai sha da zai dinga bacci ko motsi ba ya yi? Ammo mugun fata ne irin wannan wallahi irin wannan maganganun suna tasiri akan yaro....,"

"Bani waje Sa'adah" Ammo ta ce tana yin cikin ɗakinta, domin zaman ci da kai suke yi a gidan.

Sa'adah ta koma cikin ɗakin ta same shi a ƙwace, ta daddage ta kira sunansa da ƙarfi, ya runtse idanunsa sai kuma ya mirgina tare da waigowa ya zubawa Sa'adah idanunsa, da suke lumshewa suna buɗewa, ita kuma Sa'adah mamaki ne ya cika mata zuciya ganin yadda Mutallab ya buɗe ƙirjinsa ya yi faɗi ga gargasa ƙwance a ƙirjin. Ta tsinkayi muryarsa a kanta "Yaya idan na miki Allah Ya isa fa? Ki ce bani data ido haba Yaya". "To me na yi? Kai da ba a yi maka abin arziƙi" ya ƙanƙance idanunsa ya ce "Tsaraicina mana, yaya tsaraicina me ya sa za ki mini haka?" Maganar ta girmame ta ya saka ta miƙe ta ce "Masifaffe..." Ta ce tana yin waje, ya haɗe fuska tamau can ya miƙe ya zira riga cikin ƙaramin lokaci ya yi wanka, ya shirya cikin uniform ɗin, yana mamakin yadda kullum Sa'adah bata gajiya da wanke masa su ta goge don ma kala biyu ne da shi. Cikin gidan ya nufa, ya durƙusa har ƙasa ya ce "Ina kwana Ammo?" Bata kalle shi ba ta ce "Lafiya...." Ya yi jim ya ce "Ki ma yaya magana ta daina bana so" ta ce "Me ta yi maka?"

Da sauri Sa'adah ta ce "Ba abin da na yi masa daga tashinsa daga bacci fa shikenan"

Ya wani kalleta sheƙeƙe, yana nutsar da idanunsa ciki ya ce "Da daɗi na zo na buɗe miki riga kina bacci, da daɗi na kalli ƙirjinki, me ya sa za ki kalli nawa" ya faɗa da tsantsar gaskiyarsa jin maganar ta girmama ya saka Ammo cewa "Tashi ka bani waje" ya dinga kallon kunnun dake kofi, shi ba zai taɓa cewa a bashi ba ya miƙe ya

fice a zaure ya ci karo da Aby ya ce "Sannu Aby" "Yawwa ɗan'uwan turji saura zama yaronsa sai ka cigaba da kisan kai hankali ƙwance" Mutallab ya yi ficewarsa domin ya saba da irin wanɗannan maganganun.

Bayan fitarsa Ammo ta ce "Sa'adah kina rayuwa da Mutallab ba ki san halinsa ba, kin san dai ba baki zan saka muku ba, bashi da wasu abokai a cikinku mata ya tashi, sai mu yi farinciki da bai zama ɗan daudu ba, ki cigaba da ya yi masa abin da baya so, ya miki da kirki ba da yake nanata miki baya so, ina mai tabbatar miki watarana zai ɗage rigar daga nan sai ki shirya bashi dukkan amsar tambayoyin da zai miki" Sa'adah ta ce "Yanzu shi sai ya ɗaga mini riga? Kamar mara hankali ". "To hankalin ne da shi? Ki faɗa mini mata nawa ne a gidan nan kafin shi? A cikin mata nawa ya tashi, abubuwa nawa kuke yi a gabansa a kan idanunsa? Bai san wasu ɗabi'un masa yan'uwansa ba sai naku kawai dai Allah ne ya kissima masa wasu ɗabi'un, tun yana ƙarami yake sanya ku a gaba da tambayar abin da bai sani ba, kina nan aka faɗa mana cewa yana da taɓin hankali" ta ƙare maganar a raunace, hawaye ya sakko idanun Sa'adah gabaɗaya ta manta cewa yana da taɓin hankali, ta dinga kuka Ammo ta yi mata shiru "Yanzu ba za ki bari a faɗawa Anty Hameeda ba?". "A hir ɗinki, a kul na kuma ji, ko da wasa kika bari wannan ƴar ta ji maganar nan sai ranki ya ɓaci"

He late, don haka kai tsaye ya nufi cikin ajin ya ci sa'a babu teacher fuskarsa kamar ya ce ya shiga uku, ya nemi waje ya zauna yana duba abubuwan da aka yi sai ya ga ba komai. Safiyyerh ta kalle shi a hankali ta ce "How are you bestie? Ka makara ka jira bulala" bai kulata ba, littafin daya gani a gabanta ya saka yatsu biyu ya janyo yana jingina da jikin desk ya fara duba note ɗin, duk inda bai gane ba sai ya rubuta a bayan littafinsa, ta matsar da fuskarsa tana yin ƙasa da kai ta ce "Are you just coming...?"

"Hmmm"

"Laa, ka je ka saki baki da hanci kana ta bacci ai, na ji hakan ai a zuciya da jikina, Yaruba boy" ya ajjiye littafin tare da sun kuyar da kansa, itama ta sun kuya tana leƙa shi ƙamshin turaren da take yi duk ya dame shi "Bestie...." Calmly ta kiranye shi, sai taga ya juyo ya kalle ta, suka haɗa idanu sosai Safiyyerh ta ji wani irin abu ya gilma a zuriyarta, zuriyarta ta dinga motsi a ƙirjinta da ƙyar ta sauke ajjiyar zuciya kuma har lokacin cikin idanunsa take kallo a hankali ta ce "Ka zama abokina, kaga kowa yana da aboki ka ji don Allah" ta marairace fuska sosai.

Ya zazzaro mata ido, itama ta zazzaro masa idanunta ya daƙile ya ce "Dai na kallona"

"Daina kallona"

"Kee..."

"Kai..."

Ya lumshe idanunsa, itama ta lumshe "Hmmm" itama ta ce "Hmmm" sai kuma ta yi murmushi ta ce "As far as zaka ke hirar kurame dani, i will do the same nima. Na kira ka jiya fa" shi dai kallon mara hankali yake mata don haka sai ya biye mata, tunda a ce zama lafiya da mara lafiya ka biye masa ya yi abin da yake so. Zata sake yin magana teacher ya shigo wanda yake ɗaukar su Agriculture. Bayan gama Agriculture duka students suka fita, Kimiyya ya ƙarasu yana cewa "Birthday girl, yau kin buga sammako ykk ko?" Bata kalle shi ba, attention ɗinta yana kan Mutallab ta ce "Kimiyya kenan" ya ce "Ba wani kimiyya, ya shirye-shirye? Ƙarfe nawa ne sabgar kin san ina son abubuwan nishaɗi sosai, i like and i love entertainment" ta zaro invitation a side ɗin jakarta ta kalli Mutallab ta ce "First card, first invite, first person is you bestie, ina invating naka birthdayna"

Ya amsa ya ajjiye kawai, not looking at her. Kimiyya ya ce "Safiyyerh ya za'a yi ne?"

"Game da me?"

"Wallahi ina son Aafiyyah, sosai"

A hankali Mutallab ya ɗago kai ya kalli Kimiyya, yana ƙara nanata abin da Kimiyya ya ce "Wallahi ina son Aafiyyah, sosai " ya yi shiru sai kuma ya miƙe gently hannunsa ɗaya a aljihu zai fita Kimiyya ya ce "Ina zaka? Ana shirye-shiryen birthday party?" Bai kula Kimiyya ba ya saka kai ya fice, siririn tsaki Aafiyyah ta saki tana ƙarasawa wajan su ya ce "Aafiyyah ɗan bi bayan Mutallab ki kira mana shi" ta yi masa banza ya dinga magana ta share shi. Yana fita Aafiyyah ta kalli Safiyyerh,

Safiyyerh ta ce "You came early today, akwai magana ne?" Gira Aafiyyah ta ɗaga mata, sai kuma ta yi ƙasa da murya ta fara mata magana secretly a ɗan raunace, Safiyyerh ta dinga kallon Aafiyyah sai ta kasa ce mata komai ta yi shiru, a hankali ta ƙara kallon Aafiyyah sai ta sauke ajjiyar zuciya tana murmushi ta ce "Ok, dear" kafaɗa Aafiyyah ta ɗaga tana barin wajan zuwa cafeteria bayan fitar ta Safiyyerh ma ta miƙe ta fita.

Mutallab yana zaune ya lumshe idanunsa yana jin yadda cikinsa ke yi masa ƙugi alamar yunwa "Bestie....." Ya buɗe ido Kimiyya ya ce "Buddy ana neman shawararka fa akan batun birthday" ya buɗe ido sosai ya dinga kallon su kana ya ce "Me?"

"Zaka zo ai?"

"No" ta ce "Me ya sa" kai tsaye ya ce "Mene birthday? Na waye? Me ake? No please" Kimiyya ya dinga murmushi kafin ma su ƙara magana ya tashi ya bar wajan. A hanya suka yi karo da Captain ya yi masa wani ban zan kallo yana mai jin takaicin yadda Safiyyerh ta ɗauki labarin ɗan talakawan nan very serious. Cafeteria shima ya shiga, yana shiga kuma suka yi ido huɗu da Aafiyyah dake zaune saman kujera, ta ɗan jingina bayanta da kujerar sai marairace fuska take yi, da alama Vcall take yi, ganinsa kuma ya saka ta haɗe girar sama data ƙasa, ita tunda score ɗinsu ya zo ɗaya ta ji bai yi mata ba, kamar zai ƙwace mata matsayinta a class ɗin, dama daga ita sai Safiyyerh.

Shi ɗin ma, kallon tsautsayin da ya yi mata bai sake yi ba, tana zaunen ta ganshi hannunsa riƙe da ruwa, kamar mai takalarta haka ya ja kujerar dake fuskantar ta ya zauna, ya ɓalle ruwan yana kai wa bakinsa sai kame fuska take, bayan ya gama shan ruwan ya ajjiye ya dinga buga game a waya hankali kwance, yama manta da batun ta. Ta miƙe tsaye tana ƙara ja masa tsaki, ta zo gilmawa ta kusa da shi, ya saka ƙafarsa ɗaya ya taɗeta tare da murje yatsun ƙafarta guda biyar da suke cikin takalmi. Luu ta yi ta gaba zata kifa da fuskarta, ya ƙara saka mata ƙafa ta gaban sai ta yi baya daɓas ta koma ta zauna kan kujerar da take, cikin wani irin firgitaccen yanayi Aafiyyah ta ɗago idanunta da suka yi wani irin jaa, da sauri ta sunkuyar da kanta tana haɗiye wani irin abu, ta sake ɗago kai taga ya ajjiye wayar ya harɗe hannayensa a ƙirji ya zuba mata idanu.

"Are you mad? Wani irin banza ne kai shasha mara lissafi da tunani? Ni ka sakawa ƙafa na faɗi?" Magana ake mata ta cikin wayar, sai kawai ta yi cilli da wayar tana nuna Mutallab daya kafeta da idanu ta ce "Useless, kuma sai ka yi ladamar abubuwan da ka yi, har kana jin kai wani ne? Ɗan wahala kawai cima zaune" masifa take yi ta ƙarfin tsiya har su Captain su Kimiyya suka shigo, Safiyyerh ta tsaya gefen Mutallab wondering me ya yi mata haka, Captain ransa fes, kimiyya kuma sam bai ji daɗi ba. Duk masifar da Aafiyyah ke yi idanunta yana ƙasa, shi kuma yana kallon fuskarta sai kaɗa ƙafa yake yi. Ta ja tsaki ta ce "Stupid!"

Duk kiran sunan da Safiyyerh ke masa bai kalleta ba, sai bayan fitar Aafiyyah ya juya suka haɗa idanu, ya sauke ƙafarsa ya duƙa daidai kanta ganin tana kuka a hankali ya fara mata magana ita kanta da ƙyar take jin me yake cewa can ta ce "Zaka zo ɗin? Ƙarfe 8 ne, don Allah ka zo, zan yi kuka na kwana ina yi idan baka zo ba"

"Mene sunan ma?"

"Safiyyerh"

"No, rage masa tsayi FIYYA is ok for me, zan yi tunani, amma don Allah ki daina takura Mutallab, ki daina bibiyar Mutallab, tsakani da Allah nake faɗa miki yanzu bana son mutum mai naci, kai na juyewa yake, tunda na zo makarantar nan ba ki bar ni na yi numfashi mai kyau ba tare da addabawarki ba, a sanda na zo kuma na fara tattala maganganun da zan faɗa miki, sai yanzu suka kammala, i so much respect a woman, a girl, a mother, so i respect you Fiyya, wallahi bani da hankali da kike gani na, bana wasa ba wasa nake faɗa miki ba" ya faɗa yana ɗaɗɗage girarsa tare da cure su. Safiyyerh ta dinga kallonsa, a kullum abin da take ji game da shi ƙaruwa yake yana habbaƙa a ƙirjinta tare da yin yaɗo. Sharrr, hawaye suka fara sauka daga cikin idanunta, sai kuma ta ji dama za ta iya duka hakan, dama zata iya, inama zata iya, how? Never..... She failed as a girl. Ta fashe da kuka.

Sai kuma ta miƙe tsaye ta saki murmushi mai tafe da dariya tana girgiza masa kai a hankali ta dinga ja da baya, tana dariya tana hawaye yar ta kai ƙarshen cafeteria ɗin, ta ɗage masa gira itama ta ce "What if i told you, I love you?" Sai ta fashe da dariya, a lokacin ita tama manta a cikin makarantar suke, ta manta a gaban students suke, ta manta she is under age, ta manta cewa lokacinta bai kawo ba, ta manta karatu ta zo yi, ta manta ita yar gidan Professor Abdu ce, ta manta cewa Ita

yar gidan Dr Ummeyh ce, ta manta ko zata mutu a yanzu ta farko babu wanda zai amince ya aurar da yarinyar mai shekarunta.... Tana yin abin da take jin shine daidai, tana following zuciyarta ne wanda matakin Adolescencet stage ke ɗawainiyya da ita.

"What if I told you, i love you bestie? What if..... What if..... Eh?" Ta saka hannunta a fuska ta shafo ruwan da ta ji mai zafi a saman fuskar, ta ɗan waro idanunta tana dariya ta ce "Ohh Allah! I am crying, Safiyyerh is crying..." Ta yi kamar zata fita daga cikin cafeteria ɗin, sai ta matsa kusa da Mutallab wanda kansa yake ƙasa yana game, ta saka hannunta ta dungure masa kai sai kuma ta ce "Ina jiran zuwanka gidanmu, kai ne zaka yanka mini cake, ko dai ka zo ko kuma ni na zo har cikin gidanku, lastly i said what if you told you, I love you?"

Ya ɗago ya kalleta, da a ce Safiyyerh ta san Mutallab nada taɓin hankali da ba zata tsaya yi masa ihu aka ba, ta harare shi ta ce "Yaruba boy...."

Tana fita ta nufi class, Kimiyya ya sauke numfashi ya kalli Mutallab ya ce "Ka ji daɗi abin da ka yi?" "Hmm" kawai Mutallab ya ce yana miƙewa, ƙofar cafeteria ɗin Kimiyya ya kalli Aafiyyah dake murza idanu ya ce "Mene ya samu idanun naki ya yi ja?" Ta ɗan tsuke fuska ta ce "Kwaro ne ya faɗa mini ciki" Ya jinjina kai, Mutallab ya yi shigewarsa. Bayan tashi, Safiyyerh kamar ba ita ta yi kuka ba, suka fito tare da Mutallab da Kimiyya zuwa harabar gidan, a daidai lokacin suka hango Aafiyyah a gaban wata mota Ash ta ƙanƙame wani, wanda ta ƙanƙame ɗin yana ta ɗan bubbuga bayanta can kuma ya buɗe mata ƙofa ta shiga shima ya shiga driver ya ja su.

Tun daga nesa Daddy ya zubawa Mutallab idanu, ya ji zuciyarsa ta kumbura yanayinsa ya rikiɗe sosai ya yi sauri ya fito Safiyyerh ta ce "Daddy kai ne?" Bai mata magana ba sai Mutallab da yake kallo, kai gaisuwar kimiyya bai amsa ba ya ja hannun Safiyyerh zuwa cikin mota, Mutallab ko inuwar daddy bai kalla ba shima, ya matsa can. Daddy na kallon Safiyyerh bayan ya ta yar da mota ya ce "Waye wancan dana ganku da shi?" Ta ce "Wa?" Ya ce "Baƙin" kai tsaye ta ce "Ok, ban san shi ba ai yau na fara ganinsa" ya jinjina mata kai daman ya san Safiyyerh ba zata taɓa kula maza ba, balle wannan kangararren yaron ya ce "Good, koda wasa bana son naga kina magana da shi, abin da ya saka na miki magana naga a makarantar yake duk da na ji mamakin ganinsa a makarantar masu kuɗi haka, Safiyyerh kula wannan yaron shine abu na ƙarshe da za ki yi mini na ji zan iya sallama ki" ta runtse idanunta tana ambaton sunan Allah. "Kin ji?" Ta jinjina kai domin bata jin tana da

sukuni yin magana, data buɗe bakinta za ta iya cewa "Daddy he is the one i love, daddy he is the one i pray for.... Daddy he is the one da nake son rayuwa da shi, irin rayuwar da kuke yi a gida, a cikin ɗaki kai da Ummeyh" a haka suka bar makarantar.

***Mutallab na gida a zaune aka ce ana kiransa a waje ya yi sak sai kuma ya miƙe tsaye ya fita, wata babbar mota ya gani sai ya cake yaƙi ƙarasawa a hankali mai motar ya fito cikin shiga ta alfarma yana murmushi ya kalli Mutallab ya ce "Barka, kai ne Mutallab ɗin?" Ya jinjina kai ya ce "Ma sha Allahu, aiki muke buƙata muke so ka yi mana, na zo ne domin na shaida maka zuwa dare zan dawo aikin kuma na mai gidana ne" Mutallab ya sake jinjina kai mutumin ya ce "To da kyau, sai na zo" ya shiga mota Mutallab ya koma cikin gida.

Aby ya samu yana surfawa Ammo masifa har da kumfar baki yana faɗin "Ni fa yaron nan ba zai ɗakko mini magana ba, na rantse da Allah ban haifi wanda zai saka mini hawan jini ba, balle ya saka zuciyata bugawa. Tsinannen yaro la'ananne wanda bashi da wani amfani, ƙiris nake jira ka tattara ka bar mini gidan nan" ba ta yi magana ba, sai Sa'adah ce ta ce "Yanzu me Mutallab ɗin ya yi maka Malam? Ɗanka ne fa zaka iya zama da shi ka ji damuwarsa ka ji mene ya saka yake yin abin da yake? Me ya sa ɗabi'unsa suka sauya ai da ba haka yake ba" Malam ya ce "Ubanwa zan ja a jiki? Ya cinna mini wuta nima? Ai yafi ƙarfina wannan da kike gani"

"Innalillahi, ya zaka haifi ɗa a cikinka ya fi ƙarfinka Malam"

"Ni dai ya fi ƙarfina shi ya sa na tattara shi na watsar, aure ma zan yi wallahi, wannan ɗakin na zaure fita za ka yi kamar shi, ga can wata bazawara na yawo sakin wawa a gari ita zan auro"

"Malam yaushe kake ciyar damu? Ba abinci, ba magani, ha suttura amma shine kake cewa za ka yi aure? Kana da kuɗin auren ka bar mu haka cikin ƙangin rayuwa da yunwa? Ka mance mutuwar Muneeberh? Haba Malam" Sa'adah ta faɗa tana kuka, ya ɗauki bulala ya zarara mata a baya ya ce "Muneeberh ga wanda ya kashe ta nan, kuma Allah Ya isa kashe mini yarinya daka yi" yana cewa haka ya fice. Mutallab ko motsi bai yi ba, sai danna waya yake yi, Ammo ta kalli wayar tana mamakin inda ya samu sai ta kasa tuhumarsa yana ta zaune har akai kiran magariba ya miƙe tsaye tare da yin waje abinsa.

***Safiyyerh tuni ta mance ta batun daddy da gargaɗinsa, ta shige ɗaki tana ta shirye-shirye, Wahee ma haka. Sai da aka yi kiran sallar magariba ta fito tare da sakkowa ƙasa. Ummeyh ta ce "Da dai kin ci-gaba da zama a ɗaki sai a zo a tarar dake haka, tuni an gama yin decorations. Murmushi ta yi wa Ummeyh sai kuma ta leƙa wajan decorations ɗin ya yi masifar kyau, Black and white.

"Ga rigar ki can"

"Ummeyh ina tawa?" Safiyyerh ta kalli Wahee, Wahee ta harareta. "Ba Black ce taki ba?" Ummeyh ta tambaya ta ce "To tana cikin bedroom nawa, ku je ku shirya sai na yi muku rolling ko? Safiyyerh ko kina son makeup?" Ta girgiza kai ta ce "No Ummeyh"

Farar duguwar riga gown Safiyyerh ta saka mai buɗewa wacce ta zauna cif fa ita a jikinta, hatta ƙirjin ya zauna a gidansa Ummeyh ta yi mata rolling kamar Balarabiya, Safiyyerh na son Abaya sosai, bata da wasu kaya sai so. Ummeyh ta kalleta ta ce "Ma sha Allahu dear, kin ga yadda kikai kyau? Sai dai girma ya zo ba hankali kalli jikinki fa?" Safiyyerh kallon Ummeyh kawai take yi wai bata da hankali. "Ai Friends ɗin sun fara zuwa, naga ƙawarki mai fara'ar nan?" A hankali ta ce "Kinal" Ummeyh ta ce "Sure, ita"

Hannunta riƙe da waya ta fita kowanne tables an shirya abubuwa, hatta wajan zamanta har cake ya zama ready ta yi murmushi ta ce "Kinal, your welcome" "Thank you" Nahyan ya ƙarasu da wasu class mates ɗin nasu ganin Captain is here too, ya saka ran Safiyyerh ɓaci, ita ai bata ce ya zo ba. Ta kalli Kinal ta ce "Ina zuwa" Kinal na danna waya ta ce "Take your time dear" wajan duk ya fara cika da mutane yaran masu hannu da shuni kowa ka gani a wajan ɗan gata ne, daga mazan har matan shigar baƙaƙen kaya sukai, cold music na tashi a hankali. Cikin sauri ta kira Kimiyya yana ɗagawa ta ce "Baka zo ba?" Ta cikin wayar ya bata tabbacin yana hanya, sai ta samu relief da tunanin suna tare da Mutallab. Tana tsaye a wajan wata baƙar mota ta yi parking, Aafiyyah ce tunda taga an daɗe ba'a fito ba, Safiyyerh ta ƙarasa wajan ta leƙa ta ce "Yaya" ya ce "Birthday girl, mu ba'a gayyatar mu a wajan?" Ta ce "Ku ai ƙatin ƙatinne" ta faɗa tana kallon Aafiyyah da ta yi luff a cinyarsa ya ce "Lallai, to Allah ya raya ki yar nan. Ina Aliyu?" Ta ɗan yi shiru sai kuma ta ce "Baya nan" ya ce "As always.... Ke ɗaga ni" ya faɗa yana ɗago Aafiyyah, ta tashi tare da zaro shade glasses ɗinta ta saka a idanunta ya yi mata kyau sosai,

ta buɗe mota ta fito, Black ɗin abaya ce a jikinta expensive one, hannunta riƙe da L&G handbag, sallama ya yi musu ya juya Safiyyerh ta ce "Sai yanzu?"

"Na koma kenan?"

"A'a ban ce ba" suka tsaya a jikin wata bishiya dake harabar wajan, daidai nan drivern Kimiyya ya shigo wajan, a daidai nan shima ya buɗe ƙaramar ƙofar gidan ya shigo, yana cika da batsewa, at the same time kuma wasu manyan lafiyayyun ƙadangaru suka rikito kan su Safiyyerh ɗaya ya shige cikin rigar Aafiyyah, ɗaya ya sauka a saman fuskar Safiyyerh. Safiyyerh ta saki wani gigitaccen ihu tana kiran sunan daddy, ƙadangaren ya sake mannewa a fuskarta, Aafiyyah kuma ajjiyar zuciya ta sauke jin kai tsaye cikin rigarta ya shige, ta cake waje guda ta kasa motsi. Yadda take tsuma ita kaɗai ya ja hankalinsa, ya kuma dubi yadda Safiyyerh ke ihu tana neman shiɗewa ya yi kamar ya share sai kuma ya ƙarasa wajan, yana zuwa Safiyyerh numfashinta na ɗaukewa a hankali ya ce "DEER....." sai kuma ƙadangaren ya samu ya sauka ya yi baya da gudu, ya ɗaga kai ya kalli Aafiyyah suka haɗa ido, ya kalli ƙirjinta dake ta motsi alamar ƙadangaren na ciki kuma kamar bashi kaɗai bane a hankali ya sake cewa "TIGER....." Sai ya nufeta yana zuwa ta cafke hannunsa, ta riƙe ƙam zufa na yanko mata, cikin sauri kuma Safiyyerh ta miƙe bata ma kula da shi ba, a gigice ta nufi ƙofar fita, tunda taga kimiyya shi ɗaya to ba zai zo ba kuma ta yi alƙawarin zuwa har gidansu. A hankali Mutallab ya kalli Aafiyyah dake kallonsa, ya sake duban ƙirjinta sai kawai ya saka ɗaya hannunsa ya cafko ƙirjin gabaɗaya, hakan ya yi daidai da shigowar motar daddy kuma kai tsaye ganinsa ya sauka akan fuskar Mutallab da hannunsa dake riƙe da ƙirjin Aafiyyah ita kuma ta riƙe hannunsa.

Mutallab

Pay before you read

₦500.

0116886423 Union Bank Na'ima Sulaiman S. Shaidar biya ta nan 08164069385

Follow me on Arewabooks ❤

[1/7, 9:35 PM] Sis Fauzy: Chapter 30: Safiyyerh & Aafiyyah

Kimiyya ne ya bi bayan Safiyyerh da sauri yana kiran sunanta, da ɗan gudu take tafiya bata ganin ko gabanta saboda hawayen daya cika cikin idanunta, ganin tana ƙoƙarin kai wa ƙarshen street ɗin yasa Kimiyya ƙara gudu har ya cimmata, ya tsaya a gabanta tare da yi mata duba na tsanaki "Safiyyerh....." Ta ɗaga masa hannu idanunta jiƙe da hawaye ta ce "Safiyyerh me?."

"Mu koma gida don Allah"

"Sai a yi me a gidan? Me ya sa yake haka? Me ya sa baya cika kalamansa me ya sa yake yi kamar babu zuciya a ƙirjinsa, bai yi kama da mara imani da tausayi ba, me ya sa ni yake son gina tunanina da hakan? Me ya sa yake sawa da abin da nake ji a zuciyata? Is he even okay?" Kimiyya ya ji tausayin Safiyyerh, domin shima yana cikin yanayi irin nata, koma fiye da nata, sai dai suna da tarin bambanci kasancewar shi namiji mai haɗiye abubuwa da yawa a ransa, bai kuma juriya saɓanin ita data kasance ƙashin haƙarƙari mai fidda rauninta a fili, wacce bata iya controling kanta ta kuma ɗaukaki soyayyar Mutallab a cikin zuciyarta fiye da zaton duk wani mai tunani. Ya sauke numfashi kafin ya dube ta ya ce

"Da kika fito yanzu a haka sai ina? A cikin wannan duhun?"

"Zani wajan shi ne, na ji abin da ya hana shi zuwa" Ya dinga kallon ta sai ya yi murmushi ya ce "Oh, to ai kin baro shi a cikin gidan naku tuni" Ta buɗe ido ta ce "Da gaske ko wasa, ka mini wasa da komai banda lamarin bestie" ya ce "Me ya sa na makara? Saboda shi ne ai kin san da yadda ya zo? Sai dana haɗa shi da Jeddah, so you have to appreciate me"

"Aikin da ka yi, Allah ne zai biya ka domin zuciyar Safiyyerh ka ce to thank you dear" ya ɗage mata kafaɗa ya ce "A'a ba wani thank you, rabin cake za'a bani shine tukuci na, shawo kan mutum kamar buddy abu ne mai ɗan banza wahala. Mutum ne kamar me ba'a taɓa gane masa ba'a saka shi sam yin abin da bai yi niyya ba, da kuma ya yi miki alƙawari zai zo, so he told you already ai ha zai zo ba, yanzu kar ki tilast masa yin abin da zai zo yana abin da ba shi kenan ba a cikin mutane"

"I won't...." Safiyyerh said, da murmushi a fuskarta har ta mance da batun ƙadangaren da ɗaurewar da numfashinta ya yi.

Tun kafin su ƙarasa shiga harabar gidan ƙirjinta ya yi wani irin tsalle tare da doka mata a tsakiyar zuciyarta, ganin daddy tsaye ga Mutallab sai Aafiyyah, wacce take zaune saman kujera ta sunkuyar da kanta ƙasa, har lokacin fuskarta sanye take da shade glasses ɗin. Idan ta tuna yadda ya cire ƙadangarun guda biyu da suke faɗa da juna a cikin rigarta sai ta ƙara jin ta yi addition akan tarin tsanar da ta yi masa, madadin minus a'a, Aafiyyah kullum addition take. Daddy ya juya ya kalli Safiyyerh da idanunsa da suka sauya launi, ya yi mata wani irin kallo wanda yake alamta mata cewa tuhumarta yake ta yi ƙasa da kanta. Daddy na kallon yar tasa ya yi poiting Mutallab da hannunsa ya ce.

"Safiyyerh, who is he? Waye shi, what he bring him to my house? What exactly abin da yake yi a cikin nan?" Safiyyerh couldn't speak; ta dinga girgiza masa kai ta kasa furta komai sai ƙanƙame jikinta da ta yi da ƙarfi cikin tsawa ya ce "Ya zama tambaya ta ƙarshe da zan miki, da zan nanata miki ina fata ki ƙaryata tunanina da zatona akan ba gayyatar shi kikai ba, he isn't... Baya daga cikin baƙin ki Safiyyerh"

"Waye wannan Safiyyerh?"

"Abokin Kimiyya ne tare suka zo daddy" ta faɗa hawaye masu zafi na sakko mata, ta ji ta tsani kanta a dalilin ƙaryar da ta yi wa daddy, da kuma ƙasƙantar da kimar Mutallab da ta yi a gaban jama'a da kuma yan ajinsu, ta yi hakanne don kuɓutar tare da kautar da zargi daga zuriyar daddy. Aafiyyah dai na zaune tana danna waya, tana kuma jin komai ba zaka taɓa cewa ta san me ake yi ba. Mutallab kuma yana tsaye ya zubawa Safiyyerh idanu, kamar mai yin studying halin da take ciki, ya cije lips kawai. "Bake kika gayyace shi ba?" Ta girgiza masa kai ya juya ya kalli Mutallab, sai kuma ya kalli Kimiyya da sauran wanda suke wajan ya ce.

"Kimiyya ka bani mamaki, gaka yaro mai hankali da nutsuwa mahafinka ɗan mutunci mai ƙashin arziƙi wanda ya baka tarbiyya, ya ɗora ka a tubalin daya dace, ya ci da kai, ya shayar da kai da tufatar da kai daga taskar arziƙinsa. Amma ka ƙare da zama tare da tantirin yaro iron wannan?" Ya nuna Mutallab ya ɗora da faɗin "Mai ubansa yake da shi a unguwarsu, balle garin balle ƙasar? Wanne mataki ubansa ya taka ko wani ɗan'uwansa? Prof ne ubansa? Engineer, Dr, Alhaji, Senator, Rep, custom, Governor or President? Soldier or police? Waye ubansa daga cikin

waɗannan abubuwan dana faɗa?. Yaron da bashi da cin yau balle na gobe da shi kake mu'amala har ka jawo mini shi cikin gidana? Kasan waye shi bari ka ji to, sau biyu ina zuwa state cid ina ganinsa an ɗaure shi, ko dana bibiya cewa aka yi ya gagari iyayensa shine aka bawa iyayen shawarar a yi masa aure ko zai nutsu, dake iyayen wawtattu ne kamar shi suke tunanin yi masa aure shine zai kawo ƙarshen matsala ko a ina aka taɓa aurar da yaro kamar shi?. Sau biyu suna nema masa matar da zai aura sai an kusa biki sai a samu ya cinnawa yarinyar wuta ta mutu, yanzu haka cases ɗin dake kansa wanda kuma akai recorded nasa akan batun kisan mata biyun ne, ubansa malamin allo ne na ji labarin har mari ya taɓa ɗaura masa" Daddy ya yi maganar cikin zafi da ƙonar rai, sai turanci yake yana jefa Hausa kamar zai taune harshensa ya ce.

"So all this... Kuka jawo mini dauɗa cikin gidana?"

"Ƴarka ta yi maka ƙarya, idan ni ne ita ba zan ƙarya ba saboda ina tsoron Allah ya kama ni a kan hakan, ko ana zaka gane bambancin tarbiyyar talaka dana mai kuɗi". Daddy ya juyo ya kalli Mutallab, Kimiyya zai wa Mutallab magana ya hankaɗe shi. Daman wani blue black ɗin yadi ne mai kyau a jikinsa daya sha goga kasancewar yana da ɗan kauri kayan ya kama shi ya yi masa kyau duk da duhun fatarsa. Mutallab ya nuna Safiyyerh data daskare ta ƙura masa kallo irin why are you doing this to bestie? Ya yi murmushin gefen baki.

"Za ka ji kamar bani da ɗa'a ko? Da iya kai na ne zan maka shiru amma ka taɓa martaba ta da abin da nafi ƙauna a duniyata; mahaifina. Ni dai ban taɓa ganinka ba, balle na nemi alfarmar wani abu a gare ka har ka goranta mini, domin iyayene kawai a duniyar nan suke wa yaransu abu ba don son kan su ba, su dai buƙatarsu yaransu su yi nasara, na ji nawa iyayen basu da wannan halin, ba'a taɓa kama mahaifina da laifin sata ba. Muna rayuwa a yadda muka tsinci kan mu, babana malam ne bai sam komai ba sai almajiransa da allo da tawada, ni ma kuma ina rayuwa ne a yadda ta zo mini bana ɗorawa kai na abin da bani da shi, kuma ina tsagewa iyayena gaskiyar dake ƙirjina koda za su hukunta ni. Yarinyarka ta maka ƙarya, ita ke bibiyata, ita ce ta addabi rayuwata, ita kuma ta gayyato ni nan da sharaɗin idan ban zo ba zata je har can gidan Malam Abdullah mai allo da almajirai ta dawo da ɗansa, arziƙi ba shi ne rayuwa ba, ka zauna cikin farin ciki hakan ma ya wadatar". Da ƙyar ya ƙare maganar saboda muryarsa data shaƙe a maƙoshinsa ya kafe Daddy da kallo ya ce "Da na so zan yi arziƙi fiye da kai, ka ji daɗi ka huta masu arzƙi"

Ya taka a hankali ya juya sai kuma ya juyo jin Kimiyya ya riƙe shi kafin ya yi magana daddy ya ce.

"Daya daga cikin halayyar talaka da yaran talakawa, su ji cewa mai arziƙi ne ya tare musu hanyoyin ƙofar samu, banda rashin tarbiyya har ni kake kallon idanuna kake faɗawa haka? Idan duka ubanka baya abin da ka lissafa amma halinsa ne auri saki, ya tara yara kamar kaji ya sallama su, na san komai a kanka tun ranar dana kanka na ji ba ka yi mini ba" sheƙeƙe yake kallon daddy sai bai ce komai ba, da sauri kuma Aafiyyah ta tashi tare da barin wajan daman tuni ta sakawa kunnenta earpiece bata jure hayaniya. "Fita ka bar mini gida "

"Bestie...."

Safiyyerh ta kira shi a gigice tana sakin kuka zata bi bayansa daddy ya ce "Idan kin amince ni mahaifinki ne, idan kin gamsu cewa nina kawo ki duniya, idan kin ji a ranki dole ki mini biyayya ya zama dole ki kiyaye kula shi.

Wallahi by mistake kika ƙara taku guda za ki sha mamaki Safiyyerh...." "Daddy please!" Ya yi shigewarsa cikin gida rai ɓace. Ta sulale a saman ƙafafuwanta ta saki wani irin raunataccen kuka, zuciyarta na bugawa tana jin numfashinta na tafiya daidai ta takun sawayensa, fitarsa daga cikin gidan sai ta ji kamar ƙarewar rayuwarta duhu ya mamaye cikin idanunta, tamkar wata ya nutsa cikin kwanaki ashirin da bakwai don duhu, zafin da ƙirjinta ke sai take ji kamar dalma ake ɗiga mata ta dinga kallon ƙofar, jikinta na rawa zuciyarta ta dinga cewa "Follow him, bishi, follow him Safiyyerh, your love is runaway bestienki"

"I am sorry daddy...." Safiyyerh said loudly. Tana miƙewa.

Da gudu ta kwasa tare da bin bayansa, ganin ta yi waje ya saka Wahee juyawa da gudu zuwa cikin gidan to tell daddy cewa Safiyyerh ta bi bayan Mutallab. A tsaye ta ganshi yana danna waya fuskarsa wasai kamar bashi aka wulaƙanta ba, ta dinga kallonsa shi kuma ya mayar da wayar aljihun gaban rigarsa Safiyyerh ta fashe masa da kuka tana ƙoƙarin shigewa jikinsa ya yi saurin yin baya ta girgiza kai ta ce.

"I am sorry for what I did, i am sorry for what my father did, I am sorry for what we did to you. Ba wata kalma da zata iya tausasa zuciyarka a yanzu, babu tabbas" ta

share hawayenta tana kallonsa kamar yadda yake kallonta ta ce "Ka tuna? Ba na ce zan faɗa maka wani abu ba? Ba na ce zan baka gift ba?..... Bestie I LOVE YOU"

“I LOVE YOU”

Ya ji kalmar har tsakiyar kansa haka ya ji ta dirar masa, ya dinga kallon Safiyyerh domin har lokacin tunaninsa bata da lafiyar ƙwaƙwalwa kamar dai shi. "Can you love me? Za ka iya so na?" Yaƙi magana, ya kuma ƙi tafiya ya kuma ƙi daina kallonta, a daidai nan Aafiyyah ta fito sai a lokacin Safiyyerh ta lura da driven Aafiyyah ta ce "Wai tafiya za ki yi?" Ta cire shade glasses ɗin idanunta, ta kalli Aafiyyah da idanunta da suke tarr, wani irin kallo ne mai nufin You disappointed in me, you disappointed me Safiyyerh!..... Sai kuma ta ɗaga mata gira ta ce "Me za a yi after wanda kikai yanzu Safiyyerh? Kin kawo mana shasha ya rusa komai ya lalata komai, ba wani abu wanda ya fi haka, sai ki basa cake ɗin damar kamar shi ya biyo.... Ai wallahi Safiyyerh kin faɗo wanwar, akan wannan abin? saboda shi za ki saka ƙafa ki rushe sharaɗin mahaifinki, yanzu na sake yarda ƙuruciya na damunki"

"Aafiyyah Please, kar mu fara haka dake ko dan alaƙar dake tsakaninmu. Batun ƙuruciya ni za ki kalla ki cewa ina ƙuruciya, ki sani na riga jin iskar duniya ko tazarar daƙiƙa ɗaya dole ni na fara zuwa duniya kafin ke, balle ya shige haka. Idan har ba za ki iya taya ni fighting akan soyayyarsa ba, bai kamata ki ƙuntata mini ba, ko za ki ƙuntata mini kina yi i will take it, but i won't take it idan za ki wa"

"Shi wa?" Aafiyyah, asked Safiyyerh; tana rungume ƙirjinta da hannu bibbiyu ta tambayi Safiyyerh Abdu Marafa, tana sake juya idanunta ga wayarta dake ta ringing silently.... "Wannan?" Ta nuna Mutallab dake tsaye ko inda take baya kalla ta ce "Lallai kin yi asarar bakinki idan akan shine, kuma har yanzu ba ki san waye Aafiyyah Abdu ba, bana ɓata lokacina akan abin da ba zai amfane ni ba, balle akan shi, balle na taya ki ɓatawa mahaifinki rai" Aafiyyah ta yi maganar tana murmushi ganin yadda ta kunna Safiyyerh gashi bata iya faɗa ba ko kaɗan idanunta ya cicciko da hawaye muryarta na rawa da ƙyar ta iya kallon Aafiyyah ta ce.

"Now, now Aafiyyah. Mind your manners" yanzu, yanzu Aafiyyah ki iya kalamanki.

Aafiyyah ta ɗaga kafaɗa ta juya zuwa inda motarsu take, kafin ta ƙarasu ma an buɗe mata ƙofar bayan motar, wanda ke ciki ya rufo dirver ya ja a hankali tare da

yin reverse ya juya kan motar. Aafiyyah na shiga cikin motar, ta cire rolling ɗin kanta, ta ajjiye ta sunkuyar da kanta ƙasa tana sauke numfashi. "Yaya aka yi? Faɗa kukai ne?" Ta kasa magana sai kawai ta sakar masa kuka tana faɗawa jikinsa ta ƙanƙamesa, he hold her back, very tight, ta dinga kuka da ihu a motar tana birgima a jikinsa "Na shiga uku Yaya, na shiga uku yaya, wayyo yaya" sune kawai abin da take iya faɗa, wani irin karkkar jikinta ya ke yi, lokaci guda kuma jikin ya ɗauki zafi sosai, ya kasa mata magana sai kanta daya ɗora a saman ƙirjinsa, he could feel yadda hawayenta ya jiƙa masa gaban riga, duk yadda yake ƙokarin rarrashinta amma ta ƙi fahimta sai buga ƙafa take ƙaramar mitsitsiyar yarinya, bayan rungumeta da ya yi bai sake magana ba, sai ya ji tana sauke ajjiyar zuciya ta yi lamo Jikinsa ya ce "Mene ya haɗa ku?" Ta ɗago kai ta kalle shi da jiƙaƙƙun idanunta, ya kama fuskarta ya fara share mata hawayen ta ce "Dawa?" Kai tsaye ya ce "Safiyyerh...."

"Oh, ba komai ni fa kaina ke mini ciwon sosai ba ka ji ba"

Ta ce tana langwaɓar da kanta gefe, zai magana sai kuma ya sake ganin ta saki wani raunataccen kukan tana rirriƙe kanta ya buɗe ido ya ce "Subuhanallahi, Safiyyerh.... Safiyyerh!" Ya faɗa a ruɗe ganin ganin tana sanƙamewa ta kasa jan numfashi "Driver, asibiti please wanda ke kusa damu" ya ce yana cigaba da kiran sunanta da jijjigata.

After Aafiyyah lefted, sai ta ji wani nutsuwa sai dai kuma bata ji daɗin yadda suka rabu ba, basu taɓa yin faɗa ba ta ji ta damu akan maganganun data faɗawa Aafiyyah, amma ai ita ta fara faɗa mata komai, ita mema ta ce what exactly her fault?. Ta juyo ta kalli Mutallab da ta ji ya ce

"Zan tafi" ta marairace fuska tana ɗan buga ƙafa ta ce "To mu koma ciki, a yanka cake ɗin"

"Shekararki nawa ne?"

"Age mates muke da kai"

"Ƙarya kike... Ki koma gida"

Mutallab ya ce, domin shi yanzu uzuri yake mata, ba kuma lallai ta gane nufinsa yana son kyautata mata da gaske su zauna lafiya, domin duka yan'uwansa wanda Allah Ya basa mata ne irinta, mata ne kamar Safiyyerh masu rauni, but no love just friendship, shima

ya ɗauki hakan kamar childhood friends da zarar ya san me yake ba zai iya cigaba da ƙawance da wata mace ba. Ta kalle shi ta ce "Zaka zo makaranta gobe ai?" Ya ɗage mata gira, itama ta ɗage girarta tana masu wani irin kallo fuskarta ɗauke da kyakkyawan murmushi ta ce "Wai ya aka yi ka cirewa Aafiyyah lizards ɗin nan?"

"One day, i will tell you, u most laught" ta yi murmushi.

Ya juya ya fara tafiya a hankali, he looks so classy a nutse yake sosai. Har ya ɓacewa ganinta ta ja ajjiyar zuciya da sauri kuma ta juya zuwa cikin gidan, sai a lokacin ta lura ai duka babu kowa sai Captain dake zaune tare da Wahee sai kuma Kimiyya da ya yi shiru tun bayan tafiyar Mutallab. Bata kalli kowa ba ta shige cikin gidan nasu kai tsaye.

Daddy dake tsaye ta can saman bene ya saki labulen windown ɗakin Safiyyerh a hankali, tun bayan fitar ta yake tsaye a saman benen yana kallon komai, har tafiyar Aafiyyah har lokacin tafiyar Mutallab da sanda ta juyo ta dawo cikin gidan. Ya daɗe tsaye a wajan kafin ya nemi waje ya zauna a saman gadon Safiyyerh kamar mai jiran shigowarta. A hankali ta buɗe ƙofar ta shigo, ta yi turus ganin daddy zaune ya harɗe ƙafafuwansa waje guda ya zabuwa ƙofar idanu, da wani irin sauri ta juya zata koma waje ta daki jikin Ummeyh dake shigowa itama fuska a haɗe, ta saka hannu ta tura Safiyyerh cikin bedroom ɗin ta janyo hannunta ta dunƙufar da ita gaban Prof. Gabaɗaya takaici ne ya hana shi magana wai yau shi aka bijirewa magana? Ya dinga kallon Safiyyerh wacce ke durƙushe ƙasan ƙafafuwansa.

Ummeyh ta ce "Aliyu yana kan hanya, yanzu yake sanar mini sun samu hutu Allah Ya sa kar ya ce ya fasa dawowa nasan hali"

"Zan zo ya zo ɗin, zan so kuma a ce kar ya zo ɗin...." Ya furzar da iska daga cikin bakinsa ya juyar da kansa ya zubawa photon Safiyyerh idanu dake gefen gadonta idanunsa na juyewa ya ce "Me ya sa Safiyyerh? Ya kike abu kamar ba professor

Abdu ya haife ki ba? Ya kike abu kamar ba jinin ilimi da arziƙi ba? Me ya sa, why Safiyyerh?"

"I'm sorry daddy....."

"Sorry for yourself, sorry for yourself Safiyyerh!"

Ta yi ƙasa da kanta, ya gyara zama sosai ya ce "Ya sunansa?" A hankali ta ce "Mutallab" daddy ya ce "Nice name, mene sana'arsa data mahaifinsa, mene alƙarki da shi kuma? Da har kika manta cewa ni mahafinki ne?" Ta yi shiru, Ummeyh ta buga mata tsawa sai ta fashe da kuka ta ce "Ummeyh daddy don Allah ku yi haƙuri ba zan sake ba" daddy ya kalli Ummeyh ya ce "Dr dai na yi mata tsawa kar ki firgitar mini da yarinya for no reason" Ummeyh ta ce "Ba wani dalili? Wanne dalili bayan abin da muka gani da wanda ta aikata Prof?" Idanunsa still akan Safiyyerh ya ce "Still dai, mu ji daga bakinta. Safiyyerh" ta kalli daddy cikin shasshekar kuka ta ce masa.

"Mutallab sunansa"

"Na haddace sunan ai, ba kya buƙatar maimaita mini"

"A makarantarmu ta FGC yake, class ɗinmu ɗaya ajinmu ɗaya, kujerarmu ɗaya, abokina ne kawai na karatu. Ai baya sana'a nima ai kaga bana yi karatu muke, wallahi daddy he is the nice person yana da kirki.....,"

"Waya tambayi kirkin nasa?" Daddy ya ce yana gyara zamansa a hankali kuma ya janyo wayar Wahee dake kusa da shi ya fara dannawa. "Kalli Wannan Safiyyerh" ya juya mata screen ɗin wayar, muryarta ya sauka raɗau inda take kuka cikin cafeteria tana cewa "What if I tell you, I love you" ta runtse idanunta zuciyarta na rarraɓewa into pieces "Wahee munafuka" ta faɗa a ƙasan ranta kanta a ƙasa. Idanun daddy ya yi jajur sosai ya ce "Abin da kike a makarantar kenan shi ya sa kika zama daƙiƙiyya? Shine abin da na tura ki yi a FGC ɗin kenan ko?"

"I'm sorry….." She gasped out, double over in pain and trying to catch her breath. "Wanne sorry? Sorry to tell me that you love him? Ɗan mai makarantar allo da almajirai? Soyayya at your young age? Yanzu me kike buƙata?" Kai tsaye ta ce "A aura mini shi" wani irin juyawa Ummeyh ta yi ƙirjinta na bugawa da ƙarfin gaske zata daki Safiyyerh, daddy ya girgiza mata kai ya ce "Shi Ɗan'malam ɗin? Karatun kuma fa?" Ta ce "Bana son karatun Daddy, bana gane masa auren nake buƙata" Ummeyh ta zauna daɓas tana zabga salati, ba tare da daddy ya tambayi dalilin rashin gane karatun nata ba ya ce "Ƙila ke da Fgc har abada, ƙila mu bar ƙasar gabaɗaya, batun aure ke da wancan ɗan me makarantar allon babu. Safiyyerh shekara 15 kike a duniya kin san wai a yi miki aure, me kika sani a rayuwa?" Ba ki ta buɗe da nufin cewa "Na sani mana daddy, I can tell you abubuwa da yawa akan aure daga cikin har irin abubuwan da kuke yi kai da Ummeyh cikin dare a kuma kullum, wanda surutunku da ihunku ya saka mini son abun, ka fuskanci kuma ba haka kawai ake samun abun ba sai dai idan anyi aure, daga lokacin kuma bana gane komai na karatu sai wannan mikin da kwaɗaitar son abun a zuciyata" haka ta yi nufin faɗa, sai ya katse ta da cewa "Bana son jin komai, bana son jin dalilinki na banza da iska, Wahee ta yi gaskiya. Za kuma ta cigaba da saka miki ido da ita da sauran ƴan'uwanki daga nan har na yanke hukunci. Kuma a gobe ban amince ki je makaranta ba, ki ƙaddara kin isa aure Safiyyerh babu Mutallab a jerin samarin daya kamata ya zama surukina, we may leave this country as soon as possible, as far as kin cigaba da yi mini taurin kai Safiyyerh"

Miƙewa ya yi ya fita, Ummeyh ta kasa cewa komai ita buɗaɗɗiyar zuciyar Safiyyerh ke bata mamaki, duk haƙurin Safiyyerh amma yau ta buɗe baki ta ce wai aure take so? Ga wata uwar ƙiba da take yi ƙirji ya haɓaka ga buɗaɗɗan hips skin ɗinta sai wani ƙyalli take yi. Miƙewa ta yi ta fice domin ta cigaba da zama zata iya zane Safiyyerh cif wallahi. A downstairs ta samu daddy na waya da Dr bayan ya kammala ya kira Uncle Musbah suka fara magana a hankali bayan ya kammala ya ɗago ya kalli Ummeyh sai ya yi murmushi ya ce "Ni Safiyyerh ke faɗawa aure take so? Ɗan zamani ka haifa baka haifi halinsa ba, zan nuna mata ni nake da iko da ita zan nuna mata ni na haife ta.

***Washegari Mutallab shi kaɗai ne a desk ɗin, babu Safiyyerh domin bata zo ba, haka Kimiyya shi kaɗai ne babu Aafiyyah koda ya kira wayarta tun jiya bai sameta ba. Gashi bata zo makaranta ba, har aka tashi daga school ɗin Mutallab bai kula kowa ba karatu kawai yake yi yana kuma fahimta. Bayan tashi ya bi bayan Kimiyya har zuwa ɗakin computer suka dinga danne-danne a hankali ya ce "Ina recorded ɗin nan?" Kimiyya ya ce "Yana nan" Ya jinjina masa kai, wani location ya nutsu yana dubawa ya yi hakan ta bin diddigin wata number, kai tsaye ya yi sharing location zuwa ga Computer Kimiyya da mamaki ya ce "Asibiti? Waye a can?" Mutallab ya ɗaga kafaɗa ya fice.

"Ya karatu Muhammad? Kimiyya ya faɗa maka sauyin ra'ayin da akai masa? Zai bar maka sabgar na'urorin nan, zai juya shi kuma zuwa ga zama barrister in sha Allah" Mutallab ya jinjina kai ta ce "Allah Ya yi muku Albarka"

"Amin" ya ce.

"Muhammad baka da wasu kaya ne sai waɗannan?"

"Ina jin daɗin su ne"

Ta dinga jan shi da hira jinjina kai kawai yake yi ko ya lumshe idanunsa, Kimiyya kuma daɗi yake ji a kullum idan ya ga Mutallab by his side sai ya samu kansa da jin zafin mahaifin Safiyyerh ƙwarai. Sun jima har Jeddah ta kwaso shadda su yadika ta bawa Kimiyya ta ce ya kaiwa tela ya ɗinkawa Muhammad ɗin.

Bayan sun fito harabar gidan idanun Mutallab ya sauka akan wasu kyawawan karnuka ƙanana da su an yi musu irin kiwon turawa, ɗaya baƙi da ɗaya ruwan ƙasa ɗaya mai ratsin baƙi da fari "Ma sha Allah" Ya furta yana durƙosawa akan ɗaya da ya fi jan hankalinsa. "My dogs karnunaka nane, ko kana so?" Mutallab ya jinjina kai, bai taɓa nunawa Kimiyya yana son wani abu ba sai yau ya ce "Take them, na bar maka" ya riƙe ɗaya da yafi faɗa da safi ya ce "Tiger" ya shafa ɗayan ya ce "Rainbow" ya kuma taɓa ɗayan ya ce "Spider" Kimiyya ya dinga jin daɗi, ya ɗauki ɗaya shi kuma ya kwashi guda biyu sukai waje. Sun isa gidansu Mutallab dake da ɗan tazara da gidansu Kimiyya, Mutallab ya lura kimiyya baya cikin nutsuwa can ya yi gyaran murya "Uhm emm, ya dai?" Ya ce "Aafiyyah bata ɗaukan kirana duk na damu" sai Mutallab ya yi shiru kawai cikin sa'a kuma aka ɗaga wayar Aafiyyah aka shaida masa ai tana kwance a asibiti tun ranar birthday ɗin Safiyyerh. "Asibiti?" Sai ya tuna location ɗin da Mutallab ya tura masa ya juyo zai yi magana tuni Mutallab ya tashi ya bar wajan.

"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, karnunka a cikin gidana masifa ta ƙaro na banu ni Malam Abdullahi"

Mutallab ya yi shiru. "Tattara tsinannun kayanka ka fice daga ɗakin zaure juma'a ta sama amaryata zata tare, kar na dawo naga komai ka je can cikin almajirai ka dinga kwana ban amince ka shiga ɗakin uwarka ba kana baligin yaro, domin wannan ɗan tsurut ɗin gemun a tsakiyar haɓa kamar na iska daka gani na girma ne ba zai haifar da ɗa mai ido ba" Mutallab ya sake yin shiru. Malam ya ce "Tijararre, ina magana" ya ɗago kai. "Aby na ji, zan fita In sha Allah "

"Malam aure za ka yi?" Cewar Sa'adah. Ya ce "E, kina da matsala da aurena ne Sa'adah?"

"Baka ciyar damu hakƙin ciyar da yaranka a wuyanka yake Malam"

"Ki je ki yi ta kan ki Sa'adah ki nemi kuɗi kici abinci, idan kin yi saura ki bani, bani da ƙarfi bani da halin ciyar da tarin yara kamar na maguna kin ji" yana cewa haka ya fice. Ammo dai murjin taliya take yi domin tun safe ake zuwa nema ta yi har ta ƙare.

Sati guda cif, ba Safiyyerh ba Aafiyyah a makaranta har an kammala c.a ana shirye-shirye fara exam ta 3rd term. Shi ko a jikinsa domin har yanzu maganganun Kimiyya na zane raɗau a zuciyarsa na cewa talauci zai zama abokin rayuwarsa, sai maganganu mahaifin Safiyyerh, wanda suka ƙarasa confidence wajan ganin zama mai arziƙi ko wani mai faɗa aji. Ya samu sassauci daga wajan Ammo ta sakko tana kula shi wanda bai san dalili ba sai ya samu relief a zuciyarsa nutsuwa ta saukar masa sosai ya ƙara jin ƙaunar iyayen nasa har da Aby.

Yana zaune a gida a lokacin yana jin yadda karatun Almajirai ya cika masa kunne ya yi kicin-kicin da fuska. Ammo ta kalle shi ta ce "Yau kuma waya taɓa jarumin Ammo?" Ya yi mata shiru don bai fiya cewa komai ba idan ran shi ya ɓaci kafin ta sake magana wani yaro ya yi sallama ya ce "Wai bestie ya zo in ji bestie"

"Waye bestie? Injiwa jeka tambayo"

Mutallab a lokacin bai motsa ba ya hakimce kamar sarki kansa a ƙasa yaron ya dawo ya ce "Wai in ji Safiyyerh matar Mutallab bestie"

Baki buɗe Ammo ke kallon Mutallab ta ce "Na Ammo yaushe ka yi aure bani da labari yau naga abin da ya fi ƙarfina, yara ƙananu daku wacece Safiyyerh?" ya miƙe tsaye daga shi sai gajeren wando ta wata riga ƙarama "ban san ta ba"

"Ikon Allah"

Fita ya yi yana shan kunu ganinta tsaye suna haɗa idanu ta yi ƙasa da kan ta. Ya dinga kallon ta yana jiran ya ji mene "meye ne?" Ya tambaya. Hawaye ya gani a idanunta fal "Ni a gidanku zan kwana" tar ya gama buɗe shanyayyun idanunsa a kanta "wanne gidan?" Ta nuna masa gidan "sai ki ce ke wa?" Tana masa shagwaɓa wacce daman ya san hali tace "Matar Mutallab, baka zo makaranta ba yau ba kyau fashi" ji wacce ta shafi sati bata je ba ita ke faɗa masa yau bai je ba, kuma haka kawai ya ji baya ra'ayin zuwa makarantar. Ya cigaba da danna wayarsa ya barta tsaye, ita kuma sai kallon jikinsa take ya yi mata kyau sosai cikin ƙananun kayan daya saka sumarsa duk a birkice sai taga ya ƙara girma a idanunta da kwarjini ga wani tsayi da ya yi damtsen hannunsa wani abu kamar laya a duka hannu biyun. Ya ɗago kai ya kalleta suka haɗa idanu a hankali ta ce "I love you bibi" ya watsa mata harara kamar kuma an ce ya juya idanunsa ya sauka akan daddyn Safiyyerh daya fito daga cikin mota hannunsa riƙe da zabgegiyar bulala. Da wani irin ƙarfi Mutallab ya ce "Safiyyerh!" Ganin kai tsaye daddy ya yi kanta.

MUTALLAB.

PAID BOOK NE

PAY BEFORE YOU READ DEAR..... 08164069385

[1/7, 9:35 PM] Sis Fauzy: Chapter 31: Yaa Muhammad

Not edited

Kallon Safiyyerh kawai daddy yake yi, irin kallon da yake nuna na haifi yarinya a cikina tana neman fin ƙarfina, idanunsa jajur saboda ɓacin rai ya ce "Ba shakka Safiyyerh, ashe kin yi girman da za ki saci hanya tun daga gidan ubanki zuwa wajan saurayi? Saurayin ma ki biyo shi har gidan nasa iyayen Safiyyerh? Anya...." Ta yi ƙasa da kanta a hankali kuma take jan jikinta zuwa bayan Mutallab saboda bulalar dake hannun daddy. Ɓacin ran daddy ya kuma bayyana a fili wai yau shi Professor Abdu, yʼar cikinsa guda ta nemi fin ƙarfinsa? Duk yadda ya kai da yi mata bazarana akan yaron nan amma kamar ƙara tunzurata yake yi.

"Safiyyerh nuna duniya kike ban isa dake ba? Ki rasa wa za ki so a duniya sai mai kashe yʼan'mata? Mai lalata su, ki rasa wa za ki ji kina ƙauna sai ɗan talaka futuk, ki rasa wa za ki ji kina ƙaunar rayuwa da shi sai wanda ubansa bai bar masa gadon komai ba sai na allo da tadawa? Ɗan'malam mai almajirai Safiyyerh? Shi Safiyyerh? Har ki iya fakar idanuna ki biyo shi?...." Jikinta ya dinga rawa, ta sake maƙalewa a bayan Mutallab idanunta na cika da hawaye, Mutallab shi ko a jikinsa kallon daddy kawai ya ke yi. Takaicin daddy ya sake ruɓanya a cikin ƙirjinsa da zuciya.

"Kai ne ɗan iskan da yake hure mata kunne ko? Kai ne kasa ta fara bijirewa umarnina?"

"Ask her....." Mutallab ya faɗa a daƙile, idanunsa a ciki yana murza goron da yake damtsen hannunsa na dama. Daddy ya ce "Ka fita sabgar yʼata, ka fita daga cikin idanuna babu kai babu jinjina, kuma wallahi ƙararka zan yi wajan hukuma su raba mu" a gigice Safiyyerh ta fito daga bayan Mutallab, tana girgizawa daddy kai muryarta na rawa ta ce "Daddy ni na zo wajansa, daddy ni na ce ina son shi don Allah kar ka yi masa komai, kar ka ce zaka haɗa shi da hukuma Please"

"Akan wannan ɗan iskan kike magana? Wannan wanda da bashi da wani future mai kyau a rayuwa?"

Mutallab ya ce "Ka ɗauki yʼarka kuje ina da abin yi, don Allah ka ce ta rabu dani kar ta lalatawa iyayena ni, Ɗan'malam ɗin da kake magana ai bai taka zuwa ƙofar gidanka ba ya ce ana sallama da Safiyyerh ɗiyar Professor. Ita yʼar taka yʼar masu kuɗi ita ke bibiyar rayuwata, ita kuma ta addaba mini, bani da wani sukuni ita ce mara tarbiyyar, ita ce mara ajin, ita ce mai neman ribatar zuciyata, ita ke son lalata mini ƙuruciyata, ita ta aiko har cikin gidanmu wajan mahaifiyata ta ce tana sallama dani, so Please carry your daughter and leave, idan kuma za ka kyauta ka saka ta

daina bin Ɗan'malam kuma ɗan talaka" ya ƙara maganar yana huci idanunsa akan cikin na surukin nasa. Safiyyerh ta dinga girgizawa Mutallab kai, tana fashewa da wani irin gigitaccen kuka mai taɓa zuciya kamar ta haɗiye zuriyarta ta mace haka take ji don damuwa.

"Idan ma asiri ka yi wa Safiyyerh sai dai ya koma maka ka, domin ko aure Safiyyerh ta isa sai da a yi ƙwarya ta bi ƙwarya domin kowacce ƙwarya akwai burminta" daddy ya yi furucin yana nuna Mutallab da yatsa shi kam ko a jikinsa, almajirai suka fara taruwa a wajan suna kallon yadda daddy ya damƙi hannun Safiyyerh, bayan ya falla mata lafiyayyun maruka a fuska, tsananin gigitar da ta yi da yadda marin ya shige ta ya saka ta ƙanƙame mahaifin nata, tana fusgar numfashi ta kasa kuka yatsun hannun daddy ya fito jere a fuskarta ya damƙi hannunta ya buɗe mota ya cilla ta a ciki, kamar zai tashi sama haka ya ja motar ya bar unguwar yana baɗesu da ƙasa.

Mutallab ya bi motar da kallo, ya ji wani iri a ƙirjinsa sai dai ba zai kwatanta abin da ya ji ba, domin bai san ma'anar hakan ba. Ya jima tsaye yana tunanin to dame Ubangiji ya tauye shi da shi? Saboda kawai su talakawa ne? Kenan talaka ba zai iya aurar yarinyar masu kuɗi ba? Ita soyayya ta gaskiya kuma ta domin Allah ai bata duba kuɗi, nasaba ko cancanta, mutumin da kake so shine kawai a allon ƙirjinka da idanun zuciyarka... The person you loved, you still love him/her for no reason, you love him/her for the sake of Allah, for the sake of love da baya shawara da zuciya. Kuɗi na siyan soyayya, na siyan komai na rayuwa banda kwanciyar hankali da lafiya, duk auren da aka yi shi domin kuɗi baya nisa zai lalace. Ya lumshe idanunsa da ƙyar ya buɗe su, ya sake bin hanyar da motar daddyn ta bi sai ya ja ƙafafuwansa ya koma cikin gidan har lokacin Ammo na zaune tana aiki, ya yi tsaye yana jan numfashi tare da furzar da iska daga cikin hancinsa.

Ta ɗaga kai ta duba shi kamar za ta yi shiru sai kuma ta ce.

"Hayaniyar me nake jiyowa daga waje har nan cikin gida? Muryar waye kuma a wannan lokacin?"

"Mahaifinta....."

"Mahaifin wa kuma?"

"Safiyyerh....!"

Ya ce a hankali yana danna wayarsa ba tare daya kalli Ammo ba. Ta dinga kallonsa, sai ta tuna muryar yaron ɗazo da yake cewa “Wai in ji Safiyyerh matar Mutallab bestie ” tuna hakan ya saka Ammo cewa "Wace ita Safiyyerh ɗin?" Ammo ta buƙata da mamaki fal fuskarta cikin yanayin na shakku da kokwanton abin da zata ji ɗin daga bakinsa, ta san baya ƙarya, kuma ba zai taɓa faɗa mata abin da ba ita ta tambaya ba komai nasa yana da tsari, ta dinga kallonsa don ta ɗauka ba zai yi magana ba kamar yadda ta tsammata haka ɗinne ba tare daya kalleta ba idanunsa ƙasa ya fara bata raddi da faɗin.

"Wai so na take yi, shine kawai" ya ce yana lumshe idanunsa tare da saka hannu ya shafa sumar kansa da take baƙa ƙirin. "So kuma?" Ta yi furucin da madaukakin mamaki sai kuma ta ce "So na mene kenan?" Ya ɗaga kafaɗa yana miƙewa tsaye ta ce "Dawo ka zauna Muhammad" ya yi jim sai ya koma ya zauna domin allurar shiga daji ce ta tsikare shi ainun..ta duba shi ta ce "Bani labari" Ya ja numfashi ya sauke a hankali kuma ya kwashe labarin komai ya faɗa mata, banda yadda akai ya shiga makarantar iya abin da ya faruwa between him and her. Ammo ta ce "Ikon Allah, to ka daina kula musu yarinya kaga dai abubuwan da suka faffaru ina goje mata zama gawa ta uku, kuma babu mamaki shima yana da nasa dalilin, kuma kowacce ɗiya mace ai da kamon kai aka santa, nutsuwa, da kamala bai ci ta biyoka har gidan iyayenka ba, su mata ai da alkunya aka san su, ita ma zan mata uzurin wawta da ruɗin ƙuruciya da na zuciya, yarinyata ce ba wani abu ba" jin Ammo yake bai tanka ba, ta nisa ta ce "Oh wannan zamani ina zaka damu? Shine har da cewa wai matarka ce? Allah Alhakkamu"

Da zai iya murmushi ko yaya ne shi zai yi, amma ba kasafai ya fiya ba, musamman Ammo wacce a kwanakin baya da suka shuɗe ta gama gasa shi da fushinta mai albarka. Sai ya ɗan cuccure girarsa waje guda ya tsuke su yana miƙewa tsaye, kamar zai fita sai kuma ya dawo ya shiga ɗakinsa wanda kullum malam yake cewa ya fita. Kamar yadda baya gajiya da karanta saƙwannin a kullum da yake musu karatun zuban hadda, haka yanzu ma ya kwaso su kashi na uku kenan, hadda ranar birthday ɗin Safiyyerh. Ya tanƙwashe ƙafafuwansa yana kumbura zuciyarsa dake rayuwa a ƙirjinsa take motsa masa a kullum idan yana karatun saƙon. A hankali ya sake ware sabuwar mai ɗan jan hankali da sanya zuciya nutsuwa.

“Can you feel it? The way i feel it in my heart? ....In every moment we share, my love for you grows deeper. I love you.” Ya buɗe idanunsa da ƙyar da suke lumshe

masa, wani irin abu yake ji na musamman game da takardar, ya ji ina ma zai ga mai wannan rubutun a gabansa, dole taci gidansu ta faɗa masa dalili daya saka a dole take son ya fara ƙaunarta, domin da gaske he love kowacce kalma dake zane a jikin takarda, ya dinga kallon handwritten ɗin, tare da fatan ko zai gane hannun mai rubutawa. But he can't! Ya kasa.

Ya ajjiye ya sake ɗakko wata second paper ɗin yana buɗewa ya ci karo da. “Allah na son ka da Rahama YAA MUHAMMAD, shi ya sa zai jarabce ka da abubuwa masu yawa, kar ka ji babu daɗi ka ɗauka rabauta ce daga Ubangiji ka samu, ka yarda da Allah shi kaɗai ya isar maka, ka yarda babu mai yi kuma sai shi. When you feel bad, don Allah ka ɗauki rubutuna ka karanta, akwai watarana da zan tsaya a gabanka na faɗa maka yadda nake ji a ƙirjina” ya ɗan marairace fuska ya ja numfashi a hankali kuma ya ce "Why not now?" Kamar ya shiga cikin zuciyarta sai ya ga amsar tambayar a ƙasan takardar an rubuta "Ba yanzu ba, kana da abubuwa da yawa da kake buƙatar cimma, mu jira lokaci shine bamu damar kasancewa da juna, bana buƙatar komai sai alƙawari. Ka yi mini wannan alfarmar don Allah Yaa Muhammad" ya dinga kallon rubutun yana jin zufa na tsattsafo masa ta cikin ƙofofin gashin jikinsa, a hankali ya ajjiye paper ɗin ya rufe ido, sai kuma ya sake ɗakko wata paper yaga ɗan short note ne. In a love way.

“I love you more than pizza (and that's saying a lot)!” aka rubuta playful. Haɗe da zanen emoji na zuciya dana kuka.

Tsaki Mutallab ya ja, yana jin duk sanda ya kama mai yi masa irin wannan abubuwan sai sun samu mummunan saɓani. Ya yi shiru, yana ta zaune kamar an cillo Malam haka ya shigo ɗakin Mutallab ya ɗago kansa ya kalli Malam bai ce komai ba. Malam ya dinga kallon ɗakin, ya hangame baki ya ce "Iyee, likafa ta cigaba duka wannan na uban mene ka mayar mini da ɗaki kamar na aljanu? Ubanka ne ya gina mini ɗakin don ubanka?"

"Ubana Malam Abdullahi shi ya gina mana, kuma ko mutuwa ya yi ina da hakƙi akai". Baki buɗe Malam Abdullahi ya ce "Daman mutuwata kake jira kenan?" Mutallab ya girgiza kansa a ƙasa kamar zai yi shiru sai kuma ya ce "Bana fatan ganin mutuwarka Aby, sai kaga na zama abin kwatance in sha Allah. Za ka ɗauki zuri'ar Mutallab" "Kai nan tunaninka zaka zama abin kwatance ne kamar kowanne yara? Ai bana hango maka wata kyakkyawar gobe mai kyau a nan gaba, tantiri yaro mai idanu a tsakiyar ka wulaƙantacce" Mutallab ya miƙe tsaye, sai ya ji dama zai samu damar rungume Aby ya faɗa masa abin da yake damunsa, ya samu dama ko

yaya yane ya zubar da hawaye, ya faɗa masa bai san yadda aka yi Diyna ta rasa ranta ba, ya faɗa masa bashi da hannu wajan mutuwar Jaanah, bai san kuma ya aka yi hakan ya faru ba, ya faɗa masa sabon abubuwan da ƙaddara ta saka ya kutso rayuwarsa. Sai dai bashi da wani damar hakan, bashi da ikon yin hakan, bashi da wata jituwa da mahaifinsa balle ya tsaya ya ji mene yake faruwa da rayuwarsa. Da ƙyar ya ce.

"Idan bakinka ya kama ni Aby shikenan, idan abin da kake fata ya faru shikenan. Duk inda zan je kai zan nuna matsayin wanda ya haife ni, in sha Allah kuma ba zan zama silar mutuwarka ba, sai na sanyaka cikin farinciki, ko lalacewa na yi ina nan tare da kai"

Malam ya ce "Ban haifi wanda zai kashe yaran jama'a ba, ban kuma mai haura katanga ya yi sata ba" kai tsaye Mutallab ya ce "Aby, daka ciyar damu a matsayinka na uba a gare mu da hakƙin hakan yake a kan ka, ta ina zan haura katanga? Daka cinyar damu, da yanzu muna tare da Muneeberh muna rayuwa, daka ciyar damu da yanzu ƙaddara bata cilla ni halin da nake ciki ba, ka taɓa zama ka tambayi dalilin daya saka na haura katangaa? Ka zaunar dani ka ce Mutallab ya aka yi Diyna ta mutu ya aka yi Jaanah bata duniyar a yanzu. Sai dai ka aibata ni, kullum; a koyaushe duk wani responsibilities naka a matsayin uba babu wanda ka ɗauke mini, ai shikenan Aby ya yi kyau hakan ya yi kyau" ya juya zai fice daga cikin ɗakin Malam ya ce"Dawo ka kwashe komai naka, fenti za a yi ciki matar da zan aura ce zata tare a cikin ɗakin" Mutallab ya kalli Aby kallo na anya kai mahaifina ne? Wanne laifi na yi dana cancanci hakan? Ya cije bakinsa a hankali muryar a rauna ce ya ce "Sai na koma ina da kwana kuma?" Kai tsaye Malam ya ce "Sai ka dinga shimfiɗa a saman kai na kana kwana, ko a ruwan cikina"

"Zan kwashe" ya ce kawai yana fita daga cikin gidan bakiɗaya zuciyarsa na rarrabewa da tunanin makomar yau ɗinsa, da abin da gobensa zata haifa zuwa ga jibin da bashi da tabbacin ganinta. What should i do?....

Safiyyerh ji ta yi kamar zuciyarta za ta yi bindiga ta tarwatse a ƙirjinta haka take ji, ba kukan marin take ba, kukan yadda ya hanata magana da Mutallab take yi. Ta durƙusar da kanta tsakanin cinyoyinta ta fara rera wani irin kuka mai sauti tana jin yadda yake sharara gudu a mota amma bata ɗago ba, to ta ɗago ta yi me? Ta kalli yadda yake mayar da ita gida zuciyarta na ƙara raɗaɗi a zuciyarta ta tsinewa Wahee ya yi cikin carbi domin ta san ita ta faɗawa daddy cewa ta fita, sai dai ta yi

mamakin yadda daddy ya gano gidansu Mutallab ɗin kai tsaye har yazo. Mai gadi ne ya buɗe ƙofa da sauri daddy ya shigar da motar tare da yin parking ya fito, daidai nan Uncle Musbah ya fito daga cikin gidan hannunsa riƙe da key ɗin mota yana kallon yadda daddy ya fincikota Safiyyerh yana shirin ɗaga bulala ya zane ta. A hankali ya ce "A'a, kar ka yi haka kar ka fara" ya ce yana zuwa wajan, da gudu Safiyyerh ta yi bayan Uncle Musbah tana shasshеƙar kuka.

Rai ɓace kuma daddy ya ce "Wai ashe gidansu yaron ta bishi? Yanzu har Safiyyerh ta gane bin saurayi gidan iyayensa? You disappointed me Safiyyerh"

"I am sorry... I'm sorry daddy"

"Zan lallasaki ke da sorryn" Ya faɗa yana girgiza kai, yana matuƙar so da ƙaunar yarinyarsa amma tana neman bashi ciwon zuciya akan wani dalili mara tushe. Uncle Musbah ya ce "Yi shiru haka nan daughter mu je ciki ko?" Ya juya cikin gidan daddy ya bi bayansa har zuwa main parlor suka tarar da Ummeyh ita Wahee a zaune. Ummeyh ta ce "Ina ka same ta?" Daddy ya kasa magana can ya nemi waje ya zauna, Uncle Musbah ya ce "Safiyyerh, Wahee go inside kun ji ko? Allah Ya yi muku Albarka" kamar jira Safiyyerh take yi haka ta yi sauri ta hau upstairs ta shige bedroom ɗinta ta rufe tana sake wani sabon kukan domin ita kaɗai ta san mene take ji a zuciyarta. Wahee ma ta shige ciki hannunta riƙe da waya har zata zauna sai ta dawo ɗakin kamar ta manta abu, ta saka wayarta a recoding ta ajjiye ta ɗauki ruwa a deep freezer ta koma saman benen.

Uncle Musbah ya ce "Me yake faruwa ne har haka?"

"Musbah ai ka gani, daga wajan saurayi na ɗakko ta"

"Saurayi? Shi Ɗan'malam ɗin?" Ummeyh ta faɗa tana riƙe haɓa tare da yin salati da sallallami.

"Bafa wani abin mamaki bane kuke ta jimami, ku bar sharrin Adolescencet stage ɗin nan ya fi komai hatsari a rayuwar yara daga mata har maza... Yanzu ba wannan ba meke faruwa briefly?"

Daddy ya gyara zama ya ce "Wani yaro ne nina manta sunansa ba, ɗan iska ne bashi da kunya data ido, babbar damuwa criminal ne yɗan'mata biyu ya kashe sau biyu yana kashe mata biyu" da wani irin shock daya kama Uncle Musbah ya kalli daddy sosai ya ce "Kisa kuma Prof? Ba ka ce age mate bane? A age ɗin nasa zai yi kisan kai har mata anya?" Daddy ya yi murmushi ya ce "Ina da hujja ai, i have a reason.... Many reasons daya saka na ce haka. Frist of all, I don't like him, na ji bana son shi. Ka san halina da bibiyar abu ranar dana fara ganinsa a cikin state cid ne, a rana ta biyu kuma na sake ganinsa, sai na sawa kai ne duk inda yake wannan bashi da wata cikakke tarbiyya, ba shiga na samu wani Dig Johar domin bincike ya shaida mini cewa kawo yaron na farko akan cases ɗin sata ne, kuma an kama shi da wata bindiga wanda jami'an SSS state security service suke nema domin akwai laifin zargi akanta na jami'insu da ya munafurce su bayan ya san sirrin su. Abu na biyu kuma saboda da rashin ji da ɗaukar magana da yake wa iyayensa na sace sacen kayan al'umma da lalata yara, ya saka aka bawa iyayen nasa shawarar su yi masa aure, domin wata fitinar ta raya idan suna yi aka yi musu aure sai kaga an samu albarkar dake cikin auren ta daidaita komai, akai yunƙurin aura masa wata yarinya a ranar da ya je gidansu a ranar ne yarinyar ta mutu, aka sake yunƙurin aura masa wata yarinyar abu kamar gaske a ranar da ubansa ya kai sadakin auren yaron gidansu yarinyar, da daddare yarinyar ta mutu mutane sun tabbatar shine ya babbake ta. Ban san mene ya kawo shi Fgc ba, ashe ɗan ajinsu safiyyerh ne kimiyya ya saka iyayensa suka sa shi, kenan yana da planing na kashe mini yarinya ko? Yana so ya ce Safiyyerh ce gawa ta uku?.... No please impossible"

"..... Mene impossible ɗin? Hana shi auren, ko hana Safiyyerh bibiyar yaron, ko hana Safiyyerh son yaron? Wanne daga ciki Prof?" Cewar Uncle Musbah yana murmushi domin daddy baya fahimtar abi kao tsaye. "Komai ma impossible ne, idan akan maganar Ɗan'malam ɗin can ne, kama ture komai a gefe just keep a joke aside Safiyyerh ba zata taɓa auren ɗan talaka ba, ina da kyakkyawan tanadi a kanta in sha Allah"

"Ok, amma ba zaka hanata haihuwar ɗan talaka ba? Ina nufin baza ka ji komai ba when you saw her with pregnant". Daddy ya ce "Ban gane ba Engineer, wanne irin ciki ana zaune lafiya?" Uncle Musbah ya yi murmushi yana gyara zama ya ce "Da farko a cikinku wane ya nutsu Da sauyin dake tattare Safiyyerh?" Daga daddy har Ummeyh suka yi shiru alamar tunani ya ce "Daga shekaru 15-17 zuwa sama mataki ne da yake da matuƙar hatsarin gaske kafin yaro ya tsallake shi, according to psychologist suka ce a wannan matakin mu lura da yaranmu, kalamansu, furucinsu, ɗabi'arsu, abokansu... Abin da yaro ya fi yi maka magana akai shine abin da yake zuciyarsa, kuma shine abin da yake so. Ko a karatun yaro mu kaga sauyi yana da

kyau mu bibiya a tsanake lamarin yaro baya ɓaci muddin akwai kulawa da saka hannun iyaye a ciki" Ya yi jim sai kuma ya ce "Kune iyayen Safiyyerh, kuma kuke tare da ita, musamman cikin dare za kufi gane komai"

"Ni bana kwana tare da ita, bedroom ɗinta daban ai"

"Da gaske? Really..... Ita ɗaya ke kwana kenan ashe?"

Ta jinjina masa kai alamar eh. Ya ce "Ikon Rabbi, ga wani salo duk wayewa ce haka ta gidan Professor Abdu kenan? Ai duk me za ki yi Dr ko ƙarfe 3 na dare ne yana da kyau ki dawo kusa da yarinyarki ki kwana da ita, wata matsalar ai cikin dare take faruwa tunani kuma ya fi zuwa kan yara a lokacin kwanciya bacci, kin yi kuskure wannan kuma ba wayewa bace ba matar Prof, lack of parent audience kenan"

"Wallahi iskanci ne lamarin Safiyyerh, gudanawa take?"

"A faɗar gudanawa kuke ƙara ɓatar da zuciyoyinku, karka manta makaranta take zuwa, ƙawaye ne da ita, duk ƙanƙantar shekaru karka raina su wajan yaro, wayen su ya fi ƙarfin tunaninsu wallahi. Age is nothing but a number, wayo da ƙawa zuci abine da Ubangiji ke ƙissima bayinsa. A yanzu ba zaku iya tanƙwarata zuciyarta ba, domin ta bushe yau da ace bata kalli cikin idanunka ta faɗa maka cewa aure take so ba, to me sauƙi ne. Amma duk yarinyar data ce aure take so mafi sauƙi ayi mata shi kafin rawar ta sauya salo, shi ita ce tun yana ɗanye ake tanƙwara shi, kuma wallahi yadda yara suke saka lamarin soyayya a zuciya yanzu.... Uhm" Ya miƙe tsaye yana ɗaukan wayarsa ya ce "I will talk to her, kuma Prof ka sauya salo duka ba zai maka ba, domin ita yanzu wannan ba shine gabanta ba, the more kana dukanta the more tana ƙara yin abin da take yi, da zan bada shawara ka yi mata auren, idan kana tsoron talauci ko gudun wahala sai ka bawa yaron jari, gida, da duk abubuwan da suka kamata ai yarka zai aura" ya ce hakan yana nufar upstarts zuwa ɗakin Safiyyerh.

"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un" Ummeyh said loudly.

"Ina tunani za mu bar ƙasar nan, ba zan jira dawowar yaran nan ba" Ummeyh ta yi shiru, ya juya ya kalleta cikin ɗacin rai da ƙonar zuciya ya ce "Ina ce shikenan idan muka bar ƙasar ko? Mene zai faru idan ta dawo new Safiyyerh, muka bar old a Nigeria? We have to leave da zarar na kammala haɗa komai ko zuwa next week ne" tashin hankalin Ummeyh ya ninka na daddy kashi sittin ta ci kuka ta ƙoshi idanunta ya yi jajur tama kasa cewa komai a hankali ta ce "Aliyu ya dawo"

"Yana ina?" Daddy asked.

Ta ce "He lefted already, wai da ƙyar ya samu ya dawo, shima duk ya yi wani iri da shi, na ce ya jira ka da ƙyar yana ficewa daga cikin ya dube ni ya ce... He can't wait any longer, shi wai lokacinsa baya shuɗewa haka kawai"

Daddy ya ce "Ba zai sauya ba, ba ya saka abu a ransa ba na yi na yi ya haƙura yaƙi ai shikenan".

Ummeyh ta miƙe ta ce "Amma zai biya ta wajanta dole na sani, ba zai iya zuwa bai je wajanta ba"

"Dole kam"

Ummeyh ta shige bedroom ɗinta, ta ɗauki waya suka fara chatting da S Bayero akan wasu haɗin kaya da za ta yi mata. Tabbas kayan S Bayero ba kowane zai dace da samun nagartattun irinsu ba, musamman masu fama da matsalar shigar sanyi da yake saka gurajen gaba, har miji ya daina zuwa turaka, masu matsalar bushewae fata musamman a lokacin sanyi, wanda basu da wadataccen mama a ƙirji ki wanda suka kwanta,domin a zamanin nan na yanzu mace ma gyara ya aka cika balle babu, ƙarara za su nuna miki rashin ɗa'a. Masu buƙatar hips ko wanda duk abin da za suci basa ƙiba masu ƙashin wuya, ko gogewar fata tana gyalli da haske sa uwar gida tsaki, duk wani abu na mata ba'a bar S Bayero ba. Product guda take haɗawa na kamfaninta kuma testing and trust ne, da zarar ka siya you most come for more.

Wata gumba ta saka order nata da wata Haɗaɗɗun kayan ƙamshi wanda kai tsaye daddy ya nuna yabawa akan su. Bayan ta gama ta ajjiye wayar ta fara tunanin ina zata saka matsalar Safiyyerh? Ta ina zata fara? Duk inda ta juya ta yi nazari ta kasa hango sauyin da Uncle Musbah yake magana, bata kuma kawo ƙibar da safiyyerh ke yi da kuma matasan ƙirjinta da sukai girma na ban mamaki ta buɗe sosai ba. Ta yi ƙwafa tana jiran Uncle Musbah ya fito ta shiga ta ci ubanta...

Daddy ya tashi ya shige part ɗinsa ya fara tattara muhimman abubuwan domin barin ƙasar gabaɗaya hakan shine mafita. Ganin ba kowa a parlo ya saka Wahee sakkowa ta ɗauki wayarta tare da yin saving recording ɗin.

Safiyyerh, tana shiga ɗakinta ta kulle da key saboda tsoro, a hankali ta sulale ƙasa a jikin ƙofar ta durƙusa wani irin zafi take ji a zuriyarta, ta yi kuka har dana Allah wadai ta fara sauke ajjiyar zuciya, ta lumshe idanunta tana hango fararen idanunsa ta ciki, da yadda kayan jikin nasa sukai masa kyau she love everything about him, she like everything when it comes to him. Ta jima a wajan kafin ta miƙe ta ɗauki wayarta, sai tunanin kiran Aafiyyah ya zo ranta, ƙila ta ji sanyi idan sukai magana da ita sai ma ta bata haƙuri. Number ta kira kamar ba za a ɗauka ba sai kuma aka ɗauka, ta ji mamaki jin ba Aafiyyah ba ce ba.

"Ina yini?"

"Lafiya Safiyyerh, ƙawar taki bata jin daɗi ai muna asibiti"

"Aafiyyah ba lafiya Yaya? Mene ya sameta to?" A hankali ya ce "Lalura ai jikin nata da sauƙi ma"

Ta yi jima sai ta ce "Can i speak to her?" Ta can ɓangaren ya ce

"Anya? Tana bacci ne"

"Ok ka bani address ɗin asibitin, zan faɗawa Ummeyh sai driver ya kawo ni ko? Allah Ya sauwaƙe"

Bayan ta kammala wayar, sai ta fara kiran number Mutallab tama ta ringing bai ɗauka ba ta haƙura sai kawai ta yi masa dm da “I love you bby" ta ajjiye wayar da sauri jin ana knocking. Ta miƙe ta buɗe ganin Uncle Musbah ya saka ta yi ƙasa da kanta, ta gaishe shi ya zauna. A nutse ya ce "Daughter dawo nan kusa dani mana" ta ƙarasa ya sauke numfashi ya ce "Meke faruwa dake?" Ta yi shiru sai da ya zama very friendly to her ta kalle shi ta ce.

"Uncle aure nake so"

"Wa zaki aura?"

"Bestie....." Ta faɗa hawaye na cikowa ta cikin idanunta.

"Waye Bestie kuma?"

"Mutallab.... Shi zan aura"

Uncle Musbah ya dinga kallon Safiyyerh da mamaki ganin how serious she is akan maganar kuma yana hango gagarumar matsala nan kusa. A hankali ya ce "Kina son shi?" Ta yi saurin jinjina kai ya ce "Shi kuma fa?"

"He love me too"

Mutallab na zaune a ƙofar gida har wajan ƙarfe 2 na dare Malam har ya rufe ƙofa, shi ba zai iya shiga cikin almajirai ba ƙila ma akwai masu fitsarin ƙwance. "Mai dawa" aka kira sunansa domin inkiyar da aka fara yi masa kenan. Ya juya a hankali ya kalli TARIQ.

"Mai dawa"

"Tariq" Mutallab ya ce.

"A'a ka ce mini Goje kawai, me kake yi zaune a nan kai ɗaya?" Ya buɗe idanunsa sosai ya kasa magana, ai da kunya ya ce Aby ne ya kore shi daga cikin gidan, ba zai iya tozarta Aby ba balle wasu suga baƙin shi. Da ƙyar kamar mai lissafa kalmomin da zai faɗa ya ce "Shagonka, kai ɗaya ne?" Goje ya ce "Ni ɗaya nake kasa a ciki ya aka yi?" Mutallab ya yi shiru Goje ya fidda ran zai yi magana sai ya ji ya ce "Zanna kwana duk wata na baka kuɗi, haya kenan" Sai Goje ya dinga dariya ya ce "Allah Ya sauwaƙe saboda zaka kwana na karɓi kuɗinka, mu je kawai" ya miƙe a ran muhallin yana mamakin yadda dariya bata bawa wasu wahala. Bacci ya gagare shi duk juyi ɗaya biyu sai Goje ya banka masa tusa ya kasa sukuni.

Washegari a makaranta daga Safiyyerh har Aafiyyah babu wanda ya zo, ga exam na ƙara zuwa domin Monday za'a fara. Bayan an tashe school Kimiyya ya ɗauki Mutallab zuwa wani waje, ya yi ta mamakin ganinsu cikin asibiti bai ce komai ba har suka isa ɗakin da Aafiyyah ke ciki. Kimiyya ne farko Mutallab kuma ya ja ya cake a waje yaƙi shiga ciki. Ya shiga da sallama ya buɗe ido ganin Aafiyyah zaune ta kishingiɗa da jikin gado, ga Safiyyerh zaune a gefen gadon sanye da wata lafiyayar Abaya a jikinta ya ce. "Wonder shall never ends, Safiyyerh you are here"

"Kimiyya" Safiyyerh ta ce.

Shi kuma ya juya ya kalli Aafiyyah da duk ta rame lokaci guda, ta sake haske kyanta ya bayyana a fili kanta ba ɗan kwali sumar ta har baya ya ce "Crush za ki shige lahira babu announcement? At least ki sanar mini yadda zan fara tunanin rayuwa babu ke" da mamaki ta juya ta kalle shi ya kashe mata idanu ya ce "Yes, i am nothing without you, rayuwa zata mini wahala" Ta yi masa shiru, ya ce "Ya jikin crush?" Muryarta can ƙasa ta ce "Jinya nake yi?" Ya ce "A'a, saboda bake ce a gadon asibitin ba, ke da mutuminki muke yana waje yaƙi shigowa ki je ki lallaɓa shi" ya faɗa yana kallon Safiyyerh a hankali ta ce "Waye a wajan?" Domin tunaninta Captain yake nufi ya ce.

"Bestie"

Kamar an tsikare ta haka ta miƙe tsaye, Aafiyyah ta bita da kallo secretly tana lumshe idanunta tare da ɗan ya motsa fuska. Jingine ta ganshi a jikin bango, ya haɗe ƙafa yana kallon wani waje daban idanunta ya sauka a ƙirjinsa, bata ya aka yi ba sai jin saukar hannunta ta yi a tsakiyar sumar ƙirjinsa da babu riga, da sauri Mutallab ya juyo saboda wani irin da ya ji da kuma tsigar jikinsa daya tashi idanunsa ya sauka cikin nata kafin ya yi magana ta marairace fuska cike da shagwaɓa tana ɗan turo bakinta gaba da babbuga ƙafa ta ce "Bestie.... My love" ta ce tana murza hannunta dake tsakiyar ƙirjinsa zuciyar Mutallab ta girgiza, a tsora ce a zuciyarsa ya ce "Shaiɗaniyya.....

😀A cancana Allah Ya kaimu Monday kuma.

Mutallab paid book ne. Pay before you read ₦500

08164069385

Na'ima Sulaiman Sarauta

(Nimcyluv)

[1/7, 9:35 PM] Sis Fauzy: Chapter 32: Nothing will happen.

Kanƙance idanunsa ya yi, kallon da ya yi mata kuma bai saka Safiyyerh dai na abin da take yi ba. Ta rausayar da kanta gefe cike da shagwaɓa ta ce "Ka yi kyau, kuma sai ka tsaya a nan?" Ta zubawa ƙirjin nasa ido, taƙaici ya kama Mutallab ya saka hannunsa yana make nata ciki ciki ya ce "Ashe yar iska ce ke?" Safiyyerh ta ce "Yar iska kuma? Iskanci me na yi?" Kamar zai kuka muryarsa na rawa ya ce "Kirjina fa, ƙirjina kika taɓa ba ki da kunya? What nonsense" Ta tuntsire da dariya tana juya masa idanunta ta ce "Kai kuma ɗan ruwa ne ba ɗan iska ba? Ka yi mini kyau ne" ta faɗa romantically.

"Mu je ciki, Aafiyyah na ciki" ya yi mata shiru, ya juyar da kansa gefe ta sake matsawa ɗaya gefen suka haɗa ido ta ce "To haka ake zuwa dubiya?" Ya juya ido.

"Dubiyar wa?"

"Aafiyyah" Safiyyerh ta nanata masa, duk da ta san ya sani amma ba zata biye masa ba. Ya nutsar da idanunsa ciki ya kame fuska ya fi ƙarfin 30 seconds da ƙyar ya ce "Waye haka kuma?" Ta harare shi ta ce "Aafiyyah ɗin? Ba kyau ka daina irin wannan class mate ɗinka ce, da ana rabawa yan makaranta gadon mutum tsaf zata ci, Aafiyyah zata ci gadon mijina na gobe" Ya ɗaga mata kafaɗa yana tsotse lips ɗinsa na ƙasa ya bubbuɗe idanu ya ce "Sunan bai yi kama dana mutane ba, irin na wani teddy" ya faɗa yana mayar da wayar cikin aljihu.

"Teddy kuma?" Ya jinjina kai, yana sake suɗe lips ɗinsa wanda ya zame masa ɗabi'a. Ta yi jim ta ce "Ka shiga ka yi mata sannu, ta rame sosai" ya sake mata banza, kuma ya kafe ta da idanu, ita ma shi take kallo domin bata yi wa idanunta shamaki da cikin fararen idanunsa. A hankali ta zame nata idanun tana kallon gefe ta yi shiru can kuma ta yi murmushi ta ce "Ni dai kawai na san ni ce ƙaddararka, soyayyarka kuma a zuciyata ita ce tawa ƙaddarar, Ubangiji shi kaɗai ya san ma'anar haɗuwarmu a Fgc, in ma ka so ni ko ka ƙi ni, ni dai na ji zan rayuwa da kai bestie. Safiyyerh zata rayuwa da kai, kuma na ji a jikina soona or later zan amsa sunan matar Mutallab" ta yi shiru, sai kuma hawaye ya cika idanunta sosai a hankali ta ce "My parents doesn't understand me, Aafiyyah doesn't understand, and you.....," ta yi shiru.

"You never understand ma" ta sake yin dariya tana rufe idanunta, ya bi fafaren haƙoranta da kallo tana da dariya yanayinta ya nuna farinciki sosai ta kuma kasa magana ya ga ji da dariyar domin gundirarsa take yi, ya ɗan kame fuska daman kamar ya ce ya shiga uku a daƙile ya ce.

"Kee"

"Kai..."

Ta ce tana yi masa fari da jiƙaƙƙun idanunta, ta sake murmushi ta ce "Wallahi ina jin farincikin sosai mara iyaka when i am with you, bestie ba zaka gane ba, amma watarana za ka ce na faɗa maka, akwai wata manufa da Ubangiji ya ɓoye na dalilin haɗuwarmu, da kuma dalilin da yasa na ji ina son ka. Dole zama ka tuna one day, ko Safiyyerh bata raye" Ta matsa kusa da shi ta ce "Za ka dafe zuciyarka ka ce why Safiyyerh? You never tell me.....," sai kuma ta yi shiru ganin yana ƙoƙarin barin wajan ta yi saurin riƙo hannunsa tana buga ƙafa ta ce.

"I am sorry, ban san ina da yawan magana ba sai ina tare da kai"

Ya kalle ta, ya kalli hannun ya ce "Kina son taɓa jikina Fiyya"

"Fiyya!" Safiyyerh ta maimaita sunan ta ce "Fiyya, i like it "

"What?"

"The name you gave me now, Fiyya" ya girgiza kai kawai a hankali ya ce "You are impossible Safiyyerh Abdu Professor"

"I love you!" Ta faɗa soundly.

Ya dube ta sai ya kame fuska, domin shi tausayi al'amarinta suke bashi, da yana da iko daya bada shawarar ubanta Professor Abdu ya ɗauki ɗiyarsa zuwa asibiti a duba lafiyarta. Ta jinjina kai while smiling ta ce "I got you dear, ka ce i love you too". Taɓara ta dinga masa shi dai bai tanka ba, ya dinga kallon ta yana jan halaula a zuciyarsa, da ƙyar ta sakko da shi ƙasa akan ya shiga ya duba Aafiyyah da jiki, yaƙi ce mata komai sai ƙanƙantar da idanunsa daya ke yi a kanta. Ita ta fara yin gaba ya bita a baya yana tafiya majestically hannunsa a aljihu.

Kimiyya ne ya dinga bin Aafiyyah da kallo musamman sumar kanta, tun bayan fitar Safiyyerh ko ɗaga kai bata sake yi ba, balle ta tanka Kimiyya yana ta bata tabbacin nothing will happen to her, kuma ta dage da addu'a ga kuma exam. Da sauri yaga ta ɗauki mayafin dake kusa da ita ta yafa saman kanta ta kuma tattare sumar data sauka a bayanta ta tura cikin mayafin ta ja duvet ta rufe jikinta har ƙirji. Safiyyerh ce ta fara shigowa har lokacin tana dariya da faɗin "Ai bai wani dake ni ba, faɗa ya dinga yi wai ka yi mini asiri, na san kuma ba wani asiri idan ma akwai i appreciate it, domin ka taimaka mini sosai" ta faɗa tana shigowa ciki, kimiyya ya ce "Safiyyerh kamar an aiki bawa garinsu? Daga ki shigo da shi"

"Uhm, shi ai sarki ne sai da biyayya da lallashi baya tanƙwaruwa ta sauƙi" ta faɗa tana kallon Aafiyyah ta ce.

"Bacci ta yi ne?"

"Maybe, baccin ne ma" Kimiyya ya bata amsa. Ta ɗan matsa gefe ta ce "Bestie ka yi mata sannu" shiru ta ji ta juya taga waya yake dannawa ta marairace fuska ta ce "Ina magana fa" gently ya ɗago kansa suka haɗa ido, hankalin kimiyya yana ga Aafiyyah da take danna tata wayar a nutse alamar kamar game take yi. "Tunda ya zo har asibiti ai ya wadatar kika sani ko azumin magana ya fara yi?" Ya girgiza kai ta ce "Naaaa, Aafiyyah is my best friend, childhood friend" ta ce tana zama.

"Waye ba lafiya?"

Daga Safiyyerh har kimiyya suka kalli Mutallab jin wata tambayar rainin wayo da ya yi. "Aafiyyah Abdu, ƙawar Safiyyerh Abdu ita ce babu lafiya tun ranar birthday party ɗin Safiyyerh, aka kwantar da ita a gadon asibiti ta yi kwanaki, shi ne daga makaranta na ɗakko muka taho dubata ba tare daka sani ba, mistakenly kuma ashe budurwarka yɗar anacenka ta zo itama, na shigo kai kuma kaƙi shigowa, shine na ce ta fita ta kira ka, gashi kuma ka zo ɗin, shine yanzu take faɗa maka ka cewa Aafiyyah sannu da jiki" Kimiyya ya faɗa yana sake cewa "Na sake maimaitawa ko hakan ya wadatar da kai?" Mutallab ya yi shiru, hakan ya saka sukai masa banza suka cigaba da magana da Safiyyerh. Aafiyyah na jin komai ko motsin kirki ba ta yi ta haɗe fuska tamau.

"Zan tafi" cewar Mutallab, ya furta a hankali can ƙasan zuciyarsa

"Wani ya riƙe maka ƙafafuwa? Ba komai rayuwa ce, crush ɗina ka ƙiwa sannu jeka to ba yanzu zan tafi ba, sai na ƙara ganin jikin nata" Kamar jira yake yi ya ɗaga kafaɗa tare da ficewa daga cikin ɗakin, da sauri Safiyyerh ta biyo bayansa tana kiransa. "Middle class" Aafiyyah ta ce a hankali, kimiyya ya kalleta ganin ta kwanta a hankali ta juya baya. Ya miƙe ya ce "My crush, Ubangiji ya ƙara sauƙi da afuwa zan tafi babu wanda ya zo daga can gidan naku, fatan ba za ki kaɗaita da shirun ba?" Ta janye mayafin kanta kaɗan ya ce "Ba dai ciwon kan bane na ga idanunki ya yi jajur?"

"See you, i am fine"

"Glad to hear this, Rabbi ya ƙara sauƙi my crush"

"Amin dear. Ka turan timetable na exam ok?" Ya ce "Za ki iya karatun jarrabawar ne ko na yo mana?"

"Kamarya?" Ta tambaya tana tsattsare shi da shanyayyun idanunta, very sexy eyes. Ya yi mata murmushi ya ce "Shikenan Allah Ya kaimu Monday, wish you a very quick recovery, don ina jin sai na je na yi Jeddah shagwaɓa" ita dai bata kula shi ba har ya gaji ya fita, ya tarar Wizzy driver tuni ya ɗauki Safiyyerh sun tafi, sai ya ɗauka tare suka tafi da Mutallab.

***Eng Ali wali zaune akan kujera ta alfarma jikinsa sanye da wata jallabiya mai taushi da tsadar gaske, ya ɗan kishingiɗa yana sauraran abin da matarsa take cewa, ya dube ta kaɗan ya ce "Madam kenan, siyasar don suwa nake yinta? Saboda kune, domin ke matata da ƴaƴana, sai kuma yan'uwana" Ta haɗe fuska ta ce "Wanne yan'uwa kuma? Ni kake kalla kake cewa domin ƴan'uwaka? Duk faɗi tashin da na yi wacce gwagwarmaya ce ban yi ba akan harkar kamfel?" Eng Ali wali ya ɗan shafa kan shi ya ce "You are right, kawai dai suma yana da kyau na taimaka musu" ta saks haɗe fuska sosai ta ce "Sai ka yi na gani, ina faɗa kana faɗa" ya sake yin murmushi ya ce "Yadda kika ce haka za a yi Madam" Ta taɓa fuska ta ce "Ko wani abu za ka yi wa yan'uwan naka, ka tabbata ka fara sanar mini" ya buɗe ido yana faɗin"Kin tuna mini, akwai wani Uncle nawa da ya nemi alfarmar kuɗi za a yi wa ƴarsa aikin ƙoda, shaf na manta bari na saka p.a ya tura masa"

"Har nawa ya nema?"

Eng Ali wali ya ce "500k ne babu yawa ai, sai na shi 1m"

"Ya yi yawa, tura masa dubu ashirin kace harkar kamfel ta cinye maka kuɗaɗe kuma yanzu daka samu kujerar kana biyan mutane bashin daka ranta musamman banki. Amma miliyan ɗaya ta yi yawa Hon, zuwa gobe wani ma zuwa zai yi da tasa buƙatar kaga ka bashi 20k" ya yi ɗan jim ya ce "Kina ganin dubu ashirin ya isa?" Ta ce "Ko bai isa ba sai su nema wani wajan, ciwo ai ba kai ka ɗora mata ba" Sai ya yi murmushi ya ce "Yadda kika ce haka za a yi Madam"

"Hon" ta kira sunansa.

"Ya aka yi kuma? Babu dai wata matsala na sani " ta jinjina masa kai ta ce "Batun ƙanina, brother na yana son tafiya karatu ƙasar waje, ni kuma bana son sabgar scholarship ɗin nan, naga kuma Allah ya hure maka shine nake so ka ɗauki nauyinsa zuwa ƙasar da yake buƙatar yin karatun a can" yana kallon ta ya ce "Ba case, ku yi magana da shi za'a nema masa ko wacce ƙasar yake son zuwa"

"Na gode, idan ka tashi raba kujerar umara ina buƙatar guda biyar zan bawa sauran familyna da basu je ba" Nan ma ya ce an gama ya nisa ya ce "Ina Noor ne? Yana da kyau itama a fara shirin tafiyarta karatun nan, ni makarantu ƙasar nan namu sam ba su yi mini ba Wallahi, kira mini ita mu ji nata ra'ayin" ta ce "bacci take yi yanzu sai ta tashi, zata same ka yaushe zamu tafi Abuja ɗin?" Yana danna kiran P.a ɗinsa ya ce "Satin gaba, yanzu akwai wani kuɗin kasafi da ake bawa kowanne ɗan majalisa, ya siyi kayan sawa sabbi, da mota da sauran su kimanin wajan miliyan 40. Suna nan an bani, muna jiran a fara kasafin wannan shekarar naga ta wanne sashe ya kamata na sha kwana, amma dole kwangilar gyaran titi, da asibitoci zuwa makarantu ta zo wajena, ina fanshe duka wahalar da na yi. Kafin nan a ƴan'uwana su waye masu ilimi haka da wayo"

"Tajuddeen ne"

"Good, zan tura wasu miliyoyin kuɗi zuwa account ɗinki da kika buɗe da wannan Bnv ɗin, idan na tura miki kuɗin sai ki fara transfer ɗin su zuwa account ɗin driven gidan nan, shi kuma ki bashi account number Tajuddeen ya tura masa, kinga kuɗi ne gama shawagi babu wanda zai yi tunanin daga wajena ya fito, akwai kamfanin da nake so a buɗe, sai a buɗe da sunan Tajuddeen ɗin". Hakan ya yi wa matar Eng Ali wali daɗi. Kana ta fara nuna masa wasu experience kaya ta ce "Ina buƙatar wannan atamfofin da laces ɗin Distinguish" ya dinga kallon kayan kafin ya nisa ya ce "Wannan kayan Arɗo groups ne,sune na biyu a duniya fa, mai kamfanin ya ji arziƙi sosai, kuma sunan kawai aka sani har yanzu ba'a taɓa ganin Arɗon ba, tun daga kan Manager, accounter, sectary da komai ma'aikatan a cikin Arɗo's family suke, major holders sune the Arɗo's family hatta founder" ta jinjina kai ta ce "Ikon Allah, lallai ahhalin kuɗi ne" yana Miƙewa tsaye ya ce "Ardo groups ai yana daga cikin manyan Companies a ƙasar nan, domin gab yake da shige Fs world investment company".

Eng Ali wali ya dinga duban P.a kafin ya ce "Sau nawa zan ce maka karka sake kirana akan batun wasu ƴan daba? Aikin su ya ƙare ai sai zuwa nan gaba, ma'ana

nan da shekara huɗu ko". P.a ya ce "Amma saboda nasarar zaɓenka suka je filin zaɓe suka ta yar da hatsaniya, sun sace ƙuri'un abokan hamayya, sun fasa akwati al'amarin da ya nemi sawa a yi inconclusive kenan, saboda har an ɗauki niyyar sauya zaɓen wasi local government guda biyu. Yaran sun shiga tsari wasu na hannun hukuma wasu sun ji rauni kasan mun raba musu kayan da aka kawo na caji a lokacin"

"P.a"

"Ranka ya daɗe Distinguish"

"Leave, ka fita kafin ka ɓata mini rai, daman can yʻan iskan gari ne kuma yʻan daba basu da wani amfani a cikin al'umma. Wanda hukuma ta kama baza su taɓa taɗin sunana ba, ka bar su a hannunsu akwai sanda zan saka a fito da su. Na asibiti kuma zan ɗan iya yin wani abu, amma kar ka kuskura su san asalin sunana ka ji ko? Ai iyaye su ne suka bar su shigowar bangar siyasar bani ba" P.a ya ce "Na gama hon, ka yi ka kuma idan ka gaji ka karya kujerar dambu mai hawa uku" Eng Ali wali ya geɓare baki yana murmushi. Bayan fitar P.a Eng Ali wali ya juya ya fuskanci Boɗejo suka fara magana hankali kwance.

Gabaɗaya ya manta da batun wata amaryar Aby, ya shiga gidan kai tsaye kuma ya nufi cikin ɗakin domin ya yi mantuwar abu mai muhimmanci, saka ƙafar da zai yi a ɗakin ya ji an fasa ihu ana faɗin "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, jama'a ya leƙo ni kwarto ne" cak ya tsaya yana mai da ƙafarsa waje, bata fasa ihun da take ba Malam ya shigo daga waje da sauri yana faɗin "Yaa ya na ce ya ya? Mene Binta?" Ta nuna masa Mutallab ta ce "Ina shirin saka riga a jikina sai kawai ya bankaɗo labule babu ko sallama, da na yi masa magana ya ce ya shigo ɗin ai jikina ya shigo gani, da ƙyar na ƙwaci kai na" ta faɗa tana kuka sosai, Malam ya juya ya kalli Mutallab ya ce "Bayan kashe yara leƙe ka fara da neman mata? Anya ba ka yi asara a rayuwarka ba kowa Muɗallabi? Matata ta sunna kake leƙawa?" Ammo ta ƙarasu wajan ita da Sa'adah, Mama Zaituna na tsaye a hankali ta ce "Muhammad ka leƙa ta da gaske?" Tambayar ta basa mamaki ya kalli Ammo ya juya ya kalli Inna Binta yana ƙanƙance idanunsa da ƙyar ya ce "E, na leƙa" ya ce kai tsaye.

"....Ka leƙa fa ka ce? Ka kalli tsaraicin matar ubanka Mutallab?" Ya sake jinjina kai ya ce "E, amma banga tsaraicin da kyau ba maybe ko ta sake buɗewa na gani na haddace" Ammo ta ɗauke fuskar Mutallab da mari ta kasa cewa komai, Malam ya ce "To Allah Ya isa ka kalla, tsinannen yaro na kusa haramta maka shigowa gidan nan gabaɗaya"

"Amma ina da gadonka "

"Kashe ni ka ɗakka, anya ba gidan kangararru zan kai ba?"

"Kai ni mana, duk inda na je zan amsa sunan Muhammad Mutallab Abdullahi Ɗan'malam, ɗan ka"

"Ammo kin cuce ni, ba zan yafe miki ba kin cutar da zuciyata" cewar Aby, Mutallab ya ɗaga shoulders ya yi waje ransa a cunkushe saboda ɓacin rai. Yana fita kuma ya shige shagon Tariq, ya yi shiru yana tunani can kuma ya miƙe zaune ya ɗauki ƙwayar daya fara yin rubutu a cikinta da wadata, ya ƙarasa rubuta ayar da yake so, ya ajjiye ƙwayar ya kunna kyandir ya tsaka a tsakiya a hankali kyandir ɗin ya dinga ci yana cilla wasu layoyi a ciki har ya kammala, ya ɗauraye rubutun cikin ƙwayar ya ɗaure a leda. Wayarsa ta fara ringing ya juya yaga Safiyyerh ce, bai yi saving number ba amma ya haddace yaƙi dauƙan kiran daga ƙarshe ya kashe wayar gabaɗaya.

Washegari Monday suka fara exam, safiyyerh ta zo haka Aafiyyah kuma aka rarraba wajan zama cikin sa'a number exam ɗin Aafiyyah data Mutallab ya yi ɗaya. Ba wanda ya kula kowa a cikinsu har suka kammala paper ɗin, a ɓangaren Safiyyerh ta amsa ne kawai amma even questions ɗin bata fama fahimtarsu ba, balle kuma amsar da zata bayar. Aafiyyah na zaune tana danna waya idanunta sanye cikin shade glasses fuskarta ba yabo ba fallasa. Mutallab na zaune shima yana danna waya zumbur kuma ya juya saboda wani abu ɗaya faɗo masa, daman ya zo da shirin duba handwriting ɗin matan ajin yaga wacce ke yi masa haka. Da sauri ya ja littafin gaban Aafiyyah, gently ta ɗago kai ta kalle shi ganin yadda yake ta duba ruhutunta, a hankali ya ja numfashi ya sauke ganin kwata-kwata rubutun wasiƙar bai yi iri ɗaya dana Aafiyyah ba. Ya miƙe ya fara dubawa matan ajin suna ta kallonsa. Kinal ta ce "Yau kuma mai muka yi wa Moh, ake bincikar mana littatafai" ya gama duba nata bai kulata ba. Har ya zo kan Safiyyerh tana tsaye ita da Captain daya tsare ta da surutu ya ƙarasa ya ce.

"Ina littafinki"

Safiyyerh ta ce "Me za ka yi da littafi kuma? Ba dai karatu ba?" Ya tsare ta da idanu ta ɗakko ta basa, da wani irin sauri ya ɗago kansa yana jan numfashi a wahale ganin exactly handwriting ɗin Safiyyerh iri guda ne da wanda ake tura masa, kenan ita ke yi masa wasa da zuciya? Idan yana son ruhutunta to tabbas yana son Safiyyerh. Ta yi masa murmushi ta ce "Waya taɓa mini Mai dawa?" Yaƙi magana ya dinga kallonta sai ya ji a karo na farko ya nutsu da ita ya lura da ramewar da ta yi sosai ta sauya kamar ba ita ba. Captain ya ce "Kai wai yane ka zo ka tsayawa mutane a gaba? Kana sa wani business damu ne?"

"Bestie...." Mutallab ya ce a hankali yana cure girarsa waje guda tare da nuna Safiyyerh da tsaya.

"Wannan ai ba kayan talaka bace, ko a duniya Ubangiji ya ware matayen talakawa ka ji ko? Wannan tawa ce ni ɗaya"

"Ni kuma kaga bana son ka captain, Bestie nake so".

"Safiyyerh ni kike faɗawa haka?"

Ta share shi ta yi waje abin ta. Suna zaune a harabar makarantar ranar da suka kammala exam ta ƙarshe, kimiyya ya ƙarasu wajan Aafiyyah shi da Mutallab ya ce "My crush, ya exam?" Ta jinjina masa kai ya ce "Wai daman kin sauya club ne? Ba'a English club kike ba? Naga sunanki ya fito a Hausa drama kuma za ki yi playing role na budurwa" ta ɗaga idanunta ta kalli Kimiyya sai ta ce "Maybe na sauya, akwai matsala ne?" Ya girgiza kai ya ce "Kawai na ji inama nine saurayin da za a haɗaki da shi" ta juya idanunta ta ce "Ko?" Ya ce "Serious, ai ke ba zaki gane ba shi yasa"

".... kamarya?"

"Kamarya yadda kika ji Aafiyyah".

Idanunta ya kalla muryarsa a hankali ya ce "There's something about you that make me feel like you actually use magic about me, many things I do because you, many things I don't even know or remembered when I started doing them. The love I have for you is so real baby. Yet, ban san me ya sa zuciyata take yawan bijiromin da kokwanton yiwuwar samunki a rayuwata ba. I love you Safiyyerh"

“I love you Safiyyerh, or Aafiyyah" Kimiyya ya ce muryarsa na rawa saboda kwarjinin da idanunta suka yi masa, ta ɗago kai sosai suka haɗa idanu da Mutallab ta haɗe fuska shi kuma ko a jikinsa, shi tunanin yake ko tana da matsalar ido ne? Da sun haɗa ido take yin ƙasa da kai ko duk tsanar ce? Aafiyyah ta ce "Kimiyya kenan, a yanzu ai kaga makaranta nake yi, idan ka so ni babu laifi amma ka yi mini uzurin karatu ka ji ko?" Ya jinjina mata kai ya kasa magana kuma. Ta miƙe ta bar wajan domin gobe ne Friday za a yi ball kamar yadda aka sawa da clun competition.

***Safiyyerh na zaune a parlo ta kalli Ummeyh dake cewa "Kaya suna da kyau sosai, na ji daɗin su Allah dai ya biya ki S Bayero tamu ta mutunci" magana sukai sosai duk Safiyyerh na ji amma ta yi shiru ta rungume filo a ƙirjinta sosai tana jin wani iri a cikin zuciyarta a hankali kuma take tuna tambayar da Uncle Musbah ya yi mata cewa "Daughter kin fara al'ada ne?" Ta kalle shi ta ce "Uncle mene al'ada?" Sai ya yi mata shiru ya ce "Shikenan Daughter idan na dawo zan yi miki bayani kin ji ko?" Ta jinjina masa kai, ya miƙe ya nufi ƙofa har zai fita Safiyyerh ta ce.

"Uncle za a yi mini auren?"

Uncle Musbah ya dube ta, tsoro labarin yarinyar ke bashi shekarunta 15 a duniya ko al'ada bata fara ba ita ke maganar aure? Ya nisa ya ce "Safiyyerh karatun fa?" Ta girgiza kai ta ce "Uncle bana son makarantar bana gane karatun zuwa kawai nake yi, idan na rufe idanuna Mutallab nake gani a cikinsu Uncle, idan na rungume filo sai na ji kamar Mutallab na rungume, bana iya bacci Uncle ina son Mutallab sosai ka tausaya mini, daddy da Ummeyh sun kasa fahimtar aure nake so zuciyata kamar za ta yi bindiga haka nake ji"

"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, wanne irin matakin balaga ne ya zowa Safiyyerh a haka? Ya aka yi ta fahimci feelings na ɗa namiji?" Da ƙyar ya shanye mamakinsa ya ce "Safiyyerh kina da sauran lokaci fa, ke yarinya ce har yanzu"

"A'a Uncle, yaro ai shine wanda bashi da nono a ƙirji, ka dubi Ummeyh ka gani ai ta girma nima ina da irin abin ta"

"Safiyyerh!!!!" Ummeyh ta kira ta s lokacin cikin tsawa, da sauri kuma Uncle Musbah ya fice daga cikin bedroom ɗin zuwa downstairs. Yana fita Ummeyh ta zari wayar caza ta dinga tsulawa Safiyyerh, tana ihu da komai ta yi mata lalas kana ta fice daga cikin ɗakin. Jan numfashi Safiyyerh ta fara a hankali, duk wani numfashi da yake fita daga ƙirjinta da soyayyar Mutallab yake fita, ta dinga kuka tana jin duniyar ta yi mata zafi, ta rasa yadda za ta yi gashi an hanata fita ko'ina tana jin idan ba haɗa idanu da Mutallab ba zuriyarta za ta iya yin bindiga, ta manta cewa soyayya ta ɓangarori biyu ce. A wannan ranar ta saci jiki zuwa wajan Mutallab ta bisa har gidansu inda ta tura yaro ta ce wai bestie ya zo, aka sake dawo da yaron ta sake mayar da shi ta ce wai in ji Safiyyerh matar Mutallab bestie.

Ajjiyar zuciya ta sauke, domin principal ne ya kira daddy, principal na makarantarsu Fgc tsoro ya cika mata zuciya, sai kuma ta dinga addu'ar Allah ya kawo sanadin da za a cire ta daga makarantar gabaɗaya. Ta miƙe ta nufi bedroom wayarta ɗauka ta kira Aafiyyah ta ce "Dear kina lafiya? Ya gajiyar exam kuma?"

"....Good, Safiyyerh, how can i help you?" Safiyyerh ta ce "Aafiyyah mene al'ada? Na taɓa jin sunan a Islamiyya amma malamin ya ce karatunmu bai kawo nan ba tukunna" Aafiyyah ta yi shiru, Safiyyerh ta ce "Kin yi shiru?"

"I don't know ne, Safiyyerh"

"Kai Aafiyyah ke ana raba ki da sanin abubuwa ne? Kawai ba za ki faɗa bane shine". Aafiyyah ta ce "Bar shi a haka ba zan faɗa ba" tana cewa haka ta kashe kiran.

Safiyyerh ta kasa jurewa sai ta kunna data cikin sa'a aka nuna mata Mutallab a online. Bata taɓa sanin cewa yana yin WhatsApp ba, ba lallai ta sani ba domin yau kimiyya ya buɗe masa, aka tura saka shi a group na Hausa drama, aka tura musu script ɗin da su hau a goben. Shi dai kawai bin komai da idanu ya ke yi.

"Hy chocolaty"

Ta tura masa, taga alamar ya buɗe ya gani amma bai kulata ba. Ta sake tura masa "Hy love..... Hy my man.... Hy sweetheart" sunayen da Ummeyh ke kiran Daddy dasu.

Typing ta ga ya fara sai kuma ya daina sai ta tura masa emojin 😭 sai taga ya cigaba da typing.

"Kee" ya tura mata

Ita ma ta ce "Kai...."

"Zo nan"

"Zo nan" ta ce itama.

"Kamo ta nan"

"Kamo shi nan"

"Uhm'uhm" ta ce ganin ya yi mata shiru ya ƙi kulata ta sake tura masa "Uhm'uhm"

"Uhm'uhm, nima" ya ce.

Safiyyerh ta dinga dariya, ta lura gabaɗaya bai iya hirar bane sai ta kira shi vedio call ya katse.

"Bestie can i ask you?" Ya buɗe ya duba ya share ta ce "Mene al'ada"

"Wacce daga ciki, ta Hausawa ko ta mata?" Ya tura mata. Sai ta ce "Mata, Uncle ya tambayan wai ko na fara al'ada ne?"

"To kin fara?"

"Ai ban san mene ba"

Ya tura mata emojin na dariya ya ce "So fiyya still yarinya ce"

"Yarinya ita ce wacce bata da nono ai, kuma ni ina da shi"

Ya tura mata "Uhmmm"

"Zaka gani?"

"What?"

Kafin ta faɗa masa koma mene ya yi saurin cewa "Al'ada jini ne da mata suke yi duk wata, idan mace ta fara hakan yana nuna ta isa ɗaukan ciki, go and read ƙawa'idi ko fighu. Bye"

"To yaushe zan fara? Za ka iya mini ciki kenan?"

Mutallab

Paid book

#500

0116886423 Na'ima Sulaiman S. Shaidar biya 08164069385

[1/7, 9:35 PM] Sis Fauzy: Chapter 33: Love is flying

"To yaushe zan fara? Za ka iya mini ciki kenan?" Mutallab ya zubawa saƙon na Safiyyerh idanu, a hankali ya ji zuciyarsa ta buɗe, wani abu ya bi fatar jikinsa yarr, abubuwan da yake ji kuma is very different da abin da yake, Ji idan yana karanta wasiƙun nan, idan yana karantawa ya kan ji he can give his whole life, just to be with person me tura masa wasiƙun nan, ko waye, ko waye, he feels better da nutsuwa idan yana karantawa. Saɓanin wannan maganganu na Safiyyerh da suka saka masa wani tunani na daban, wanda yake shirin neman sashe na musamman cikin ƙwaƙwalwarsa ya zauna, sai ya ji sanyi na neman kama shi haka kasai ba don yana jin zazzaɓi, ya fara tunanin sanda ya ji Ammo na cewa "Hameeda wani cikin kika samu?" Ya buɗe ido, ba dai irin wannan cikin Safiyyerh ke nufi ba. A hankali ya ce "You are impossible Safiyyerh" bai sake buɗe saƙonta ba, ya lura da emojin da take tura masa na kuɗi, da kuma na zuciya a rabe.

Hankalinsa ya mayar zuwa ga cikin group wanda suke tattauna yadda Hausa drama ɗin sai kasance, ya kura malamin ne yake bayani da kansa, shi dai bai ce komai ba, lura da wani username da ake typing da shi na S.Abdu. a hankali ta fice daga group ɗin, sai a lokacin ya lura da maganar Kimiyya data Nahyan, sai kuma main group na makarantar Fgc da aka yi adding nasa, immediately ya yi exit daga cikin main group ɗin sai kuma ya kashe datar ya fara duba karatunsa don shi ne a gabansa, kiran Safiyyerh bai ƙaƙƙauta a wayarsa ba, har sai da ya kashe wayar bakiɗaya.

Mutallab ya yi tsaye a tsakar gidansu jin yadda Inna Binta ke cewa "Ke har kin isa ki hanani yin abin da na ga dama? Ina cewa kwana ne kuma girki nane ko? To wallahi dole ki jira na ba ki iya tuwon da na yi niyyar bayarwa" caraf Mama Zaituna ta ce "Saboda kin samu yau an yi cefane har kike da bakin magana ko? To a yi dai mu gani idan tusa zata hura wuta, idan yau kin samu na dare bari muga wayewar garin gobe juma'a ko?" Inna Binta ta yi shewa da ta fi tana buga cinya ta ce "ahhhayee cas, ai daman albarkacin kaza ƙadangaren ke shan ruwa, kinga ko babu komai kin ci albarkacin Binta, kuma ba zan taɓa zaman yunwa a gidan nan ba" Mama Zaituna ma ta yi nata shewar tana buɗe hannu ta ce "Ai bari kiji na faɗa miki, ko yanzu Giwa ta faɗi, tafi ƙarfin Allah wadai, kuma ban miki kama da bora ba, ba boranci nake a gidan nan baƙi wannan uwar matan ba" ta yi maganar tana nuna Ammo da hankalinta ke kan manjan da take aunawa, duk abin da suke tana jinsu bata kula su ba.

Inna Binta ta ce "Ke da kika sani, tuwo ne dai kwasa uku zai kai ɗakina saboda tsaro"

"Ai kowa ba ki isa ba, sai dai a yi a sarar tuwon duk mu rasa"

Inna Binta ta juya mazaunai ta ce "Allah ko? Shege ka fasa" ta ce tana kwasa tuwon a ƙatuwar ruba ta ƙiba ta saka murfi ta rufe. Mama Zaituna ta ce "Ki daina wani juyi kina taƙamar jina da ƙiba, muma duk da ita muka zo wannan gidan, wannan tuwon ɗuwawun da kike taƙama da su in dai a cikin gidan nan ne sai sun dawo silifas, zaman ci da kai da wahala kike taƙamar kin aure mana miji". "To ko duka na za ki yi ne ban sani ba? Na ce ko za ki dake ni na matso?"

"Allah Ya rufa mini asiri haɗa ƙirji da kishiya, bai san da uwar da kike taƙama ba ki ci kan ki".

Janye idanunsa Mutallab ya yi daga kallon su, ya nufi ɗakin Ammo yana ɗaga labule, Sa'adah ya gani zaune tana yanka alawar madara gwanin sha'awa, ya ƙarasa shiga ciki ya yi tsaye akan Sa'adah can ya nemi waje ya zauna kusa da ita, ya dinga kallon alawar madarar a hankali kuma ya saka yatsu biyu ya ɗauki guda ɗaya ya cilla a baki, ya yi saurin runtse idanunsa saboda wani zaƙi daya ratsa kunnensa can ya buɗe ido jin Sa'adah ta ce. "Ta hamsin ka shafa Tayo, hamsin zaka bani" bai kulata ba ya ƙara ɗaukan guda biyu ya tura a bakinsa, ta ɗago kai ta ce "Tayo, kasan neman kuɗi da wahala kuwa? Kasan nawa ne gwangwanin madara yanzu?"

"Tsaya wai jarin zaka rusa mini ne?" Ta faɗa ganin ya sake biyu ya tura a bakinsa hankali kwance. Baya ya yi a hankali yana jingina ya harɗe ƙafafuwansa ya zubawa waje guda idanu. A hankali kuma bayan shafe mintina ya ce "Yaya" ta kalle shi ta ce "Autan Ammo ya aka yi ne?" Ya ja numfashi ya ce "Yaya me ya sa ni kaɗai ne namiji ne? Ina yan'uwan Ammo?"

"Suna gidan ubanka, na ce suna gidan ubanka" ta faɗa tana ƙarasa shigowa cikin ɗakin, idanun Ammo ya yi jajur ta ce "Mutallab, duk sanda na kuma jin ka yi tambaya makamancin haka wallahi idan ranka ya yi duhu sai ya ɓaci. Da kake tambayar me ya sa kai kaɗai ne namiji daman Ubangiji idan ya tashi yin halitta a ciki yana yin shawara da mai ɗauke da cikin? Ko butukcewa Ubangiji za ka yi da ka zo a namijin? Muhammad na daɗe ina taraka, yanzu kamar kai ka yi wayon da zaka riƙe waya? Kasan yadda ake bada labarin waya na lalata mutane? Ka ɗauki wasu halayya ka azawa kan ka babu gaira babu dalili? Idan ka sake na kuma ganin waya a hannunka sai ranka ya yi mummunan ɓaci, sakarai kawai" kan shi a ƙasa, jiyiyon

kansa na sarawa har tsakiyar kan shi yake jin faɗan Ammo, he miss it, tabbas wannan abun ya yi missing tare da kewa a rayuwa, faɗan uwa mahaifiya, sai dai ta yi masa faɗan a lokacin da bashi da iko da kansa a can baya kafin yau ya kamata a yi masa faɗan. Ya na ji ta gama ta sake fita, ko motsi bai yi ba. Sa'adah za ta yi magana sai ta fasa wayarta ce ta fara ringing ta yi saurin ɗauka ta ce "Assalamu Alaika Habibi" shiru ta yi sai kuma ta kashe wayar, a hankali ta fara hawaye tana kuka sosai, ta dinga kuka idan ta ji alamun Ammo zata shigo sai ta yi saurin goge hawayenta. Siririn tsaki ya ja, yana miƙewa tsaye kamar zai fita sai kuma ya saka ƙafa ya yi ball da wani kwano ya ƙara saka ƙafa ya daki ƙofar ɗakin idanunsa na fitowa waje ya ce "Wai mene Yaya"

Ya ce a firgice.

"Wai ya ce ya fasa auren nan nawa" ta faɗa tana sake wani kukan, sai ya zama kamar shi ne babba ya dinga kallon ta. A daƙile ya ce "Shi wa?"

"Saurayina, wanda zan aura"

Mutallab ya ce "Namiji kikewa kuka, namiji kikewa kuka yaya? Raina ki kike so ya yi ko mene?" Ya ce yana ɗaɗɗaga mata gira, ta shiru ya sake matsawa wajanta muryarsa a saman kanta ya ce "Kuka kikewa namiji?"

"Na Ammo baka san soyayya ba ko? Saboda kai yaro ne?" Ya dinga kallon ta, yana nanata yaro a kansa ta ce "Wallahi ina son shi sosai, burina bai shige na yi aure na bar zaman gidan nan ba, na je gidan yanci ko zan samu halin taimakawa Ammo, shine yanzu sai ya fasa auren, ya gaji da ɗagawa da ake yi, ga matsalar Malam na aure aure yana sakin yara kara zube ya je kunnen iyayensa, ina jin tsoron gorin dangin miji, kuma ina son shi" A hankali ya ja numfashi ya durƙusa daidai kanta fuska a kame yana yi yana riƙe gefen kansa, ya dinga kallon ta ya nisa ya ce "Sau biyu kenan, sau biyu yaya, kin kalle mini ƙirji, kin ce mini yaro" idanunsa har wani ruwa ne yake kwanciya a cikinsu, jikinsa na ɗan rawa. Sa'adah ta ce "Tayo"

Ya zuba mata ido.

"Daman ba rarrashi na za ka yi ba? Yayarka ce ni fa?"

"Na sani ai yaya, bana son ana ƙasƙantar da kimata, da gaske ban so" a sanyaya Sa'adah ta ce. "Allah Ya baka haƙuri" ya ƙanƙantar da idanunsa ciki, ƙirjinsa na buɗewa ya daɗe a haka sai kuma ya ja numfashi ta ƙirjin ya haɗiye ya ce "Ki ce ya zo gobe ya amshi komai nasa" ta yi saurin kallon shi ta ce "Bama a sasanta ba? Na gaji da zama a gidan nan shine zaka ce ya zo ya amshi kayan, wallahi ina son shi....,"

"Quiet yaya, silent"

Ya ce yana miƙewa sai ya girgiza kai ya ce "Abin da zan yi dole sai ya zo ok,ai bani da burin lalata miki farinciki ok? Zan kawo miki ganyen LIMƘABIN KALGO ki haɗa da jar kanwa ki jajjaga shi, bayan kin jajjaga ki saka a rana ya bushe, bayan ya bushe sai ki daka ya zama gari. Sai ki samu madubi irin naku ki wanke ki shafe garin da kika haɗa da jar kanwar ki shafa a saman madubin, idan ya ɗan jima kaɗan sai ki kwashe na saman madubin ki shafa a fuska, ba shima ko Gwamna sai buzunsa ok, aure dole ne" ya ce kai tsaye yana taune lips, Sa'adah ta dinga kallon shi tana tsoron ta yi magana ta tunzuro shi. Ta kasa yin shiru ta ce "Ina kasan wannan sirrin Tayo?"

"Ki bar shi idan bakya so, sirri ne mai zaman kansa na ba ki saboda Allah da Manzonsa, wallahi ko faɗa kukai da mijinki kafin ya dawo kikai wannan sirrin uhm... Yaya kenan kina bina sau da ƙafa ina miki abubuwa, amma yaya ni kike cewa yaro ni, a nan ɗina na ji zafin maganar nan yaya"

Ya nuna mata tsakiyar ƙirjinsa, yana shigar da idanunsa ciki, Sa'adah ta miƙe tana murmushi ta ƙarasu zata taɓa shi sai data miƙo hannunta ya zame, ta tuntsira ta kifa ƙasa ta ce "Wayyo hannuna,zaka karya ni fa" ya kalleta sai kuma ya dunƙule hannunsa ya dinga haɗa zufa, ta miƙe tsaye ta ce "Saboda ka taimaka mini shine kuma zaka kassarawa mijina ni? Ture ni fa ka yi Mutallab?" Bai tanka ta ba, sai kallon gefe da ya dinga yi, hannu ta miƙa zata riƙe shi babu zato kamar kuma daga sama ta ji saukar kunama a cikin rigarta, wani ihu Sa'adah ta kurma a gigice ta hau zazzage rigarta tana cewa "Wayyo Allah, Ammo, Malam Anyy Hameeda, Bafullatana wayyo na shiga uku wani abu a rigata wayyo Allah, Mutallab ka taimaka mini" ya saka hannu ɗaya ya ɗan tushe kunnensa guda, bai kuma motsa ba. A haka Ammo ta shigo da gudu zuwa cikin ɗakin ta ce "Sa'adah lafiya ne wani abun ne?" Sa'adah ta kasa magana sai haki take tana ƙanƙame hannun Ammo. Rigar suka fara zazzagewa sai ga ƙatuwar kunama ta faɗo daga cikin rigar Sa'adah ta mace, Ammo ta ce "Subuhanallahi kunama ce ai garin yaya haka?" Ta girgiza kai tana kuka har

lokacin, ta juya ta kalli Mutallab ta ce "Auta kai kuma kana jinta ko ka taimaka mata eh?" Ya juyo ya kalli Ammo sai bai ce komai ba sai zufa dake tsattsafo masa a tsakiyar goshinsa ta ce "A rayuwa idan baka taimaki yan'uwanka ba Muhammad suwa zaka taimaka? Baka da kamar su a duniya wallahi, ina sake maka tuni da ƙarfin zumunci idan mutum bai yi a duniya ba dole zai yi a lahira. Ka fita can ana kiran sallah ka bani waje" ta yi ta gama bai motsa ba a hankali ya saka babban yatsarsa ya shiga murza tsakiyar goshin nasa. Har zai fita ya juyo ya ɗauke bokitin alawar madarar ita dai Sa'adah bata kula shi ba ta a hankali take jan numfashi saboda zafin ya fara raguwa ba karamar ɗazo ba.

***Tana zaune a ɗakin tsakiyar gado ta tanƙwashe ƙafafuwanta waje guda, ta ɗora filo a cinyarta hannunta ɗaya riƙe da waya ɗayan kuma wani ƙaramin littafi ne a hannunta. A hankali take danna wayar tana yi tana sauke numfashi a hankali take duba bayanin da ake yi akan drama ɗin, ita ba san ya aka yi aka cire sunanta a English club, aka mayar da ita Hausa drama shi ya sa ya rasa amsar bawa Kimiyya, gashi kuma dole idan aka zaɓi mutum sai ya yi abin da ake buƙata, but ita a takure take wannan bayanin is too much ita duk ta ina zata iya haddace waɗannan? Babu space ɗin haka a ƙwaƙwalwarta.

"Safiyyerh...!" Aka kira sunanta a ana buɗe ƙofar tare da shigowa cikin ɗakin nata.

"Ummi" ta ce a hankali.

Ummi ta ƙarasa shigowa cikin ɗakin hankalinta duka a kan Aafiyyah. Ta ce "Me kike yi ba ki fito dinner ba? Kin sha maganinki" Aafiyyah ta buɗe ido sai ta ce "Laa, bana jin yunwa ne Ummi" Ummi ta nemi waje ta zauna gefen gadon, ta miƙa hannunta, Aafiyyah ta miƙa mata wayar hannunta, Ummi ta amsa ta shiga WhatsApp ɗin Aafiyyah ya gama dube dubenta, ta shiga wajan bidiyos da photos ta gama dubawa, ta dawo wajan call logs ta duba ta shiga wajan messages nan ma empty sai alert na banki da aka tura mata kuɗi. A hankali ta ce "Safiyyerh...!"

"Na'am Ummi" Aafiyyah said.

"Ki yi haƙuri kin jini daughter, kina kan daidai muma haka, haka kuma daddy don't feels bad"

Jinjina kai kawai Aafiyyah ta yi tana lumshe idanunta bata ce komai ba. "Safiyyerh"

"Uhm'uhm Ummi, kar sunana ya ƙare haba Ummi" ta ce tana yarfe hannunta idanunta ya cika da ƙwalla kamar mai jira dama. Ummi ta ce "Wai yaushe za ki daina shagwaɓa da kukan banza ne? Ni duk na rasa meke damunki sai wani zuƙewa kike kina ramewa? Ko wani abu kika saka a ranki?" Sai Aafiyyah ta fashe da kuka, ta faɗa jikin Ummi tana birgima da ihu tana cewa "Ummi kai na, kai na ne?" Ta dinga kuka tana birgima, Ummi ta saki baki tana kallon ikon Allah, can kuma ta buɗe ido a tsorace tace.

"Safiyyerh mene a jikinki nake gani kamar jini? You are bleeding"

"Bleeding?" Aafiyyah said, loudly with shocked a fuskarta. Sai ta tsayar da kukan nata tana zazzare ido. A hankali Ummi ta yi murmushi ta ce "Ashe da akwai abin da zai ba ki tsoro? Yaushe kika fara ganin haka?" Aafiyyah ta gigice ta sake sakin wani kukan cikin shagwaɓaɓɓiyar muryarta ta ce "Innalillahi, Ummi I'm scared jinina zai ƙare wayyo daddy my blood jinina" Ummi ta riƙe ta, ganin how scared of na abin da ta gani, gabaɗaya bata son ganin jini hankalinta tashi yake yi. Ummi ta jata har zuwa bathroom ta ce "Yi wanka ki wanke jikinki sosai ina zuwa" har Ummi ta fita sai ta dawo ta ce "Ki saka warm water" fita ta yi. Kafin ta dawo Aafiyyah ta gama yin wankan, ta buɗe banɗakin kai tsaye ta shiga, tana sanye da towel a jikinta Ummi ta dinga kallon ta sai ta miƙa mata pant da audigar data haɗa mata ta ce "Saka" bata musa ba ta amsa ta saka, bayan ta kammala ta bata wani ƙaramin turare ta ce saka a ƙasan wuyanta a hammata.

Aafiyyah na zaune tana jinta duk wani iri a jikinta, ƙaramin short jeans ne a jikinta sai wata rigar pallazo mai faɗin hannu. Ummi ta kira sunanta ta ce "Safiyyerh wannan jinin da kika gani a jikinki shi ake kira da jinin al'ada, wanda Ubangiji ya ɗorawa kowacce ɗiya mace hakkin yinsa face wacce take da ciki ko shayarwa, ana cewa wacce bata al'ada to bata haihuwa ne. Ina faɗa miki wannan ne saboda hakkina ne nauyi nane, it's my responsibilities ba sai na jira malami ba, ni ce nan malamarki Safiyyerh. Wannan jinin da kika gani duk wata ake yinsa, wasu farkon wata wasu ƙarshe, wasu tsakiya idan ana yi ba'a sallah kuma ba'a yin azumi, kinga kenan bake ba yin azumin ranar litinin da kike na Alhamis da juma'a, ba'a rama sallah amma ana rama Azumin da mutum ya sha kin gane?" Aafiyyah ta jinjina kai.

"Abu mai mahimmanci"

"Ummi" Aafiyyah kira sunan a raunace ta ce "Tsoro kike bani da waɗannan bayanin"

"Babu tsoro Safiyyerh, matakin girma ne duk da na yi mamaki da ganin hakan sai dai ko wacce ɗiya mace da yanayin yadda take farawa, sai yanzu na san dalilin rashin lafiyarki farawar da za ki yi ne, sai dai Dr bai yi mana mentioning hakan ba. Safiyyerh daka ranar da mace ta fara jinin al'ada tana bari namiji ya taɓa hannunta zai mata ciki, kuma kin san yin ciki haramun ne Ubangiji ya yi hani ga hakan idan ba aure aka yi ba, shi kuma aure ana yi ne sanda yarinya ta cika shekara 25 a duniya ba a irin wannan shekarun ba, kinga You have to be very careful, cikin shege ai ba kyau ɗiya mace da nutsuwa aka sonta da kamewa ki riƙe mutuncinki sai kowa ya girmama ki, mu mata ƙashin haƙarƙari ne"

Ta sauke numfashi ta ce "Ki taya mu tattala tarbiyyarki har zuwa sanda ya dace kin ji?"

Aafiyyah da idanunta ya cika da ƙwalla ta ce "I will, i will Ummi as so much as I can, zan kula"

Sai kuma ta yi shiru, can ta ɗago kai ta kalli Ummi ta ce. "You promised me, daddy promised too, everyone promised me Ummi, don Allah keep your words and promised don Allah Ummi, zan yi abin da kuke so nima ku yi mini"

Ummi ta dinga kallon Aafiyyah kallo na tsanake da haƙiƙa, ta san halin yarinyar da mugun saka abu a rai, amma tana kiyaye duk wani abu da za ta yi ransu ya ɓaci tana tsananin ƙaunar mahaifinta. Ummi ta sauke numfashi slowly ta ce "keep praying Safiyyerh" ta miƙe ta fice. Aafiyyah ta bita da kallo a hankali ta cije lips ɗinta, tana kiran sunan Allah a zuciyarta. Daman 10:00 ake sawa ta kashe ta ajjiye idan karatu ne ta buɗe system, ta kwanta ta shige cikin duvet ba bacci take ba tana ji Ummi ya shigo ɗakin ta kwanta kusa da ita, har wajan 2 da rabe na dare da Ummi ta miƙe a hankali ta fita without making any sounds da zai sakawa Aafiyyah ya farka ba tare data san idanunta biyu ba, har dab da asuba da Ummi ta sake dawowa ta kwanta kusa da Aafiyyah idanunta biyu still. Har aka fara kiran sallah ta farko ta miƙe, ta yi wanka ya sake gyara jikinta sanin ba sallah za ta yi ba sai ta zauna ta fara azkar thinking ko daddy na gari yau?.

7:15 ta fito entrance na gidan a hankali take tafiya, kasancewar kuma Friday ne sai ta yi using sportswear na makarantar wanda yake kasance brown colour ya yi mata kyau sosai, ta saka baby hijab ko breakfast bata tsaya ba. Murmushinta ya faɗaɗa tana lumshe idanu ta buɗewa a hankali ta ce "So you are here Baba, daka yi zamanka sai na yi driving"

"Rufa mini asiri ƙaramar Hajiya, ai tuni na gyara mota muje kawai"

"Baba....," Aafiyyah said with smile on her face, tana zura hannunta ɗaya wando ya ce "Hajiya ƙarama barka da wayewar garin juma'a muje na kai ki makaranta na dawo na yi shirin masallaci" Aafiyyah ta dinga murmushi ta ɗan rusuna kaɗan ta ce "Ina kwana Baba?" Ya amsa cike da farinciki, ya buɗe mata bayan mota sai ta ingiza kai ta ce "Ko gaba zaifi?" Ya buɗe mata ta shiga, a hanya ya dinga mata hira ta yi shiru wani lokacin kuma sai ta yi murmushi ta juyo ta kalle shi ta ce "Baba ka yi mini addu'a". "Addu'a kullum ana yi Hajiya ƙarama, rayuwa za ta yi albarka in sha Allah" ta ɗakko kuɗi ta ce "To ga sadaƙa" ya amsa ya dinga sanya mata albarka cike da fara'a.

A kusan tare motoci wajan ukun sukai parking a harabar makarantar Fgc. Kimiyya ya buɗe ya fito yana mamakin ganin Aafiyyah yau a gaban mota kuma ita da driver ya yi murmushi ya ƙarasa yana buɗe mata ya ce "Barka da zuwa crush" Ta yi masa murmushi ta ce "Morning Kimiyya" Safiyyerh ta ƙarasu ta ce "Hi" Kimiyya ya ce "Ta bestie ikon Allah irin wannan sammako haka, ko kema kina da drama a club naku?" Ta yi murmushi kawai.

"Safiyyerh how are you?"

"Allahamdulilah, as you can see Aafiyyah ya jikin nakin?" Shoulders Aafiyyah ta ɗaga, bayan ta fito da shade glasses ɗinta ta saka hannunta duka biyun cikin aljihun, ta ɗan matsar da ƙafarta ɗaya baya, ɗayar kuma a gaba, yanayin tsaiwarta zai saka ka fahimci ta saba buga ball. Gabaɗaya sportswears ne a jikinsu, na Safiyyerh black colour Kimiyya ma nasa black ne sai Aafiyyah mai brown. Tafiya suka yi a tare har zuwa cikin makarantar tun daga nesa ta hango shi ya harɗe ƙafarsa ɗaya a saman ɗaya, shi kaɗai sai hannunsa dake riƙe da wani abu da yake busa yaƙi a hankali yana yin sama. Murmushi ta yi tana jin wani irin farinciki a

zuciyarta ganin Aafiyyah kuma ya saka ta kasa ƙarasawa gare shi ɗin, duk da yadda zuciya ke janta zuwa gare shi, daman da damuwa ta kwana kuma.

Aafiyyah ta zaro wayarta a aljihu, still hannunta ɗaya a cikin aljihun, ta ɗan matsa kusa da Safiyyerh a hankali ta ce.

"Ba'a sanyin jiki, da sanyin safiya ake kama fara safiyyerh. Ga bestienki can ki je"

"Aafiyyah!"

"Yes, go mana"

Safiyyerh ta kalli Aafiyyah da mamaki ta ce "Wonderful, Aafiyyah kuma lafiya kike yau ɗin nan? Naga bakwa shiri da Mutallab what exactly wrong with you har kike cewa na je wajansa, shi ya ce yana buƙatar ganina?" Aafiyyah ta girgiza kai, tana ɗan cilla ƙafarta gaba ta cake ta akan ball ɗin da Kimiyya ya cillo mata ta ce "Oh, ai bani da wani business da shi, me ya sa zan faɗa da shi? Why should i Safiyyerh? Bani da matsala da shi and he never be my headache. Tunda daga nesa kike ƙoƙarin sauya hanya zuwa gare shi, Safiyyerh ki yi soyayya mana ai ba wani matsala idan hakan zai sama miki farinciki, kina yi kina tuna muhimman abubuwa, soyayya akwai daɗi sai dai love is flying...."

"... love is flying?"

Safiyyerh ta maimaita tana kallon Aafiyyah. "Yes, mana"

"Bangane ba, me hakan yake nufi?" Safiyyerh repeated again. Aafiyyah ta ɗaga kafaɗa ta ce "Love is flying, ki yarda mana"

"Aafiyyah kenan, kina raina tunanina sometimes, ko babu komai i older than you"

"And? Shi wai shekarun nan da kike proud da su kina ɗaɗɗaga shoulders a kan su, a tsakiyar goshi ake rubutawa ne?"

"Namesake kenan, na san ki fa"

"Kamarya?" Aafiyyah ta tambaya tana murza ball ɗin ƙafarta Kimiyya na jin su. Safiyyerh ta yi shiru kawai, Aafiyyah za ta yi magana Kimiyya ya ce "No, please. A bar maganar my crush" banza ta yi masa, ya miƙa hannunsa zai riƙe nata ta yi saurin kallon shi tana buɗe masa manyan idanunta ta ce "Kar ka fara Kimiyya" ta juya kan Safiyyerh ta ce "Ke sometimes kan ki baya kawo nepa Saff, ki yi amfani da lokacinki wajan janyo hankalin wanda kike so a kan ki, love him, care about him, ki sauya shi zuwa yadda kike so, ina ba ki tabbacin zai ba ki duk me kike buƙata trust me" tana cewa haka ta sunkuya ta ɗauki ball ta ce "Ki je mana, bari na ɗan buga ball"

Aafiyyah ta juya ita da Kimiyya. Safiyyerh kuma ta nufi inda yake zaune ya hakimce tare da kame fuska, shima sportswear ne a jikinsa brown colour, sun haska baƙar fatarsa ya saka p.cap ta rufe masa ido. Ta ƙarasa tana cewa "Assalamu Alaika bestie me" bai kalle ta ba, sai naɗe ƙafarsa da ya yi kawai ta nemi waje ta zauna a hankali ta leƙa fuskarsa suka haɗa ido, ya buɗe mata manyan idanunsa. Ta yi murmushi ta ce

"Good morning Mai dawa"

Ta miƙa hannunta ta amshe abin hayaƙin da yake busawa, ta miƙa hannunta a hankali zuwa bakinsa ta buɗe, a hankali ta kai nata bakin ta shanshana ta lumshe idanunta jin ƙamshin minti. "Na ɗauka zan ji warin hayaƙi, so amazing bakinka ƙamshi sosai" ta buɗe abin hannunta, breakfast ɗinta ta buɗe ta gyara zamanta, soyayyan dankali ne da ƙwai sai Indomie wacce aka yi fried Indomie with egg da sauran potatoes soup. Ta saka masa spoon a gabansa ta ce "Ina gaishe ka kaƙi amsawa babu kyau fa, kuma amsa sallama wajibi ne in ji faɗar Annabin tsira.

"Kina zuwa islamiyya ashe"

Ta ji maganarsa a nutse ta sauka a kanta har zuwa ƙirjinta ta ce "Me ka ɗauka to? Ina zuwa makarantar islamiyya a bayan layinmu, weekend ma ai tahfix nake yi don ka ji, ina da ƙoƙari sosai sai dai" ta yi shiru yanayin fuskarta duk ya sauya idanunta ya cika da hawaye ta ce "Bestie, ban san meke damuna ba, an kasa fahimta ta, ba wanda yake son jin damuwata, hatta kai ma da abin da nake yi, na yi dominka ka kasa fahimtar zuciyata ka kuma kasa yi mini uzurin cewa ba yin kai na bane, hatta a Islamiyya bana gane karatu wallahi, a baya na fi kowa bada hadda amma yanzu ko aya biyu bana iya riƙewa, na kasa yanzu bana fahimtar karatu" ta sunkuyar da kanta ƙasa tana goge hawayen idanunta ta ɗago ta ce "Ni sai nake ji kamar na mutu" ta sake yin shiru ta kalle shi tana murmushi ta ce.

"Kuma ba lallai na mutun ba ko?" Hawaye ya zararo mata ta kifa kanta a kan ƙafarsa ta shiga rera masa kuka, irin kukan data ke fata ta samu damar yi ta kasa, sosai take kukan wanda hakan ya saka take jin sauƙi a zuciyarta. Mutallab dai kallon ta yake, deep down na zuciyarsa yana jin tausayinta, idan ya tuna Jaanah baya jin daɗi, ba zai so Safiyyerh ta rasa ranta sabo da shi ba, baya kuma buƙatar zutar da zuciyarta.

"Maybe ban da rabo ne, wannan Safiyyerhn ba rabon Mutallab ba ce. Soyayya rayuwa ce bestie, abu biyu ke cutar da kowanne mai rai SO da ƘI, ka yi mini uziri maybe ina over acting, wallahi ban san ina yi ba, da so kawai idan Ubangiji yaga dama sai ya azabtar da bawansa, ƙilan akwai abin da na yi wanda bai kamata ba" Ta yi dariya tana goge hawayen idanunta, ta ɗaga masa gira da kashe ido, a hankali kuma ta ɗaga kafaɗa ta ce "So i realise cewa na yi failing, na faɗi a soyayya kuma i accepted it."

"Are you going to give up?" Ya ce yana tsattsare ta da idanunsa.

Safiyyerh ta ce "Over my died body…. Ina nan ina son ka, kuma i will wait for the day da zaka amince zan ihu da murna sosai"

"Hmmm"

"Mu ci abinci"

Ya kalli spoon ɗin, ya kalli hannunta ya girgiza kai ya ce "Da hannu nake ci ai" ta ce "Tab, ban yarda da tsaftar hannunka babu mamaki ka shiga jeji jiyan nan, muga hannun" ta saka hannu ta janyo hannunsa ta dubi yatsun hannun taga farce ya taro sosai ta ce "Ƴan yʷan yʷan mai dawa ƙazami, bari na yi aikin lada na fara aikin lada, kuma aikina tun yanzu, as your wife" ya dube ta, ta ɗakko abin yankan farce mai kyau ta fara yanke masa a hankali. Bayan ta kammala tas ta saka ruwa ta wanke masa daidai nan su Aafiyyah suka ƙarasu wajan Safiyyerh bata lura da su ba don haka ta ce.

"Bestie..."

"Hmmm" ya ce yana duba yatsun hannunsa yadda ta yanke masa farcen ya yi kyau sosai.

"Sweetheart

"Hmmm"

"Ka san me? Dole sai fa ka aure ni wallahi, ko kana so ko baka so i don't care, Allah sai na zama matarka da gaske kuma zan zame maka mace ta gari da na ji ana faɗa i promise you, zan amsa sunan matar Mutallab"

"Matar Moh, za ta zama mai irin halin Moh ne kawai Safiyyerh "

Safiyyerh ta gyalgyale da dariya sosai, har tana ƙwarewa ta girgiza kai ta ce "Mene a halin naka banda son kai? E, kana da halin son kan ka as always, baka damu da damuwar wani ba, you don't care about my feelings, all the time kana wasa sa emotions and feelings nawa saboda wani ra'ayinka mara tushe. Shariya, rashin fara'a kamar ka ce ka shiga uku, rashin sukuni da zuciya ƙifaɗi ɗagawa taƙama, duk halin mijina Mohammed Mutallab Abdullahi, kuma bai daman ba i am still loving you dear, the way you are zaka sauya ne"

"You are not serious Safiyyerh"

"I love you "

Aafiyyah na zaune ta ce "Iyee ga wasu sabbin ƙinƙisa, lemme snap them na nunawa jikoki da yʻa yʻa" pictures ta yi musu. Mutallab ko inuwarta bai kalla ba, ya tattara hankalinsa waje guda yana cin abincin yana sauraren hirar Safiyyerh jinjina mata kai kawai ya yi. Ji ya yi ta yi shiru ya ɗago kai ya kalleta, ya ga shi take kallo idanunta cike da hawaye ya ɗauki dankalin ya miƙa ta maƙale masa kafaɗa a kumbure ya ce "Ko dai ki amsa, ko na danne ki na ɗora miki da sai ki tsaya kina kallo na" ɗan ƙaramin bakin nata ta buɗe masa ya zubawa fararen haƙoranta ido ya zura mata dankalin ta amsa ta fara ci. Safiyyerh ji ta yi nauyin ƙirjinta ya ragu, suna zaune aka ce lokacin drama ya kusa a shiga drama hall.

Hall ɗin ya cika sosai Safiyyerh ta dinga dubawa babu Mutallab. Hausa drama aka shirya wani ɗan ƙaramin script da yake nuna rashin jituwar aure da ake samu akan ƙabilu biyu Yaruba da Hausa Fulani, yadda Yaruba basa son bawa Hausawa auren yaransu daga ƙarshe yaran su bijire musu illar hakan har a rasa ɗaya daga cikin yaran, inda macen ke mutuwa shi kuma namiji ya samua depression. Title kuma na Hausa drama ɗin shine DANGANA. A hankali aka dinga gabatar da gida-gida na shirin har aka zo inda za a nuna saurayin ya zo wajan budurwar har ƙofar gidansu ita kuma ya fito a gigice.

“Yaruba boy”

Safiyyerh ta ce a hankali, ganin ya shigo hall ɗin a hankali jikinsa sanye da kayan yarabawa, har da gashin hannun ya yi wani irin kyau, ba zaka taɓa cewa shi ɗin ba jinin Yarabawa bane yana wata tafiya majestically sai cije laɓɓansa yake da sukai jajur. A hankali ya duba agogon hannunsa sai wani yaro ya zo shigewa a hankali Mutallab ya ce "Hey you"

Yaron ya tsaya ya ce "Bawo ni MO ṣe le ṣe iranlọwọ? Ta ya zan iya taimaka maka?"

Mutallab ya yi jim, zuciyarsa cike da tsoro da fargabar ko za ta fito? Ko iyayenta a wannan karon za su bar ta? Ko za su yi masa alfarmar auren Aafiyyah? He can't do without his Iyafin.

"Call.....," ya ja numfashi a ƙirjinsa ya ce "Kira Aafii.....

"Aafiyyah dai?" Cewar yaron. Mutallab ya jinjina kai, yaron ya juya zuwa cikin gidan. Mutallab ya tsare ƙofar gidan da idanu, babu jimawa sai gata ta fito kyakkyawan shigar Hausawa ce a jikinta shigar Hausa Fulani, atamfa riga da zani ɗaurin ya ɗan zame ganinta ya fito. Kallon cikin idanu suke wa juna, Aafiyyah na yi wa Mutallab kallon "You are here?" Shi kuma yana mata kallon "Are you ready to runaway Aafiyyah?"

Aafiyyah ta zame idanunta ta ƙarasa muryarta na rawa ta ce "Suna nan a kan bakan su, ba za su bari mu yi aure ba, za su raba mu" hawaye ya fara zuba daga cikin idanunta ya matso dab da ita, numfashinsa na sauka a fuskarta har tana jin ƙamshin bakinsa calmly ya ce "I know, na sani" Aafiyyah ta yi shiru. Ya saka hannunsa ɗaya ya tallafo haɓarta ya ce "We have to runaway Aafi.."

"Kana nufin mu gudu daga wajan iyayenmu? Kana nufin na bar iyayena na bika?" Ya ɗage mata girarsa duka biyun yana sake ƙarewa fuskarta ta asalin fulani kyau, ya saka yatsa ya dinga share hawayen fuskarta da tsayarsa ɗaya a hankali ta matso kusa da shi, ta saka hannunta ta kamo nasa ta riƙe sosai ta ce.

"Iyayenmu masa son soyayyarmu Tayo, Kabi umarnin naka iyayenka nima zan bi nawa, ka auri yar'uwarka Yaruba, nima na auri Hausa Fulani. Something is over doesn't mean your life is over, love is flying, shi kuma zan iya ajalina" Aafiyyah ta ɗago ta kalli cikin idanun Mutallab ta ce "Wannan shine damar da nake shi na faɗa maka how much i love you. Idan har zuciya zata dinga bugawa da amfanin iska tana zagayawa da jini a dukkan lungu da sako na jiki tsawon shekaru ba tare da gajiyawa ba, bana tunanin zan taɓa gajiya da son ka Tayo. Da ace ana ganin shauƙi da tunanin zuci a zahirance, da na nuna maka yadda son ka ya mamaye zuciyata. Tun dana sanka zuciyata ta kasa tsayawa da tunaninka, akwai wani abu na musamman game da kai da bazai taɓa barina na manta da kai ba. I love you endlessly! I love you secretly! I love you like a crazy! I love you today tomorrow and always"

Aafiyyah ta fara ja baya yana binta, ya rufe bakinta saboda kuka sosai ta ce "You still remain in my heart, amma mu haƙura da juna mu bi umarnin iyayenmu"

"I can't Aafiyyah!"

"Why?" Ta ce masa, tana sake yin baya yana matsowa wajanta ya saka hannu ya damƙo hannunta a daidai kunnenta ya ce "Because you are a tiger, ke ya dace da zama matar Moh fil'duniya kuma til-janna i adore you Aafi" juya ta yi saboda kukan da ya ƙwace mata yaƙi sakinta "Ka cika ni, ka sake ni Please mu haƙura da juna haka Tayo" Ya girgiza mata kai sai kawai ta faɗa jikinsa tana sakin wani irin raunataccen kuka zuciyarta na bugawa da ƙarfi, Mutallab ya yi shiru sai ya fara tuna last abin da zai yi a cikin script ɗin, he hold her back a jikinsa ya rungumeta, Aafiyyah ta dinga kuka zuciyarta na buɗewa, a hankali ta fara tari jini na fita ta cikin bakinta idanunta na rufewa jikinta ya saki ta zame daga jikin Mutallab ta faɗi a wajan babu numfashi.

“Cut.....!" Mai kula da drama ɗin ya ce, aka buƙaci Aafiyyah ta miƙe. Abu kamar wasa Aafiyyah bata motsi. Class teacher ɗin ya ƙarasu ya fara kiranta "Aafiyyah, Aafiyyah" amma shiru ya ce "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, Aafiyyah died bata numfashi" da sauri Muhalli ya ture class teacher ya durƙusa akan ƙafafuwansa ya fara jijiiga Aafiyyah amma ina bata numfashi bata motsi. Safiyyerh da tun ɗazo ta daskare tun farkon fara drama ɗin tanja wani irin numfashi ta miƙe da gudu ta ƙarasa wajan itama, a daidai nan daddyn Safiyyerh ya shigo hall ɗin hannunsa ɗauke da tafkekiyar bulala, daman daga office ɗin principal yake kai tsaye, idanunsa ya sauka akan Mutallab, sai yake ganin Aafiyyah dake kwance tamkar Safiyyerh bai tsaya jiran komai ba ya rufe Aafiyyah take sume a ƙasa da duka idanunsa rufe.

Gana yau da Laraba, mu haɗu Alhamis 😀😀.

Mutallab paid book ne #500.

Pay before you read

08164069385

[1/7, 9:35 PM] Sis Fauzy: Chapter 34: Frist visit

Safiyyerh ta ƙarasa wajan da sauri tana fasa ihu ta ce "Daddy Aafiyyah kake duka, Aafiyyah ce" amma ina sam idanun daddy ya rufe, tsoro kuma da mamaki ya saka mutanen wajan suka kasa yin wani motsin kirki. Da dukkan ƙarfinsa ya saka hannunsa a ƙirjin Prof ya hankaɗe shi zuwa baya, jikin Mutallab sai kyarma yake yi sai kuma girgiza kansa yake yi.

Da mamaki Prof ya kalli Mutallab da kyau yana gyara tsaiwa ya ce "Wato ba za ka rabu da yaya ta ba? Ka zame mini masifa da anno ba?" Ya yi ƙwafa.

"Point of correction, yarka ta zame maka masifa dai ba ɗan Malam Abdullahi ba" Mutallab ya ce yana huci kamar ya ci babu, yana sake kallon bulalar dake hannun daddy. Shima daddyn ya ce "Ka bani waje, laifina ne dana saka Safiyyerh a makarantar da zata iya haɗuwa da yayan talakawa irinka. Kuma zan yi wa malaman magana na ji yadda aka yi suke barin lalataccen yaro irinka a wannan makarantar mai mugun nufin lalata mini yarinya"

"Ko? Wannan da kake duka ba yar taka bace, ka je ka yi iko da wacce ka haifa ba wannan ba. Kuma ba'a nunawa Mutallab ba'a son abu ka gane ko?" Ya ce yana cije lips. Har zai juya sai kuma ya ce "One more thing, zan yi farinciki idan ka hana gudaliyar yarka bibikona" kafin Prof ya yi magana principal ɗin makarantar ya shigo hall ɗin, tare da wani, sai bawa wanda suka shigo da shi haƙuri yake ko kallonsa bai yi ba, da wani irin mamaki yake duban Aafiyyah dake ƙwance kamar bata numfashi, ya yi saurin durƙusawa ya ɗago ta zuwa jikinsa yana jijjigata idanunsa yayi jajur ya ɗaga kai ya dubi malamin nasu Aafiyyah ya ce "Waye ya yi mata dukan nan? Wane ya dake ta?"

Teacher ɗin ta ce "Don Allah ka fahimta, kuskure aka samu"

"Problem? Kuma akan ta za'a samu matsalar? Kalli jikinta? Ya haifeta ne da zai mata wannan jahilin dukan? Mari wannan rabon da ta yi abin da za'a mare ta na manta ba wai don ta shige duka ba, shine zai yi mata wannan mummunan dukan? For what reason eh?". Cike da banbaki Principal ɗin ya ce "Ka yi haƙuri, kowa ya san yarinyar nan bata da wata matsala a makarantar nan, kuskure aka samu, ya ɗauka yarinyarsa ce shine ya rufe ta da duka da nufin hukunci" teacher ɗin ya ce

"We are very sorry please"

"Sorry for yourself. Idan yarsa ce haka ake tarbiyyar yarinya, wane ya ce duka yana gyara yaro? To hukuma zata raba ni da shi" teacher zai sake magana ya ɗaga masa hannu ya ce "Ka yi addu'ar wani abu bai same ta, sai mu ɗora bayan jan kunnen da na yi akan kada a saka ta a drama ɗin, ai tun kafin yau na san za su yi kuma ban amince ba, har makarantar na shigo na nemi alfarmar hakan" ya ja siririn tsaki tare da ɗaukan Aafiyyah ya fice daga cikin hall ɗin. Tun kafin ya ƙarasa wajan motarsa dake waje guda sai sheƙi take yi, kafin ya ƙarasa driver ya buɗe masa ƙofar, ya shiga cikin motar hannunsa ɗauke da Aafiyyah, a tsorace yake jijjigata da kiran sunanta tare da fargabar abin da zai faɗa a gidan, they won't take it, ciwon Aafiyyah barazana ce a gare su, musamman mahaifinsu ba zai ɗauka ba,sau huɗu yana kiransa a hanya akan is she ok? Wani abu ya samu Safiyyerh ne? Jikinsa ya yi babu daɗi, go and check her, ka tabbatar lafiya take kuma ka kira ni vedio call na ganta i want to see my daughter. Shine abin da Paah ya dinga faɗa masa a waya, bai san zai zo ya same ta haka ba yana shigowa yake ganin ƙaton banza na dukanta? Yana da hankali? Ko yar cikinsa zai wa haka ne?. Ya sake jan tsaki ya ce

"Mu je asibiti Baba, ba zan iya zuwa gida da ita haka ba, ina mai jin tsoro a zuciyata sosai" Baba ya ce "Ka yi addu'a babu abin da zai samu Hajiya ƙarama"

"I hope so...." Ya ce yana rungume Aafiyyah a jikinsa cike da ƙauna.

*

Safiyyerh ta durƙushe a wajan, dukkan jikinta rawa yake da ɓari hatta zuciyarta rawa take yi kwatankwacin yadda jikinta ke rawa, ta cure waje guda, ko kukan ta kasa yi wani abu ya tsaya mata a ƙirji ta fara kokawa da abin da kuma numfashin daya tokare mata ƙirji zuwa maƙoshi, a yanzu ba damuwarta faɗan daddy ba, ba damuwarta dukan da zai yi mata ba, ba damuwarta hantarar da Mutallab zai yi mata ba, ba damuwarta ƙazafin Wahee ba. Wani abu take ji yana rayuwa a ƙirjinta da ginowa a cikin ƙwaƙwalwarta mai kama da kishi, baƙin ciki, takaici ta kasa goge bidiyon Aafiyyah da Mutallab a idanunta, ganinsa take kamar zahiri ba shirin kwaikwayo ba, ganin abun take kamar labaran nan na littafan Hausa na soyayya da ta ji ana faɗa, shakku da tsoro sukai mata hawan ƙawanya a zuciya ta kasa sukuni ta ji ta tsani kanta komai ya dai na yi mata daɗi, bata so koda wasa zuciyarta ta kamu da tsanar wani rai a duniya ballantana Aafiyyah, her childhood friend, forever and ever wani irin deep friendship mai wahalar bada wani labari ne, a tsakaninta da Aafiyyah.

A razane ta ɗago saboda fisgota da ta ji an a yi, tana ɗago kai ya sauke mata lafiyayyun maruka a fuska, without letting her to recovering daga marin ya sake sauke mata wasu a gigice ta yi baya ta cakume Mutallab tana haɗiyar zuciya.

"I am sorry daddy, don Allah ka yi mini komai a rayuwa ban da raba ni da bestie, zuciyata zafi take mini, daddy don Allah.....,"

"Ko mutuwa za ki yi ki farfaɗo wallahi Safiyyerh kin yi kaɗan na yi miki yadda kike so, ki je ki yi duk abin da zuciyarki ta raya miki" ya yi ƙwafa ya juya tare da ficewa daga hall ɗin, ya ji tsoron dukan Aafiyyah ƙwarai, tsoron daya sanya jikinsa yin sanyi wanda daya tabbatar cewa ba Safiyyerh bace ba zai taɓa saka hannunsa akan yʻar mutumin nan ba, still tsoron ya saka ya kasa huɓɓasa hukuncin da ya yi niyya akan Safiyyerh, again tsoron ya saka ya ƙara yin addition na irin matakin da zai ɗauka akan yaron da ita kanta Safiyyerh, again and again wannan tsoron ne ya saka ya kasa tafiya da gudaliyar tasa ya nufi waje kai tsaye idanunsa kuma a rufe, komai zai zo ƙarshe, but when? Dole sai ya bar ƙasar.

"Safiyyerh!"

Captain ya ce yana tsayawa dab dasu, ta kasa ɗagowa domin ganinta har yanzu daddy na tsaye ta ƙanƙame Mutallab ƙirjinta na ɗagawa da ƙarfin gaske. Shi ma Mutallab bai motsa ba, gabaɗaya jinsa yake wani iri abin da bai taɓa ji ba a duniya, jin Safiyyerh a jikinsa, kukan nata, marukan da aka yi mata ya ƙara tunzura hauhawar zafin da zuciyarsa take masa, da wani irin jin zafin Aafiyyah da yake ji haka kawai, daga yin abu ta faɗi kamar ba jaruma ba abin wasa shine zata faɗi haka? Shine za ta yi haka?.

"Leave, bar nan" Mutallab ya cewa Captain yana fiddo idanunsa waje.

"Idan naƙi fa?"

"Tambaya ta kake? I said leave"

"Ba inda zani sai da Safiyyerh na mayar da ita gida ka gane, tunda naga Safiyyerh taƙi so na, na san cewa ba haka kawai bane, domin ruwa baya taɓa yin tsami banza. Ina son ka buɗe kunne da kyau ka ji, Safiyyerh ba ajinka ba ce, she never be your mate, gwara kasan na yi tuntuni domin matar talaka daban Ubangiji yake yin su, tare da halittar su a duniya, ka fara gina kanka domin a yanzu baka da abin kula da Safiyyerh ko abincin da take ci a gidan ubanta baka da kwatankwacin shi, ita ɗin tawa ce kuma zan tabbatar maka da haka very soon"

"Ok..." Mutallab ya ce a kumbure, har yanzu Safiyyerh na riƙe da shi bai kuma hanata raɓarsa ba domin a tsorace take. Hannu Captain ya kai zai riƙo Safiyyerh, bai san ya aka yi ba, shi dai ya samu kan shi da yin wani irin azababben ihu yana kiran hannunsa kafin ya ji sautin ƙarar ƙashin hannun nasa dake alamta masa Mutallab ya karya masa hannu, ya ji wani irin fitsarin wahala na bin cinyoyinsa. Cikin sauri Kimiyya ya matso ya ce

"Buddy sake shi, ka karya masa hannu fa? Ka cika shi"

Yaƙi sakin hannun yana ƙara murɗewa, Captain sai ihu yake. "Mutallab me ya sa kake yin haka ne? Ka karya shi bayan haka me kake buƙata kuma?"

"Stay away from her"

"Ita wa?"

"Kimiyya ka daina saka mini baki cikin lamurana, bana son illataka" ya ce yana sakin hannun Captain tare da saka ƙafa ya hankaɗa shi baya sai kuma ya damƙi hannun Safiyyerh ya jata zuwa waje, kimiyya ya bisa da idanu domin yanayin idanun Mutallab da sautin muryarsa ya firgita shi ainun tare da bashi maɗaukakin mamaki, sai ya nufi wajan Captain shi da Nahyan, Wahee ma ta ƙarasa wajensa tana cewa "Kai ma ka daina kula shi, idan Safiyyerh ce ka rabu da ita don Allah, let her be, kai ba ajinta bane" wani lafiyayen mari ya saukewa Wahee a fuska zuciyarsa na yi masa ɗaci, kafin ya miƙe da ƙyar yana riƙe karyayyen hannunsa ya yi waje.

Sai da suka yi nisa sosai a dai cikin makarantar ya sake ta yana cilla ta baya, idanunsa ciki-ciki, yanayin kallon da yake mata ya saka ta marairace masa fuska hawaye na bin kuncinta.

"Ka yi haƙuri"

"Da haƙurin ya mutu sadaƙar nawa kika bayar?" Ya ce yana tsuke fuska, babu walwala sam a tattare da shi. Ganin yadda ya fusata sai ta fara dariya tana girgiza kai tare da ja da baya ta ce

"You are impossible, you are impossible Fiyya".

"Kee" ya kira ta a tsawace, kiran da ta ji ya saka zuciyarta girgiza fitsari na shirin ƙwace mata wando saboda firgice. Maimakon ta bar shi, kamar yadda yake fata sai ta matsa kusa da shi tana maƙale masa kafaɗa ta ce. "Bafa rainaka na yi ba, ni ban ce haka ba, yaushe ma na ce haka? Sai ka yi ta tsangwama ta wai? Nima fa mutum ce kamar ka wallahi, at least ka girmama ni saboda kasancewata yʼar'uwarka musulma" ta saka kafaɗa ta ture shi, ko gezau, kamar ta ture gini. Tana sake yin murmushi ta ce "Dalilin Annabi Adamu, Alaihissalam muka zama yʼan'uwa don ka ji, kuma na zama matarka very soon na haifi Yaruba child"

A hankali ƙanƙancewar idanunsa ke rikiɗewa zuwa wani yanayi nada ban, ya lashe laɓɓansa, sai kuma naman ƙirjinsa ya fara rawa yana jinsa kamar a tsakiyar daji ana kaɗa masa ƙahon busa yayin farautar naman jejin.

A ƙirjinsa ya ji maganar "Me kika ce za ki nuna mini? Nunan" ya ce yana narkar da idanunsa.

Girgiza kai ta fara tana buɗe ido ta ce "Laaa la la ni kuma? Yaushe? A ina? Ba dai Safiyyerh ba"

"Kin ce, kin fara irgan dangi"

"Wanne dangin zan irgo?"

"Na girma" ya ce a daƙile.

"A'a, ba ruwana, ba wani irgan dangi"

"You are not serious, sai kin nuna mini, ko ki nuna ko na buɗe na gani na tabbatar" ya faɗa very serious, yana kuma haɗe fuska da kyau kamar ya ce ya shiga uku. Ta dinga masa dariya ta san wasa kawai yake mata, sai dai babu alamar wasa a tattare da shi, ya yi taku ɗaya, ganin kamar kamata zai yi ta juya da sauri tana masa gwalo, duguwar ƙafarsa ya saka mata ya taɗo ta, ta fasa ihu zata faɗi ya riƙo hijabinta, tare da ɗago ta tsaye kamar abin arziƙi sai ta ji ya damƙi kunnenta ya murɗe sosai, idanunta ya cika da hawayen azaba amma murmushi take masa, domin bata bashi damar da zai gane fushinta.

"Kakewa matarka mugunta ko? Kake mini mugunta ana mana aure zan....," bata ƙarasa ba, ta ji ya kama lips ɗinta na ƙasa ya murje, ta kasa kuka ko ihu, sai zufa take yi na azaba, tana jin kamar leɓen bakinta zai cire gashi sai sake murɗe mata lips ɗin yake. A hankali wasu hawaye suka fara sintiri a idanunta, bata san cewa yana da taɓin hankali ba, da ta yi yunƙurin ƙwatar kanta for sure.

Ya zame hannunsa, sai kuma ya shaƙe wuyanta kamar zata rasa mutu haka tane ji, ta fara shura ƙafa, tare da kakarin ceton rai a firgice shima jikinsa na rawa ya ce "Me ya sa kika zame mini ƙarfen ƙafa? Me ya sa kika zame mini kaska ne? Me ya sa kike so mahafinki ya yi ta cin mutuncina? Saboda kina son haka?" Ya sake shaƙe wuyanta idanunta na fitowa alamar numfashi na yi mata wahalar shaƙa, domin maƙoshinta take jinsa, baya sauka ƙirjinta yadda zata shaƙa da kyau ɗin.

Ya sake lashe laɓɓansa ya ce "Ni mahaukaci ne, mahaukacin gaske. No ina da hankalina me ya sa zan zama mahaukacin? No... No..."

Ya ce, jikinsa ya dinga kyarma da wani irin ɓari da kakkarwa wata asaba yake ji a tsakiyar kansa tana sauka cikin kwakwalwar sarrafa tunaninsa, ya birkice haukan ya motsa masa da gaske.

Da sauri wasu securities suka ƙarasu wajan, su wajan huɗu suka fara ƙoƙarin ƙwace Safiyyerh daga hannun Mutallab, amma suka kasa, ya saki dukkan ƙarfinsa, yadda yake misbehaving, zai nuna da gaske bashi da hankali, aka fara kokawa da shi da ƙyar aka ƙwace Safiyyerh ta faɗi a wajan tana dafe ƙirji da shaƙar wata wahaltacciyar iska, ganin suna kokawa da shi da alama za su iya yi masa duka tunda sun fi ƙarfinsa, kuma su biyar ne ta miƙe da ƙyar ta shiga tsakiya tana girgiza kai.

"Kar ku yi masa komai, ina ruwan ku da shi? Me ya yi muku?"

"Saboda kin yi free, kike tambayar me ya yi mana, da mum bari ya kashe ki fa?"

"Ko kashe ni ya yi mene ruwanku ne? Ina saboda Allah kuka taimaka mini ko?" Safiyyerh ta ce idanunta cike da hawaye. Mutanen suka kalli juna kana suka ce "Mahaukaci ne fa?" Rai ɓace ta ce "Ko a turo yake mene naku? Mijina ne shi ɗin"

"Mijinki? You are too young for marriage yarinya"

"Ko yanzu aka haifan dai, mijina ne, shi ɗin mijina ne" ta juya ta ce "Ko Bestie....." Kifa mata mari ya yi, tare ƙoƙarin shaƙe mata wuya.

"Kin gani ko? A haka kike cewa mijinki ne?" Safiyyerh da ƙyar take buɗe idanu, saboda tsananin azaba ta yi murmushi hawaye na bin fuskarta ta ce "E, mijina ne" ta ce tana nufar Mutallab, ya yi saurin kawar da kansa wani irin ciwo kansa yake masa, kamar ya rabe biyu, ƙirjinsa sai rawa yake masa, fuskarta ɗauke da murmushi ta ce "Manta da su yan saka eyes ne" bai kalle ta ba, bai kulata ba, tana tafe yana binta a baya, yana ƙarewa dukkan wani takunta kallo har suka fita titi, ta tsayar da napep ta ce "Birget zaka kai mu, nawa ne kuɗin?" Ya faɗa mata, ta juya

ta kalli Mutallab, taga ita kawai yake kallo ta kashe masa ido ɗaya ta ce "Kuɗin napep?" Ya ɗaga mata shoulders.

Hannu ta saka cikin aljihunsa ta dudduba babu ko sisi ta ce "Laa dattin aljihu bashi da ko sisi" shiga napep ya yi itama ta shiga, mai napep ya ja su, yana tafe yana kallon su ta madubi, shi kansa ya ji shakkar ganin idanun Mutallab ɗin balle ita ɗiya mace. Har ƙofar gida suka tsaya, ta fito shima haka ta ɗakko kuɗi ta bashi kana ta kalli Mutallab sai zare ido yake yi kuma yana ta binta da kallo a ransa yana jin anya tana da hankali kuwa? What wrong with Fiyya? Is she even okay?. Yaga ta shiga gidansu, ya bi bayanta da sauri ta shiga da sallama. Sa'adah dake zaune da Ammo a tsakar gidan suka amsa, Ammo ta dinga kallon Safiyyerh kana ta kalli Mutallab, bata je komai ba.

"Ina yi Ammo?"

"Safiyyerh ko?" Ammo ta ce, tana bin Safiyyerh data tsuguna kanta a ƙasa ta ce "E, sunana Safiyyerh"

"Allah sarki, ta shi mana" Safiyyerh ta miƙe tsaye Ammo ta shanye mamakin daya gama cika ta, ta ce "In ce dai lafiya?"

"Rako bestie na yi, baya jin daɗi ne" ta ce a hankali, fuskarta faɗaɗe da murmushi tana jin kamar a gida take. "Sannun ki da ƙoƙari Safiyyatul-khairi, sannu da ɗawainiyya kin ji, kema ki tafi gida ki daina biyo namiji kin ji ɗiyar arziƙi". Sa'adah ta dinga kallon Safiyyerh, ganin yarinya kyakkyawa fara tas, idanunta manyan farare ga gashin gira a cunkushe baƙi suɗik so ma sha Allah, ganin jikinta kasan tana hutawa sai dai babu nutsuwa a tattare da ita sam. "Safiyyerh" Ammo ta kira sunanta ta ce "Jeki gida yamma na yi kar aga kin jima" ta girgiza kai ta ce "I will stay with you, zan zauna a nan ni"

"Ikon Allah, dole ai ki tafi"

Safiyyerh ta fashe da kuka sosai, Sa'adah ta dinga kallon ikon Allah. Inna Binta ta fito tana masifar abinci hakan ya baƙanta ran Sa'adah bata ganin idon baƙuwa.

"Idan na je gida daddy duka zai yi, zai buge ni zai mini faɗa, zai hanani fitowa, zai bar ƙasar dani...," ta kasa maganar ta fashe da kuka tana haɗe kanta da cinyoyinta ta dinga rera kuka ta ce "Ammo don Allah ki faɗawa Ummeyhna ta aura mini Mutallab please, don Allah ni bana son zaman gidanmu Please..... Please"

"Turƙashi!"

"Safiyyerh, wakike so ɗin?"

"Mutallab"

"Yana son ki?"

"E, yana so na"

"....Liar, ƙarya ne" ya ce a hankali, ta kalle shi ta ce "Wallahi kana so na, Ammo ko baya so na ba dai ni ina son shi ba?". "Haka ne, to babu damuwa zan zo da kai na gidan naku sai mu yi magana ta fahimta da mahaifiyar taki ko? Amma ki je gida yanzu" a hankali ta ce "Daddy shirin barin ƙasar yake dani" sosai ammo ta yi mamaki, kuma ta ji tausayin Safiyyerh yarinya ƙarama amma zuciyarsa ta buɗe ta samu balagar zuci ta lallashi Safiyyerh ta kalli Mutallab ta ce "Auta raka ta ko?" Ya yi kicin-kicin da fuska, domin kawo lokacin daidai yake jin kansa zai ciwon kai. "Muhammad"

Gaba ya yi, Safiyyerh ta yi wa Ammo sallama ta bi bayansa da sauri ta ruske shi a waje. Ya dube ta sosai cikin ɓacin rai ya ce "Ya zama First and the last time da za ki yi yunƙurin biyo ni gida ok? Kar ma ki cigiyata ko result aka fitar ba zan zo ba, sai an dawo hutu kin gane ai?" Ya yi maganar yana ɗaɗɗage mata girarsa biyun. "But i am going to miss you" ya mata banza idanunta ya cika da hawaye da sunkuyar da kanta ƙasa, tana shasshekar kuka ya matso dai-dai da ita ya ce "Only friends.... Only friends, friends kawai" ta yi murmushi ta ce.

"I appreciate hakan ma"

"Fece to"

"Uhm'uhm" ta ce. Ya juya.

"I love you Mai dawa, ka kawo mini naman jeji ka ji? Kuma ka zo zance if not i will come, idan ka ji ka neme ni ka ji masoyi? I love you" ta sake yin murmushi ta ce "I heard you, ka ce i love you too "

"Allah Ya baki lafiya Fiyya"

A hankali wani mutum dake cikin baƙar mota da ya zo wajan Mutallab ya dinga bin Safiyyerh da kallo, musamman fuskarta ya ɗauki wayarsa ya ɗauki photon fuskarta, cikin sauri kuma ya tayar da motar ya bar wajan, domin wannan abin ya fi batun wajan Mutallab amfani. A good and bad news in the same time.

*

Yana cikin jeji wajejen Kumbotso yana neman kayan LIMƘABIN KALGO, da zai wa Sa'adah magani jikinsa sanye da bunjuma sai hular saƙi, da sauran kayan mafarauta daga bayansa ya ji an ce "Ga ganyen nan a gabanka" ya ɗago kai, tabbas ya gano dattijuwar nan, karan farko da ya zo har suka samu saɓani da Kimiyya, me take yi to? Me ya sa take son shiga rayuwarsa saboda shisshgi? Ya ɗauke kai ta ce "Me ya sa baka son yi wa kan ka aiki domin zama mai kuɗi duk da zaka iya? Baka yadda da aikin naka bane?" Ya yi mata banza ya ɗauki ganyen, da sauran abubuwan da suka kamata zai bar wajan ta ce "Gaba kaɗan bukkata take, ina cike da farincikin sanar da kai cewa a shirye nake da taimaka maka, a duk sanda ka yi niyyar zuwa wajena, ina baraba lale" ya juya yana tafiya cike da buɗawa ya bar wajan. Ta bishi da idanu.

Tiger da yafi ƙauna fiye da sauran ya dinga tajewa gashi sosai, yana jin yadda saurayin Sa'adah ke ta magiya da ban haƙuri cewa da wasa yake ba har zuci ba. Ya miƙe tsaye ya shige shagon Tariq, tiger kuma ya dinga zagaye Sa'adah yana shanshanata. Wandon kayan daya cire ɗazo ya ɗakko yana duba abu, takadda ya ji, da sauri ya ɗakko ya buɗe idanunsa ya sauka akan rubutun dake ciki.

“Ban taɓa tsintar kai na a mai raunin zuciya irin wannan lokacin ba, do you know why? Masoyi may find himself screaming Saboda raɗaɗin dake addabar zuciyarsa akan soyayyar abin son zuciyarsa, ina son ka, abin ƙauna na nesa da idaniya, abin ƙauna kusa without feeling. Ya ilahil alamin,so ne lakin ɓuɗini shu'urin. Duk tarin dangin da mutum, duk yadda ake son shi duk abin da ya mallaka,so na sawa ya ji ya kaɗaita, ana kaɗaici a ƙauna komai tarin dangi,when your love cast aspersions on you violently Tash'uru bi'annaka wahidan a duniya kuma ba ruhi....,” da sauri ya ja numfashi, yana sake zubewa rubutun idanun wani abu na fusgarsa, abin da baya taɓa rabe ɗaya biyu a ciki,ko shauƙin kalaman, ko shauƙin furucin mai kalaman data zuba su bisa tsari masu taushi da ratsa zuciya, idan baya son ƙaryata kansa lallai yana jin wani abu, yana son rubutun, yana son mai rubutun, he just falls in love with the secret love message. A hankali ya sake buɗe idanunsa domin bawai ya kammala karantawa bane, a'a; ya tsahirta daga ainahin bugun luguden da zuciyarsa ke masa tana masa tsalle a ƙirji, ya ji ya fara rayuwa as a man, as a good man, who is ready to find himself in love.

“Ba za ka gane ba! Domin masoyi bai cika sai ya zam majnuni If you have any sensibility, sonka fih nuƙsani Overemotional connection ba zunubi ba saɓo kawai biyayya na kewa son, yana ta rayuwa a zuciya, ina jin motsin numfashinsa a ƙirjina. Ina rayuwa ne kawai amma ba tare da ruhi ba, Yaa Muhammad, kalmar so ya yi kaɗan ƙwarai wajan faɗa maka kawai tuni ne, lallai watarana ka tuna I LOVE YOU, INA SON KA, ANA UHIBBUKKKKAAA”

“Smile... Smile”

Mutallab, he really out of words ya dinga jin kamar yana faɗaɗa fuskarsa, sai ya tsuke tas ya tuna kalar punishment ɗin da zai yi mata Fiyya ta raina shi.

Wayarsa ya ɗakko, kamar zai kira ta sai kuma ya rasa to me zai ce mata? Ya ce ya karanta saƙon ko ya? Ya girgiza kai kawai, ya damƙe takardar zuciyarsa na tsuke masa a ƙirjinsa tana tatarewa tare da fara sabon gini, ginin daya tabbatar na so ne, motsin da ya tabbatar na ƙauna ne, sabuwar halittar data fara rayuwa a ƙirjinsa matsayin abar so, son bana kowa ba, son ɗiyar Professor Abdu, son Fiyya, shauƙin Safiyyerh Abdu.

"But, Jaaanah is no longer alive, Diyna is no more, after them, who is the next person?"

“Safiyyerh”

Shauƙin fuskarsa ya fara rikiɗewa sannu a hankali zuwa yanayin na damuwa, damuwar Safiyyerh, tsoron rasa Safiyyerh, tunani yadda zai ruski gawar Safiyyerh. A hankali ya yi shiru yana jin sanyi na ratsa ruɓin fatar jikinsa har bakwai yana ratsa ƙashin jikinsa.

*

Da sauri ya fito daga cikin ɗakin emergency dake ɓangaren ICU ɗin yana yarfe zufa daga tsakiyar goshinsa a gigice kuma ya nufi Ummi zuciyarsa na rarrabewa da wani irin rauni ya ja ya tsaya a gabanta yana fusgar numfashi.

"Ya aka yi? Ta dawo hayyacinta?"

"Ummi.....,"

"Kar ka wani damu, ko mutuwa ce ai haka zamu haƙura ko? Mu ɗin musulmai ne, zan ɗauka ba zan ji tsoro ba, faɗa mini mene?"

"She is not responding..... The the treatment bata amsa Ummi" Ummi ta zubawa fuskarsa idanu, kamar mai yin studying yanayinsa sai kuma ta ce "Ikon Allah"

Kafin ya yi magana sun ji kyakkyawan takun Paaah wanda ke alamtar dasu gare su yake, hakan yana nuna daga saukarsa airport asibiti ya yo kai tsaye, ya juya a hankali zuwa bayansa suka haɗa idanu da Paaah ɗin kamar ya tsammata haka ne, idanun Paaah ya rikiɗe sosai tare da yin launi na ban tsoro, kyakkyawar shigar dake jikinsa kaɗai zata nuna maka arziƙin da yake da shi, da kuma tarin kadarorin daya

mallaka. Simple jallabiya ce a jikinsa da alama kuma da ita ya shiga jirgin sai takalmi mai kyau sauciki hannunsa goye a bayansa sai farin Bluetooth ɗin dake kunnensa da alama magana ake masa ta ciki amma ya raba hankalinsa gida biyu.

Paaah ya yi wa Ummi kallo ɗaya ita da wanda suke tare, a hankali ya shige su kai tsaye daƙin ya nufa duk da tarin doctors ɗin wajan da yadda ake ƙoƙarin nuna masa komai zai daidaita ba wanda ya kula ya sanya ƙafarsa cikin room ɗin hakan ya yi daidai da buɗewar zuciyarsa, wani jiri ya neme zubar da shi a wajan, hannunsa ya hau rawa kamar jira ake ya shiga kafin komai ya faru ya wakana ya runtse idanunsa a rarrabe da ƙyar ya iya cewa "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, Allahu Akbar....

Na'ima Sulaiman sarauta

Nimcyluv

08164069685

[1/7, 9:36 PM] Sis Fauzy: Chapter 35: Husband and wife

Kacokan ta baru zuciyarta a wajansa, duk da cewa she feels better and comfortable a zuciyarta, sai dai ta wanzu da tunanin shirin da daddy ya yi mata daga shi har Ummeyh, ta dai ji koma mene she is ready to farc it. A hankali ta lumshe idanunta tare da mirginawa a tsakiyar gadon da take ta yi lamo, tana hasaso kanta ta cikin idaniyar zuciyarta a matsayin matarsa, matar Mutallab, halaliyyarsa, sai ta ji gudun zuriyarta na ninka aikinsa a kaso tamanin bisa ɗari. Murmushi ta yi kamar a lokacin take hango masifar dake cikin idanunsa da ƙifaɗi yana nanata.

"Only friends.... Only friends, friends kawai"

"Daga aboki zaka koma saurayi, daga saurayi zaka koma mijin Safiyyerh Abdu".

Ta mirgina kaɗan sai ta ƙanƙame filo tana murmushi ta ce "Allah ka bani Mutallab, Allah ka duba ni"

Sai ta ji zuciyarta na tuna mata da cewa Safiyyerh ki yi addu'a, ki fadawa Ubangiji. Siririn tsaki taja sanda ta tuna abinda ya faru, ya shige, ya zama tarihi ga duka su biyun,amma banda ita, maimakon ta ji sassauci a zuciyarta sai ta ji ta sake ruɓanya abin da take ji dongane da Aafiyyah, ta ji kawai ta yi ladama, da nasani mai girma, fiye da girman yadda take fargabar amsar hukuncin daddy, ta yi regret, regretting na sani Aafiyyah, she regretted knowing anything, she regretted knowing Aafiyyah as her childhood friend, to wanne abota? Duk wani abu da zai mata togashiya ga sadata da Mutallab bata so, she hates it don haka ba wata abota, the friendship is gone ya mutu, mutuwa a zuciyarsa Safiyyerh, ko motsin sa bata ji balle ta sakawa ranta tashin nasa.

Wayarta ta ɗakko tare da shiga message ta nemo number Aafiyyah kai tsaye ta fara typing tare da tura mata saƙon karta kwana, ta riga ta mance yadda aka ɗauki Aafiyyah tsakanin rayuwa da mutuwa. Idan ta tuna abin daya faru ranta ɓaci, it hurts her, a lot hurts. Ta miƙe tsaye tana jin zuciyarta ta rage mata nauyi, wanka ta yi kana ta ɗaura alwala tare da yin sallah ta jima saman ladduma kafin ta miƙe ta nufi gaban dressing mirror ta ɗauki, set ɗin mayukan da aka haɗa mata wanda sai yanzu ta lura order ne, kuma products ɗin Aysha S Bayero ne, ta ɗauko Oil mai sanya fata sheƙi da glowing ta ɗakko ta shafa, tana jin jikinta daɗi, kana ya ɗakko corrector mai fidda tabo ko wani ɓoyayyen abu da baka san da shi ba. Bayan ta gama shiryawa ta ɗauki turare ta fesa, ta ji ƙamshin har tsakiyar kanta, wani sabon shauƙi ya kama ta, murmushi ta yi kawai a haka ta nufi ƙofa tare da sauka downstairs.

"Safiyyerh!"

"Na'am, Ummeyh"

Safiyyerh ta ce jiki a sanyaye ta nufi wajan Ummeyh dake zaune saman kujera, ta nemi waje ta zauna kanta a ƙasa. Ummeyh ta dinga kallon ɗiyarta ta kafin ta ce "Kin ji daɗi ko Safiyyerh? Kin yi farinciki ko?" Ta ce cike da ɗacin rai da ƙonar zuciya.

"Me na yi Ummeyh?"

"Kike tambayata? Da gaske tambayata kike yi? Kuma amsa kike buƙata ko? Kina son ji?"

"Ki yi haƙuri don Allah Ummeyh, ku yafe mini please "

Ummeyh ta juyo, da ƙyar ta ce "Sorry for what? There is nothing to forgive, kin nuna dai kin isa ne, kin kuma yi farinciki kin saka jinin mahafinki hawa, Safiyyerh wannan shine tarbiyyar? Wannan shine sakayyar da za ki yi mana a matsayinmu na iyayenki? Tun kina zanin goyo muke ɗawainiyya, har girma har kika isa zuwa makarantar, makarantar da yanzu muke dana sanin saka ki gwara ki zo a jahila kuma ki koma wajan Ubangiji haka, kin mini kuka, kin mini fitsari, kin mini abubuwa da yawa, ba ki taɓa cewa wayyo Allah bamu yunƙura mun ji matsalarki ba. Shi ne yanzu za ki yi ƙoƙarin kwasar ƙasa ki baɗa mana a idanu? Za ki wofitar da tarbiyar da muka yi miki? Ki ka rusa kuma Safiyyerh? Why Safiyyerh why me ya sa? Shin bamu cancanci ki yi mana wannan alfarmar ma, bamu dace da alfarmarki da biyayyarki ba?"

Kuka Safiyyerh ta fara ta ce "Ummeyh ku yi mini afuwa, don ku yi mini afuwa ku yafe mini" Ummeyh ta ce "Ki manta da batun shi, batun auren, ki yi karatu we can leave the country idan kina so ma, kin ji ko?"

"Ummeyh, Mamansa ta ce mini za ta zo ku yi magana " ta ce cike da ƙoƙarin tsage gaskiyar dake ƙirjinta. Ummeyh ta ce "Maman wa? Maganar me?"

"Mutallab, na je gidansu....."

Saukar duka ta ji a jikinta, ta ko'ina ta fara ihu da ƙoƙarin neman ɗaukin Ummeyh, amma Ummeyh bata motsa ba, duk da kukan na Safiyyerh na taɓa ta. "Daddy ka yi mini komai amma don Allah ka aura mini bestie, ka yi mini aure da Mutallab, na rayuwa da shi kamar yadda kuke rayuwa da Ummeyh..." Ta saka ƙafa ya yi ball da ita, cikin sauri Uncle Musbah ya zo ya fisge bulalar hannun daddy, yana janye Safiyyerh da jikinta ya yi jina-jina. Uncle Musbah ya ce "Mene ya yi zafi haka? Kashe ta za ka yi ne?"

"Musbah, ka rabu sani ka bari na kashe Safiyyerh na huta, Safiyyerh ta ɗora mini hawan jini, ina saurayi ban yi hawan jini ba sai yanzu? Ka duba a makarantarsu aka kira ne gabaɗaya exam ɗinta zero, f f kawai nake gani, still dai Ya sayyadi ya kira ni Safiyyerh bata gane yanzu ko karatun Alkur'ani me take nema me take so? Mene kuma ban yi mata ba"

"Aure nake so daddy, aure ne ba ka yi mini ba wallahi bana gane karatun ma sam, uncle ka taimaka mini" Safiyyerh ta ce tana daga bayan uncle Musbah.

"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un"

"Uhm, professor kenan, auren nan fa shi za a yi mata in sha, da Mutallab ɗin"

"Wallahi wallahi dana aurar da Safiyyerh at her young age kuma aurar ma ga Ɗan'malam gwara naga gawarta a gabana na san cewa mutuwa ta yi kawai"

Juyawa ya yi zuwa part ɗinsa yana neman layin Aliyu. Uncle Musbah ya ja hannun Safiyyerh zuwa upstarts, Ummeyh kuma kamar statue haka ta zama saboda shocked.

*

Paaahh ya sandare ganin yadda Aafiyyah bata ko motsi, ba zai ce ta mutu ba, tunda bai ji tasa zuciyar ta tsaya ba, yana mai jin tsoron abin da kan iya zuwa ya dawo don gane da abin da yake damun Aafiyyahr kai tsaye.

Bai kai ga shiga cikin ɗakin ba, wani likita ya dakatar da Paaah ta hanyar cewa "Ranka ya daɗe ka yi haƙuri ka jinkirta mu ƙarasa aikin da muke yi Please" Paaah ya dinga kallon likitan kana zame idanunsa ya kalli Aafiyyah dake kwance a saman gadon asibitin ta yi flat lokaci ɗaya ta yi wata muguwar rama kamar ana zuƙe ruwan jikinta, ta zama kamar wata kuɗin guzuri. Ya ja numfashi ya sauke yana sake kallon Aafiyyah da ƙyar ya iya cewa "Ya jikin nata? Is she response?" . Dr ya ce "Za ta yi in sha Allah, mu yi addu'a" yana faɗin hakan ya shige ciki, Paaah ya yi sak, yana jin nutsuwarsa na yin hijira daga zuciya da gangar jikinsa, a shirye yake da

rasa ko mene muddin Aafiyyah zata samu lafiya. Juyawa ya yi yana gyara Bluetooth ɗin kunnen nasa ya ce

"Ko anjima? Maybe zuwa gobe, yanzu na sauka ƙasar nima, mu yi addu'a shine don Allah" shine abin da ya ce kana ya nufi inda su Ummi suke, ya duba agogo Ummi ta ce "Ka samu ganin nata? Ya take? Tana magana? Ƙirjinta na ɗagawa zan dai ta samu lafiya?"

Paaahh ya ce "In sha Allah"

Shiru duka sukai kafin Paaah ya ce "Ina son ganin mahaifin ita ƙawar daughter, dalilinsa na dukan gudan jinina zai bani"

"Sun ce kuskure ne, yaɗar shi ya je duka ya ɗauka Aafiyyah ita ce"

"Ko?" Paaahh ya ce, yana duban mai maganar, MJ ya yi saurin sauke kansa ƙasa sai kuma ya duba wayar Aafiyyah dake hannunsa, bai san mene ya ƙunshi saƙon ba amma saƙon karta kwana ne kai tsaye ya sauka a cikin DM ɗinta ɗauke da number mai rubuce da sunan Safiyyerh. MJ ya juya cikin sasarafa ya bar wajan bayan ya yi nisa ya buɗe saƙon tare da karantawa.

“Ko a wasa ban ɗauka za ki aikata abin da kika aikata ba, haka kuma ban ji wani mamaki ba, na san cewa kin faɗi da gangan ne bisa son zuciya da kifar da tunanina da kike raina nawa Aafiyyah. Ina tuna miki wanda ya rigaka kwana ya rigaka tashi. Na ji bana buƙatar sake ganin fuskarki a cikin idanuna, Aafiyyah kar ki yi kuskuren nuna mini fuskarki saboda i don't know what i am going to do, kin san wace ni, duk haƙurin da nake da shi idan na yi niyyar abu bana fasawa, ki manta kin taɓa sanin wata Safiyyerh a cikin rayuwarki, bana buƙatar ko a zuwa gaba ki yi mentioning sunana a matsayin wacce kika sani, ina miki fatan alheri, stay away from me”.

MJ ya ji mamakin saƙon na Safiyyerh, sarai ya santa ai, abotar da suke da Aafiyyah tun ta primary school ce, duk da cewa Aafiyyah ta samu ƙalubale amma bata da magana sai ta Safiyyerh, dalilin ƙaunar da Aafiyyah ta kewa Safiyyerh ya saka Paaah zama a Nigeria, ya tattara nutsuwarsa a naija. Ya ja numfashi ya dinga kallon

saƙon baya son Aafiyyah ta gani, amma ya zama dole ta sani ya dinga mamaki sai dai ya jingina hakan da ƙuruciya kuma daman zaman duniya a saɓa ne yau a kuma shirya gobe wannan tabbataccen abu ne dake zuƙatan duk wanda suke abokantaka.

Dr ne ya fito, har lokacin Paaah na tsaye hannunsa goye a bayansa yana yi yana sauke ɓoyayyiyar ajiyar zuciya, Ummi ma tunani ne fal ranta da tsoron abin da kan iya biyo bayan ciwon na Aafiyyah.

"Dr ya ake ciki"

Ya yi murmushin yana zare glasses ɗin idanunsa ya ce "Allahamdulilah, numfashinta ya dawo mun cire suka oxgeyn ɗin zuwa anjima zamu mayar da ita ɗakin hutawa daman matsalar ɗaukewar numfashi ne"

"Bayan shi fa?" Paaah ya buƙata a ƙagauce, domin jikinsa da zuciyarsa basu gama amsar batun Dr ɗin ba. A hankali dr ya ce "Ranka ya daɗe mu yi magana office please" ya yi jim sai kuma ya miƙa hannunsa ya ce "After you" Dr ya yi gaba Paaah ya bi bayansa zuwa cikin office ɗin, Mj ya yi shiru yana ta tunanin masifar ƙaddarar dake shirin kunno kai babu gaira ba dalili.

"Alhaji wannan shine gwaje-gwajen da muka yi wa yarinyarka. Maganar gaskiya bai dace ace kamar Aafiyyah a ƙarancin shekarunta ba ta kamo da hawan jini ba, yana da kyau a tsaya a duba idan wani matsalar ne a fara jin damuwarta sai a magance mata, na san duk abin da yake damunka ba zai fi ƙarfinka ba, so ka fini sanin abin da take buƙata meet your daughter". Paaah ya yi shiru, shirun zullumi da tunanin abin da ya saka Aafiyyah ta samu hawan jini. A hankali ya ce "So ba Limoniyyar ce ta tasar mata ba?" Dr ɗin ya girgiza kai ya ce "Ai kuna kula da ɓangaren limoniyyar, Aafiyyah bata bacci, Aafiyyah ba nutsuwar zuciya a tattare da ita, Aafiyyah bata cin cikakken abinci, ba komai a tare da ita sai damuwa, here is the results" Paaah ya amsa da ƙyar, Dr ya dinga bawa Paaah tabbacin zata warke idan an shawo kan matsalar.

A hankali ya tura ƙofar room ɗin da aka sauya mata, hannunsa ɗaya ya saka ya cire Bluetooth ɗin kunnensa sai ya jinkirta ya ce "Tunda dai haka ne ka yi zamanka kawai, nima zan yi tafiya idan ta samu sauƙi ina tunanin tunda hutun makaranta sukai, zan tafi da ita, i will go with her sai ta sami peace of mind" ya ce yana cire

Bluetooth ɗin. Kujera ya ja ya zauna ya ce "Sweetie" Aafiyyah ta juyo tana buɗe idanunta a hankali ta kalli Paaah ta yi murmushi da ƙyar tana miƙa masa hannunta, riƙo hannun ya yi cikin nasa gam, ta lumshe idanunta tana jin yadda Paaah ya riƙe ta da kyau irin he is already missing her.

"Dad....," Aafiyyah said, a hankali har yanzu fuskarta ɗauke da murmushi, shi dai kallonta yake yi yana sake damƙe hannunta da ya ji zafi sosai, amma ita sai murmushin nan nata take irin you will never understand my situation daddy. "I miss you so much Dad, yaushe ka dawo?"

"You will never change Safiyyerh, you are smart, smarter as always"

"Daddy...."

"Zan tafi dake, kafin ku yi resuming school ok" ta yi shiru ya ce "Ya jikin naki?"

"Alhamd, dad ko ɗan rungume ni ba ka yi ba, na yi kewarka ba" ya ɗan harareta sai kuma ya miƙe ya ƙarasa wajan gadon, yunƙurin miƙawa ta yi sai kuma ta runtse idanunta saboda ƙirjinta da yake doka mata, kanta ya sara da wani irin ƙarfin, yanayin daba kowa zai jure ba amma fuskarta ɗauke da murmushin tana lumshe idanunta ta buɗewa, ganin ta kasa tashi sai ƙifta idanu take ya saka ya janyo ƙafafuwanta zuwa dab dashi, da sauri Aafiyyah ta shige jikin Paaah tana sauke ajjiyar zuciya, a hankali kuma hawaye ya dinga taruwa a cikin idanunta.

Kwananta biyu aka sallame ta zuwa gida, Paaah ya fara shirye-shiryen nemawa Aafiyyah visa, ita dai bata cewa komai saboda bata fiye magana ba, ta dinga avoiding kanta ga mutane.

"Assalamu Alaiki"

Mj ya ce yana shigowa ɗakin, tana daga kwancan ta buɗe idanunta hannunsa ta gani ɗauke da wayarta har ya ƙarasu ya zauna ya ce "Favourite ya ba ki fito wajan

ba" ta yatsuna fuska tare da ɗauke kanta zuwa gefe ya yi murmushi ya ce "I'm sorry I was so overjoyed to ask, ya jikin naki?". A hankali ta ce

“Absolutely fine physically, but not mentally and emotionally”

Ya zuba mata idanu sai kuma ya ce "Ki yi haƙuri don Allah Safiyyerh, kar ki ɗauke ni matsayin mai laifi, ni bani da iko ban san kuma yadda zan yi ba" ta ɗan ɗaga masa kafaɗa tana share hawayen idanunta. "Mene ya haɗa ku da Safiyyerh ƙawarki?"

Aafiyyah ta ce "Kamarya?"

"Kamar yadda kika ji"

Ya zaro wayar ya shiga message ɗin ya nuna mata, ta yi mitsi-mitsi da idon murmushi kawai take yi bata ce komai ba, sai ta juya bayanta tana sake share hawayen idanunta.

Paaahh ya ɗauke Aafiyyah ya bar ƙasar, gabaɗaya. Safiyyerh ƙuncinta ya ƙaru, an ƙwace wayar hannunta an hanata fita ko'ina bata da wani sukuni sai kuka, ta rasa meke mata daɗi ta ji duniyar ta mata girma sosai, ta ji kamar ita kaɗai ce a cikinta wani tashin hankali ne ya rikitowa rayuwarta. Sauƙinta ɗaya an ƙi bawa Prof damar barin ƙasar har yanzu. Kullum cikin lissafa komawa makaranta take yi, ba don karatu ba, ba kuma don Aafiyyah ba, saboda shi, shi kawai just for him. Only for MUTALLAB. Sai ta ji kuma ta damu, da ace Aafiyyah na nan tabbas zata nema mata mafita, ta ji dama bata turawa Aafiyyah saƙon ba.

A hakan lokaci ya dinga mirginawa, rana na juyewa zuwa kwanaki, kwanaki na juyewa zuwa satuttuka har suka cinye adadin kwanakin da aka basu, za su koma makaranta, komawar kuma da kusan shine ya zama silar faruwar ƙaddarar, komawar da ya yi kama da ƙaddara ce ke kiran su tare da jirayar zuwan nasu, komawar data baƙanta zuƙanta kowa, komawar data raya zuƙata biyun, komawar data zama silar farinciki da baƙin ciki ga zuƙata da yawa, komawar data saka suka fahimci wata duniya bayan wacce suke ciki, komawar data tunasar da Prof abubuwa

da yawa, wacce ta raba abu mai muhimmanci ga Ɓangaren da idan babu ginin nasa ɓangaren kan iya rushewa. When a destiny call.

Da sauri take sakkowa daga steps ɗin benen, hannunta riƙe da school bag, sai wayar data samu aka bata da ƙyar, cikin sabbin uniform kana ganinta kasan she is ready for Jss3. Prof baya nan, Dr kuma dutyn kwana ta yi daga ita sai Wahee hakan ya sake tabbatar mata Allah ne ya ɗora ta a sa'a Wahee bata isa ta hanata fita ba.

Tana ƙoƙarin fita Wahee ta ce "kurkuku ta sake ki kenan, ai na so an saka ki a mari kuma kika fita sai na faɗawa Daddy"

"Wahee, kin jima ba ki faɗa ba"

Miƙewa Wahee ta yi daga kan dining ta ce "Oh, haka ma kike cewa ko? Haka za ki ce ya miki kyau, sai ki fita mu gani, kuma in sha Allah sai kin fara bin maza tunda hakan kike so ɣar wahala kawai banza mai ƙaunar Almajiri"

Murmushi Safiyyerh ta yi, maganar ta yi mata zafi sosai sai ta shanye ta ce "Idan har ba zina aka yi aka haifi Safiyyerh ba, to ƙaddarar Safiyyerh bata iskanci bace, wannan dalilin ya saka nake so a yi mini aure. Ke kuma da kike zaune Form dubai to America daga gidan ubanki zuwa nan ai kin fini wahala, Wahee ki fita a lalurata ki fita ba ruwanki" Wahee ta ce "Kan uba kike zagin ubana? Ni kikewa gorin gidan uba?" Ta yi kan Safiyyerh ta ce "A'a kar ki fara, ba wani hankali garan ba a yanzu, ba Safiyyerh baya bace wannan Safiyyerh a shirye take, kafin na yi miki rauni leave"

Ta matsa, ya shige kitchen ta ɗauki lunchbox nata ta nufi waje ta bar Wahee a wajan. Wizzy na ganinta ya miƙe tsaye ya ce "Barka da fitowa"

"Good morning Wizzy"

"Morning how are you?"

"Allahamdulilah"

Motar ta shiga, suka fita Safiyyerh ta ji kamar ta fita daga cikin kurkuku ta dinga jin farinciki a zuriyarta a hanya ta dinga kiran number Mutallab tunda ta haddace sosai, tana ta ringing mai ɗauka ba. Motar Safiyyerh ta riga tasu Aafiyyah tsayawa, Wizzy ya buɗewa Safiyyerh mota ta sakko ya miƙa mata jaka da lunchbox ɗin, kai tsaye motarsu Aafiyyah da taga an buɗe murfin ƙofar ta ƙarasa da mamaki ta kalli Aafiyyah dake ƙwance a cinyar Mj shi kuma yana riƙe da gorar ruwa da magani data lura sai taga kamar ma kanuna ce a hannunta.

"Yaya"

Mj ya ɗago ya ce "Safiyyerh ya kike?" Ta yi murmushi ta ce

"Alhamd Yaya, ya ayyuka?"

"Good, Aliyu bai dawo ba?"

Ta ɗan ɓata rai sai bata ce komai ba. Mj ya ɗago Aafiyyah, ƙirjin Safiyyerh ya buga ganin wani irin ramewa da Aafiyyah ta yi, idanunta sun sake girma ƙwarai sai cute lips ɗinta da sukai jajur sai kuma ɗan haki take. "Favourite mu koma gida ko? Paaah shi ya biye miki wallahi"

"Safiyyerh help her kin ji, bata jin daɗi jiyan nan suka shigo Nigeria ita da Paaah so Please take care of her zan dawo na ɗauke ta"

"In sha Allah Yaya, kenan ba'a nan ta yi holiday ɗin ba?"

"E, ku je ga can za'a fara assembly" ya gyarawa Aafiyyah baby hijab ɗin jikinta kana ta sauka suna haɗa ido da Mj ta ce "Kuma sai ka yi ta tallata dani Yaya? Kowa sai ya san bana ƙasar kuma bani da lafiya, haba Yaya"

"Ohhho miki dai" ya faɗa yana ɗaga mata shoulders.

"Aafiyyah ya kike?"

Aafiyyah ta juya ta kalli Safiyyerh, sai ta ji tsoron kallon kamar kallo ne na zargi ta ce "Good"

"Ya jikin"

"He just kidding you, lafiya lou nake fa" ta ce seriously. Daidai nan suka ƙarasa wajan assembly ɗin, Kimiyya ya dinga murmushi ganin Aafiyyah suna haɗa ido ta ɗaga masa gira alamar ya?.

A hankali ta shigo cikin class ɗin hannunta riƙe da lunchbox da textbook sai school bag data goya, hijab ɗinta daidai da ƙirjinta ita ce ta fara shigowa da mamaki take kallonsa zuciyarta na bugawa ta je ga zauna inda yake ta zuba masa idanu sai kuma ta ce "Ka yi holiday assignment?"

Ya buɗe manyan idanunsa bai ce komai ba ta sake yin ƙasa da murya ta ce "Na san bama ka yi ba ka daina haɗe mini fuska, ka naso a yi ta faɗa da kai da teachers" nan ma bai kula ta ba a hankali ta ji sautin da cikinsa yake yi sai ta jawo lunchbox ɗinta ta buɗe tare da tura masa gabansa ta ce "Your breakfast, ka ci kafin a shigo na san baka karya ba" sai a lokacin ya buɗe idanu ya juya gabaɗaya yana kallonta sosai ya yi ƙasa da murya kamar zai yi faɗa sai kuma a hankali ya ce

"Kuma ga mayunwaci ko?" Ta yi murmushi ta ce "Da ƙyar na jure ban biyoka gida ba, na yi kewar ka sosai bestie" ya yi mata shiru sai kuma ya haɗe fuska da kyau yana janyo abincin yaga dankali ne aka soya da ƙwai ya yi ɗan tsaki ya ajjiye spoon ɗin ya damƙa ya kai bakinsa ta yi saurin kama hannunsa ta ce

"Kai baka iya komai bane? Sai a yi maka dariya cin abinci da hannu" ya ware idanu sai kuma ya murtuke fuska ya ture hannunta a hankali duk da muryarsa a kumbure take ya ce "Ki daina kusanta kan ki dani, ni fa ba ɗan iska bane"

"Laaa Allah Ya baka haƙuri kai duk abin soyayya baka iya ba" a taƙaice ya ce "Ke kika santa" ta ja baya tana ɗaga hannu ta ce "Lalala to shikenan ni dai ƙaddararka ce, na faɗa a gida a yi mini aure, ka san me na ce?" Ya girgiza mata kai kawai yana sake damƙo dankalin yana dannawa cikin bakinsa saboda yunwa ko gani baya yi sosai ta buɗe gorar ruwa ta miƙa masa a hankali ta ce

"Na ce su yi mini aure wallahi bana son karatun nan, na ji aure nake so kuma na faɗa musu kai nake so, amma wai ban isa ba karatu ya zama dole kuma shekaruna sun yi kaɗan amma ai na girma shekararmu 15 years fa, ko kai baka isa aure bane?" Ya yi mata shiru sai ta fashe da kuka sosai ta ce "I love you so much Bestie, don Allah ka aure ni zan zauna dakai a duk yadda kake ka taimakawa rayuwata" ya zame hannunsa tas ta miƙa masa tissue ya goge ya ja baya yana lumshe idanunsa har yanzu students basu fara shigowa ba, ta ɗan yi gaba kamar za ta shige masa cikin tsawa ya ce

 "Zan kwaɗe ki kuwa"

"But what if i told you i love bestie? You mean the world to me, wallahi aure nake so ba karatu ba" ta faɗa tana shasshekar kuka sai a lokacin ya kalleta fuska babu walwala ya dubi yadda take kukan sosai ya ce

"Ke, babanki ne ya mutu? Ko uwarki ce?" Ta girgiza masa kai ya sake haɗe fuska yana rarraba idanu a cikin ajin kamar mai neman wani abu can ya ce "To kece za ki mutu kenan?" Ta girgiza kai sai kuma ta ce "A'a"

"Kukan fa?"

"Na soyayyarka ne bestie taɓa ƙirjina ka ji wallahi ni ce ƙaddararka ba zaka gane hakan a yanzu ba, da ina da ikon cire abin da nake ji a ƙirjina da na yi hakan ina jin dama na mutu na huta kuma idan ban aure ka ba zuciyata zata iya bugawa"

"To gwara ta buga na huta da na ci, shekaruna 15 za ki lalata ni da batun aure, ke tashi ki ware daga nan ɗauki kwanukanki kar ki ƙara kawo mini abinci" ta miƙe jiki a sanyaye zata bar wajan ya nuna mata lunchbox ɗin daya cinye komai

"Ko daɗi bai yi ba abincin"

Sai a lokacin ta kyalkyale da dariya kamar ba ita ta yi kukan ba, dimples ɗinta na lomawa ta ajjiye masa 500 ta yi waje tana cewa "You're my darling jarumina, i love you Mai dawa da jeji" ta faɗa tana sake yin dariya tare da yin waje.....

Ya bi bayanta da kallo cike da tausayawa, idan ya tuna Jaanah ji yake ba zai yafewa kansa ba, idan ya tuna Jaanah ji yake yi ya tsani kansa, haka idan ya tuna Diyna sai ya ji duniya ta masa faɗi, ba zai ƙara sakacin barin wani rai ya salwata ba a dalilinsa, kula mace ba dole bane, aure ba wajibi bane, soyayya ba tilashin ɗan gidan Malam Abdullahi ba. But...

"But what?" Zuciyarsa ta tambaye shi kai tsaye, ya cije lips ɗinsa "But what about the secret love message? Idan zuciyarsa zai wa adalci ya san yana son mai message ɗin nan, hakan ya tabbatar da yana son Safiyyerh.

Bayan fitowa break, Aafiyyah na zaune ita da Kimiyya a cafeteria meat pie ne a hannunta da Kimiyya ya kawo mata da ƙyar ta ɗauka amma ta kasa ci sai ta ajjiye "crush wai meke damunki"

"Like?"

"Duk kin rame, kin zame wata kala kin zama so silence haka"

"Shine na ce Kamarya?"

"To Allah Ya baki haƙuri"

"Dame?" Ta ce tana taɓa wayarta. Safiyyerh ta shigo ta nemi waje ta zauna a hankali ta ce "Aafiyyah i need a favour kin ji" Aafiyyah ta dinga danna waya, Safiyyerh ta ce "Ki yi haƙuri da message ɗin dana tura miki, a lokacin ban san meke damuna ba, i don't know what comes over me, ki yi haƙuri don Allah Ki taimaka mini kamar koyaushe ki yi Mutallab magana, ki fahimtar da shi halin da zuciyata take ciki" da sauri Kimiyya ya kalli Safiyyerh, saboda ya san komai shi kallon mamaki yake mata data iya rufe idanunta.

"Soyayya ƙaddara ce Aafiyyah, rayuwa wa'adi ce, mutuwa wajibi ce, hisabi gaskiya ne, soyayya halitta ce a ƙirji a zuciyar kowanne mai raye, don Allah don ko tausaya mini wallahi na kai stage ɗin da zan iya rasa raina" ta yi shiru tana fashewa da wani irin raunataccen kuka ƙirjinta na buɗewa. "Ba lallai ki gane ba, saboda ba ki taɓa faɗawa cikin jarrabawar so ba"

"Ai kam" Aafiyyah said.

"Ya kike so ta yi miki" cewar Kimiyya.

"Ta yi magana da Mutallab"

"Amma Safiyyerh....."

"Uhmm ehem, shikenan zan masa magana Safiyyerh, kin dai san ba wani magana muke ba amma zan yi saboda ke. Maganar wasiƙa ƙila kin yi missing number ɗaya daga cikin number Aafiyyah saƙon bai zo ba" ta saka shade glasses ɗin ta miƙe tare da ficewa daga cikin cafeteria ɗin.

Yana zaune a cikin aji har lokacin yana buga game a wayarsa, ta ƙarasa cikin ajin tare da jan kujera ta zauna a gabansa. Ƙamshin turaren da bai taɓa ji ba ya ji, yana ratsa hancinsa da saukar masa a ƙirji, ya cigaba da game bai ɗago ba, amma sai ya zubawa yatsun ƙafarta idanu saboda flat takalmi ta saka.

Aafiyyah ta kasa magana sai a hankali ta ɗora kanta a saman table ɗin da yake zaune, sun jima a haka, zaman ya gundire shi ya miƙe zai fita ya ji siriryar muryata, sautin daya fito a raunace ta ce "Love Safiyyerh"

"Ka so safiyyerh"

A hankali ya dawo ya zauna. Ya fara kallonta ganin ta gyara zama, ya dubi kanunar hannunta sai ya ja tsaki ya saka hannu ya zare glasses ɗin idanunta, sai ya ga ashe shi take kallo ta yi saurin haɗe fuska tamau.

"Munafuka ce ke? Za ki magana kamar bani kike kallo ba"

"Hmmm"

"Hmmm ɗin"

"Ka auri Safiyyerh"

Ya dinga kallonta ganin yadda take jan numfashi "Don Allah"

Miƙewa ta yi zata fita ya ce "Jiiiii" sai ta tsaya ya ƙarasu inda take "Are u sick?" Tsaki ta ja masa kawai ta fice da sauri. Baya ta koma can ta goge hawayen idanunta da yaƙi tsaya mata.

*

Duka suna a cikin ajin a washegarin ranar da aka koma makaranta. Mutallab da suka bashi nickname na MOH, sai Kimiyya da Nahyan, sai Kinal da sauran students. Kamar an cillo captain haka ya shigo class ɗin ya ce "Safiyyerh ji mana"

"Ya aka yi Captain?"

"Magana za mu yi"

Ciki ciki Moh ya ce "Yi a nan"

A ƙufule shima ya ce "Baka isa ba, kuma ka yi kaɗan wallahi, baka da uban komai ka zauna har kake bata umarni kamar wani mijinta"

Moh ya ɗan shagiɗar da bakinta yana murza goron hannunsa ya ce "Zan aure ta ne" cike da baƙin ciki Captain ya ce "Idan zaka iya aure ta yanzu mana" ya faɗa yana huci kamar kumurucin maciji.

"Kaga ni sai na zama waliyin ango, Nahyan ya zama waliyin amarya Safiyyerh, Kinal da kai Captain da sauran students su zama shaidu" Nahyan ya dinga dariya ya ce "Bari na fita na siyo chocolates matsayin goran ɗaurin aure" ya miƙe ya fice. Kimiyya ya ce "A'a abu ya yi kyau, kamar na san da wannan sabga na watsu kuɗi cikin aljihuna ashe rabon na biyawa yarona kuɗin sadaki ne" Kinal ma dariya ta yi ta ce "Kaga ni kuma sai na zama photographer, na ajjiye shaidar ɗaurin aure mai albarka" suka dinga shaƙiyanci. Safiyyerh tana ta murmushi abin a haka Nahyan ya dawo, Kimiyya ya ce "To bisimillah, ni Kimiyya ina nemawa ɗana Muhammad Mutallab Abdullahi neman ƴar wajanka Safiyyerh Abdu" Nahyan ya ce "To na gode, nima Nahyan Nasim Wasim, ina mai farin cikin faɗa maka na bawa ɗanka Muhammad Mutallab Abdullahi auren Safiyyerh Abdu"

Kimiyya ya ce "Thank you, ga sadaki har naira dubu goma, sai mu yi salati" kamar wasa suka fara salati "Allahamdulilah aure ya ɗauro" Ya fara raba chocolates Nahyan, Kinal ta dinga yin recoding tana dariya ya ce "Safiyyerh ga sadakinki" ya miƙa mata kuɗin ta amsa.

A hankali ya juyo ya kalli Safiyyerh ganin ta amshi kuɗin sai taga ya kashe mata idanu ɗaya ta masa gwalo ta ce "Mijina"

"Anyi abu kamar wasa, haka watarana zai muje ɗaurin auren MUTALLAB da SAFIYYERH bestien beastie "

Daga bakin ƙofar shigowa class ɗin aka ce "And who told you ana wasa da aure? Yanzu ma ai kun yi musu aure, kuma auren gaskiya they're now husband and wife.

Sai kuma Saturday.

MUTALLAB

Paid book ne

500

Yi magana via WhatsApp only 08164069385 to subscribe urs

Na'ima Sulaiman Sarauta

NIMCYLUV

[1/7, 9:36 PM] Sis Fauzy: Chapter 36: The first kiss

Ɗaya daga cikin ɗaliban ya yi furucin yana shigowa cikin ajin, Nahyan ya ce "Wanne irin aure ya ɗauro? Kamar a garin gaɓa-gaɓa?"

"Yes, auren safiyyerh da Mutallab ya zama halittacen aure, on my understanding". Ya ce yana zama tare da juyawa ya kalli Safiyyerh ya ce "Kuka ya ƙare ko? Lallai Safiyyerh soyayya ta miki mugun kamu, to, mu dai mu ne masu shirya events idan

al'amarin ya kankama". Duk suka yi, banda Kimiyya da ya yi shiru yana tunani can kuma ya ce "How comes auren zai zama halittace?"

"Kai bafa wani abu ka basar kawai, is just a suggestion"

"To haka ake suggestion ɗin?"

Nahyan ya ce "Amma ku tsaya, na yi missing wani abu bayan fitata siyan chocolates. What did i missed?". Kimiyya ya ce "zazzafan kisses ka yi missing don ka ji" jikin Nahyan na rawa ya ce "Haba? Don girman kar ka yi haka, da gaske ango da amarya sumbata sukai wa juna?"

Kimiyya ya jinjina kai ya ce "E, halal sumbata mai zafi"

Mutallab dai bai ce komai ba, jinsu duka yake yi, ya san dai ba wani aure domin ba haka ya yi lissafin yadda ya kamata aure ya kasance, kuma ya kasance ba. Ya yi shiru, yana ƙanƙance idanunsa akan safiyyerh da take kashe masa ido tare da masa murmushi, murmushin dake nuna masa cewa “Ka gani ba? Ba na ce sai na zama matarka ba? Gashi na zama, Safiyyerh ta zama matar Mai dawa". Shi kuma kallon tsaf yake mata, yana son ya ji zuciyarsa ta gamsu da Safiyyerh kamar yadda ta gamsu da wasiƙun da take tura masa kodayaushe.

Nahyan ya yi gyaran murya da gyara zama ya ce "Ehmn, amma kun yi hauka fa, ta ya kuka bari suka sumbaci juna auren wasa ne fa? Haramun sukai"

"Ba wani auren wasa, me ake buƙata da aure? Shaidu, waliyai, sadaki, amincewar ma'auratan ko na ce masoyan shikenan fa" Kinal ta ce, tana watsa hannayenta. Ta ƙara da cewa "Kuma ai kai Nahyan uncle din Fiyya ne, kana da ikon zama waliyin Safiyyerh ko a ina ne, domin mahafinka ai ƙanin mahaifinta ne ko?" Nahyan ya ce "E, haka ne kuma, amma ai sai da amincewarta idan ta amince na zama waliyinta"

"Ta amince ai" cewar Kimiyya.

"I said, what did I missed?"

*

“What did I missed?”

Nahyan na murmushi ya fita siyan chocolates ɗin matsayin goran ɗaurin auren Safiyyerh da Mutallab kamar yadda suke planing ɗin yi, auren wasa ne, amma basu ɗauka zai zama silar shigar zuƙatan wani irin aure ba, ba tare da duk sun san sharuɗan auren ba, ba tare da sun san cewa ba'a yin auren wasan ba. Nahyan ya ji zai yi komai ko dan ya baƙanta ran Captain, da kuma wannan tunanin ya fice daga ajin nasu na Jss 3 cikin sa'a kuma duk suka zauna a A ɗin gabaɗayan su.

Bayan fitar Nahyan, Kimiyya ya kalli Safiyyerh ya ce "Bestien beastie kar mu shiga haƙƙin ki, kin amince Nahyan ya zama waliyin aurenki? Ya karɓi aurenki, kuma kin amince da dubu goma matsayin sadakin aurenki da Mutallab" ya yi tambayar in a serious way, cike da zaƙwaɗin jin amsar da zata mayar masa, deep down na zuciyarsa yana addu'ar Allah ya sa watarana su halicci auren nasu a zahirance domin cikar burin Safiyyerh. Safiyyerh ta kalli Mutallab da yake kallon ta, har mamakin kallon da yake mata take yi kamar mai zarginta ko tuhumarta, idanunta ya yi rau-rau hawaye suka ciki idanunta ta ce

"Ni a raina nake jin auren gaske za ku yi mana, a raina nake jin yau zan amsa sunan da nake mafarki, a raina nake jin nima zan zama wata wacce zata iya cimma muradinta kafin wa'adin da Ubangiji ya ƙare mini a duniya. Wallahi Kimiyya duk yadda zan kwatatan maka halin da zuciyata ke ciki ba lallai ka fahimta ba, ba kuma lallai ka gane ba, auren Mutallab da rayuwa dashi matsayin miji shine fatana. Me ya sa kake tunani a wannan halin da nake ciki zanƙi amincewa bayan na san daddy ba zai taɓa cika mini muradina ba? Ko da kuwa zan mutu ne na bar duniyar"

Ta sunkuyar da kai, tare da kallon Mutallab sai ta juya ta kalli Kimiyya ta ce "Duk na amince, ni kam na amince da gaske ta amince Nahyan ya zama waliyinta" ta ce in her lower voice.

"Allahamdulilah, daman amincewar muke buƙata ai Nahyan ya cika ta amshi walicci domin a girme ma ya girme mana, bana ya dawo daga kawo goran auren kai har musulmar walima zamu haɗa ko dan su yan hana ruwa gudu. Kuma auren nan til-janna in sha Allah"

"Allahumma amin, Ubangiji ya amince Kimiyya, shi ya sa nake yin ka kana da fahimta"

"Uhmm, anything for you Safiyyerh ai kin cancanta kina bani tausayi"

"Thank you, again and again" ta ce cikin karewar muryar mai matuƙar sanyi irin ta yi giving up tuni sai kuma abin da take fata ya kasance. Suna cikin maganar Nahyan ya dawo ɗauke da chocolates da yawa masu kyau kuma, ya zauna aka fara gabatar da aure har aka kammala shine shine yake tambayar ne aka yi bayan ya fita me ya rasa a hirar he, yake faɗin what did i missed?

*

Present continues....

Suka sauke ajjiyar zuciya a tare fuskarsu ɗauke da farinciki musamman da suke tunanin a yanzu su bawai auren wasa sukai ba, maybe wata hanya ce da Ubangiji ya nuna musu wajan kuɓutar da daughters daga kamuwa da ciwon zuciya. Nahyan ya ce "Kenan dai yau da gaske na amsa matsayin babban yaya kuma ni uncle ne ko cousin, I don't know actually, wish you all the happiness in your marriage dear"

Safiyyerh ta yi murmushi ta ce "Thank you" tana jin wani irin farinciki na ratsa mata zuciya tamkar bata da wata sauran damuwa a duniya haka ta ruski kanta ta samu wani sashe mai girma a cikin gurbin zuciyarta ta sanya Mutallab ciki matsayin abokin rayuwa, kuma Matsayin mijinta, Safiyyerh's husband.

"Ango naga akwai free time bari na leƙa waje ko?" Kimiyya ya ce. Cikin sauri Nahyan ya miƙe ya ce "Bari na biyoka a bar su, su ɗan sarara su huta kuma su sha iska"

"Gaskiya dai" cewar Kinal.

Bayan fitar su, Safiyyerh ta kalli Mutallab da yake danna waya a hankali ta matsa kusa da shi, sai kuma ta saka hannunta ta ƙwace wayar hannunsa, a wani irin firgice ya ɗago rikitattun idanuwansa da suka ƙanƙance, ya kasa magana saboda murmushin da ta yi masa, ya yi yunƙurin miƙewa ta yi saurin saka hannunta ta riƙo hannunsa, ya haɗiye maganar maƙoshinsa da ƙyar, jin ta manna tafin hannunsa a ƙirjinta, bugun zuciyarta ya dinga ɗagawa da tafin hannun Mutallab, ta riƙe hannun da kyau a ƙirjinta ta ce. "Ban taɓa jin kalar wannan bugun zuciyar ba sai yau, sai na ji kamar tana bugawa ba bisa ƙa'ida ba, sai na ji kamar ta fara bugu a ƙirjina irin bugun nan na wa'adin ƙarshe a rayuwa"

"Ko dai yanzu na mutu, ai na san zan mutu ne a tafin hannunka, a jikinka, kuma a ƙirjinka" a hankali ta share hawayenta tana murmushi ta ce "Soyayyata a gare ka tsarin Ubangiji ne, don Allah ka kyautata mini Ka ji?"

"Fiyyya..." Shi kan shi a saman kan shi ya ji kiran sunan nata, ya ji kalamanta da hawayenta na narkar masa da zuciya, ya ji saukar abu mai kama da tuni, da tunasar da shi Jaanah da Diyna sai firgici ya gitta masa a zuciya. Ta yi murmushi ta ce "Kai nawa ne, ni taka ce in sha Allah, koda daddy bai amince ba ai yanzu mun yi aure ko? You are my husband ni kuma matarka ce, ka je ka faɗawa Ammo matarka na gaishe ta"

"Fiyyya, zare hannuna a ƙirjinki"

"Ina so ka ji yadda zuciyata ke bugawa" ta faɗa truly, with smile on her face tana sake riƙe hannun.

"Wani abu nake ji, zunubi Fiyya, ɗan iska za ki mayar dani, na ce iskancin kike ji da shi" ya ce yana mata ihu a saman kanta tare da ƙanƙantar da idanunsa ciki-ciki. Safiyyerh ta buɗe ido cike da tsoro ta ce "Wani abu? Wanne abu kenan?" Ta ce a ruɗe.

A ruɗan shima ya ce "Tomatir"

"Tomatir? A ƙirjin nawa?"

Harara ya watsa mata ta kyakkyawa ta yi da dariya ta ce "Yanzu fa kai babban mutum ne, ka fahimta ni matarka ce"

"Safiyyerh!" Ya kirata.

Ta ɗago ta kalle shi a hankali tana tsayar da dariyarta while she is keeping eye on him. Tare da jinkirin jin abin da zai fito daga cikin bakin nasa, she wish ya ce Fiyya i na son ki, na amince dake.

Ya durƙusa dab da fuskarta, suna shaƙar numfashin juna ya ce "Ke barewa ce, ke deer ce, deer ce Safiyyerh, matar moh daban, mai halin Moh daban, matar moh, zata kasance mai hali irin na Moh ne kaɗai, ki gane ki fahimta kin ji?"

"Me zan fahimta?" Ta ce a rarrabe, kamar kuma yadda ta yi furucin a rabe haka ta ji zuciyarta na rarrabewa a cikin ƙirjinta. Ya ɗage mata gira biyun tare da tsuke bakina ya yi mata feɗuwa mai sauti ya ce "Just friendship, abota kawai Fiyya ya wadatar" ta ce "Aure na da yake kan ka fa to?"

Ya ɗage kafaɗa ya ce "Sake ni"

Fita ya yi daga cikin ajin ya yi waje, idanunsa ya fara sauka akan Aafiyyah ita kaɗai zaune ta yi shiru hannunta riƙe da counter, kamar koyaushe ta saka baƙin gilashi a saman fuskanta ya yi mata kyau, ramarta ta sake fitowa fili kallo ɗaya za ka yi mata kasan cewa bata da lafiya, baki yaga ta murguɗa masa ta kawar da kai gefe da sauri kuma ta miƙe ta bar wajan tana ɗan danna wayarta ta yi hanyar lap ya tsuke fuska shima.

*

Paaahh na zaune a cikin ƙaramin parlonsa nasa yana sanye da men's slim fit 3pcs suit dark blue, ya jingina bayansa da jikin wata Morden chenille flocking floor yana

juyawa a hankali idanuna zube a kan wanda yake gabansa, Yana sauraron abin da yake cewa. Mutumin ya gyara zama ya ce "Kamar yadda tawa Safiyyerh take yɑ ta, haka na ɗauki yɑr wajanka Aafiyyah matsayin yɑ ta, wallahi dukkan da na yi mata akasi aka samu kuskure ne na san kuma sam ban kyauta ba, shi ya sa na nemi ganawa da kai domin na sake baka haƙuri don Allah"

Paaahh ya ce "Professor"

"Na'am, Prof "

Daddy ya amsa, kamar yadda shima mutane da yawa suke kiransa Matsayin Prof ya ce "I am very sorry professor"

"Idan dukan yɑ ta kuskure ne, dukan taka yarinyar fa?"

"Dukan tawa yarinyar gyara ne, saboda ta ɓata mini" daddy ya ce cike da damuwa ya ɗora da faɗin "Kamar Safiyyerh shekarunta 15 a duniya ita ce zata zo ta kalli cikin idanuna ta ce mini wai wani take so? Wanin ma ɗan iska can wani waje? Wai Ɗan'malam wanda bashi da cin yau balle na gobe. Gudanawa Safiyyerh take banda cewa ka haifi yaro baka haifi halinsa bane, wai ita aure take so ba karatu ba kuma bata gane karatun, ka duba fa?"

Paaahh ya ce "Ka fara fuskantar ta, amma duka baya kawo mafita a rayuwar raya, Aafiyyah da kake ganinta nan uhmmm" ya cije lips sai ya ce "Ina tsananin so da ƙaunar yɑta Aafiyyah bana iya kwatanta son da nake mata dana wani abu a duniya. Ba zan cika ka da magana ba, kawai don batu kake akan abin da ya shafi tsagina ne Allah ya raya mana su"

Daddy ya miƙe yana miƙawa Paaah hannunsa ya ce "Thank you professor" ya ce na jijjiga hannun.

"Ba damuwa, Prof"

Miƙewa ya yi a hankali hannunta riƙe da ƙaramin bottle of water, ya nufi hanyar shiga main parlo yana shiga ya samu MJ, da sauri ya ce "Sannu da zuwa dad"

"Safiyyerh fa" Paaahh ya tambaya kai tsaye ba tare daya kalli MJ ba, Ummi ce ta fito daga kitchen ta ce "Tunda ta dawo daga makaranta take ɗaki fa, sau biyu ina shiga ina tararwa tana bacci sai ban tashe ba domin kwana biyu bata baccin"

"Kuma kin yarda baccin take?"

"Na yarda mana Paaah"

"Uhmm" ya ce yana nufar ɗakin Aafiyyah, a hankali ya yi knocking can ƙasa ya ji muryarta ta ce "Daddy come in" buɗewa yi ya shiga, tana ganinsa ta miƙe tsaye tana murza idanunta ta ce "dad ƙwaro a ido, idona dad" ya dinga kallon ta, ya san cewa she is crying sai ya juya ya kalli frame ɗin photonta a hankali ya yi murmushin ya ce "As always, she is clever girl, smartness" ƙafarta ta ɗan buga a ƙasa ta fara yarfe hannunta tare da kiran sunan dad. Paaah ya juyo ya kalleta sai ya kama hannunta tare da janta zuwa bakin gadon ɗakin nata a hankali ya duba ta da kyau sai kuma ya ce "Gaya mini inda na taɓa tauyar rayuwarki?" Ta girgiza kai, ya tsare ta da idanu ya nisa ya ce "buɗe baki ki mini magana Safiyyerh" ta ce "Dad, komai ka yi da rayuwata daidai ne kuma ka cancanta ka yi komai ɗin, kai ne ka haife ni ka kula dani tun ina zanin goyo, ka ciyar dani daga halak, ka shayar dani daga halak, ka tofatar dani daga halak, ka bani kyakkyawar tarbiyyar da nake farinciki da ita. Babu wani hukunci a rayuwa da zaka zartar a rayuwata ban amsa ba Paaahh, zan maka biyayya ko da zai cutar dani ne " da sauri ta buɗe idanunta tana masa dariya ta rufe bakinta ta ce "Oh no my mouth, my mouth dad, na ce Professor Abdu the whole prof"

Idanun Paaah ya jirkice ya san wace Aafiyyah farin sani ya girgiza kai ya ce "Safiyyerh"

"My handsome dad"

"Yi kuka Safiyyerh don Allah"

Ta yi saurin ɗago kanta ta kalli Paaah da tunani daban-daban a ranta sai ta yi ƙasa da kanta ta shiga wasa da yatsun hannunta, ya kamo hannunta cikin nutsuwa ya ce "Komo zai daidaita kin ji, kar ki ji kamar ke kaɗai ce a duniya, You are not alone Safiyyerh, Paaah is here, Ummi, Mj da sauransu kin ji? Ki yi ta addu'a zan ƙaro miki wasu azkar ɗin. Ki yi ibada, ki karatu zan ma kawo miki wasu teddy amma ki rage abubuwa kina bacci, ina buƙatar rayuwarki, ki taimaka mini wajan ganin mun inganta lafiyarki kin ji?" Ta jinjina kai ya ce "Ki kuma taya ni kula da tarbiyyarki kin ji?" A hankali ta ce "In sha Allah, dad amma ban son teddy na ji bana son komai kuma a dai kawo mini teddy ɗin kuma na bana son wayata dad ka amsa" ta ɗauki wayar ta miƙa masa.

"Zo nan Safiyyerh"

Aafiyyah ta ƙarasa wajan Paaah, ya sanyata a jikinsa ya rungume ta sosai ya ce "Yanzu ko a kilo na saka ki ba lallai ki yi jaka guda ba" murmushi ta yi tana jin daɗi ta rungume Paaah, addu'a ya dinga mata yana shafa sumar kan nata. A hankali ya ji hawayenta na sauka a jikinsa ya ce "Ai na ce ki yi kuka, cry Safiyyerh ki yi kuka"

Shasshеƙar kuka ta fara ta riƙe shi gama ta saki wani irin raunataccen kuka Paaah ya rungume ta yana jin kamar ya tsaga ƙirjinsa ya mayar da ita ciki. A hankali ya buɗe ƙofar ɗakin ya shigo, fuskarsa nan kamar ya ce ya shiga uku, Paaah ya ɗaga kai ya kalle shi ba sai kuma ya juya ya ce "Mj ka same ni a part ɗina"

"Ok Paaahh "

Ya fita, yana ta tsaye a hankali kuma shima ya juya ya fice daga ɗakin. Paaahh ya ji saukar numfashinta a hankali ya ɗago ta daga jikinsa ya kwantar da ita ya rufe ta da duvet sai sauke ajjiyar zuciya take yi ganin kanta a buɗe ya ɗauki abu ya rufe mata ya rage mata gudun a.cn sosai ya kunna mata karatu ya kashe hasken ɗakin a hankali ya fita yana rufe ɗakin. Bacci ta fara yi peacefully.

*

Malam ne ya fito ƙofar gidansa da sauri saboda busar da ya ji da kuma ƙara kamar ana gangi tare da haushin karnuka, sak ya yi ganinta Mutallab wanda ake wa kirarin tare da laƙaba masa sunan Mai dawa. Shi kuma ya cake a tsakiyar tarin mutanen wanda suke sanye da kayan farauta, bunjimar riga da hular saƙi ga gorori a hannunsa yawanci hannunsa duk sun maƙala goro sai tarin karnuka da suke a wajan. Ƙaho suke busawa sun zagaye Mutallab da yaƙi motsi ya cake waje ɗaya yana jin naman jikinsa na motsawa da yin wani irin karkarwa musamman ƙirjinsa bai taɓa yin kirari ba, baya so kuma a tunzura shi amma gani yake da ƙyar ya iya shallakewa.

"Kai ne uban masu dawa, shiga jeji idan babu kai ƙarya ne, sai kai mai gidan tururuwai. A gaida ɗan gidan Malam Abdullahi shalelen Ammo, ba dai gaba da gaba ko ta baya sai an shirya don abin takazan nan. Mai dawa katarin masu dawa mai Sa'adah da Hamida, ina gwanin wani gana Bafullatana mai tiger kaga gwanin masu shiga farauta, farauta idan babu Muɗallabi yawan ta zubar ne, a lafiya Muhammad Mutallab Abdullahi Ɗan'malam"

Jikin Mutallab ya hau rawa, gabaɗaya gaɓɓan jikinsa mazari suka ɗauka kansa a durƙushe wani irin kururuwa Goje ya yi yana cigaba da yi masa dariya. A kiɗima ya ɗago kansa kamar an ce ya juya ya hango ta tsaye tana ta yi masa dariya, a mamakin ta sai taga ya kashe mata ido tare da yi mata alama ta zo.

A hankali ta taka tana shige mazan wajan ta ƙarasu tsakiyar filin ta tsaya a gabansa, uniform ɗin makaranta ne a jikinta. Ya tsora mata ido sai kawai taga ya rabe ƙafarsa biyu, ya ɗaga hannayensa sama ya buɗa su cikin wata murya mai sauti a kuma kumbure ta ji ya fasa wani ihu da kururuwa ya ce.

"Sai ni Muɗallabi na Bestien beastie, mai ƙaunar Allah da Manzonsa, ɗan Abdullahi da ammo ƙanin Hamida da Sa'adah, Allah ya ji ƙan Jaaanah Allah ya gafarta ran Diyna, dawa tamu jeji namu, naman jeji namu masoyin tiger da teddy wo!wo!wo!!! Sai ni Ɗan'malam jikam yarabawa" gabaɗaya ya firgice ya fita hayyacinsa yana jin busar ƙahon na tsuma naman ƙirjinsa zuciyarsa na motsa masa. Safiyyerh ta yi baya zata gudu ganin idanunsa kamar hayaƙi yake, tako ɗaya ta yi ya damƙo hannunta ya dawo da ita gabansa, ya saka hannunsa ya murza gashin kansa da gumin kansa ya saka hannunsa ya farke gaban rigarsa ya shafo gumin jiki, Safiyyerh ta daskare a wajan ganin ya shafa mata gumin a fuska, tare da zaro harshe kamar zai suɗe fuskarta sai taga allurai suna fita, askira ya ɗakko a jikinsa bata taɓa sanin yana da ita ba.

Ji ta yi fitsari na neman ƙwace mata, numfashinta ya fara ɗaukewa ta gama sandarewa tare da tunanin wa'adin rayuwarta ya zo ƙarshe a lokacin daya fara dirza mata askirar a fuska kamar zai mata bille. Luuu ta yi zata faɗi saboda sumewar da ta yi, ya saka hannu ya taro ta, ta faɗa jikinsa ya riƙe ta gam kuma ya kasa cigaba sai jikinsa daya ɗauki rawa, dakatawa sukai da kirarin da kuma busar, Goje ya ƙarasu wajan ya taɓa Mutallab ya ce "Mai dawa"

Cak ya miƙe tare da saɓa Safiyyerh a wuya ya shige da ita cikin shagon Goje dake ƙofar gidan Malam Abdullahi.

Malam ya yi saurin juyawa ya faɗa cikin gida yana tattare babbar riga ganin Mutallab kamar gidan zai shigo. Mama Zaituna ta ce "Malam ko lafiya?"

"Wanne lafiya? Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, matar nan ta gama cutata Allah ya yi wadaran halin Muɗallabi ya yi gutsi -gutsi da halinsa, na shiga uku wannan yaron shi ne zai yi ajalina"

"Hakan ba zai taɓa faruwa ba In sha" cewar Ammo. Cikin faɗa ya ce "Zaki rufa mini baki ko sai na yi ƙasa-ƙasa dake a wajan nan? Kina ganin masifar da kika ja mana, kina kallon yadda zunubin da kika aikata yake yawo ko? Kina gallo yadda shuƙar da kika yi take yaɗo ko? To gashi can kuma ya kashe wata baturiyar yarinya ba ruwana wallahi tallahi "

"Safiyyerh?" Cewar Ammo a kiɗime kuma ta yi waje cikin sauri malam ya ce "Kina fita ina miki Allah Ya isa, kuma a bakin auren naki " cak ta tsaya ta zubawa idanunta da sukai jajur a hankali ta juya kuma ta shige cikin ɗaki zuciyarta na yi mata wani irin zafi da raɗaɗi a hankali ta fara kiran sunan Allah maɗaukakin sarki.

Mutallab ya zubawa Safiyyerh idanu da har yanzu taƙi motsawa, sai ya lumshe idanunsa a hankali ya ce "Deer"

"Matar Moh, zata zama irin moh"

Wani abu ya shaƙa fata ta tashi a firgice tana kiran sunansa dana daddy da Ummeyh, hannu ta saka ta fara kai masa duka a ƙirji ya tsaya yana kallonta can ya fisgo hannunta ta dawo dab da shi cikin faɗa na ce "Bana ce miki abokai kawai ba? Ban ce haka ba?" Girgiza kai ta fara ta ce "Wallahi ni matarka ce ba abokiya ba" kuka take masa sosai jikinta na rawa bai kulata ba, bai kuma ce ta yi shiru ba a hankali ta zame jikinta ta kwanta a cinyarsa ta sauke ajjiyar zuciya, kansa a ɗora a fuskarta ya leƙa suka haɗa idanu ta yi masa murmushi ta ce "Kana da kyau sosai, ina son ka sosai, ina son yadda kake tsoro na ji ne"

"Hmmm"

"Nima hmmm" ta ce tana kallon lips ɗinsa da suke da damshi, hannu ta miƙa zata taɓa ya make hannunta ya ce "Tashi ki fece"

Miƙewa ta yi, ta ɗauki jakarta ta yi waje ta ce "Ba zaka raka ni ba? Na san ma sai an dake ni kamar koyaushe, to ai gwara su kashe ko?" Ta faɗa a raunace tana langwaɓar da kanta gefe ya zazzaro mata idanunsa. Ta ce "Bye bestie. I love you"

A wannan karon ma akan idanunsa ta fito yana daga cikin motar ya zuba mata idanu, cikin sauri ya sake ɗaukan photonta wannan lokacin har bidiyo ya yi mata, bayan ta tafi shi kuma ya sakko daga motar ya shiga wajan Mutallab domin aikin daya kawo shi sai juya masa tunani yake.

*

“Banbancin kowacce shigewar rana tana tare da yadda take sake kusanta zuciyata da kai Yaa Muhammad. WAIT FOR ME”

Ya dinga karantawa da wani irin sabon feelings a zuciyarsa, feelings ɗin rubutun, feelings ɗin mai rubutun, feelings Safiyyerh.

*

Har ta shiga gidan ta yi wanka tai sallah ba wanda ya nemeta sai ta naɗe ƙafa kawai domin hakan ya yi mata daɗi sosai a cikin ranta ta kuma ji daɗi da babu wanda ya tanka mata ɗin. A hankali Wahee ta buɗe ƙofa ta ce "Ki zo in ji daddy" Safiyyerh ta juya ta ce "Daddyana kike nufi?" Wani irin kallo Wahee ta yi mata sai ta ce "Allah ya sa ba daga sama na faɗo ba Safiyyerh balle ki mini gorin gidan uba, ke da Captain kuma sai dai gani daga nesa wallahi"

"Matsalata dake kan ki baya kawo wuta Wahee, ke Captain ya dama"

Fitowa ta yi, ta samu daddy shida Yaa sayyadi ta zauna bayan ta gaida Yaa sayyadin daddy ya ce "Bayan tashi daga makarantar ina kika je Safiyyerh?"

"Gidansu Mutallab"

"Uhmm ka ji ko malam? Ta shi ki tafi ina zuwa" ta miƙe ta koma sama, uncle Musbah ya bita da idanu kawai tausayin yarinyar ya ke ji ta samu balagar zuciya har haka wanann zamani ina za shi dasu ƙananun yara su ɗora kansu masifa har haka? Yaa sayyadi ya ce "A shawarce ka aurar da Safiyyerh, ita ɗiya mace idan ta nuna aure take so mafi samun kwanciyar hankali kawai a yi mata shi, saboda gudun samuwar wata fitar tada ban, ka daina ganin Safiyyerh tsaf za ta yi zaman aure ka tuna zamanin baya har a shekaru 9 an aurar da yarinya duk da cewa su ba fita suke janyowa ba, tunda Safiyyerh ta san ta fara bin saurayi har gidansu to abin ya lalacewa. Ita ɗiya mace fitina ce musamman idan suka samu balagar zuciya, Safiyyerh yʻarka ce ka aura mata yaron, ka bashi sana'a, gida yadda zai kula da ita, idan ka yi hakan ai ba faɗuwa ka yi ba ko? Yi wa kai ne da kuma kare tarbiyarta"

"Ai har yanzu ba wanda ya san dalilin daya saka take son auren" cewar uncle Musbah.

"Masifa mana irin ta yaran yanzu" Ummyh ta bada amsa kai tsaye.

"Kʻaddara Safiyyerh ta isa aure ba zan taɓa aura mata Ɗan'malam ba, domin za'a kawo mini ita gawa ne kamar sauran yʻan'matan, ƙaddara ba hakan bama, wallahi ba zan bawa Safiyyerh auran talaka futuk kamar Ɗan'malam ba, jira nake komai ya

yi daidai zata gane bata da wayo kam" ya girgiza kai ya ce "Kai bama shirya ganin auranta yanzu ba, bu bar maganar nan" Yaa sayyadi ya dinga janyowa Prof aya da hadisai amma ua rufe kunne tas.

*

Kimiyya ya dinga murmushi ganinta yau akan wani ɗan ƙaramin lifan ya ce "Yau an tuna babur ɗin nan kenan" ta yi masa murmushi kawai Safiyyerh ta ƙarasu ta ce "Yau kam dole a ɗana ni" Aafiyyah dai murmushi kawai take yi can ta ce "Ki je wajan bestie ya ɗana ki" Safiyyerh ta ce "Mijina za ki ce ai, au bakya nan aka ɗaura ko kimiyya baka bata labari ba kenan?"

"I almost forgot "

"Shi ya sa bata mini murna ba"

Aafiyyah dai murmushi kawai take tana kallon wani waje daban Safiyyerh ta ce "Kuma bai iya babur ba ai, even keke ma"

"Anya?" Aafiyyah said without looking at her tana ta gyara glasses ɗin idanunta.

"Bai iya bafa"

"Gwada shi kiga" cewar Aafff.

"My crush yau ba gaisuwa, to good morning baby" ya ce yana murmushi. Safiyyerh ta ce "kaga Aafiyyah na gaida mutane daman?" Daidai nan Mutallab ya ƙarasu, kamar Aafiyyah shima yau ba uniform suka saka ba, sportswears ne a jikinsu kuma duka farare gabaɗaya, abayan rigarsa an rubuta masa MOH ita kuma an saka mata S. ABDU.

Aafiyyah na kallon Safiyyerh ta ce "Hmm, mene a gaisuwa ne namesake? Kawai bana yin abin da ban niyya bane, amma wanda na girma ma ai zan iya gaishe ki"

"Then.... Greet us"

"Kimiyya good morning"

"Lafiya lou za ki yi albarka Aafiyyah in sha Allah"

"See, Safiyyerh ina kwana?"

Safiyyerh na dariya ta ce "Alhamd" Aafiyyah ta ɗan gyara zama glasses ɗin, ta ɗan yi baya kaɗan a hankali ta sake ja-da-baya direction ɗin idanunta kamar akan Safiyyerh a hankali ta ce

"Good morning Tayo"

Da sauri ya ɗago jin an ce Tayo, tuni Aafiyyah ta juya ta shige class, bai taɓa jin maganarta mai ɗan tsayi ba sai yau akwai sanyi da kuma tsiwa a sautin muryarta, akwai haƙuri da juriya da ƙulufuci duk a cikin muryarta, sai ya basar kawai ya yi gaba shima bayan ya dungurewa Safiyyerh kai da take masa dariya, ta bi bayansa da sauri tana riƙe hannunsa ya mintsini tafin hannun nata.

A hankali Kimiyya ya ce "take heart please Aafiyyah"

Suna tsaye za su shiga practical a lokacin, ya jingina da jikin bango ƙafarsa ɗaya a jikin bangon ɗaya a ƙasa ya harɗe hannayensa duka biyun a ƙirji students ɗin yake kallo yana mamakin abin da ya saka ɣan mata ke burge wasu mazan, as a man kuma good man kawai ka nemi kuɗi ka yi arziƙi ka shahara a duniya shi ya fi, ka zama mai iƙo da faɗa a ji, ka zama wanda zai iya samun abincin da zai ci da safe kuma ya ci da rana ya ci kuma da dare ya bawa ɣan'uwasa da duk mai jin yunwa ya

zamana kuma ka kasance mutumin da ake shakka duniya ta san da zamansa bawai kana namiji ka ƙare a wajan wata yarinya ba. Yana cikin wannan tunanin ya ji an ja mugun tsaki ya buɗe idanu ya ganta sosai ya buɗe idanunsa da suke a rufe kodayaushe cike da gashin idanu masu tsayi.

Aafiyyah ce tsaye take kallonsa can har zata shige sai ta ce

"Kai ai babu macen da zata so ka a school ɗin nan, sai dai kaga ana soyayya" bai taɓa tsayawa ya tanka ta ba sai lokacin har zai mata shiru sai ya ce "Ok" ta haɗe fuska "Saboda macen abinci ce ko iskar shaƙa daya zama dole Mutallab ya amfana dasu?" Ta yi masa sheƙeƙe tana nuna masa ɗaliban makarantar da kana ganinsu zaka san iyayensu nada arziƙi sosai kowanne a cikin students ƙuruciya da tashen balaga na ɗawainiyya da su. Ta ce "Mata ai sune jin daɗin maza, kai fa mace ko kiss bata taɓa yi maka ba a school ɗin nan" Mutallab ya yi ta kallon ta daga sama har ƙasa "Matar Moh zata zama mai irin halin MOH" har ya juya sai yaga bata ci bulus ba ya tako har inda take ya zuba idanunsa cikin nata kamar yadda take kallon tsakiyar nasa idanun a karon farko yana sake matso da fuskarsa "About the kiss, ƙilan Moh ya ji ƙan ki ya yi miki don naga shi kike buƙata"

Tsoro ya kamata amma ta dake ta fara ja baya ya yi saurin saka ƙata ya falleta kamar zata kifa ya saka hannu ya cafko gaban wandon uniform ɗinta ya dawo da ita dab dashi yana sauke mata numfashi a hankali kuma ya ɗora fuskarsa a saman tata yana zare glasses ɗin idanunsa sai ya ga ƙwalla ta cika idanunta fal ta dinga kallon tsakiyar idanunsa, suk dinga kallon kallo ta kuma jan tsaki.

"Aafi.....yyahhhh"

"Yaaa..." Sai ta yi shiru baki ta buɗe da niyyar cewa ya sake ta sai ta ji saukar bakinsa cikin nata, ya haɗe bakinsu waje guda.

Sai kuma ranar talata.

Za'a samu page 37-41 a ArewaBooks yanzu haka.

MUTALLAB

[1/7, 9:36 PM] Sis Fauzy: Chapter 37: Heartbreak

He just give her a small kisses, gani ya yi numfashinta ya tafi zai ɗauke, sai ya fasa abin da ya yi niyya ya tura ta baya ba can ba, da ƙyar ya ce "hmm bakin ma wari". Aafiyyah ta miƙe da sauri jikinta na ɗan rawa, ta yi kuma ƙasa da kanta taƙi yarda ta kalle shi, shi kuma ya cake a gabanta ganin yadda take ta murguɗa masa mitsitsin bakinta ya saka kawai ya girgiza kansa tare da ɗage mata kafaɗa ya yi gaba yana abinsa yana faɗin.

"Na sha banza"

Ta yi shiru kawai, kanta har lokacin a ƙasa, sai ya tsaya ya juyo da baya da baya yana ɗan tsalle ya dawo gabanta, ya jima sama da minti biyar sai ya sake juyawa ya tafi yana sake nanata mata. "E ɗin, na sha banza" a hankali Aafiyyah ta ja jikinta tare da jingina da jikin bango ta yi shiru, maganganun Ummi take tunawa "Ko hannu namiji ya riƙe miki, to ya miki ciki" hawaye masu zafi suka cika idanunta ta lumshe idanun, zafi kuma da damshin da ta ji a saman fuskarta da kuma ɗanɗano mai kama da gishiri ya gamsar da ita cewa kuka take yi, zafin hawayen ya sake ƙara tabbatar mata hawayen baƙin ciki ne.

"Allah na tuba, wallahi shine"

Sai kuma ta sulale a wajan tare da cusa fuskarta a tsakanin cinyoyinta tana fusgar wani irin numfashi, bata son tunawa, bata son tuna yadda abin ya ruskeka wani sanyi-sanyi ya ji yana ratsa fatarar jikinta yana kaiwa ƙashinta hari karkarwa bakinta da haƙoranta ya alamta mata zazzaɓi ne ke shirin rufe ta. A hankali ta duba lokaci, taga an kusa tashi ma daman tuni ta daina zaman extra lessona ɗin nan gwara ta zauna a gida kawai ta yi bitar karatun yafi mata, ta miƙe tsaye bayan ta saka glasses ɗin ta nufi hanyar class ɗin ta fasa zuwa lap ɗin daman wannan shine lokacin na farko dalilin wani abu da za'a nuna musu, tunda sai sun je Ss1 kowa zai bi layin da yake buƙata domin cimma muradinsa.

"Moh" Kimiyya ya kira shi, sai ya basar da kiran duk da ya ji.

"Da gaske fa an aura maka Safiyyerh wallahi ita matarka ce"

Mutallab, ya sake yin shiru tas kuma yake jin maganganun Kimiyyar a kunnuwansa kawai he is not interesting anymore. "Amma a ganina kar ku bari a gida a sani, more especially ita Safiyyerh saboda daddy ɗinta kaga ba zai amince ba zai iya rabaka da matarka ni kuma bana fatan abin da zai iya rabaku" sai a lokacin Mutallab ya ce "Hmm"

"Ba hmm, gaskiya ce ni a matsayin ɗan'uwana na ɗauke Mutallab, wallahi ban taɓa yi maka kallon aboki ba, ko a baya misunderstanded ɗin da muka samu laifinka ne, ka wulaƙanta ban maka komai ba, ni kuma bana ƙaunar wulaƙanci na ji zafi da gaske, na ji babu daɗi a cikin zuciyata. Jeddah ta ce mutum tara yake baya cika goma, to as a brother nake cewa don Allah ka daina wulaƙanta Safiyyerh tana tsananin son ka sosai wallahi tana maka son da ba zata iya yi maka bayani ba, da gaske nake trust me" ya yi shiru "don Allah Mutallab, ka gwada bata lokacinka ku tattauna wasa da zuciya babu daɗi raunin mata daban yake, koda muke yara ai wani abun mun san gaske and we are no longer a kids, beside yaran ne ma shi yaro ai yana son mai kyautata masa da gaske wallahi"

"Safiyyerh zata mutu ne, idan na ce zan yi soyayya da ita, ka sani"

"Ba lallai Safiyyerh ta mutu ba, idan ma ta mutu wa'adin ta ne ya cika da Ubangiji ya ɗiba mata, kuma kowanne bawa mai rai akwai silar mutuwarsa, ko ka ƙi ko ka so Safiyyerh cikon lissafin rayuwarka ce ka yi accepted nata ka amshe ta don Allah"

"I can't, Kimiyya "

"Za ka iya mana"

"Ka tsahirta mini, ka fini sanin daidai ne? Ko ka fini sanin rayuwata da kai na ne? Na san komai ina fahimtar komai, sai dai bada idanun da kake fahimta ni nake fahimta ba, ƙaddarar Moh bata zama da mace bace za'a dinga bi ana kashe duk wanda na nuna interest na aurenta ko wacce nake developing feelings a kanta. Rayuwata ba irin taka bace, ina da ƙalubale ina da muradan da nake son cimma, ni talaka ne futuk, ka sani"

"Mena na sani?"

"Ubanka ka sani, banza mayan magana kawai" Mutallab ya yi furucin a daƙile a kuma fusge cikin ɓacin rai da zafin zuciya, domin gani yake kimiyya bango yake son kai shi, idan ya tuna maganganu mahaifin Safiyyerh ƙirjinsa zafi yake masa, shi ya sa ko da wasa baya buƙatar ya ji an ambaci sunan mahaifin nata.

Kimiyya yana ta dariya ya ce "Kake zagina saboda ka ganka wani shirgege ko? Ni dai ba zan fasa fada maka gaskiya ba wallahi domin idan ban faɗa maka ba babu mai faɗa maka ba tunda ba wasu abokai gare ka ba, ni dai" Mutallab bai ƙara tanka Kimiyya ba, suna cikin tafiya zuwa harabar makarantar Safiyyerh ta yi murmushi tana kallon Mutallab ta ce "Na ɗauka ka tafi fa?" Ya dube ta sai ya yi shiru ta ce "Faɗa kuka yi ne naga yana muzurai kamar mara gaskiya?" Kimiyya ya sake yin wata dariyar yana girgiza kai a hankali yana ja baya ya ce.

"Ce mini ya yi fa ya jima yana son ki ashe kullum da son ki yake kwana yake tashi a ran shi"

Ta juya ta kalli Mutallab da yake dubanta ta ce "Bestie da gaske wai? Don Allah haka ne?"

"Ƙarya yake" Mutallab ya ce kai tsaye, ta yi murmushi kawai tana sunkuyar da kanta ƙasa tare da hawayen daya cika mata idanu sai ya ɗago kai ta ce "Na sani daman" ya juya idanunta tana ɗaga kafaɗa ta ce "Ni dai ba ina son ka, idan na mutu ruhina ba zai barka ba, fatalwata zata dinga bibiyarka ne har sanda zaka dawo gare ni mu rayu a aljanna shikenan Ubangiji ya rama mini duk wani damuwa dana shiga ta hanyar sadani da kai a cikin jannatul-firdausi" kallon tausayi kimiyya ya bita da shi sai ya juya ya kalli Mutallab shi bama su yake kallo ba, can kuma

yaga ya ɗan cije lips kamar zai yi murmushi sai kuma ya tsuke fuska. "Ni driver ya yi latti maybe na tari napep ko?"

"Aafiyyah ta rage miki hanya mana tunda a lifan dinta tazo"

"No, ai ba hanyar mu ɗaya ba"

Suna tsaye shima kimiyya na jiran drivern gidansu, a hankali yaga wata lafiyayar mota ta shigo cikin makarantar da wani irin fitinanen gudun kamar zata tashi sama, Mutallab ya saki siririn tsaki, bayan motar ta shigo kuma sai ga ambulance na asibiti suma sun shigo da sauri. Wanda yake cikin baƙar motar ya fito, mutane biyu ne da MJ da wani fari tsayayye akan ƙafafuwansa, a ɗan gaggace Mj ya kalli Safiyyerh yana ƙarasawa wajan ya ce "Safiyyerh ina Aafiyyah take? Fews minutes back ta kira ni bamu gama magana ba sai na ji ta yi shiru kuma a wayar bata katse ba, alamar numfashinta ya tsaya, so daman kin san bata da wani lafiya" a rikice Safiyyerh ta fara rawa da murya ta ce

"Aafiyyah ɗin? Yanzu na fito....,"

Wani sirrin tsaki aka je mai matuƙar ƙarfi, ta juya taga wanda suke tare da Mj ya zura wayarsa cikin aljihu kai tsaye kuma ya fara takawa da ɗan sauri zuwa cikin class ɗin nasu Aafiyyah.

"Yaya meke damun Aafiyyah ne don Allah" Safiyyerh ta ce hawaye na sauka a cikin idanunta jikinta sai rawa ya ke yi.

"Ki yi mata addu'a, idan dokin rai ce tabbas zata rayu amma tana cikin halin jinya " Mj ya ƙare maganar yana kallon Mutallab daya zuba hannunsa cikin aljihu kayan dake jikinsa yana kallon gate ɗin shigowa cikin makarantar fuskarsa a kame. Ganin ya fito da Aafiyyah rungume a jikinsa ga jini duk ya ɓata farar t.shirt ɗin daya saka ya saka cikin sauri ambulance ɗin suka fito da gadon marasa lafiya "her bag, da sauran kayanta" ya cewa Mj yana ɗora ta a gadon asibitin cikin sauri kuma ya tura ta ciki Mj ya dawo da sauri ya shiga cikin ambulance ɗin aka ja suka fita, shima motarsa ya shiga tare da yin reverse ya juya da gudu ya bar cikin makarantar.

Kuka sosai Safiyyerh ke yi, Kimiyya idanunsa sukai jajur ya kasa cewa komai jin kukan na gundirarsa ya saka ya damƙi hannun Safiyyerh ya jata suka fice, napep ya tsara ya faɗi unguwar su Safiyyerh ya tura ciki "Idan kika sake zuwa gidanmu sai na karya wannan sillan ƙafafuwan naki ok, kuma ki bashi kuɗin napep ɗinsa, kar ki sake kirana a waya kin ko?" Ta kalle shi da jiƙaƙkun idanunta sai ta yi murmushi ganin yadda lokaci ɗaya fuskarsa ta haɗe babu kyan gani "E ɗin, ni dai ina son ka"

Ya yi kamar bai ji ba.

"I love you, I love so much Bestien beastie, kuma sai na kira ka ɗin"

Mai napep ɗin ya ja yana yin dariya shima, Mutallab ya bi napep din da kallo sai kuma ya shafa kansa, ya juya ya sake kallon makarantar da kyau da kuma sunan dake zane raɗau na Federal college school FGC.

*

Safiyyerh na zuwa gida ta tarar da Uncle Musbah a parlo da shi da Wahee sai Ummeyh. Ta durƙusa har ƙasa ta ce "Uncle barka da yini" ya yi mata murmushi ya ce "Yawwa daughter, ya karatu"

"Allahamdulilah, uncle"

"Daman ke nake jira, amma ki fara shiga wajan mahafinki tun ki saman a nan parlo kin ji?"

Ta jinjina kanta, jikinta ba kuzari ta ajjiye jakar hannunta ta miƙe zuwa part ɗin daddy a hankali ta tura ƙofar bakinta ɗauke da sallama, yana zaune akan kujera ya yi shiru idanunsa suna kallon sama "shigo mana Safiyyerh Abdu" ta shiga cike da tsoro ta nemi waje a ƙasa kusa da ƙafafuwansa ta zauna ta ce "Daddy barka da hutawa" ya yi shiru sai ta fashe da kuka ta ce "ka yi haƙuri don Allah daddy ka yafe mini ka daina fushi da gudaliyarka"

"Gudaliyar dake ƙoƙarin haramta kanta dani?"

Ta girgiza kai tana dafa ƙafarsa ta ce "Ba zai taɓa jin daɗin rayuwa kana fushi dani ba, haka ba zan taɓa wanyewa lafiya ba idan ka wofitar dani, kar ka yi fushi dani daddy kai ne komai nawa, duk abin da na zama wallahi dalilinka ne, ina yi maka komai wajan kare hakƙin bibiyarka daddy don Allah don girman Allah ka bar ni da makaranta, bana so daddy wallahi bana fahimtar komai a karatun nan daddy ka bar ni na rayuwa da Bestie don Allah ka yi mini wannan alfarmar koda zai zama buƙata ta ƙarshe da zan nema wajanka, Safiyyerhrka ce daddy gudaliyarka, jaririyarka, ƴar gidan professor Abdu ɗin nan"

Tunda ta fara magana daddy ke kallon ta, ya haɗe hannayensa biyu waje guda yana kaɗawa idanunsa sun yi jajur a hankali ya ce "Tashi ki fita "

"Ba zan iya barin wajan nan, zuciyata zafi daddy ba zan iya jurewa ba, na kasa, na kasa"

"Safiyyerh wannan yaron yana baki abu a waje kina sha ko ci ko? Ya miki asiri kin shanye yanzu yake ɗawainiyya dake?"

"Daddy bestie bai mini asiri ba, koda ya yi mini na yafe masa wallahi duniya da lahira na yafe masa ai ina son shi, kuma babu kyau mace tana yi wa mijinta mummunan zato kar ka saka na ɗauki zunubi don Allah" ta ce cikin fitar hayyaci ƙirjinta na ɗagawa sama-sama. A harzuƙe daddy ya miƙe tare da yin kanta zai daka Uncle Musbah ya yi saurin riƙe shi, ba tare ya ce komai ba ya kama Safiyyerh suka yi waje, kai tsaye upstarts suka nufa inda ɗakinta yake. Ganin sun fito haka ya saka Ummeyh miƙewa ta nufi wajan daddy ta same shi a tsaye idanuna jajur a kiɗime ta ce "Prof ba dai Safiyyerh kakewa kuka ba? Ba dai wannan hawayen dominta yake zuba ba?"

"Ya kike so na yi idan ban yi kuka ba Dr? Wacce kalar jarrabawa ce wannan tsinannen yaron MUTALLAB, tsakanina da shi Allah ya isa ban yafe masa ba wallahi, Allah ya isa" ya zube saman kujera yana dafe kansa, Ummeyh ta ce "Me zai hana ka aura mata shi? Ko dan samun nutsuwar zuciyarka Prof dani kai na wannan issues

ɗin Safiyyerh gab yake da sawa zuciyata bugawa" ta faɗa a raunace, tana zama kusa da shi cike da damuwar data gama addabar zuciyarta, ita yanzu tsoro abin ke bata wallahi ta gama dawowa daga rakiyar yaran yanzu.

"Dr, bawa Safiyyerh Mutallab idan bai zama sanadin barina duniya ba to zai zama silar mikin da zai iya ajalina komai jimawa, idan ya zama auren take so lallai sai na bata wannan yaron Captain da yake son ta, ko na bata auren Nahyan ɗan wajan Wasim"

"Kana ganin zata amince?"

"Innalillahi wacce kalar jarrabawa ce? Yaron nan anya ba wajan yan hisba zan kai shi a yi masa nasiha ya kunce asirin da ya yi wa Safiyyerh ba? I need my Safiyyerh back, wannan ba Safiyyerh ta bace, ba haka Safiyyerh ta ya kamata ta kasance ba". Ummeyh ta girgiza kai ta ce "I don't think hakan zai zama daidaito, idan ka kai shi hisba ko kana so ko baka so sai sun ɗaura mata aure da shi ai, saboda za su tuhumeka da laifin child abuse da physical violence a part from violence against women. Prof as a mother nake maka wannan maganar don Allah ka sakko da zafin kanka ka aurawa Safiyyerh yaron nan, let bygone be bygone don Allah bana son wani abu ya samu Safiyyerh at first na ɗauka iskanci ne"

"Na aura mata ɓaraho? Mai kashe yan'mata? Gawarta kike so a kawo mini ko mene Dr? Sau biyu fa yana zuwa state cid? Sau biyu"

Cak Safiyyerh ta tsaya jin Abba Nasim ya kira sunanta, Mutallab bai juya ba sai sake riƙe hannunta kawai da ya yi. Ta juya ta kalle shi taga ba ita yake kallo ba, ta yi ƙoƙarin cire hannunta zuwa ga kiran Abba Nasim,Mutallab ya hanata, a hakan kuma Abba Nasim ya ruske su yana kallon Mutallab sai kuma ya kalli Safiyyerh ya ce "Mu je daddynki na kira" ya faɗa babu wasa a fuskarsa shi saɓanin uncle Musbah ne. Idanunta na rawa tare da cikowa da hawaye ta ce

"Abba, amma ba raba ni zai yi da bestie ba ko?" Ta yi furucin.

"Da abin da ya fi bestie zai raba ki, za ki shige muje ko sai na kifar dake na tattaka ki a nan wajan"

Ta juya ta kalli Mutallab, shi kuma yaƙi kallon ta, yana jin dai yadda hannunta ke rawa cikin nasa, ta kasa motsi zuciyarta cike da fargaba da zullumin abin da zata tarar a wajan daddy. Takaicin Safiyyerh ya kusa saka Abba Nasim yin shigewarsa, domin idan ya cigaba da tsayawa zai iya saka ƙafa ya yi ƙwallo da ita, tamkar yadda ake cilla ƙwallo cikin raga. Safiyyerh ta fara shasshеƙar kuka, kukan da yake ƙara tunzura zuciyar Mutallab, ta dube shi ta ce

"Me ya sa kowa ya kasa fahimta ta? Ummeyh ta kasa fahimtar halin da yarinyarta je ciki, Abba Nasim ya kasa, Wahee ta kasa ita da nake mata kallon yayata wacce zata iya bani shawara, kuma zata iya fuskantar halin da zuciyata take ciki, uncle Musbah ne yake gane shi kaɗai, only him, shi kaɗai ya san ciwon da nake ji a cikin nan ɗina bestie, a nan ɗina nake jin zafin komai a cikin nan ɗina"

Ta nuna masa tsakiyar ƙirjinta, wajan saitin zuciyarta. "Hatta kai ka kasa fahimtar halin da nake ciki, saboda kai na shiga wannan halin saboda kai ne Mutallab" sai ta durƙushewa a wajan tana fashewa da kuka shi kuma yaƙi tankata ta yi mai isarta idanunta jiƙe da hawaye ta ce.

"Ba zaka rarrashe ni ba?"

"Hmmm"

"Ka rarrashe ni ko zan ji daɗi"

"Ban iya ba" ya ce without a manners in his speech.

"To ai riƙe ni za ka yi,ka rarrashe ni ka dinga cewa na yi haƙuri har sai na haƙura haka ake yi"

Ya cije lips ɗinsa, ya dube ta yana fiddo mata da manyan idanunsa farare tas sai taga ya ɗage kafaɗa ɗaya tare da yi mata shiru. Safiyyerh ta ji rauni, wani irin rauni da tunanin cewa ta rasa komai sai shi, shi ɗin da bai ɗauki feelings da emotions ɗinta a bakin komai ba, shi ɗin da yake kallon ta matsayin da ita da babu duka ɗaya ne. "Please bestie, i need ur care mana, ka daina wulaƙanta ni Allah ba kyau ni fa matarka ce sirrinka, hijabinka, tsaraicinka, al'aurarka ni Safiyyerh"

Ya dinga kallon ta a mamakance wani irin kallo da zata iya ɗaukarsa da manufofi da yawa, ya girgiza kai yana matsawa dab da ita a daƙile daidai kunnenta ya ce

"Bangane ma'anar ni al'aurarki bace, ni ɗin? Ni ne al'aurar taki"

"E, ni Safiyyerh matarka ce, sirrinka, kuma tsaraicinka"

Ya nuna kan shi, da babban yatsarsa yana buɗe ido ya ce "Wuuuhh, ni ne al'aurar, nuna mini al'aurata a jikin ki, Fiyya gaggauta nuna mini na gani"

Ta fara ja baya ta ce "Hausa ce, Hausa na yi maka ba wani abu nake nufi ba, ai akwai sirri tsakanin ma'aurata"

"Oh"

Ta yi saurin cewa "Wallahi tallahi"

Ya wani suɗe gefen bakinsa, wanda most of the time sai ya ji an raina masa wayo ya ke yi, ya dinga kallon ta from head to toe. Da ƙyar muryarsa a cikin ƙirjinsa yana jin tana masa amsa kuwwa a kunne ya ce "Ai sai kin nuna mini, ko dai ki nuna mini ko ki mini bayanin yadda na zama al'aurarki" ya ce yana miƙa hannu zai damƙo ta, ganin Abba Nasim ya sake fitowa a karo na biyu yayo kan Safiyyerh ya saka ta yi bayan Mutallab da sauri ta ce

"Innalillahi, wallahi na manta"

hannu Abba Nasim ya tattare ya ce "Ke, nima yanzu zan nuna miki ɗan zamani ne, wacce irin yarinya ce ke? Na shaida miki ubanki yana kira amma ki manne jikin mutum kamar wata gaska, wanda ma na ji labarin baya ta taki? Za ki shige ki je kiran ko sai na yi miki bugun shekararriyar dawa a wajan nan hankali kwance?"

Abba Nasim, damuwa biyu ya dame shi, ya so haɗin auren Safiyyerh da Nahyan, sai abu na biyu yadda shegiyar yarinyar ta kafe akan faƙiri ɗan talakawa, ya yadda bata damu da damuwar iyayenta ba, sai abu na gaba shegen yaron da take naci a kansa ko darajar iyayenta da danginta bai sani ba, tun ɗazo Abba Nasim yake zarya amma kallo wannan bai haɗasu da Mutallab ba, balle ya saka ran jin sannu ko gaisuwa, Mutallab ba ya yarda ya kalli direction ɗin Abba Nasim ɗin. Sai ran Abba Nasim ya soso ainu ya kaiwa Safiyyerh duka cikin sa'a Mutallab ya tare dukan da hannunsa guda ɗaya, ɗaya hannun kuma ya riƙe Safiyyerh da shi still kuma bai kalli Abba Nasim ba kamar yadda shi kuma yake buƙatar hakan ido rufe.

Cikin ɓacin rai ya ce "Ko ɗan gidan uban waye? Dame kake taƙama? Ba shakka"

"Ɗan gidan babana malam Abdullahi ne mai rufar almajirai"

Cewar Mutallab, sai kuma a lokacin ya juyo suka haɗa ido da Abba Nasim, cikin sauri Abba Nasim ya haɗiye sauran maganganun, saboda wani irin abu daya gitta a cikin zuciyarsa, mai kama da tsoro da kuma kwarjinin idanun Mutallab ɗin, a shekaru dai, yana da ƙanƙantar su, a kamanni da tsare girarsa ya ninka ruɓin shekarunsa.

Ya tura Safiyyerh gaban Abba Nasim, ya gyara tsaiwa sai ya ji kamar ya cinnawa Abba Nasim su tiger sai kawai ya karkatar da kai ya tsuke bakinsa ya yi feɗuwar data saka Abba Nasim rufe kunnuwansa a hankali yake kallon shi kamar ba zai magana ba sai kuma ya shagiɗar da bakinsa da suke masu kyau madaidaita musamman laɓɓansa ya ce. "Dake ta, idan kana so"

"Dake ta, amma ba akan idanuna ba, kuma ƙwarza ne na gani a jikinta sai an biyani jikin matata"

"Bestie.....,"

"Quiet Fiyya!" Ya ce a dame.

"Ke jaka ce da za'a dinga dukan ki? A faɗawa Mutallab haramcin abin da kika aikata, a faɗa mini in ji ko zaɓar jinin talaka faƙiri mara gata wanda cin yau ke masa wahala balle na gobe shine kuskuren ki, da har suke miki haka?. Tell me, Safiyyerh answer my question right now"

Jikinta ya fara rawa ta kasa magana, ya ƙarasa gabanta ya daka mata wata razananniyar tsawa data saka ta kusa sakin fitsari a wando, hatta Abba Nasim sai da tsawar ta girgiza masa zuciya. Idanun Mutallab ya jirkice ya sauya launi ƙwarai. Baki ya buɗe zai mata magana sai ya kasa ya yi ƙwafa kawai, ya sake trying yin magana a wannan lokacin har tsartuwa harshensa ke yi yana alamta zafin zuciyarsa ya ce.

"Yes, Safiyyerh. Ni mahaukaci ne, mai taɓin hankali, mai rangwamen gata, mara dukiya da arziƙi, wanda bashi da wadatacciyar sutturar sawa, ɗan gidan Malam Abdullahi mai alamjirai. Yes, Safiyyerh, na kashe mata biyu Diyna da Jaanah, of course Safiyyerh ni ɓaraho ne, na haura gidan Alhaji Wada na saci garin kwaki da biredi domin na bawa Muneeberh, satar da bata mini rana ba, na je a lokacin da Muneeberh ke shaƙar numfashinta na ƙarshe. Yes, Safiyyerh, na shiga state cid har sau biyu wanda a nan mahafinki mai taƙama da arziƙi, wanda kuma duk arziƙinsa bai kai ƙaruna ba, a nan ya gani, and i saw him too. Yes, Safiyyerh ni mafarauci ne, ni mai shiga jeji da kuma dawa ne, mai yawo da karnuka,kuma yake jin daɗin

mu'amala da su, wannan shine MUTALLAB TAHHB SCORPION, ko ki ce mini Mai dawa, wannan shine zahirin wanda kike gani"

Safiyyerh sai ta ji rauni ya kamata, rauni irin na miji da mata, ta ji raunin Mutallab a cikin idanun zuciyarta ta ji kuma ba zata jure ganin wannan raunin ba.

Ya damƙo kaɗunta ya ce "Amma fa, wannan talakan ya san me yake yi, wannan mahaukacin ya san me yake, ina da zuciya, zuciyar da ba zata iya bari naga kin wulaƙanta ba, ina son ko ko bana son ki, wannan matsalar Moh ne, damuwar Moh ne, kina so na wannan kuma jin daɗina, i promise ba zan bar ki da yunwa kamar yadda suke tunani ba, zan nemo halak wajan kula dake"

"Fiyyya, ban miki alƙawarin soyayya iya tsayin rayuwa ba, domin rayuwar Moh, ba'a hannun Moh take ba, ba zan ce ina jin soyayyarki ba a raina, domin ban taɓa nutsuwa da tunanin hakan ba, ke dai ki cigaba da so na, ki so ni, love me, ki so Moh Safiyyerh" duk ya hargitsa kan shi, ya kuma har gitsa baiwar Allah, Safiyyerh kallon shi kawai take da jiƙaƙkun idanunta da sukai laushi.

Ya sake ta, yana ɗaga shoulders

"And i promise you, you'll never regret it, kin ji?".

A hankali ta ce "Thank you" sai kuma ta fashe da kuka sosai.

Ya sake dubanta, sai sakawa take ran shi yana ɓaci for no reason. Ya kama fuskarta sai ta kalli cikin tsakiyar idanunsa, ta ji zuciyarta na rawa ainu tana rawa da soyayyarsa, ta ji tana buƙatar jinta a tsakiyar ƙirjin nan nasa. Mutallab tunani ya faɗo masa, tunanin da bai ci a ce ya wanzu cikin ƙwaƙwalwarsa ba, tunanin Aafiyyah. Ya wanzu da tunanin Aafiyyah ba zata taɓa kallon tsakiyar idanunsa ba, bata da ƙwarin zuciyar yin haka, sai ya ji sanyi ya sauka akan gaɓbansa.

"Je ki, zan jira"

"Ba zaka tafi ba?"

Ya mata shiru sai ta juya tana waiwayo shi ganin ya sunkuyar da kansa zuwa ƙasa kamar mai tunani, sai ta ji tsoron tunanin nasa har ƙasan zuciyarta sosai.

A jingine jikin bango Safiyyerh ta ruski daddy idanunsa ya kaɗa ya yi jawur, uncle Musbah yana gefe sai Abba Nasim daya shigo tare da biyo bayan Safiyyerh. Malamin hisbar kam an kasa jin ta bakinsa har zuwa lokacin. Safiyyerh ta ƙarasa wajan daddy ta zube a ƙasa tana riƙe hannunsa ta ce "I am sorry daddy, I am sorry, ka yafe mini don Allah kar ka yi fushi dani don Allah kar ka yi mini haka" daddy ya zuba mata ido sai kuma ya yi murmushi mara sauti yana riƙe hannunta da kyau.

"Fushi? Why should i?"

"Ka yi haƙuri, ka yafe mini ban zama yarinyar arziƙi a....,"

"Stop saying this gudaliya" ya faɗa a hankali. Ya yi shiru sai kuma ya sake sauke ajjiyar zuciya mai nauyi yana jin zafi a ran shi, da ƙyar ya tattaro kalaman dake cikin bakinsa yana ƙarfafa zuciyarsa wajan kallon Safiyyerh da faɗin cewa. "Safiyyerh!"

"Daddy"

"I am sorry Safiyyerh, ki yafe mini Safiyyerh Abdu, ki yafewa Professor ɗin ki, ki mini alfama"

"Daddy please, why are you saying this to me? Ba ka mini komai ba ni ce mai laifi na maka laifi na bijire maka, na kasa yi maka abin da kake so, daddy ba yin kai na bane, soyayya ce daddy, abin da nake so ne ya haifar mini da hakan?"

"I knew, na sani"

Ya ja numfashi ya ce "Kina son aure, kuma shi Ɗan'malam ɗin kike so right Safiyyerh?"

"E, haka ne daddy"

"Bani da nutsuwar fahimtar auren ya yi ko bai yi ba, za'a duba hakan daga baya. Safiyyerh ni na ja miki balagar zuciyar dake wahalar da zuciyata a yanzu, sai yanzu na san dalilin son auren ki, shi ya saka mahaifiyarka ke ta kuka ashe mu ne sila, we are the reason behind all this, ban ɗauka hakan matsala bane, ban ɗauka kina lura damu ba, ban ɗauka za ki ji wani abu a zuciyarki ba, bai ɗaukan kaifin tunaninki zai kai ga abin da muke aikatawa ba. Safiyyerh da nake cewa ba zan aurar dake ba, ba hakan ne bana so ba, mu iyaye muna tsoron dukkan abin da zai taɓa yaranmu, ni ne mahaifinki Safiyyerh,tun kina ciki, cikin uwa mahaifiya nake kulawa dake, har kika zo duniya kika kawo yanzu har kika kai munzalin bijire mini, na ji daɗi dana fahimta tun wuri domin idan Ubangiji ya ƙaddara akwai zuri'a tsakaninku ke da Ɗan'malam to ko na hana auren tabbas za'a haife su ne a tsakiyar titi, bana buƙata hakan ko a mafarki. Na ji kawai ina son na sama miki rayuwa mai inganci ne amma ke bakya fatan hakan, soyayyar kike hangowa, auren kike buƙata, ba ki san damuwar dake cikin aurar ba, daɗin auren da abubuwan ƙawatarwar cikin su kike hangowa, Safiyyerh ko kin yi aurar a yanzu ba za ki samu abin da kike kwaɗayi ba"

"Zan samu daddy, I promise zan samu ka mini addu'a "

"Hmmm shikenan, zan miki yadda kike so, damar visa naki ya tsayar damu, In sha Allah a gobe zamu bar ƙasar nan, na amince ki auri yaron ki zauna da shi matsayin miji, amma ko da wasa Safiyyerh kar ki wajena da buƙatar wani abu, na zame hannuna daga cikin lamuranki, haka ban amince ki je wajan yan'uwana da zummar neman taimakon su ba, ki je tunda shi kika ɗauka, Allah ya tsare ki ya kuma kiyaye ki a duk inda kike, zan saka a aiko miki da kayanki ko ta hannun uncle naki ne"

"Kar ka mini baki daddy, ka saka mini albarka don Allah"

"Na saka miki, na jima da saka miki wish you a happy marriage dear, ki bi mijinki kamar yadda ki kaga Dr na yi mini biyayya" kuka kawai Safiyyerh ke yi, ta ji dama

zata iya haƙura da soyayyar Mutallab, ta ji dama zata ita haƙura da auren, but she couldn't tana jin wata dauwamammiyar soyayyar bestie a ƙasan zuciyarta.

Malamin hisbar ya ce "Amma ina da magana mai muhimmanci....,"

"Na janye, ba sai ka ce komai ba, jeki wajan mijinki Safiyyerh yana waje daman albarkacin shi na ci kika zo nan ɗin" cewar daddy, bayan ya katse malamin hisbar wanda shima bisa dole ya yi shiru ya zubawa sarautar Allah ido kawai. Safiyyerh ta yi ta kuka aka rasa mai rarrashinta, uncle Musbah kan shi a ƙasa. Abba Nasim ne ya dakawa Safiyyerh tsawa ya ce "Bar nan don ubanki" da sauri ta miƙe jikinta na rawa ta fita kai tsaye wajan Mutallab ta nufa tana zuwa wajansa ta zube a wajan ta haɗe kanta da qwwia ta dinga rusa masa ihu, shi kam ko a jikinsa ko a kwalar jikinsa ya dinga girgiza ƙafarsa is like yana enjoying kukan nata ya nuna.

*

Ammo na zaune a tsakar gida tana kaɗa miyar yauƙi wacce za'a haɗa aci tuwon dawar da ta yi, gefe guda kuma man ja ne data ɗaura saboda masu siya. Bata ji sallama ba sai tsaiwar mutane ta gani a kanta, ta kalli malam ganin ya shige ciki abinsa, sai kuma ta kalli Mutallab da yake kallon ta, irin kallon ki taimaka mini da yake mata tun yana yaro sai kuma ta kalli Safiyyerh dake raɓewa a bayan Mutallab, a hankali ta sauke ajjiyar zuciya daman tunda aka ce ana kiran su a ofishin hisba gabanta ke faɗuwa ta miƙe ta ce

"To da kuka yi tsaye gidan ne baƙin ku ko yaya?" Ta ɗora da faɗin "Kama marasa gaskiya"

Da ƙyar Safiyyerh ta ce "Ina yini"

"Lafiya lou Safiyyerh shige ki rabu da shi, daman shi zaman gidan ba wani damunsa ya yi ba"

Safiyyerh ta kalli Mutallab, sai taga ya ɗage gira sai kawai ta yi murmushi ta bi gefensa ta shige zata zauna a tsakar gidan Ammo ta ce "A'a shige ciki mana"

Ta yi jim, sai kuma ta shige ɗakin Ammo bakinta ɗauke da sallama, ta dinga kallon ɗakin tsaf yake yana ƙamshi amma bashi da wani girma katifa ɗaya ce tal a ƙasan ɗakin, sai kwanoka da kayan miya da sauran tarkace ta nemi waje ta zauna bata ma lura da Sa'adah ba sai da ta ji alamar kamar ana kallon ta ta juya cikin sauri ta ce "Anty ina yini?" Ta ce muryarta na rawa sosai tana bayyana tsoran daya shige ta sosai.

"Yaya za ki ce ba Anty ba, shima Tayo haka yake ce mini yaya"

“Tayo” it seems like ta taɓa jin sunan nan Tayo, a ina? A wajan wa yaushe kuma? Da sauri zuciyarta ta ce mata “Aafiyyah”

So Aafiyyah ta san komai akan Mutallab ta san everything na rayuwarsa ko mene? Ta yi shiru tana tunanin wanne hali yanzu Aafiyyah ke ciki? Ya jikin nata? Allah ya sa soyayyar Mutallab ba zata kassara ta ba. Safiyyerh sai ta ji hawaye na neman cika mata idanu, tabbas ta san cewa Aafiyyah na son Mutallab, ta faɗa mata, Aafiyyah bata taɓa nuna tana son abu ko da wasa idan har ba son take ba, she is always serious bata ma fiye wasa ba, komai zata faɗa sak take faɗa. Sai dai ita ta rasa ya aka yi idanun zuciyarta ya manta cewa Aafiyyah na son Mutallab ɗin? Ya akai zuciya ta kwashe ta zuwa ga soyayyar abin da Aafiyyah ke so? Bata sani ba, ta ji kawai itama tana son shi kuma data san cewa something ɗin da Aafiyyah ke cewa zata faɗa mata da tun a lokacin a wannan daren a cikin wayar zata faɗa mata cewa tana son Mutallab. Aafiyyah ta saba haƙuri a kodayaushe, ta saba yi wa Safiyyerh uzuri ta saba haƙura da komai ta bar Safiyyerh, sai hakan ya ƙarfafawa Safiyyerh zuciya tare da bata tabbacin a wannan karon ba, Aafiyyah za ta yi sadaukarwa, za ta iya sacrifice na soyayyar Mutallab ga Safiyyerh, sai ta ji cewa Aafiyyah ba za kuma neman Mutallab ba, sai dai shi ya neme ta, kuma ta san Aafiyyah ta yarda da ita, ta yi trusting cewa zata bawa Mutallab duka tarkacan wasiƙun ta ce masa Aafiyyah ce ke yi masa, da wannan tunanin da kuma yardar Aafiyyah ta bata za ta yi amfani da ita ta rayu da Mutallab, ba zai taɓa sanin cewa Aafiyyah na son shi ba har abada.

"I am sorry Aafiyyah!"

"Wace Aafiyyah?"

Da sauri Safiyyerh ta dawo tunaninta ta ce "To yaya zanna cewa nima as from today"

"Me kika ce?" Cewar Sa'adah.

Murmushin yaƙe kawai Safiyyerh ta yi, a haka Ammo ta shigo ta zauna ta ce "An yi kiran magariba"

"Ayya bamu ji ba" Sa'adah ta ce tana yin waje. Safiyyerh sai ta kasa haɗa idanu da Ammo, ita kuma Ammo sai kallon Safiyyerh take yi, kallon mamaki kyakkyawar yarinya mai gata da nutsuwa amma ƙaddarar soyayya ta afka mata sai kuma ta yi murmushi ba tare data san ta yi ba saboda wani shuɗaɗɗan abu data tuna years back.

"Ki je ki yi alwala"

"To" ta miƙe ta fita, tana kallon yadda Inna Binta da Mama Zaituna ke binta da kallo ganin jar fata sharr da ita cikakkiyar yarinya kuma girarta luff. Ganin kallon ya yi yawa sai ta durƙusa ta ce "Ina yininku?"

"Lafiya" cewar Mama Zaituna.

"Baƙuwa muka yi ne?"

"E, baƙuwa ce. Safiyyerh zo ki yi alwalar kin ji" Sa'adah ta faɗa tana nuna mata buta, ɗauka ta yi ta shiga banɗakin da yake da tsananin duhu jikinta ya ɗauki rawa, ga banɗakin duk zarni ga duhu gashi duk ruwa tsigar jikinta ta fara tashi, ta saba shiga banɗaki haske ko'ina har ma ta tanƙwashe ƙafafuwanta ta yi karatu. "Ya Allah" ta ce tana tsugunawa jikinta duka rawa yake yi, tana ɗora hannunta ta ji hannun ya sauka akan wani ƙaton abu mai numfashi mai laushi kuma, wani ihu ta kurma tana yin tsalle tare da fitowa a guje, da sauri Ammo ta fito haka Sa'adah wacce ke shirin tayar da sallah, Mutallab ma shigowarsa kenan ya yi tsaye a bakin

ƙofa yana kallon ikon Allah, a zuciyarsa kuma ya ji kamar ya tuntsira saboda yadda Safiyyerh ta bashi dariya ya riga da ya san abin data gani.

Ammo ta ce "Lafiya mene ya baki tsoro Safiyyerh?" Safiyyerh ta kasa magana sai hawaye jikinta duka rawa yake yi.

"Wani abu ne, there is something inside the toilet, na taɓa wani abu"

Ya ƙarasu ciki, ya zauna kan kujera ya dinga kallon su. Ammo ta ce "Wani abu ne kuma? Anya akwai abin tsoro a banɗakin nan?" Kai tsaye Mutallab ya ce.

"Akwai"

"Mene to? Babu komai fa tas na wanke banɗakin nan"

"Ba lallai ki gani ba, ita za ta gani matar Moh ce ai"

"Muhammad"

Ya miƙe tsaye kawai yana girgiza kai can ya nisa ya ce "Na ajjiye maciji ciki, maciji ta taɓa" ya ce yana shige cikin banɗakin sai gashi ya fito ɗauke da ƙaton maciji ya yi gammo da shi, idanun Ammo ne bai hana Mutallab maƙalawa Safiyyerh macijin a wuya ba. Inna Binta da Mama Zaituna ɗuwawu suka haɗa suka kifa baya, suka ƙara miƙewa zasu gudu ganin macijin na fasa kai, nan ma suka sake faɗuwa a tare sai kawai suka rungume juna tare da fasa ihu a tare.

Ammo ta bi Mutallab da kallo har ya fice daga cikin gidan "Sa'adah tsaya a nan ta yi fitsarin a bakin rariya sai ta yi alwalar ta tsorata da yawa wallahi". Sa'adah ta ce "To Ammo" haka Safiyyerh ta yi fitsari da alwala a nan wajan. Har ta yi sallah ta idar dana matsalar hawaye, sai dai ta samu kanta da addu'a akan Aafiyyah, addu'a akan

Allah ya ƙara nisanta Aafiyyah da ƙasar Nigeria ko mutuwa ce Allah ya ɗauki ranta a ƙasar da take a yanzu haka ya wanzu da wannan addu'ar.

"Ga abinci nan"

Safiyyerh ta dinga kallon tuwan, bata son taƙi ce ace ƙyamar tuwon take yi haka ta ci lauma ɗaya ta ce ta ƙoshi, tana ta zaune har wajan ƙarfe tara amma Mutallab bai shigo ba sai ta ji zaman ya dame ta, ga sauro nata ciwon farar fatar jikinta ga babu wayarta zaman ya gundire ta sosai. Cikin dare sama-sama ta ji Mutallab yana cewa "E matata ce" ta dube shi sosai ta ce "Haka mahaifinka ya ce, amma aure yanzu Muhammad ba ka yi gaggawa me kake dashi ina zaka saka yarinyar nan? Ba zata iya zama a nan ba, kuma ba zata iya cimar mu ba"

"Hmmm" ya ce yana miƙewa tsaye ya ce "Mu kwana lafiya"

Safiyyerh sai ta ji kamar ta miƙe ta bi bayansa, amma ba zata iya ba. Yana barin gidan kuma cikinta ya fara ciwo tun tana daurewa har ta ce "Wassh" ta miƙe zaune taga duka bacci suke a lokacin kuma an kawo wutar nepa, tana ta yarfe hannunta wani irin matsanancin ciwon cike ke addabar ta, da ƙyar ta miƙe a durƙushewa ta nufi hanyar waje a hankali ta zare sakata ta fice daga cikin gidan. Ta duba hasken gari dana wuta, ga almajirai duk sun kwanta, a zaune ta hango shi ya saka gabansa gabas yana zaune saman ladduma shi kaɗai kaf unguwar idanunsa biyu, ta rarrafa ta je wajansa ta kasa magana sai hannunta data saka ta taɓa ƙafarsa, ya juyo kaɗan ya dinga kallon ta sai taga idanunsa a ɗan juye.

"Cikina, bestie cikina zan mutu"

Sai ta fashe da kuka, ya yi ta kallon ta kuma bai motsa ba, a hankali ya juya ya mayar da kan shi gabas kawai, ta ƙara taɓa shi ta ce "Baka ji ne? Cikina ke mini ciwo amai nake ji, wayyo ni" ya sake juyawa ya kalle ta, sai ya ɗauke kan shi ya miƙe tsaye kawai yana saka hannunsa ya ɗago ta, ta miƙe da taimakonsa ta ce "Ba zan iya tafiya ba sosai yake mini ciwo" hannu ya saka ya ɗauke ta, ya nufi cikin shagon da yake da ita. Shi kaɗai ne ciki, Goje sunje farauta can wani gari, ya kwantar da ita da ita ya je ya kashe hasken ɗakin ta yi zumbur ta miƙe ta ce "Ya kuma ka kashe hasken ɗakin ka kunna"

Ya yi mata shiru. Ta sake cewa "Bana son duhu tsoro nake ji"

Bata san yana dab da ita ba sai data ji hucin numfashinsa a fuskarta murya kamar ba shi ba da ƙyar ya ce "Shhhh, shittt "

Baki ta buɗe za ta yi magana sai kuma ta ji ya rufe mata bakin ya ce "Shiru, ke bakya ganewa ba ki san lokacin da za ki addabi mutum ba, ki nutsu ki kwanta ba daidai nake jin kai na ba yanzu ok" sai ya sake ta, ya kuma kunna hasken. Tana ta murƙususun ciwon ciki idanunta na cika da ƙwalla taga ya kwaso wasiƙun Aafiyyah yana ta dubawa, ya jima yana dubawa sai kuma ya jingina da jikin bango ya ja numfashi ya sauke ya ce "Safiyyerh, kalamanki na zahiri daban, kuma na wasiƙun daban" ya sake dubawa.

"Yaa Muhammad"

Ya ce a fili, sai kuma ya ce "Na ji kin mini kamar wasiƙun nan, ba zan ƙara duba su tunda dai gaki"

Ta fara ƙifta idanu sai ta wayance ta ce "Cikina ke mini ciwo fa"

Bai kalle ta ba, kuma bai tanka ta ba sai wasiƙun daya ɓoye cikin aljihunsa ya kwanta tare da juya mata ba, ta cikin idanunta ya hango ciwon cikin nata, kamar yadda ta yatsun ƙafarta ya san ajin da take a cikin ajin yaran soyayya dana ma'aurata. Safiyyerh ta zubawa faffaɗan bayansa idanu, da yake ta sheƙin baƙin ta ji dai abu na janta, ta ji kuma ciwon cikin nata ya ƙaru sai ta fashe da kuka tana gangarawa zuwa inda yake, yana jin ta bai motsa ba, a hankali ta shige jikinsa tana wani irin kuka tare da ɓoye fuskarta a ƙirjinta.

Ya buɗe ido, sai ya girgiza kai yana buɗe hannunsa data takure shi sosai, a hankali ta sake tura kanta a cikin ƙirjinsa ya yi maza ya buɗe ido ya ce "Kika cije ni sai na rama, kuma ba ki da tabbacin inda zan rama Fiyya"

Ta marairace fuska ta ce "Kai baka iya rarrashi bane? Cikina ke mini ciwo, da gaske nake maka"

"To ɗauki abin da kike ƙulafuci"

"Meee?"

"Mele"

"Kai ko?"

"Ke ko?"

"Uhmmm"

"Nima ummmm ɗin"

"Ina son ka sosai, ina kishin ka sosai, ina jinka a raina sosai "

"Hmmm"

"Wai me hmm ɗin ke nufi ne?" Ta ce tana jan karan hancinsa da ɗan gemun data fara gani a ƙasan haɓarsa, sai ta fara tunanin topic ɗin da aka yi musu a subject ɗin basic science. Developmental Changes sai ta wanzu da tunanin topic ɗin a daidai lokacin da take cin gemun Mutallab a hannunta.

Past tense....

A lokacin suna zaune ita da Mutallab cikin sabon ajinsu na Jss 3, hira take masa amma ya yi shiru yana kallon gefe. A daidai lokacin kuma Aafiyyah ta shigo ciki,. domin da sun yi tunanin ba zata zo bama, bisa mamaki sai Safiyyerh taga Aafiyyah ta ja kujera ta zauna gabansu musamman Mutallab fuskarta ɗauke da murmushi ta ce "Namesake iyayen ƙauna" ta ce with smile on her face. Safiyyerh ta ce "Aafiyyah to ya ranki"

"Kamarya?"

"Da kiga ganni ina ƙauna da bestie nake nufi mana?"

Sai Aafiyyah ta ɗaga kafaɗa duka biyun ta ce "Alhamd, na san kina sane ai so ba zan damu ba, kina dai tuna maganata"

"Hmmm" kawai Safiyyerh ta ce. Mutallab na jinsu ya yi shiru domin baya wani fahimta, tunda Aafiyyah ta shigo ya sunkuyar da kansa ƙasa, ya zubawa yatsun ƙafarta idanu, takaici duk ya cika masa zuciya, bata san cewa tamkar tsirara take yawo bane da yan tsunta a bayyane, yana hango tsayin kowanne da ajin da ko wanne yatsa yake da kuma ma'anar zurfin ƙafarta da tudun dunduniyarta. Ya ja tsiririn tsaki.

Safiyyerh ta kalle shi ta ce "Wannan tsakin fa?" Ta tambaya da mamaki a fuskarta, kafin ya yi magana Aafiyyah ta kalli Safiyyerh ta ce "I am sorry "

"Sorry for what "

"Na dame ku" cewar Aafiyyah. Ta faɗa tana zubawa gefe guda ido, a hankali kuma ta sunkuyar da kanta ƙasa, sai ta ji ya take mata yatsun ƙafarta sai ta yi murmushi kawai ta miƙe tsaye "Ga basic science teacher nan, bye"

Sai a lokacin Mutallab ya ɗago kan shi ya dubi Aafiyyah, duban da hargaban abada ba zai manta da shi ba, memoryn da ba zai taɓa gushewa daga cikin tunaninsa ba, kallon daya zame masa abin tunawa. Maimakon ya ga Aafiyyah cikin uniform ɗinta

sai ya hangota tsirara, ba uniform ɗin yake kallo fa, farar fatarta yake kallo, babu wani abu da yake jikin Aafiyyah wanda Mutallab bai haddace shi a lokacin ba, mistakenly ya sunkuya ya murza kwallin daya jima da haɗawa sai yanzu ya saka domin gwadawa, gwajin ashe akan Aafiyyah sai sauka, sai a lokacin ya lura da ɓoyayyiyar baiwar dake tattare da jikin Aafiyyah, ya ji ya kasa shan iska, numfashi ya yi masa ƙaura "Auuuuhhh" ya furta da ƙyar, a lokacin da Aafiyyah ta juya ya ji kansa ya sara lokaci guda, a firgice kuma ya saka hannunsa ya murje kwallin cikin idanunsa tas ji ya yi wani abu na fusgarsa, sanyi na ratsa shi da kyau yana jin kamar zai yi zazzaɓi a lokacin.

Basic science teacher ɗin na zuwa ya fara musu revision akan Developmental Changes da kuma Characteristics features of Developmental Changes irin su, childhood stage, puberty stage, adolescence stage, and adulthood stage. A haka ya ce "Ok class, our today topic is Temporary and permanent changes in growth and development". Sai ya umarci yin shiru duk wanda ya yi masa dariya kuma zai gani.

Ya ɗora da faɗin "Wanann stage ɗin shine mai matuƙar wahala akan na bayan, tun farko na yi muku bayanin yadda maza ke jin feelings akan mata, haka suma maza. Da zarar girma ya fara zuwar wa namiji ko mace, akwai abubuwan da suke nuna wannan girman a bayyane kuma a ilimance, wanda kuma kai tsaye ke nuna mutum ya shirya zama father or mother ok. Baby age yana farawa daga 2-years, childhood age 11-years. Adolescence age 11-18 years, Adulthood age 18- and above. Daga ɓangaren mata akwai daɗin murya, muryarsu zata sauya wacce zata iya attracting feelings ga maza su ji suna sha'awar muryar wance, sai maƙerin budurci za kaga yarinya ta ƙara kyau sosai, sai bayyanar mama a ƙirjin budurwa...,"

Sai ya yi shiru, Safiyyerh ta yi ta murmushi like ta shige wajan ita, Aafiyyah kuma ta haɗe fuska tamau ta harɗe hannunta a ƙirji ta zubawa teacher ɗin ido.

"Bayan fitowar mama, akwai fara al'ada ga mace wanda kuma da zarar mace ta fara al'ada alamu ne dake nuna ta shirya ɗaukan ciki, rounded buttocks in girls, appearance of breast in girls, public hair in both boys and girls, breken voice in boys, well formed bones and become stronger very active boy, zai haifar da emotions da feelings, anan kuma ake bambanci sex and romance. Maza akwai buɗewar murya, gashin hammata, da kuma gashin gaba haka ma mata, idan an zo wannan stage ɗin kowa ɗari ɗari yake da ɗan'uwanasa. Time up sai kuma next topic"

Aafiyyah ce ta fara miƙewa ta fice jin yan class ɗin nata dariya kamar mahaukata. Mutallab ma ya miƙe ya yi waje jin Nahyan na cewa "Thank God, yanzu zamu gane ƙwailayen aji da wanda suka shiga matakin...."

"Dalla ɗan iska" cewar Kimiyya.

Safiyyerh ta miƙe ta fice tana murmushi ta fara duba inda zata hango shi.

Present continues....

Safiyyerh sai ta sake yin murmushi tana cigaba da jan ɗan gemun Mutallab, ya yinda shi kuma yake tunanin wasu ƙalamai da Safiyyerh ta yi masa a wata wasiƙa, lokaci ɗaya suka kalli idanun juna ya kasa magana ya kuma zuba mata ido a hankali ya ce "Kin ce kina son chocolates?"

Sai ta yi shiru can ta ce "Eh"

"Ok wace?"

Sai ta nuna masa lips ɗinsa ta ce "Wannan chocolates ɗin, ita miji ke bawa matarsa as a love"

"You are impossible Fiyya"

"Ko? Impossible ko?" Ta ce tana shafa ƙirjinsa, ya runtse idanunsa, maimakon ya ji emotions akan Safiyyerh sai ya dinga hango suffar Aafiyyah cikin yanayin daya kasa juyawa. Ya juya muryarsa a dame ya ce "uhmm Fiyya, ni.....ni... I am no ready, ban so ban iya ba muna da sauran time fiy....." Sai sauran maganganun suka tsaya masa ganin ta sauke masa numfashinta a ƙirji, ta fashe masa da wani irin kuka ta ƙanƙamesa ta ce "Don't you trust me? Idan ka amince da wasiƙuna me ya sa ba zaka amince mini ba? Ni ko? Ni bestie, shikenan ka bani wasiƙuna zai koma wajan iyayena ka riƙe soyayyar taka na fasa" sai ya ji rabuwa da wasiƙun shine abin da ba zai iya ba kuma. Ya dube ta da ƙyar ya ce "Me kike so?"

Mu haɗu litinin.

Mutallab paid book

08164069385

"You"

"Gani to"

"Kiss me"

"I don't know how to do it "

Sai ta yi murmushi ta ce "Nina iya ai, come bari kaga yadda ake yi" ta faɗa tana kai bakinta zuwa ga nasa a daidai lokacin kuma aka ɗauka wutar nepa sai ta ji daɗin hakan a ranta ta sake matsar da fuskarta zuwa ga tashi.

[1/7, 9:36 PM] Sis Fauzy: Chapter 40: My love for him.

Zame fuskarsa ya yi a hankali ya ce "Kama ta nan" ta yi saurin ɗauke fuskarta tare da fasa yin abin da ta yi niyya na daga sumbatar sai ta yi shiru, thinking how Aafiyyah feel a zuciyarta idan ta ganta tare da Mutallab a koyaushe? Da sauri kuma ta ɗauke tunanin Aafiyyah a ranta ta kwantar da kanta a jikin hannunsa tana jin ciwon ckin na sanɗarta a hankali a haka kuma bacci ya ɗauke ta sosai, bacci cike da mafarkai wai ga Aafiyyah a gadon asibiti, ga a Aafiyyah cikin makara, still ga Aafiyyah na mata magiya, magiyar da bata san ta mece ba. A haka har aka fara kiran sallar farko na shigowar asuba sai baccinta ya sake nauyi.

A hankali ta ji yana ɗan zungurinta ta miƙe zaune tana kiran sunan Allah, ta kalle shi ta ce "Shine ka tashe ni ko?"

"To wani daren za'a sake miki?" Ya ce yana ɗan gyara rigar jikinsa, sai ta dubi kayan jikinsa taga uniform ne a jikinsa ta ce "What, ba dai lokacin makaranta ya yi ba?" Ya jinjina mata kai kawai sai ɓata fuska ta ce "Sallah, ban yi sallah ba ai subuhanallahi"

"Ok, kina yi kenan"

"Bangane ba ina yi ba"

"Wai ba ki fara abin da teacher basic ya ce something al'ada" ya ce seriously.

"Ban sani ba, ido kake saka mini kenan? Ni ba wannan ba kunyar Ammo nake ji ba zan iya shiga ba, kuma ban zo da kayan makaranta ta ba, ko na saka sportswear ɗinka sai na je da su tunda nrml ne ai?"

Ya yi mata shiru ya cigaba da shiryawa, ta zuba masa ido kamar zata haɗiye shi, saboda wani irin kyau da taga ya yi mata ainun, bata taɓa lura da yadda uniform ke masa kyau ba sai yau, wani irin murmushi mai sauti ya suɓuce mata ta ce "Ka san wani abu? An taɓa faɗa maka kana da kyau? Kalar fatarka baƙa haka tana da wahalar samu, kuma an ce baƙaƙen maza ko a aure sun fi qualities right? I am very lucky dana sameka matsayin mijina" yana ta jinta dai, bai kula ta sai da ta ce "Ba zan iya haɗa soyayyarka da kuwa ba a zuciyata, kai ma Please kar ka mini kishiya ko a mafarki ne balle gaske"

"Hmmm, Safiyyerh Indomie generation ke damun ki, da addu'a kikai Allah ya bani kuɗi na kula dake, na yi miki haɗaɗɗan gida mai kyau, ki samu nutsuwa a zuciya yadda ya kamata, amma kin zauna kina wani imagination"

"Ai ni son ka a zuciyata ba ruwan shi da wani babban gida, ko garin kwaki a jiƙa ka gani zan sha"

"Sallah Safiyyerh!"

"Ohhh"

Ta miƙe da sauri tana gyara jikinta har yanzu rigar abaya ce a jikinta tun ta jiya, ta ɗauki hijjabinta ta saka, sai ta fara rarraba idanunta domin bata san ta yadda zata shiga cikin gidan ba, ta sake duban Mutallab taga yana zaune ya tanƙwashe ƙafarsa ɗaya saman ɗaya yana duba wani littafi a nutse, tafin ƙafarsa fari tas kuma jajur, yatsun ƙafarsa dugwaye faratan farare dasu, ta zubawa sumar kansa idanu baƙa ce sosai kuma ta ɗan cuccure waje guda sai ta yi kyau. A hankali ta ji ya ce "Ina girma ina sauya kala da kama ne Safiyyerh, ki ɗauki sallah da muhimmanci ok?" Sai ta sauke ajjiyar zuciya ta ce "ai kunyar zuwa wajan Ammo nake bata san na fito ba wallahi sam"

Ya ɗaga kan shi ya yi mata kallo ɗaya, sai ya ɗauke kai yana miƙewa tsaye ya yi waje ta bi bayansa da sauri, duk yadda taso cimmasa bai tsaya ta ba, a tsakar gida ta tarar dashi tsaye yana kallon Sa'adah dake masa magana... "Ba dai ba ki yi sallah ba?" Cewar Sa'adah ta faɗa tana miƙewa ta ɗauki buta ta bawa Safiyyerh, da sauri ta amsa ta shiga banɗaki, a tsaye ta yi fitsarin ta ɗaura alwala don ko wanka bata jin zata iya yi a cikin banɗakin. Har kuma ta idar da sallah bata jin tarin Mutallab ba, kuma yan tsaye a tsakar gidan.

A sanyaya ta ce "Ina kwana?"

"Lafiya, ya kwanan baƙun ta kuma Safiyyerh?" Cewar Ammo.

Murmushi kawai ta yi, sai kuma ta shafa kai ta ce "Daman jiya...." Da sauri Ammo ta dakatar da ita da faɗin "A'a ba sai kin faɗa ba kin ji? Fatan dai bai miki komai ba, domin na san halinsa ƙwarai"

"A'a, hira ma mukai"

"A'a ki daina wani goyan bayansa, Kodayake ai miji ne, shi kuma miji haka yake zuma ga daɗi ga harbi watarana zan ji kan ku ne ai" Ammo ta ce, cike da fara'a a fuskarta da ƙoƙarin ganin ta saka Safiyyerh ta saki jikinta. Murmushi kawai Safiyyerh ta yi, a hankali ta ga ya ɗago labulen ɗakin daga bakin ƙofa ya tsaya, yana ta ƙissima abin da zai ce kwana biyu bakinsa har ciwo yake kuma duk Safiyyerh ta ja masa yawan yin surutu haka kawai. "Sakar mini labule, idan ba wani abu ya kawo ka ba malam"

"Hmm, ta je a waje" ya ce so clam.

"Ita wa?"

"Safiyyerh, ur uncle is here" yana cewa haka ya saki labulen ya juya abin shi yana duba agogon dake jikin wayar hannunsa. Safiyyerh sai ta ji gabanta ya faɗi, ba dai zuwa akai tafiya da ita ba? Ba dai daddy shawara kuma ya sauya ba daga baya? Innalillahi in sha Allah ba haka bane. Sai da Ammo ta nanata mata sannan ta miƙe a hankali tare da fita, sai Mama Zaituna da Inna Binta suka bi bayan Safiyyerh da kwallo.

"Kwaɗayi maɓuɗin wahala, ashe yar gidan masu kuɗi aka hango masa shine ya kashe waɗancan?" Mama Zaituna ta faɗa tana riƙe haɓarta cike da mamakin kyawun Safiyyerh ga jikinta so ma sha Allah. Inna Binta ta ce.

"Bana jin cewa iyayenta sun san yana kashe mata fa, kuma basu da labarin ya taɓa yin sata ko?".

"Ko shakka babu, domin duk mai hankali ba zai bawa Muɗallabi auren yarinya tsaleliyya kamar wannan ba, duk yadda aka yi an rufe su, ni banda kar ace sokar aure wallahi tallahi da gidan su yarinyar zan nema na faɗa musu komai, idan ya so a raba auren ya je ya auri daidai da shi, domin wannan yarinyar idan ya kashe musu ita wallahi tallahi har ya mutu yana gidan ɗan'kande" Mama Zaituna ta yi furucin da mamaki da takaici kuma, tana ƙara jinjina kyan Safiyyerh a fili. Inna Binta ta ce "Au ke jira za ki yi? Ai a yau ɗin nan zan nemo gidan iyayenta na labarta musu komai, ba mamaki na dawo da tukuici mai girman gaske, suna sane suka nema masa aurenta ai saboda sunga yar masu kuɗi ce zakka ba zata shige su ba" Inna Binta ta ce tana miƙewa.

"Ke Binta sokar aure za ki je yi kenan ko? Ba kyau ba"

"Zauna nan Zaituna, da sanyin safe ake kama fara wallahi "

Safiyyerh, kanta a ƙas ta ƙarasa wajan motar uncle Musbah, shima yana ganinta ya buɗe motar ya fito cikin sauri ta ce "Good morning uncle" ya yi murmushi ya ce "Morning daughter, ya kwanan amarci kuma? Hankalinki ya kwanta ko? Kin samu Mutallab" a hankali ta ce "Uncle ka fahimce ni" ya jinjina mata kai ya ce "Na fahimta ai, na jima da fahimtarki Safiyyerh fahimtar ce ma ta saka na ce haka, kuma na miki uzuri hakan kuma ya faru ne saboda lack of parent guidance and careless, iyayenki sune silar komai, sai ƙuruciya da balagar zuciya dake ɗawainiyya dake, ina miki addu'ar kar bijirewar Prof da kika wani abu ya shafe ki, domin na karaya ainun da yadda naga ya amince kuma hawaye na fita daga cikin idanunsa. Safiyyerh hawayen iyaye masifa ne, ba zan yi mata ya zama masifa a gare ki ba domin bayin kan ki bane sakacin tarbiyyarki aka samu, wanda kuma ance icce tun yana ɗanye ake tanƙwara shi, amma su sun yi sake ya bushe har yana neman karye musu, wannan shine kuskure na wasu iyayen, yanzu duk abin da suke buƙata ki yi ba za ki iya yi ba, saboda kin yi nisa ba za ki taɓa jin muryarsu ba, balle sunanki da suke kira"

"I am sorry uncle"

"Sorry for yourself Safiyyerh, kawai na ji ina jin tausayin ki da kuma auren naki, daka ke har mijin naki kuna buƙatar kulawar iyaye sosai. Safiyyerh ki gane da gidan mahaifinka Professor da nan gidan surukanki akwai bambanci, kar ki yi tsammanin samun abin da kike samu a gida, ki zama mai haƙuri da ɗauke kai, mai jajircewa akan mijinta, ki zama mai taimaka masa a kodayaushe kin ji ko?" Ta jinjina kanta, hawaye na cika mata cikin idanunta sai ta samu kanta da tambayar "uncle daddy, Ummeyh?" Ya dinga kallon ta da tausayi a fuskarsa sai kuma ya kalli sama jin ƙarar jirgi ya ce

"Idan wannan bai zama jirginsu ba, to jirgi na gaba nasu ne, daga airport na zo nan, nima ɗin zan yi tafiya shima Abba Nasim ya shige"

Safiyyerh sai ta ji kamar ita kaɗai ta rage, wata kewa ta mamaye jikinta so da ƙaunar iyayenta na girmama kansu a zuciyarta ta dinga kuka ita ɗaya tana ajjiyar zuciya "Kukan mene? Kin samu abin da kike so ai, no more crying" sai ta ji zuciyarta na cewa "Yes uncle, I'm not alone Mutallab is here" a fili kuma ta ce "Yaushe za su dawo to uncle?"

"I don't know" ya ce yana ɗaga kafaɗarsa. Bayan mota ya buɗe ya sakko da jakar kayanta, da uniform da komai, amma banda takardun makaranta, takalma da bags ɗinta da duk tarkacan kayanta na mata har ma da wayarta. Ya ce "Ga kayanki nan"

"Thank you uncle" ta faɗa a hankali, sai kuma wani ɗan murmushi ya suɓuce mata ashe haka ake kai amarya? So ko wacce amarya haka ake aurenta dama? Shikenan ta zama matar Mutallab? Allah, Allahamdulilah! "Ga wannan" ya miƙa mata zoben gold ɗinta,ta amsa ta saka a hannunta ya ce "Zan tafi, Allah Ya sanya albarka kin ji gudaliya"

Ta yi shiru, sai ya ce "Akwai wani abu da kike buƙata ne Safiyyerh? Faɗi kafin na shige nima"

"Uncle ka bani kuɗi na siyawa bestie kaya shima, please uncle" ta ji ta samu kanta da cewa haka. Uncle Musbah ya dinga kallon Safiyyerh sai kuma ya ce "Ai na san mijinki, na taɓa masa kyautar kuɗi yaƙi amsa, yana da zuciyar nema na yarda da shi, zan aiko miki da kayan ok? Ga kuɗi sai ki riƙe a hannunki ko? Kinga ba gida ne dake ba balle a yi maganar shirgin kayan mata furnitures, ko gara sai sanda kukai gidan kan ku" ta yi murmushi ya miƙa mata bandir ɗin kuɗi masu yawan gaske ta amsa tana masa godiya, da hannu ya kira Mutallab da yake shirin tafiyarsa makaranta hankali ƙwance. Mutallab ya ɗan yi sak kamar ba za shi ba, sai kuma ya ƙarasa yana ɗan sunkuyar da kan shi kansa "Mutallab ga kayan matarka nan, ka shigar mata dasu ciki?" Ya jinjina kai kawai, sai uncle Musbah ya ɗora da faɗin "Safiyyerh ta zama Mutallab, Mutallab ya zama na Safiyyerh, Bestien beastie. Ina neman alfarma daka tsayawa Safiyyerh don Allah ka ji yaron arziƙi?"

Mutallab ya kalli uncle Musbah, can ya nisa ya ce "Uncle, idan kana ce mini yaro sai na ji ba zan iya ba kuma" ya faɗa yana yin kicin-kicin da fuska. Uncle Musbah ya ce "Waye mutum, ai kai babban mutum ne irin ku basu da yawa, ina da mata kana da mata kaga babu batun yaro ko?" Bai ce komai ba, ya ɗauki kayan Safiyyerh ya yi cikin gidan dasu a hannunsa biyu.

"Na gode sosai uncle"

Ya jinjina mata kai, ya dinga kallon ta sai ya ji gabansa na faɗuwa haka kawai musamman murmushi da kuma hawayen da yake gani at the same time. "Safiyyerh" ya kira sunanta, sai ya miƙa mata hannu bayan ta ɗago kanta da sauri ta ƙarasa ya rungumeta a jikinsa yana jin wani iri, yana jin kamar yana rabuwa da tsaginsa ne, ya ji tsoron barin Safiyyerh da gaske, amma bashi da wani zaɓi haka ta nema kuma ta samu da ƙyar ya zame ta a jikinsa ya ce "Allah Ya yi miki Albarka" ya ce a hankali har ya shiga mota tana tsaye, sai kuma ta fashe da kuka tana juya da sauri zuwa cikin gidan a zaure sukai karo da Mutallab zai fito, tana ganinsa taga bata da wanda ya shige shi, ba kuma da wanda zata iya tisawa a gaba ta yi wa kuka sai shi ɗin, only him ya rage mata, da sauri ta faɗa jikinsa tana fashe masa da kuka ta ƙanƙamesa da kyau tana gunjin kuka, bai hanata ba, kuma bai mata shamaki da jikinsa ba, tunda ya fahimci jikinsa na ɗaya daga cikin abubuwan dake sanya zuciyarta nutsuwa ya daina hanata hakan. Suna tsaye har ya gaji ya yi ɗan gyaran murya, sannan ta ɗago kan ta a hankali daga jikinsa

"He lefted" ta ce.

"Hmm"

"Ya tafi, ba zai dawo ba"

"And? Ki bi shi mana"

Sai ta yi murmushi ta ce "Ai ba zan iya ba ka sani, salon ka auri wata ko? Bayan yanzu kai kawai nake da shi, kai nawa ne ka ji?"

Komawa ya yi ciki, ta bi bayansa, cikin sauri ta shirya tsaf kayan sun mata kyau sosai, ya jingina da jikin bango yana zuba mata idanu har ta gama shiryawa ta ce "Na yi kyau ko? Ka ce na yi kyau, nima ai na faɗa maka cewa ka yi kyau" ya ƙanƙantar da idanu yaƙi magana, s haka Ammo ta shigo ta ce "Ba za ki karya ba, zauna ki sha kunu da ƙosai kafin a kammala ɗumame" Safiyyerh ta yi shiru "Zauna

mana" ƙoƙarin zama ta fara sai suka ji ya ce "zan ta fi, ta fito kawai" ya ce yana yin waje.

Da sauri kuma ta bi bayansa.

*

Kamar yadda yake a ɗabi'ar makarantar sai da aka yi assembly kana aka fara shiga class, Safiyyerh ta dinga rarraba idanun ganin Aafiyyah amma babu ko inuwar Aafiyyah, haka babu Kimiyya. Kinal ta ce "Safiyyerh wai ya jikin Aafiyyah ne? Na yi ta ƙoƙarin kiran numberta amma bata shiga, har ya yayanta na kira amma baya tafiya is she ok? Lafiya take?"

"Safiyyerh!" Kinal ta sake kirata fuskarta ɗauke da damuwa, domin tana da tabbacin Safiyyerh ta san komai ta san inda zata samu Aafiyyah, domin ko a school idan Aafiyyah ta ɓoye ana nemanta Safiyyerh ke nemo inda take kodayaushe. A hankali Safiyyerh ta kalli Kinal ta ce

"Me kika ce?"

"I asked you Aafiyyah, where she is?" Ta faɗa loudly.

"An yi mata aure, kamar yadda aka yi mini kuma ba'a ƙasar zata zauna ba, Aafiyyah da Nigeria har abada, nima ɗin na nemi numberta bana samu kullum"

"Safiyyerh?"

"Kinal"

"Ita Aafiyyah a kaiwa aure? Kin san Aafiyyah da karatu?"

Safiyyerh ta watsa hannunta ta ce "Ohh Kinal, ba za ki fini sanin Aafiyyah ba dai ko? Kawo wayarki na saka miki wata number ƙila ki same ta ko?" Cikin jin daɗi Kinal ta bawa Safiyyerh wayarta itama Safiyyerh ta amsa.

In few minutes, ta goje number kimiyya tas, ta goge ta Aafiyyah haka ta goge da Mj daga wayar Kinal, sai ta saka mata wasu fake ta kuma saka mata wata as Aafiyyah's new number kana ta bata number. Haka ma ta amshi wayar Nahyan ta goge komai. Mutallab dai hankalinsa na kan littafi gabansa duk da yana jin conversation ɗin su.

"Safiyyerh ana kira a office na principle" cewar Class captain na su Safiyyerh. Sai ta yi sak can kuma ta miƙe ta fice ta jima har aka tashi daga makarantar bata dawo ba. Mutallab sai ransa ya ɓaci sosai, ya yi gaba zai tafi sai ya hangota zaune ita ɗaya ta ci kuka idanunta ya kumbura sosai gently ya ƙarasa wajan, madadin ya yi magana sai ya cake mata aka ta ɗago ta kalle shi, sai ta miƙa masa envelop ɗin hannunta ya saka hannunsa ya amsa, muryarta a rarrabe ta ce "An kore ni, na yi failed exam har sau uku" sai ta sake fashewa da kuka sosai fuskarta ta yi jajur, ta miƙe tsaye tana mustsika fuska sosai sai kuma ta kalli Mutallab tana dariya while hawaye na zuba cikin idanunta ta ce "Na zama drop out, ko out of school wanne, sun kore ni daga makarantar innalillahi, bestie ba zan sake zuwa makaranta ba" ta faɗa tana sakin raunataccen kuka jikinta har wani kakkarwa yake sosai. Mutallab ya kasa ce mata komai, ta dinga kuka ita ɗaya yana tsaye a gabanta sai data gaji da kuka ta ce "Mu je"

Yana tafiyar nan tasa majestically, a zuciyarsa yana nanata "Ke kika ja komai, ke ce Safiyyerh" a wannan tafiyar kuma tunanin Mutallab ya sauya, tunanin kula da Safiyyerh, tunanin yadda zata samu wata makarantar, ko kuma ya yi musu karatu duk abin da ya zama ai kamar ita ce, a wannan tafiyar ya ji ya yi believing na duka wasiƙun wajansa, ya ji ya gamsu da su, ya kuma yarda cewa Yes, yana son wasiƙun yana kuma son mai wasiƙun he trust Safiyyerh so much a lokacin, ya amince he loves Safiyyerh, without knowing yadda love ɗin yake, ba tare da sanin mene gaskiyar abin da ke zuciyarsa ba, bai kuma ya yarda ya zauna ba, ya ji cewa duka wasiƙun is belong to Safiyyerh's. Har suka fita yana nanata sunan FGC a zuciyarsa.

A cikin napep ya same ta zaune yana shiga ta ce "Kai ta tafiya kana bubbuɗawa haba bestie"

Ya cije lips, yana kallon ta.

"Uhm, i feel like crying"

Ya yi shiru "Na kwanta a cinyarka? Bacci nake ki kai na ciwo yake mini sosai"

"Uhmmm" ya ce.

Sai ta zame ta ɗora kanta a gefen kafaɗarsa, shi kuma ya gyara hannunsa yana yin game a wayarsa suna tafe bacci ya ɗauke ta. A hankali ya kama hannunta yana kallo, tare da zoben dake jikin madaidacin hannunta sai a lokacin kuma ya ji jikinta zafi ga cikin na ƙogi ashe fa ko karyawa ba ta yi ba. Ji ta yi yana taɓa kumatunta ta miƙe bakinta ɗauke da addu'a sai ta yi murmushi ta ce "Thank you da auron wajan bacci"

Zata ɗakko kuɗi cikin jakarta sai taga ya miƙawa mai napep ɗin kuɗi ta ɗan tsaya ta ce "Kabar naka zan ba yar fa" ko kallon ta bai yi ba. Maimakon ya shiga cikin gidan sai ya yi gaba abinsa, bata kula shi ba ta shige cikin gidan, wannan karan tarin yaran da suke zaune a tsakar gidanne suka zaba mata na mujiya sai kuma Malam ta durƙusa ta ce "Ina yini Aby"

"Safiyyerh ko?"

"E, Aby"

"Ke kin zaɓi zama da wannan tantirin yaron ko? Kin zaɓi bijirewa iyayenki saboda wannan yaron da bashi da wata makoma mai kyau ko? Wannan yaron ko kinwa iyayenki adalci kenan yanzu idan ya kashe ki me za ki cewa iyayenki eh?" A hankali Safiyyerh ta ce "In sha Allah Aby ba zai kashe ni ba, in sha Allah" ran Aby ya ɓaci ya ce "Saboda ke nake magana idan don tashi ne wallahi ko a jikina, tashi ki je duk abin da kika jawa iyayenki shikenan ai" ta miƙe jiki a sanyaye ta shiga ɗakin Ammo ta sameta zaune tana ɗaura man ƙuli Sa'adah kuma na yanka alawar madara lokacin bikin Sa'adah saura kwana biyar ciff.

"Barka da gida Ammo, Yaya"

"Sannu Safiyyerh, ya makarantar?" Ammo ta tambaya da kulawa tana ajjiye abin hannunta ta ce "Ki fara yin wanka sai ki yi alwala tunda magariba ya kusa sai kici abinci ko". Safiyyerh ta ce "To Ammo" uniform ɗin ta cire ta saka towel ta saka hijab, sabon soson wanka ta gani an bata da sabulu ta amsa, da ƙyar ta yi wankan a tsaye tsigar jikinta na tashi a haka ta yi ta fito. Sanda ta shiga ɗakin ba kuwa a ciki haka ta sutale kayan jikinta tana shafa mai a jikinta, ganin tana ƙoƙarin cire towel ɗin gabaɗaya ya yi gyara murya, ta juyo da sauri a ƙoƙarin ɗaukan riga sai towel ɗin ya faɗi ƙasa, shi kuma ya ɗago kai ganin ta fasa ƙara tana ƙanƙame jikinta ta rasa inda za ta yi, ko inda take bai sake kallo ba ya mayar da hankalinsa kan alawar madarar da yake kwasa yana dannawa a cikin bakinsa hankali kwance. Ganin ba kulata zai ba ta saki kuka ta ce "Ba zaka tashi ka fita ba, kaya zan saka fa, ni ka tashi" ta ce tana yarfa hannunta.

Ta fara diddire masa ƙafa "Please mana, ka tashi" ta ce silently.

"Bestie"

Ya yi iska da ita, ta sake cewa "Bestie kaya zan saka ka fita"

Ya ɗago kan shi, suna haɗa ido ta rufe idanunta sai ya tsuke fuska ya mayar da kan shi akan bokitin alawar madarar hankali ƙwance.

"Bestie.....,"

"Damn it..!"

Ya ce yana miƙewa, ya yi kamar zai fita sai ya dawo baya idanunsa sun nutsa ciki yana mata wani irin numfashi, harshensa na yin tsartuwa ya dunƙule hannunsa da yake jin kunama na yawo a ciki. Sai kawai ya girgiza kai ya ce "Shhh" numfashinta

na fita da ƙyar bata taɓa jin tsoron shi irin yau ba, sai taga kamar ba shi ba, jikinta ya ɗauki rawa sosai a hankali ta ga ya yi baya yana cillo mata rigar data yar a ƙasa. Ɗauka ta yi ta zura da sauri ko halpvest ɗin bata saka ba, tana gama sakawa ta ɗauki hijjabi ta yar da sallah, har kuma ta idar bai kalle ta ba. Ta juya taga ya juye gurasa irin ta wajan masu balangon nan ta sha romo a faranti, taga hadda nama da kuma awara mai kyau sau turiri da ƙamshi suke yi. Tunda taga ya ɗan kalle ta kaɗan ta san magana yake son yi mata amma kuma bai san ne zai ce ba, sai taga ya share ta ya fara cin gurasar murmushi ta yi ta ƙarasa gabansa tare da tanƙwashe ƙafarta, juyawa ta yi zata ɗauki cokali sai taga babu hannunta ta saka cikin farantin ta fara cin naman.

Suna cikin cin abincin Ammo ta shiga, ta kalle su ta jima tana kallon su musamman yadda Safiyyerh ke ta yi masa hira shi kuma kamar baya wajan, sai ta juya ta bar musu ɗakin kawai. Shi ya fara ɗauke hannunsa ya miƙe ya fice yana fita itama ta fice ta wanke hannunta.

Cikin ɗakin ya dawo ya zauna, Ammo ta ce "An kawo kaya naka ne Muhammad?" Da sauri Safiyyerh ta ce "E, nasa ne"

"Tom".

"Yau zaman gida kake da shi kenan? Ba zaka fita ba?"

"Ammo ki na fita ne?" Cewar Mutallab yana kame fuska

"Ban sani ba don gidanku" ta ce tana miƙewa, saman katifa ya samu ya kwanta yana ware ƙafa ɗaiɗai bacci ya ke ji sosai, yana kwanciya bacci ya ɗauke shi, Safiyyerh ma kusa da shi ta samu ta kwanta, bacci ya ɗauke ta lokacin data gama shigewa jikinsa yayinda shi kuma ya zagaye ta da hannunsa gabaɗaya ba tare daya sani ba, sau biyu Ammo na shigowa tana ganinsu rungume suna bacci ta rasa kunya ke kamata ko mene? Ita dai ba zata jure wannan abin ba, duk da tana da yaƙinin basu gama sanin mene auren ba yanzu. A dawowa ta uku kuma sai taga gabaɗaya Safiyyerh ta haye ruwan cikin Mutallab tana bacci hankali kwance ta ƙanƙamesa kamar ta samu filo cikin sauri ta saki labulen ta fita.

*

Switzerland/ Bern

Yanayin ƙasar tana matakin hadari ne, sama-sama mizanin saukar ruwan sama 5% sai laimar iska 93% daIska km/s 6 sai hakan ya saka gabaɗaya yanakin ɗaukan wani irin sanyi mai rasa jiki da ƙasasuwan mutane, kowa ka gani da rigar sanyi jikinsa da kuma takalmi babba snow nata sauka a jikin mutane da kyau kamar yayyafin ruwan sama domin ita ke sauka madadin ruwan da ake saka ran samu a yau ɗin.

A cikin haɗaɗɗan gidan ma hakanne, sai ya zama gidan shiru kamar ba kowa. A hankali ya murɗa handle ɗin ƙofar ɗakin da hannunsa da yake cikin safa ya shiga, idanunsa ya dinga rarrabawa ta cikin baƙin glasses ɗin daya saka, gano ta ya yi tsakiyar gadon da rufe jikinta sosai tana bacci peacefully. A hankali ya ƙarasa ya tsaya sai kuma ya nemi waje ya zauna ya saka hannunsa mai ɗan sauran sanyi duk da safar hannun ya zame duvet ɗin data rufe kanta da shi, ko ya ce aka rufe mata. Farar fuskarta ta bayyana, ya zuba mata ido ta yi wata ramewa ta ban mamaki, ya sake haske sai siririn hancinta da ya sake yin tsayi ƙwarai, hannunta ɗaya cikin bakinta ta ƙanƙame teddy ɗin dake kusa da ita, ga azkar ɗin dake kuma gefe, ya miƙa hannunsa ya kama hannunta ya riƙe cikin nasa, ya jima zaune sai kuma ya tashi ya fice daga cikin ɗakin gabaɗaya yana rufe ƙofar without making any sounds.

Bayan wasu mintuna aka sake buɗe ƙofar tare da shigowa, daidai nan itama ta buɗe idanunta da ƙyar suka haɗa ido da Mj ya yi mata murmushi ya ce "bacci daɗi favourite" ta ɗan ɓata fuska sai ta ce "He is here?"

"Yes, he is here, but he already lefted" ta yi shiru kawai tana mirginawa gefe. Mj ya nemi waje ya zauna ya ce "Ya kika sani?"

"Me fa?"

"Yazo"

"Kamarya?"

Ya watsa mata harara ya ce "Aafiyyah ki rage tunanin nan please kin ji, tunda Paaah ya yanke hukunci shikenan babu sauyi kin sani, ki yi addu'a idan akwai rabo sai kiga komai ya zama labari da tarihi ko?"

"Labari? Tarihi?" Aafiyyah repeat the words tana kallon Mj tana kame fuska sosai ba wasa.

"Yes mana, Aafiyyah amma kina da tabbacin Safiyyerh zata bawa yaron wasiƙun nan?" Mj ya tambaya yana kama hannun Aafiyyah ya riƙe cikin nasa, a hankali ta langwaɓe a jikinsa tana jan numfashi, tunda suka zo ƙasar aka je asibiti da ita, bata san meke faruwa ba, da zuwan da komai sai farfaɗuwa ta yi taga ana maƙala mata jini a jika, satinta uku kuma aka sallame ta zuwa dawo gidan Paaah da yake ƙasar. Bata taɓa fita ba, ko parlo bata fita kodayaushe tana ɗakin al'amarin kuma daya damu duka yʻan gidan kenan, sun san Aafiyyah bata barin kowa ya zauna lafiya ko ba zata kula mutum ba sai ta yi tsokana ta nemi faɗa ga tsinannen bada labari kamar yʻar jarida.

A hankali ta ce "Yaya, i trust Safiyyerh zata bashi in sha Allah" ta ce ƙirjinta na ɗagawa da ƙarfi sai kuma ta kalli Mj kamar za ta yi magana tai shiru.

Mj ya ce "Allah ya sa, at least da wayarta ya shiga shine kuma kinga an sauya miki sim an yi deleting komai, i am sorry Aafiyyah, ki fahimci Paaah"

"He is my father, my father yana da iko dani ko ka manta?"

"Ban manta ba, ina tsoran ki furta kina son abu, na san yadda kike son Mutallab, na sani Aafiyyah,na ji ban kyauta ba da na yi supporting naki wajan faɗa masa a wajan karan amma na hana ki, it's all my fault, fault ɗina ne Aafiyyah, laifi na ne" shasshekar kuka ta fara tana girgiza kanta

Mj ya ce yana matse hannunta, ƙara shigewa jikinsa ta yi kamar mage hawayenta na sauka a jikinsa sosai ta ce "But they promised me, sun mini alƙawari yaya, sun mini yanzu me ya saka suka karya al'ƙawarin nasu? They break the promises"

"Sun miki alƙawari tabbas, kin cika naki al'ƙawarin tabbas, kin kuma yi biyayya tabbas, ban san ya aka yi reshe ya juye ba"

"Kamarya?"

"I don't know, amma dai yanzu tunanin Paaah na amincewa da Mutallab bana karatunki bane, ya sauya shawara you can ask him "

Aafiyyah ta yi cak, tana kallon Mj idanunta ya yi jajur ƙirjinta na bugawa da ƙyar take fusgar numfashi, ta ji iskar wajan na neman yi mata kaɗan a hankali kuma ta fara tuna ranar data ganshi, ranar da ta yi wa zuciyarta alƙawari, ranar da Paaah ya yi mata alƙawari, ranar data ji ta fara rayuwa domin shi, ranar data ƙara samun ƙwarin zuciya da confidence ɗin yin karatu domin ta same shi as her husband,domin ta rayuwa da MUTALLAB. Ranar asabar ce na fito da sauri jikina sanye da blue black ɗin abaya cikin sauri kamar zan faɗi, ina tafe ina faɗin "Yaya zan ranka ka please, ina son siyan chocolates a hanya,kaga da muka dawo ban fita ko'ina ba, please yaya" a hankali naga ya juyo ya kalle ni sai ya mini alama nazo, ina ƙoƙarin shiga motar Yaya Mj sai motarsa ta shigo ya fito cikin sauri, wata uwar harara ya doka mini da sauri na ɗauke kaina a raina ina faɗin ya ci kansa, na shiga gaban motar Mj ya ja. A lokacin sai na ji i feels comfortable na ji zuciyata wasai na ɗauki wayata na dinga yin bidiyo a hanya ina yi wa yaya Mj gwalo, sai ya yi mini murmushi.

"Oh Allah" na ce daidai lokacin da muka tsaya a danja, sai dai me tsayuwar tamu ya yi daidai da ƙarin gudun zuciyata, irin gudun da take mini a duk sanda zan haɗu da abin alheri ko na tsiya, na lumshe idanuwana ina shaƙar iskar ƙasata Nigeria da na yi missed nata, buɗe idanun da zan yi na buɗe akan ƙaddarata, when my destiny started, i saw him, i just saw him da wasu kaya a jikinsa duk datti da gajeren wando hannayensa ɗauke da bulo, yana ɗauka daga right side zuwa left side. "My future husband" na ce a fili ina binsa da wani irin kallo, kamar ban taɓa ganin wata halitta ba a lokacin sai shi.

"Who?" Mj ya tambaye ni, ba tare dana ɗauke idanuna ba na ce "Gashi can yaya, ɗan matsa na yi masa bidiyo na ajjiye" ya zame kafaɗarsa ya bani damar zura wayata na dinga masa bidiyo, ina murmushi ina kallon shi ina cewa "Aafiyyah's

husband, til-janna, ina son shi yaya, ina son shi i love him" na ce soundly da wani irin farinciki a fuskata a lokacin.

Mj ya dube ni sai naga ya juya yana kallon shi ya ce "Waye mijin naki? Yaushe kuma aka ɗaura?"

I see the tsokana in his eyes, na gano tsokana a cikin idanun Yaya mj, but i don't think cewa tsokanar ta gaskiya ce. Sai na ce "Yes, zai zama mijin Aafiyyah wallahi ina son shi, za ku aura masa ni?"

"Ask Paaah first, ki tambayi Paaah ki ji" na ɗaga kafaɗa na ce "Zan iya" daga nan na fara ƙoƙarin buɗe ƙofa, trying to out of the car, sai Mj ya yi saurin sakawa motar key ya ce mini "Ina za ki Aafiyyah?" Ina yarfa hannuna na ce "Wajan shi, Yaya zani gunsa ne don Allah" sai kawai ya ja motar ya yi gaba, ganin da gaske ƙoƙarin fita nake son yi, a lokacin na ji zafin Mj na ji kamar kuma zuciyata ta buɗe ne, na ji wani irin damuwa a cikin raina sai na fara tunanin ta ina zan sake ganinsa? I don't know, ban sani ba, san ina zan sake ganin Blackman ba. Sai na fara kuka hakan ya saka naƙi siyan chocolates ɗin har muka koma gida. Was the first abin da na fara zuwa wajan Paaah a lokacin kuma ya dawi gida, na same shi zaune akan kujera yana duba jarida cikin jin daɗi na ƙarasa na ce "My Paaah, my handsome father, the great and greatness father, good evening "

"My talkative and smartness daughter in the world" Ya ce yana mini wani irin murmushi cike da soyayya. Muka rungume juna, sai kuma na yi shiru na ji abin da zan faɗa kamar ya yi girma, sai kuma na tuna Paaah ya ce mini shi ɗin abokina ne dukkan matsalata aboki ake faɗawa, sai na gyara zama na shirya faɗa masa cewa naga mijin aure.

"Ya aka yi kuma? Wannan bakin gulma ya ɗakko mini ko hira?"

"Dad, i love him"

"Who? Waye? Wa kike so?" Na ji ya tambaya a yanayi na ruɗewa, domin i can see the fear in his face. Na ce "Daddy, wani na gani kuma ina da tabbacin zaka yarda,

kai abokina ne, na gani wani ina so daddy, shi nake son aura, shi nake so ka aura mini don Allah, don Allah, don Allah" na faɗa ina haɗa hannaye biyu wajan yi masa magiya. Paaah ya zubawa Aafiyyah zuciyarsa na tsananta faɗuwa, shekarar Aafiyyah nawa a duniya har ta san aure? Wanne irin girma ne haka, a hankali kuma yanayinsa ya fara sauyawa sai naga ya yi mini murmushi ya ce "Waye wannan kuma?"

"Ban san shi ba, ban kuma san sunansa ba, ban san inda zan ganshi ba, ina da tabbacin zan sake ganinsa in sha Allah"

"Accepting, na amsa amma da sharaɗi biyu zuwa uku"

"Na amince daddy, idan zaka mini al'ƙawarin aura mini shi"

"Kar ki kuskura ki faɗa masa kina son shi, babu kyau haramun ne a cikin addinin musulunci yarinya ƙarama ta ce tana son namiji sai ta girma, kuma Allah yana yin azaba ga duk wanda ya yi hakan, ni da kaina zan aura miki shi idan lokacin ya yi, kawai ki san waye shi ok? Na biyu ki mayar da hankali a karatunki, ki nutsu kar ki sake mini zancen shi sai ranar da kika kammala secondary school ok? Idan kika mini wannan alfarmar to kin cinye zan kuma aura miki shi, yanzu karatunki nake buƙata fiye da komai ina da buri akan karatunki?" Sai na ji daɗi duk da ina fargabar ina zan sake ganinsa? "Daddy ina son zama kamar ka ai"

"Da gaske?"

"In sha Allah, kuma na maka al'ƙawari" ya jinjina mini kai ya ce "Za ki zama kamar ni ɗin, tabbas za ki zama darling"

Na miƙe na fita, a daren na kasa bacci burina na faɗawa Safiyyerh na yi saurayi, mijin aure naga wanda nake so, sai na tuna Safiyyerh bata da waya, kuma bani da number Ummeyh dole na yi haƙuri. Juyi kaɗan kuma shi nake gani cikin idanuna. Washegari weekend na shirya zuwa Fgc, babban abin da ya bani mamaki ganin abokina kimiyya tare da wanda zuciyata ke bugawa a yanzu domin shi, na yi

yunƙurin masa magana sai na zubawa yanayinsa ido, nan take na gano waye shi, sai na share maybe shariyata zata janyo attention nasa zuwa kai na.

"Kimiyya waye wannan?"

"Muhammad Mutallab Abdullahi"

"Uhmm, bani labarinsa"

"Me ya sa?"

"Ina son shi, na faɗawa Paaah, Mj ya sani amma kar ka faɗa masa, zan sanar masa da kaina, alƙawari na yi wa Paaah ba zan masa magana ba, kaga idan ina son gamawa da duniya dole na bi umarnin daddy. Amma zuciyata zafi take a yanzu, na ji ina son masa magana wallahi ina son shi"

"Sunansa Mutallab a nan unguwar Birget yake, mahaifinsa kuma shine mai makarantar almajirai sunansa Malam Abdullahi. Mutallab an taɓa yunƙurin yi masa aure amma Allah bai yi ba, yʻan matan na mutuwa Diyna da Jaanah, kuma ya taɓa shiga state cid da laifin sata, wannan makarantar da kike gani Jeddah ce ga saka shi, rayuwarku ba zata yi ɗaya data Mutallab Aafiyyah "

"Shi ba mutum bane?" I ask Kimiyya. Ya ce mini "Tsarinku ne ba ɗaya ba, kuma mahafinki ba zai amince ba Aafiyyah"

"Uhmm, Kimiyya kenan na faɗa maka dai, kar ka faɗa masa ina ta neman Safiyyerh saboda na mata albishir sai na tuna bata da waya. Ganin Mutallab na neman zuwa wajan namu na yi sauri na bar wajan zuciyata na rawa da yadda naga fuskarsa a cunkushe da sauri na faɗa mota. Tun daga ranar kullum da tunaninsa nake kwana nake yi ne, na ji ba wanda nake tausayi a duniya sai shi, na fara saka shi cikin jerin wanda nakewa addu'ina. Ranar da Safiyyerh ke faɗa mini ta faɗa soyayya sai na yi tunanin ko Captain take nufi? Na buƙaci ta faɗa mini taƙi, sai na share domin ta saba yi mini irin haka, na yi yunƙurin faɗa mata cewa nima ina son wani sai Paaah

ya buɗe ƙofa ya shigo hakan ya tilasta mini cewa “I will tell you something” sanda na faɗawa Safiyyerh da dukkan yarda ta na faɗa mata, kuma na ji sauƙin zuciyata daman na riga na jima da iya rubutun Safiyyerh.

Sai na fara yi masa wasiƙun da Safiyyerh's handwriting. Ina son karatun English novels hakan ya saka na iya wasu abubuwa da yawa, kuma ina jin yadda Ummi ke yawan yi wa Paaah addu'a sai na yi addition addu'a ta akan Mutallab a cikin wasiƙun.

Duk wata exam da zan yi ina yini da tunanin ina gamawa zan cika muradin Paaah, bana gazawa na amince yin karatun shine zai bani damar amsa sunan matar Mutallab. Sanda na ji Safiyyerh na cewa bestie ko a jikina domin na yarda da ita, kuma na ji zata iya mu'amala da Mutallab ba wani abune, tsoro ne ya kama ni don ba zan manta cafeteria ba sanda take cewa what if I tell you I love you? Na hango soyayyar Mutallab a cikin idanun Safiyyerh. Fargaba ta kama ni na fara saka tunani wanda ya haifar mini da ciwo, naƙi faɗawa kowa dalilin wannan ciwon domin na yi alƙawarin ba zan sake maganar Mutallab a wajan Paaah ba amma Yaya Mj ya san komai, na fara saka shade glasses domin kallon Mutallab is my favourite thing.

What a blind love!

"Aafiyyah" na firgigit ta dawo cikin hayyacitaa da sauri ta hantsila ta sakko duk da jikinta ba ƙwari, idanunta rufe ruf. Tun daga cikin ɗaki take kiran sunan Paaah har ta isa cikin bedroom ɗinsa.

"Aafiyyah"

"Ummi, ina daddy"

"Gani, ya aka yi ne?"

Cikin sauri Aafiyyah ta zube a gaban Paaah tana riƙe ƙafafuwansa ta ce "Paaah ka mini al'ƙawarin aura mini Mutallab, daddy na yi maka al'ƙawarin yin karatu, ka

ɗauke ni daga ƙasar ba tare dana faɗa masa ina son shi ba, daddy ka ce yanzu ba zan koma ƙasar ba, zuciyata daddy, daddy zuciyata ina son Mutallab Ka mini al'ƙawari kar ku karya, kamar yadda nima ban saɓa sharuɗan daddy ba" Aafiyyah ta faɗa tana sakin wani irin kuka tare da riƙe ƙafar Paaah.

"Ummi ba har dake a yi mini al'ƙawarin ba? Don Allah ku mayar dani Naija, ina son komawa Nigeria don Allah "

A hankali Paaah ya ajjiye jaridar hannunsa, ya juya ya kalli Aafiyyah sai kuma ya ce "Yes, i promised you, e, na miki al'ƙawari zan aura miki shi, amma na sauya al'ƙawarina a ranar dana fahimci kin yi zurfi a soyayyarsa, ban san waye shi ba,ko sunansa ban riƙe ba, ban kuma taɓa ganinsa ba, talaka ne mai kuɗi ne yaya yake i don't know, i really really don't know. Buɗe kunnenki da kyau Aafiyyah, kina da mijin aure, kina da wanda za ki aura, ki cire wannan yaron a ranki, ki daina wani mafarkin da kike na soyayyarsa..." Ya miƙe tsaye, Aafiyyah ta tsaya da kukan cak da ƙyar ta ce "Me ya sa?"

"Saboda na yi miki mijin aure tun kina zanin goyo, kina yi al'ƙawarin bada auren ki, kina da wanda za ki aura, not him...

Akwai update a arewa bayan page ɗin nan keep reading and following.

[1/7, 9:36 PM] Sis Fauzy: Chapter 41: No Options

Gaban Aafiyyah ya tsananta faɗuwa ta dinga kallon Paaah da yake cewa "Ba zan aura miki shi ba, ba shi nake da ra'ayin ki aura ba kin ji ko?" Ta jinjina kai kawai ta kasa cewa komai sai ajjiyar zuciya da take saukewa.

"Kar kuma ki ji kamar auren dole ne, bana dole bane, za ki so ɗayan ma, kamar yadda kike son wannan" Paaah ya ce yana kallon Aafiyyah sai kuma ya nemi waje

ya zauna tare da harɗe ƙafafuwansa waje guda ya cigaba da kallon Aafiyyah kafin ya ce.

"Safiyyerh!"

Aafiyyah, ta kasa amsawa sai kanta data ɗago ta zubawa Paaah jajayen idanunta da suke buɗewa da ƙyar. Ya ja numfashi ya ce "Buɗe bakinki ki amsa ni Safiyyerh, buɗe baki ki yi mini magana domin na tabbatar da abin da nake faɗa miki ko kina fahimta ok?" A hankali ta ce "Na'am, ina ji daddy" Ummi ta zauna, Mj ya nemi waje ya tsaya yana mai jin tausayin Aafiyyah a cikin ransa, domin an gama saka mata rai, an yi mata al'ƙawari.

Paaah ya ce "Safiyyerh, nagartattun yara sune masu bin umarnin iyayensu, kuma baza su taɓa taɓewa ba idan sun yi biyayya. Ina da wanda na zaɓa miki a matsayin mijin aure, ba dan wancan da kike so ba cancanta ba, ba kuma don bashi da nagartar da zan iya ɗaukan ki na bashi bane, da ace ban yi al'ƙawari akan ki ba, wallahi wallahi wallahi Allah kenan a yau zan koma Nigeria na nema miki auren shi, ko halin riƙe ki ne bashi da shi ni mai iya yi masa komai ne, wanda zai riƙe maka yarinya har tsayin rayuwa ai ba abin wulaƙanta wa bane. Kar ki ji a ranki ko wani dalili ne, a'a, sunan auren ki AL'ƘAWARIN AURE. kuma in sha Allah mutuwa ce kawai zata hana hakan faruwa"

Ya yi shiru yana fahimtar Aafiyyah, sai ya ɗora da "Daman kuma ita yarinya budurwa ba ita ke da hakƙin zaɓawa kan ta mijin aure ba, yau da ke bazawara ce to ba ruwan kallo da gajiya, Safiyyerh kina da miji, idan yanzu ma kika ji kina son auren in sha Allah a satin nan zan miki shi, domin da wata matsalar gwara wata, ke yarinyar kirki ce na san za ki fahimce ni ba zan cutar dake ko cutar da rayuwarki ba"

Kai ta fara girgizawa ta riƙe ƙafafuwansa da kyau ta ce "Na roƙe ka don Allah, kar ka mini auren dole Paaah, kar ka haɗa ni da wanda bana so, an ce mace na iya mutuwa ko ta kashe mijin idan aka yi mata auren dole, Paaah kai ka mini al'ƙawari, ka nanata mini, na yi yadda kake so, na jure kar ka zo mini da wata buƙata ta auren wanin Mutallab don Allah Paaah, don Allah...," ta kasa cigaba da maganar sai ta ɗora kanta a saman cinyar Paaah tana shassheƙar kuka.

"Don't do this to me"

Ta ce very slowly. Mj ya ce "Paaah don Allah, ka janye maganar nan"

"Get out my friend"

Paaah ya cewa Mj yana nuna masa hanyar waje fuska a kame babu alamar wasa, Ummi ta buɗe baki za ta yi magana nan ma ya yi mata alamar ta yi masa shiru. Aafiyyah ta dinga rusawa Paaah kuka da birgima kar a yi mata auren dole, fuskarta ta yi jajur ya tanƙwashe ƙafafuwansa yana kallon ta kawai, idan tashin hankali ne irin wannan ai ya saba gani wajan Aafiyyah, kuma ya san at the end dole za ta yi haƙuri ta bar maganar yana da wannan tabbacin. Sai data gama kukan ta yi bacci saman carpet ɗin parlon Paaah daman kuma ba wani kuzari gare ta ba, ya miƙe a hankali ya ƙarasa wajanta yana duƙawa ya ɗauke ta, kai tsaye bedroom ɗinta ya shige da ita. A hankali ya kwantar da ita saman bed yana gyara mata kwanciya da rufe ta da duvet.

"I am sorry Safiyyerh" ya ce a nutse domin ya san ya yi mata laifin, ya yi wasa da tunaninta tun farko, wataƙila da ya ce mata tana da wanda zata aura a sanda dazo masa da tata buƙatar da tuni ta mance da wannan babin.

"Ki yi mini afuwa, ki wa mahafinki afuwa, ki fahimci mahaifinki Safiyyerh. Stay strong my darling" ya ce yana shafa kanta sai kuma ya fara mata addu'a kamar kodayaushe idan tana bacci bayan ya kammala ya miƙe ya fice daga cikin ɗakin.

Mj ya samu Paaah a ɗakin hutawa, kallo ɗaya kuma Paaah ya yi wa Mj ya ce "Idan akan batun Safiyyerh ne kar ka mini magana"

"Paaah, dole zan maka don Allah, ka saurare ni"

"To Ubana"

"A'a ka yi haƙuri, ba haka nake nufi ba wallahi"

"Ok, ya kake nufi Mj?"

"Paaah, Aafiyyah yarinya ce mai saukin kai duk da rigimarta da karaɗinta da iyayinta, tana da faɗa na sani kuma tana da haƙuri, duk wanda zai san haƙurinta to baya na zai bi. Tun tana ƙarama ake raba faɗa da ita, domin bata yarda aci zalinta kuma bata yarda taci zalin wani, amma ana ce ta yi haƙuri an gama. Amma tana da ƙulafuci da saka abu a rai, ban san me wannan zai haifar ba".

"Ok, kana tunanin shawarar dana yanke zai haifar da wani abu ne?"

"A'a, alheri kawai nake hangowa Dad. Amma wannan zamanin da muke ciki an daina auren dole saboda fitun-tun da hakan ke haifar wa, ana shiga haƙƙin yara ne kuma kasan auren yanzu da soyayya ma yaya aka ƙare balle wanda iyaye suka ƙulla? Sau nawa ana bada labarin an yi wa yarinya auren dole ta kashe mijin da abokansa, ko ta kashe kanta, ko ta fara yawon bin maza. Astagafirulla; ba haka muke fata ba, lokaci bai bar komai ba, zamaninku daban na yanzu daban don Allah Paaah ka janye, a bar Aafiyyah ta yi karatun kamar yadda aka yi al'ƙawari ta koma ta auri wancan yaron shikenan"

"Ina Mj"

"See me here Paaahh "

"Wannan maganar mu bar ta iya nan, koda wasa na ji kuma ka yi hanya ko zama sanadin haɗuwar Aafiyyah da yaron zaka gane cewa ni ne ubanka kuma nine na kawo ka duniya. Kuma daga yau ka zama idanunta, ka ajjiye tunaninka a kan ta, motsinta da duk abin da take yi duk da na yi yaƙinin ba zata bijirewa umarnina ba, amma she is smart girl, bana son maganar ta yi tsayi"

"Yadda ka ce haka za'a yi ranka ya daɗe, Allah Ya ƙara girma"

"You can leave"

A daddafe Aafiyyah ta yi baccin mai cike da wahala, da wani irin mafarki mai ban tsoro, tun kuma daga sanda ta farka wani abu ya tsaya mata a maƙoshi, ga wan irin ciwon kai daya saukar mata mai tsananin zafi da ƙyar take buɗe idanunta. A hankali ta sakko daga kan gadon tana dafe bango, ruwan zafi ta haɗa ta yi wanka tare da yin brush saboda bakinta babu daɗi, tana gamawa ta ɗauki alimon ta shafa a jikinta kamar yadda Ummi ta nuna mata saboda tsane jiki da kare kai daga tashin wari saboda shigowar lokacin girma daya gama bayyana muraren a tattare da Aafiyyah ɗin. Sallar issha ta yi, sai ta samu kan ta da yin addu'a, addu'ar zaɓin alheri tsakaninta da Mutallab, da kuma wanda Paaah ya zaɓa mata a matsayin wanda zata aura ɗin. Babban tashin hankalin Aafiyyah bai shige yadda bata san waye zata aura ba, ita tana da kalar zaɓin ba kowanne namiji ne zai iya zama kalar ta ba, zaɓin ta ba, ba kuma kowanne namiji ne zai iya zama test ɗin ta ba.

Ummi ce ta buɗe ƙofa ta shigo, da sauri Aafiyyah ta yi murmushi tana sakin fuskarta kamar ba ita ba, Ummi ta nemi waje ta zauna tana duban ta kafin ta ce "Ki fito ki yi dinner, sai na rasa zaman da kike cikin ɗaki kwana biyu"

"Bana jin yunwa"

"Me kika ci"

"Kawai, na ji i am ok"

"Safiyyerh"

"Na'am Ummi" Aafiyyah ta amsa, tana jingina da jikin gadon idanunta rufe tana jin yadda ake mata ihu a cikin ƙwaƙwalwarta. A tausashe Ummi ta ce "Wallahi ba za ki taɓa wulaƙanta ba a wajan yi wa iyaye biyayya, ki ci-gaba ki jure ai ke jaruma ce, ki yi ta addu'a dare ta rana Allah ne kaɗai ya san wanda zai zama mijinki"

"Ummi ku ne kukai mini al'ƙawari fa? Me ya sa tun farko ba'a faɗa mini gaskiya ba? Ai kun san kuna da hakƙi akai na, wajibi ne a matsayina na ɗiya a wajanku na sauke hakƙin iyayena. Da ba ku yi mini al'ƙawari ba, kun san yadda duk maganarku ke zama hadda a cikin tunanina bana wasa da kowanne furucinku, i trust you, me ya sa Ummi?" A hankali Ummi ta ce "Saboda mun san mun isa dake ne, shine kawai" murmushi Aafiyyah ta yi, tana goge idanunta ta ce "You are right, kin yi gaskiya ni ikon ku ce ai, na amince da zaɓin Paaah, na amince" ta ce a hankali tana jin ƙofofin zuriyarta na tushe kansu da kansu ta rasa iskar shaƙa ko kaɗan ta rasa kuma yadda za ta yi ta daina jin zafi a cikin ƙirjinta.

"Da gaske kin amince da zaɓin mahafinki?"

"E, na yarda"

Ummi ta ɗago Aafiyyah ta rungumeta a ƙirji tana ta mata addu'a, sai Aafiyyah ta kyalkyale da dariya ta ce "Ke uwa ce, you are the best mom ever Ummi"

"Ma sha Allah, Allah Ya yi miki Albarka ya shiga cikin lamuranki"

"Amin"

Ummi ta jima tana yi wa Aafiyyah hira kana ta miƙe ta fita, tana fita Aafiyyah ta sulale ƙafa tare da durƙushewa ta saki wani irin gunjin kuka tana fige hijjabin jikinta tare da farke gaban rigarta, ji take kamar kayan jikinta ne suka hanata shaƙar iska yadda ya kamata, bata san cewa gabaɗaya zuciyarta ta ce a cunkushe kuma a ƙuntacce ba, duk yadda Aafiyyah taso amincewa tare da kawar da batun Paaah kuma ta yi accepting amma zuciyarta taƙi bata damar hakan, tunaninta ya tsaya ƙwaƙwalwata ta yi hooking ta daina fahimtar komai. Ta yi shiru tana zubawa wani waje idanu, sai kuma ta zabura ta ɗauki wayarta tare da shiga wani waje data ɓoye pictures, bidiyon data fara yi masa a ranar data fara ganinsa ta shiga ta fara gani, sai murmushi ya suɓuce mata ta dinga kallon bidiyon tana murmushi da hawaye at the same time. Sai ta harare shi kamar yana gabanta ta ce "Ka dinga fushi dani for no reason, kana fushi dani ni, ni ko?" Ta tambayi bidiyon tana nuna kanta, sai ta yi baya ta zauna zaman dirshen a hankali kuma ta shiga ɗaya picture ɗin ranar da ta yi masa shi da Safiyyerh suna zaune, ya jingina da jikin bishiya ya kafe Safiyyerh da kallo fuskarsa ba walwala sai lips ɗinsa da sukai jajur, Aafiyyah ta yi zooming

photon ta saka yatsa ta shafi fuskarsa tana murmushi ta ce "Stay strong my, kar ka manta ni ko sauya, ko a dramar da mukai ne kar ka manta ni don Allah" sai ta sake shafa fuskar ta ce

"Na san kana so na" sai kuma ta yi shiru ta ce "Zaka kira ni? Ka kira ni don Allah zan ta jiran kiran ka, a sanda Safiyyerh ta faɗa maka saƙona a sannan zaka fara nemana ido rufe" Aafiyyah ta kwaɓe fuska ta ce "Amma ina jin tsoron haɗuwa da kai, kuma ina son ganinka ka zo mini a mafarki ka ji? Za ka zo?" Ta tambayi photon Mutallab kamar yana gabanta. Haka ta wanzu ta ce Wannan ta ce wancan.

"Ya Allah make it easy for me, for him Allah ka sadani da shi a duniya kafin na koma gare ka" ta ƙanƙame jikinta waje guda, sai yau dinga jin wani iri a lokaci na farko, ta rufe idanunta kamar a lokacin yake kissing lips ɗinta. Bata taɓa tunanin tana jin tsoron wani abu a rayuwa ba, irin yadda take jin tsoron ganin cikin ƙwayar idanunsa, a duk sanda zata kalle shi ta cikin glasses ɗinta, tana hango wutar faɗa sosai a cikin jirkitattun idanun nasa, tana hango kamar yana mata kallon mai laifi, kallon jin haushi, abu ɗaya ne ke mata daɗi idan ta hango abu mai sanyin a cikin idanun nasa. "Innalillahi, i love him so much, i love you so much Tayo, i love you today, tomorrow and always forever. Allah Ya tsare ka ya kare ka, ko aure ka tashi yi ka auri Safiyyerh kafin na zo gare ka, don Allah ka neme ni, ka ji ɗan baƙin Muɗallabina? Ka ji masoyi"

Har dare ya raba tana zaune. Sai dai har aka yi kiran farko na asuba idanunta ko motsi bai yi ba da zummar yin bacci, bata ma jin baccin kuma tana jin daɗin zama ita ɗaya, sai ta ji bata son ganin kowa da komai, ta ji kamar sabuwar duniya akai mata ita ɗaya wacce zata dinga rayuwa a cikinta, sai kuma ta dinga hira ita ɗaya ko ta dinga jin kamar ana kiran sunanta.

*

Yamma ce lis amma a haka ya kammala abin da yake yi ya nufo gida, fuskarsa a kame kamar wani babban mutum a kodayaushe tunda ya jima gina kan shi akan cewa ya kai munzalin kowanne namiji da yake kawai. Yana yi yana sosai tsakiyar goshinsa a haka ya tsallake almajiran da suke faman karatu ya shigo cikin gidan, shi shaf ya manta da wani bikin Sa'adah da ake shirin yi a kwanakin nan. "Ya zaka dinga faɗo mana babu sallama ne? Ni sam banga ma'anar da zaka dinga zarya a tsakaninmu ba tunda ka mallaki hankalinka ka tunda har mata ka mallaka" Inna

Binta ta faɗa cike da masifa da kumfar baki. Bai kulata ba ya tsallake ya shige ɗakin Ammo yana ajjiye ledar dake hannunsa.

Sai Mama Zaituna ta yi shewa ta ce "Wannan fanɗararren yaron ne kike tunanin zai mana sallama? Dama dai ba jinin yarabawa bane" ta ce tana miƙewa.

"Ko jinin waye shi ta shafa kuma zan ɗauki mataki a kan shi wallahi idan gidan ubansa ne ni kuma gidan mijina ne ehhe" Inna Binta ta bada raddi.

Sai kuma Mama Zaituna ta girgiza kai kawai kamar za ta yi shiru sai kuma ta ce "Kee iya bakinki ɗan masu gida ne, kada kuma ki saka ya miki kiranye ki zura da gudu har haɗeja wallahi"

Mutallab na jinsu ya yi shiru domin ya lura Ammo da Sa'adah bata nan. Yana shiga ɗakin suka haɗa idanu da sauri ta sunkuyar da kanta idanunta ya yi jajur alamar ta ci kuka, bai kula ta ba ya tsaya daga tsayen Safiyyerh ta miƙe tana murmushi domin wata jarrabawa data faɗa data ganshi dukkan wani damuwarta ke yayewa ta ce "Shine sai yanzu zaka dawo? Babu daɗi gidan" ta ce tana ƙarasawa inda yake sai kuma ta yi sauri ta ce "yen yen ƙazami warin dauɗa kake yi, sai gumi kake haɗawa bestie ƙazami"

Ya yi mitsi-mitsi da idanunsa ta ce "ba zan taɓa ka ba, kar ka shafa mini dauɗa, dama Ammo ta ji ƙan ka ta yi maka wanka yau"

Ya zuba mata idanu, sai ya cije lips ɗinsa ya fara takawa zuwa cikin ɗakin ita kuma ta yi baya tana cewa "Mai dawa ya zama ƙazami, mijin Safiyyerh mai warin dauɗa" idanunta ya faka ya damƙo ta, tare da janyo ta kusa da shi idanunsa da suka ƙanƙance a kanta da ƙyar ya ce "Kika ce me?" Sai ta fara inda-inda tana ƙifta idanunta sosai ta ce "Ba magana na yi bafa, don Allah ka je ka yi wanka sai ka dawo mu yi fira ko?"

"Ƙazami ne ni?" Ya faɗa a daƙile yana jin muryarsa a ƙirjinsa saboda yadda furucin ya fito kamar an masa dole. Ta girgiza kai kai ta ce "Yaushe na ce haka?"

"Ni kike cewa ƙazami?"

"Ka yi haƙuri to"

"Ni ne ƙazami? Kwaɗo kike so na zama? Na dinga rayuwa a cikin ruwa ƙarewar wanka ko"

Ta tura masa bakinta tana kawar da kai gefe ta ce "Ai wanka cikon imani ne, don na ce ka yi wanka bai zama haramci ba ai" ta ce a shagwaɓe tana sake matsawa baya, ganin yadda yake nishi da numfashi a gaggauce yana sake matsawa inda take yaƙi ce mata komai kuma.

fuskarta ya dinga bi da kallo, da ɗan mitsitsin bakinta da laɓɓanta da suke motsawa. A sama ta ji maganarsa ya ce "Zo ki mini wankan, yau sai kin mini wanka"

"Wallahi ba zan iya ba"

"Hmmm" ya ce kawai yana cire rigar jikinsa ya yar a tsakiyar tsakar ɗakin, ta yi saurin rufe idanunta, sai kuma ta buɗe su da ƙyar saboda ganin suma ƙwance a ƙirjinsa baƙa suɗik. "Don Allah na zuba maka ruwanka, ka je ka yi "

"Wari nake ko?"

Ta girgiza kai ta ce "Ni ban ce ba"

"Kin ce mana, ko dai ki mini wankan nan, ko na kashe ki da warin, ke ko na yi niyyar yin wankan ba zan ba" ya yi maganar yana sake tunkaro ta. Safiyyerh ta ce "Haba mana, idan ka kashe ni kuma yaya kenan? Ni dai don Allah na zuba maka ruwa ka yi?"

"Nawa za ki biya na yi?"

"Sai na baka kuɗi"

Ya ɗaɗɗage girarsa biyun da suke a cunkushe, sai ya yi baya ya kwanta a kan katifa alamar bashi da niyyar yin wankan. "To yanzu idan na baka kuɗi za ka yi?" Ya jinjina kai ba tare daya kalleta ba, ita dai haka kawai yau ta ji tana jin shakkarsa. Ta je cikin kayanta kuɗin da bai san dasu ba ta ɗakko dubu ɗaya ta ce "To gashi a yi mini wankan dubu ɗaya, daga jeji kake fa ƙila wata dabbar ka farauta shine zaka kwanta haka?" Yana daga kwancan ya mirgina idanunsa suka nutsa ya miƙa mata hannu alamar ta bashi kuɗin, cikin rashin sanin dabara ya yi mata sai ta matsa daga tsayen ta miƙa masa kuɗin ta ce "Yawwa gwanin na iya mijina" maimakon ya amshi kuɗin sai ya cafko hannunta ya cillota kan shi, ya mirgina ƙasa ya danne ta yana sakar mata nauyi, Surayyerh ta runtse idanunta tana jin warin rana na dukanta cikinta na juyawa tana nishi ta ce "ƙirjina, cikina, cikina" ya sake danne ta ya ce "Wa kike cewa ƙazami?"

"Da kaina nake"

"Kan naki na waye?"

Ta yi shiru, sai ta fara masa shagwaɓa ta ce "amai nake ji, cikina juyawa yake ka yi yawo a raina da yawa bestie" wani irin miskilin shagiɗar da baki ya yi zuwa gefe yana sake tura kanta tsakiyar ƙirjinsa yana da zata shaƙi warin da kyau idan ma shi ɗin yake yi, Safiyyerh ta dinga muruzai idanunta ya yi jajur saboda yadda ya yi mata nauyi a ƙirji, ganin tana kakarin aman da gaske ya saka ya sake ta, ai kuwa ta gudu ta miƙe tsaye ta yi waje tana sheƙa uban amai kamar kayan cikinta zai fita. Mama Zaituna ta bita da idanu, sai suka kalli juna da Inna Binta ta ce "kin san Allah muna zaune a gidan nan sai dai mu ji kukan jariri, ba dai auren gata da son garta akai masa ba? Ɗan mitsitsin yaro a bashi yarinya haka? Amai take yi fa ki duba?" Ta ce hankali tashe tana leƙa Safiyyerh dake bakin rariya.

"E, to. Abin kunya ne dai an yi an zuba masa ido yana danne yar mutane a ɗaki saboda ta ƙamar shi auta ne, yaro sai ƙifaɗi da ɗan iskan faɗin ran tsiya kuma a ɗakin uwar saboda wani kalar jin daɗi, ana sake masa yana yin yadda ya so" Inna Binta ta faɗa tana ɗan kyaɓe bakinta.

Da sauri kuma suka sauya zancen ganin Safiyyerh tana shigewa ɗakin Ammo, Mama Zaituna ta ce "Sannu yar masu kuɗi, Allah ya raba ki da kayan nauyi lafiya"

"Amin" Safiyyerh ta amsa, ba tare data san abin da suke nufi ba.

Safiyyerh na shiga ɗakin shi kuma yana miƙewa fuskarsa ba wasani, kamar daren ashirin da bakwai saboda duhu. Ya fice ba tare daya kalleta ba, sai ta ji a ranta bata kyauta masa ba, ai mijinta ne taya kuma zata ce masa yana warin rana? Sai ta ji ta muzanta kuma ta ji zata bashi haƙuri. Tana ta zaune bai shigo ba, har su Ammo suka dawo daga kasuwa siyayyar bikin Sa'adah data gabatuwar azumi.

"Safiyyerh sannu da zaman waje guda, amma mene ya same ki haka kikai zuru-zuru haka?"

Murmushi ta yi ta ce "Ba komai, bacci na yi fa" ta ce a hankali.

"Ban yarda ba, ko Muhammad ya miki wani abu ne? Na san halinsa"

Sai ta yi ƙasa da kanta tana wasa da yatsun hannunta, dokawar da ƙirjinta ya yi da ƙarfi ya saka ta fahimci zuciyarsa ke kusantuwa izuwa tata zuciyar. Ta ɗaga kanta suna haɗa idanu ya watsa mata harara ta yi saurin ɗauke kanta gefe tana kawar da hawayen idanunta, da kuma hana zuriyarta jin zafinsa da gaske. Ya nemi waje ya zauna yana tanƙwashe ƙafafuwansa ya fi ƙarfin mintuna goma sha biyar da zama da ƙyar ya cira kan shi ya ce "Sannu Ammo" ya ce bisa dole yana kame fuskarsa sosai da kyau kuma.

Wani irin kallo take masa kafin ta ce "Me ka yi mata?"

"Ita wa?" Ya bi ba'asi tambayar.

"Safiyyerh, kuka take"

A cikin kansa ya nanata sunan Safiyyerh yana jinjina ƙarfin halinta a ran shi. "Ina tambayarka mai ka yi mata ne?"

"Nima ɗin ai na shirya kawo ƙararta ai, zuwa ta yi tana shinshina ni wai ina wari, ni nake wari ni zata cewa ina wari" ya faɗa a daƙile yana nuna kan shi da yatsarsa tare da nutsar da idanunsa zuwa ciki sai ya yi ƙwafa yana tsuke fuska. Safiyyerh ta girgiza kai ta ce "Ammo wanka fa kawai na ce ya yi, daga cewa ya yi wanka shine ya danne ni na shaƙi duka zufar jikinsa"

Ya juya ya kalli Safiyyerh sai ya ce "Bana ce ki mini wankan ba, ban ce ki mini ba? Kin zo kin mini ne"

Ammo ta hangame bakinta ta ce "Na ga abin da ya dame ni, yanzu ita ce zata maka wankan don Allah, kai baka ji kunyar maganar nan akan idanuna ba yanzu?"

"Ita bata ji nauyin kallar cikin idanun mijinta ta ce masa yana wari ba? Naga dama sai na yi sati ban wanka ba kuma wallahi tare zamu shanye warin dauɗar" ya miƙe tsaye yana doka ƙofar ɗakin ya yi waje ƙirjinsa har rawa yake yi saboda tsananin zafin zuciya. Sa'adah ta bi bayansa da kallo ta ce "Yau autar ta motsa, masifaffe yaro kawai" Ammo ta girgiza kai kawai ta ce "Allah ya shirya"

Safiyyerh sai ta fashe da kuka, ganin kamar bata kyauta ba kuma ta yi zunubi mai girman gaske. Sai da ta yi kuka son ranta sannan Ammo ta ce "Ki yi haƙuri, zuwa anjima ya manta kin ji ko?" Ta jinjina kanta Ammo ta ce "Murɗaɗɗen yaro ne, abin da kake ganin shi ne daidai shi a kuskure yake gano shi. Ki ko yi riƙe sirri Safiyyerh, dana shigo bai dace ki ce ya danne ki ba,ai mijinki shi, sirrinki ki koyi iya zama da shi, idan ya yi niyya yana da sauƙin kai a lokacin da bai niyyar magana ba kar ki kula shi, a sanda ya yi niyyar maganar ma kar ki kula shi kin ji? Sannan kina yin fitsari a tsaye idan ba ki yarda da banɗakin ba, kuma kina tsarkake jikinki, idan za ki yi tsarki ki fara wanke ƙasanki sosai kana gabanki kowanne daban daban, da kin fito wanka ga alimon ki jika ki shafa jikinki yana tsane zufa da hana tashi, ki dinga yawaita addu'a cikin lamuranki shima kina yi masa, Allah yana amsar addu'ar mata ga mijinta"

Ta jinjina kai a sanyaye ta ce "In sha Allah. Na gode sosai Ammo"

Yana ƙwance wajejen ƙarfe goma na dare, tunaninta ne a ran shi, yana son yi mata magana sai dai bai san mene zai ce sai ya share ta kawai ya cigaba da kwanciya yana jin gajiya na saukar masa.

Ƙofa ya ji an buɗe ta cikin shagon, bai juya ba domin ya san ba Goje bane, ya kuma fahimci ita ce, Safiyyerh ce sai ya rufe idanunsa pretending yana bacci. Ta ƙarasu tare da zama kusa da kan shi, tana hango fuskarsa ta cikin wutar nefar da aka kawo, asalin kyawun fuskar Mutallab yana da shi tabbas, duhun fatarsa ba mai muni bane oval face a zagaye take irin zagayayyiyar fuskarsa da ƙasumba ke cika ta, yana da madaidaitan laɓɓa kuma jajur dasu sai manyan idanu, kamar mace girarsa a cunkushe baƙa ƙirin haka sumar kan shi. Safiyyerh ta samu kanta da taɓa girarsa wacce ta mata kyau, yana jin ta ya yi shiru ita kuma ta ɗauka bacci yake yi, a hankali ta kama hannunsa ta riƙe cikin nasa.

"Zafi nake ji a nan ɗina, a nan ɗina nake jin zafi idan ka ci zalina amma na yafe maka bestie"

Ta ce, muryarta na rawa maganganun na rarrabe kan su da kan su. Hawaye ya cika idanunta ya sauka har ƙirjinsa ta ce "Ai kai ba mugu bane, ko kana mugunta ba za ka yi wa Safiyyerka ba, ka duba yanzu bani da kowa sai Allah da Manzonsa sai kai mijina" sai ta fashe da kuka, a lokacin kuma kewar su daddy ce gabaɗaya ya addaba ta, ta dinga kuka kamar zata haɗiye zuciya bayan ta gama ta yi yunƙurin miƙewa ta fita ta ji ya riƙo hannunta ya dawo da ita baya, sai ta fara inda-inda domin bata san idanunsa biyu ba. Ya buɗe idanunsa ya zuba mata su bakinta na rawa ta ce "Uhm am ashe idanunka biyu"

Ya mirgina ya ce "Idanun kina son ganina a cikin aljihu za ji ajjiye ni, so that kina tare dani always Deer" ya miƙe zaune.

"Uhm" ya ce.

Ta yi shiru, sai ya saka ƙafa ya zungure ta, ta ɗago kai idanunta jiƙe da hawaye ta ce "Ka yi fushi ɗazo, an ce ba kyau fushin miji"

"Za ki kyau da wasan kwaikwayo, kina da iya ƙirƙirar hawaye"

Da wani irin mamaki da takaici take duban Mutallab, sai ta shanye ɗacin zuciyar ta ce "Haka ne"

"Deer"

Ta yi shiru, ya saka ƙafa ya zungure ta, ta ɗago ta kalle shi ya ɗage rigar alamar ya? Ta sunkuyar da kai kawai. "Deer"

"Wai waye Deer?"

"Barewa"

"Ohh dabba ka mayar dani?"

Ya ɗaga kafaɗa ya ce "Mai lasisi ma, a cikin dabbobin ta musamman" ta maƙale kafaɗa ta ce "Ni special name nake so, sunan masoya ba kaga ni har sweetheart nake cewa ba? Shine zaka haɗani da dabba? Ni ko?"

Ya yi mursisin, bata tsammaci zai sake magana ba sai da ya ji saukar muryarsa ya ce "Ni ma'abocin jeji ne da namomin dawa, duk wacce zan bawa special nane to apart from animals ne, You are a Deer"

"Waye tiger?"

Ya yi mata shiru ta ce "Ni tiger nake so, na fi son tiger"

"Hmm" ya juya mata baya, sai ta lallaɓa bayansa ta ɗora kanta tana sauke ajjiyar zuciya "Safiyyerh" ta amsa ya ce "Maganar gaskiya ina da gundira, bana da halin ƙwarai a duk sanda kika ji ba za ki iya ba tell me, i will give you a chance to go, a freedom. Ki je wajan iyayenki daman nima ba auren na isa ba, ba zan miki yadda kike so ba, ina da gundira. Moh halinsa daban ne ok" ta girgiza kai tana shafa sumar kansa ta ce "Ko zaka gundiri kowa ban da ni, i never get tired of you, saboda ina son ka, na san baka so na, ba lallai ka so ni ba amma mu amshi ƙaddara kuma ka yafe mini"

Ya juya ya ce "Me kikai mini?"

"Kawai ka yafe mini, na san na maka laifi mai girma Mai dawa"

"Gaskiya ba zan iya yafe miki ba, kar a cuce ni kamar yadda bana cuta ok?"

"Ka cuce ni nima, ka cutar da zuciyata ina son ka, zuciyata na son ka kai baka gani, ko kana so na? Kana so na?" Ya juya ya kalle ta sai ya ce "Friends Safiyyerh, mu yi abota ta amana ki zama babbar abokiyata, mu jingine batun aure don bana jinsa a kaina kin ji?" Ta yi shiru tana kallon shi, wani irin kalla na ban fahimta ba, wani irin kallo na what do you mean by this, wani irin kallo na i am nothing to you, wani irin kallo na You never love me, ba za ka taɓa so na ba. Sai ta yi ƙasa da kanta kawai tana haɗiye hawayen idanunta da suka tarar mata.

Ya saka yatsu biyu ya ɗago fuskarta ya ce "Bana jin auren nan a kaina, mu ajjiye batun auren mu a gefe, mu yi abota, ki zame mini babbar ƙawa kuma animiyata, zanna goyaki da safe, da rana har dare amma duk goyo ɗaya naira ɗari biyu, kinga ɗari shida a rana, sai kina tara mini kuɗin a wajanki, kin ga fa har ce mini kikai ina wari? Wai wari nake kar na taɓa ki, da ban kai zuciya nesa ba da tuni kin samu karaya biyar har wannan tsukakken ƙugun naki zan ƙarya, ni ina da gundira ne, gwara zama abota da zamowarki matata"

Sai ta yi murmushi ta ce "Shikenan, idan hakan ya yi maka" ya ɗaga shoulders ya ce "Moh, baya da wani zaɓi sai abin da zuciyarsa ta ƙissima masa"

Ya miƙa mata hannu ya ce "Friends" ta miƙa masa nata ƙaramin hannun ya kama yana jin kamar ya riƙe sillan kara. A hankali ta ce "Friends"

A karo na farko taga ya ɗan faɗaɗa fuskarsa sai ya saki hannun ya ce "To zo na zauna a cinyarka ki mini hira har na yi bacci" ya figota zuwa kusa dashi kamar zai ɗora kansa a cinyarta sai kuma ya janyota jikinsa saman ƙirjinsa ya rungumo ta sosai, ajjiyar zuciya ta sauke a hankali.

*

An yi bikin Sa'adah lafiya an kuma kaita gidan mijinta lafiya. Koda Anty Hameeda ta zo babu wanda ya faɗa mata abin da yake faruwa, haka ta dinga bin Safiyyerh da idanu, Bafullatana kawai aka faɗawa saboda an san ita kurma ce. Azumi ya zo ya shuɗe, sana'ar Ammo na garawa tana kula da Surayyerh sosai. Malam kallo ne kawai nasa da Mutallab sai muguwar magana ta aibatawa wanda idan da sabo ya saba da hakan. A hankali kuma ɗabi'un Mutallab suka sauya, duk inda shiga dawa yake da jeji yana kan gaba ko farauta za'a yana daga kan gaba. Mutane suka san shi matsayin mai dawa a ɓoye kuma ake zuwa wajen shi neman taimako.

Tsakaninsa da Safiyyerh mutunci duk da sai ta yi kwana biyu bata gansa ba. Suna yin waya dai ta dinga tsokanarta, rabin hirar duk ita ke yi. Daga ita har shi suka shiga shekara ta goma sha bakwai. 17 years. A lokacin kuma yana Ss2 sai aka yi masa jumping zuwa Ss 3 zangon karatu na farko. Kuma yana ajin Q ne science class. Sai makarantar ta fara damunsa, ba Kimiyya hatta Nahyan ya sauya makaranta shi kawai ya rage, a hutun da aka yi ne kuma aka shirya tafiya dawa domin farauta wanda suka shafe wata guda a can, amma Malam bai taɓa cewa don me, Safiyyerh iyayenta basu taɓa cigiyarta ba a cikin wannan shekaru buyun da watanni.

Tana tsaye ta juya baya a tsakiyar ɗakin Ammo taga inuwar mutum, a lokacin kuma daga ita sai guntun zani ta fito daga wanka, bata shi bane, bata san zai dawo ba, domin tunda suka tafi farauta bai taɓa nemanta ba. Hucin numfashi ta ji a bayanta ta juya da sauri suka haɗa ido, sai gabanta ya faɗi ganin yana binta da wani irin kallo, a jerin shekaru biyun da suka zo tare da shuɗewa da kuma wata guda da ya

yi bai ganta ba, sai yaga ta ƙara girma a cikin idanunsa ainun ta zama cikakkiyar budurwa mai shekaru 17 da watanni a duniya.

Bunjimar rigar farauta ce a jikinsa, sai hular saƙi, hannunsa duka goro da layoyi, gashi tubarakallah a tsaye mai faɗi gemu duk ya fito masa ya sake buɗewa daman gashi da faffaɗan jiki. Sai ya yi mata kwarjini a cikin idanunta da shakkarsa kuma.

A daddafe ta ce "Sannu da zuwa"

Ya yi shiru. Ta ce "Ya hanya? Ya jeji kuma mai dawa?"

"Kece?"

Ya ce, yana binta da wani irin miskilin kallo ganin ta sauya completely ta sake kyau, diri da cikar ƙirji gabaɗaya. Ta harare shi ta ce "Daman na san ka manta dani ai, ai shikenan ka zauna na kawo maka abinci"

Ya shafa kai kawai ta saka hijabi ta fita sai ya bita da kallo a makake, ya sauka numfashi a ƙirji a lokacin duk wani kaifafar tunani Allah ya bawa Mutallab, ya gama gamsuwa Safiyyerh matarsa ce, ya kuma shirya rayuwa da ita zai mata halacci kwatankwacin yadda ta yi masa zai bata abin da take ƙulafuci tsayin shekaru.

Ya yi baya ya kwanta, a lokacin akwai ƙaramin gado a ɗakin Ammo, ya rufe ido daidai nan ga shigo ta matsa gefe ta ce "Ka yi wanka ko? Kafin abincin"

"Yau ma warin nake?"

Ta ji ya tambaya, sai ta yi shiru ya miƙa mata hannunsa ya ce "help me" ta kasa fahimta,ya buɗe idanunsa ta suka ƙanƙance ta ce "Me ka ce?" Ya yi shiru yana miƙewa zaune ta juya zuwa ɗaukan kayanta, daidai nan kuma aka ɗauke wuta bata san ya aka yi ba sai jin saukar jikinta ta yi a cinyarsa da sauri ta ce "abota, abota,

ka manta cewa abokiyarka ce ni ba mata ba?" Bai kulata ba, sai zabura da ta yi ganin ya yaye hijjabin jikinta da sauri kuma ta ƙanƙamesa jikinta na rawa jin hannunsa inda bata taɓa tunanin ji ba a karo a farko a rayuwarta.

[1/7, 9:36 PM] Sis Fauzy: Chapter 42: My love is back

Not edited

Ta cikin hijjabin ta fara ture shi ta ce "mene haka, me kake yi....," ta haɗiye sauran maganganun a cikin maƙoshinta, bisa tilas sai rarraba idanunta take ta cikin duhun ɗakin. A wata guda da ya yi a cikin daji yana farauta bata jin muryarsa ba, balle ganinsa, shiyasa yanzu daya faɗo kamar daga sama ta ji faɗuwar gaba, kamar irin wanda ya shekara haka taga sauyi tattare da shi, yanayinsa sun jirkice, banda ƙamshi ciyayi da warin jeji babu abin da yake yi, girmansa na lokacin ɗaya kuma ya sake tsoratar da ita ya saka mata jin shakkarsa da kwarjininsa akan dole, ta lura kuma bai fahimta ba.

Da ƙyar ta ce "Mai dawa"

"Hmmm" ya ce yana ɗan buɗe idanunsa, tare da kunna hasken wayar hannunsa ya haske fuskarta da ita. A hankali ta ce

"Me kake yi haka ne?"

"Abin da ya dace"

"To hakan bai dace ba ai, mene haɗin namiji da hijabi? Namijin mai Mai dawa gwarzon maza?"

"Uhm"

Ta ce "wai mene wani uhm, kamar mai ciwon baki don Allah? Ni ka sake ni wanka na yi fa, ƙilama da sauran ƙurar jeji a jikinka" ta ce tana marairace fuska, tare da ƙoƙarin ƙwace kanta ganin idanunsa a lumshe kuma a jirkice. Zata zame ta gudu ya saka mata ƙafa ya danne ta, yana jan numfashi ta cikin ƙirjinsa ya yi kuma kamar ba ita yake kallo ba can ya nisa ya ce "hmm"

"Sake ni na fita, ba zaka kashe ni da wannan hmm ba, mu je ka yi wanka sai ka ci abinci na maka tausasa ko? Meka kamo mana ne?" Ta ce tana murmushi fafaren haƙoranta a bayyane, ya fahimci haƙurin Safiyyerh a bayyane, ya fahimci sauƙin kanta a zahirance, ya fahimci sanyin halinta a ɗabi'ance ya fahimci baiwar fara'a da Ubangiji ya wadata zuciyarta da ita, wacce ita ke sawa ta manta da abubuwa da yawa, she is nothing but a simple, silly girl.

Ya kamo hannayenta biyu a daƙile ya ce "So still deer yarinya ce"

"Ban fahimta ba?"

"Deer, ke yarinya ce" ya ce yana cure girarsa guda, ɗayar kuma yana matsar da ita can gefe guda. Cikin rashin fahimta ta ce "Uhm'uhm ni dai ban gane ba"

"Tuna mini" ta ce ganin ya yi mata shiru, kuma yaƙi sakinta idanunsa kuma a rufe amma tana da tabbacin yana kallon ta. Ya cije lips ɗinsa "Moh baya manta abu" sai ta harare shi ta ce "Ni na manta, ka tuna mini kawai" ya mirgina gefe ya tashi zaune ita kuma tana daga kwancan ya hanata tashi ya danne ta da ƙafarsa. Bata ɗauka zai sake magana ba sai da ta ji ya ce "Zan miki abu idan na tuna miki fa?" Ta ce "Kai baka abu saboda Allah ne? Kamar kai ka fi kowa son kuɗi bestie? Ba kyau son kuɗi"

"Idan ban so kuɗi ba, ke zan so"

Ta yi jim, sai ta ce "A'a, ban ce ka so ni ba ai ban isa ka so ni ba"

"Good" ya ce without care.

"Tuna mini"

Ya buɗe gajiyayyun idanunsa a lokacin ya zuba a kanta, to make sure ita ɗin ce, a zuciyarsa mamakin sauyinta ya yi, girman jikinta, kyan fuskarta nacin da take masa duka sai ya ragu, irin raguwa da musamman, sai kuma ya hakan ya ɗan sosa ranshi, don me zata rage yi masa naci? Shi ya saba da nacinta yana jin daɗin nacin. A fili kuma ba wani kallon arziƙi yake mata ba, gani yake zata iya raina shi tana ganin shekarunsu ɗaya shi ya tsani raini bai so ko kaɗan shi ya sa baya wasa. Kamar daga sama ta ji ya ce

"Yarinya ita ce wacce bata....," da sauri Safiyyerh ta hantsila gefe tare da mirginawa har towel ɗin na zamewa bata sani ba, ta saka tafin hannunta ta rufe masa bakinsa da shi tana zazzare idanunta wanda suka tara ruwa, kamar ya yi dariya sai kuma ya tsuke fuska yana sakar mata cizo ta ɗauke hannun tana yarfewa ta ce "Auchhh, my hand" sai kuma ta fashe da kuka sosai kamar daman jira take yi irin ta tara kukan sosai, ya zuba mata idanu sosai yana kallon ta yana jinjina kai kamar yana jin daɗin kukan nata. "Ba zaka bani haƙuri ba? Cizo na ka yi fa? Ka bani haƙuri" ya yi shiru ya zubawa waje guda ido, da sauri ta kalli inda yake kalla innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, ashe ilahirin ƙirjinta a bayyane yake hijjabin ya cire, towel ɗin hakan, ta kasa motsi ta kuma kasa rufe jikinta, idan ta ɗago kai sai taga wajan yake kallo, jiyiyon kansa duk sun fito sai cije lips ɗinsa yake yi. Sai kawai ta cure waje guda ta fara wani irin kuka, ganin yaƙi kulata ta matsa kusa dashi ta fara kai masa duka a ƙirji da iyakar ƙarfinta, shi dai bai motsa ba kamar statue ita kuma bata fasa dukan ƙirjinsa ba.

Jikinsa ta faɗa, irin i need a shoulder to cry on.

"Bestie"

"Hmm"

"Mai dawa, mijina mijin Safiyyerh" ta ce tana shasshekar kuka da dukkan ƙarfinta, kan ta kuma a kafaɗarsa hannunta ɗaya a ƙirjinsa. "Na yi kewar su daddy, ina kewar Ummeyh, ina kewar babban abokina, ina jin kewa,ina jin kamar ni ɗaya ce,

don Allah abokina ya kasance dani, ina son abokina ina son shi" ta ce a raunace muryarta na sarƙewa hawayenta na fita kamar famfo.

"Kina jin daɗin kuka, kuka na miki daɗi Deer" ya ce yana yin ƙasa da kansa suka haɗa ido.

"Au bama zaka rarrshe ni ba?"

"A saboda na miki wani abu? Jin daɗi ne ya miki yawa Safiyyerh"

Ƙoƙarin tashi ta fara daga jikinsa ba tare da ta ce komai ba, ganin ba zai kulata ba ta ce "Kai kullum kafi gane ka yi ta haɗe fuska, ka yi ta fushi murmushi fa ni'ima ne yana wanke zuciya wallahi" ta ce hawaye na sake gangaro mata.

"Ji" ya ce mata.

Ta juya ta kalle shi. Sai ya ce "Kina da matsala da yanayin da Ubangiji ya yi mini ne?" Ta ce "Kana yin murmushi dai don Allah" ta yi furucin a raunace jikinta kuma a sanyaye, ganin bata ji daɗi ba ya kamo hannunta ya ce "To nawa za ki bani na rarrashe ki? Kin ga lokacina zan ɓarnatar a iska"

"Saboda ka rarrashi matarka ya zamana ka ɓarnatar a iska? Baka son Manzon Sallallahu alaihi Wasallama ya umarci mazaje da su zama abokan wasan matayensu ba? Lada fa zaka samu Mai dawa, ladan ne baka so? Ni dai ina maka kwaɗayinsa"

Ya dube ta, yana zame bunjimar rigar jikinsa, sai ta lura hatta ƙugunsa wasu manyan layoyi ne, a ƙirjinsa ta lura da zane, zanen da bata san na mene ba kuma da alama ya jima a jikin nasa.

"Ai sai kice rarrashi kike so daga wajan mafaraucin mijinki"

"Ni yaushe na ce haka?" Ta faɗa tana ƙifa idanu ganin ya ajjiye askira a gefe ya cire hular saƙin ma. Baƙin jikinsa ya bayyana a fili, ya taune harshe yana ajjiye guttun busar hayaƙin ƙarfe na tsari ya ce "Yarinya kenan" ta ɗauke kai ta ce "Whatever, ni ban ce mijina ba, yaushe zan ce maka mijina akan me to?" Yanayin maganar tata a ƙufule ya fito. Sai ya ɗaga kafaɗa ya ce "Kin ma ƙaton kan ki ai, kin wa kan ki"

"Ni yanzu bani da wata alfarma a wajanka? Shiga cikin jeji kayi rayuwa da dabbobi yafi maka?"

"E, ina jin daɗin hakan, jeji shi ne ni, jeji na Allah, Mai dawa na jeji"

"To ai shikenan"

Ta faɗa tana juyawa, sai ta sake tsayawa ta ce "Wai ba zaka ce ya nake ba a matsayina na matarka? Ba kyau, ba kyau abin da kake"

Ya yi mata wani irin miskilin kallo ya ce "Sai ki ce mijinki kike buƙata, idan ya kike ne na abota na miki ai, ki ce mijinki kike buƙata kawai ki daina nunƙufarci ba zan gane ba, uhm" ya ce yana miƙewa tsaye sosai akan ƙafafuwansa ya kere mata a tsayi ta yi ƙasa da kai ta ce "Ni bana buƙatar wani miji" sai ya ɗaga kafaɗa kawai, ya nemi hanyar fita cikin sauri ta ce "I need my husband, I need my bestie, ina son mijina, ina son Mai dawa na"

"Yarinya kin yi kyan kai, kina da minti biyar ki faɗa mini komai"

Sai Safiyyerh ta samu kanta da yin shiru, ta rasa me zata ce masa, ta ji tana son faɗa masa nauyin saƙon Aafiyyah da yake kanta tsayin shekaru biyu, da shi take kwana da shi kuma take tashi a rai, sai kuma ta fara tunanin mene makomarta a wajansa idan ta faɗa masa cewa the message is not belong to her, is for Aafiyyah, ya matsayinta yake a zuciyarsa? "Think Safiyyerh" zuciyarta ta ce mata, ya yi accepting nata a lokacin data nuna masa wasiƙun, ya sauya mata a wannan lokacin, what if ya goje mata idan kuma ta ce ba ita bace? Mene matsayar ta?" Ta fara tunanin zuci.

"Barewata" ta ji ya kiranye ta, cikin taushin murya duk da a daƙile ya yi maganar amma akwai laushi cikin furucin nasa.

"Safiyyerh" he called her gain.

"Na'am" ta amsa a firgice, bata san zuwansa ba sai ganinsa ta yi tsaye a gabanta ya zuba mata gajiyayyun idanunsa da sukai laushi cike kuma da gajiya. Safiyyerh ta yi ƙasa da kanta taƙi magana sai kuma ta ji nauyinsa, ta san kuma ba lallai bane ya ce mata komai ba. "Hmmm, five minutes left" yana cewa haka ya fice daga cikin ɗakin da sauri. Sai ta ji kamar ya tafi da ruhinta ne, kamar ya tafi da tunaninta da nutsuwarta ne gabaɗaya, a hankali ta sulale ta zauna daɓas a jikin gado ta cure tana sakin wani irin kuka mai cin zuciya a fili kuma ta ce "I am sorry Aafiyyah, ki yi mini alfarma kina da komai, kin fini ƙarfin zuciya za ki iya haƙuri i am sorry, i am sorry Aafii" ta dinga kuka ita kaɗai zuciyarta na yi mata zafi sosai.

Da ƙyar ta tashi, ta saka kayanta duguwar riga mai ɗan kauri wacce ta zauna a jikinta das ta saka hula daman kanta ba wani kitso har yanzu tana da sauran mayuka fatatar jikinta tas take.

Saman gado ta hau ta zauna, ganin har yanzu Ammo bata dawo ba, ta jima tana tunanin yadda zata iya rayuwa da Mutallab da wannan botsararren halin nasa, shi komai a baibai yake ganinsa, taga bata da wani zaɓi daya shiga yin addu'a da neman zaɓin Ubangiji wanda tun farko ya kamata ace ta yi. A hankali ta ja numfashi ta sauke cikin rauni murya ta ce "Ya Allah kai ne ka ɗora mini soyayyar bawanka a cikin zuciyata, Allah kai ka dasa mini ƙaunarsa a cikin ƙirjina, ka wanzar da tausayi a cikin nawa ƙirjin nake jin so da ƙaunarsa na yi yaɗo da gina kansu, kullum ina rayuwa da soyayyar mijina, ina rayuwa da ƙaunarsa, ina shaƙar numfashin da tausayinsa a zuciyata, duk shuɗewa da ƙiƙa da gittawar lokaci basa tafiya ba tare da sun tunatar dani begen shi ba. Idan soyayyar da nake masa kuskure ce Allah kai ka ɗora mini, idan ƙaunar da nake masa wawta ce Allah kai ka dasa mini ita, rayuwa da nake dominsa ne Allah kai ka kawo numfashi ne a ƙirjina kawo war haka. Idan bari iyayena da na yi da nazaɓe masa shine laifina Allah na tuba, idan wonfitar da aminiyata da na yi shine abin da nake girba Allah bani na sawa kai na ba, zuciyata ce. Idan ina da rabo na alheri Allah ka kar kato da hankalinsa izuwa gare ni, Allah ka shirya mini mijina Mai dawa, ubangiji ka sanya masa hannu cikin lamuransa ka bani ikon cinye dukkan wata jarabbawa da zaka sadar da matsala tsakanina da shi, Ya Allahu Yaa Rahmanu"

Sai ta ji nutsuwa a ranta, ta ji damuwar ta kau har ta manta.

Mai dawa na fita kuma wanka ya yi ya shirya cikin wasu ƙananun kaya, ɗaya daga cikin kayan da uncle Musbah ya kawo, wando ne three qauter mai duhu sai riga Jessy wacce ta kama jikinsa, ya saka wata hular angara ya karkatar da ita zuwa gefe. Yana zaune saman buzu ya saka ƙwarya a gabansa daya zuba ruwa a ciki da wasu allurai ya yi shiru idanunsa rufe, da sauri kuma ya buɗe idanunsa a ɗan firgice ya ce "Safiyyerh!" Ya faɗa yana jin kiran sunan yana nanata kansa ta cikin ƙirjinsa, ya yi shiru sai kuma ya sake rufe idanunsa ji ya yi kansa na masa girma yana juyawa bisa dole ya ajjiye tare da miƙewa hannunsa zube cikin aljihu ya fita, tunanin kimiyya ya dirar masa amma gabaɗaya baya samunsa a waya.

*

Suna zaune cikin ɗaya daga cikin manyan gidansa a sashi na musamman a ɗaya daga cikin manyan parlors dake gidan. A hankali ya gyara zama da ya yi a saman kujera cikin shigar alfarma sai kuma ya ajjiye abin hannunsa da yake juyawa kamar game. yaja gwauron numfashi a hankali ya ce

"Jaa'afar"

"Ranka ya daɗe" Jaa'afar ya amsa cikin girmamawa. "Bana son wasa, da kai ɗaya na amince na kuma yarda Jaa'afar, lokaci ya yi da zaka nutsu ka tsayar da hankalinka waje guda ok?"

"In sha Allah ranka ya daɗe"

"Good" mutumin ya yi shiru sai kuma ya ce "Akwai magana ne?"

Jaa'afar ya ce "Kusan hakan, amma ga wannan ka fara gani" Ja'afar ya miƙawa mutumin wayar hannunsa, a hankali ya dinga bin screen ɗin wayar da kallo ya ɗauki a ƙalla 10 minutes yana kalla kafin ya ce "And what is this Jaa'afar?" ya tambaya yana juyawa Jaa'afar fuskar wayar shima ɗin fuskarsa da alamar tambaya domin bai fahimci kurman baƙin na Jaa'afar ba. "Ranka ya daɗe ina ganin kamar...," ya katse Jaa'afar da faɗin "Ba wannan ne a gabana ba tukun ka ji ko?"

"Amma yana da kyau ka tsaya ka ji me zan ce ne"

"Na ji me? I am not ready "

"Shikenan sir"

"Ja'afar, aikin yaron nan Ɗan'malam i appreciate it, ban ɗauka muna da malamai a cikin gari irin haka ba, nake ta wahalar da kaina a iska da ɓarnatar da kuɗi ba tare da buƙata kuma ta biya ba, na ji daɗin aikin sosai, zan ƙara masa kuɗi mai yawan gaske ka kai masa" cewar mutumin. "Sir, ai shi ba wai boka bane kuma ba sananne bane kawai dai Allah ya bashi baiwar abinne sama taka duba da cewa ɗangado ne, shi aikin yake yi kawai wallahi".

"Ko ma dai yaya ne, bana son ka yi mentioning sunana a wajansa, ya yi maka aiki ba tare daya san asalin wanda ya kewa aikin ba ka ji? Ka fahimta?" Jaa'afar ya ce "Kar ka ji wani ɗar bai san komai ba, aiki kawai yake yi mana, kuma zai cigaba da ya yi mana in sha Allah, kuɗin daman yake da buƙata"

"Kuɗi wajan ya tarar zai kuma samu, as far as buƙatuna suna biya shikenan. Ka je za mu yi magana zuwa dare" cikin girmamawa Jaa'afar ya miƙe tare da ficewa daga cikin parlon. Yana fita mutumin ya ɗauki wayarsa ta sirri ya kira wata waya da sauri kuma ya ce "bana son kuskuren da aka samu na baya, a ƙara sakawa gidan idanu da kyau don Allah, a sake nema yara sosai masu cikakkiyar lafiya da kuzari ko nawa ne a dinga biyansu suna tarayya da yaran kun ji?" Yana kammala wayar ya kashe ya ajjiye. Waya ce wacce sai time to time yake buɗe ta, kuma yake amfani da ita kamar dai yanzu.

Cikin isa da izza yake takawa har zuwa cikin wani haɗaɗɗan ɗaki, a takure ya hangota can ƙuryar gado ya nemi waje ya zauna.

"Laylerh" ya kira ta.

A firgice ta ɗago kanta ta zuba masa idanunta da sukai jajur taƙi cewa komai jikinta sai rawa yake yi, ya miƙa hannunsa zai riƙota ta sake matsawa a tsorace "Laylerh" ya kira sunanta da ƙarfi, ƙarfin daya sakata magantuwa bisa dole kamar doluwa haka take binsa da idanu ta ce "Laylerh me?" Ta faɗa cikin sigar tambaya.

"I want you, ina nufin ina buƙatar ki, ina buƙatar ki Laylerh"

"Uhm, kana buƙatar Laylerh?" Ta girgiza kai ta ce "Wanne irin mutum ne kai wai don Allah? Wanne irin zuciya gare ka ne? Bana so bana so na gaji, abin da Ubangiji ya haramta shi ka mayar ado? Neman mace ta baya? Macen ma matarka ta sunna? Neman mace ta dubura? Me kake nufi? Tsafi ka fara ko ƙungiyar mafia ka shiga? To wallahi wallahi wallahi akan wannan sai dai duk abin da zai faru ya faru I'm tired, na gaji na gaji i am tired of this married"

"Me kike nufi?"

"Ina nufin abin da duk kake nufi, ina jin abin da duk kake ji, kai duk abin da zuciyarsa ta ƙissima maka shi nake nufi, i am ready for you"

Ya nufeta, ta yi saurin direwa ta gadon ta miƙe tsaye da kyau samar kanta duk ta sakko, ya yi wani irin miskilin murmushi ya ce "kin san mene? Ki daina wahalar da kan ki, aurena dake dole ne, zamana dani dake wajibi ne, rayuwa a cikin gidan nan tilasta ne, and and nemanki ta baya dole ne, ko da za kina mutuwa kina dawowa ne Laylerh, kin san waye ni, kar ki tsaya jayayya" ya ce yana cire babbar rigarsa ya wular saman gado. Idanunta ya yi jajur ta ce "Idan kai, kai ne nima Laylerh ni ce ɗan halak ka fasa"

"Yanzu idan ke kin fasa kece ba yɑr halak ba Laylerh? Ke fa ɗiya macace ba ki da wata power a cikin gidana, ba ki da wannan freedom ɗin Laylerh"

Ta ɗaga kafaɗa ta ce "Za mu gani"

Yatsu biyu na hannunsa ya kaɗa suka bada wani sauti, cikin sauri wani garjejen mutum ya fito daga cikin wani ɗaki hannunsa riƙe da sirinji, kai tsaye wuyan Laylerh ya nufa ya faki idanunta tare da soka mata sirinjin a wuyanta, gigitaccen ihu ta saki tana dafe wajan, bata iya juyawa taga waye ba, idanunta daya cika da hawaye ta zubawa mijin nata, tana yi masa wani irin kallo mai kama da zargi, tuhuma kallo na me ka yi mini? Kallo na ka ji tsoron girman Allah, kallo na ka tuna ni matarka ce, kallo na ka tuna akwai tashin alƙiyama. A hankali idanunta ya fara lumshe hawaye masu zafi na sauka daga cikinsu ta yi gaba zata kifa saboda gabaɗaya jijiyoyin kanta dana jikinta sun saki, ta ji duniyar na juya mata, ta jita kamar matacciyya hatta yatsun hannunta ji take kamar ba'a jikinta ba, sauran hawayen suka ƙarasa sauka saman farar fuskarta a lokacin da yake taro ta jikinsa ta faɗo, ya saka hannayensa duka biyun ya rungumeta da kyau ya ce "wannan shine girman iko na, wannan shine bambancin dake tsakanin mace da namiji, wannan shine jinkimata kin kasa gane cewa i love you Laylerh, dole zan yi amfani dake wajan cimma buƙatata, afuwa za ki mini"

Ɗaukan ta ya yi, ya shige cikin ɗaki da ita yana mai yin murmushi mai sauti cike da gamsuwa.

*

Shigowa cikin gidan ya yi karnuka na biye dashi hannunsa ɗaya riƙe da leda, ya ja ya cake ganinta zaune tsakiyar tsakar gidan tana yin wanki, ya juya idanunsa ya ga babu kowa hakan ya sake tabbatar masa cewa Ammo ta fita zuwa kasuwa, sai ya ji ransa ya ɓaci ganin duk suna ƙuryar ɗaka sai ita, tana yin wahalar da bai san ta mece ba, ya kuma kasa yi mata magana sai gadon bayanta daya zubawa idanu.

Ganin karnukan Mai dawa suna zagaye ta ya saka Safiyyerh sakin zanin hannunta, ta tsame hannun daga cikin bokicin wankin ta juya kaɗan sai suka haɗa idanu, da wannan mikislin kallon nasa na tuhuma kuma a sheƙe.

Murmushi ta yi ta ce "Idan an ji motsin karnuka to Mai dawa is on the way, ranka ya daɗe"

"Wa kike wa wanki?" Ya tambaya yana zubawa kayan idanu sai ta sake yin wani murmushin ta ce "kayana nake wankewa, sun yi datti shine" yanayin maganar tata akwai ƙarya a ciki kuma nan take ya gano hakan tun kafin ta yi furucin, ya jinjina kai

"Maƙaryaciya kika zama?"

"Bangane ba?"

"I asked you, wa kikewa wanki"

"Uhmm ni fa, ni kayana....,"

A dame yana ɗaga mata hannu ya ce "Quiet Deer" dole ta yi shiru, ya taka a hankali zuwa wajan, ya fara ɗaɗɗaga kayan sai yaga kayan Inna Binta ne, ya ɗago ya kalli Safiyyerh sai ya ajjiye kayan ya ce "Ya miki kyau Deer" yana cewa haka ya juya zuwa ɗakin Inna Binta, Safiyyerh ta ce "Don Allah kar ka ce komai" kallon da ya yi mata ne ya saka kayan cikinta juyawa ta yi saurin shigewa cikin ɗakin Ammo.

Inna Binta na kishingiɗe tana gyangyaɗi ta ji an banko ƙofar ɗakin ta miƙe zumbur tana faɗin "Auzubillahi, mugun ji da mugun gani Ubangiji ya kare, waye a nan?" Cikin buɗaɗɗiyar murya ya ce "Mai dawa" zuciyarta ta harba, ya zuro kan shi cikin ɗakin yana ƙare mata kallo ya ce.

"Me ya sa za ki saka matata wanki? Hannu ne ba ki dashi?"

"Daga cin albarkacin yarinya sai ya zama tsiya? Na ga ita ta ce na kawo ta wanke mini"

Ya jinjina kai ya ce "Ok"

Ta yi saurin cewa "Wallahi ita ce, kuma ai lada zata samu ma ko?"

"Matata ce ita, ni nake da alhakƙun sata wanki, nima kuma bana yi. Ki dai na ganinta hakan nan ɗiyar arziƙi ce, ina sane da ita da duk motsinta, ba yau kuma

kika saba sakawa ta yi miki aiki ba, ita zuciyar Mai dawa ce, halaliyyarsa zan jure komai a karan kaina amma banda a kan ta. Ita yar aljanna ce kina ji? Ya zama na farko kuma na ƙarshe da za ki saka mini mata aiki, ita ba baiwa bace, wabillahillazi zan miki abin da ban taɓa wani ba, zan saka ki a cikin duhu zan saka su tiger cinye mini namanki ɗanye, idanu a rufe suke banda a kan matata ok?"

"A cinye nama ne ɗanye kuma?"

"Idan kina da waufi, just continue"

"Allah Ya baka haƙuri"

"Da haƙurin ya mutu sadaƙar nawa kika bayar eh?" Ya ce cikin hargagi yana doka ƙafarsa jikin ƙofa. Inna Binta ta buɗe baki sai kuma ta ji saukar abu cikin rigarta, ta zumduma ihu tana karkaɗe jikinta tana wani irin kururuwa na tsananin zafin da azaba, da azama ya fice daga cikin gidan jin muryar malam ya fito yana tambayar ko lafiya?. Malam ya tsaye jin Inna Binta na cewa "Shegen yaronka ne zai kassara ni wallahi ba zan yadda ba idan ya yi wa rayuwata illa, daga saka matarsa yi mini wanki shine zai zo yana mini azaba? kunama ya saka mini a cikin riga na daɗe ina faɗa maka ƙulafucina yake yi banda haka duk jikina bai masa inda zai saka kunama ba sai saman ƙirjina sai a ƙirjina?"

A ruɗe Aby ya ce "Ƙirjina kuma? Mene haɗinsa da kunama?"

A sheƙe Inna Binta ta ce "Kana nufin baka san yana bokanci ba ko? Kaga irin layoyin dana tsinta a cikin ɗakin nan? Wallahi bokanci yake yi wallahi da ƙyar idan ba jinina yake zuƙa da kunamar ba"

Malam ya yi jigum sai kuma ya ce "bokanci fa kika ce Binta?"

"Idan ƙarya zan maka shikenan"

A fusace Malam ya fita, daidai lokacin kuma Ammo ta shigo sukai kiciɓus ya ce "Madallah, gwara da kika dawo na gaji da halin wannan mugun yaron naki mai baƙin hali da mummunar ɗabi'a, wallahi ba zai kashe ni kwana na bai ƙare a duniya ba, ban kuma haifi yaron da zai lalace akan idanuna ba, abin da ya saka kika ji na magantu matata ya taɓa saboda ta saka matarsa aiki, to mata ai bata fi mata ba, ya gaggauta neman gida ya ɗauke mini yarinyar mutane da cikin gidana, ya je can waje ya yi tsafi ma idan ya so babu saka hannuna kuma ba'a cikin gidana ba" ya ƙare maganar cikin korari. Ammo ta yi tsaye sai kuma ta ce "Yanzu me ya yi kuma?" Ya ce "Ba lallai ke kiga laifinsa ba, tunda daman shi laifi tudu ne, kuma ina gaf da shata miki layi tsakanin ke da shi, zan saka muku hijabi. Na faɗa nan da wata guda ya nemi gidan da zai ajjiye matarsa ba gidana ba, ba zai yiwu iyan shiga ɗakin matata ba na ƙure a ɗaki shima yana shiga cikin ɗaki da yarinya ba, sam sam ba zan lamunta ba, tsinannen yaro mai mugun nufi da ƙyar idan ba shaye-shaye ya fara ba" Ammo ta ji zafin maganar sosai ta dake ta ce "Ko ma dai yaya ne hannunka ba zai taɓa ruɓewa ka yanke ka yar ba, duk abin da Muhammad zai zama silar ka ne,

kai ne sadani Abdullahi, kuma ita dauɗar gora ciki kan shata, kuma daina ganin ina maka shiru duk lalacewa jikina Muhammad ya tsaga ya fito, ka bar raina allura domin ƙarfe ce"

"Kike da ƙwarin zuciyar tsayawa gabana kika faɗa mini haka, tuni kike buƙata ko mene da za ki ce duk abin da ya zama nine bayan kin fi kowa sani?"

"Ban san komai ba, iya mugun bakin da kake jifansa da shi ya isa ya lalata shi, kuma in sha Allah Mutallab ba zai taɓa zama dalilin mutuwarka ba, ko hawan jininka"

Ya kaɗa babbar riga ya ce "Can miki, ni dai ya gaggauta neman gida ya bar mini nawa duk abin da zai zama ya jima bai zama ba"

Cikin sauri Mama Zaituna ta fito ta ce "Da ƙyar idan ba ciki ya ɗirkawa yar mutane ba" Ammo ta juya suka haɗa idanu da Mama Zaituna, sai ta shige ɗaki tana shera hawayen daya taro a cikin idanunta. Malam ya fita yana sababi duk abin dake faruwa kuma Safiyyerh na ɗaki tana ji, sai kuma yanzu ta sake fahimtar abubuwa da yawa akan Mutallab, a iya rashin maganarsa hadda tasirin iyaye na rashin kwaɓa kamar yadda itama tata rayuwar ta jirkice dalilin iyayenta, her parents course everything.

*

Harabar wajan ta ɗauki shiru sai kukan tsuntsaye da sanyin wajan, da ƙamshin furanni da suke tashi, gabanta coke ne da pizza tun da mutuncinsu har vacteria ta shiga without knowing. Fararen idanunta zube a kan pizza ɗin duk maganar da ake mata ji tunaninta ya rabauta da wajan. "Aafiyyah"

Shiru ba amsa aka buga teburin gabanta da ƙarfi aka ce "Aafiyyah"

"Blackman" ta ce a fili ba tare da sanin kalmar ta fito daga cikin bakinta ba, sanyin muryarta ya ƙazanta har ba'a iya jin me take cewa sosai. Wace take gaban Aafiyyah ta ce "Waye Blackman"

"Kamarya?" Aafiyyah said, tana juya idanunta akan Shila.

"You just said it"

"Say what Shila?"

"Blackman" cewar Shila tana murmushi kana ta ce "Kin san me Aafiyyah, ai kin yi zurfin da ba ki isa kin hana a gano matsalarki ba, kawai ki faɗa mini waye Blackman a shige wajan"

Aafiyyah ta share Shila ta yi kamar tana taɓa wayar hannunta, amma ya sake tafiya duniyar tunani gani take kamar mutuwa za ta yi, kamar ba zata yi rayuwa mai tsayi ba, bawai mutuwar take tsoro ba, kullum zuciyarta ke raya mata cewa Aafiyyah you most die, sai ta ji gabaɗaya duniya ta yi mata zafi ta yi mata ɗaurin huhun goro wani irin baƙin ciki take ji a ranta da kuma ɗaukewar tsammani mai kama da hopelessness, ta ji rayuwarta bata da wata ma'ana ga zafin zuciya da Ubangiji ya ɗarsa mata a yanzu da saurin fushi. Duk yadda ake ƙoƙarin sama mata farinciki musamman Mj sai ta ji bata buƙatar wannan pleasure ɗin, ta ji kamar bata da wani amfani a duniya yanayinta ya yi mata kama da worthlessness ta ji kamar ta yi laifi mai girma mai kama da guilt.

"Aafiyyah" Shila ta sake kiran sunanta, sai ta yatsuna baki ta ce

"Ina da kune Shila"

"Na san kina da shi, amma tunaninki baya nan wajan idanunki ya yi kama da wacce bata samun bacci wallahi"

Aafiyyah ta yi baya kaɗan ta ce "Haba?" Cikin damuwa Shila ta ce "Wallahi, kin rame da yawa"

"Ok" kawai Aafiyyah ta ce. Tana kallon pizza ɗin, duk ƙaunarta da pizza amma yau ta kasa kai ta cikin bakinta. Sai ta yi murmushi a fili ta ce "So it's true?" Ta tambayi kan ta, ta samu kan nata da tunanin message ɗin da ta yi wa Mutallab inda take cewa “I love you more than pizza” murmushi kawai ta sake yi tare da yin shiru. Shila ce ta fito da baƙin coke a cikin jakarta ta tsiyayawa Aafiyyah a cikin cup ta ce "Sha lemon nan za ki ji daɗi, kuma za ki yi bacci" ta ce tana turawa Aafiyyah, ta kalli lemon baƙi ne zubin cokacola, a hankali ta ɗauki cup ɗin ta shanye, shila ta sake zuba mata lemon ta shanye sai ya ɓata fuska ta ce "Shila ɓarnar kuɗi, kina da lemon kika samu siya?" Shila ta ce "Nawa ai special one don kiji"

Aafiyyah ta duba agogon hannunta, sai ta miƙe jikinta sanye da Black ɗin abaya three pieces, ta yi rolling kanta da brown ɗin vail, sai wani brown neck data saka, idanunta cikin shade glasses ko jakar hannunta ta kamfanin Arɗos group bata ɗakko ba. "Baza ki jira Mj ba"

"Zan iya driving, thanks Shila"

Ta ce, tana nufar wata ƙaramar baƙar mota sai sheƙi take yi, buɗe motar ta yi ta shiga, key ta yi tare da yin reverse ta fita daga cikin restaurant, tun a hanya wani irin bacci yake cin idanunta motar na juya mata daidai sanda mai gadi ya buɗe mata gate daidai sanda su biyun suka fito, kallon ta yake cikin rasa da mamaki yadda kamar ta sauya halayye da ɗabi'a, hannunsa biyu zube cikin aljihu kunnensa ɗaya ya saka bluetooth fuskarsa a kame, ya juya a hankali jin Paaah na cewa

"Rayuwarka sai a hankali" ya ɗan cire hannunsa yana shafa kansa bai ce komai ba "Daga nan sai ina kuma?"

A nutse ya ce "Airport"

Sai kuma ya sake buɗe idanunsa ta cikin baƙin glasses yana ƙarewa Aafiyyah kallo tas, ya kalli Paaah kamar zai yi tambaya sai ya share. Da murmushi ta ce "Paaahh" ya jinjina kai yana ƙarewa mata kallo kamar mai nazarin ta sai ta yi saurin washe fararen haƙoranta tana buɗe idanunta da ƙyar ta ce "shine ina ta kiran numberka ana cewa a kashe fa" ya ɗaga mata gira ya ce "Saboda wayar bata da wayo irin naki safiyyerh, bata da halin Safiyyerh" ta marairace fuska sosai ta ce "Haba mana"

"Ina cikin jirgi time ɗin"

Ta rungume shi ta ce "Na yi zaton haka ai, you look great Daddy"

Sai kuma ta juya ta ce "Welcome Yaya" ya yi shiru. Paaah ya ce "Ana magana" sai ya yi gaba abinsa ya ce "Zan yi missing jirgi" cikin sauri ya shige mota abinsa driver ya ja suka fice. Aafiyyah ta bi bayansa da harara. Paaah ya ce "Laa la harara" ta yi murmushi ta ce "Kai Daddy idona ke rawa kamar ƙwaro" hannunta ya kama ya ce

"As always, kina da kalman kare kai Safiyyerh"

Tunda Aafiyyah ta kwanta take bacci, baccin rabon da ta yi sa tun tana Naija, ko motsi ba ta yi a cikin baccin take jin nutsuwa na saukar mata damuwarta na yayewa baƙincikin zuriyarta na tafiya, ta shafe sama da awa biyar cif tana bacci ba tare da shirin tashi ba tamkar bata da rai.

*

Tunda ya shigo ya gama sababin faɗa Safiyyerh bata sake ganinsa ba, har dare ya yi gari ya waye wani daren ya sake yi. Ta ji ta kasa jurewa a hankali ta ɗauki wayarta sai ta shiga WhatsApp ta yi log-in da numberta, message suka fara shigowa

ta samu ta yi lefted daga group nasu na FGC. Saƙon Nahyan ta gani dana Captain sai ta share hankalinta ta tafi akan wata number wacce bata ƙasar bace, tarin messages ne sun kusa guda ashirin idan ka ɗauke emojis ga voice note. Safiyyerh ta shiga saƙon, sai ta duba username taga empty ta duba dp taga babu sai ta yi murmushi ta ce "Aafiyyah" ta san ita ce kawai, bata son kayan wahala da tarkace.

“Hy Safiyyerh” shine maganar farko sai magana ta biyu da aka ce

"How are you dear, kina lou??"

“Are you okay?"

"Ok, i won't disturb you”

“Safiyyerh”

“Safiyyerh”

“Safiyyerh”

“I so much miss you Safiyyerh, fatan alheri Safiyyerh”

Safiyyerh ta cigaba da duba saƙwannin Aafiyyah wanda suka shigo cikin mabanbanta lokaci. Ta yi murmushin takaici kawai tana lumshe idanunta da hawaye ta taro a cikinsu.

😭

“Ina jin kunyar tambayarki, na san kina sane dani da zaman jira da nake shekaru biyu, na san za ki bawa Yaa Muhammad saƙona"

Sai voice note ɗin. Ta buɗe sai ta ji muryar Aafiyyah na fita da ƙyar very slowly muryarta ta juye cikin harshen German language a hankali ta fara saurara;

"Kuna lafiya duka, to good. Safiyyerh Paaahh yana son haɗa ni aure da wanda bana so, ba zan iya ce masa a'a ba, bani da wani zaɓi Safiyyerh i love Muhammad so much and i meant it, billahi ina son shi don Allah ki daure ko bidiyo na fuskarsa ki mini idan ba zan iya jin muryarsa ba, na san watarana zai neme ni, i missed you Safiyyerh and i missed Muhammad, my stubborn boy, na san yanzu ya sake girma zafin zuciya zai ƙaro, help me please"

Ɗago kai Safiyyerh ta yi suka haɗa idanu da Mutallab sai ta yi saurin ajjiye wayarta ta ce "Yaushe ka shigo?" Ya ce "Kina aikin wofi"

"Na ji dai"

Ta ce a ruɗe. Sai ya juya ya fita abinsa miƙewa ta yi tabi bayansa tana shiga shagon suka haɗa idanu da Jaa'afar, cikin sauri ta yi baya domin har ta buɗe baki za ta yi magana, Jaa'afar ya bita da wani irin kallo yana son sake ɗaukan picture nata a karo na babu adadi. Cikin gida ta koma ta jima kafin taga wayarta na haske ashe yana da numberta? Ɗauka ta yi ta kai kunne ya jima kafin ya ce "Zo" ya ce yana kashe wayar.

Sanda ta shiga ta same shi kwance ya yi rufda ciki a hankali ta shiga bakinta ɗauke da sallama, bai juya ba sai ma sake rufe idanu da ya yi, ta matsa ta ce "Gani" ya yi shiru ta sake cewa "Gani"

"Mai dawa"

Ya juyo yana ƙura mata idanu fuskarsa babu walwala ya ce "Waya kira ki?" Ta buɗe ido ta ce "Yanzu fa ka kira ni a waya" ya cije lips ya ce "Muga" har ta miƙa masa wayar sai ta ɗauke ta ce "Ba sai ka gani ba, amma dai ka kira ni" ya dinga kallon ta da ƙyar ya ce "Ba ki da gaskiya". "Da gaskiyata Allah kai ka kira ni"

"Uhmm"

Sai ya miƙe kawai ya nufi hanyar fita, sai taga ya tura ƙofar ya rufe ya kuma saki windows ɗakin ya yi duhu, ta miƙe da sauri zata gudu ya cafko ƙugunta ya dawo da ita baya, ya saka hannunsa biyu ya riƙe ƙugun nata ya ce "Kike mini zirga-zirga ina aiki, kin ji daɗi wani ya ganki kin burge shi ko?" Ya faɗa a daƙile

"Waya ya ganni? Wana birge ohh ni ashe zan iya birge wani?"

Ta cikin duhun taga ya bubbuɗe idanunsa alamar mamaki sai ya yi ƙwafa ya ce "Oh, a saboda ba ki san darajar aure da kuma darajar kan ki ba? Ko an ce miki ba'a kishinki ba'a son ki ne? Yaushe kikai lalacewar haka?" Safiyyerh sai ta kwakkwaɓe fuska ta fara yarfe hannunta, ta yi kamar zata faɗi sai ta juya wayarta ta shiga WhatsApp wajan contact ɗin Aafiyyah ta danna voice. Gabaɗaya bai san me take yi ba sai da ya ji ta ce "To ni mene laifina don wani ya ce na burge shi, ba shi zakai wa faɗa ba? Ni ka sake ni na tafi tunda faɗa ka kira ka yi mini, ba ruwana da kai"

"Safiyyerh!"

Ya ce cike da mamaki "Anya kina son wanyewa lafiya? Daɗi kike ji kin burge wani bayan zunubi ne a kan ki?" Ta yi shiru.

"Answer me" ya faɗa a tsawace.

Tsoro a kamata sai ta fashe da wani irin kuka tana bubbuga ƙafarta ta yi waje zata fita ta manta ƙofar a rufe yake, still recording ɗin na ci-gaba da ɗauka.

"Kina fita za ki gane baki da wayo, dole yau naga abin da ya saka sakarancan cewa kin yi masa, dole ki nuna mini abin da kike ta ɓoyewa, dole ki nuna mini iyakar iyawarki Safiyyerh" shi sam bai san kishi yake ba, tunaninsa faɗa kawai yake mata ganin tana da kuka kamar ranta zai fita ya ce "Zo" sai ta maƙale kafaɗa. "Rungume ki fa zan yi, idan kikai asara shikenan, ki zo mu yi sallama ina da farautar da zani" ya taka zuwa gabanta, ba ta

yi tunanin hakan ba, sai ji ta yi ya kusantota, ya damƙo kafaɗunta a hankali kuma ya ɗora kanta a saman ƙirjinsa da yake a buɗe, ta lura yana jin daɗin zama ba riga ko duk zaman jeji ne?. A hankali kuma ya zagaye hannayensa biyu a bayanta ya ce "Shhhh" sai ta ƙanƙamesa ta rasa wani irin kukan farinciki za ta yi, ko bai ce yana son ta yau kaɗai ya gama mata komai muryarta na rawa ta ce "My love is back "

A hankali ya ce "Kuma forever"

Sun jima yana rungume da ita, kafin ya ɗago kanta suka haɗa idanu ta ce "Na ji me ka ce"

"What?"

"I love you too Safiyyerh" cikin sauri ta danna voice ɗin tare da danna send ya tafi sai ta cilla wayar can gefe. "You not serious"

"Ina son ka Bestie"

"Thank you Barewata"

Sai ta dinga kallon bakinsa, musamman lips ɗin a hankali shi kuma ya ɗora goshinsa a nata bai ce komai suna sake haɗa ido taga kawai ya yi mata murmushi sai ta lura ashe har wushirya yana da shi he keep smiling "me kake wa dariya wai?" Ya girgiza kai ta ce "Don Allah dariyar me ce" yana ta murmushi ya ce "Ba ki da gaskiya Safiyyerh, Allah ba ki da gaskiya"

"Rashin gaskiyar me na yi?"

"Kina son sumbatar mijinki"

"Uhm, oh ni nake so?"

Ya ɗage mata gira ya ce "E, ni ban niyya ba ai, ki yi kawai Barewa"

Sai ta ji zuciyarta na harbawa, wani abu na janta zuwa gare shi musamman saman laɓɓansa, ta ji tsigar jikinta na tashi, bata san ta manne da jikinsa sosai ba sai daya ƙara matse ƙugunsa da nata da kyau yana riƙe ta, bata san kuma ya aka yi ba sai gani ta yi ta ɗora bakinta a saman nasa kuma ta samu kanta da riƙe kansa ta fara kissing ɗinsa...

MUTALLAB.

PAID BOOK

08164069385

[1/7, 9:37 PM] Sis Fauzy: Chapter 43: Soulmates

Sai ta ji yana ɗan sakin ajjiyar zuciya da numfashi, ta yi saurin zame bakinta daga nasa, ta ji nauyi da kunyar sumbatar da ta yi masa, ta fara tunani abin da su Ummyh da Daddy suke ji kenan? Sai ta ji ƙafafuwanta na rawa zuriyarta na motsawa ta yi ƙasa da kanta bata son haɗa idanu da Mai dawa. Jin shiru ya saka Safiyyerh ɗago kan ta sai suka haɗa idanu, bakin nata yake kallo, ta lura da zufar dake tsakiyar goshinsa sai ta fara ƙoƙarin juyawa tare da niyar barin wajan.

"Washh" ta ji ya furta underneath his berth yana langwaɓar da kai.

"Mene? Baka da lafiya?" Ta tambaya a ruɗe, sai ya yi shiru, ta miƙa hannunta tare da yin ɗage zata shafo zufar goshin ya kauce

"Goge maka zan yi"

"Me?"

"Gumin, baka da lafiya"

Hmm" ya sake cewa.

Ta marairace fuska sosai tana sake miƙa hannunta zata goge ya zame "Don Allah ka bari mana"

Ya lumshe idanunsa ya buɗe ya ce "Lou nake, lafiyar kenan" sai ta ce "Ok, kawo na goge maka" muryarsa cike da laushi da wata iriyar nutsuwa a cikinta ya ce "Barewata, ke bakya ganewa?" Ta ce "E, zan gane idan na goge maka zufar uhm'uhm ni dai zan goge ka ji mijina" ta ce a shagwaɓe

"Za kiga abin da ba ki yi zato ba kika goge mini, za ki gani Deer"

Da rashin fahimta ta ce "Wani abu ne a ciki idan ma goge maka?"

Sai taga ya yi murmushi yana ta jinjina kan shi, ya cigaba da murmushi a hankali yana girgiza mata kai can kuma ya fara murmushi mai sauti fararen haƙoransa ya bayyana musamman siririyar wushiryarsa. Safiyyerh was shocked, ta buɗe bakinta tunda Allah ya yi ta san shi bata taɓa ganin murshinsa haka ba, he is always serious kodayaushe cikin fushi yake da kame fuska bashi da walwala, sai ta ji murmushinsa yana saukar da nutsuwa a zuciyarta tare da sanyawa ta fara nata murmushin, suka dinga kallon juna suna murmushi da ƙyar ta riƙe hannunsa ta ce "Wai mene"

Sai ya kyalkyale da dariya yana girgiza kai ya ce "Ban sani ba, ban sani ba, ni kam ban sani ba Safiyyerh" ya dinga dariya.

Dariyarsa make her smile and laugh ta maƙale kafaɗa ta ce "Uhm'uhm ni dai, ni dai, ni dai"

"Uhm'uhm ni dai, ni dai" ya kwaikwayi muryarta, ya kuma nanata abin da take cewa. Ta sake miƙa hannu zata goge masa zufar goshin nasa, a lokacin ta sake yawa tana sauka a hankali ya riƙe hannayenta biyun yana ta dariya.

Sai ya tsuke fuska ya ce "Bari"

"A'a" ta ce.

"Wallahi za ki iya ɗaukan ciki a daren nan Barewata, ki kiyaye ni"

Ta yi sak sai ta ce "Bangane ba? Wannan zufar ta mece?"

"I re..... I just appreciate it ne"

"Appreciate for?"

"Your kisses" ya ce kai tsaye.

Sai ta yi murmushi tana sunkuyar da kanta ƙasa, sosai ta ji daɗin abin da ya ce, ta ji ta fara gamsuwa Mai dawanta ya fara nuna mata sauyi, tabbacin son ne babu tunda har yanzu bai taɓa buɗe baki ya ce ina son ki Safiyyerh ba, bai taɓa koda a kalmar wasa, balle shi baya magana don wasa idan ya ce hakan ɗin ne ko zai maka daɗi ko akasin hakan kai ta shafa. Sai ya kama hannunta daidai lokacin aka kawo wutar nepa, ya zubawa zanen hannun idanu sosai "Me kake kallo, na dai fika laushin fatar hannu Allah" ya saki hannun damar ya kama na hago ta sake cewa "Wai me kake kallo ne?" Bai kalleta ba ya ce "Shekararki nawa ne?" Ya ce yana saka yatsarsa manujiyya a tsakiyar hannun ya danna ta ce "Auchhh"

"Shekarunka, shekaruna"

"Uhmmm"

"Allah baƙin ciki ne yake kama ni idan ka ce uhmm ɗin nan, kamar mai hangum" sakin hannun ya yi ya kamo can saman katifa ya kwanta ya ɗan yi rufda ciki ya lumshe idanunsa ta ƙarasa ta zauna ta ɗauki kansa ta ɗora a cinyarta ta dinga shafa sumar kansa ya yi kamar yana jin bacci a hankali ta saka yatsarta a tsakiyar goshinsa ta shafa. "Washh" ta ji ya ce a hankali ta yi saurin cewa "sannu sannu sannu" ya yi shiru, Safiyyerh ta cigaba da shafa masa sumar kansa a hankali cikin nutsuwa tana zaune ta ji numfashinsa na sauka bacci ya ɗauke shi, ta rufe idanunta wasu hawaye suka samu damar sauka daga cikin idanunta nauyin zuriyarta ya ragu, ta kama hannunsa ta riƙe ta ce "Allah ka kula mini da mijina, da sharrin da yake cikin jeji ka bashi sa'ar rayuwa, ka wadata shi da arziƙin da zai yi mana gidan kanmu, Allah ka bashi ikon ɗaukan ɗawainiyyata, Allah ka yafe mini kuskuren barin iyayena da na yi na zaɓi mijina, Allah ka gani a lokacin ban san na yi hakan ba, na ji kawai ina son rayuwa da Mutallab ne, Allah ka bawa iyayena sassauci a zuciya. Idan soyayyar da nake wa Mutallab jarrabawa ce Allah ka bani ikon cinta ba ƙorafi nake, amma tabbas na azabtu zuciyata ta wahala akan bawan Allan nan, Allah ka gwada mini ranar da zai ji irin abin da nake ji a zuciyata saboda shi, Allah ka nuna mini sanda zai fara ɗaukan responsibilities ɗinsa as my husband, ko bai so ni ba, ya nuna mini matsayi, irin matsayin da miji ke nunawa matarsa, Allah ka yafe mini wawtar da na yi a baya, ka yafe mini" ta fara shasshеƙar kuka a hankali ta zame ta kwanta kusa dashi, a haka bacci ya ɗauke ta cikin shagon. Saukar numfashinta a fuskarsa ya saka ya tabbatar baccinta ya yi nisa ya buɗe idanunsa ya zuba mata idanu, domin daman bawai bacci yake ba, a hankali ta a dinga ƙarewa fuskarta kallo irin kallo na ƙurilla, idan ana neman real definition of beauty, to saka sunan Safiyyerh, Kyakkyawar fuskarta fara tas ba fari na shiga idanu ba, ba fari mai cutarwa ba, wani irin fari ne na zallar kyau fuskarta na sheƙi da glowing dalilin raguwar mayukan S Bayero da basu ƙare mata ba, duk jan da laɓɓansa suke da shi Safiyyerh ta fisa, gashin idanunta zara-zara sun kwanta a idanunta, haka girarta luff cunkus sai ya ji ransa ya ɓaci da kyan gabaɗaya ya zabga mata harara kamar tana idanu biyu, sai ya kai hannunsa zuwa gefen cikinta ya kama ya latsa a gigice cikin magagin bacci ta shige jikinsa tana cewa "Uhm Nawan, ni taka ce, kai nawa" sai kuma ta fara jin tsigar jikinta na tashi wani abu na fuskarta, da ƙyar ta buɗe idanunta suka haɗa idanu da shi sai ta lumshe tana ɗaukan hannunsa ta saka a bayanta "Ka riƙe ni sanyi nake ji, wani abu na mini yawo a jiki"

Sai ta koma baccin, kana ya rungumeta a jikinsa da duka hannunsa biyu kan ta a ƙirjisa, tana bacci peacefully.

"Ko ban so ki ba, lallai ke tsagina ce deer, ke tsagina ce" ya ce yana sumbatar goshinta.

*

Buɗe ƙofar ɗakin ya yi, tana ganinsa ta zabura jikinta na rawa da ɓari idanunta jajur, da wata kalar soyayya mai shiga rai yake duban Laylerh kafin ya ce "Ya kike son wahalar da kan ki ne? Kina wahalar da tawa zuciyar Laylerhna? Haba yʻar kyakkyawata? Ki bawa mijinki haɗin kai wannan abin fa is nothing apart from love, ki yi mini sacrifice na hakan, dukiya nake so mai tsananin yawa, shahara nake buƙata, iko da izza nake nema idanu rufe Laylerh, will you help me? Kin san yadda nake jinki a ƙirjina shi ya saka bana son ƙuntata miki, i na son ki"

"Kʻarya kake, ƙarya ne Boɗejo ba wani so na da kake yi, buƙatarka kawai kake biyawa kan ka dani, na yi baƙin ciki na kuma yi da nasanin a aurenka, aurenka bai ƙara mini da komai ba sai baƙin ciki da tashin hankali, ina ji ina gani zan kasa zama zuwa gaba na ruɓe ma dalilin amfanin da kake yi dani ta wajan bahaya, i regret it, I regret knowing you as a person, i regret l knowing as my husband, i regretting loving you as a lover, i regret everything Boɗejo" ya dinga kallon ta maimakon ya ji zuciyarsa na tsinkewa duk da son da ya kewa Laylerh, sai ya dinga jin nishaɗi da furucin nata, kalamanta ba komai bane face tsana, tsana ba komai bane a wajansa inda ta Laylerh ce ya san zata sakko. Ya yi murmushi mai kyau cike da jin daɗi ya dubi Kyakkyawar shigar dake jikinsa ta blue ɗin yadin kashmir jamper ce babu yʻar ciki, sai ƙaramin hannu yadin ya kwanta a jikinsa ya cire baƙar hular zanna dake kan shi da wani irin yanayi ya kalle ta ya ce "Oh, ni yau Laylerh take kira da Boɗejo? Ni mijin Laylerh"

"Ina son ki, ke matata ce fa"

"Kʻarya kake Boɗejo" ya rausayar mata da kansa gefe ya kwaɓe fuska ya ce "Allah kam"

"Show me? Where is the love? Saɓon Allah da kake yi dani shine soyayyar? Kasan ƙarfin zunubin da kake aikatawa? Manzonsa Allah Sallallahu alaihi Wasallama, ya ce; ku jewa matanku tamkar gonakinku a duk sanda buƙatar tazo, ku je musu cike da soyayya da ƙauna, amma ka saka ƙafa ka yi fatali da faɗin Manzon tsira, kana

amfani da matarka ta baya ta dubura wajan da aka yi hani da shi, wajan da babu kyau"

Kuka ta fara tana haɗe hannaye ta ce "Boɗejo na roƙe ka saboda darajar da Allah Ya yi wa ManzonSa ka daina amfani dani ta baya, bana jin daɗi, bana iya zama yadda ya kamata yin bayan gida yana mini wahala, ka duba darajar dake cikin aure ka yi mu'amala dani kamar yadda addini ya koyar...," ta kasa ci-gaba da maganar tana kuka, a hankali ya riƙota zuwa gefensa ya ɗora kanta a kafaɗarsa ya ce "Hakan ƙaddarar mijinki ce, ina son yin arziƙi Laylerh, bana son talauci,ina son sunana ya yi amo a duniya, amfani da nake dake ta baya umarnin malamina ne, shi ne ya saka ni, kuma da matata ya umarce ni na yi hakan bani da wani zaɓi, ki taimaka mini kin ji?"

Da wani irin takaici take kallon shi ta ce "Bayan wannan zunubin zaka iya tarayar da wacce ba matarka ba? Zina za ka yi Boɗejo?" Ya buɗe baki, sai ya yi murmushi yana ɗaga shoulders

"Arziƙi nake so" ya ce without care

"Ina buƙatarki Laylerh"

Ta ɗago jajeyen idanunta kamar gauta ta ce "Wallahi bani da lafiya, kuma yau 15 ga wata al'adata tazo" ta ce a sanyaye.

"Oh really? Da gaske jinin al'ada kike me ya sa ba ki faɗa mini ba?"

"Dame hakan zai ƙare ka?"

Ya tsare ta da idanu, tabbas Boɗejo kyakkyawa ne a kamalance da wani irin kwarjini ka ɗaukan wanka tamkar ɗawisu don ado ya yi murmushi ya ce "Ina da alhakƙun sani ai, malamina ya bani umarnin kwanciya dake sanda kike tsaka da jinin al'ada Laylerh" da wani irin sabon tashin hankali Laylerh ya juyo take kallon shi ƙirjinta na

bugawa da tsananin ƙarfi ta ce "Yanzu sai ka kwanta dani ina al'ada Boɗejo?" Ya ɗaga mata kai ya ce "Arziƙi nake so, i will do anything, i can do anything"

Sai kawai ta juya zata fice daga cikin haɗaɗɗan bedroom ɗin daya gama gajiya da katafaren furnitures na U.S. na Kamfanin Ashley Furniture Industries. Cikin sauri ya sha gabanta ya ce "Laylerh ina buƙatarki, bana son taurin kai bana son nuna miki ƙarfina kin gane" ta kalle shi taƙi magana ganin da gaske zai cimmata ta fara tattare rigar jikinta zata gudu duk da cewa tafiyar wahala yake mata, suka fara kokawa tun tana yi da ƙarfinta har ta gaji, amma bata sare ba ganin zata bashi wahala ya saka Boɗejo zaro sirijin dake cikin aljihun haɗaɗɗun kayan jikinsa ya daidaici wuyan Laylerh wajan jijiyarta ya soka mata sirinjin tare danna mata ruwan allurar da yake ciki, a hakan ya zaro hankici ya danna mata a hancinta, ta zuba masa shanyayyun idanunta da suke zubar da hawaye masu zafi, tana jifansa da wani irin kallo mai kama da nufin kaje kai da Allah, kallon da nuna you aren't a good person, husband, life partner, kallon ba zan taɓa yafe maka ba.

Ajjiyeta ya yi da nufin ya je ya shirya ya dawo kafin nan allurar ta rasa mata jijiyoyin jikinta, Laylerh ta fara fusge -fusge jikinta na rawa da kakkarwa ta faɗo daga saman gadon ya dinga buga kanta da jigon bango tana ihu da kururuwa gashi ta kasa magana, ji take yi kamar ana fisgar jijiyoyin data haɗa abubuwa wajan uku, kanta, ƙwaƙwalwarta, idanunta. Ta faɗi ƙasa tana birgima ta jurewa sassauci take nema bata samu ba sai ta fasa tsakiyar goshinta. Da sauri Boɗejo ya shigo ya ɗauke ta ya azata saman gadon babu ko ɗigon imani ya fara ƙoƙarin farmata ta baya.

*

Safiyyerh na zaune hannunta riƙe da sunayen Allah tana karantawa ta sake yin sanyi sosai magana bata dame ta ba, dama can sai tana tare da Mutallab take yi. Ganin Ammo ta ɗakko leda zata fara ƙulla kanwa ya saka ta ajjiye sunayen Allah ta ce "Ammo zan yi" ta ce tana miƙewa ta koma kusa da Ammo domin tamkar uwa haka ta ɗauke ta, bata yi mata kallon suruka ko kaɗan "Safiyyerh ke bakya gajiya ne? Na ce ki kwanta ki huta ki yi bacci kin ƙi ko?" Ta yi murmushi as asual ta ce "Na yi fa, na gaji da kwanciya jikina ciwo yake yi" ta ce a hankali.

"To bakya zuwa ko'ina ba dole ba"

Bata ce komai ba, ta fara auna kanwar a kwankwani tana zubawa a leda tare da ƙullawa can ta ce "Ammo kina yin kantu mana mai suger da gishiri Allah"

"Wannan ai sabgar yara ce Safiyatou-khairi" cikin sauri Safiyyerh ta ce "To ni zanna yi" Ammo ta bubbuɗe idanunta waje ta ce "Ki yi me? Rufa mini asiri da mijinki ya ce na saka ki yin abin siyarwa, ko ya amince ba zan amince ba ni" sai Safiyyerh ta ɓata rai sosai ta ce "Allah ba zai ce komai ba, akwai kuɗi wajena sai na siyo a koya mini yadda ake yi"

Ammo ta girgiza kai ta ce "Sabgar riɗi akwai wahala dakawa da wankewa ma aiki ne idan kin ɗauke soyawa Safiyyerh"

"Zan iya fa"

"To fara tambayaraa ki ji" cewar Ammo. Safiyyerh ta ce "Bari ya shigo dai ko?" Ammo ta zuba mata idanu haƙurin Safiyyerh tsoro yake bata sosai can ta ce "Ke yaushe rabon da ki gansa da idanunki?" Ta ce "Sati biyu kenan"

"Baya nan to, bai faɗa miki ba?"

Safiyyerh ta san cewa bai faɗa mata ba, domin ba kiranta yake a waya ba shiyasa bata fiya barin wayarta a kunne bama, bata san kuma faɗar laifinsa wajan mahaifiyarsa domin ba daɗi sai ta ɗan buɗe ido ta ce "Laa la, ya faɗa mini mantawa na yi sam, zan kira shi" ta ce tana ci-gaba da ƙullin Ammo a ranta ta ce "Matar rufin asiri " domin ta san Safiyyerh kare laifin Mutallab kawai ta yi. Sa'adah ce ta yi sallama ta shigo cikin farinciki Safiyyerh ta miƙe da sauri ta rungume Sa'adah ta ce "Oyoyo yaya da na san gidanki da tuni na je Allah" Sa'adah ta kama hannun Safiyyerh ta ce "Haba, matar autan Ammo guda bata san gidana ba anya?"

Ta yi murmushin da baya barin fuskarta, Sa'adah ta zauna tana amsa gaisuwar Safiyyerh kana ta ce "Ammo ina yini"

"Lafiya lou, lafiya dai?"

"Kai Ammo, mutum da gidansu don ya yi aure baza shi ba? Gidan iyaye ai baya girma baya kuma tsufa daga gidan Bafullatana nake" sai Safiyyerh ta ji rauni ya kamata irin raunin rashin nata iyayen jikinta ya sake yin sanyi. Ammo ta ce "Ai shikenan ga gidan nan" Sa'adah ta ce "Gida daɗi" sai ta buɗe warmer ɗin data zo dashi jallof ɗin taliya ce ta sha bushasshen kifi sai ƙamshi take yi ta ce "Ga abinci bai iya zama jira na ci a can ba,ina ta ɗoki"

"Ni dai kar mijinki yana cewa kina taɓa masa kayan abinci Sa'adah kar ki fara wannan ɗabi'ar nan"

"Kai Ammo, shima na kai gidansu fa ai ba wani abu bane hakan"

Safiyyerh na jinsu ta yi shiru ta miƙe zata fita don basu waje, sai mayafin kanta ya faɗi Sa'adah ta dubi kan Safiyyerh ba kitso gashin duk ya yi wani iri sosai ta ce "Zo ki ci abinci na miki kitso akan nan"

"Kitso kuma?" Ta faɗa cike da fargaba bata son kitso ko kaɗan "Ai ki haɗa mata hadda dungulmi ƙafa fara fat ita bata san abubuwan mata, ki yi mata ƙunshi Sa'adah don Allah" Safiyyerh sai ƙifta idanu take ta ce "To a yi mini ƙunshin kawai" Ammo ta ce "Har kitson za'a haɗa miki,jeki wanke hannun" fita ta yi tana kwaɓe fuska. "Ko a bar ta da kitson ko?" Sai Ammo ta girgiza kai ta ce "Kitson ne fa bata so, ko kalba ce yi mata kawai"

Salatif Sa'adah ta yanka irin yankan nan na zamani ta haɗa lallan cikin ƙaramin lokaci. Kaɗan Safiyyerh ta ci abincin sai ɓata rai take Ammo ta yi kamar bata gani ba. Cikin nutsuwa aka jera mata salatif ɗin hannu da ƙafa bayan an ɗaura mata Sa'adah ta kunce kan ta ce "Tubarakallah,ma sha Allah al'umma bareek" har gadon

bayanta gashin ashe cure shi ta yi, baso san cewa Safiyyerh ajebo ce sai da aka fara taje kan, ta zage ta dinga rusa musu kuka wai zafi fuskarta ta yi jajur sansa aka fara jera mata kalbar ƙanana har da majina tana da kuka gashi ba damar tashi. Sam basu san cewa ba'a yi mata kitso ba sai dole.

Kamar daga sama haka su kaga inuwarsa, Sa'adah ta ɗaga kai ta kalle shi suka haɗa idanu bata taɓa ganinsa da shiga haka ba, farin yadi ne a jikinsa tas kamar tissue ya sha guga hannunsa duka zube cikin aljihun wandonsa an gyara masa sumar kansa ta yi baƙi tas sai sheƙi take yi, haɗaɗɗan sajen daya fara kewaye fuskarsa ya sauka daidai da gemun daya fara tasawa idanunsa fari tas laɓɓansa jajur, sai suka sake bayyanar da kyakkyawar baƙar fuskarsa jikinsa ya sake buɗewa sosai ya zartar shekarunsa duk da yana kokarin tunkarar 18yrs ne. Fuska kame ba annuri Sa'adah ta ce "zuwan yaushe? Ko sallama babu" ya yi mata shiru domin ya san ya yi sallama "Ina kiran nunberka baka ɗagawa kuma tana shiga fa"

Bai amsa ba, ya nemi waje can bakin gado ya zauna ta ce "Ai na ɗauka zaka shige satin biyu, sai gashi ka cika al'ƙawari"

"Ina yini Ammo?" Ya ce cikin husky voice ɗinsa ba tare daya tanka maganar Sa'adah ba. Ammo ta ce "Alhamd, ya hanya?" Ya jinjina mata kai. Sa'adah ta ce "Mutallab ina yini? Tunda ban isa ka gaishe ni ba" ta ce da wasa

Da mamakinta sai ta ji ya ce "lafiya" ta buɗe baki ta ce "kuma ka amsa? Ai shikenan" ya yi mata banza. Safiyyerh koda Mutallab ya shigo bata fasa kukan ba, sai ma sake gunjin kukan da ta yi, jijiyoyin kanta duk sun tashi gashi kitson ba wani zafi kawai taɓara ce ana ƙoƙarin kama na ƙarshe ta fasa ƙara wai kanta zai cire, sai a lokacin ya buɗe idanunsa da suke ciki sosai Sa'adah ta ji ya ce "Yaya"

Ta juya ta kalle shi ta ce "Na'am"

"Sake mata kan nan" ya ce

Sa'adah ta ce "Bangane ma'anar na saki kan ba, haka za'a bar shi ya lalace kenan? Kuma ai mun gama wallahi sai na gama"

Ya jinjina kai ya ce "Ki cika mata"

Ta ce "A bar ɗayan a tsefe ba kaga ta yi kyau ba daga fuska don Allah?" Kai tsaye ya ce "Ban gani ba, ni bana sha'awa bai mini ba"

"To wallahi ko me za ka yi sai na gama, ƙarya kake kuma ka ce bai yi kyau ba domin har kuɗin kitson sai ka bayar wallahi" bai ƙara tanka Sa'adah ba ya tsuguna daidai inda Safiyyerh take ya kama farar ƙafarta ya ƙunce ledar ya cire ƙunshin tas, ya kama hannayenta har lokacin kuka take ya cire tas na hannun, Sa'adah ta juya ta kalli Ammo suka haɗa ido sai Ammo ta yi mata alamar ta yi shiru. Bayan ya cire fuska a ɗaure ya ce "Tashi" sai kuma kunya ta kama Safiyyerh ya daka mata tsawa ya ce "Stand up" Sa'adah ta ce "Bari na gama ɗayan"

Cikin ƙulewa ya kalli Sa'adah ya ce "Yaya ki dai na yi mini irin haka, kin ce mini yaro, kin ce ta yi kyau idan ta yi kyau ai ba sai kin ce ba, Allah sai na tsefe su ni basu yi mini ba gwara sumarta" yana cewa haka ya fice daga ɗakin da sauri ta bi bayansa ya tsaya ya waigo ya kalle ta sosai, sai yaga da gaske kamar ba ita ɗin ba, kalbar ta sauka a fuskarta da bayanta ta yi kyau sosai tsaki ya ja ya yi gaba ta sake binsa ya sake tsayawa bai kalle ta ba ya ce "Wanke abin nan ki saman waje" yana cewa haka ya fice daga gidan. "Ammo ki yi masa magana a ƙarasa mata " ta ce "Ke ba ki da baki ne Sa'adah?". "To daman yana son ta ne?" Ammo ta ce "Ki tambaye shi mana, kin san kuka ci masa rai yake balle yanzu zai iya birkicewa yanzu gwara da kika rabu da shi suje su ƙarata ta daina kitso daga yau har yauma takumu" Sa'adah ta dinga dariya sosai ta ce "Tab, yana magana kamar an masa dole zuwa gaba cewa zai yi shi ya haifan fa? Yanzu kalle shi a tsaye" murmushi kawai Ammo ta yi "Ammo ba'a faɗawa Anty Hameeda ba har yanzu, duk matsalar Mutallab babu wanda ta sani daga ciki fa balle auren"

"Kar ki faɗa mata na gaya miki"

Sanda Safiyyerh ta fita baya waje, sai nufi shagon bakinta ɗauke da sallama murya a dashe, zaune ta ganshi a saman ladduma ya tanƙwashe ƙafafuwansa ya harɗe waje guda, ya cire kayan jikinsa sai gajeren wando hatta farar singlet ɗin ya cire sai layoyi da suke damtsen hannunsa, sai ta ji kunya ta yi ƙasa da kanta, ta ƙarasa ta zauna a gabansa leda ce a gabansa yana cin doya da ƙwai sai tsire daya sha albasa sosai ta saka hannunta ta ɗauki tsiren zata kai baki ya riƙe hannun ta ce "ci zan yi fa?" Ya kai hannunta bakinsa ya tura duka yatsun hannun ya cinye tsiren ya fara tsotse yatsun nata one by one, jikinta ya kama rawa saboda abin da ta ji ta ce "ka cinye tsiren shine zaka haɗa da yatsuna, ka sake mini" yaƙi sakin hannun ya sake tura su a bakinsa "Uhm" ta ce don kan shi ya saki ya ce "Naman ci ka biya ne, ko

maiƙo bana son ki lasa" ta ce "Ai shikenan sai na biya" ta kalle ta ya ce "Ba ki isa biya ba ai" ta ce "Allah ina da kuɗi" ta ce da sauri

"Uhmm"

"Allah zan biyaka"

"Barewata"

"Na'am, bestie"

"Za ki biya?"

Ya jinjina kai ta ce "Eh" sai ya ɗakko wata ledar ya buɗe zallar tsire ne sai lemo da yougourt masu sanyi ya ce "Mu cinye wannan, sai ki cinye wancan" tare suka ci sai lafta masa surutu take da labari kala-kala har batun kantun da sukai magana da Ammo, bai tanka ba ta lura idan yana cin abincin baya magana sam, idanunsa a ƙasa sai ƙarewa zanen lallen ido yake ya zauna raɗau sosai ƙafar ta fito ta sake kyau sosai gata ƙarama, a hankali ya kai yatsarsa ya shafa tsakiya da gefen ƙafar da sauri ta ce "Auchhh" sai tsuke fuska ya ce "meye za ki zungure mini hannu bakya zama waje guda" ta ce "abu na ji yana taɓa mini ƙafa" ya cije lips kawai ya cire hannunsa yana miƙa mata ya ce "Wanken ɓata ni da kika yi" ta juya ta ce "Ba ruwa ai, bari na ɗakko ruwa da bowl"

"Yanzu, ina so"

"To ai ba ruwa"

Ya ɗaga kafaɗa irin ina ruwansa ta ce "To ka suɗe mana" ya bubbuɗe idanunsa ya ce "Ƙafar taki zan suɗe?" Ta ce "To ba ƙazanta a ƙafata ai, to kawo ni na suɗe maka

hannun ai ba zan ji ƙyanƙyaminka ba" ya mata shiru ya sake tura mata hannun, ya kama dugwayen yatsun ta fara suɗe masa ya ce "Washh" ta yi sauri ta ce "Mene?"

"Washh, deer na gaji yi sauri bacci" ya ce kamar gaske.

Ta marairace ta ce "Sorry sweety"

Yatsun ta suɗe idanunsa a fuskarta, kafin ta gama goshinsa ya jiƙe jagab da gumi sosai ta ce "Gashi nan to, nama ya yi daɗi Allah ya ƙara arziƙi da wadata nawan ya karo arziƙi na halak" ya dai kalleta bai ce komai ba ta ɗauki yougourt ta sha ta ajjiye ta miƙe ta ce "Bari na ɗakko ruwa ka wanke hannun ko"

Ya ɗago ya ce "Wanne?"

"Naka"

"To ban gama jin ƙamshin tsiren ba" sai ta yi dariya ta ce "Wanne tsiren? Bana wanke maka ba?"

"E, sai yanzu ne nake jin ƙamshin" ta koma ta zauna ta yi shiru, shima shirun ya yi mata sunfi minti ashirin can ta ce "Baka ce na yi kyau ba, baka ce ƙunshin da kitson ya yi ba?" Ya yi shiru ta ce "Ba zaka ce na yi kyau ba?"

"A saboda ba ki yi bane"

Sai ta ji babu daɗi ta ce "Ai shikenan, amma kai ka yi kyau kana saka manyan kaya Please"

Ya miƙe zaune da kyau ya jingina da jikin bango ya ce "Kin tuna mini, zo na tsefe" ta buɗe ido ta ce "Wallahi na sha wahala a kitson ka bar shi kawai tunda an yi" ya

girgiza kai ya ce "Naaa..." Dole ta matsa kusa da shi ya nuna mata cinyarsa ta kalle shi, sai ya damƙo hannunta ya zaunar da ita a kan cinyar ta ɗan zame ta kwanta jikinsa shi kuma ya jingina da jikin bangon da kyau ta ce

"To ka iya tsefewa ne kar ka yi mini jagwalgwalo fa" ya yi shiru ya ƙurawa ƙananun kalbar idanu sun yi masifar kyau, ya kai hannunsa ya dinga shafawa ya taɓa wancan ya saki wancan can ya ce "Barewata kayan jikinki sun jiƙe sanyi sanyi" ta tura bakinta ta ce "Kai dai saka aiki ne da kai, ka ce wannan ka ce wancan, ba zan iya tashi ba gaskiya tunda na ji laushi kuma, bari na zame rigar" ta yi unzip ta sauke rigar ta sauka har wajan ƙirjinta, bata san yaushe aka yi hakan ba sai ji ta yi ya ƙarasa sauke rigar zuwa ƙasa, daga ita sai halpvest ta juya ta

kalle shi taga ba ita yake kallo ba

"Tsefe" ta ce

Ya tattaɓa kan sai ya ce "to fara biyana kuɗin tsiren" ta ce "Sai na shiga gida ai" ya ce

"Tab, yanzu za ki fito da su yarinya" musu suka fara tafkawa ya ce wallahi sai ta bashi daga ƙarshe aka sasanta akan za ta yi abin kuɗin ya ce bari yaga.

Hannunsa ya zura ta ƙasan hannunta ya ɗago ta sama ta sake mannewa a jikinsa ya haɗe hannu biyun ya rungumeta sosai sukai shiru, shi tunanin inda zai samu gidan da zai kai ta yake yi, yama mance da kuɗinsa na wajan Jaa'afar ko yau sai da Aby ya yi masa magana. Safiyyerh kuma hannunta a saman hannunsa tana wasa da yatsun hannunsa, shi kuma ya yi shiru idanunsa lumshe. "Bestie"

"Bestie"

"Uhm"

"Wai ya aka yi ka cire Aafiyyah lizards ranar nan" bai buɗe ido ba, bai kuma amsa ta ba ta juya ta kalle shi ta ce "Don Allah ka faɗa mini, ka mini alꞯawari ka ce watarana zaka faɗa mini ka ce zan yi dariya idan na ji, kuma na san cikin riga ƙadangarun suka shige mata faɗa mini"

"Bestie"

"Deer"

"Mutallab"

"Deer"

"Ka ce Safiyyerh"

"Uhm" ta ce "Talk please"

"Me?" Ta ce "Say Safiyyerh"

Ya ce "I can't". "Why? Ni na ce Mutallab ina son na ji ka ce Safiyyerh" ya buɗe idanunsa da ƙyar ya ɗora kansa a goshinta ya ce "Idan kin ce Mutallab ra'ayinki ne haka Abdullahi ya raɗa mini, kina da matsayin da ba zan faɗi sunanki ba ai" ta ce "Wanne matsayin?" Ya ja hancinta ya yi shiru, ta yi murmushi ya ce "Kamata nan" itama ta ce "Kama shi nan" ya ce "Matsa can" ta ce "Matsa can" a hankali ta ce "I love you" ya yi shiru.

"I love you"

"Thanks"

Idanunta ya yi rau rau sai ta yi shiru kawai ya ce "Biyani tsirena" hannunta ta saka a bayan wuyansa ta yanyo kansa ta sumbaci kuncinsa ta ce "Gashi nan" ta faɗa tana murmushi har ɓacin ran ya tafi ya goge sumbatar ya ce "Za ki mini dode ne?" Ta dinga kallonsa ya sake covering face nasu ya ce "Uhm'uhm ni dai biyani" tab ashe ace auta ne ai kam yanzu taga auta domin taɓarar da ya yi yanzu ko ita albarka, ta ɗora lips ɗinta a hankali saman nasa a hankali ta fara sumbatarsa tana yi masa wani irin special kisses zata janye bakinta ya sakar mata nauyin fuskarsa dole ta cigaba da abin da take yi shi kuma ya rirriƙe hannunta da gam.

"Hmm yෆen yෆen yෆen ƙazama"

Ya ce da sauri yana janyeta tare da yin rufda ciki ta ce "Ba kyau rufda ciki ka tashi" ya yi shiru ta ce "Allah ba kyau" ya ce "Kashe hasken ɗakin nan" ba tare data fahimci komai ba ta miƙe ta kashe hasken ɗakin ya yi duhu amma duk da haka ya yi rufda ciki ya maƙale, ta yi ya tashi yaƙi sai kawai ya bi bayansa a haka ta kwanta ta fara bashi labarai.

*

Cikin dare ne duka suna bacci kamar daga sama suka fara jiyo ihun Aafiyyah da wani irin sauti kamar ba ita ba. A tare Paaahh da Ummi da Mj suka fito sanye da kayan bacci masu sulɓi jikin Paaah har rawa yake yi ƙwarai ya nufi bedroom nata suna shiga suka hango Aafiyyah can ƙuriyar gado ta ƙanƙame jikinta waje guda kanta a hargitse kamar mahaukaciya Paaah ya matsa ya ce "Safiyyerh, Safiyyerh lafiya?" Amma ina jikinta rawa kawai yake bata ma so Paaah ya taɓa ta sai jan jiki gefe take yi ya miƙa hannunsa sai taɓa ta, ta fasa gigitaccen ihu ta hantsila ta ɓoye bayan Mj "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, ko gamo ta yi? Ko aljanu?" Cewar Ummi.

"Subuhanallahi!" In ji Paaah.

Mj ya janyo Aafiyyah data rufe idanunta, jikinta sai rawa yake a hankali ya ce "Aafiyyah?" Kasancewar ta ce su daina ce mata Safiyyerh bata so. Ta kasa magana sai ya rungumeta yana bubbuga bayanta ta yi lamo jikin Mj tana sauke ajjiyar zuciya, dungur haka ta kwana ba bacci ta dinga jin ana mata ihu a tsakiyar kanta

ana kiran sunanta bedroom ɗin ya dinga juya mata can ta ji kamar ana jan ƙafafuwanta wai za'a kai ta kabari.

"Yaya... Yaya..." Sai kuma luuu ta faɗa jikin Paaah babu numfashi, shima ɗin rungumeta ya yi kamar jaririya idanunsa ya kaɗa ya yi jajur sai kiran sunan Allah yake, ya rasa meke damunta tunda bata sake yi masa maganar Mutallab sai bai kawo hakan ba.

"Allah Alhakkamu" ya ce a tausashe yana shafa kanta, Ummi ta yi zaune bayan ta ci kuka ta ƙoshi ya dinga yi wa Aafiyyah tofi tana jikinsa suna zaune a haka har akai kiran sallar asuba, Mj na tsaye idanunsa jajur duk motsin da zuciyarsa za ta yi da tunanin Aafiyyah take yi can ya juya ya fita, wayarsa ya ɗakko neman duniya ya yi wa layin Safiyyerh a kashe, ya fara neman Kimiyya shima babu haka Kinal kashe Paaahh ya ce ya haramta musu zuwa Naija. "I am sorry Aafiyyah" ya ce cike da damuwa.

Da ƙyar Paaah ya je ya yi sallah ya dawo haka Ummi ganin kamar tana bacci bayan ta yi sallah suka ja mata ƙofar tare da ficewa.

"Alhassan lokaci ya yi ka fara zuwa wajan Safiyyerh ko fahimci juna ka ji? If possible ka zo ƙasar da muke I'll address you" cewar Paaah yana faɗin hakan ya shige part ɗinsa.

11:30 ta sakko kamar korarriya ko part ɗin Ummi bata je ba balle na masoyin nata Paaah bacci kawai take buƙatar yi ta kira number Shila domin ta bata irin lemon data bata amma wayar taƙi tafiya.

"Aafiyyah"

ta juya ta kalli Mj ya ce "Ina za ki?" Ta ce "Inda ka aike ni" bakinsa ya buɗe da tsananin mamaki ya ce "Favourite ni kike faɗawa hakan?" Ta yatsuna fuska ta ce "Who are you? Ka haife ni ne Mj? Ka daina yi mini shisshige" ta ce tana murguɗa masa bakinta, tsoro ya kama shi tsoron daya saka ya kasa yi mata magana har ta fice.

Tsananin damuwa da mamakin sauyin ɗabi'un Aafiyyah ne ya saka Mj bai tashi ba har ta dawo tun a ƙofar shigowa parlo ta yi cilli da jakarta da takalmi ta nemi faɗuwa ya yi saurin miƙewa ya taro ta hannunsa ta ture ta ce "leave Mj" bai barta ba ya kwantar da ita saman kujera ta juya ta ƙura masa idanu hawaye na fita daga cikin idanunta a haka bacci ya ɗauke ta.

Shanshanata ya fara yi ya ɗakko jakar ya bubbuɗe babu komai sai robar lemon coke ko sha ba ta yi ba, ya duba ya tabbatar lemo ne ya ajjiye ya sake dawowa ya shanshana Aafiyyah ya ce "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un" domin ji ya yi kamar tana wari ko ƙamshin club.

MUTALLAB PAID BOOK

08164069385

[1/7, 9:37 PM] Sis Fauzy: Chapter 44: The Message

Not edited 😂

MJ ya zubawa Aafiyyah idanu zuciyarsa na tsananin bugawa na tausayinta, he course everything, he is the reason behind, da ace ya bawa Aafiyyah dama ya ƙarfafa mata zuciya da qwwia wajan faɗawa Mutallab abin da yake zuriyarta duk da tarin ƙuruciya da yanzu ya san ba wannan maganar ake yi ba, wata daban ce.

"Mj me kake ka sata a gaba da kallo haka? Me ma take yi a parlo duk da wannan sanyin bayan ka san yanayin jikinta, sai limoniyyar ta ya tashi muzo muna fama?"

Mj ya juya ya kalli Ummi a hankali ya ce "Bacci take yi" ya faɗa a sanyaya yana ɗauke damuwar zuriya data fuskarsa. Waje Ummi ta nema ta zauna ta zubawa Aafiyyah idanu sai kuma ta juya ta kalli Mj cikin yanayin damuwa tana gyara zama ta ce

"Na tambayeka tsakani da Allah zaka bani amsar da nake buƙata Mj? Zaka iya mini wannan alfarmar?" Mj ya yi jim, sai ya ce "Ummi ai kin san baku gina mu akan yi muka ƙarya ba, ko da gaskiyarmu za ta yi sanadiyar hukunci a gare mu, za mu faɗa"

"Good, na ji daɗin hakan"

"Mene Ummi?" Cewar Mj

Ta yi jim sai ta sake kallon Aafiyyah kafin ta ce "Lamarin Safiyyerh tsoro yake bani, na san cewa ba wani jikin kirki gare ta ba

amma yadda kullum take ƙarewa kamar ana tsotsar jinin jikinta yafi bani tsoro, ba zan ɓoye maka ba kullum da tunaninta nake kwana nake tashi, na ji ta ce ta amince da batun auren da Paaah ya yi mata, kuma na yarda musamman da na ji bata sake ɗakko batun wancan yaron da aka mata al'ƙawari a kan shi ba. Amma bani da yaƙini da zuciyarta Safiyyerh nada tsananin wayo ta iya takun da baka isa ka gane sahun ƙafafuwanta, tana da faɗa idan an mata ba daidai ba, tana da tsiwa idan bata so ba, tana da magana musamman a cikinmu amma when it comes to jokes, she love entertainment, miskila ce ta ajin ƙarshe tana da surutu amma maganarta for some reason idan tana buƙatar abu wajan mutum...,"

Ummi ta yi shiru tana kama hannun Aafiyyah ta riƙe a hannunta, sai ta ji hannun zafi zau kamar garwashi. Ta ɗora da "two step ne da ita, shi ya saka gane mata yake da wahala, don Mj kai zan tambaya kafi sanin komai kana ganin da gaske ta amince da auren? Kuma ta bar batun wancan yaron da mahafinku ya yi mata al'ƙawarin aura mata idan ta gama makaranta ko yaya ne?"

"Ummi me ya saka kuka karya naku al'ƙawarin ne?"

"Shut up, why are you answering my question with a question?"

Cikin sauri ya ce "Ki yi haƙuri, ki yafe mini kin ji?" Ya ce yana rusunar da kan shi ƙasa.

Ta sauke ajjiyar zuciya "Ka bani amsar tambayar da na yi maka, idan babu kuma you may leave"

"Ummi kin san wace Safiyyerh, ita tun tana ƙarama kuna cewa bari Safiyyerh zata bari, kuma ta bar abin kenan ko da zai cutar da ita, ina jin sau ɗaya ta taɓa bijire muku lokacin data kafe ba zata wata ƙasar karatu ba tare da

takwararta zata yi karatu, ba kalar tashin hankalin da bamu gani ba, kuma bamu fuskanta ba, har ciwo ta kusa tana da ƙulafuci da saka abu rai tana da naci da taurin kai, tana da biyayya da saurin afuwa da yafiya. Kamar yadda ta ce da gaske ta amince haka ne, kuma ta bar wancan batun shima she is nothing but a darling yarinyar da kowanne iyaye suke buƙatar samu, amma don Allah kada a yi amfani da biyayyarta a cutar da ita, ku bata listing ears" Ummi ta tsare shi da idanu sai kuma ta yi murmushi ta ce "Why are you telling me this? Me ya saka kake faɗa mini duk wannan?"

"Ba komai"

Ya yi shiru kawai domin bashi da abin cewa can ya miƙe zuciyarsa a cunkushe ya nufi part ɗin Paaahh, ya jima yana knocking kafin a ce "Come in" ya tura ya shiga tsaye ya same shi kamar kodayaushe ya zubawa picture ɗin Safiyyerh idanu dake gefen frame nashi cikin kyakkyawar shigarsa.

"Daddy"

Ya juya a hankali jin kiran Mj ya kalli yaron nasa kafin ya ce "Ya akai Mj?" Cikin girmamawa ya ce "Ina son zuwa Nigeria Please"

"No!" Shine kawai abin da Paaah ya ce yana neman wajan zama ya zauna da kyau ba tare kuma daya sake kallon direction ɗin Mj ba, shima zaman ya gaji da shi ya miƙe ya fice ransa babu daɗi. Paaahh ya san auren AAFIYYAH da ALHASSAN was a destiny, ko bai zama destiny ma zai iya ce a promised marriage, baya taɓa saɓa

al'ƙawarin daya ɗaukarwa zuciyarsa ba zai kuma fara a kan yar cikinsa ba, ko da can ya yi amfani da ƙuruciyar Aafiyyah wajan wasa da tunaninta tare da tsayar da zuciyarta waje guda akan karatu baya son batun namiji domin ya san ya jima da ya yi mata mijin aure, mijinta na nan already, bai ɗauka tasirin alƙawarin da ya yi mata zai zauna a zuciyarta har haka ba, da kyau yake mamakin batun soyayyar da tazo masa da shi a baya, at her young age bai ci tunaninta ya bata cewa ta zo ta same shi akan batun ta ga mijin aure ba, sai dai ya mata a kullum zamani sauyawa yake kullum ana haifar yara masu tsananin wayo da kaifin basira ne, wasu yaran tunaninsu na fin ƙarfin shekarunsu ainun, kuma ita tarbiyya a wannan gaɓar tana da tsananin wahala, so mene nasa kuskuren? Alƙawarin da ya yi mata saboda yadda dashi da ta yi? Ko auren da ya ƙulla tsakaninta da Alhassan? Only God knows!

Har a ka kira sallar magariba tana kwance tana bacci bata ko motsi sai hucin numfashin dake fita ta hancinta mai ɗauke da fitar zazzafan zazzaɓi yadda ƙirjinta ke ɗagawa da ƙyar ya saka zaka fahimci ƙirjin ciwo yake mata, tana matuƙar shan wahala wajan yin numfashi. "Lafiya take wannan baccin kamar matacciyya?" Ya ce calmly yana gyara lins ɗin hannunsa. Ummi ta ce "Allah masani, kila ta samu sauƙi idan ta yi baccin wadatacce"

"Tashe ta" Paaah ya faɗa yana tsayawa tsakiyar parlon.

Tashin Aafiyyah ta fara, amma shiru ta dinga jijjigata amma shiru ta ce "Taƙi tashi fa" ya ƙarasa ya zauna ya fara tattaɓa kumatunta da kiran sunanta. Shanyayyun idanunta ta ƙyallaro masa da ƙyar cikin wata kalar murya ta ce "Dad....dad.... Daddy..." Sai ta yi shiru, hannunsa ya saka ya ɗago kafaɗunta yana girgizata sosai kana ya dire ta zaune kamar yadda yake mata tana yarinya, Aafiyyah tana tsananin ƙaunar bacci kullum faɗa ake idan za'a tashe ta. "Allah mai iko"

"Daddy.... Paaahh na, kyakkyawana, daddyna lovelyna"

Murmushi kawai ya yi mata, ya saka yatsa ya ɗalla mata mari ta buɗe idanunta da sukai jajur a hankali kuma hawaye ya fara cika idanunta sai ta yi saurin ƙasa da kanta ta ce "Ohh, ant idona" Ya kama fuskarta a hannunsu ya ce

"Safiyyerh"

Sai ta shagwaɓe fuska ta ce "Not Safiyyerh, Aafiyyah"

"Safiyyerh Abdu....,"

"Ka bar ta a Aafiyyah ɗin, mu huta da na ci ta mita" ya jinjina kai kawai ya ce "Ok Aafiyyah. Aafiyyah cry if you want, cry if you need, cry if you feel better"

"Kuka? The whole me na yi kuka ina da Paaahh no no never in sha Allah, ka cire mini ant a idanuna, idona ruwa yake yi" sai ya ji daɗi a ransa ya yarda ba kukan bane ba, sai buɗe idanun ta miƙe da sauri ta ce "Kwaron ya san Aafiyyah, ya gudu Paaahhh bari na yi sallah" da sauri ta shige bedroom ɗinta duka suka bita da idanu, ta juyo kaɗan ta yi murmushi tana murza idanunta har ta shige bedroom ta rufe ƙofa, kukan dake neman ƙwace mata saboda rauni na idanun mahaifi da tunanin kuma ta samu wajan kai kukanta, a yanzu sai ta ji kukan ya kama gabansa hawayen ya tafi zuciyar ta tsaya, ta dinga buɗe baki try to cry, but she couldn't. wani abu ya tsaya mata a ƙirji ya tokare maƙoshinta ya haddasa mata rashin shaƙar iska yadda ya kamata wacce zata sauka a ƙirjinta, a yadda ta yi shiru sai take ganin kamar mala'ikan ɗaukan rai malakul maut Azra'ilu na kusa da ita, jira yake ta motsa ya zare mata rai, ta mutu bata ganshi ba, ta mutu bai ganta ba, gudun wannan mutuwar da zuwan lokacin ya saka ta bubbuɗe idanunta wai kar ta yi bacci, kamar kuma abin almara sai ta fara ganin wai gashi nan yana zuwa wajanta dole zai rabata da duniyar, Aafiyyah ta daddage ta fasa ihu, without knowing cewa muryarta baya fita ihu take da kururuwa amma ita ɗaya ta fara ja da baya ta birkita ɗakinta tas ta hargitsa sumar kanta tare da yayyaga kayan jikinta.

"Safiyyerh"

"Safiyyerh"

Paaahh ya jera mata kiran, amma bai ganta ba ya ƙarasa shigowa yana dubawa cak ya yi ganinta da ya yi a ƙuryar gado kamar zautacciyya sumar nan ta yi ɗaiɗai kamar bishiya har wajan waist ɗinta babu cika sai masifar tsayi kamar an saka mata dayin saboda yadda sumar yake jaa. Ya durƙusa gabanta ya ce "Safiyyerh" taƙi ɗagowa ya dafa kafaɗarta kamar mai tsoron buɗe ido haka ta fara buɗe idanunta

tana ganin Paaahh ta riƙe hannunsa ta ce "Daddy wai kabari za a kai ni, ba zan mutu ba, ba yanzu zan mutu ba bana son mutuwa wai ni zan mutu" daidai nan Ummi ta shigo ta ce "Idan na ce aljanu sun kama yarinyar nan ka ce ba haka ba, wannan wani irin masifa ce duk dare bama bacci bamu da kwanciyar hankali" a hankali ya ce "Aljanu kuma?"

"E, su nake nufi hakan duk sharrin su ne, ai ji suka yi an fara batun aure kasan wasu a nan suke nuna wa wallahi" ta ce idanunta cike da hawaye sai kuma ta fashe da kuka.

Paaahh ya rungume Aafiyyah yana ta shafa kanta yana mata addu'a jikinta sai rawa yake yi ta kulle idanunta gam, da ƙyar ya samu ta yi shiru ta nutsu da kansa ya ɗaura mata alwala ta yi sallah ya ce "Yi addu'a" ta jinjina kai ta ɗaga hannunta ta yi shiru "Yi addu'a" a hankali idanunta a ƙafe ta ce "Me zan ce?"

"Addu'a"

"Ban san me zan ce ba"

"Duk tarin addu'oin da kika iya Aafiyyah? Addu'ar aka ce "

Aafiyyah ta juya ta kalli Ummi sai ta yi murmushi ta ce "Me zan ce"

"Tashi, zo nan" cewar Paaahh. A daren duk yadda aka so Aafiyyah ta yi bacci ta gagara yadda su kaga rana haka su kaga dare sun jikata sun sha wahala ta yi kamar mai hauka tuburan sai bayan sallar asuba ta ce "Bani lemo ne Mj" ya ɗakko lemon Paaah ya ce "Muga" ya amsa ya duba yaga nrml lemo ne baƙi ga suna da komai ya bata, tas ta shanye ta ajjiye abin ya ce "Yau Alhassan zai zo ku gaisa kin ji?" Ta buɗe idanu sai ta yi murmushi ta ce "Finally, yau zan ga mijina Allah ya kaimu" Ummi ta ce "Amin"

Mj ya ce "Kina son shi?"

Ta ɗaga idanunta daya fara lumshewa da ƙyar ta ce "Kamarya?"

"Shi Alhassan ɗin, nake tambaya kina son shi?"

"Kamarya kenan?" Ta ce silently tana binsa da idanu sai yatsuna fuska take yi. Daga nan kuma bacci ya ɗauke ta.

*

Finally secondary exam yake rubutawa sai ya tattara nutsuwarsa ga jarrabawa domin ya saka wa ransa cewa karatun kawai shine mafita a gare shi shine zai kai shi ga tubalin da yake son kai rayuwarsa zuwa ga tudun mun tsira, ba tambaya ya yi ba amma a ransa har yanzu yana mamakin rashin kimiyya a makarantar haka Nahyan sune kawai suke zuwa tunaninsa idan yazo makarantar hakan tuna tuna abubuwa da yawa banda marasa amfani. A hankali yake fitowa daga ɗakin jarrabawar daya samu ya kammala Finally paper today, hannunsa ɗaya riƙe da rigar makarantar sai yar ciki wacce da ƙyar aka samu ya yi a bayan rigar an rubuta MOH shine school nickname ɗinsa daman.

Ya jingina yana ƙarewa ajin daya fara rayuwa a ciki har kawo yanzu yanzu da yake cikin Ss3 A class gama makarantar yayi daidai da cikar sa 18yrs da watanni a duniya, idanunsa lumshe iskar wajan na kaɗa shi, ba zai taɓa mancewa da FGC ba, ba zai taɓa mantawa da tarin zunubai da alkairai data wanzar masa ba a rayuwa, labarinsa ba zai cika ba sai da sunan FGC domin ta zama abu mai tsananin tarihi a gare shi da duniyarsa the unforgettable thing. Ya shafi awa guda tsaye kafin ya saka hannunsa ɗaya cikin aljihu ɗaya riƙe da rigarsa sumar kan nan nasa luf sai ɗaukan idanu take yana tafe ƙirjinsa na motsawa six packs ɗinsa kamar mai ɗaga ƙarfe asalin kyan fuskarsa na jinin yarabawa ya bayyana musamman manyan idanunsa, dark-skinned ta sake nuna kanta har shinny take baƙi mai wahalar samu mai tsananin kyau kyan daya ninka na farin mutum, ya amsa sunan Blackman a zahirance.

"Muhammad Mutallab Abdullahi, inkiya MOH, jinin talakawa ɗan gidan mai almajirai". Ya ji an furta a bayansa, a sautin farko da ya gane mallakin muryar sai ya share domin bashi da wannan isasshen lokacin. Ganin ya ci-gaba da tafiya ya saka Captain shan gaban Mutallab yana murmushi ya ce.

"Saboda kai kawai na shigo makarantar nan, saboda na faɗa maka wani abu Ɗan'malam"

Moh ya yi shiru, Captain ya ce "Ka samu Safiyyerh ka ji daɗi, ka rabani da first love ɗina ka yi farinciki, ba kai zanwa baƙinciki ba, ita Safiyyerh ita nake tauysawa domin zata zauna wajan wanda ba zai ƙare ta da komai ba a rayuwa, na farko ba sonta kake ba, duk makarantar nan sun shaida baka son Safiyyerh ni da nake son ta Ka bar ni da ita kaƙi, na biyu baka da arziƙin da zaka kula da ita. Zan baka shawara ka yi ƙoƙari iya ƙoƙarin ka wajan kyautata mata ka fara cin moriyar auren ku..,"

Sai Captain ya buɗe ido ya ce "Oh no, ashe fa har yanzu kuna matakin Adolescencet stage ne, har yanzu ku yara ne, maybe dai ni zan fara zama namiji a wajan Safiyyerh, domin wallahi wallahi sai ta dawo gare ni, sai na mallake ta ba zan taɓa barinka ba, na faɗa maka wannan ne ka sani. MOH ina da sirrin da kake ɓoyewa, wanda kai baka san cewa wani ya sani ba, ka fara tuna ɓarnar daka aikata a ranar da aka zo da ambulance aka tafi da Aafiyyah, not a kisses.... Not only a kisses!"

Captain ya dinga dariya yana tafa hannunsa ya ce "I watched it, I watched you, i watched everything, playboy"

“Aafiyyah” haka Mutallab ya ji sunan a cikin kan shi da tunaninsa, a hankali kuma sunan ya dinga saukar masa a ƙwaƙwalwa da zuciya, who is Aafiyyah? Shi ne tambayar da ya kewa kan shi, ya kasa tunawa sunan gabaɗaya, sai ya wanzuw da tunani shuɗewar ranar, e tabbas ya samu matsalar motsawar taɓin hankalinsa a cikin aji baya ga haka ba zai iya fahimtar komai ba sai ya ɗaga idanunsa masu zubin sexcy eyes ya kalli Captain ya ce.

"Wanne sirri?"

"Ka manta? ka manta abin da ka yi wa Aafiyyah a lokacin? Ko haka kawai aka zo da ambulance ɗaukan ta? Ni ba wannan ba ka fara lissafawa ranar ƙarshe da zata zame muku kai da Safiyyerh, shine abin da ya kawo ni" yana cewa haka ya barin wajan da sauri yana yi wa MOH dariya.

Da idanu ya bi bayan Captain, daidai nan kuma Kinal ta ƙarasu tana murmushin ta ce. "Congratulations MOH, yau dai bari na yi maka magana ina tunanin sau ɗaya magana ta taɓa haɗa mu, ita ma ni na yi sanda ka zo duba note nawa. Ina maka murnar kammala karatu, sai kuma lokaci ya sake haɗa mu maybe ko a Jami'a ne" Kinal ta ce tana masa murmushi, wani waje can yake kalla nada ban bai ce komai ba ta sake cewa.

"Ya Safiyyerh?"

Sai ya juyo ya kalle ta, zuriyarta ta buga da ƙarfi domin bata taɓa ganin wani da irin ƙwayar idanun MOH ba. Ya jinjina mata kai ya fara tafiya a hankali sai kuma ya dawo da baya ya kalle ta da ƙyar ya yi tear out na maganarsa ya ce

"Who is Aafiyyah?"

"Your classmate" ta bashi amsa.

Ya yi jim, sai kuma ya ɗaga kafaɗa ya ce "Oh" ya yi gaba abinsa.

"Kan uba, kai ba kuɗi ba, ba mulki ba sai masifar ɗagawa da faɗin ran masifa, tabɗimjam"

Sai ta duba yadda yake tafiya cike da mazantaka da izza da cikakkiyar lafiya da kuzari irin na kowanne ɗa namiji, he walks like a king not as Ɗan'malam.

Daya isa gida shago ya shiga ya kwanta jin zazzaɓi na neman cin masa, kansa ya fara wani irin masifaffen ciwo yana sarawa da ƙyar yake buɗe idanunsa, ya dinga jin amsa kuwwa a cikin kansa ya fara ƙoƙarin yin processing na maganar Captain amma ya kasa, abu ɗaya ƙwaƙwalwarsa da idanunsa suke tunawa, she kneel on her feet, begging him to stop, kar ya yi, sai kuma sautin kukan da ya ƙushi

kamar hadda cizo ba, but; stop what? Shine bai gane ba idan ka ɗauke waɗannan abubuwan ba abin da ya yi tunanin sai the darkness duhun wajan, cikin librar the old library dake bayan can school wajan lap-room. Da ƙyar ya iya miƙewa jin ana kiran sallar asr ya fito waje, wandon FGC ne a jikinsa sai rigar graduation ɗin wacce ta zama ash, a haka ya yi sallah ya nufi cikin gidan kai tsaye yana jin ciwon na ƙara saukar masa.

Safiyyerh na zaune bata jima da shigowa daga maƙota ba, tana ƙulla kantu ya shigo ta ɗaga kai ta kalle shi suka haɗa ido, ganin yanayinsa sai ta sha jinin jikinta kawai ta ɗauke kanta bata ce masa komai ba Ammo ta ce "wasalamu Alaika, har ka dawo" ta amsa domin tana da yaƙinin ba zai shigo ba sallama ba

Ya nemi waje can bakin gadonta ya jingina ya harɗe hannunsa a ƙirji can Ammo ta ji ya ce "Munee" ta yi saurin ɗago kai gabanta na faɗuwa ta ce "Baka da lafiya?"

Sai Safiyyerh ta ce "Bestie baka da lafiya? Innalillahi mene ya same ka?" Ta ce a rikice ta manta da Ammo shi kuma ya tsuke fuska kawai Ammo ta miƙe tsaye ta ce "Ai tunda ya ce Munee bashi da lafiya, ina zuwa Safiyyerh" ta ce tana fita. Safiyyerh ta ƙarasa ta zauna kusa da shi kamar jira yake ya kwanto jikinta ya ce "Wash beb..." Ya ce a shagwaɓe sai ta ji kansa zafi idanunta ya cika da ƙwalla ta ce "Baka da lafiya?" Bai taɓa cewa bashi da lafiya ba sai ya samu kan shi da cewa "Ciwo Deer"

Ya ce yana shigewa jikinta. Idanunta ya cika da hawaye ta shafa kan shi ta ce "Sannu, da sauƙi ai ko? Meke maka ciwo?"

Ya girgiza kai yana kama hannunta ta ce "Da sauƙi?"

"Uhm babu" ya ce shortly.

"Na baka abinci? Sai ka sha magani ko?" Ya maƙale mata kafaɗa ta ce "Me kake so"

"You" ya ce.

"Ni kake so?"

Ya buɗe idanunsa da kyau ya kalli fuskarta ya ce "Me na ce?"

"Ka ce kana so na"

Ya girgiza kai ya ce "You're not serious, ba haka ba" sai ta yi murmushi ta ce "To ai daman ban yadda ba, saboda ba so na kake ba, ni dai yanzu me kake so?"

"You" ya sake cewa.

Sai ta yi shiru, sam bata jin zafin maganarsa koda wasa balle gaske ya ɗaga mata gira ya ce "Barewata" ta ce "Mai dawa"

"Sumbace ni"

Ta harare shi ta ce "Magani na ce ka sha fa, magani na ce" shima ya harareta ya ce "Shi ne maganin" ta saka hannunta ta dungure masa kai ya ce "Washh" ta yi saurin cewa "Sorry, idan so kake why not ka yi requesting sai na yi approve"

"Ke za ki request and approve ɗin"

"Why not you?"

Ya ɗaga mata kafaɗa sai ta ɗakko wayarta ta miƙa masa ta ce "Yi searching a nan na gani nima" ya zuba mata idanu sai ya miƙa mata hannunsa zai amsa da sauri kuma ta ƙwace wayar domin a lokacin picture ɗin Aafiyyah take kallo, ya tsare ta da idanu yana miƙa mata hannunsa alamar ta bashi ta ce "A'a, zan yi maka kawai, zan

koya maka" sai taga ya yi murmushi kawai ta ce "Mene?" Ya ɗaga shoulders ɗinsa yana ci-gaba da murmushi duk da tsananin ciwon da yake jin kan shi na yi masa.

"Na fara gajiya murmushin mene kake yi haka ne? Faɗa mini"

"Ba ki da gaskiya, Allah ba ki da gaskiya Safiyyerh ba ki da gaskiya" ya ce yana yin baya tare da yin murmushi fafaren haƙoransa a bayyane yana rufe idanu. Ta yi shiru jiki a sanyaye sai ta ce "Rashin gaskiyar me na yi?" Ya mata banza, ta fara yi masa na ci sosai sai ya miƙe tare da figota zuwa cinyarsa ya kama hannunta ya riƙe ya ce

"Kalli idona"

Ta kalli cikin idanunsa sosai sai ya ce "Yau kin yi mafarkina, yau kin yi wanka domin ni, yau kin yi ciwon mara, yau kin yi ciwon ciki, yau dai da muradina kika yini"

Ta kwace hannunta ta ce "Ba haka bane, Allah ya sauwaƙe"

Ya tuntsire da dariya ita abin har mamaki yake bata ya ce "Tun ina yaro ai bana ƙarya balle yanzu"

"To, ta ya ka sani?"

Ya yi shiru. Ta ce "Ya ka sani? Ban yarda da kai ba Allah duba kake?"

"Eh" kawai ya ce.

Sai ya kwanta ya ce "Ki yi addu'a na kai ki gidanki, bana son kai hannuna jininki yarinya" sai ta lura da zufar goshinsa ta dinga kallonsa sai ta miƙa hannunta ta fara shafa lips ɗinsa, idanunsa rufe a hankali kuma ta fara kissing nasa, jikinta kuma duk

rawa yake yi, baya motsi sai yawan zufarsa data ƙaro har tana sakkowa, ta buɗe ido jin abin da yake mata kunya ya kamata ya shafa kanta ya ce "Allahumma Barik" ta yi shiru. Shi ya san me take tunani ya kuma san me take so ɗin, ta juya masa baya bai kulata ba ya yi shiru shima, Ammo na can neman maganin da take bashi duk da baya sha.

*

SSS state security service

Gabaɗaya jami'an tsaron sun haɗu kana ganin kowa ka san yana cikin tashin hankali, yana tsaye tare da kallon su ɗaya bayan ɗaya cikin baƙar suit ɗinsa a hankali ya ce "Akwai information ne?"

"Har yanzu" cewar.

DIG JOHAR ya jinjina kai yana sake kallon su a hankali ya fara tafiya yana kewaye wajan kana ya dawo baya ya ce "Batu ne akan neman bindigar IMI TAVOR, wacce jami'an mu suke amfani da ita tana daga cikin daidaitun bindigon harin SSS combat operatives/ security protection officers (SPO) IMI TAVOR Tar-21, wanda ɗaya daga cikin jami'in mu ya ci amanar mu, mun samu guda ɗaya daga sama kuma an ce lallai a fito da ɗayar domin barazana ce ga ƙasa muddin akan mune muka yi saken da aka ɗauke"

Ɗaya daga cikin jami'an ya ce "Sir, muna nan muna bincike in sha Allah za mu yi nasara"

DIG JOHAR ya jinjina kansa ya ce "A wajan wa aka samu ɗayar ma?"

"Sir, mun manta sunan shi amma akwai reported da aka shigar, wajan wani yaro ne" DIG JOHAR ya ce "Aje a kawo mini report ɗin now" suka ƙame tare da cewa "Yes sir" fita suka yi, shi kuma ya nemi waje ya tsaya kyam hannunsa a baya ya yi shiru yana tunani, a hankali kuma yake duba agogon hannunsa. Ba jimawa ɗaya daga cikin team ɗin suka ya dawo a ruɗe ya ce "Sir" ya ce yana sarawa Dig Johar ya kalle

shi da alamar ya aka yi? Ya ce "Sir akwai matsala, we missed the report ba komai an goge komai babu"

A gigice ya ce "What? Impossible "

Ya ce ya ficewa da gudu daga cikin hall meeting ɗin.

*

Ammo ta kalli Uncle Ade ta ce "Ashe kana hanya?" Ya ce "E, nama samu matsalar hanya da tuni na ƙarasu ai, ya wajan su Tayo da sauran yaran" Ammo ta yi murmushi ta ce "Ya yi aure fa"

"Tayo ɗin?"

"In sha Allah, wajan shekaru" a taƙaice ta faɗa masa yadda komai ya faru sai Uncle Ade ya ce "Ikon Allah, Allahu Akbar, Allah Ya sanya musu albarka ni kam na ji daɗin auren nan sosai, na san dole ya rage wasu abubuwan Allah Ya bashi wuyan ɗauka" Ammo ta ce "Amin, ai ya kammala karatu ma" sosai a nan ma Ade ya yi mamaki sai ya lura kuma akwai damuwa a tattare da Ammo ɗin ya ce.

"Akwai matsala ne?"

"E, yaya. Mutallab bashi da ƙarfi mahaifinsa kullum magana yake akan ya samu gida ya ɗauke yarinyar mutane, abubuwan da suke faruwa bana jin daɗinsu kawai ina ɗauke kai ne saboda bani da wani zaɓi, bana jin daɗin yadda yarinyar ke binsa zuwa shago hakan ba ɗabi'ar arziƙi bace ko na faɗa ko bana faɗa ba, dole akwai masu saka musu idanu kuma rashin kunya da fitsara, tsakanin mata da miji sai Allah ba zan iya hana Safiyyerh zuwa wajan mijinta ba, kuma ba zan bari a yi abin da bai dace ba a cikin ɗakin nan, amma Yaya zaman shago ba daidai bane duk da na san babu haramci ga hakan amma ya saɓa dokar musulunci idanu guba ne, ɗabi'un Mutallab sun sauya ina tsoron ya faɗa muguwar hanya, na san ina da saka hannu a duk abin da ya zama, amma komai ya zama sanadin mahaifinsa ne"

Uncle Ade ya ce "Haka ne, kina da gaskiya jin daɗin dai matarsa ce ni kuma gare ni ba wani abu bane don ta je inda yake"

"Yaya kai fa dabanne, ba zan kira ka da Hausa Fulani ba, Yaruba za su iya komai shi ya saka gabaɗaya an Mutallab ɗabi'unku ya ɗakko"

"Ba'a sauya tuwo suna ai, you're also Yaruba ai".

Ta yi murmushi ya ce "Babu damuwa, akwai kuɗi wajena zamu zaga da shi a nemi gidan hanya ko na shekaru uku ne na biya masa, sai a gyara inda yake da buƙatar gyara ko? Hakan ba zai gagara ba in sha Allah" sai daɗi ya kama Ammo ta dinga godiya sosai ta ce "Amma ita yarinyar bata da kayan ɗaki da abubuwan mata" nan ma ya ce "Ba zai gagara ba, zan yi iya ƙokarina abin da babu sai ya yi mata a hankali, ya ciwon nasa"

Ta ce "Ya jima bai motsa ba gaskiya, daman ai ka ce likitoci sun ce zai dinga jimawa bai motsa ba sai idan abu ya yi wa kan shi yawa ko?" Ya ce "Haka ne"

Hira suka cigaba da yi a haka Safiyyerh ta yi sallama zata juya ya ce "Shigo mana daughter" shiga ta yi tana raɓewa ta gaishe shi, ya amsa da fara'a yana yaba kyanta da nutsuwarta ya dinga janta da hira sosai a haka Mutallab ya shigo shima, duk kame fuskar Mutallab da yaga uncle Ade sai da ya yi murmushi yana tsananin ƙaunar uncle ɗin nasa, har ƙasan zuciyarsa yake jin soyayyarsa sosai daga ƙarshe suka fita neman gidan haya ɗin duk da MUTALLAB ya so ya bijire ɗin. Har magariba basu dawo ba, sai da suka samu wani gida can aka biya komai.

*

Ali wali ya dinga juya kujerar da yake kai ya dubi wanda yake gabansa kafin ya ce "zuwa gobe safe jirgina zai tashi zuwa Abuja, yana da kyau a gabatar mini da aikina domin na fara samun matsala a the green chamber, zauren Majalisar tarayya, matsayin da ake ƙoƙarin bani ana shirin ɗauka a bawa Bebeji, ni kuma ban shirya ba ina buƙatar muƙamin domin cika wannan sharaɗin malamin dole ne a yi aikin nan" cewar Ali wali.

Mutumin ya ce "Sir, amma ka san cewa duka yaran suna hannu tun kama su da aka yi"

"Oh no! bari zan yi magana za a saki wasu daga ciki kar ka damu"

Sallama sukai kana suka rabu.

*

Aafiyyah ta zubawa waje guda idanu, tunda kuma ta shigo parlon bata ce komai ba, ta hardɛ ƙafafuwanta dɗaya kan dɗaya kyakkyawar shigar turawa ce a jikinta mai tsafta. A hankali ta dɗago kai ta kalle shi tunda ya fara maganar bata ce komai ba sai yanzu, suka haɗa idanu, sai taga gabadɗaya babu wannan abubuwan da suke cikin idanun Mutallab babu shi, babu nutsuwar da take ji idan ta kalli cikin idanun Mutallab ta glasses.

"Iike your style"

"Thanks" ta ce, sai yanzu kuma ya ji muryarta a tsayin minti wajan 40 da suka yi. Alhassan ya ji ya nutsu da Aafiyyah kuma yana son ta, domin bai taɓa zaton kyan Aafiyyah ya kai har haka ba, bai taɓa tunanin ajinta ya kai haka ba, sai ya ji completely ta birge shi. "Sunana Alhassan ana ce....,"

"No need" ta ce a miskilance.

"Amma da buƙatar mu gabatar junanmu na san wace ke, kema ki san waye wanda za ki aura"

Ta dɗago shanyayyun idanunta tana jin kamar ana fusgarta ta fita sai ta ce "Na amince da auren ai, sauran bayanin ba sai na ji ba"

"Ok, ok.... Hakan ya yi"

Ya miƙe tsaye kyakkyawa ne fari tas da shi ga kuɗi ga aji ya ce "Zan je sai mun yi magana, i love you Aafiyyah kin kama mini zuciya" ta yi masa banza har ya fice daga cikin ɗakin, yana fita ta ɗakko wayarta ta fara duba picture ɗin Mutallab wanda ta yi musu shi da Safiyyerh a lokacin tana cewa "Ga wasu sabbin ƙinƙisa lemme snap them" addu'ar take masa a kullum idan taga picture ɗin a yanzu ita ta nema ta rasa, ta shafa fuskarsa ta ce "Na san abin da ya faru kuskure ne, ban san yadda zan yi wa su Paaah bayani ba, shine karo na farko da na yi musu ƙarya dominka saboda kai, ina neman yafiyar Ubangiji"

Hawaye na zubu mata ta sake shafa fuskarsa ta ce "Na san baka sani ba, na kuma yi maka uzuri kawai dai har na ja numfashina na ƙarshe ba zan manta ranar ba, ba zan manta FGC ba, no one knows but only Mj, zai mini wannan rufin asirin" sai ta yi murmushi ta ce "Ta zan iya auren waninka? Ta ya zan iya yi wa wanda na aura bayani? Don Allah Blackman come back to me, ka tuna ni ka tuna komai da kanta, wannan tsanar soyayya ce" kuka ta fara da ƙarfi gaske jikinta kuma na rawa ta shiga WhatsApp ɗinta domin ta manta, already gidan akwai WiFi bata chat da kowa sai saƙon Safiyyerh ya shigo, voice ne da rubutu kawai jikinta na rawa ta buɗe voice ɗin muryar Safiyyerh ce ta fara sauka a kunnen Aafiyyah da take cewa;

“To ni mene laifina don wani ya ce na burge shi?ba shi za kaiwa faɗa ba? Ni ka sake ni na tafi tunda faɗa ka yi mini ba ruwana da kai”

Aafiyyah ta yi murmushi tana cire talmanta ta yi zaman dirshen a wajan ta ce "Oh my love Safiyyerh, you never known your lover, just shout at him too, shout Safiyyerh"

Ita kaɗai Aafiyyah ta dinga surutai tana sauran conversation ɗin, har aka zo inda muryar Mutallab ta yi mata dirar mikiya a zuciya ta fara farfaɗo mata da mikin dake zuriyarta, wani abu ya dinga motsawa a ƙirjin Aafiyyah yana raya kan shi da kan shi dalilin jin muryar BLACKMAN.

“Rungume ki fa zan yi, idan kikai asara shikenan, ki zo mu yi sallama ina da farautar da zani” haka Aafiyyah ta ji muryar Mutallab yana magana, da wani

irin sautin da a wajensa kawai take ji. Sai ta fara dariya ta ce "Subuhanallahi, his voice" sai ya ji ya sake cewa “Shhhh” sai kuma ta ji muryar Safiyyerh ta ce

“My love is back”

“Kuma forever"

“Na ji me ka ce ai”

"What?”

“I love you too Safiyyerh!”

Da sauri Aafiyyah ta yi cilli da wayar tana ƙanƙame jikinta, idan Mutallab ya ce abu to he meant it, lallai yana son Safiyyerh sai ta ji ba ta ji baƙin ciki ba, kawai wani abu ta ji me kama da kishi, to ita fa? Yana son ta? Kˆila baya son ta tunda yaƙi nemanta tsayin shekarun nan "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, Yaa Muhammad don't do this to me, ka bari mu haɗu ina da abin faɗa maka wayyo Allah na wayyo ni Aafiyyah na shiga uku" da sauri ta ɗauki wayar ta duba last rubutun Safiyyerh bayan voice ɗin abin da taga Safiyyerh ta rubuta mata, fata a rayuwa ta yi wa wani irin rubutun sai ta ji numfashinta ya tsaya ya fige rolling ɗin kanta ta miƙe tsaye ta fara ja da baya, sai ta ji bacci take ji lemon ta ɗakko wanda bata rabuwa dashi, ta shanye tas.

"Aafiyyah" ta ji kiran sunan Paaah, da sauri ta buga wayarta da ƙasa daidai sanda yake zuwa wajan ba tare daya lura da abin da Aafiyyah ta yi ba. Yana zuwa Aafiyyah ta fashe da kuka ta ce "Daddy my phone, wayata ta fashe" ta ƙanƙame Paaahh tana rushewa da wani irin raunataccen kuka numfashinta na ɗaukewa, riƙe ta ya yi ya san ba iya kukan wayar bane dole akwai wani abu, sai ya tuna ta saba kukan banza dama, Paaah ya buɗe idanunsa jin kamar motsi ta cikin Aafiyyah.

MUTALLAB

PAID BOOK

08164069385

A PAGE 50 ZAMU DAWO LABARI, BOOK 2 ZAMU FARA A TELEGRAM ALREADY KUN SANI IDAN KUNA DA TELEGRAM FINE IDAN BABU A GAGGAUTA BUƊEWA 😁DAMAN WASU ALREADY SUN BUƊE DOMIN MUTALLAB.

GODIYA GA ANTY MERO AS ALWAYS, GODIYA GA KHADHASFSUM. INA SAKE GAIDA ANTY AISHAMADAWAKI

[1/7, 9:37 PM] Sis Fauzy: Chapter 45: I am coming

Paaahh ya sake riƙe Aafiyyah domin ya tabbatar da abin da yake ji, motsin dai ya sake ji a cikin nata, ya yi saurin janye ta daga jikinsa zuciyarsa na rawa kamar yadda jikinsa yake yi. Ya dinga bin Aafiyyah da wani irin kallo na tsoro da mamaki jiri na neman yasar da shi a ƙasa.

Da ƙyar ya ce "Aafiyyah"

Launin idanun Paaah ya saka Aafiyyah nata ƙirjin bugawa da matsanancin ƙarfi, za ta juya ya damƙo hannunta ya miƙa hannunsa zuwa cikinta da niyyar taɓawa sai ta yi saurin girgiza rigar jikinta a hankali ribbon ɗin daya faɗa cikin rigarta ya zazzago zuwa ƙasa. Paaah ya bi ribbon da kallo mai laushi, sai ya yi ajjiyar zuciya a ɓoye yana da yaƙinin motsin da ya ji na ribbon ɗinne, sai ya fara tunanin how smart she is, ya ji zuciyarsa ta kasa nutsuwa a hankali ya ce "Ki same ni a part ɗina yanzu" ya ce yana juyawa tare da barin wajan yana mai kiran wata number ya a hankali ya ce "Dr, ina buƙatar ganinka yanzu, yanzu fa yau ɗin nan?"

Shiru ya yi sai ya ɗora da "Ina buƙatar gwajin ciki, amma secretly" ya ce yana ficewa.

"Pregnancy test?" Aafiyyah ta maimaita a fili tana zazzaro idanunta waje, sai kuma ta yi baya ta jingina jin jira zai yar da ita, cikin sauri ta saka hannunta ta toshe bakinta saboda kukan da yake shirin ƙwace mata, yadda ƙafafuwanta suke rawa ya haddasa mata sulalewa a wajan ta durƙushe akan qwiwoyinta a hankali ta ɗaga hannunta ta ɗora saman cikinta tana lumshe idanunta hawaye masu zafi na sakkowa daga cikinsu, sai kuma ta yi murmushi jin wani abu nada ban, ta sake maimaita kalmar gwajin ciki? Sai ta shiga girgiza kanta da sauri ta miƙe bayan ta kwashe kayanta na wajan, kai tsaye part ɗinta ta nufa ba jimawa ta sakko fuska duk a jeme.

Ummi ta bi Aafiyyah da kallo kafin ta ce "wannan zaryar ta mece kuma kike mana ita?"

"Cake zan ɗauka" Aafiyyah ta bawa Ummi amsa, cikin sauri ta shige kitchen ta samu Glory na aiki "Good day Madam"

Ba tare data kalli Glory ba ta ce "Can you help me?" Cikin sauri ta ce "Madam mai zai hana?"

"Ruwa a freezer na parlo, mara sanyi" cikin sauri Glory ta yi waje jin daɗin yau Aafiyyah ta yi mata magana, banda haka tunda ta fara ganin Aafiyyah ko maganarta bata taɓa ji ba, sai ta gama zaman parlo ko tarinta baka ji ba, yanzu kuma ba fitowa take yi ba gabaɗaya ba ma. Glory na fita Aafiyyah ta ɗauki ƙaramin cup ta zuba ruwan zafi a ciki, da sauri ta ɗauki spoon ta buɗe robar salt dake ƙaramin cokali ne sai ta ɗibi gishiri cikin cokalin ta zuba a ruwan zafin ta jujjuya, tana gamawa ta ɗauki ruwan ta kafa a bakinta ta shanye duk da zafin da ruwan da yake da shi, da kuma rashin daɗin ruwan da gishiri ya yi yawa. Wanke cup ɗin ta yi ta mayar inda yake daidai nan Glory ta dawo tana murmushi ta ce

"Madam, ga shi sai dana zaɓo"

Kallo ɗaya Aafiyyah ta yi mata, sai ta ɗauke tare da ficewa ba tare data tanka Glory ko amsawar ruwan ba. Har lokacin Ummi na zaune tana kallon news arise t.v ta sake kallon Aafiyyah ta ce "Ina cake ɗin?" Aafiyyah ta bubbuɗe idanunta domin har ta manta da batun wani cake sai juya idanunta take yi ta kasa magana.

"Ina cake ɗin?"

"Kamarya?" Ta tambayi Ummi, sai Ummi ta yi mata daƙuwa ta ce "Kamar haka, ba cewa kikai cake za ki ɗakko ba?" Sai ta buɗe ido ta ce "Ohh, na fasa ai" bata bawa Ummi damar yin wata maganar ba ta yi saurin shigewa bedroom ɗinta ta rufe ƙofa, a hankali ta zaune jikin gadon ta janyo teddy nata ta rungume, ita dai ta san cewa bata da wani abu da za ta yi a rayuwa wanda ya shige yi wa iyayenta biyayya, kuma tana ƙoƙarin hakan, bata san mene ya saka suka ɗauki al'ƙawarin da baza su iya cika mata ma, ta cika nata su sun kasa yi mata wannan alfarmar, duk yadda take ƙoƙarin jurewa amma zuciyarta taƙi bata

wannan damar, tana zama ta yi tunanin akan abu ta nemi shawara amma yanzu tunani na tsananin yi mata wahala, ta yadda zata auri Alhassan amma su fahimce ta, tana buƙatar ganin Blackman tana son faɗa masa abin da bai sani ba. "Na shiga uku" ta furta da ƙyar laɓɓanta duk ya bushe. Ga ramewa ta rashin dalili. Loss of body weight, cin abinci yana mata tsakanin wahala ta shiga cikin loss of appetite, sai tai ta ganin abubuwan da ba kowa ke ganinsa ba, ko zuciyarta ta dinga yi mata tunanin abubuwan da babu su a duniya, yanayin mai kama da hallucination da delusion ta dinga jinta a birkice like anxiety, da yanayin panic attack cikin halin tsoro da razani.

"Aafiyyah think, yi tunani"

Zuciyarta ke faɗa mata, amma sama bata ganewa bama ta fahimtar komai har tsayin lokaci tana zaune a wajan bata motsawa. A hankali aka buɗe ƙofa tare da shigowa, ta ɗago kanta gently sai ta yi sak ganin wanda yake tsaye kamar bata gane shi ba, sai kuma ta ɗauke kai wa a hankali ya ce "Safiyyerh!" Ta sake ɗago kai sai kuma ta janye idanunta.

Paaah da yake tsaye ya ce "Bata ta kawo maka abin da kake buƙata mana Dr, zo ki amsa" Dr ya bawa Paaah ƙaramar robar hannunsa shi kuma ya miƙawa Aafiyyah ya ce "Ki kawo fitsarinki a nan"

"Dad...."

"No question"

Ta miƙe ta nufi toilet, ba jimawa ta dawo ta miƙawa Dr ɗin ba tare data kalle shi ba, ta nemi waje ta zauna fuskarta babu walwala ta cika kamar ta fashe ƙiris take jira, hakan ya saka duka basu kulata ba suka fita daga cikin bedroom ɗin. Wayarta ƙarama ta ɗakko ta fara kiran Shila ba jimawa ta ɗakko daga can ɓangaren Shila aka ce "Hi Aafiyyah ykk?"

"Shila wannan juice ɗin yana da bambanci da wani ne?"

"Hello, Hallo bana jinki bari na ɗan fita zan kira ki yanzu"

"Mtwsss" Aafiyyah ta saki siririn tsaki, domin ƙarar kiɗa ne ya cika mata kunne tana zaune sai ga kiran Shila ta yi kamar ta share sai kuma ta ɗauka Shila ta ce "You said something? Me kika ce?". "Mj ya je siyo mini juice ɗin nan ya kuma samu iri ɗaya amma baya sani bacci, bana iya bacci ina buƙatar yin bacci Shila ina kike siyo naki ne?" Murmushin Shila ya fito a bayyane kafin ya ce "Ko yanzu ina da wani mai kyau ma, kina sha za ki yi bacci damuwarki zai yaye In sha Allah"

Aafiyyah ta rufe idanunta ta ja numfashi ta ce "Ki kawo mini"

"I can't, ba zan iya barin inda nake ba, idan kina buƙata ki zo kawai ki amsa Aafiyyah, kin ji"

Aafiyyah shiru ta yi, sai Shila ta ce "Za ki zo?" A hankali ta ce "Ina ne?" Ta ce "Club ne, kina zuwa sai ki kira ni na ba ki ko?"

"No, ba zan iya zuwa club ba, Allah Ya sauwaƙe ki kawo mini kin ji Please" ta faɗa a marairace, domin da gaske tana buƙata ji take kamar kanta zai yi bindiga komai ya daina yi mata daɗi bata son komai, bata son shiga cikin mutane baya son hayaniya ko farinciki ma bata so rayuwarta bata cancanci komai ba yanzu.

"Aafiyyah ki haƙura to, ba zan iya zuwa ba, zan tura miki address idan kin yi shawara shikenan" tana cewa haka ta kashe wayar, Aafiyyah ta shiga tunani ba lallai Shila ta kawo mata ba, idan Shila tazo ma ba lallai Paaahh ya bari ta shigo ba, kawai ta ji zuciyarta na cewa jeki Aafiyyah cikin sauri ta miƙe ta zura after dress ta yi rolling da brown vail, key ɗin wata ƙaramar mota ta ɗauka kuma duk a dalilin Shila ta ƙara ƙwarewa a driving. Lucky ta yi sa a ba kowa a main parlor cikin sauri ta fita, kai tsaye ƙaramar motar ta shiga wata Black mai kyau sai ɗakkan idanu take yi. Tana driving map na nuna mata direction ɗin, lokacin tuni magariba ya yi a entrance da club ɗin ta tsaya, ta ɗauki waya ta kira Shila ta ɗauka ta ce.

"Ina waje"

"Come in Aafiyyah, ba zan iya fitowa ba ki zo mana"

Tsaki ta ja, ta buɗe motar fararen ƙafafuwanta cikin flat shoe ta sakko da su ƙasa, yatsun dugwaye looking so sexy a jere da su, tana tafiya kamar bata so fuskar nan a ɗaure ta fara shigewa wasu gayu na kallonta, ganin ba walwala a fuskarta ya saka kowa kasa tanka mata. "Hi Aafiyyah" ta ji muryar Shila ta juya, zaune ta ganta hannunta riƙe da shisha ga wani kyakkyawan namiji kusa da ita baƙi mai duhun fata, ba tare data zauna ba tace "Bani"

"Haba zauna mana"

"I can't"

"Haba Aafiyyah, ki zauna ki samu peace of mind kin ji?" Shila ta ce tana kama hannun Aafiyyah ta zaunar da ita, lemon ta tsiyaya ta bata sai da sha cup uku kana ta kyale Aafiyyah ta ce "Kina zuwa gida sai bacci, just chill and enjoy"

Shiru Aafiyyah ta yi, jin yanayin ya fara fusgarta ta fara samun nutsuwa a hankali ki ɗan dake tashi ya fara saukar mata a zuciya, sassayen waƙar Jonny ce ta wait for me, sai ta ji taimakar ita akewa waƙar tamkar ita da Yaa Muhammad ne, kamar ita da Blackman ne, idanunta ya cika da ƙwalla ta kai hannunta ta sha cikinta, yanayin

club ɗin ya fara yi mata daƙi a hankali ta kishingiɗa a jikin kujerar bacci ya ɗauke ta, hannunta a saman cikinta ga kiɗa na tashi a wajan.

"Shila me ya saka kike bata irin wannan abubuwan? Bata san cewa maganin maye kike juye a cikin lemon ba" Shila ta yi murmushi ta ce "Gwara amutu har liman, kamar yadda ƙawa ta yi sila na fara shaye-shaye haka itama Aafiyyah, hakan yana mini daƙi ka gane ai"

*

Dr ne ya kalli Mutallab da kuma Uncle Ade sai ya juya ya kalli Safiyyerh ya ce "Ciwon ciki ne Allah ya kawo shi kawai, da farko na yi tunanin ko baƙon wata ne to bincike ya nuna mini kamar yanzu bata fara ba, ciwo ne daga Allah da kuma irin lamuran mata"

Uncle Ade ya ce "Dr amma shekarunta ai ya kai ta fara al'ada ɗin ko? Naga wanda basu kai ta bama suna farawa ai"

"Mata kashi kashi ne, idan bata ɗaya dagacin matan suke yin al'ada bafa? Kuma daman wasu na ɗaukan lokaci kafin su fara, waye mijinta nata a nan?" Dr ya tambaya uncle Ade ya nuna Mutallab ya ce "Gashi nan"

"Ok i need to see him, in privacy"

"Take your time Dr"

Uncle Ade ya fita, Dr ya nufi office ɗinsa Mutallab na tsaye yana kallon Safiyyerh da idanunta ke rufe ruwan hannunta ya kusa ƙarewa, a hankali ya juya ya fita zuwa kiran Dr ɗin. Yana fita Safiyyerh ta buɗe idanu daman ba bacci take ba, kuka ta fara ta san cewa duk wanda baya al'ada to ba zai haihu ba, shikenan ba zata haihu ba? Bata da kowa, babu Daddy babu Ummeyh babu kowa kusa da ita sai Mutallab da danginta? Idan ta mutu fa? Babu abinda zata bari da za'a dinga tunawa da ita "Allah na tuba, Allah ka yafe mini ka sanya Mala'ikunka su yafe mini, kuskuren da na yi Ubangiji ka gafarta mini, Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un" ta ce tana fashewa da kuka z zuciyarta babu daƙi sam kanta na juyawa.

Ya jima tsaye yana jinta, yana sauraren kuka da maganganu da take yi a hankali ya ƙarasa shigowa ciki ya tsaya kanta can kuma ya nemi waje a gefen ta ya zauna, ganinta bata niyyar dai na kukan ya saka ya ɗan saka hannunta ya zungure ta, ta ɗago rinannun idanunta ta zuba masa, bai taɓa ganin yanayi irin yanayin daya gani a cikin idanunta yanzu ba, ya kasa ce mata uffan bawai don bata cancanci rarrashi bane ba, shi bai san me zai ce. Takaicin shirun shi ya saka ta sake fashewa da kuka jikinta na rawa da ɓari har jiyiyon kanta na tashi, ta sake ɗago kai suka haɗa ido ta ce "Ku kukan jini zan yi nasan ban cancanci kulawarka ba, ganina kake tamkar shasha ban san me nake yi ba, na sani ina son ka, na sani ina ƙaunarka, kuma duk ban damu da ka so ni ba, in dai ina son ni ya wadatar, kana ganin bani da kima saboda na bar iyayena na zo gare ka, na yi wawta tabbas, da a gaban daddy nake kukan nan da tuni ya ce Safiyyerh lafiya? What do you want? Ba komai ai shikenan Allah ka yafe mini laifin da na yi maka"

Mutallab ya ji rauni ya kama zuciyarsa, ya ji wani irin tausayin Safiyyerh bai san me zai mata, bai kuma san me take buƙata ba, kamar yadda bai san dalilin daya saka take cewa hakan ba.

"Za ka yi ladama Allah Bestie, sai kazo kana kuka sanda ba wanda zai rarrshe ka maybe fatalwata, domin ko a cikin kabarina ruhina ba zai samu nutsuwa ba idan kana cikin damuwa, na ji dama zan iya barinka a yanzu "

"Safiyyerh!" Ya kira sunanta a tsawace, ta ji faɗuwar gaba.

Sai kawai ta yi masa murmushi while hawaye na zuba ta cikin idanunta, sai ta ɗaga masa gira ta ce "Ya akai? Kake ta wannan abin kana avoiding nawa, ni ƙamshin mutuwa nake ji fa, Allah kuma kar zo kabarina ko da wasa, kar ka zo kana cewa Please Barewata come back to me, uhm'uhm ko maganarta ba zan ji ba, ba zan taɓa jin maganarka ba" a hankali taga kamannin Mutallab na juyewa fuskarsa ta haɗe kamar hadari idanunsa ya yi jajur sai huci yake yi ya kafe ta da idanu.

Ta sake yin murmushi tana matsawa kusa da shi ta ce "Ai shikenan ni kawai tausayinka nake ji sanda bana nan, ai daman ka ce dama na mutu ka huta, zan mutu da soyayyarka mai kyau mara algus Mai dawa" ta faɗa a sanyaye tana kwanciya a jikinsa, kamar jira yake tana kwanciya a jikinsa ya ƙanƙameta a ƙirjinsa

ya kasa furta komai sai ajjiyar zuciya da numfashin da yake ja ta ƙirjinsa, itama rungume shi ta yi tana fashewa da kuka, da sauri kuma ta sake shi ta juya masa baya tana rusa kuka. Hannunsa biyun ya saka ya juyo da ita gabansa, kamar mai counting words ɗin zai faɗa haka laɓɓansa suke rawa da ƙyar ya riƙe fuskarta ya ce "Ke tsagina ce"

Ta yi masa shiru a hankali ya ce "Me kike so?" Ta girgiza masa kai ba tare da ta yi magana ba.

"Talk deer"

"I love you" ta ce a hankali hawaye na fita daga cikin idanunta, ya zubawa fuskarta idanu sai ya girgiza kai ya saka yatsa ya fara goge mata hawayen idanunta amma wasu na sake fita, bai gajiya ba da sharewa cikin ƙulewa ya ce "Shiru, ya isa" ta girgiza kai ta ce "Me ya sa? Me ya sa zan daina kukan? Na ji kawai daddy nake son gani, Ummeyh nake son kwanciya a jikinta"

Ya tsare ta da ido ya kalle ta, sai ya kalli jikinsa ya ce "Ni bai ishe ki ba? Jikina ba jiki bane?" Ya faɗa seriously yana sake duban jikinsa.

Murmushi ta yi, sai ta masa shiru.

"I hite it, I hated ur smile"

Domin ko bata faɗa ba, ya san murmushin baƙin ciki ne, murmushin takaici ne na damuwa ne, idan ta yi murmushin kuma ba lallai ta yi magana ba. A hankali ta dinga murmushi ta ce "Sai huci kake yi, nifa ba abincin jeji ba ce"

Ya tsuke fuska ya ce "Zo nan, kina ɓarranta jikina dake, what's on your mind? Ki dai na yi mini murmushin nan bana so, ko kyau baya yi miki ma" ta girgiza kai ta ce "Allah Ya shiryeka Mijina" sai kuma ta kwanta jikinsa, a hankali ta rungume shi ta ce "Ba lallai na samu nutsuwar da nake buƙatar samu ba a yanzu, na ji nutsuwar a wajan Ummeyh zan iya samunta, da gaske ina samun nutsuwa idan na raɓeka wani

lokacin kuma azaba take zama a gare ni, ina son ganina kusa da iyayena ina so" ta yi saurin ɓoye fuskarta a ƙirjinsa, tana cigaba da shasshe ƙar kuka mai tsuma zuciya ta ce "Kilan kuma ba zan taɓa haihuwa ba, ba zan taɓa ganin jina da kai ba, kodayake ai ƙyanƙyamina kake yi" ta ce tana dariya kamar ba ita ke yin kukan ba.

Kan ta ya ɗago fuskarta a cikin tafin hannunsa ya ce "Who's that?" Ta ce "Dr, ai har yanzu ban fara al'ada ba kuma idan ba'a al'ada ba'a haihuwa"

"Shi faɗar likitan ta Allah ce?"

"Amma....,"

Yatsarsa ta tsakiya ya ɗora a lips ɗinta ya ce "Shhhh "

A hankali kuma ya ɗora fuskarsa a saman tata, hancinsa na gogar nata yana kallon laɓɓanta da suka jiƙe da yawo, yana jin yadda ƙirjinta ke ɗagawa, ya saka hancinsa ya lakace mata nata cikin wata kalar husky voice very classy and emotional ya ce "MATAR MOH, BESTIEN BEASTIE"

Ta yi murjajjiya kawai, ya sake saka tsinin hancinsa a lakace mata nata hancin ya ce "Yʻar budurwata" ta marairace fuska ta ce "Uhm'uhm" while hawaye bai bar zuba a cikin idanunta ba. Ta ce "INA SON KA" shhha hawaye ya sauka fuskarta har zuwa laɓɓansa, ya buɗe bakinsa sai ya ji hawayen zafi, gently ya ɗago kamar zai ja baya sai ya damƙo fuskarta ya ɗora bakinsa a saman idanunta, ya fiddo jan dugun harshensa mai tsini slowly ya fara ɗauke mata hawayen idanunta da harshen, sai da ya shanye tas kana tsotse idanun wajan lashes ɗin, jin ƙirjinta na ɗagawa ya saka a hankali ya ɗora hannunsa a ƙirjinta, da sauri ta kama hannun nasa, ya ɗan danna ta lumshe idanunta tana jin jikinta na rawa.

Kʻoƙarin janye jikinta take yi, amma ya sake matseta. "Look" ya ce with his golden voice.

Taƙi kallon shi, domin bai taɓa yi mata kwarjini irin na yau ba, bata taɓa jin nauyinsa irin na yau ba.

"Safiyyerh!"

Ya kira ta, sai ta kasa kallon shi, yau ɗin a Yaruba boy ɗinsa yake, wannan yanayin is not for her, duk da hakan take so. Ya ɗago haɓarta da yatsunsa biyu "kar ka na maimaita kai na, umarni ni"

Ya ce, sai ya buɗe ido "Look into my eyes Safiyyerh, look"

A hankali ya buɗe idanunta ta saka cikin nasa, suka kalli juna wajan shuɗewar daƙiƙo ya ce "Ke matar moh ce, jinin yarabawa ke yawo a jikina, zan miki ciki, kuma za ki haifa mini a baby gal, mai tsananin haƙuri irin naki, mai duka ɗabi'unki. You are a blessing to me Fiyya, i appreciate your royalty, yana da kyau ki fahimci waye ni, waye mijinki ok?"

"Baka so na"

"Saying i love you is nothing apart from relationship, babu mamaki na ce haka kuma ya zama ƙarya nake, kin san me? Na ji zamana dake akwai cutuwa, ina cutar dake kullum kina kuka domin Mutallab, nafa san yadda kika rasa abubuwa da yawa, na ga magana akan hakan baya da amfani, Idan kina ganin za ki iya zama dani da rigamata to, za ki iya zama da rigimammen mijinki to. Bani da wani ƙarfi amma ina da tabbacin ba za ki yi kukan rashin ba, zan wadataki da komai ba zan taɓa zama butulu ba, kar ji kuma halarci ya saka zan zauna dake kawai MOH yana son rayuwa da SAFIYYERH ne, wannan soyayyar, wannan bibiyar, wanann rashin iyayen, barin makarantar duk ba zai tashi a banza ba, i will sacrifices all my happiness to you, i will stay with you, i will be with you"

"You don't love" ta ce a raunace.

Ya sake riƙe fuskarta cikin hannunsa ya ce "Kar ki matsa dole sai na ce ina son ki, zan rayu dake ya wadatar kin ji?" Ta jinjina kai ta yi murmushi ta ce "I love you "

"Thank you" ya ce yana jan hancinta. Sukai shiru.

Motsin da suka ji ya saka Safiyyerh barin jikinsa, wani Dr ne daban ba wancan ba ya ce "Sannunku" Safiyyerh ta ce "Yawwa, in yini?" Ya ce "Alhamd, k ce ba lafiya ko shi?" Ta juya ta kalli Mutallab, ba zak gane yanayinsa ba, waya ma yake dannawa sai ta yi murmushi mai sauti ta ce "Shine"

"Yawwa ko da na ji, na ce kyakkyawa kamar ki ba lafiya ai gari ba sauƙi thank God bake bace" ta yi murmushi ya ce "Oga Allah Ya ƙara kaffara" ko inuwarsa Mutallab bai kalla ba, bai kuma motsa ba Dr ya ce

"Yayanki ne?"

Ta ce "E, yayana ne muna kama ko?" Ta tambaya tana dariya.

Mutallab dai bai motsa ba, ya ji kalmar yayen ta sauka a ƙasan zuciyarsa. "A'a wanne mutum, kalle ki tubarakallah kyakkyawa son kowa ƙin wanda ya rasa, fatabarakallahu ahsanul kali'ƙin irin ku ne matan aljanna hurul'in, ki gode Allah domin ban yi tsammanin kina jin Hausa ba"

"Na gode" ta ce sai kuma ta kalli Mutallab tana ta dariya ta miƙa hannu ta ja gemunsa ta ce "Amma yayana ya fini kyau Dr, domin da shi baƙin Balarabe za'ayi, kalar yayana tana da wahalar samu irin shi mata suke rububi idanu rufe, kyakkyawar fuska, fararen idanu gasu manya so ma sha Allah, don haka sai na nema masa mata"

Wata nurse take tsaye ta ce "Gaskiya, American man, ni ina son yayyen nan naki da gaske sister idan za ki shige mini gaba, Allah Ya yi mini" cikin sauri Safiyyerh ta ce "An yi masa mata"

"A'a sister, ai bai riga daya aure ta ba, ki bari na gwada sa'a ta ko?"

"Ki yi haƙuri, ba'a kasuwa yake ba" cewar Safiyyerh.

Nurse ta ce "Yayanmu a bani number waya, zan yi trying"

Safiyyerh ta yi kicin-kicin da fuska tuni idanunta ya cika da ƙwalla ta ce "Baiwar Allah an yi masa baiko" suka fara jayayya Mutallab na jin su amma ba zaka ɗauka domin shi ake yi ba. "Don Allah an yi maka mata? Ka bani numberka don girman Allah ka ji"

Gently ya ɗago kan shi, bai kalli nurse ɗin ba, sai ya miƙa hannunsa alamar ta bashi wayarta ya saka number, Safiyyerh ta ɗago suka haɗa idanu tuni hawayenta ya fara sauka, ta fara ƙoƙarin tashi akan gadon marasa lafiyar ya janyota kusa da shi. Nurse ɗin ta ce "Ko jikin nata ne? Saka mini number na duba ta...," saurin shanye magana nurse ta yi ganin Mutallab ya haɗe bakinsa dana Safiyyerh ya fara kissing ɗinta romantically.

More than 3 minutes ya cilla ta gado, yana miƙewa har yanzu bai ga kalar nurse ɗin ba, da kuma Dr ɗin yana yin waje ya ce "She is my wife" ya faɗa yana fita daga room ɗin. Wata kunya ta kama Safiyyerh ta yi saurin rufe idanunta, tsigar jikinta na tashi bata taɓa tunanin zai iya sumbatarta ba, bata taɓa tunanin hakan ba, sai gashi ya yi hakan akan idanun mutane a gaban su.

Har bacci ya ɗauke ta bai dawo ba, sanda ta farka aka sallame su ko inda take bai kalla ba ya yi gaba abinsa tana biye da shi, daman uncle Ade tuni ya yi gaba, yana sake duba gidan daya kamawa Mutallab ɗin haya.

*

Furnitures uncle Ade ya siya mata masu kyau da Kayan kitchen aka fara shirin tariya Malam Abdullahi ko a jikinsa domin ko gaisuwar Mutallab baya amsawa.

Uncle Ade ya ƙara kwanakin da zai yi domin tariyar Ammo ta fara kulawa da Safiyyerh ta hanata zuwa shagon Mutallab ɗin.

Sa'adah ba ta fara gyara ta, a lokacin Safiyyerh she feels uncomfortable kowacce yarinya danginta da iyayenta suke mata komai na aure, amma ita dangin miji ne ke yi mata ta dinga addu'ar Allah ya sawa aurenta albarka, Allah ya yafe mata. Kullum sai ta yi kuka idan ta tuna Aafiyyah, tana neman gafarar Ubangiji akan hakƙin Aafiyyah da Mutallab data ɗauka, domin bata jin zata iya faɗa masa har abada.

*

Paaah na zaune dawowarsa kenan ya dinga duba result ɗin a hankali ya sauke ajjiyar zuciya ya ce "Allahamdulilah" ya faɗa yana sake wata sauke ajjiyar zuciyar.

Dr ya ce "Me ya sa ka yi tunanin ciki wajanta?" He asked.

"Zuciya, mai ƙissima abu"

"Lallai Allah ya kyauta"

"Amin"

Miƙewa Paaah ya yi, domin yanzu baya barin Aafiyyah fita ko'ina abu take musu kamar mahaukaciya bata gane komai bata fahimta. A hankali ya tura ƙofar ɗakin nata, kamar kullum a rakuɓe ya same ta, tana jin motsi ta yi saurin curewa waje guda tana rufe cikinta jikinta duk rawa yake kamar kace mata ket ta arta a guje. Ya durƙusa gabanta.

Ya ce "Aafiyyah"

Taƙi ɗagowa ya tausasawa harshe ya ce "Ke ɗiyata ce, ke ƙawata ce ki faɗa mini mene yake damunki? Me kike so kike buƙata? Kinga ba ki da wani aboki sama dani ko?"

Still Aafiyyah taƙi magana, bata ma son buɗe idanunta, maganar duniya kuma taki tanka Paaah daman yanzu key yake sakawa ya rufe ta a ɗaki, kuma daman itama ba son fitowa take yi ba.

Paaahh ya miƙe yana danna wayarsa, ƙamshin wanda ya gani da wanda yake tsaye ƙikam kamar saƙago ya saka Paaah buɗe idanunsa ya ce "You are here?"

"Afternoon"

"Ka zo lafiya?"

Ya jinjina kai alamar “Allahmd"

"Kwana nawa za ka yi?"

Ya ɗan shafa kan shi da yake ƙwalƙwal ta cikin glasses idanunsa yake ƙarewa Aafiyyah kallo, a ransa yana mamakin ita yarinyar nan mene ya same ta ne? Me ya sa komai nata ya sauya a zahiri ya ce "Zan ta fi"

Paaah ya juyo ya ce "Mene?"

"Eh" ya bawa Paaah amsa.

"To Allah Ya tsare, baka yi mata sannu ba?" Har zai shiru sai ya ce "Who?" Paaahh ya ce "Safiyyerh"

"I will call you, bye"

Ya ce da sauri yana ficewa. Yana fita kuma Paaah ya kira wata number ana ɗagawa ya ce "Dr ina son ganin Neurologist Dr" saurin da yake yi ya saka ya manta ya bar ƙofar ɗakin Aafiyyah a buɗe, Ummi na can ba lafiya tun ranar da Mj ya ɗakko Aafiyyah daga club, take ta kuka ranar ba wanda hankalinsa bai tashi ba, hatta Paaah a ɓoye sai da ya saka aka gwada jininsa, ya kasa ɗaukan mataki akan Aafiyyah batun club ɗin ba ƙaramin girgiza shi ya yi ba, ya zubawa Aafiyyah idanu ya kasa furta komai.

Jin sautin fitar Paaah ya saka Aafiyyah buɗe idanunta da suke a kumbure ta zubawa ƙofar ɗakin dake a buɗe idanu, wanda mistakenly Paaah ya manta bai rufe ba, tana kallon ƙofar a lokacin kuma a ƙwaƙwalwarta ta fara aikinta na tunanin maganar da Safiyyerh ta ce a chat, magana data tsaya mata ta ƙara dagula mata lissafi maganar dake mata amsa amo cikin tunaninta.

“Aafiyyah ya kwana da yawa? Ashe kina raye, na san daman ba za ki iya haƙuri ba, sai dai jin ki shiru ya saka na ɗauka cewa kin mutu ne wallahi. Na bada saƙon ki wajan mijina Mutallab, sai dai ya nuna he is not interested, ya mini faɗa sosai da ƙyar na iya lallaɓa shi, ya ce ko mata sun ƙare a duniya babu abin da zai yi dake, kalar ki bata burge shi, kuma shi Alhamd yana dani sauran mata tamkar maza suke cikin idanunsa, ya ce dai na yi miki albashir duk sanda na haihu sai saka sunanki, saboda ƙaunar da kika nuna masa. I am sorry Aafiyyah, yana da kyau ki daina bibiyar mijina, tunda ya nuna baya so, na ji tabbas kin rigani ganinsa, kuma kin rigani faɗawa soyayya da shi, kuma kin rigani furtawa kin faɗa mini, bawai mantawa na yi cewa kina son shi ba, a'a, ina sane na sani kawai na san za ki iya sadaukar mini da soyayyarsa, za ki iya mini shi. Aafiyyah i have to congratulate to myself, ranar ta farko na zama winner, kin sama loser, kina cinye komai, kin fini a komai kuma na yarda amma a wannan karan ni na yi nasara akan ki. Ki manta da suka shekarun da muka kasance a tare, ni a gare ni kamar ba'a halicce ki ba wallahi haka nake ji, kuma koda Mutallab ya amince miki ba zan taɓa bari ki same shi ba. Sai watarana AAFIYYAH”

Zumbur Aafiyyah ta miƙe tsaye, sai kuma ta shafa cikinta da sauri ta saka hijabi da flat shoe zuciyarta na ingizata. Ta yi turus da ƙarfi kuma ta ce "Ƙarya kike Surayyerh, ƙarya kike, kin yi kaɗan, kin yi kaɗan ki amshi Muhammad daga wajena, i can't sacrifice my love for you, wait for me Safiyyerh i am coming to you"..

Tana cewa haka da gudu ta fito daga ɗakinta jikinta na rawa ta fice daga cikin gidan gabaɗaya

[1/7, 9:37 PM] Sis Fauzy: Chapter 46: When a destiny call

Bata san ina zata je ba, kawai ta ji koma yaye ne duk abin da zai faru tana buƙatar ganinsa, duk da rashin sanin inda zata same shi ɗin. Aafiyyah ta ɗan takure jikinta ita mutane tsoro suke bata yanzu, ko da zata mutu gwara ta mutu bayan ya san gaskiya, ba zata iya auren wani ba tare da sanin abin da zata kare kan ta da shi ba.

"What should i do?" She Asked herself. Tana neman waje can ta zauna, ta yi jigum zuciyarta na tashi, gabaɗaya ta fige ta tsotse ita kaɗan ta san meke damunta, me kuma take buƙata ta dai ji damuwarta a yanzu, bata iyayenta bace, dole dai wata rana zasu sani, the only person da zai fahimce ta shine BLACKMAN.

"Shila" ta ce da sauri tana miƙewa, tare da fara ƙoƙarin kiran number Shila domin handbag ɗinta ta ɗakko gabaɗaya, mai ɗauke da password nata, a.t.m da sauran abin buƙata, tana sake jin cewa this is the right time, da ya kamata ta yi fighting akan shi, ta yi fighting for his love, ta yi fighting for her destiny, ba zata kuma yi Safiyyerh sadaukarwar komai ba, har abada ko za ta yi ba a kan shi ba, not him in sha Allah.

Texci ta tsayar ta faɗa masa inda zai kaita, suna cikin tafiya ta tsaya ta siyi sim ta cire na wayarta, ta saka sabo, ta gaske gudun take son yi, not forever ganinsa ya wadatar, ba zata iya rayuwa inda babu Paaahh da Ummi ba.

Ta cure kanta, sai a lokacin ta fashe da wani irin kuka jikinta ya ɗauki zafi zau, haƙoranta na rawa da suna datse kansu a firgice ta ce "I am sorry, Paaah, I am sorry Ummi, I am sorry MJ"

Ta ɗora da “I will be back, zan dawo na auri Alhassan”

*

Yin duniya Safiyyerh taƙi zuwa ganin gidan, domin ana mata magana sai ta ji gabanta ya faɗi haka kawai, hakan ya fara sanya mata rame sai Ammo ta yi tunanin irin fargabar nan ce ta amare, ya dai ci kawo yanzu ta saba da Mutallab amma hakan dole ne zama ne daga ita sai shi. Kullum idan ta ji hakan ta kan yi addu'a, ta rage walwala da magana. Sa'adah ta dake wajan gyara Safiyyerh da iyaka cin iaywarta da kuma abin da za ta yi, har maganin sanyi Saboda yanayin banɗakin gidan. A lokacin kuma tuni uncle Ade ya saka hannu an kammala gyaran gidan da komai, har furnitures an saka an rufe gida an kasa ranar tariya kwana biyu masu zuwa.

A wannan karan ma, Ammo ta ce kar a sanar da Anty Hameeda, Bafullatana na zuwa kuma ta saba da Safiyyerh sosai, duk da Safiyyerh ita bata iya yaran kurame ba, sai dai ta dinga murmushi kawai, ko kuma a yi mata bayanin me Bafullatana ta ce ɗin, ita kuma Bafullatana sai a yi mata bayanin me Safiyyerh ta ce a lokacin, hirar bata jimawa.

Safiyyerh na zaune tana kallon zanen lallen hannunta, ya fito ya yi raɗau gwanin sha'awa haka na ƙafarta, kitson da bata so shi Sa'adah ta sake yi mata wannan karan ma kalba ce ƙanan, aka sanya mata wasu kalar duwatsu masu kyau, ta fito sosai a amarya daidai gwargwado. Sa'adah ce ta ce "Maganar gaskiya wannan karan ki saka mijinki ya bani lada, wannan kyan ya yi miki yawa"

"Ki dinga tubarakallah Sa'adah"

Sa'adah ta juya ta kalli Ammo ta ce "Allah Ammo Safiyyerh kyakkyawa ce, da na ɗauka ko Bafullatana ce kamar mu amma yanayin nata kyan ya shige na zallar Fulani akwai mix, bana iya ɗauke idanuna a kan ta tsakani da Allah kenan, Allahumma Barik"

"Haka Ubangiji ke ikonsa akan bawa ai, wannan ma ni'ima ce"

"Haka ne, za dai abar wajan Ammo a tafi wajan wancan botsararren yaron" Sa'adah ta ce tana dariya tare da kallon Surayyerh da ta yi murmushi sai kuma ta ce "Wai mene laifin da muka yi miki ne yaya? Yana da kyawawan ɗabi'u Allah" Sa'adah ta riƙe bakinta ta ce "A saboda mijinki ne? Kodayake babu matar da zata zauna ta kushe mijinta, amma dai Tayo zama da shi sai mai irin halinsa, ba kowa ba"

“Tayo” Safiyyerh ta maimaita a ranta nan take kuma Aafiyyah ya faɗo mata a rai, gabanta ya cigaba da faɗuwa sai ta dake ta ce "Ko ba haka ba, bashi da ƙarya, yana da zuciyar nema, mai zuciya baya bari ya wulaƙanta, yana da son yan'uwa ko bai nuna ba, iya soyayyar da yake yi wa Ammo da Aby sai zaka ki fahimci yana da halin ƙwarai, yana da matsalar magana ne, shi kuma iya magana halitta ne, kuma haka baya raba nasaba da rashin ƙaryar da bai iya ba, ba ruwan shi" ta ƙarasa maganar tana murmushi tare da sake kallon ƙunshin hannunta.

Sa'adah ta jinjina kai ta ce "Kuma bashi da kara ba ruwansa, ko magana zata kashe ki sai ya faɗa, ba zan taɓa mance cewa da ya yi zai ɗaga mini riga ba, zuciyarsa kuma ta yi yawa ga shegen miskilanci, shi ba kowan kowa ba"

"Kai Yaya, miskilanci hali ne fa, ba sai ka zama wani abu ba, Allah ba kyau abin da kike masa" Sa'adah ta ce "Kawai ki ce za ki rama masa?" Ta girgiza kai ta yi shiru kawai tana sake jin Aafiyyah na yi mata motsi a cikin zuciya, bata son mutuwa ba tare da Mutallab ya san komai akan Aafiyyah ba, bata son faɗa masa ya goje mata,

tana tsoron barin abun a cikin zuciyarta, bata san zuciyar Mutallab ba, amma yadda Aafiyyah ke da confidence ta san dole akwai abin da take taƙama da shi, seeing Mutallab with another lady shine abin ba zata iya mantawa ko ta yafe masa ba, idan ƙaddara ta zo dole ya kasance da wata banda Aafiyyah, zata iya jure ganinsa da kowa amma banda Aafiyyah. Aafiyyah she is darling, wata halitta ce mai tsananin shiga ran mutane da zuƙatansu ta zauna, Aafiyyah bata yadda ta yi faɗa akan abu sai tana da hujja, maybe zata iya rabata da Mutallab gabaɗaya.

Ta lumshe idanunta, ita sai ta ji abin da ta yi daidai ne kawai, za kuma ta cigaba da roƙan Allah akan ya yafe mata idan ta yi laifin, ta sha wahala, ta rasa komai, ta jure komai, harda yadda Mutallab ɗin ke treating nata, ta kuma san ba lallai yana son ta bane, yana ganin ta masa halicci ne. Ba zai taɓa son ta ba. Tunanin hakan ya saka ba tare data sani ba ta fashe da kuka, kuka mai tsananin ɗaci da cin zuciya, ta sake addition na promising ɗin rabuwar Aafiyyah da Mutallab, har abada ba zai taɓa sanin wannan secret ɗin ba.

"Safiyyerh" Sa'adah ta kira sunanta da mamaki ta ɗora da "Kukan na mene? Wani abu akai miki ne?" Safiyyerh ta yi shiru, tana ƙoƙarin danne kukan nata. A lokacin Mutallab ya shigo yana tsaye hannunsa biyun zube cikin aljihu, ya tsaya yana kallon gefe guda, yana jin kuma kukan na Safiyyerh, kukan damuwa kuma.

"Idan saboda na kushe mijinki ne Allah Ya baki haƙuri, abin har ya kai haka kenan, sannu Layla da majnun" cewar Sa'adah.

Sai ta ɗago kan ta tana murmushi ta ce "Kai Yaya". "Ba wani ki yaya, Ubangiji ya saka yadda kike ƙaunar Tayo ya soki fiye da hakan, Ubangiji ya yi wa rayuwar aurenku albarka, ya baku zuri'a ta gari ya kaɗe fitina, ya ba ki haƙurin zama da halinsa a yadda yake, Allah Ya ba ki ikon yi masa biyayya, shi kuma ya bashi wuyan ɗauka yadda zai tsare mutuncinki da kimar ki, Allah Ya shiga cikin lamuranku ya baku farinciki na har abada, za ki yi farinciki"

Ita dai murmushi kawai take yi kan ta a ƙasa, Ammo ta amsa da Amin a cikin ranta. "Kai ba soja ba ka yi mana ƙigam, ka shigo ka bani kuɗin ƙunshi da kitso"

Sai ya tsuke fuska, yana ciccin magani ta ce "Wannan har ya fi na baya kyau, Allah Tayo matarka kyakkyawa ce dubi ƙunshin nan" ta ce tana nuna masa tafin hannun Safiyyerh, sai ya sake tsuke fuska kuma bai ce komai ba. "Ka bani kuɗin, tunda aka fara sabgar nan banga uwar daka kashe ba, komai uncle ke maka"

"Ɗan Abdullahi ne ni, bani da ƙarfin yi ne" ya ce yana jingina da jigin ƙofar ɗakin. Idanunsa ƙasa-ƙasa yana duban yatsun Safiyyerh, yana mamakin zanen ƙunshin, sai ya ji ransa ya ɓaci, yaƙi gano kyawun da ƙunshin ya yi sai wani abu da yake tunani nada daban a sashen zuciyarsa daban a keɓance da yake keɓance abubuwa da yawa a zuciyar, wanda baya son tunaninsu hana shi rawar gaban hantsi. "Ohho dai, kai ta matsewa na san dole a ce ya yi kyau, na kuma iya ƙunshi ya ji farar fata ma sha Allah"

"Yaya"

"Ya akai Tayo?"

Ya yi mitsi-mitsi da idanunsa ya ce "Ko mayya ce Allah ki ci kan ki" ya juya ya kalli Safiyyerh ya yi ƙwafa sai ya sake dubanta ya ce "Ki zauna tana miki zanen bishiyoyi, gwara ƙafarki fara tas, at all bai kyau ba, sam sam" ya ce seriously.

"Mene bai yi kyau ba?" Sa'adah ta tambaya, ta ce "Wallahi kamar a India haka Safiyyerh ta zama"

Ya juya ya ce "Zo ki amsa"

Safiyyerh ta san da ita yake amma ta yi ƙasa da kanta, har ya fita ya dawo ya ce "Ki nemi baƙar leda ki rufe ƙafar nan, ba zan fita ana nuna ni da baki ba, ki nemi baƙar leda, ki nema" ya ce yana fita abinsa, Sa'adah ta bishi da idanu kana ta ce "Tab, wannan matarsa ba zata taɓa yin abu ya ce ya yi kyau ba, naga maza na son ƙunshi ko Ammo?" Ammo ta kalli Sa'adah sai ta kalli ƙafar Safiyyerh ta ce

"Shi baya so, Safiyyerh ta shi ki je kar ya sauke miki sababi" .

Sai ta marairace fuska ta ce "Yaya a goge ƙunshin to, tunda baya so"

"Wallahi ko zai dinga gani yana amai haka zai haƙura, kar ki saka komai a ƙafarki fita"

"Umarnin miji ne Sa'adah" cewar Ammo tana miƙewa tsaye.

Sa'adah ta ce "Ammo ki yi shiru don Allah, ki zuba mana ido, saka hisabi ki fita, ke ɗauki mayafin abayar ma, ki yi rolling kin ji?"

Bisa dole ta yi yadda Sa'adah ta ce tsoro dai ya kamata, amma ta yi shiru ta dinga mamakin jin Sa'adah na shafa mata humra da kwalacca, masu tsananin ƙamshin ta ɗauki lipstick ta shafa mata a ƙaramin bakinta. Sa'adah ta ji zuciyarta na rawa da kyawun Safiyyerh, ta jigum tare da yin tagumi ta ce "Komai zai ce ki toshe kunnenki, amma kin ja magana" sai Safiyyerh ta yi sak ta ce "bangane ba? Faɗa zai ko" ta girgiza kai ta ce "Jeki kawai, ba abin da zai yi, idan ya miki faɗa ki rama a haka ake samu a zauna lafiya dashi, da ya ce kee ki ce kai" ita dai Safiyyerh bata gane ba ta saka kai ta fice bayan Ammo ta ce ta yi addu'ar fita daga gida.

Sa'adah ta fashe da dariya ta kifa tana riƙe ciki ta ce "Yarinya da a gidanku kike za ki gane ba ki da wayo, wannan bom na haɗa"

A waje ta same shi zaune saman dakali yana shafa kan tiger, tuni Spider ya zo kusa da ita yana zagaye ta, ta fahimci baya son manyan kaya sama, kamar takura shi suke yi yanzu ma wata t.shirt ce a jikinsa ta kama shi, buɗaɗɗan ƙirjinsa ya bayyana a fili, sai wani wando three qauter kamar sabo ne ya masa kyau, ya ɗauki hular saƙi ta masarautar ya saka ya ɗan lanƙwasar da ita. Sosai ya yi kyau ya ƙara girma cikin idanunta. Yaga inuwarta ya kuma san ita ce, domin jan lallen ya fara sauka a idanunsa na yatsun ƙafarta, sai ƙamshin daya ratsa cikin hancinsa ya saka zuciyarsa girgiza.

Ta cikin inuwar ya ƙare mata kallo yana cigaba da danna wayarsa. Ta gaji da tsaiwa ta ce "Ɗan saurayi mijin mata, zance ka zo ko fita da budurwarka ka zo?" Ta ce tana murmushi mai sauti, sai murmushin ya ƙular da shi ya miƙe tsaye ko inda take bai kalla ba ya yi gaba abinsa. Bayansa tabi, karnukansa suka tsaya nan ƙofar gidan Malam Abdullahi. Da ƙyar ta iya cimmasa lokacin ya tsayar da napep ya shiga, itama ta shiga bata san ina zasu ba, tunda suka fara tafiya

mai napep ɗin ya fara kwaɗa Safiyyerh, yana yaba kyanta kamar ya dawo kusa da ita sai kallon ta yake ta cikin madubin yana murmushi da jinjina girma da kaɗaitar Ubangiji wajan iya tsara halittar kyau irin na Fiyya

"Tsaya" ya ce a ciki.

Mai napep ya juyo ya ce "Ai bamu ƙarasu inda ka ce ba"

"Idan na sake cewa ka tsaya ko ban sumar da kai ba, zan iya makantar da idanunka" jin hakanya saka mai napep ɗin yin parking waje guda, yana tsayawa Mutallab ya fito, ya ciro ɗari biyar ya cilla masa, ya fara takawa a ƙasa tabi bayansa itama ganin suna tafiya sosai ya sa a hankali ta ce "Ƙafata na gaji" ya yi mata banza, ta san kuma ba zai kulata ba ta sake cewa "Wallahi na gaji, bamu kai ba ka

saka an ajjiye mu kuma kana ta janmu a ƙasa" ta ce daidai lokacin da suke ƙarasawa gaban wani katafaren gida, iya kyau da haɗuwa ya yi babu mai kyan gidan a layin, ga almajirai fal an cika ana sadaƙa, ya ja ya tsaya yana dannawa waya, wata number ya kira aka ɗaga magana ɗaya ya yi ya kashe wayar.

Sai a lokacin ya juya ya fara kallon ta daga sama har ƙasa, idanunsa a juye ya cije lips kamar dole ya ce "Jira ni nan" ta ce "To kar ka daɗe"

Ya yi gaba, sai ya sake cewa "Ki jira, ki jira ko?" Ta jinjina masa kai tana neman waje ta zauna, a hankali ta dinga kallon gidan tana tunawa da nasu gidan, tana murmushi ta dinga kallon almajiran wajan sai ta ɗauki dubu ɗaya cikin kuɗin da uncle Musbah ya bata har yanzu suna nan. Wani ɗan ƙaramin Almajiri ta kira.

Ta ce "Ya sunanka?"

"Tasi'u"

"Ma sha Allah, sannu Tasi'u me kuke yi a nan? Naga kuna da yawa" ya juya ya kalli yan'uwansa sai ya ce "Sadaƙa ake rabawa kullum, shine muke bin layi, Alhajin yana da kirki sosai yana da taimako baya barinmu zama da yunwa wallahi"

Ta riƙe hannunsa ta ce "Allah sarki haka ake so, yana da kyau kai ma ace a gaban iyayenka kake ba bara ba, ka yi ƙarami da yawa, riƙe wannan ka sai abinci idan ka tuna dani ka yi mijina addu'a ka ce Allah Ya bamu zama lafiya ko?"

Dubu ɗayan ta bashi Tasi'u ya dinga murna ya ce "Allah Ya amfana in sha Allah mutuwa ce zata raba, Allah ya sawa zama lafiya anty, ma gode sosai" ta yi masa murmushi tana jinjina kan ta sai ta ce "Kuma kace Allah ya yafe mini kuskuren da na yi ka ji?" Ya ce "In sha Allah, zan dinga saka ki a cikin addu'a ya sunanki?" Ta ce "Safiyyerh!"

"Allah Ya amfana Anty Safiyyerh"

Tasi'u ya yi murna sosai da kuɗin da Safiyyerh ta bashi, ta bishi da kallo tana jin nauyin ƙirjinta na raguwa haka nan take jin kamar ta aikata babban zunubi.

Ja'afar ya dinga kallon Mutallab a cikin parlon kafin ya ce "Yau kuma da kan ka? Na yi mamaki" Mutallab ya yi shiru ya harɗe ƙafarsa. "Daka kira ni na zo da kai na ai, ina da wani aikin ma da nake buƙata ka yi mini"

"Kuɗina na zo amsa, ba aiki ya kawo ni ba, bana bin mutum domin batun aiki ka gane?" Yanayin furucin Mutallab babu wasa, duk da cewa Ja'afar gaba yake da shi nesa ba kusa ba amma sai da ya ji shakkar Mutallab ta gitta ta zuciyarsa. Ya jinjina kansa ya ce "Wannan ɗin ma daka kira"

"No need"

Ja'afar ya ce "Kuɗi ne masu nauyi, kuma a lokacin na faɗa maka hannun jari zan saka maka tunda ka nuna mini baka buƙata" cewar Ja'afar ya ɗauki glasses cup ya kai lemon ciki bakinsa, kana ya tsiyaya wani ya turawa Mutallab gabansa ya ce.

"Bisimillah"

Mutallab ya gyara zama ya ce "Ya sunanka ma? Ɗawainiyya ce ta hau ni, na maka aiki kuma Alhamd, ina buƙatar kuɗin yanzu zan tafi dasu ok?" . Ja'afar ya ce "Haka ne, amma already suna cikin hannun jari karɓar kuɗin kuma sai an bi wasu long way, zai ɗauke mu zuwa 3-4 weeks"

"Kut, hauka kenan. Kaga malama yanzu a ni nake, ɗakko ka bani" Mutallab ya ce yana miƙewa tsaye, shima Ja'afar ya miƙe tsaye ganin yanayin Mutallab ya saka ya yi murmushi ya ce "Shikenan zan kawo maka gida zuwa anjima, sai na je banki na ciro da kana da account sai saka maka". "Zan maka abin da ba ka yi tunani ba, ba'a saɓa mini al'ƙawari"

"Na sani"

Ja'afar zai sake magana yaga ta shigo, sai gabansa ya faɗi ya zuba mata idanu ita kuma ta kalli Mutallab ta ce "Haba mana, daga cewa yanzu zaka fito shine shiru" yanayin kallon da ya yi mata ya saka jikinta ya hau rawa, idanunsa ya yi jajur, cikin sauri ta juya ta bar palron tana tsakiyar compound ɗin gidan tare ƙoƙarin fita Safiyyerh ta ji an cakumeta, jikinta ya ɗauki rawa, matar ma jikinta rawa yake ta ƙanƙame Safiyyerh sosai tana cewa "Ki taimaka mini, ki taimaka mini, mugu ne, macuci ne yana mini abin da bana so, azzalumi ne da rarrafe na fito ko wajan nan"

Safiyyerh ta kasa magana sai matar take kallo, ganin jikinta duka rawa yake musamman ƙafafuwanta ta yi goho alamar bata iya zama. "Ki taimaka mini"

"Innalillahi, me zan miki?" Safiyyerh ta tambaya a ruɗe tana riƙe matar a hannunta ganin zata faɗi zuwa ƙasa. Laylerh ta ce "Ki fita dani daga cikin gidan nan, ki fice dani mijina zai kashe ni"

Safiyyerh na ƙokarin jan matar zuwa bakin gate na baya, wasu ƙartin maza suka yo kansu ita da Laylerh, kiɗima ya saka Safiyyerh yin ihun gigita ta ƙanƙame Laylerh tare da rufe idanunta. Suna zuwa suka fara jan Laylerh da ƙarfin gaske, ganin tana musu kaddama ya sa suka soka mata sirinji a wuya tare da saɓata a wuya zuwa cikin gidan inda ta fito, Safiyyerh ta yi waje da gudu, jin ihun Safiyyerh ya saka Mutallab fitowa, sai dai ba kowa a harabar gidan cikin sauri kuma ya yi waje. Yana fita Ja'afar ya fito haka ma Boɗejo suka bi bayan Mutallab da kallo.

Boɗejo ya ce "Me ya sa zaka kawo mini gidana? Me ya sa Jaa'afar?"

"Kuskure ne, ban san zai zo"

"Ya zama last " cewar Boɗejo yana juyawa dama daga shi sai boxer shorts ya fito ko riga babu.

*

Bayan sun dawo gida ta bishi shagon amma har lokacin bai kulata ba, ta gaji da zama ta miƙe zata fita ya ce "Ji mana" sai ta waigo ba ita yake kallon ba idanunsa ne a rufe, kamar ta fice sai ta dawo tana ƙoƙarin zama ta ji ya janyota ta faɗa kan shi gabaɗaya sukai baya suka faɗa saman tabarma, ya dinga binta da jirkitattun idanunsa wanda suka birkice, kamar ba shi ba. Ƙoƙarin barin jikinsa take yi, domin wannan yanayin ba nata bane, ya ji ba zata iya ɗaukarsa ba.

Muryarta na rawa ta ce "am unm ka sake ni, Ammo na kirana"

"Ammo babata ce, ni kuma mijinki ne, ke kuma surukarki ce" ya ce yana kunce rolling ɗin da ta yi. Ƙananun kalbar kanta suka sauka a kan fuskarsa ya tattare ya matsar gefe, a hankali ya ɗago kanta ya zubawa fuskarta idanu sai ya yi murmushi idanunsa har yanzu a ƙanƙance. Ta ce "Mene?"

"Ba saboda ni aka baɗa miki turare irin na yaɗan bori ba? Aka zana miki wasu bishiyoyi kamar karaba, ga wata aba da aka miki kamar bayyanar ya juju, ke dole sai an ce kin yi kyau?" Ya ce da husky voice ɗinsa, ta kuma ji mamakin yadda ya yi magana mai tsayin hakan ƙwarai. A hankali ya tura kanshi wuyanta ya shanshani ƙamshin humrar ya lumshe idanunsa yana jan numfashi.

"Hmmm"

Ta ture kan shi, ama yaƙi matsawa ta ce "sai wani shanshani kake yi....," ya dube ya da sexcy eyes ɗinsa ya ce

"Wannan shanshanan zunubi nake rage miki, a dole na yi saboda ina son ki rabauta" da rashin fahimta ta ce "Zunubin me?" Ta yunƙura zata tashi ya mirginata zuwa ƙasan shi. Ya ɗan yi mata rufa sosai sai jikinta ya fara rawa, wani kyarma da ƃari tsoro ya mamaye zuciyarta bakinta na rawa ta ce "Don Allah ka ɗagani, ka mini nauyi ƙatoto da kai" lips ɗinsa ya manna a wuyanta, sanyin laƃƃansa ya sauka har tsakiyar kan Safiyyerh, wani shock taji kamar jan wutar lantarki, gashin jikinta ya mimmiƙe sosai, ƙirjinta ta ji na yi mata wani, wani irin da bata san na mene ba, ta sake yunƙurawa zata tashi sai ta ji ya rungumeta gabaɗaya nauyin da ya yi mata ya saka dole ta yi holding nasa back.

"Bestie"

"Uhm" ya ce, while he's kissing her neck yana shafa mata kyakkyawan sajensa mai san yi.

"Bestie"

"Bestien bestie"

"Mutallab"

"Safiyyerh....,"

"Mai dawa"

"Deer..."

Hawayen idanunta ya taro muryarta na rawa ta ce "Don Allah ka sake ni, na shiga uku mene haka, wai me kake yi ne?" Cikin lalatacciyar muryarsa data shige can cikin ƙirjinsa ya ce "Abin da kike so ne..," ta girgiza kai, tana duban ƙofar shagon ta ce "Wallahi bana so, ban ce ka sake ni"

Bata lura ba, sai ganin rigata ta yi ƙasa, ta buɗe idanunta da ƙyar yadda taga Mutallab sai da gabanta ya faɗi a ruɗe ta ce "Na shiga uku, wannan ba bestie na bane, I'm scared" idanunsa rufe kamar ba zai magana ba sai kuma ya buɗe bakinsa ya ɗora a kunnenta ya ja numfashi ya ce.

"You're right, wannan ba mafaraucin mijinki bane, wannan ba bestienki bane, wannan ba mai dawa bane, wannan ba abokin wasanki bane. Wannan da kike gani,

jinin yarabawa ne Tayi ne a gabanki, mijinki ne, i am here for you, abin da kike muradi ne fa"

Ta girgiza kai ta ce "wallahi bana muradi, ka sake ni ka dawo Mai dawa ɗinka, You scared me"

"Uhm" ya ce.

Ta tallafo kan shi ta ce "Me kake so? Ka faɗa ka sake ni, ni na fasa auren ma Please ka cika ni"

Sai taga yana yi mata murmushi yana cije lips ya ce "Idan mugunta kikai mini kan ki kikai wa, Allah kan ki kikai wa, wannan muguntar tare zamu raba ta, ba zan ɗauki asara ba ko kaɗan"

Idanun Safiyyerh ya raina fata, ta kulle idanunta gam ta riƙe kansa, abin da bai taɓa ba shi ne yake yi, wani irin zafi da raɗaɗi ƙirjinta ya fara, ta shiga ture shi amma ko motsi ba yayi, ganin numfashinta na ƙoƙarin barin ƙirjinta ya saka ya zame kan shi daga ƙirjin yana riƙe dariyarsa. A kunnenta ya ce "Bafa rago bane ni" ya kama hannunta ya kalli ƙunshin sosai sai ya zura yatsun bakinsa ya yi kissing ya sake ta. Idanunta a rufe still sai taga hawaye na bin idanunta can ta ce "I am sorry, don Allah Mutallab ka yafe mini"

"Ka yafe mini don Allah Bestie"

"Me ya sa?"

Ta girgiza kai ta ce "Kawai ka yafe mini don Allah, ka ka yafe mini"

Ya girgiza kai, yana ta kallon ta, shi wuyanta yake kallo da ƙirjin data rufe, bai damu da yafiyar da take masa magana akai ba,

domin bai ga abin da ta yi masa ba, har take wannan roƙan kamar maroƙiyya. Ta riƙe tafin hannunsa duk biyun tana kuka ta ce "I am sorry, don girman Allah ka ce ka yafe mini don Allah" tana riƙe hannunsa da kyau tana kuka.

Sai ya tsuke fuska ya ce "Wallahi ba zan ce na yafe miki ba, domin banga me kikai mini ba"

"Please, ni dai"

"Safiyyerh, wallahi ba zan iya yafe abin da ban sani ba, ki faɗa mini mene sai na ji" ta yi shiru tana kallonsa cike da tsoro sai taga ya yi dariya ya ce "Forgiveness for no reason, no please ni bani da kara idan an mini dole zan rama"

Ta jinjina kai ta ce "To ɗaga ni"

Ya dinga kallon ta sai ya ce "Wallahi wallahi ba ki da gaskiya, Allah ba ki da gaskiya, ba ki da gaskiya Safiyyerh, na kuma tsani ɓoye abu, da kuma na san me kike ɓoye da tuni na tunkare ki"

"Kawai daga tambaya?"

Ya hararеta ya ce "Zo ki ji"

Ta miƙa masa kunnenta maimakon kunnen sai ya haɗe bakinsa ya fara kissing nata with love and care, kuma in a romantic style. Saɓanin hakan Safiyyerh ta ji, ta fara ƙoƙarin ƙwace kanta ƙirjinta na bugawa da ƙarfi, sai ta fara hasaso Daddy Ummeyh, idan haka ne to azaba ce wannan wannan, ta fita hayyacinta tun ba'a je ko'ina ba ta fara kuka ganinta ta fita hayyacinta ya ɗan sake ta kaɗan sai kuma ya juya mata

baya gabaɗaya, da sauri ta yunƙura da ƙyar tana jin azaba ta saka rigarta da mayafinta ta yi waje da sauri tana sauke numfashin wahala.

Bayan hakan har dare Mutallab bai shiga gidan ba, yana waje da uncle ade. Cikin sauri Malam ya ce "Kai Muɗallabi, ashe abin da kake yi kenan? Wato Ɗan'malam yaƙi halin malam ko? Ba shakka sai dai har naci yayina ban taɓa buga ƙasa ba, ban taɓa sauka daga tsarin addinin musulunci ba".

"Aby ce mini ka yi na je zan gani fa? Abin da nake gani kenan"

Aby ya ce "Oh haka kace? Daman kai ɗan asara ne dama bani ne ubanka ba, tsinannen yaro la'ananne mai zuciyar fir'auna, baƙincikinka bai isa ya kashe ni ba, shaiɗani ka je zaka gani ɗin, Allah da ina tunanin ɗan ta'adda za'a yi, kake kallo na kamar wani tantirin ɗan daba kai da ba zaka wanye lafiya ba" shi kan shi Aby bai san furucin na fita daga cikin bakinsa ba saboda ɓacin rai, sai mugawayen alkaba'i yake jawa Mutallab, uncle Ade ya kasa magana yana kallon malam Abdullahi da mamaki fal cikin ransa, da tarin takaici.

Mutallab tsoro ne ya kama shi, idanunsa ya cika da ruwa muryarsa na rawa ya ce "Don Allah Aby, ko baka so ni ba, kar ka saka rayuwata a shiga uku, baka binciki mutuwar Diyna ba, baka binciki mutuwar Jaaanah ba, baka san ya aka yi na fara abin da kake kira da bugun ƙasa ba, baka ya aka yi Muneeberh ta mutu ba ka bar ni hakan ya wadatar" ya ce yana sunkuyar da kansa ƙasa, da sauri ya saka hanky ya share hawayen idanunsa. Aby ko a jikinsa ya ce "Me zan bincika? Komai aka ce ka yi bana waufi, lalataccen yaro watsastse irinka duniya ce ka je zaka gani"

Sai kawai Mutallab ya miƙe zai bar wajan ya ji Aby ya ce "Ka zo ka ɗauki yarinyar mutane ka bar mini gidana bana son ganinka"

"Ka kore ni daga gidanka?"

Mutallab ya ce a sanyaye "E, ka je can kama cire sunana daga naka, na ji ka sake laƙaba sunana a naka zan maka Allah Ya isa"

"Ya maka kyau Aby"

Ya juya zai je ya kirawo Surayyerh su bar gidan, daman ai gobe ne tariyar, yin duniya Uncle Ade ya yi amma Mutallab ya kafe ba zata sake kwana cikin gidan ba. Da ƙyar ya lallaɓa Mutallab akan ya bari sai gobe dai Safiyyerh ta shigo shagon ta kwana, haka kuma aka yi Safiyyerh dare na ya ta fito zuwa shagon, Ammo idanunta ya yi jajur ta kasa cewa komai, a lokacin kuma Aby ya ce tana furta komai a bakin aurenta.

Safiyyerh ta dinga kallon Mutallab yana zaune ya kasa bacci, da ƙyar ta tashi ta taɓa shi ta ce "Bestie" bai kalleta, daman ko riga babu jikinsa ta taɓa shi, ta ji jikinsa zafi, a hankali ta zaga hannayenta ta bayansa ta rungume sa, hannunta a ƙirjinsa tana shafa sumar ƙirjin ta ce "Bai kamata mijin Safiyyerh ya samu raunin zuciya har haka ba, ka daure, ka jajirce, haba Mai dawa na Barewa ɗan gatan Ammo, haba sadauki" ta ce hawaye na cika idanunta, a hankali ta cigaba da shafa ƙirjinsa, ta ji ya sauke ajjiyar zuciya, ta saka hannunta ta juyo suka fuskanci juna sai ta lakace masa hanci, a hankali ya kwanta jikinta har lokacin bai ce mata uffan ba. Can ya ce "Aby baya so na" ta ce "Injiwa? Halinka ne baya so" ya yi shiru ta ce "Mu bar maganar nan za mu yi daga baya"

"Uhm"

Ta dinga shafa kansa tana addu'a a zuciyarta, a hankali ta cigaba da shafa ƙirjinsa nasa, sai ta ji ya yi murmushi ya riƙe hannunta ya ce "Allah ki bari, ba za ki iya ba"

Ya ce yana juyawa ya rungumeta sosai a jikinta ya ce "Thank you"

*

Guje-guje ake yi sakamakon faɗan da ake yi da yan cikin gari da nan Birget ɗin. Kwance suka same shi cikin jini yana kakari ɗayan ya ce "Kambu wane ya yi maka wannan jahilcin? Sun kashe Zarto"

A kiɗime Jan wuya ya ce "Zarto waye ya yi maka waye ya caka maka wuƙa waye?" Cikin kakarin mutuwa yana ƙoƙarin cewa “Ɗan-fito” sai harshensa ya maƙale ya fara “Ɗan ɗan Ɗan'ma"

"Ɗan'malam?" Cikin sauri Zarto ya jinjina kai alamar e, nan take numfashinsa ya ɗauke. Bazama suka yi neman waye Ɗan'malam unguwa unguwa a nan Birget ɗin.

Uncle Ade na zaune yana alwalar sallar asar domin anjima kaɗan zai koma can garinsu yana shafa fuska yana mutane tsaye a kan shi, ya ɗago kai ganinsu ababen tsoro duka yan'daba ne. Ya ce "Bayin Allah lafiya?" Ya ce da faɗuwar gaba da tsoro.

Ɗaya daga cikinsu ya ce "Don babanka lafiya zata kawo mu area ɗin nan ne? Kai waye Ɗan'malam"

Uncle Ade ya ce "A gidan nan yake amma yanzu baya nan ai"

"Dar, sabga ta ɓaci"

"Idan saƙo ne ku bayar za'a bashi idan ya dawo ni uncle nasa ne"

"Tsoho ka yi gaskiya, kai ma ɗin nrml ne fansa kan iya zuwa akan kowa, don haka zaka amsa masa"

"Ku riƙe mini shi"

Uncle Ade ya fara ihu, mutane gashi yammaci ne ba kowa a unguwar hatta alamjirai babu suka dinga keta masa reza a fuska, ya dinga kiran sunan Allah sai kawai ɗaya daga ciki da idanunsa ke yin hazo-hazo kansa na hayaƙi yana jin duniyar na juya masa ya zaro almakashi mai baki biyu ya cakawa Uncle Ade wajan maƙoshi, ya ciro ya sake caka masa a ciki ya murɗa ya fisgo sai gashi hadda kusan hanjin uncle Ade ya sarƙo a jikin. Almakashin, da gudu suka bar wajan. Ya dinga shure-shure a

wannan gaɓar uncle Ade su yake ya ce Tayo. Sa'adah ce ta fito sai ta fasa ihu tana yin kan uncle Ade nan ya fara nuna mata hanya yana cewa "Tayo Tayo Tayo"

"Me Mutallab ya yi? Waye ya yi maka haka?" Uncle ya sake cewa "Tayo" Malam Abdullahi ma ya dawo kenan daga wajan abokinsa yaga meke faruwa ya ce "Ya kashe shi, shikenan Muɗallabi ya kashe Ade innalillahi wa'inna ilaihirraji'un" da gudu Ammo ta fito suka rufu akan Uncle Ade idan an tambaye shi waye ya yi maka sai ya ce Tayo yana nuna hanya. Kamar an cillo Mutallab haka ya yanko kwana hannunsa na zubar da jini, daga dawa yake ya ɗakko wani ƙaton maciji shine ya farɗe shi hannunsu ke zubar da jini.

Tun daga nesa suke binsa da idanu, ganin wuƙa hannunsa ga jini ya tabbata shi ya kashe uncle Ade? Yana zuwa yaga abin da yake faruwa sai ya ji ƙafafuwansa na rawa sosai, ya zubawa gawar uncle Ade idanu daya cika yanzu, idanunsa ya tsaya cak zuciyarsa ta tsaya cak da aiki na wani lokaci. Kau! Kau! Kau! Ammo ta jera Mutallab wasu tagwayen maruka, ta kasa cewa komai ta fashe da kuka Aby ya ce "Ka kashe shi ka huta ka kashe ka ji innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, na haifi ɗan ta'adda, wallahi tallahi yɑn'sanda zan kira maka" cewar Aby.

Mutallab ya fara ja baya, tsoron zuwa gidan yari ya kama shi, idan aka kama shi Safiyyerh fa? Ya Safiyyerh za ta yi? Bata da kowa sai shi, baya son zuwa gidan yari kashe shi za'a yi. Sai ya fara ƙoƙarin guduwa, hayaniyar da ya yi yawa ya saka Safiyyerh fitowa, Aby ya riƙe muƙamin yana a kira masa hukuma, Mutallab ya saka hannunsa ya kwashe kuɗin gaban rigar Aby, a kiɗime ya ture Aby ya faɗi zuwa gefe, ya juya zai gudu Safiyyerh ta tare shi tana kuka ta ƙanƙamesa ta ce "Kar ka tafi ka barni, don Allah kar ka tafi bani da kowa sai kai" ya girgiza mata kai idanunsa jajur gabaɗaya tsoro yake ji, sai ya rungumeta da ƙyar ya ce "Zan dawo, saboda ke, i will be back Safiyyerh" ya sake ta da gudu ya yi kwana zuciyarsa ta ƙissima masa ya gudu zuwa Lagos.

[1/7, 9:37 PM] Sis Fauzy: Chapter 47: Suffers

Not edited 😂

Kuka ta saka bayan tsallakewa da ya yi ya gudu ya bar ta, ta nufi wajan Ammo tana riƙe ta jikinta na rawa ta ce "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, Ammo na shiga uku na

shiga uku, ya gudu, ya gudu ya tafi ya barni me ya sa zai bar ni, mijina ya gudu na shiga uku"

Ita kanta Ammo ɗin, idanunta ya yi jajur duk ƙoƙarinta na zama jaruma ta kasa, raunin ya gama cin zuciyarta ta yadda har ya bayyana a fuskarta, matsanancin tausayin Safiyyerh ya kamata ga kuma gawar uncle Ade dake a ƙasa cikin jini, yayenta uwa ɗaya uba ɗaya yau shi ɗan data haifa a cikinta ya kashe? Ba tausayi babu imani ya kuma tsallake gawarsa, duk da a ranta tana jin shakku na kisan kamar Mutallab ba zai iya aikatawa ba, ba zai iya kashe uncle ɗin nasa ba.

"Me ya sa baya tausayina na shiga uku Ammo, wayyo Allah"

"Ba ki shiga uku ba Safiyyerh"

Ammo ta ce, tana riƙe ta ganin jikinta na jijjiga sai ihu take musu a wajan ta fita hayyacinta.

"Wallahi na shiga uku, me ya sa hakan ke faruwa da rayuwata, me ya sa zai tafi ya bar ni a lokacin da nake buƙatarsa, me ya sa ƙaddararmu ta zo a hagunce ne, ko laifin da na yi wa iyayena hakan ke bibiyata, he lefted, he lefted me, ya san shi ne kawai madogarata, me ya sa bai ɗauke ni mun tafi tare ba, ya san ni me mai rufa masa asiri ce, saboda baya so na, na shiga uku na lalace mijina ya gudu ya bar ni"

Ganin numfashinta na tafiya ya saka Sa'adah zuwa da sauri ta kamata, amma kamar mai aljanu haka Safiyyerh take misbehaving, ƙirjinta na ɗagawa da matsanancin ƙarfi, zafi da raɗaɗin da yake ratsa ƙirjinta ya saka take jin hucin har maƙorar zuriyarta da take bugawa dalilinsa, dalilin soyayyarsa, numfashinsa shike sanya nata numfashin daidaita, ta ɗauka zasu iya raba ƙaddarar tare, ashe ƙaddararta tata ce kawai, zunubinta nata ne, kuskurenta nata ne, wawta tata mallakinta ce kawai, ita kaɗai.

Ashe hauka ta yi data rabu da kowa ta zaɓe shi matsayin inuwarta, ashe hauka ta yi data zaɓi cin amanar aminiyarta tun ta ƙuruciya, ashe hauka ta yi data ɓoyewa

Mutallab gaskiya akan Aafiyyah. Wanne irin so ne da lokaci baya kawo daidaiton shi?.

Safiyyerh sai ta ji zuciyarta na matsewa ta cikin ƙirjinta, tana yi mata motsi, motsin dake motsa mata da tarin soyayyar MOH, hucin da yake yo mata sama har zuwa maƙoshi, ta ɗauka soyayyar zata mutu a yanzu, sanda ya tsallake ya bar ta ranar tariyar aurenta, sai zuciya taƙi yi mata wannan halaccin taƙi mara mata baya, ta kunyata ta, a hankali soyayyar MAI DAWA ta fara raya kan ta, tare da yin sabon reshe tare da zuba yabanya cikin zuciyar Safiyyerh, sai ta ji koda Professor Abdu mai haife ta domin rayuwa da MOH ba, to ƙaddararta ta MOH ce, domin kowacce rana da faɗuwarta ƙara kusanta zuciyarta da tashi take, rayuwata take yi kawai domin shi, only him.

"Safiyyerh ki shiga hankalinki"

Ta dai ji sautin muryar Sa'adah tabbas, ta ga kuma laɓɓan Sa'adah na motsawa tabbas, bata da tabbacin dai ta ji me take cewa ɗin, juyar bakin kawai take gani, hawayenta yaƙi tsayawa yana sake bayyanar da raunin zuciyarta a zahirance.

Riƙo kafaɗunta Sa'adah ta yi ta ce "Safiyyerh ki nutsu, kar ki haukata kan ki, ki dawo duniyar tunaninki"

Safiyyerh ta yi murmushi ta ji furucin a ƙirjinta a mamakance take duban Sa'adah kafin ta ce.

"Kullum da sharri yake rama alheri, kullum da mugunta yake rama abin arziƙi, da gwatsalewa yake nuna godiyarsa, da ɓacin rai yake mayar da raddin murmushi, shi rigimammen namiji ne, rigimammen mijina kuma duka na ɗauki rigimar tasa, Just to be with him, to live with him, ko kuka zanyi ƙirjinsa ya zame mini mafaka, madadin haka qwiwoyina nake sawa na yi kukan, ku zan mutu ya zamana Ubangiji ya ɗauke numfashina a tafukan hannayensa, he is the man who i pray for, he is my husband, shi ne zai gudu ya bar ni, shi ne zai guje mini, shi ne ko?"

Baya ta fara yi tana murmushi hawayen na sake zuba tana kallon gawar uncle Ade, tana kallon Sa'adah ta juya ta kalli Ammo, kana ta kalli Aby ta ce.

"I realised, i am nothing to him"

"Safiyyerh!"

Ta juya ta ce "Bafa zan mutu saboda shi ba, zan dai jira ranar dawowarsa, satuttuka, watanni, shekaru zan rayuwa da zaman jira"

Sai ta fara kuka mai ƙarfi, kukan tunanin barin iyayenta da ta yi, ta fara tunanin soyayyar ƙuruciyar data ja mata komai, ta fara tunanin lack of parent audience ya ja mata, ta fara tunanin matakin adolescence stage ya ja mata, she just love him, for the sake of the, for the sake of love, love ɗin data fara tunanin Forbidden love ne, akan soyayyar da Aafiyyah ke masa.

Safiyyerh sai ta ji iskar wajan ta fara yi mata kaɗan, bata sauka a ƙirjinta a hankali ta fara kokawa da numfashinta, a ƙoƙarin shaƙar iskar bisa dole, sai ga ji saukar iskar a kurɓace cikin ƙofofin ƙirjin nata, wani sanyi maikama da sanyin shigar zazzaɓi ya fara ratsa fata baƙwai da Ubangiji ya halitta a ƙirjinta, yana huda ƙasusuwan gaɓɓanta. Ta yi murmushi ta ce.

"Allah kar ya sake na mutu bai dawo ba, ku faɗa masa saboda ba zan yafe masa ba, kar ya zo mini kabarina, kar ya razana ruhina da kukansa, dole zai yi kuka dole bayan babu Safiyyerh a duniyar"

Duka bin ta suke da kallo, gani suka yi idanunta ya fara lumshewa jiri na ɗaukar jikinta. "Sa'adah riƙe ta"

Kafin Sa'adah ta cimma Safiyyerh, tuni ta sulale ta faɗi a wajan babu numfashi a ƙirjinta kan ta ya ɗan daki dutsen da yake wajan.

A gigice Sa'adah ta yi kanta ita da Mama Zaituna, hankali a tashe. "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, innalillahi wa'inna ilaihirraji'un!" Shine kawai abin da Ammo ke nanatawa ta zube a kan gawar ɗan'uwanta, Inna Binta ta yi wuƙi-wuƙi sai ta ji tsoron Mutallab ya zauna daram a zuciyarta, ta fara tsine masa without knowing the truth. Daidai nan motar jami'an tsaro ta ƙarasu wajan, kai tsaye gawar uncle Ade suka ɗauka zuwa cikin mota, wasu kuma suka tsaya ɗaukan statement na abin da ya faru, Inna Binta ce a gaban wajan faɗar labarin ƙanzon kuregen, duk wank bincike da suke samu sai ya nuna musu cewa MOH ne ya yi kisan, amma basu haƙura ba, suka ɗauki gawar uncle Ade zuwa asibiti. Sa'adah da Mama Zaituna suka ɗauki Safiyyerh zuwa asibiti itama, Ammo ta zama kamar statue ta rasa mene yake damunta, me kuma take ji akan Mutallab? Bata cewa komai sai idanu.

Duk da faruwar faɗan daban da aka cilla sunan Mutallab da bai ji ba, bai gani ba, da baya alaƙa da duk wani ɗan daba, amma an gaza gano gaskiyar abin da ya faru sunan Mutallab ya fara amsa amo matsayin wani ɗan daba ya kashe wan babarsa, mutane suka hau tare da zama akan ƙanzon kuregen da aka ɗora su. Faruwar hakan baya rasa nasaba da abin da Aby yake jingina da Mutallab da shi koyaushe, sunan ɗan daba ko tantirin da yake faɗa masa suka fara tasirin ba tare shi kansa Aby ya san cewa mugawayen alkaba'in da yake jifan Mutallab da shi, sune suka fara tasiri.

Wayar Uncle Ade Sa'adah ta yi amfani da ita wajan kiran can garin, amma maganar da ta ji ya gigita mata lissafi sosai. Ta juya ta kalli Ammo ta ce "Ammo kin ji me suka je?"

"Bana buƙatar ji, ki riƙe duk abin da kika ji, kuma bana son tambaya za'a yi masa jana'iza a nan Allah Ya yi masa rahama"

"Amin"

Sai suka yi shiru, Bafullatana na can wajan Safiyyerh har yanzu bata farfaɗo ba. "Ammo don Allah kar ki ji zafin Mutallab, kar mu yanke masa hukuncin don Allah"

"Sa'adah zai fi kyau ki mini shiru, akan idanunki komai ya faru, Ade da kansa ya ce Mutallab ne ya yi masa hakan, ba zai masa ƙarya ba domin n kaɗai na san so da shaƙuwar dake tsakaninsu haka kawai ba zai wa Mutallab sharrin kisa ba" a hankali

Ammo ta fara kuka sosai ta ce "Bana son zubarwa da MUTALLAB waye, bana son yin kuka saboda shi, bana son na ji kamar ya gagare ni, ɗa namiji tilo a cikinku rayuwarsa ta zama haka?"

Sa'adah itama kukan take yi ta ce "Me ya sa kuke aibata shi, me ya sa kyakkyawan kalami baya fitowa daga cikin bakinku a kan shi, har gwara ke kina sassautawa, Ammo iyaye fa gwarkuwa ne a rayuwar yaransu suna iya yin kowacce sadaukarwa saboda kawai su gina goben yaransu. Mutallab ya buɗe idanu da mugun bakin Malam, duk wahalar duniya akan shi, zagi, hantara ki duba har ce masa yake ɗan ta'adda ko jinin fir'auna, baya bashi ci baya bashi sha, ba suttura ba kulawa ba tarbiyya. Wallahi wallahi akwai hakƙin Mutallab da yawa akan ku ke da Malam, mu ma kanmu Ubangiji ke riƙe da tarbiyarmu, kina kallo gari zai hawaye babu abin karyawa za'a ce kowa ya nema da kansa, ni da nake mace ina zan fita nema idan ba bara zan yi ba? Daga nan rayuwar yara mata ke lalacewa, su fara bin maza muddin aka gaza riƙe su a gidan iyayensu, ba ki taɓa zama da Mutallab kin ji ina yake samun kuɗin da yake cin abinci ba, ba ki taɓa zama kin tambaye shi ina yake samun kuɗin da Malam ke amsa a wajansa ba tun ba yanzu ba, ba ki taɓa tambayarsa ya aka yi ya fara zuwa makaranta ba, ba ki taɓa cewa ya taɓin hankalinsa ba, ba ki taɓa zama kin tambaye shi mene ya faruwa a mutuwar Diyna da Jaanah, mene ya faru a inda aka kai shi wajan jami'an tsaro ba, ba ki san ya akai ya fara yawo da karnuka ba, ya akai ya fara farauta ba, ya akai ya fara yin bugun ƙasa ba. Ammo ba haka kawai Ubangiji ya fara ambatar UWA kafin Uba ba, ba haka kawai Ubangiji yake halittar Ɗan'adam a cikin uwa ba, akwai manufarsa ta yin hakan, lallai furucin Malam shi ya fara tasiri a kan Mutallab"

"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un!" Cewar Ammo tana sakin wani irin kuka sosai.

A nan akai jana'izar Uncle Ade.

*

Hon Ali wali, ɗan majalisar tarayya shine ya mike tsaye yana ƙyaƙyacewa da dariya cikin sauri Boɗejo ya miƙe shima suka taɓa tare da haɗa cups ɗin hannunsu alamar cheers.

"Ai na faɗa daman, duk wanda ya haɗa hanya dani ya shiga uku, dole a bar mu,mu yi yadda muke so in sha Allah"

"My friend Hon Ali wali, siyasa taku, makirci naku, tukku naku wanda ya haɗa neman kujera daku ya cikin tashin hankali"

"Hahahaha, Boɗejo ikon Allah" ya ce suna sake tafawa da rungume juna.

Boɗejo ya ce "Distinguish, wannan celebration ɗin fa? Na mene?"

"Mun yi magana da kai akan muƙamin bulaliyyar majalissa da na ce ina so akai mini zaƙon ƙasa a green chamber wai za'a bawa Bebeji, to an yanka ta tashi, ɓas ɓas ɓas yanzu nine aka saka sunana a matsayin"

Jinjina kai Boɗejo ya yi ya ce "Ka yi tsiyar kenan, me ka yi cikin sauri haka?"

"Tsugunar da shi na yi kawai, ya zama gurgu ba zai taɓa tashi ba, kaga kowa ba yadda za a yi su bashi wannan matsayin".

"Ikon Allah, a sabgar siyasa dai ba'a matsoyi na dindindin, ba'a maƙiyi na dindindin?"

Ali wali ya ce "Absolutely right, idan kana son zama wani a siyasa dole ka zama mara kunya, ka zama jan biro maganin daƙiƙin yaro, ka cire tsoro ya zamana ko'ina kana da idanu. Yanzu shi wannan Ɗan Majalisar na Bebeji P.a ɗinsa yaro na ne, P.a ɗin na bawa abin ya saka Bebeji na takawa ya tsuguna, wani aiki ne da aka yi mini da jinin mutane da allurai, wannan alluran suna cikin ƙafafuwan Bebeji"

"Wonder shall never ends, ni sabgar siyasar nan tsoro take bani gwara na tara arziƙi da dukiya sosai" Boɗejo ya ce yana neman wajan zama a hankali ya kai cup bakinsa yana zuƙar lemon. Hon Ali wali ya zauna shima yana kallon Boɗejo da kyau ya ce.

"Kai zafin kai ne da kai, da kuma izza kana son iko Boɗejo, amma siyasa duniya ce, kuɗin gwangila, gyaran titi, asibiti, makarantu uhm"

Boɗejo ya ce "Great, mene ainahin aikin ɗan majalissar tarayya ne Friend?"

Murmushin Ali wali ya yi kana ya ce "A matakin gwamnatin tarayya dama matsayin uku garemu Shugaban ƙasa, Sanata. Dan majalisar tarayya, Dan majalisar tarayya.

A najeria Muna da local government 774 a jahohi 36 harda Abuja akwai yan majalisa guda 360 a najeria wani Dan majalisa yana wakiltar karamar hukuma guda daya wani biyu wani har 5 Shiyasa suka zama guda 360. Aikin Ɗan majalisar tarayya shine yin doka da samar da kudirin da zai kare muradin yan kasa aduk lokacin da zaayi doka Ana zama a karanta kudirin sai asake zama na biyu aji raayin yan majalisa acikin mutum 360 idan aka Samu kaso biyu cikin uku suka aminche to kudin ya zama doka sai ayi zama na uku a tabbatar ya zama doka. Yana iya samo ayyukan daga gwamnatin tarayya Kuma duk shekara zaiyi budget na abinda mutanen da yake wakilta suke bukata shine constituency project"

Boɗejo ya jinjina kai, Ali wali ya ce "Wannan shine gaskiyar magana"

"To wacce gwangila za'a bani ne? Wacce zata kawo mini kuɗi da yawa sosai"

"Hahaha zan duba, yanzu gobe zan koma Abuja in sha Allah, Madam na da juna biyu kuma inda namiji ne da haihuwarsa gwara ɓarinsa"

Cewar Ali wali, sai Boɗejo ya buɗe ido with shocked ya ce "But why? "

"Ina da plan ɗina, ina sabga da yara yan daba wasu ma duka mune dalilin zamuwarsu yan daba saboda siyasa ni ba zan iya haifar ɗa namiji ba, balle hakƙin yaran ya shafi abin da na haifa Noor ta ishe ni, itama kaffa kaffa nake yi bana son abin da na yi ya shafe ta"

Boɗejo ya miƙe ya ce "Shegen kaya, to ina murna sosai congratulations for Chief Whip. Ensures party discipline and cohesion"

"Boɗejo ɗan iskan kaya, sai mun yi magana"

Kasancewar tsakiyar dare ne ya saka Boɗejo yin driving da kansa zuwa keɓantaccen gidan abokin nasa Hon Ali wali, ya shiga haɗaɗɗiyar motarsa black colour mai zubin Toyota Camry a hankali ya fara driving, yana tafe zuciyarsa na ƙissima masa tunani kala-kala, shahara yake so ko ta halin yaya ne abin da yake da shi sam bai gamshe shi, ko a yanzu yana cikin jerin masu kuɗin unguwar da yake dama jihar amma ƙasa fa? Ai kasa bata san da shi ba, da wannan tunanin ya ƙarasa unguwar da yake zaune ta Railway.

*

Kan shi a duƙe ƙasa duk irin tsala gudun da ake a cikin motar data ɗauke su zuwa Lagos bai sani ba, shi bai san meke damunsa ba, da zarar ya rufe idanunsa sai ya hango gawar uncle Ade cikin jini, mutumin da ɗauka matsayin uba, shi aka kashe kuma aka jingina alhakin kisan nasa a kan shi, sai ya ji ko ma yaya ne koma su waye sukai masa haka wallahi tallahi jinin uncle ɗinsa ba zai tafi a banza ba, sai ya ɗauki fansa, fansar kisan wulaƙancin da akai masa. Sai ya ji zuciyarsa da idanunsa sun bushe baya gane komai kuma baya fahimta bai san wanne irin mataki zai ɗauka ba, yunƙurin fansar ne kawai yake kai komo a tunaninsa. Wani dake gefensa ya dinga taɓa shi amma bai sani ba, sai da aka girgiza shi da sauri ya ja numfashi ya ɗago rinannun idanunsa, ya kalli mutumin.

"Bawan Allah mun ƙarasu, sai biyu ana tsayawa yin sallah da cin abinci baka cewa komai"

A hankali Mutallab fara juye juye alamar yana neman wani abu, ganin bai ga abin da yake nema a cikin motar ba ya miƙe ya fara dubawa kujera zuwa kujera. Mutumin ya ce

"Me kake nema ne?"

"Safiyyerh, matata" ya ce da ƙyar.

"Ai kai kaɗai ka shigo motar nan, ko kaya babu a hannunka balle mace, ko ka mantata a tasha?" Mutumin ya tambaya.

MOH ya yi saurin rufe idanunsa a hankali ya tuna abin da ya faru ya juya zai gudu Safiyyerh ta tare shi tana kuka ta ƙanƙamesa ta ce "Kar ka tafi ka barni, don Allah kar ka tafi bani da kowa sai kai" ya girgiza mata kai idanunsa jajur gabaɗaya tsoro yake ji, sai ya rungumeta da ƙyar ya ce "Zan dawo, saboda ke, i will be back Safiyyerh"

So she lefted her? Ya bar Safiyyerh? Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, ninkin tsoran shi ya ƙaru kar aje a kamata madadinsa, yanzu Safiyyerh bata da kowa sai shi, da wanne idanu zata kalle shi? Da wanne baki zai mata bayani, dole ya koma ya ɗakko ɣar mutane duk mai zai fuskanta su fuskanta tare. Ya zaro kuɗin aljihunsa na Aby daya kwaso juya kuɗin ya yi, yaga za su kai 100k ko zasu mayar da shi gida su sake dawo da shi Lagos da ita?.

Ya dinga tunani yaga dole zai haƙura ya zauna for a while kafin ya koma yana da tabbacin za ta yi kaɗaici za ta yi kuka, kukan Safiyyerh kuma a yanzu shine abin da baya so ɗin, shi abin da yake jin tsoro. Mutallab a Lagos, Lagos ɗin data sake zama sila ko kuma mafarin faruwar ƙaddarar, mutuwar uncle Ade ya zama key na faruwar zama abin da ya zama.

Gararramba ya fara yi domin bai san ina shi ba, mutane a Lagos kamar me gari ne da komai da kazo anfika idan iskanci ne, idan ilimi ne, idan arziƙi ne, idan kasuwanci ne. Gari ne mai tarin albarka da tarihi, duk abin da kake so zaka samu abu ɗaya ne masa lamunta shine “Sata” akan sata za'a iya kashe mutum murus a saka masa taya basu da imani ta wannan ɓangaren sam. Waje ya nema ya zauna bayan ya yi sallah ya dinga kallon garin yadda ake musu ruwa koyaushe weather ɗin mai kyau ce irin wacce yake so, sai dai bashi da nutsuwar jin daɗinta, har dare ya nutsa yana zaune a kuma lokacin ya fahimci wata kasuwar naci.

"Yaa?" Ya ji an ce masa.

Ya juya kaɗan, ya ga wani matashin saurayi amma zubinsa ba mai kyau bane gabaɗaya sai Moh ya yi shiru, matashin ya ce "Kai a Lagos kake, ba'a zana haka kurum za'a ja maka jarfa ka yi ka dafe sawayenka"

"Baƙo ne ni"

"You dey crazy, take ur foot and leave"

"Why? Garin na babanka ne?"

"Kut?" Wani irin fito ya yi sai ga wasu gang team manyan dasu sun zagaye Mutallab, ya dube su gabaɗaya sai ya ɗauke kan shi gefe, ƙoƙarin matsar da shi suka yi ya cije, ɗaya ya ɗakko wuƙa ya nufi Mutallab amma yana yanka masa wuƙar ta lanƙwashe madadin ta yanki Mutallab, suka kalli juna VJ ya ce

"Kambu, ku danne mini ɗan tsakon nan"

Su wajan biyar suka fara kokawa da Mutallab ya ɗauki ɗaya ya buga da ƙasa, a haka suka kai shi ɗaya, mutane nata shigewa amma ba ruwan kowa da kowa suna danne Mutallab ɗaya ya sake ɗakko wuƙa da niyyar yanka wuyan Mutallab, amma wuƙa ta yi al'ƙawarin ba zata ci jininsa ba, ganin sun kasa sanya masa ƙarfe ya saka suka fara kai masa duka, yadda saka su kabel fuskarsa ta kumbura, wannan tsananin azabar ya sake ƙeƙasar da zuciyar Mutallab, ya ji duk wani tausayi da imaninsa sun fara tafiya domin jahilin duka sukai masa, kana suka ɗaure shi a wani ɗaki amma tari wannan bai yi ba, daya rufe idanunsa sai ya hango gawar uncle Ade, da ya yi shiru kuma sai ya fara jiyo sautin kukan Safiyyerh, zuciyarsa motsi take masa da Safiyyerh sai ya ji ko zai rage tausayi dominta ne kawai ita kaɗai.

VJ ya buɗe ƙofa wajan 3 na dare mamaki ya kama shi ganin Mutallab ko gyangyaɗi baya ya yi, sai ya ji jarumtar yaron ta birge shi sosai ya dinga kallon zanen da yake ƙirjin Mutallab, nan take ya fahimci zanen SCORPION ne.

"Ya sunanka?"

Ya yi shiru yaƙi magana, sai huci yake yi, idanunsa jajur jijiyoyin kansa duk sun fito, a lokacin tunanin yadda Aby ya yi masa muguwar tsana haka yake. "Kaga ba sake dukan ka za mu yi ba, zamu shigar da kai Gang team namu ne muna buƙatar irin su"

Ya fara kunce shi ya ce "Sunana VJ zan kula da kai, mene naka sunan ga abinci ka ci, ka kuma kaya ka saka sai mu yi magana, mene naka sunan?" Ya tambaya yana zama.

"Ɗauke abincin, ka fita"

"Ok, zan fita ga magani ka sha saboda raɗaɗin jikinka ko? Zaka samu ka yi bacci"

Sai Mutallab ya ji baccin yake so, da gaske baya buƙatar tuna duk abin da ya faruwa ya amshi maganin ya shanye kwalbar tas, ya yi shiru ya fara tunani ya jima a haka kafin ya ce. "Sunana Moh daga Kano nake, an kashe mini uncle ɗina ance nine, babana ya ce sai kai ni wajan hukuma shine na gudu bana son gidan yari"

Vj ya dinga murmushi ya san dole zai yi magana "Yanzu me kake son yi?"

"Wanda ya kashe mini uncle ya mutu"

"Fansa kenan?"

Mutallab ya yi shiru, idanunsa na lumshewa ya fara jin nauyin zuciyarsa na raguwa amma duk wani fitar numfashinsa da tunanin fansar uncle Ade yake fita. "Idan mutum ya ɗauki makami ya kashe maka wani, sunan hakan zalunci, idan kuma kana son ramawa dole ne ka ɗauki makami domin shine mafitar ka"

Idanunsa yake son buɗewa amma ya gagara hakan ya dinga jinjina kansa ya dinga cije lips ɗinsa a firgice kuma yana razana ya ce "Bana son kashe mutum, ina son ramawa a hukunce wajan jami'ai" Vj ya daki kafaɗar Mutallab ya ce "U dey crazy, hukuma ba uwar da zata yi maka yadda baka da shaida kai za'a kama kaci ubaka cinnaku ba imani gare su, kai zaka ɗauki mataki da kan ka" Vj ya miƙe ya fita. Maganin yaƙi saka Mutallab bacci saboda ƙarfin jininsa, sai maye da yake sashi hakan ya taimaka wajan yarda da maganar da Vj ya faɗa masa, daya runtse idanunsa zai zabura yana wallahi ban kashe shi ba, bani bane. Ko kuma ya dinga tuna Safiyyerh a ransa.

A sati guda da ya yi, ya ci ubansa a wajan Gang team ɗin, sai a haɗa shi faɗa da ƙaton mutun a yi wa Mutallab jahilci, shi kuma zuwa ya ce sai ya rama ya dinga jin targaɗe da tsagewar ƙashi zuciyarsa ta sake bushewa a haka suka dinga ɗora shi a tsarin da suke. Suna siya masa abinci da komai da kayan sawa, amma baya iya cin abinci kullum cikin dare baya bacci. Ranar daya fahimci yan fashi ne ya sulale cikin dare ya gudu daga wajansu ya yi nisa sosai ya nemi wani ɗaki haya aka ce 20k duk kwana ɗaya, a haka ya yi kwana uku ga kashe kuɗi sai ya ji zai mutu saboda wahala ya siyi abinci ya ci, ƙosai ɗaya 100 komai tsada a Lagos. Kuɗin ya ƙare sai ya fara yin bola-bola yana tarawa kamar yan gwangwan yana siyarwa domin ba zai iya taɓa hakƙin wani ba a gabansa aka yanke hannun wani ɓaraho jikinsa ya saba da wahala ya sake yin duhu jikin ya buɗe lokaci guda.

*

Kamar yadda ya shafe sati da tafiya haka Safiyyerh sati guda bata farka ba a gadon asibiti, duk kuɗin hannun Ammo ya ƙare Sa'adah kuma sun tafi Haɗeja ita da mijinta.

A hankali ta fara motsawa tana buɗe idanunta da sukai mata nauyin gaske. "Safiyyerh"

Jin muryar Ammo ya saka Safiyyerh buɗe idanunta da sauri tana dubawa muryarta baya fita ta ce "Mijina"

"Ki yi haƙuri haka, ba ki da lafiya"

"Shikenan ya bar ni shima? Wai laifin me na yi wa Ubangiji haka? Bani da kowa zafi nake ji a zuciyata ƙirjina ya mini nauyi Ammo"

Kuka ta fara sosai Ammo ta rungumeta ta ce "Ƙaddara ce ta faɗo mana, babu yadda muka iya ki taya shi da addu'a Ubangiji yana amsa addu'ar mata ga mijinta watarana sai labari"

A hankali ta girgiza kai zuciyarta na ta fasa ta ce "Kawai baya so na ne, ni kuma Ubangiji ya ƙaddara zama na da shi, ya gaji ne ya gaji da zama dani shine ya gudu ya bar ni. Daddy ya tafi Ummeyh haka, uncle Musbah uncle Nasim yanzu mijina ma ya gudu, ya zan yi da raina ne" ta ce tana shasshekar kuka.

"Haƙuri za ki yi, ni ina tare dake, komai zai zama labari kin ji?" Ta ɗago kai ta kalli Ammo ta ce "Sanda na mutu ne zai zama labari? Ai shikenan zan cigaba da haƙuri lokaci alƙali"

Fita Ammo ta yi zuwa wajan likita ta faɗa masa Safiyyerh ta farka. Tana fita Safiyyerh ta ɗauki wayarta ta fara kiran number daddy amma baya shiga ta kira ta Ummeyh duk wanda zata kira a family har Wahee amma bata samu ko mutum ɗaya ba, a hankali ta danna number Mutallab shima baya tafiya. Ta haɗe kanta da qwwia ta fara wani irin kuka mai cin rai da zuciya, tana nan zaune likita ya duba ta ya tabbatar ba komai aka sallame su suka nufi gida. Ta dinga bin ɗakin Ammo da kallo babu komai sai katifa, hatta kayan siyarwar babu komai to suna ina? Ta juya ta kalli Ammo sai ta ce "Zauna ki ci abinci"

Ta nemi bakin katifar ta zauna, awara mai zafi ta kawo mata da aka soya da ƙwai sai miya dake gefe wacce aka sakawa kifi. Safiyyerh ta dinga kallon abincin, to bayan hakƙin iyayenta maybe akwai hakƙin Aafiyyah a kanta wanda ya hanata sukuni. Ta lumshe idanunta hawaye na sake bin kuncinta, tabbas idan ta ce bata san ya Aafiyyah ke son Mutallab ba ta yi ƙarya, sanda Aafiyyah ta fara son Mutallab ita bata san da shi a duniyar ba, a ranar data fara ganin Mutallab, haɗuwarsu is not about the love, just friendship ne, bata kawo soyayya a ranta ba, ta san kowa nada aboki a makarantar, sai kuma taga Mutallab shine abokin zamanta a class why not ya zama bestie ɗinta ba friend ba? Kamar yadda Kimiyya yake shi da Aafiyyah, kamar yadda Nahyan yake shi da Kinal itama ta zama ita da Mutallab, kwanansu biyu da Mutallab a makaranta amma bata taɓa kawo soyayya a ranta ba, sai sanda ta yi searching a goggle aka nuna mata baƙaƙen mutane sun fi kowa iya kula da

mace, sun fi iya sosai, with romantic and sex style. Sai ta ji why not ta so Mutallab? Ita bama ta tabbatar soyayyar bace shi ya saka ta kira Aafiyyah, ita kuma Aafiyyah a lokacin she is crazy a soyayyar Mutallab.

Sometimes ko a chatting ko a makaranta Aafiyyah ta kan ce "Safiyyerh bamu muke faɗawa soyayya ba, soyayya ke faɗawa kan mu, da laifin na yi Ubangiji sai na ce babu mamaki don ya azabtar dani ya saka mini soyayar Yaa Muhammad, true love bashi da reason, baka da dalilin cewa ga abin da ya saka kake son wani, kawai dai kana son shi ne"

Safiyyerh sai ta fara tunanin, ita farko soyayyar Mutallab ai manufa ce a ranta saboda shi baƙin namiji ne zata samu duk abin da take so, Aafiyyah kuma ƙaunar shi kawai take with no reason, bata da hujja son ne kawai ya hudu ƙirjinta da zuciyarta.

"Aafiyyah me ya saka kike ce masa Yaa Muhammad kuma?" Safiyyerh asked Aafi.

"Idan ke age mate kuke, ni ya girman ko yaya ne, idan mutane sun ce masa Mutallab yana da kyau na zaɓa masa wani sunan, ina jin daɗi idan na kira shi da Yaa Muhammad"

"Tell him kina son shi"

"Sweetheart sau nawa zan faɗa miki? Banda umarnin iyayena da tuni muna soyewa da ɗan baƙina, na san tunda Paaah ya mini al'ƙawari dole zai aura mini shi, i love him so much"

"A duk sanda na saka glasses bana ɗauke idanuna akan shi, shi Jarumi ne, my Blackman, ina hura zuciyata da avoiding nasa, da yadda nake treating nasa wallahi, don Allah Safiyyerh ki kula da shi kafin na samu lokaci ya bani damar kasancewa da shi"

***"I am sorry Aafiyyah, ba zan iya jure ganinki tare da mijina ba, kina da qualities ɗin da zai iya juya mini baya dominki, na san kina da sadaukarwa ki yi mini alfamar ki bar mini shi, na san kina jure komai a kaina wannan ma za ki jure, wallahi i can't tell him"

Sai ta ture abincin zuriyarta a cunkushe. A daren ta fahimci Ammo ta siyar da komai nata dalilin zaman asibiti sai ta fito da kuɗin wajan uncle Musbah ta bawa Ammo suka saka jari, lokacin kuma azumi na gab da zuwa, duk abin da suka fara kamar saka hannu zai lalace, kuma time ɗin Inna Binta bata jima da dawowa daga garinsu Katsina ba.

Sai ya zamana hatta Safiyyerh ta je ta siyar da zobenta na gold a ɓoye ta kawo kuɗin nan ma ya ƙare, cin abinci ya yi musu wahala Bafullatana kuma ranta ta ne a ɓace bata ma san halin da suke ciki ba, kuma daman bata shiri da Malam. Bata da haƙuri sam ko yatsa aka ɗaga sai ta ce da ita ake kasancewarta kurma akwai saurin tsarguwa.

"Safiyyerh" ta ɗago ta kalli Ammo tana murmushi Ammo ta ce "Wannan murmushin bai kai zuciya ba, ki yi haƙuri da halin da kika tsinci kan ki Safiyyerh, in sha Allah za ki ci ribar haƙuri ko ba yanzu ba, duk kin rame duk hasken fatar nan babu idanunki ya shige ciki duk akan shi kike haka?" Murmushi ta sake yi s hankali ta ce "Kai Ammo, ba komai fa"

"Daman ba komai ai, haka kike faɗa zurfin cikin ki ya yi wa, gashi kin ɗauki abu mai daraja kin siyar haba Safiyyerh"

"Ke fa uwa ce Ammo"

"Allah ya sanya albarka, Ubangiji ya shiga lamuranki ya wadata farinciki a rayuwarki"

"Uhm am"

"Akwai magana ne Safiyyerh?"

Idanun Safiyyerh ya cika da ƙwalla ta ce "Ammo idan iyaye sukai fushi da yaransu hakan yana nufin basa son su?" Ammo ta yi jim sai ta ce "Ke macace Safiyyerh, kafin kasancewa da namiji sai ka jika a wata duniya ta daban, wannan raɗaɗin daban yake, shigar ciki da laulayinsa mata kaɗan ke jurewa, zaman ɗana cikin uwa mahaifiya watanni tara a mahaifa, ya dake ta a ciki ko cikin bacci ya motsa sai ka farka, naƙuda ba kowacce uwa ke hayewa ba, ka shayar da yaro watanni goma sha bakwai wasu shekara biyu, kashi, fitsari wanki kuka rashin lafiya duka uwa ce. Safiyyerh duk wannan abubuwan taya kike tunanin uwa zata daina son ɗan ta? Wannan soyayyar, wannan ƙaunar daban Ubangiji ke samana a zuciya, duk inda uwa take tunanin yaranta ne a zuciyarta. Iyaye ba za su taɓa daina son yaransu ba har abada kin ji?"

"Me ya sa dani da Mutallab iyayenmu suka wofintarmu suka kasa tsayawa mu raba ƙaddararmu tare Ammo, iyayena sun bar ni, shi ya bar nasa iyayen yaushe zai dawo bamu sani ba, Ammo shin mu wanne laifin mukai muku ne? Don Allah ku yafe masa ku sanya mu cikin addu'a, ki yi wa Mutallab addu'a kalli halin da muke ciki, mu yara muna da taurin kai, ba komai muke ganin daidai bane ku da kuka san hakan sai ku yi mana uzuri, mufa kiwo ne a gare mu Ubangiji zai tambaye ku"

Jikin Ammo ya yi sanyi sosai damuwarta ta bayyana dai ta miƙe ta fita. Karo suka suka ci da Malam ya ce "Yawwa yarinyar"

"Wacce yarinya?" Ammo ta tambaya fuska babu walwala. Ya ce "Safiyya ko? Tunda mijin nata ya zama ɗan ta'adda ta tattara kawai ta koma gidan iyayenta kin ji ko, bana son zamanta a nan gandan-gandan"

"Ba inda zata Malam"

Ya buɗe idanunsa ya ce "Mene? Ni da gidana ina bada umarni to wallahi za ki bita ku tattara ku fice tunda kin haifa mana masifa"

Ta yi murmushi kawai ta ce "Abdullahi matsa ka bani hanya don Allah" da wani irin tarin mamaki ya ce "Abdullahi? Za kiga kin kira sunana ke fito ki tafi gidanku kin ji ko?" Ya ce yana ɗaga labulen ɗakin Ammo da sauri Safiyyerh ta miƙe tsaye jikinta na rawa, itama Ammo jikin nata rawa yake ta ce "Na faɗa Abdullahi ba sunanka bane? Wallahi ba inda Safiyyerh zata je ka fahimta? Kuma ko sakina za ka yi ka daɗe baka sake ni ba, nan gari nan bari babu inda zani wallahi, naga kai baka fahimtar kawaici da haƙuri don fa ka sake ni babu abin da zai faru dani mene a cikin auren naka Audu? Dan Allah kauce ka bani waje" ta ce idanunta na cika da ya ce "Ko duka na za ki yi ne?" A cikin zafin rai ta ce "Tas, wallahi sai na bugaka da ƙasa a wajan nan"

Ya jinjina kai ya ce "Ki je na sake ki"

Sai ta ji jikinta ya yi sanyi da furucin nasa, amma ta gwammace ta yi sadaukarwar sakin nan akan Safiyyerh da kuma Mutallab ta kula da yarinyar mutane a sanyaye ta ce "Saki nawa?" Ya ce "Ɗaya"

Safiyyerh ta rushe da kuka, duk akanta hakan ke faruwa wai? Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un Ya Allah ya kawo mata mafita cikin gaggawa. Har dare ya yi tana kwance ciwon kai take yi sosai, Ammo kuma ta fita ta san neman abinci ta fita yi, ita ta farka taga Safiyyerh cikin sauri ta miƙe ta yi alwala da sallah tana jin Inna Binta da Mama Zaituna suna sakin yʻan habaice-habaice ita dai bata fahimta, cikin sauri ta saka hijjab ta fita daga cikin gidan. Tafiya ta dinga yi ƙafarta futu-futu tana ganin duhu cikin idanunta ga jiri yunwa take ji sosai, a haka har ta kawo ƙofar tangamemen gidan an cika tare da yin layi na amsar abin sadaƙa ta dinga kallon layin da almajirai suke bi, da kuma layin da mata suke bi taya zata iya bin wannan layin? Yunwa take ji kamar ta ci babu.

Jiki ta ja ta je ƙarshen layin, amma har wajan 12 layin bai zo kanta ba, bakinta ya bushe da ƙyar take buɗe idanunta, a hankali ta juya ta fara tafiya ba wani nisa ta yi ba sosai ta ji an ce

"Matar Mutallab"

Ta yi saurin juyawa, idanunta ya sauka akan Ja'aafar, daya fito daga cikin mota wacce kuma kana gani cikin gidan Boɗejo zai shiga a hankali ta ce "Ina yini?" Ta ce a sanyaye fuska a ɗan kame tana ɗauke idanunta.

"Lafiya, Safiyyerh ko?" Jaa'afar ya ce.

Ta jinjina kai, ya juya ya ce "Kar ki ce mini kar dai layin masu barar kike bi kema? An kin shige hakan Safiyyerh ina mijin naki"

Ta yi shiru kawai.

"Zo muje ki amshi kayan abinci, ai mabarata ke zama wake ke kam ko albarkacin mijinki ai za ki ci ko? Mutane irinku cikin gidan ake kai ku"

Safiyyerh abincin take buƙata, don haka bata tsaya nazari ba ta shiga gaban motar da Jaa'afar ya buɗe mata, daman kuma ta san Jaa'afar ɗin tare da mijinta. Ta shiga motar ya rufe shima ya shiga ciki ya ja aka buɗe masa ƙofar gate ɗin ya shiga, fitowa ya yi tare da yin gaba ta bisa zuwa wani parlour ya ce "Ga ruwa sha bari na saka a fitar miki da kayan"

"Na gode" ta ce.

Ya juya ya fita, ganin ruwan da sanyi sosai sai ta buɗe ta sha fiye da rabi har ya ƙullar mata da ciki, bata san ya aka yi ba, ba kuma ta san mene ya faru ba bacci ya ɗauke ta cikin gidan Boɗejo a parlon da Jaa'afar ya ajjiye ta.

Da salati ta farka ta miƙe da ƙyar kanta na juyawa, ta yi mamakin ganin hijjabinta can nesa sumar kanta a barbaje "Subuhanallahi" ta ce tana saka hijjabin Jaa'afar ya shigo yana murmushi ya zuba mata idanu ya ce "Kin tashi? Daga shan ruwa sai bacci? Muje na saka miki kayan a motata sai na sauke ki" da ƙyar take cilla ƙafafuwanta da suka mata nauyi ta fita sai ta samu kanta da tunanin matar nan data riƙe ta gam, motar ta shiga ya sauke ta har gida da buhun shinkafa kayan

abinci fal ya ɗauki kuɗi ya bata wani almajirin Malam ya shigar da kayan ciki zumbur Malam ya miƙe yana washewa Safiyyerh baki ya ce.

"Sannu yar nan"

Ta durƙusa ta ce "Aby ina yini?"

"Lafiya allahamdulilah ta shi kin ji"

Ammo kallon kayan kawai take, Safiyyerh ta ce kuɗinta take ta siyar da ɗan kunnenta, ita dai Ammo ta kasa magana. Safiyyerh ta yi cefane ta yi shinkafa da miya da kifi ta zubawa Aby da Inna Binta da Mama Zaituna. Suka dinga godiya sai kuma suka ji ba daɗi na abin da sukai mata nan take soyayyarta ta wanzu a zuƙanta su, itama ta ci abinci sai ta samu nutsuwa ta fara miƙa ƙoƙwan bararta ga Ubangiji akan ya dawo da hankalin Mutallab.

*

Da sauri yake tafiya gaf gaf ƙirjinsa na rawa, gama yin gwangwan ɗinsa kenan su VJ suka biyo shi, ya fara bin lungu-lungu domin tsere musu ya san suna kama shi ba za su bar shi dare ba, shi kuma a wannan lokacin tunaninsa ya yi kan Safiyyerh ya ji Kano kawai yake buƙatar komawa idan na kashe shi za'ayi gwara ayi hakan ya yi kewar Safiyyerh, ko bacci yake murmushinta yake gani, ko ya jita a jikinsa ko ya dinga surutan ta da wannan mitsitsin bakin nata ya kasa sukuni, ya kuma yi kewar shiga dawa da yin farauta, ya sake yin kewar karnukansa, ya kuma ki ɗaukar fansan mutuwar uncle Ade kawai yake son yi.

Wani layi yayo tun a bakin wajan yaga mutane sun cika sosai, amma sai ya ƙarawa tafiyarsa sauri daga shi sai jan gajeren wando da kuma wata blue ɗin singlet duk ta yi dauɗa.

"Wata na kiran ka"

Ya ji saukar muryar wani ɗattijo, sai ya yi sak domin tunda ya zo Lagos bai taɓa tsayawa da wata mace ba, bai taɓa magana da wata ɗiya mace ba. Ya dinga juya manyan idanunsa can ya ce "mistake ne"

"Wanne mistake? Duk tarin jama'ar da suka baibayeta amma ta nunaka sai ka ce mistake? Muna zaune kawai mu kaga ta fito daga mota ta yanke jiki ta faɗi jini na zuba ta bakinta da hanci, sai kuma ta fara tari ba'a san wace ba, amma kana zuwa gilmawa ta nunaka muka ce ko ta sanka shine ta ɗaga ko magana bata iyawa fa, malam da kai take "

Girgiza kai Mutallab ya yi, kamar an masa dole ya ce "Sorry, bani ba" ya faɗa yana juyawa ganin su VJ they already here. Har ya fara tafiya sai ya ji ƙafafuwansa sun yi sanyi to wace wannan? Ya juya yaga an cika wajan kamar ma accident aka samu, mutane sun zagaye ta a hankali ya fara takawa zuwa wajan yana kutsa kan shi, dam! Ƙirjinsa ya buga da matsanancin ƙarfi domin da fuskarta ya fara cin karo.

BOOK 1 ZAI ƘARE A PAGE 50 KUMA ENDING NA DAWOWA LABARI.

ZAMU FARA BOOK 2 A TELEGRAM KU SANI BOOK 2 SHINE MADARAR LABARIN KU HANZARTA SAUKE TELEGRAM WANDA BAYA CIKIN GROUP NA TELEGRAM YA YI MINI MAGANA.

ZA KU JI RASHIN KUNYAR TAYO KO YANZU DAI ZUCIYA TA GIRGIZA KUMA SAƘO YA FARA ISA.

A CIGABA DA FOLLOWING NAWA ON AREWABOOKS.

[1/7, 9:37 PM] Sis Fauzy: Chapter 48: Sleep with me

Tana kwance idanunta rufe a gefen titin, mutane duk sun zagaye ta ganin kyakkyawar yarinya a wannan halin, shi ma ɗin kallon fuskarta yake da kyau,

mamakin ganinta ya saka shi kasa wanin yunƙurin taimaka mata, shi tunani ya yi daman tana raye a duniya? Lagos ta dawo da zama? Sai ya ɗauke tunanin hakan a ransa tunda ba damuwarsa bace, abu ɗaya kawai ya tsora ta shi da ganin yadda Aafiyyah ta sauya, duk tsananin iya wankanta da ajin nan nata amma ita ce yanzu kamar ka hura mata iska ta faɗi, ta koɗe ta yi wani iri kamar mai ciwon ƙanjamau.

"Ba tsayawa za ka yi kana kallon ta ba, ka santa?" Cewar wani daga cikin mutanen wajan, ya tambaya yana juyawa ya kalli Mutallab dake tsaye kamar an dasa shi ya kasa cewa komai.

Da ƙyar ya ce "E"

"To allahamdulilah ya kwana gidan sauƙi ai"

"Matarka ce?"

Ya juya ya kalli mai tambayar yana jifansa da wani irin kallo bai tanka shi ba, saboda bai san me zai ce ba, hankalinsa ya rabu amma ya ji ko su Vj zasu kashe shi he can't go without her, ko taimaka mata duk da basa wani good time, in fact ma ya manta da ita completely, kuma ganinta a yanzu sai ya ji kamar irin wacce ta yi masa laifi shekara da shekaru ta gudu, wani irin haushinta ya kama shi. A hankali Aafiyyah ta dinga buɗe idanunta da ƙyar, dam! Ƙirjinta ya buga lokacin da idanunta ya sauka a kan shi, lokacin da idanunta ya shiga cikin nasa, jikinta ya fara rawa amma ta daure saboda mutanen da suke wajan, sai ta ji inama tana da ƙwarin miƙewa ta isa gare shi? amma ina ko hannunta ba zata iya ɗagawa ba, zuciyarya ce ta dinga rawa ta kasa cigaba da kallon shi saboda tana kallon yadda ya haɗe mata fuska yana zabga mata uwar harara kamar yadda ya saba.

"Baiwar Allah mijinki ne?"

Aafiyyah bata kalli mai tambayar ba, sai sake kallon Mutallab da ta yi suka haɗa idanu, ya tsare ta sexcy eyes ɗinsa wanda suke launi da classy guy ɗin nan, kallon da yake mata mai kama da jin amsar da zata bayar.

Mutumin ya sake cewa "Mijinki ne?"

"He is" ta ce shortly silently.

"To madallah, bawan Allah bai kamata ka dinga barin matarka a irin wannan halin, amana ce ita a wajanka fa, ba haka aure ya ce a dinga wofitar da yaran jama'a ba"

A lokacin Moh Safiyyerh ce ta faɗo masa a rai, domin tabbas ya wofitar musu da yarinya a lokacin da take tsananin buƙatarsu, a lokaci na farko da ya ji ya yi ladamar yin komai, a lokacin da ya ji he is ready to be with her har numfashinsa na ƙarshe. Juyawa ya yi ganin su Vj suna kusa dab, ba kan shi yake jin tsoro ba ita Aafiyyah yake jiyewa ɗin, cikin sauri ya ƙarasa kusa da ita, so yake ya ce ta tashi su bar wajan, amma ji yake kamar ya saka ƙafa ya yi ball da ita haka kawai, a hankali ta juyo da kanta zuwa direction ɗin da yake durƙushe suka kalli juna, hannunta ta miƙa masa ya dubu tafin hannun fari fat kamar ba babu jiki ya bi zanen hannunta da idanu, da sauri ya kalli idanunta da fuskarta ya sake kallon zanen hannunta, sai ta jinjina masa kai da rausayar da kanta zuwa gefe idanunta na lumshewa, shirunta ya nuna masa ba zata iya tashi ba domin ko numfashi da ƙyar take yi, gashi sai lumshe lulu and sparkling eyes take yi a cikin idanunsa kamar mai jin nauyin ganinsa.

Aafiyyah kallon da take wa Mutallab irin kallon nan ne da yake nufi da. “I see my future in your eyes” ta janye idanunta tana sake miƙa masa hannunta, ɗaya hannun kuma ta ɗora a cikinta.

Siririn tsaki ya ja, ya saka hannunsa ya ɗauke ta gabaɗaya, sai ya ji ko Safiyyerh ta fita nauyi, a kafaɗarsa ya sakata yana jin jikinta zafi zau, ya saka hannunsa ya kwashe tarkacanta ya ɗauki jakarta, daidai nan su Vj suka ƙarasu sai ya ƙarawa tafiyarsa sauri, suka mara masa ya ɗaya ya saka dutse ya cillawa Mutallab, cikin rashin sa'a ya sauka a kansa ta baya, sai da ya runtse idanunsa ya ji ɗomin jini ta bayan nasa, amma a haka ya ƙara sauri a lokacin kuma Aafiyyah tuni numfashinta ya daina harbawa, ya nemi texci ya ce "Hospital"

Suna zuwa asibiti aka amshi Aafiyyah a emergency, ya dinga duban bills ɗin inda Allah Ya taimaka sai an gama dubata za'a biya, akai mata komai. Yana zaune a reception wani dr ya ce "Hi Man, mu je office"

Miƙewa Mutallab ya yi yana shiga ya jingina da jikin bangon office ɗin, dr ya ce "ka zauna mana? Magana za mu yi ai"

"I'm okay here" ya ce in short.

"Mene matsayin yarinyar a wajanka?"

"Stop bushing around the bush, just go to the point ok?" Cewar Mutallab.

Dr ya ɗaga kafaɗa ya ce "Ok, kasan yarinyar nada ciwon hawan jini kuma yana nema ya yi worse? Kun san cewa tana yin shaye-shaye? Ka san cewa damuwar da take ciki yana gab da taɓa mata zuciya? Duka kasan wannan?"

Shaye-shaye! Kalmar ya daki zuciyar Mutallab, idanunsa ya ɗan sauya ya dinga kallon dr ɗin a hankali a kuma daƙile ya ce "Ka yi komai, zamu koma gida ko?" Dr ya ce "Shikenan, ruwa muka saka mata saboda zazzaɓin jikinta da gajiya sai injections da mukai mata, zuwa anjima zaku iya tafiya Allah ya ƙara afuwa". Ta shi Mutallab ya yi tare da barin office ɗin.

Cikin dare ruwan ya ƙara, zazzaɓin ya sauka motsin da ta ji ya saka ta buɗe idanunta dr ya ce "My patient, are you awake?" Bata ce masa komai ba, ya gama cire mata ruwan ta ɗan yunƙura kaɗan tare da jingina da jikin gadon, numfashinta na sauka a hankali. Dr ya ce "Ya kike jin jikin naki yanzu?" Bata kalle shi ba, ya ɗauki file ɗin ta yaga sunan da aka buɗe mata da shi an saka “Safiyyerh Abdu” ya ce

"Safiyyerh ya jikin?"

Ta ɗago jin sunan daya kira ta, kenan da sunan matarsa ya buɗe mata file? A hankali ta ce

"Yana ina?"

"Ya je zai biya bills"

Dr ya ji kamar ya yi mata maganar me ya sa take shan kodin? Har ya fara ratsa jikinta? Sai kawai ya share tare da fita daga cikin ɗakin yana mai cewa "Allah Ya ƙara sauƙi"

Aafiyyah ta rufe idanunta, hannunta a cikinta basa tuna ranar ko kaɗan, da Allah ya nufa da a wannan ranar zata mutu, sai take ganin kamar a yanzu ne hakan ke faruwa. Bayan ya yi kissing ɗinta ya tafi, ta gama zamanta a wajan can ta miƙe a hankali ta yi kamar zata tafi class sai ta fasa ta nufi hanyar library domin nan ne babu kowa can kuma wajan lap, tana shiga gabanta ya faɗi ganin Mutallab tsaye jikinsa na rawa ya hargitsa kansa, sai kuma buga kansa yake da jikin bango, idanunta da glasses tuni wani irin rauni ya kama zuciyarta, tsoron rasa

Mutallab ya wanzu a zuciyarta, ta nufe shi da sauri tana cire glasses ɗin idanunta a hankali ta ce "Yaa Muhammad"

Juyawa ya yi zuwa gare ta, suka kalli cikin idanun juna, ya dinga kallon cikin idanunta, a zafafe ya fara yin baya ya cigaba da buga kansa wani yake jin kamar ana buga masa da guduma idanunsa jajur haƙoransa sai gab-gab suke yi, a tsorace ta sake nufarsa ba tare data san cewa baya cikin hayyacinsa ba.

"Yaa Muhammad"

"Out!" Ya ce cikin tsawa.

"I can't go anywhere"

"You can't?" Ya ce yana fiddo idanunsa, sai ta matsa kusa da shi suna fuskantar juna, idanunta cike da hawaye ta jinjina masa kai ta ce "E, i can't"

Ya taune lips, yana jinjina kansa idanunsa kamar gauta ya ce "Why?"

"I love you"

"Out"

Ta sake cewa "I love you"

Aafiyyah ta saka hannunta ta riƙe nasa, sai ta ji hatta hannunsa ya kasa zama waje guda, ta ɗan juya the place is so dark, akwai duhu. Ta matse hannunsa a hankali ta kifa fuskarta a tafukan hannunsa ta fara shasshekar kuka, hawayen na sauka a hannunsa cikin sanyin murya ta ce.

"Zamu raye tare in sha Allah, zamu kasance tare idan Allah ya nufa, zamu zama ma'aurata da izinin Allah. Kullum ina karatu saboda kai, kullum ina ƙarfafa zuciyata akan ka, ba zaka fahimta ka yi mini al'ƙawari zaka jira ni"

Kau! Ta ji saukar maruka a fuskarta, a gigice ta ɗago kanta domin tunda aka haife ta ba'a taɓa yi mata irin wannan ɓarin makauniyyar ba, ta buɗe baki za ta yi magana Mutallab ya sake ɗauke Aafiyyah da wasu gigitattun maruka laɓɓansa na rawa ya ce "What?"

“I love you”

Shuuu, ta ji saboda gwara kanta da ya yi jikin bango nan take hancinta ya fara zubar da jini, ganinta ya fara ɗaukewa ta sulale a wajan ta zube saman ƙafafuwanta, sai ta ji kanta kamar ba'a jikinta ba, ta buɗe idanunta da ƙyar ta sake dubansa sai girgiza kansa yake cikin rawar murya ta ce "I never stop loving you"

gani ta yi yayo kanta, yana zuwa ya durƙusa gabanta, cikin sauri ta yi kneel down, tana haɗe hannunta tana bashi haƙuri, kar ya yi hannunsa ya miƙa ya shaƙe mata wuya, ta fara kai masa cizo da ya ƙushi, sai ya yi cilli da ita ko ganinta ba ya yi sosai shi gabaɗaya ji ya yi kamar ana hura masa wuta cikin kansa, Aafiyyah ta kasa kuka har ya yi waje ta sake motsi, motsin da ya sake motsa ƙwaƙwalwarsa da ciwon da yake ciki a yanzu,ya dawo da sauri ya ɗaga ƙafa ya taka mata gefen ciki a lokacin idanunsa ya cika fal da hawaye, ya fice da sauri. Dukan cikinta da ya yi numfashinta ya ɗauke, sanyin wajanne kuma ya farfaɗo da ita, da ƙyar taja jikinta bata gani sosai ta nufi class lokacin an tashi wayarta ta ɗauka ta kira Mj, bata sake sanin inda kanta yake ba. Likitoci suka tabbatarwa Mj duka ne, kuma Aafiyyah ta dinga samun matsalar ciwon ciki kenan, ya ce sai ya ɗaure Mutallab ta dinga kuka tana bashi haƙuri akan ko Paaah kar ya faɗawa, wannan dalilin ya saka take yawan riƙe cikinta.

*Ajjiyar zuciya ta sauke, ta ji zafi-zafi a maƙogaranta ko ƙurajen ne suka dawo mata? Daman dalilin ƙurajen maƙogaran take shan ruwan zafi da gishiri saboda ta ji dama.

A hankali ya buɗe ƙofa ya shigo, ta yi saurin rufe idanunta iya yan minutes ɗin nan da ta yi da ganinsa tunaninta ya ragu haka nauyin zuciyarta. Ya dinga kallon ta sosai.

Calmly ya ce "Who are you?"

Ta buɗe idanunta, ta kalle shi sai taga ƙasa yake kallo kamar zai ta yi magana sai ta share shi.

A ƙule ya ce "Who are you"

"I have to ask you this, who are you?"

Ya ɗago ya kalle ta, sai yaga itama wani wajan take kallo, ya lura da hawayen dake sauka a hannunta sai ya share ta. Ya daɗe yana tunanin me zai ce can ya ce "Ki tashi ki koma gida"

"Binka zan yi"

Ya bubbuɗe idanu sosai ya ce "Me?"

Ta ɗago masa shanyayyun idanunta a hankali can ƙasa kamar mai raɗa ta ce "Ka ji ai"

Ya dinga kallon bakinta, ba dai zata sauya ba, a tiger most be a tiger. "Bani da kowa a nan ɗin, Allah ka yi mini faɗa ramawa zan yi" ta ce tana turo bakinta idanunta ya sake lumshewa, ya lura bata iya barin idanunta a buɗe sosai.

Sakkowa ta yi ta saka vail ɗin rigarta, sai yaga ta ɗan kusa kama shi a tsayi, juyawa ya yi ya fita, ta ja jakarta ta bi bayansa, a cikin asibitin ta ciri kuɗi masu yawa ta saka a jakarta, lokacin data fita har ya shiga texci itama ta shiga ɗakin da yake ɗaukan haya ya nufa, mai wajan ya ce ai ba zata shiga ba shima ba zai shiga ba sai ya ɗauki kuɗinsa ya bashi, Aafiyyah ta ciro 100k ta bawa mutumin, kana ta shiga ciki, tana shiga taga ɗakin kaca-kaca amma jiri take ji ta yi saurin kwanciya ta rufe idanunta nan take bacci ya ɗauke ta.

Sanda ta farka taga shi kwace can gefe guda, ya rungume hannunsa da alama ya saba rungume abu a ƙirjisa idan zai yi bacci, daman jiya ta gama al'ada sai ta yi alwala tai sallah, addu'a take son yi amma ta rasa me zata ce ta yi shiru, can kuma ta durƙusa ta fashe da kuka, duk abin da take yi yana jinta ya share, kukan Safiyyerh ma bai ɗaɗa shi da ƙasa ba balle na Aafiyyah, Aafiyyah tun a Switzerland kwananta biyu wajan Shila ta kashe wayarta domin ta san defenetly sai Paaah ya yi tracking location nata, daga nan sukai booking tickets, a nan kuma Shila ta ce zata je Lagos lokacin suna tsaye a cikin airport, Aafiyyah ta dinga kallon airport ɗin tana jin kamar bata kyauta ba, wanne hali su Ummi zasu shiga yanzu? Kasancewar bata jima da gama shan Kodin ba a cikin lemo hakan ya taimaka ta kasa yanke shawara da ganin abin da yake daidai da kuskure.

“Aafiyyah follow Shila to Lagos” haka ta ji zuciyarta tana ƙissima mata a lokacin, duk da cewa bata da kowa a can Lagos ɗin, ta yi shiru tana kallon mutanen da suke shiga jirgi, ta samu kanta cikin difficulty in decision-making, ta dai ji ba zata jure

zama waje guda ba, ƙokarin nemawa kanta farinciki take ko ta yaya ne, yanayinta ya zama irin psychomotor agitation, ita dai kawai ta ji she have to go, she have to runaway jikinta na rangaji idanunta na lumshewa ta fara taka steps ɗin jirgin da zai kai ta Naija to Lagos ba tare da sanin a can ƙaddarar take ba. Sanda suka ƙarasu ta nemi Shila ta rasa ta dinga tafiya har ta yanke jiki ta faɗi a daidai lokacin ne kuma ta hango shi.

"Za ki iya fita waje, idan kin gama kukan ki dawo kin gane ai"

"Ok" ta ce tana miƙewa tsaye ta nufi hanyar buɗe ƙofa, ya tuna ta nan Lagos ne? Ya miƙe jikinsa sanye da full dress ya nufi ƙofar ya saka hannu ya rufe, ya juyo ya kalle ta sai ya koma ya zauna itama dawowa ta yi can kusa dashi ta durƙusa a gabansa ta ɗora kanta a cinyarsa, a hankali ta fara sakar masa wani irin kuka mao rauni da cin zuciya kukan da duk kafiyar Mutallab sai da ya ji zuciyarsa ta raunata, ya saka hannunta ya ɗago fuskarta ya ce.

"Kee"

Ta ce "Baka san sunana bane? Safiyyerh"

"Safiyyerh ɗaya na sani, matata"

Ta jinjina kai ta ce "Ta faɗa maka saƙo na?"

A message? Wanne saƙo "Na bata saƙona ta baka mana" Mutallab sai ya tuna sanda a makaranta ranar da za'a kori Safiyyerh tabbas ya ji tana cewa Kinal anyi auren Aafiyyah kuma ba'a ƙasar zasu zauna ba, maybe wannan shine saƙon sai ya jinjina kai alamar eh.

"So You received the message, baka neman ba? Shine baka neman ba ko Yaa Muhammad?"

Ya yi mata shiru, a lokacin tunani ya fara ko a cikin maye take? Tunda dai an ce shaye-shaye take yi abin yana ransa kawai baya jin zai iya mata magana wannan personal life ɗinta ne, don haka yanzu ma sai ya ɗauka she is on drug.

"Meka yanke?"

Ya yi shiru, a hankali ta yi murmushi wanda bai taɓa gani a fuskarta ba ta ce "Ya Safiyyerh tana lafiya? I want to meet her"

"Me ya kawo ki Lagos kina mace?"

"Ƙaddara!" She replied.

"Ya Kimiyya da Nahyan da Kinal?" Ya mata shiru, ya fahimci idan ta yi magana bata sake yi sai da zubawa mutum ido sai sanda ya amsa mata gently ya ce "Lafiya"

"Me ya kawo ki Lagos?"

"Kai ne dalili Yaa Muhammad"

"What?" Ta kashe masa idanu ɗaya tana ɗaya gira ta ce "Ina son chocolates"

Ya yi shiru, can ya juya ya kwanta ta ce "Za mu yi magana da safe ok?" Ta kasa bacci sam, sai juyi yake yi, shima ɗin kasa baccin ya yi saboda wani irin ciwo da kansa yake masa, ya manta bai sha magani ba, kamar ciwonsa kuma na son tashi idanunsa rufe ya ji Aafiyyah ta gangaro jikinsa a karo na farko bacci ya ɗauke ta, kanta a damtsen hannunsa hannunta ɗaya a waist ɗinsa irin baccin da take yi a jikin Paaah idan bata da lafiya. Ya zubawa fuskarta idanu yana rage girman idanunsa saboda hasken fuskarta dake shigar masa cikin idanu, Aafiyyah idanunta kamar na mage suna da jan hankali tana da dugun wuya, cikin kaya jikinta a ɓoye yake amma Ubangiji ya yi mata halittar dirin jiki, fuskarta looking so sexcy, idan

tana bacci innocent face ɗinta ke bayyana za ta yi saurin yafe laifi, amma tana da bakin tsiwa, a hankali ya zame ta daga jikinsa ya koma can gefe ya buɗe ido, ya sake tashi zaune a lokacin Safiyyerh ce a ransa, yana mai ɗauke da daɗɗan tunanin dake ransa tare da replacing nasa dana Safiyyerh.

“Tiger!" Ya ce a fili.

*

Safiyyerh na zaune ta iddar sallah hannunta riƙe da carbi tana azkar ta ji an yi sallama sai Ammo ta amsa sai yaron ya ce "Wai gashi a bawa Safiyyerh" tana zaune Ammo ta ɗaga labulan ɗakin ta ce "Safiyyerh gashi wai"

"Mene Ammo"

"Kuɗi ne"

Ta dinga kallon kuɗin, ta miƙe ta amsa ta duba 200k cif, da sauri ta fita wajan tana fita motar na barin wajan sai ta yi tunanin ko Jaa'afar ne? Ta dinga juya kuɗin ta ce "Ammo anya ni aka ce?" Ta ce "Wace Safiyyerh bayan ke?"

"Kuɗin da yawa, ban san waye bafa"

Mama Zaituna ta ce "Wanda ya kawo kuɗin nan yana sane fa, gidan nan ya turo kuma kece Safiyyerh kinga taimako ne daga Allah"

Inna Binta ta ce "Haka ne kam"

Ita dai ta dinga tunani a ranta, sai ta ɗauki dubu goma goma ta bawa Mama Zaituna da Inna Binta, ta siyi sabulun wanka da mai da sauran amfani sauran suka sai kayan abinci.

Kawo lokacin Safiyyerh ko kuka ta daina yi, Allah kawai take kawai kukan ya kawo mata sauƙi kuma ta yarda duk abin da Ubangiji ya yi da rayuwata a lokacin shine sauƙin da take nema. Kullum tana saka Mutallab cikin addu'arta sai ta ji tana neman idan ta zalunci Aafiyyah to Allah Ya sakawa Aafiyyah tun a nan duniya. Hijabinta ta saka ta cewa Ammo zata bakin titi yanzu zata dawo, Ammo bata hanata ba domin tana buƙatar nutsuwarta ta dawo jikinta sosai. Safiyyerh na fita ta tsari napep ta nufi gidan Boɗejo, cikin sa'a ta same shi wannan karon ma sai shiga gidan yana murmushi ya ce "Matar Mutallab again"

"Ina yini?"

"Alhamd, shigo" ya ce yana buɗe mata ƙofar motar shiga ta yi, suka nufi ciki a ranta tana jinjina girman gidan da ƙarfin arziƙin mai gidan yadda baya gajiya da bata sadaƙa, bayan sun zauna palron ya ce "Lafiya dai?"

"Kai ne ka bada kuɗi a bani?"

Jaa'afar ya ce "A'a, mene?"

"Babu, daman aiki nake nema idan zan samu Please?" Jaa'afar ya dinga kallon Safiyyerh da mamaki ya ce "Bai dawo bane?"

Ta ɗaga masa kai ya ce "Ina zuwa"

Ficewa ya yi daga cikin ɗakin, Safiyyerh ta miƙe ta dinga zagaye tangamemen parlon idanunta ya sauka akan wata ƙofa haka kawai ta ji bari ta nufi ƙofar, tana zuwa ta buɗe ƙofar sai ta sake cin karo da wata ƙofar glass, ƙofar kuma da idanun mutum take amfani, idanun ma sai wanda aka saita da shi, amma abin mamaki Safiyyerh na kallo ƙofar ta fara buɗewa ta tura kanta ciki, bakinta ɗauke da addu'a

gabanta ya faɗi ganin yɑn mata da yawa wasu a ɗaure wasu a ƙwance wasu da jarirai a hannunsu, wasu kuma da ƙaton ciki, tsala-tsalan yɑn mata ajin farko. Sai ta fara tunanin ko asibiti ne? Wata ce ta kalli Safiyyerh ta ce "Kawo ki akai nan?"

Da rashin fahimta ta ce "A'a, da kai na shigo"

"Baiwar Allah ki bar wajan nan kafin ƙaddara ta saka ki zaman cikinsa, runaway"

"Ban fahimta ba"

"Mene ba ki fahimta ba? Nan da kika gani duk zawara ne mu, kawo mu nan ake maza na yi mana fyaɗe har sai mun samu ciki, kuma cikin daman suke buƙata wata su saka ta yi ɓari wai ɓarin suke so, wata kuma tana haihuwa ko jaririn bata gani ake ɗauke shi, wata kuma a wajan haihuwa take mutuwa su cillar da gawar, ke har ƙoda an taɓa cirewa wata a cikinmu, da suka tabbatar zata mutu kuma ƙodarta tana da kyau sai aka cire daga cikinta suka ƙarasa kashe ta" budurwar ta fashe da kuka sosai tana kallon Safiyyerh ta ce

Ya ƙarasu kusa da ita, zata gudu ya damƙo ta ya zare hijabin jikinta, da wani expression yake kallonta ashe daman ba kaya bane a jikinta ya dinga kallon saman ƙirjinta da cinyoyinta da shafaffen cikinta, ya sake matsu da ita, ya manne ƙugunsu waje guda da kuma kyau har tana jiyo tudun mararsa da motsin ta, yatsarsa ɗaya ya saka ya cire ribbon ɗin kanta sumar ta sauka muryarta na rawa ta ce "Mene haka? Baka da gaskiya ko?" Ya jinjina kai alamar eh can ya ce "Kin gudu without my permission saboda ban isa ba, zan nuna miki mijinki ne yau yadda daga yau ɗin zan zama gefanki" jininta na rawa sosai jinin ya sake manna mata ƙugunsa ta ce "to mu yi sallah, ka zar amarci?"

A kunnenta ta ji saukar dariyarsa yana shafa tsakiyar bayanta da yatsarsa ya ce "Allah ba ki da kai Fiyya, ba kin ye mini nama da coke ba?" Ya faɗa yana kunce igiyar gaban skirt ɗinta daidai nan rigar jikinta ta faɗo ƙasa. Muryarta na rawa ta ce "Bestie" yana zura tongue ɗinsa cikin kunnenta ya ce "Uhm call me TAYO" can ya ce "Fiyya" ta ce "uhm" yana sake riƙe ta ya ce "Yi unzip ɗin wandona...

MUTALLAB PAID BOOK

#500

PAY BEFORE YOU READ

08164069385

[1/7, 9:38 PM] Sis Fauzy: Chapter 50: Died

Book 1 end

Jikinta ne ya tsananta ɓari jin abin da yake mata wanda bata shirya ba, baya ma gabanta domin ta cire rai da samun hakan shi ya sa sometimes bata son raɓa jikinta da nashi domin yana sata kwaɗayi tare da tunanin abin da ya riga ya yi mata nisa, musamman data lura ba haka ɗinne shi a zuciyarsa kuma a gabanta. Ta runtse idanunta da kyau kyarmar jikinta na sake yawa, numfashinta ya fara ɗaukewa, da ƙyar ta buɗe idanunta saboda ƙafafuwanta da suka kasa ɗaukar gangar jikinta. Lura da hakan ya saka shi ma ɗin ya tsahirta daga tsayen da suke duk da cewa riƙe take a hannunsa ya kuma jingina da jikin bangon bedroom ɗin, a hankali ya zare fuskarsa daga wuyanta ya cire hannunsa daga ƙirjinta a hannayensa ya ɗauke ta

zuwa saman gado, jinta a gadon kuma ya saka ta yunƙura tana sakin kukan shagwaɓa.

Ta rirriɗe shi da hannunta ta ce "Ka mayar dani gida, ni ban so ban so"

"Auren ne bakya so, ko ni? Ko sunnar dake cikin auren?" Ya ce yana riɗe dariyarsa ganin yadda duk ta fita hayyacinta sai kukan banza take yi.

"Ni ka kyale ni" ta ce, bai kulata ba ya cigaba da abin da yake mata, deep down na zuciyarsa shima ɗin a tsorace yake domin sai ya samu kansa tamkar bai taɓa aikata abin da yake shirin yi ba, a duk sanda ya kalli fuskar Safiyyerh sai ya ce Astagafirulla wa'atubu ilai, sai ya roƙi yafiyar Ubangiji sai babu adadi, domin har azumin kwana uku ya yi, ya kuma dinga sadaƙa, a kullum gani yake Safiyyerh kamar zata fahimci abin da ya aikata. Cire wannan tunanin hakan ya yi a ransa completely ya fuskanci matarsa dake cikin ƙirjisa wacce aure ya halatta masa ita halak malak.

Dukkan wata soyayya da gangar jiki ke nunawa zuwa ga masoyinta tuni gangar jikin Mutallab ta gama bada shi, ya amsa asalin sunansa na TAYO ya amsa sunan jinin yarabawa masu tsananin son matansu da ƙwarewa wajan nuna soyayya. Dukkan wani asirin da yake lullube a zuciyar Moh don gane da Safiyyerh a wannan lokacin ya gama bayyana kan shi. Wannan qualities ɗin na baƙin namiji Safiyyerh ta gama ganinsa, wani irin tsoro da shakkar mijin nata take ji, da tasan cewa abin da ake ji kenan da ƙaddara bata gwada mata ganin Ummeyh da Daddy ba, babu komai cikin abin da take kwaɗayin sai tsananin azaba. Ta ɗaukan yadda take jin small touches ɗin da yake mata yana ratsa zuciyarta da kisses and hugs ɗin haka shima yake amma sai ta fahimci shi na musamman ne domin ɗan ƙaramin yaƙi suka yi da Mutallab. Ya dinga tausayinta ya ji ya haƙura sai ya rabu da ita, can kuma ya ji he can't.

Kissing ɗinta ya cigaba da ya yi, ya hanata damar yin magana kamar yadda jikinsu ke a haɗe waje guda, haka zuciyoyinsu, a haka ya samu nasarar zuwa inda yake buƙata a wannan lokacin Safiyyerh ko motsi ba ta yi idanunta a lumshe jikinta zafi sosai. Mafarkin Safiyyerh ya zama gaske, mafarkin Safiyyerh ya tabbata ta amsa sunan Mrs Muhammad Mutallab Abdullahi.

Almost 20 minutes ya kasa motsi he still lay on her body, ya riƙe ta sosai idanunsa rufe, bai san me yake ji a zuciyarsa game da Safiyyerh ba, ya dai ji no matter what happens zata cigaba da amsa sunan matar Moh, wannan kimar har abada tana nan a idanunsa til janna. Can ya mirgina ya sauka a kanta tare da saka hannunsa ɗaya ya dafe kansa dake sara masa yana masa ciwo sosai, haɗuwarsa da kimiyya ƙaddara, zuwansa Fgc mafarin ƙaddarar ne, haɗuwarsa da Safiyyerh toshen ƙaddarar ne kamar yadda Ubangiji ya ɓoye manufar haɗuwarsa da Aafiyyah. Safiyyerh is nothing but a blessing to him. Ya sai ji kamar an ɗauki tawada an rubuta sunansa dana Safiyyerh a jikin tagulla ne. A hankali ya juya kaɗan ya kalle ta, fuskarta ta yi jajur hawaye, majina musamman lips ɗinta kamar zasu cire saboda tsananin azaba haka ƙirjinta. Ya ja jikinsa a hankali zuwa gare ta, tana jin motsinsa ta yi saurin juya masa baya.

A raunace ya ce "I'm not a virgin right?" Ya yi maganar a hankali kuma cikin ƙirji domin yadda yaga ta juya masa baya sai ya ɗauka ta fahimci shi ba cikakken namiji bane kamar sauran masana. Ya saka hannunsa biyun ya dawo da ita jikinsa ya ɗora kanta a ƙirjinsa duka su biyun sukai shiru, ita kunyar haɗa idanu take yi dashi. Ya ɗora bakinsa a kunnenta yana hura mata iska a hankali mai daɗi ta lumshe idanunta, da sauri ta juya da kumburarrun idanunta tana kallon shi cikin kuka ta ce "Ka she ni ka wuta"

"For second round"

"Me?" Ta ce a ruɗe. Yana shafa sumar kan ta slowly ya raɗa mata "ina son zaƙin strawberry nan, ya nuna sosai ya yi gardi Ubangiji ya sa ya zubar da yabanya mai kyau, i appreciate it, i appreciate the sweetness, my appreciate goes to Mr Moh. Jannatul-firdausi ta ki ce"

Ta yi masa shiru. Ya sake riƙe ta a jikinsa idanunsa na shigewa ciki. "I am sorry"

Ta yi saurin buɗe idanunta, da ƙyar ta ce "Sorry for what?" Ya ce "Na miki laifi mai girman da ba za ki iya yafe mini ba, kuma duk matakin da za ki ɗauka kin cancanci ki ɗauke shi ne" ta dinga kallon shi gabanta na tsananta faɗuwa zuriyarta na karaya sosai a hankali ta ce "Me kenan?" Ya juyo da fuskarta zuwa gare shi numfashinsu na sauka a hankali ya ce "Zan faɗa miki, bana daga cikin masu ɓoye zunubi. I slept with Uhmm uhm Aaf.....," ya kasa ƙarasawa ganin ya buɗe ido lokacin gudu ƙirjinta

ya yi wani masifar bugawa ta cikin nasa ƙirjin muryarta na rawa sosai ta ce "Aafiyyah?"

"Uhm"

"Ina ka ganta? Is she still alive dama?"

Ya dinga kallon fuskar Safiyyerh sosai jin ta ce daman Aafiyyah har yanzu tana raye, sai ya kasa magana a hankali ta yi murmushi ta ce "Ikon Allah, kaga hukuncin Allah lallai babu abin bautawa da gaskiya face Ubangiji, mai yin yadda ya so a kan bawa a kuma sanda ya so, mai yin hukunci a gurbin da ya so" shi dai kallon ta yake yi idanunsa sun yi jajur, ƙoƙarin haɗiye hawayen idanunta take yi tana sake yin murmushi ta ce "bani labari" ya girgiza mata kai ta saka hannunsa ya shafi sumar kansa ta ce "Zan fi cutuwa idan ka ɓoye mini" a hankali ya bata labarin duk abin da ya faru duk da ba ɗabi'ars bace bada labarin abin da ya faru, ta dinga murmushi kawai taƙi cewa komai. Muryarsa na rawa ya ce "Ina jin tsoron Allah, tsoran haɗuwa da Ubangiji deer, tana aure keta haddin aure ba abune mai sauƙi ba a wajan Ubangiji, kamar ke ce wani ya miki haka sai inda ƙarfin Moh ya ƙare zan iya bada rayuwata wajan ganin an hukunta shi Allah zan iya kashe mutum"

Taƙi kallon sa idanunta can gefe ɗaya, zuriyarta ta tsaya can ƙirjinta ya mata nauyi kuka take son yi gabaɗaya ta kasa wani irin duhu take gani ta cikin idanunta, abin da ya faru tsakanin mijinta da Aafiyyah ta fara jin tsoro da kuma tuhumar kanta, idan Ubangiji ya ƙaddara samu ɗa tsakanin Mutallab da Aafiyyah kuma ta zama hijabin hana haka ta hanyar hana shi wasiƙun Aafiyyah tabbas za'a samu ɗan shege kuma sanadinta ne. Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, Ubangiji ya saka gwada mata cewa ƙaddarar Mutallab ta Aafiyyah ce duk wayonta da dabararta sai Allah ya haɗa su a Lagos a lokacin da take zaton Aafiyyah bata duniyar.

Ya girgiza ta ya ce "Talk deer"

"Baka tunanin Aafiyyah ta rasu akan wuƙar daka caka mata?"

Ya yi shiru bai taɓa kawo hakan ba, domin yama ɗauke wannan tunanin "yaushe ta yi aure kuma?" Safiyyerh ta sake tambaya. Sai ya tsare ta da idanu can ya ce "Ke kika ce ta yi aure a wata ƙasar kece nan" ta buɗe idanu ashe ya ji lokacin yana lura da wasu abubuwan. Ta yi masa shiru ya sake juyo da ita ya ce "I am sorry please" zame jikinta ta yi duk da ciwon da yake mata ta sauka a gadon jikinta na rawa, shima miƙewa ya yi ganin kamar jikinta rawa yake yi.

"Safiyyerh, wait" ya ce yana zuwa wajan, kafin ya ƙarasu ta ɗauki wata ƙatuwar kwalba data gani can gefen gadon ta cilla masa, ya yi saurin gocewa, ya nufi wajanta zai riƙe ta, ta yi saurin cillewa ta ɗauki wani ƙarfen labule ta dinga buga masa tana wani irin kuka jikinta duka rawa yake da ɓari da kakkarwa idanunta rufe ga wani zazzaɓi daya saukar mata, ta gaji ta sake ɗaukan dukkan abin da ta gani tana cilla masa, ya yi tsaye kamar an datsa shi idanunsa jajur wani irin tausayin Safiyyerh yake ji, ya ji dama bai faɗa masa gaskiyar abin da ya faru tsakaninsa da Aafiyyah ba. Amma baya son su yi zaman aure yana ɓoye mata wani abu, da sauri ya ƙarasa wajanta ya saka hannunsa ya riƙo ta sai a lokacin wani irin raunataccen kuka ya ƙwace mata, bata da wani wajan yin kukanta inda ya shige ƙirjinsa. Kuka take tana dukkansa da faɗin "Why? Why?"

Ya kasa furta kuma komai sai "I am sorry wife" shine kawai yake cewa, sorryn da take fitowa tun daga ƙasan zuciyarsa, sulalewa suka yi tare da zubewa a tsakar ɗakin kuka take sosai shi kuma ya kasa cewa komai, domin kukan shine sauƙi a zuriyarta ya fahimci matsanancin kishin Safiyyerh tun da jimawa, ba kowacce mace mijinta zai tunkara ya ce mata ya kwanta da wata mace ba ta lamunta ba. Muryarta na rawa ta ce "Sa mini kayana" ya jinjina kai ya ɗauki kayan ya saka mata ya ɗauki hijabin ya saka mata. "I am sorry deer" ta kalle shi idanunta kamar gaushin wuta sai ta yi murmushi ta ce "Allah Ya shirye ka"

"Za ki iya tafiya?"

"Uhm" ta ce kawai, cikin sauri ya zura nasa kayan ya durƙusa gabanta ya ɗauke ta, ya sake tabbatar Safiyyerh ta fi Aafiyyah nauyi nesa ba kusa ba, har mota ya kaita ya koma ya rufe gidan ya shiga, a hankali yake driving very careful, ganin yadda jikinta yake...

"Mu je asibiti?"

"My mother was a doctor" ya jinjina kai, tare da kwantar da kujerar idanunta rufe sosai sun ɗan jima suna tafiya ya saka hannunsa ya kamo nata, taƙi buɗe ido ya matsa hannun kaɗan ta juya ta kalle shi ya ce "ba ki ce kin yafe mini ba?" Ta harare shi ta ce "Allah shi ne shaida na yafe maka" ya ce "Uhm" Safiyyerh ta ji har abada ba zata bari Mutallab ya san komai game da Aafiyyah ba, kuma ta ji daɗin yadda ya ɗauka tana da aure sai dai bata yi tunanin a budurwa ya samu Aafiyyah ba ko bazawara, ta ji Allah Ya sa Aafiyyah ta riga ta mutu tun a Lagos. Da wannan tunanin suka ƙarasu zata fita ya ce "Ji mana" ta juyo ta kalle shi "bari na shigar dake" ta haɗe fuska ta ce "sannu, na yafe to" ya jinjina kai kawai, damar motar uncle Musbah ce ya kira shi ya aike shi shine ya biyo ta gidan.

Yana kallon yadda take tafiya a hankali har ta yi nisa ta juyo ta ce "Mutallab" da mamaki yake kallon ta, yana jiran jin me zata ce sai ta ce "Ka bawa uncle Musbah takaddar sakina, ba zan iya cigaba da zama da kai ba, na haƙura da kai matsayin miji" tana cewa haka ta shige gidan nasu, Hausa ta yi masa tabbas amma sai ya kasa fahimtar me take cewa. Wayarsa ya ɗauka ya kira ta tana ringing bata ɗauka can ya shiga DM nasa abin da bai taɓa yi ba kenan.

"Kin yi kaɗan, rayuwa yanzu Moh ya fara dake ki nemi wanda za ki rainawa hankali ban dani yarinya, a allon lauhil Mahfouz Ubangiji ya rubuta sunana da naki matsayin ma'aurata"

Yana gama rubutawa ya tura mata sai ya ji hakan bai gamshe shi ba, a lokacin na farko bayanin shuɗewar shekaru da haɗuwarsa ya rubuta mata “Muhammad Mutallab Abdullahi loves Safiyyerh Abdu” ya sake tura mata yana cije lips.

Abu kamar wasa, Safiyyerh ta kashe wayarta shi kuma yaƙi zuwa gidansu, har Ammo ta gaji ta tambaye shi Safiyyerh sai ya ce tana nan kawai, ya fahimci idan ya nuna mata waye shi raini ne zai shigo ciki ta je ta ƙarata ai ba mutuwa zai yi ba, sai dai duk dare baya iya bacci ya fara kiran wayarta amma a kashe sai ya dubata a WhatsApp shiru.

Ya sake shiga DM nasa ya rubuta mata

"Ni ko? Ya miki kyau"

"Ba za ki kashe ni ba Fiyya"

A haka har wajan sati biyu, lokacin kuma yaje neman Ja'afar amma baya samunsa numbersa ma baya tafiya. Ummeyh na zaune a main parlor ita da Safiyyerh da kuma Prof da uncle Musbah Wizzy ya shigo Daddy ya ce "Wizzy lafiya?" Ya rusuna ya ce "wai mijin Safiyyerh yana waje" da sauri Safiyyerh dake cinyar Ummeyh ta miƙe zaune ta ce "ka ce bana nan" uncle Musbah ya watsa mata harara ya ce "ce masa ya shigo" Safiyyerh na ƙokarin miƙewa tsaye zata bar wajansa ta ganshi ya shigo, idanu suka haɗa ya watsa mata uwar harara kai tsaye kuma wajanta ya nufa uncle Musbah ya ce.

"Safiyyerh tsaya mana, mene ya haɗaku"

Idanunta cike da hawaye ta ce "uncle ba komai" Mutallab ya ce "liar"

"Muhammad mene?" Cewar uncle Musbah. Mutallab ya buɗe ba ki ya ce "Cewa ta yi wai na sake ta" daga Prof har Ummeyh kallon Mutallab sukai da Safiyyerh, ita Ummeyh sai yau ta fara ganin Mutallab, a fuskarsa akwai nutsuwa kuma baya ɗaukan raini ko wasa yanayinsa ya nuna rashin iya ƙaryarsa a fili, tsayayyen namiji. Ya sake yin ƙwafa yana kallon Safiyyerh sosai ya ce "me na gaza miki dashi? za ki zo mu tafi ko yaya? Ni ba zan iya sakin ki ba amma ke ki saken" murmushi kawai uncle Musbah yake yi, daidai nan Wahee ta shigo ita da Nahyan.

Duka su biyun kallon Mutallab suke musamman Nahyan, ganin yadda Mutallab ya dawo ya kare masa nesa ba kusa ba, ga sumar kansa da saje da gemu wanda suke sake bayyanar da girman nasa. Uncle Musbah ya ce "gaskiya, ke Safiyyerh saki ɗan mutane tunda kin fasa auren" Ummeyh ta miƙe ta haura upstarts Dady ma ya miƙe ya ce "Musbah ka bari su yi magana" yana cewa hana ya nufi part ɗinsa, uncle Musbah ya fice.

Nahyan ya ce "Wonderful, Moh don't tell me cewa kai ka dawo haka?" Ya faɗa yana ƙarasawa wajan. Moh bai juyo kamar bai gane mai magana ba ya ce "Sannu" Nahyan ya ce "Ikon Allah kwana da yawa kana lafiya?"

Ya jinjina kai, Wahee ta sake jinjina girman kan Moh yanzu fa ta ji yana magana ko iya Safiyyerh ya kewa? Ta dinga kallons shi sai ta ji ya yi masifar burgeta tana son namiji mai aji ko a cikin maza hakan yana nuna mata basa gabansa. Wahee ta juya ta kalli Nahyan ta ce masa "Uncle Aliyu yana hanya"

Sai gaban Safiyyerh ya faɗi sosai. Nahyan ya bar wajan haka Wahee suna barin wajan Safiyyerh ta ce "bani hanya"

"Sa'anki ne ni? Ni za ki cewa na ba ki hanya idan ban watsa miki yatsu ba"

"A'a fa, ko ka manta age mates muke? A shekaru dai ba zaka nuna mini fankama ba" ya dinga kallon ta ya kasa cewa komai ta ce "a saboda kaga ba damu da kai kake duka wannan abin? Ina ta wahalar banza a wajan da bani da kima da mutunci inda ba'a so na?". "Ina ne ba'a son ki ɗin?" Ta ƙure shi da idanu ta ce "Wajanka kana so na ne? Baka taɓa furtawa ba ko a cikin wasa balle gaske so ba zan iya zama da wanda baya so na ba"

Ya damƙo kafaɗunta yana huci ya ce "Safiyyerh cewa i love you na Indomie generation, akwai soyayyar da baki ba zai iya furtawa ba sai dai gangar jiki ya yi aikinsa, na fa san me nake yi, a duk sanda kika ce bana son ki ina jin kamar na watsa miki yatsun hannuna a fuskarki, ki nutsu ki gane na miki kyakkyawan tanadi, Moh ya shirya ba ki farinciki, ke zinariyata ce kece gwarzuwata fiyya, ni kawai bana gane wannan kalmomin ban iya su ba, amma zuciyata na motsawa dake a kullum, You are my wife my role model berewata" ya ce yana sake riƙo ta. Tana kuka ta ce "To ka ce kana so na" ya kalle ta sai ya dungure mata kai ya rungumeta sosai suka sauke ajjiyar zuciya "Da ana wa mutum albishir ɗin shiga aljanna da na miki albishir da cewa na ba ki aljanna, i am sorry for everything wife"

"It's okay, i love you"

ya sumbaci goshinta ya ce "akwai abubuwan dana tanadar miki da yawa a gidan Moh, har wanda ba ki yi tsammani ba, na shirya mana komai"

"To faɗa mini komai da komai" ta ce yana riƙe ƙugunsa tana murmushi.

"Sai kin shigo, amma daga ciki har da sunan da zan sawa babyna na fari"

Ta bubbuɗe ido sosai ta ce "Sannu, wannan gaggawa haihuwa ba yanzu ba, ai ba zan haihuwa ba don ka ji ko zan haihuwa baka nan" sai ta tsoro mata ido ya ce "To ina zani? Ni da na yi cikin"

Ta ɗan daki kafaɗarsa ta ce "To wanne suna zaka sawa babyn?"

Sai ya ɗora hannunsa a cikinta ya ji shafal ya dinga yi mata irin kallo narkar da zuciya a hankali ya ce "Safiyyerh M. Abdullahi" wani irin farinciki ya lullube zuriyarta idanunta ya cika sosai ta ce "Na ji dama na haihuwa yanzu" a hankali ya ce "with time"

"My husband my problem, my husband my headache I adore you so much"

"Ke zinariya ce, zara cikin taurari ki ji daɗinki matar Muɗallabi ni halaliyyarki ne" sun jima a haka bayan sun fahimci juna ya dinga mata labarin Lagos ya shaida mata su Vj ne suka kowa masa mota da wasan banza ya faɗa mata har abin maye suka bashi sai bata ji daɗi ba, a wajan ya yi mata promise ba zai sake barinta ba duk tsanani ta ce zata zuba masa abinci ya ce a'a baya so.

Duk abin da suke yi Daddy yana ganinsu ta cikin part ɗinsa Safiyyerh kawai yake kallo. Bayan Mutallab ya tafi Wahee ta sakko ta ce "Safiyyerh wai ina ƙawarki ne?" Ta ce "wakike magana Kinal?"

"Nop, Aafiyyah"

Ta yi shiru sai ta ce "Ta yi aure ai"

"Ikon Allah, tana da kirki sosai kin san cewa ita ta yi wa Captain magana akan ya daina takura miki, kin san faɗa mukai da ita sosai har na yi mata gorin cewa ta daina shisshigi ake ke yar'uwata ta daina shiga family issues, tana murmushi ta ce Wahee kenan soyayya Ubangiji ke ƙulla ta yadda nake son Safiyyerh sai dai ke ki nuna mini jininta ce amma ba za ki fini son ta, fitina a ƙwance take babu ribar kina ƙuntata zuciyar Safiyyerh saboda tana da haƙuri ki ji tsoron Allah Wahee ba faɗa zan dake ba, gaskiya nake faɗa miki next time kika sake yi wa Safiyyerh abin da zai sata kuka wallahi sai na rama mata kuma ki zuba ido ki gani kenan" cewar Wahee ta ce "ban ɗauka za ta yi aure bamu ji labari ba, duk da ba mate ɗina bace Aafiyyah nada kirki over"

Murmushi kawai Safiyyerh ta yi ta ce "Allah sarki" ta faɗa tana barin waje.

Wata guda aka saka tariyar Safiyyerh, Ummeyh ta dage wajan gyarata ta sake yin order na kayan S Bayero tun a cikin sati biyu idan Mutallab ya zo wajan Safiyyerh baya iya riƙe kansa, baya ce mata komai sai dai ya yi ta kallon ta, burinsa yaga lokacin ya yi. Uncle Musbah ne ya siya mata sabbin furnitures Daddy ya bawa Mutallab gida amma ya ce a'a ya gode da karamci amma nasa ya wadace shi in sha Allah. Ya dage da aiki har lokacin kuma ya rasa Jaa'afar. Sa'adah ta faɗawa Anty Hameeda cewa za'a yi bikin Mutallab ba shiri ta sauka a Kano, suka je har gidansu Safiyyerh lokaci ɗaya ta ji ƙaunar Safiyyerh a ranta domin ita bata ɗauka an yi auren ba. Ta dage zata bawa Tayo gudunmawa ya ce baya so.

*

Sunan Boɗejo ya amsa amo a ko'ina arziƙinsa kamar hauka kullum ƙara yawa yake kuɗi ya rasa ma ya zai yi dasu al'umma kowa Boɗejo saboda tsananin taimakonsa da jin ƙan da yake nunawa mutane, mabuƙata suka sake yin yawa a ƙofar gidan nasa kuma baya gajiyawa.

Jaa'afar ya kalli Boɗejo daya kasa zaune ya kasa tsaye ya sake juyawa ya kalli Jaa'afar a hankali ya ce.

"Na kasa fahimtar hakan zata faru sam Jaa'afar, bana fatan wani ya san da zaman yʻan matan nan a gidan nan, bana fatan asan asalin abin da ake aikatawa a wannan gidan, Jaa'afar na samu duniya ina kan samu kuma na ji daƈin yadda yaron nan bai sanni ba, bai kuma san ni ya kewa aiki ba, ina tunanin zamu matsa zuwa next plan"

Ja'aafar ya yi murmushi ya ce "mene shiri na gaba Sir?"

"A nemo mini su waye masu Arƈos group, ina son shiga kamfanin FS WORLD INVESTMENT COMPANY"

"Sir gano masu Arƈos group zai yi wahala ko a fuska ba'a taɓa ganinsu ba, kuma a yanzu sune gaba da FS WORLD INVESTMENT COMPANY" cewar Jaa'afar.

Boƈejo ya yi shiru a hankali ya ce "Zan gano sannu a hankali, Jaa'afar kana maganar DNA test ƈin nan hakan ba mai yiyuwa bane domin ban taɓa samun ƈa ba, kuma ban shirya samu ba, bana ra'ayi zan ji daƈi Laylerh ma sau ƈaya tausayin ya saka ta samu ciki, shima kuma Allah ya rufa mini asiri tun ƈan ciki ya mutu sanda aka yi mata Sc a mace aka ciro shi

duk sanda ta samu ciki sai na zubar da shi saboda ra'ayin kaina da abin da nake shiryarwa" Jaa'afar ya ce.

"Sir shikenan maybe mistake ne"

"Haka ne ma, Ja'aafar ko Ali wali ya nemi ganina ka ce bana ƙasar wayoyina basa shiga ka ji ko?"

"In sha Allah Sir"

Sallama suka yi, Boƈejo ya nufi part ƈinsa haka kawai ya samu kansa da kunna CCTV camera ƈin ɓangaren da yʻan'matan suke, a hankali ya dinga kallon su da yadda maza ke kokawa dasu wajan kwanciya har ya kawo in da Safiyyerh ta shiga a ruƈe ya miƙe tsaye jikinsa yana rawa ya dinga kallon fuskar Safiyyerh, yana

mamakin yadda idanunta suka buɗe ƙofar har lokacin da wata kewa Safiyyerh magana ya lura kuma kamar ta bawa Safiyyerh wani abu, da sanda Safiyyerh ta bar gidan. "Damn it, who's she? Wayarsa ya ɗauka yana fita ya nufi ɓangaren daya ajjiye jibga jibgan mazan da suke masa aiki yana kiran sunansu ko ta kan Ja'aafar bai bi ba saboda gigicewa da tsoron fallasar sirrinsa.

*

US/ NYU Langone Hospitals

Wata guda Aafiyyah ta shafe bata san inda kanta yake ba. Dr Zuhair na tsaye kanta yana duddubata yana mamakin yadda zuciyarta ke gudu sosai amma babu inda yake motsi a jikinta. A hankali ya ja kujera kusa da ita ya zauna cikin ƙwarewa da likitoci ya kama hannunta yana shafawa cikin turanci ya fara kiran sunanta a tausashe.

"Sofiia Sofiia Sofiia"

Kasancewar da Safiyyerh Abdu aka buɗe mata file, kalamai yake mata masu taushi da ƙarfafa mata qwwia na cigaba da rayuwa da samun abin da take so amma har ya gama zuciyarta bata amsa ba. Fita ya yi, a hanya ya ci karo da wani dake sanye da farar t.shirt da amy colour ɗin p.cap ba'a ganin fuskarsa sai gemunsa da lips ɗinsa hannunsa zube cikin aljihu, suka haɗa idanu da Dr Zuhair amma ya kasa cewa komai sai dubawa yake ko zai ga Mj amma baya nan.

"Hy, how can i help you?"

Ya faɗa yana miƙawa mutumin hannu sai yaƙi bada hannunsa can ya ce "Safiyyerh Abdu Please?" Dr Zuhair ya ce

"Oh, she is my patient yayanta ne?"

Shi dai bai ce komai ba, Dr Z ya ce "Daman muna buƙatar taimako Please follow me" ya ce yana yin gaba,ba hankali ya taka ƙafafuwansa ya bi bayan Dr Z sanda idanunsa ya sauka akan Aafiyyah ji ya yi gabansa ya faɗi ya yi saurin saka hannunsa ya cire p.cap ɗin kansa ya ƙarasa kan ta. "Ka yi mata magana masu daɗi ka faɗa mata sunanka ta ƙarfafa mata qwwia?" A hankali ya ja ya tsaya ya yi shiru can ya nemi waje ya zauna ya kama hannunta ya riƙe cikin nasa, me ya sameta har haka? Me ya sa ba'a faɗa masa ba? Meke faruwa ne? Ya yi shiru a hankali ya ce "I need ur life angel, i just need you angel" ya ce yana murza tafin hannunta ya sake yin ƙasa da muryarsa kamar tsoro magana ya ce

"Rayuwa akwai wahala, Allah na son bawa mai takwalli Ubangiji na tsananin son ki little sis, ba zamu ji daɗi ba idan babu ke, Paaahh is here, Ummi is here, ur brothers even me I'm here saboda ke"

Ƙara na'urar ta fara cikin farinciki Dr Zuhair ya ce "Go on please"

"Safiyyerh wake up or else i will shoot your head" ƙara computer ta cigaba da yi sosai sai ya ji ta damƙe hannunsa sosai, ya ɗaga kai yaga idanunta na zubar da hawaye ya miƙe ya nufi kanta da sauri Dr Zuhair ya kwaso kaya ya fara danna mata ƙirji lokaci kaɗan gabaɗaya computers ɗin ɗakin suka fara ƙara.

"Continue, cigaba da magana" cewar Dr Z

Shi dai kallon fuskarta yake a hankali ya duƙa daidai kanta ya ɗan mari fuskarta ya shafi hawayen idanunta da ƙyar ya iya cewa "I love you Safiyyerh"

Jikinta ne ya ɗauki rawa sosai kamar mai jijjiga da sauri ya sake ta ya fita, yana fita Mj ya shigo don haka basu haɗu ba, Paaah yana dogara sanda ya shigo haka Ummi suka rufu akan Aafiyyah. Ummi kuka take haka Mj Paaah idanunsa ya yi jajur. Idanunta ta fara buɗewa slowly slowly har ta gama sauke ganinta akan Paaah, a hankali ta lumshe idanunta da sauri ya kama hannunta ya ce "No please Mahmah". Lokaci ɗaya suka salati suna kiran sunan Allah guda ɗari babu ɗaya har Aafiyyah ta samu zarafin kama abu guda muryata bata fita ta ce "Astagafirulla Ya Allah" ta ce a hankali tana lumshe idanunta can ta sake buɗewa ta ce "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un innalillahi".

"Ku faɗa mata duka abin zaku faɗa cikin minti talati ku saka ta yi sallah" ya ce yana cire mata abubuwan jikinta. Mj ya matsa ya ɗago ta jikinsa ya rungume a hankali ya ce "Maamah, kin bar gida ke da shila ƙawarki kin bita zuwa Lagos" ta juya kanta dake ƙirjinsa ta zuba masa idanu, kallon dake nuna maganarta ta kamarya? Ya riƙe hannunta ya ce "Da gaske nake bayan hakan kina shaye-shaye shila na ba ki abin maye cikin lemon da kike sha, kin yi abubuwa da yawa Maamah but we love you, we believed ƙaddara ce"bakinta ne ya fara rawa idanunta na zubar da hawaye da ƙyar ta fusgi maganar ta ce "Na kasa tunawa" ya ce "Ba ki san kin yi ba" ta kalli Paaah da yake kallon ta, ta miƙa masa hannunta ya tashi ya koma kusa da ita nunawa ta yi tana son kwanciya jikinsa, a hankali Mj ya dawo da ita jikin Paaah jikinta kamar wuta ta damƙi gaban wuyan Paaah ta ce "Allah na fushi dani Daddy ban amsa sunan yarinyar kirki ba, ban san komai ba, ban san mena aikata ba, na kasa tunawa na ji kamar daga mafarki na tashi, ban san na bar gida ba, ban san na je...," ta yi shiru Mj ya ce "Lagos" ta jinjina kai "Paaah ka yafe mini, don Allah" sai ta fashe da kuka.

"You have been raped"

Da wani irin sauri ta juyo ta kalli Mj da ya yi maganar yana rushewa da kuka, Paaahh ya runtse idanunsa. Aafiyyah ta yi saurin barin jikin Paaah ta sakko daga kan gadon tana miƙewa ta yanke jiki ta faɗi, ta sake miƙewa nan ma ta sake yanke jiki ta faɗi. Mj ya sauri zuwa zai riƙe ta, ta nufi wajan Paaah ta zube a gabansa ta riƙe ƙafafuwansa tana sakin wani irin kuka ta ce "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un na shiga uku Daddy na shiga uku na lalace ka ce mini ba haka bane, ku ƙaryata abin da na ji. Wayyo Allah wayyo Allah don Allah don Allah ku ce ba haka bane, ku ce ba'a yi mini fyaɗe ba innalillahi wa'inna ilaihirraji'un" Paaah ya kasa riƙe hawayen idanunsa ya durƙushe gaban Aafiyyah Ummi ta fara magana.

"Repeat after me Maamah"

Kuka Aafiyyah take tana fisge-fisge ƙirjinta na ɗagawa Ummi ta ce "Astagafirulla wa'atubu ilai"

A gigice ta ce "Astagafirulla wa'atubu ilai"

Paaahh ya riƙe Aafiyyah ya ce "Allahumma rabba jibra’ila wa mika’il wa israfil fadiras samawati wal ard aalimal gaibi wasshahada anta tahkuma baina ibadika fima kanu fihi yakhtalifun,Ihdini’ila makhtulifa fihi minal hakki bi’iznik" numfashinta na ɗaukewa ta maimaita ta ce "Ka yafe mini Daddy kar na mutu da hakƙin ku i don't know what comes over me, ban san na yi komai ba, Ummi, Yayaku yafe mini ko tayani neman gafarar Ubangiji, Ummi shikenan na rasa mutuncina ba wanda zai aure ni a haka na shiga wayyo Allah"

"Safiyyerh na yafe miki duniya da lahira, kuskure na ne, laifina ki yafe mini"

"Daddy ba ka yi mini komai ba kana da hakƙin sani duk abin da kake so"

Dr Zuhair fita ya yi yana goge hawayen idanunsa, gani yake kamar ƙwaƙwalwar yarinyar ta samu matsala, ta jima tana yin abubuwan da bata san tana yinsu ba. Paaah da kansa ya ɗaura mata alwala, tai ta yin sallah bayan ta idar sai Ummi ta fara addu'a da sauri Aafiyyah zata kama ta ƙarasa tana kuka sosai. A hankali ta ɗora kanta a ƙasa shiru shiru bata ɗago ba, suka dinga kiran sunanta amma shiru Dr Zuhair ya shigo da sauri ya ce "su fita gabaɗaya su yi mata addu'a lokaci ya cika" a wannan karan ma Paaah yake jiki ya yi ya faɗi babu numfashi.

Mj na zaune kusa da Aafiyyah ya ji tana cewa "I am waiting for you, zaka dawo ko? Zan jira ka Allah kar ka manta ni"

*

An gama jeran gidan Safiyyerh tas tariya ya rage gobe an hana shi zuwa ganinta komai. Ta vedio call ta yi masa gwalo tana nuna masa zanen ƙunshin da Sss henna ta yi mata har gida. "Kwalelen mutum don ka ji" ta ce tana nuna masa gyaran gashin kanta da ya yi kyau sosai

Ya yi shiru ta ce "Kana ina ne?"

"Gidanki" ya ce a hankali idanunsa na ɗan jirkicewa ya zuba mata ido.

Ta yi dariya ta ce "Allah sarki gwauro"

"Yau ne kawai, gobe yarinya muna manne da juna ki adana shagwaɓarki kamar yadda na adana miki abubuwa masu yawan gaske yar nan" ta yi masa fari da idanu ta ce "Wani ya yi missing matarsa ko ba ka yi ba?" Cikin sexcy voice ɗinsa ya ce "kullum cikin kewarki nake ai Safiyyerh, i miss You all the day"

Ta yi mamaki kwarai domin bai taɓa faɗa ba, sai ta yi murmushi tana sunkuyar da kai domin kunyarsa ce ta kamata a tsakiyar kanta ta ji muryarsa ya ce "About the henna, ya yi ƙwarai ya zanu raɗau kamar yadda zanen sunanki yake zuciyata Safiyyerh"

"Uhm thank you"

Ta ɗago kai suna haɗa ido ta langwaɓar da kai ta ce "Ya Anty Hameeda?"

"Lovey-dovey" ya furta silently

Ta haɗe fuska ta ce "Amma tana nan?"

Ya hankali ta ce "mo nifẹ rẹ"

"Ina Ammo"

Sai ya kalleta yana murmushi ya ce "Ban taɓa tunanin zan taɓa so irin wanda nake miki ba. Ban taɓa yarda zuciyata zata cika da tunanin wata mace irin haka bayan ta Mahaifiyata ba. I never thought I'm gonna get attached to someone like this. I just love you without no reason. My biggest fear right now is losing you. I don't wanna lose you. Thinking of losing is what makes me really sad. I love you so much. I'm gonna love you to the rest of My life!..." lumshe idanunta ta yi idanunta na cika da hawaye farinciki sosai ta ce "Kana so na ashe?"

"Tun kafin yanzu" ya ce can ƙasa yana sake kallon ta zanen ƙunshin hannunta.

Cikin nutsuwa ta ɗaga masa hannun ta nuna masa ta ce "I'm grateful you do but little ne. Bai kai nawa son ba" ya kashe mata ido ɗaya yana zaro mata harshensa tare da mata wasa romantically.

Ta sake cewa "Smile. A bayyane yake ai. Har yanzu baka faɗa mini yadda kake jina a ranka ba sai yau. You keep giving excuses, ban sani ba kunyata kake ji ko kuwa bakya so ne in raina ka"

Ya yi ta girgiza kai yana murmushi jin abin da ta ce ya jima yana murmushi gwanin sha'awa ta ɗauka ba zai magana ba sai taga ya ɗaga kafaɗa ya ce "But i love you, Fiyya come please"

"Ina?"

"Our house"

Ta yi dariya ta ce "Ka jira gobe don ka ji" bata taɓa ganin taɓarar ɗan auta ba sai yau ya zage yana mata shagwaɓa sai ta ji kamar su kaɗai ne a duniyar a haka dai ta lallaɓa shi ya kashe vedio call ɗin. Minti biyu da kashe kiran taga ya sake kira ta ɗaga ta ce "Huh my headache"

Yana mata dariya a kunne sosai ya ce "Na ji ɗin nan" ta ce "Ya akai?"

"I love you, Muu'ahh" ya sauke mata kiss ta cikin wayar kana ya kashe kiran.

*

State cid suka sake matsa neman wanda suke zargi tare da baza jami'an tsaro ta ko'ina duk da kwana biyu abubuwa sun musu yawa. Sai ya zamana idanunsa yana ko'ina har inda ba'a yi zato ba.

Muhammad Mutallab Abdullahi ya sha gyaran kai su gyaran farce au gyaran fuska, gifts ya tanada kala-kala daya tana da domin bawa Safiyyerh.

Wayarsa ya ɗauka ya kira Sa'adah ta ɗauka ya ce "Yaya" ta cikin wayar ya ce "Ya aka yi?" Ya haɗe fuska sosai ya ce "Bangane ya aka yi ba, kun kai mini mata ko yaya?" Sai ta yi dariya ta ce "Ban sani ba ɗan rainin wayo kamar wani son ta kake yi" kashe wayar ya yi ka kira number Anty Hameeda.

Bayan ta ɗauka ya ce "Babbar yaya, mene labari ne?" Ta ce "Auta manya, kaga mun kusa ƙarasawa ai, mun ɗakko maka Safiyyerh in sha Allah zamu kai ta, kaga dare ya kusa sai ka shirya da wuri" kashe kiran ya yi ya dinga kallon farar shaddar daya ɗinka, daman ya yi wanka sai ya shirya tsaf cikin shaddar yana banza wani irin ƙamshi, ya zauna ya dinga kallon pictures ɗin data tura masa

farar lafaya Ummi ta saka mata ta yi kyau matuƙar kyau, har bidiyon da Wahee ta yi mata tana kuka sosai tana riƙe Ummi da Daddy Wahee ɗin ta tura masa ta wayar Safiyyerh ɗin. Yana zaune yaga shigowar saƙon ta ya duba yaga ta saka "Ina son bestie sosai"

Ya yi murmushi ya ce "Bestien beastie"

Ya yi sallama da Ammo already daman Aby baya kula Mutallab, bashi da wasu abokai Goje har yanzu bai dawo ba, Nahyan ya koma kimiyya still har yanzu bai san duniyar daya shiga ba. A hanya ya tsaya ya siya mata balago mai zafi da lemo da yougourt. A haka ya nufi gidan wani irin nutsuwa yake ji da kwanciyar hankali a zuciyarsa, yaga ƙofar a buɗe ya duba bai fi minti biyar da tafiyar su Anty Hameeda ba da suke cewa yɑn kai amarya, sai ya yi tunanin ko wasu ne basu tafi ba ko mantawa sukai ƙofar a buɗe, kan shi tsaye ya nufi cikin gidan tsit ba kowa ya shige parlo ba kowa sai ya yi murmushi ya nufi bedroom yana cewa "Ina matar Moh ta shiga?" Ya shige bedroom ɗin yaga wayam ya girgiza kai ya ce "Allah Ya shirya Barewata" ledar hannunsa ya ajjiye ya dinga dubata bata sai yaga ƙofar banɗaki ya ce "Fiyya my wife...," maganar ce ta tsaya masa a maƙoshi ganin ya ɗora ƙafarsa cikin jinin dake kwance a bakin banɗakin ƙirjinsa ya yi wani irin bugawa da ƙarfin

gaske, ya dinga kallon jinin sauri ya yi zai juya sai ya ji na bugo ƙofar banɗakin ana kakari, da sauri ya shiga.

Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un! Kwance ya hangota cikin jini farar lafayar jikinta kamar an tsoma ta cikin jini, tulin gashin kanta ya hargitse ya jiki sosai kamar jini ke fitowa ta cikin kan, cak zuciyarsa ta tsaya, sai ya fara ganin duhu-duhu cikin idanunsa, da ƙyar ya ja ƙafarsa zuwa wajanta ya zube sai a lokacin a lura wuƙar da take cake a maƙoshinta kamar ma maƙogaro aka yanka mata, ya sake ganin gefen cikinta da aka caka mata wuƙa har bai san adadi ba, jikinsa duka rawa yake ya cakomo ta jikinsa saman farar shaddarsa ya rushe da wani irin kuka yana girgizata tare da faɗin "Safiyyerh, Safiyyerh buɗe idanunki waye ya yi miki wannan waye ya yi wa matata haka, me ya sa ba'a jin tausayina ne me na yi wani, Safiyyerh don Allah don girman ki tausayawa ki buɗe idanunki ki faɗa mini waye ya miki haka? Kar ki tafi ki bar ni, na rasa Munebbehy, na rasa Diyna, na rasa Jaanah, na rasa uncle Ade, ke da nake shirin ki haifa mini zuri'a, ke da nake mu rayu har abada Barewata...,"

Idanunta ta buɗe da ƙyar hannunta take ɗago masa ya dubi hannun yaga farar takadda ce, ga biro can gefe kamar yanzu ta yi rubutun ta damƙa masa takaddar, kallon shi take yi tana murmushi kallon kaga zaɓin Ubangiji dana nema ko? Ƙoƙarin zare wuƙar dake cake a wuyanta yake amma daya ɗago jini yake ambaliya.

"No Safiyyerh please, zamu rayu tare kar ki mini haka" numfashinta ne ya fara tafiya ta ƙura masa ido sai ta yi masa alama daya rungumeta, kamar zai tsaga ƙirjinsa ya mayar da ita ciki haka ya ƙanƙameta, yana wani irin kuka yana ji ta tura masa farar takaddar aljihu da wani abu kamar memory. A daidai kunnensa ta ce "Ka tabbatar ka rama mini, kai gwarzo kar ka yi kuka" jikinta ne ya fara saki duk maganar da zata yi sai jini da ya yi fitar gurbi daga wuyanta domin rami akai mata sosai ta ce "Soyayyar nan da kake mini na gamsu, soyayyar nan da kake mini ka tabbatar

ta nuna kanta wajan ɗaukar mini fansa, kar ka yi kuka don Allah mijina kar ka yi kuka ka toshe kunnenka, i love you"

Kansa ya kifa a fuskarta yana wani irin kuka sosai sai ya ji ta ƙanƙame shi tana razana alamar ɗaukan rai numfashinta idan ya fita baya dawowa sai ya ji ta riƙe gaban rigarsa da ƙarfi duk da sabuwa ce amma sai data yaga masa ita saboda tsananin azabar fitar rai a hankali ta furta "Love Aafiyyah, duk inda take a duniya ka

nemo ta marry her, Aafiyyah's loves you so much, ka mini al'ƙawari auren Aafiyyah" ta faɗa tana miƙa masa hannunta ya girgiza kai ya ce..

"Dake kaɗai zan rayu, MUTALLAB na Safiyyerh ne only you" ta yi murmushi ta ce "Allah Ya shirya ka, take heart baby"

"Ba zan yafe maka ba idan baka auri Aafiyyah ba, ban yafewa"

Ya ce "stay with me don Allah Safiyyerh"

Jikinta na saki gabaɗaya a gigice ya fara ambaton sunan Allah, sai ya ji ta fara kalmar shahada cikin sauri ya sake ta ya nufi waje da niyyar neman mota gabaɗaya ya ruɗe, jikinsa gabaɗaya jini ƙafarsa ko takalmi babu sai kuka yake yi, haka ya nufi titi. Amma babu abin hawa ya gama bulayi lokacin minti ashirin da tafiyar su Anty Hameeda. Sake dawowa ya yi da niyyar ɗaukan Safiyyerh a hannunsa zuwa asibiti sai dai me, manyan motocin yƙan'sanda ya gani cike fal a unguwar yana zuwa sukai kansa domin sun gane shi da CCTV camerar dake kan titin, dukansa suka fara faɗin ya kashe matarsa, daidai nan su Anty Hameeda suka zo a gigice da kuma Ummeyh da daddy, Mutallab ya yi cak yana binsu da idanu domin baya fahimtar komai kuma baya jin komai sai sunan Safiyyerh da batun cewa wai ya kashe ta, ya san ba zata taɓa mutuwa ta bar shi ba. Rufe su sukai da duka nan take suka karya masa hannu, lokacin da suke saka masa ankwa a hannun a lokacin aka fita da ita zuwa ambulance an rufe ta da farin ƙyalle, kururuwa ya saka ya nufi wajan da kiran sunanta wani ya ɗaga ƙasan bindiga ya buga amsa a tsakiyar kansa, suka zura shi a mota zuwa state cid.

(Wannan shine dalilin shigar MOH state cid tsayin shekaru uku).

*

Continue...

Back to story.

Kuka take yi sosai idanunta ya yi jajur bata taɓa jin labari irin wannan ba, shi dai yana jingine da jikin kujerar da yake zaune a ƙasa kusa da ita, kansa a ƙasa jijiyoyin kansa sun fito sosai a saman goshinsa, jikinsa sai rawa yake yi yana sake hango

Safiyyerh ta cikin idanunsa a cikin jinin da murmushin da take yi, abubuwan da ya faru a zamansa cikin state cid abu ne wanda ko maƙiyinsa baya masa fatan ya shiga, zaman shekara ukun nan shine ya rusa masa komai a cikin ya san komai, a ciki kuma ya fahimci komai. Kukan ta yake ji har tsakiyar kansa a hankali ya ɗago kan shi ya kalle ta sai bai ce komai ba. Ta kalle shi ta ce "Da gaske matarka Safiyyerh ta rasu? An kashe maka ita?"

Ya jinjina kai ba tare daya ce komai ba ta sake cewa "kuma kai ne Scorpion?"

"Uhm" ya furta a cikin ƙirjinsa.

"Me ya sa ka bani labarin nan?"

Ya buɗe rinannun idanunsa a kan ta ya ce "Da gaske Safiyyerh ta rasu, da gaske nine Scorpion, ba ki labari kuma saboda na yarda kina so na, shi ya sa kikai mini alfamar so na ba ki labarina" ta jinjina kai ta ce "Allah Ya ji ƙan takwara Safiyyerh, Ubangiji ya bi mata haƙƙinta" bata da tabbacin ya amsa sai ta sake cewa "Ina Aafiyyah?"

Gefe yake kallo jin abin da ta ce ya saka ya juyo ya kalle ta a hankali ya ce "Kalli madubi za kiga kamanni da surar Aafiyyah a tattare dake, bayan barinki Lagos mene ya faru" ta yi murmushi ta ce "Stop kidding me, baka tantance mutanen da suke tare da kai" ta faɗa tana miƙewa tsaye jin kamar ƙarar mota ta leƙa taga, miƙewa ya yi shima a lokacin Goje da Mangal sun fita, bayanta ya je ya tsaya ya ce "Aafiyyah ina ɗana?"

Ta juyo ta kalle shi sai ta ce "Ɗa kuma?" Hannunsa ya miƙa zai riƙo ta ta zame a hankali ya ce "Kin ce kina so na?" Ta ce "Uhm" yana sake matsawa wajanta ya ce "Me ya sa kika ɓoye son da kike mini Ifemi? Why? Na yi Safiyyerh al'ƙawarin auren ki, kin san mene a cikin paper ɗin?" Sai ta fahimci da gaske ya yarda cewa tana son shi bayan ita tana da aure kuma tana da mijinta bayan haka duk abin da yake tunani ba haka bane. Sai ta juyo ta kalle shi ta ce "Ka yi haƙuri na baka ƙarya, ban taɓa son ka, bana jin kuma zan iya son ɗan daba kamar ka, ina da aure ina da miji, sunan mijina Maj Aliyu Abdu Marafa, matar aure ce ni kawai na yi amfani da SO wajan jin labarinka da dalilin zamanka haka, na fahimci fansar matarka ya saka ka zama ɗan daba, damuwa ta saka ka fara shaye-shaye mafita ta saka ka fara bin

Eng Ali wali" da mamaki yake kallon ta jin ta ambaci sunan Eng Ali wali, daman ta san shi ya saka ya yi kidnapped nata? Ta ce "Bani da haɗi da matarka Safiyyerh amma na tausaya mata ƙwarai ina sake jajanta maka rashin macen ƙwarai kamarta, haka bani da haɗi da Aafiyyah kawai dai sunana Safiyyerh kuma yanzu zan bar wajan nan in sha Allah"

Da sauri ya leƙa window dai yaga wasu kalar jami'an tsaro wanda bai taɓa ganin irinsu ba. Da sauri ya ce "Zo bar wajan nan waje na suka zo, dole zan cikawa Safiyyerh burinta na auren ki"

Taƙi motsawa ya ce "ki zo mu fita"

"Where? Wannan mutanen ni na kira su ai wajena suka zo ba inda zani" ya dinga kallon ta da mamaki zai kama hannunta jin jami'an tsaron na shigowa ta yi saurin ɗaga hannunta ta kifa masa mari a fuska Mutallab sai ya sak, daidai nan jami'an tsaron suka kewaye Mutallab da Safiyyerh cikin sauri ya ce "ku yi mini komai banda ita" Safiyyerh ta yi dariya

ta saka hannunta cikin wandota ta zaro wani i.d card ta ɗaga sama daidai idanun Mutallab ta ce "Ba iya Manager of FS WORLD INVESTMENT COMPANY ku kai kidnapped ba. Sunana Safiyyerh Abdul-Johar Marafa, jami'a a FID federal investigation department yar ga Dig Johar kuma tsohon laccara mai amsa sunan Professor Abdu Marafa, ba kai ne ka yi kidnapped nawa ba, ni ce na yi naka na ganka tun sanda kuka zo ƙofar kamfaninmu a napep kai da wani, aikin namu ne ya zo ɗaya, banda dalili kana tunanin zan iya zama tare daku ne?"

MOH kallon ta kawai yake yi, ina son data ce take masa to? "Team arrest him"

Daidai nan Dig Johar ya shigo, da sauri ta nufi wajan mahafinta tana sara masa, Moh Dig Johar yake kallo tabbas ya san shi tun sanda aka kai shi state cid lokacin Muneeberh. Safiyyerh ta ce "Paaah i made it" murmushi ya yi mata yana sara mata ya ce "Federal investigation department basu da kama" Safiyyerh ta yi murmushi sai kuma ta ɗan yi shiru jin kanta na motsa mata kamar yadda yake mata ta juya suka haɗa idanu da Moh binta kawai yake da idanu a hankali ta ji ya ce "Wannan key ɗin da kike nema na sanin abubuwa da suke faruwa a FS WORLD INVESTMENT COMPANY kamar yadda Ashraf ya ce ki buƙata gashi zan ba ki shi. F tana nufin friends S ɗin kuma dukkan yaran masu kamfanin sunansu ya fara daga S ɗin"

gabanta ya faɗi ta juya ta kalli Paaah da yake cewa "Mu je ko, team ku saka shi a mota"

Ya kama hannun Safiyyerh zuwa waje, jami'an tsaron kuma suka nufi wajan MOH tana gab da fita ta ji ya ce "ki tuna Fgc, Kimiyya, Nahyan, Kinal ki tuna Tayo" sarawar da kanta ya yi ya saka ta yi baya da sauri Paaah ya riƙe ta a gigice yana neman number Dr Hash a kan ya shirya allurar gasu nan "Paaah kai na, Paaah ina ganin wani a cikin idanuna" da ƙarfi Moh ya ce "Aafiyyah ki tuna Tayo kuma ki shirya bani ɗana i am for you"

Wata ƙara ta yi tana riƙe Paaah ta ce "Mutallab.....Tayo"

END OF BOOK 1

MU HAƊU A BOOK 2 PAGE 1 KUMA CHAPTER 51.

A farinciki da walwala yake anan soyayya da asalin dakakkiya take.

DA GASKE SAFIYYERH TA RASU?

MUTALLAB ZAI HAƘURA DA AL'ƘAWARIN DA YA YI WA MIRGAYIYA NA AUREN AAFIYYAH?

SU WAYE SUKA KASHE SAFIYYERH?

BATUN MAJ ALIYU ZAI SAKI MATARSA KO YA?

PAAAHH HAR YANZU BAI SAN YARON DA Y'ARSA KE SO BA.

DAM! GA MOH HANNUN JAMI'AN FID.

WAYE BOƊEJO

YA BATUN LAYLERH

INA AMSH?

MUJE ZUWA

MU HAƊU A TELEGRAM DOMIN FARA BOOK 2 IN SHA ALLAH. MUTALLAB PAID BOOK NE AKAN #500 A NEMI WANNAN NUMBER

08164069385

Na'ima Sulaiman Sarauta

Nimcyluv